□-BAKAR WASIKA-□
Mai Farin rubutu

From the writer of

RAI BIYU
HAFSATU MANGA
ZAGON KASA
ZABIN RAI
KHADIJATU
GOBENA
ZAKI
FULANI

©®Hakkin mallaka nawa ne ni Khadeeja Candy, ban yarda a sarrafamin labari ta kowace siga ba balle har a dorashi a YouTube ba tare da izinina ba, yin hakan kuskure ne babba domin zai iya janyowa mutum matsala saboda haka a kiyaye ⚠

SADAUKARWA.
Na Sadaukar da littafin nan ga Hajiya Habiba da iyalanta.

GAISUWA
Ga Mutanen Kirki, Rahma Kabir, da Mrs J Moon.

GABATARWA.

BAKAR WASIKA...
Mai farin rubutu

Idan aka ce Bakar Wasika Mai Farin Rubutu. Ana nufin wani dunkulelen sako mai wuyar fassara, kamar mutum mai nagarta sai wani mummunnan kaddara ta fada masa.

Ban ce tafiyar mai sauki ba ce.
Ban muku alkawarin zallar soyayya ba.
Ban ce babu farincikin ba.
Kunci, bakinciki da damuwa, sune abubuwan da suka taru suka tare farincikin AMINATU, kalubalen rayuwa bayan wata rayuwar, tabbas akwai kuka akwai damuwa da bakinciki.

Labarin Tafida, Rafi'a, Laila, Madina, Ramlee, Faruk, Amal, Kabir da kuma Aminatu.
Labarin BAKAR WASIKA. Labari ne da zai tabo wani bangare na rayuwar mace, kuma wani bangare na rayuwar al'ummarta da iyayenta...
Ina fatar zaku karbe shi kamar sauran, duk kuwa da na san ba lallai ne yai muku dadi ba domin ba soyayya ce zalla ba, kalubalen rayuwa ne da fadi tashin yar gudun hijira!
A ina zata kwana? Wa zai bata masauki? Taya za a fahimce ta har a nade mata damuwarta? Wa zata kaiwa kukanta iyeyenta ko al'ummarta? Ta ina mafarkinta ke tabbatuwa? Ashe bayan wuya akwai wata wuyar, bayan dadi ma akwai wata wuyar, bayan wuya kuma akwai dadi.
Tabbas akwai ciwo a rayuwar da baka san karshenta ba, akwai tsoro a mafarkin da ka gagara farkawa! Ta ina lamarin ya fara? Ina tsakiyarsa da karshe? Yaushe

damuwar zata wuce? yaushe bakincikin zai gushe? Sai yaushe hawayen zasu tsaya? Zuwa yaushe ne kuncin zai yanke?
Ashe a cikin rayuwa akwai wata rayuwa? A cikin rayuwar ma akwai mutuwa?

Labarin BAKAR WASIKA kirkiraren labari ne kamar sauran labaraina, kun san dai ban saba baku kunya ba ko?😉 Wannan ma zai zo muku fiye da yadda kuke tsammaninsa inshallahu. Sai dai ba free ba ne na kudi ne, but ina da free pages daga 1-10 ga masu son jin dandanon labarin kamin biya.
Kamar yadda kuka sani bana editing labari so ku yi hakuri da duk abun da zaku gani.

P. O. V
Na nufin Point Of View.

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

Page -1

Matashiyar yarinya ce yar shekara goma sha-bakwai dauke da farantin giɗa tana tsaye jikin window makaranta tana leken daliban da ake yi wa darasi.
Yadda ta maida hankali tana sauraren darasin da ake wa dabiban sai ka rantse da Allah har da ita a cikin daliban. Ilmin zamani na daya daga cikin abubuwan da suke matukar burge Aminatu kuma shi ne kadai abun da ta rasa a yanzu, wanda ta riga ta maye gurbinsa da talla a halin yanzu, a izuwa yanzu ta tabbatar bata da muhalli a ilmin zamani, sai dai shi ilmin yana da muhallin a zuciyarta.

"Ba ni gidar goma"

Wata dalibar ta fada da kamar rada gudun kar malamin da yake musu darasin ya ji ta, a munafunci ta jefowa Aminatu wata tsohuwar naira goma, sannan ta maida hankalinta gurin Malamin.
Aminatu ta duka kasa ta sauke farantin dake hannunta sannan ta dauki naira goma din ta daga hijabinta ta saka naira goma din cikin hular dake kanta ta gyara hijabinta sannan ta dauki giɗar ta mika mata, yarinyar ta karba da sauri ta boye.
A lokacin ne malamin ya hango Aminatu tana kallon allon da yake koya musu darasin, kusan wannan shi ne karo na barkatai da yake arba da yara na shigowa makarantar talla, wani lokacin har cikin ajijuwa suke zagayawa idan sun ga babu malamai a ciki.
Sai dai tsayawa a nasu ana daukar darasin karatu babu kamar Aminatu domin ko daliban makaranta basa nuna mata natsuwa da maida hankali sai dai su nuna mata iya rubutu da kuma fahimtar darasin yadda ya kamata domin su a kullum suna aji ne, ita kuma sai idan talla ta biyo da ita.

"Mtcheesss idan ba makarantun kauye ba ina ake wannan abun? Ace makaranta a bude har masu talla suna shigowa, ko wane aji babu ganbu (Kaure) balle har ma ace an zagaye mana makarantar"

Malamin ya fada cike da jin zafin yadda aka wofintar da abun da ya shafi ilmin boko a yanki.
Aminatu na jin haka sai ta duke kasa gabanta na faduwa, daman can yarinya ce mai gujewa fitina da tsoron bacin ran mutane. Dukuduku tai ta fice daga gurin

cikin sanda ta koma can bakin kofar makarantar inda suke zama ita da sauran masu talla suna jiran a tashi yan makaranta fito siye siye.
Rayuwar Aminatu rayuwa ce da ta ginu da ilimin addinin da kuma talla, domin bayan noma da mahaifinta yake yi wanda shi ne mafi akasarin mutanen garin galadi suke yi, babu wani abu da aka doraga da shi a gidansu kamar tallar da take, da rana zata kai gidɗa makarantar boko, dare kuma ayi mata tuwo, da safe kuma ta fita tallar koko, hakan yasa rabin rayuwarta ta kare a talla. Sai dai ko kadan bata da matsalar rayuwa ta ko'ina domin ita kadai ce mace da mahaifiyarta ta haifa bayan zaratan maza bakwai. Rayuwarta kusan haka rabin rayuwar yan matan garin take ba kowa ya ke damuwa da karatun boko kamar yadda suke damuwa da talla ba, domin talla tana ba su komai cikin har da kayan dakin da ake yi ma yan mata.
Garin Galadi wani yanki ne dake cikin karamar hukumar mulki ta shimkafi, gari ne mai cike da albarka manoma, kusan idan ka ambashi shimkafi kowa ya san gari ne na manoma garin mai cike da albarka da kuma mutanen kwarai.
Karamar hukumar Shinkafi tana cikin jihar Zamfara, shiyyar arewa maso yammacin Najeriya. Hedikwatar karamar hukumar tana cikin garin Shinkafi kuma karamar hukumar na da iyaka da karamar hukumar Zurmi Maradun da wasu sassan jihar Sokoto da jamhuriyar Nijar.

Garuruwa da kauyukan da suka kunshi karamar hukumar Shinkafi sun hada da Miyasa, Shinkafi, Bwane, Tunga, Fidani, Tubali, da Faru. An kiyasta yawan al’ummar karamar hukumar Shinkafi ya kai 177,811 mazauna yankin da ‘yan kabilar Hausa da Fulani suka mamaye. Yaren Hausa dai ana magana ne da shi a karamar hukumar, addini Musulunci shi ne addininsu.
Karamar hukumar Shinkafi tana da fadin kasa kilomita murabba'i 674 kuma tana da matsakaicin zafin na digiri 34. Karamar hukumar tana da kogin Tafin Kaiwa da ke ratsa cikin yankinta yayin da matsakaicin saurin iska a yankin ya kai kilomita 11/h. Noma wani babban aiki ne na tattalin arziki da al’ummar karamar hukumar Shinkafi ke aiwatarwa.
Sauran muhimman ayyukan tattalin arziki da al'ummar karamar hukumar Shinkafi suka gudanar sun hada da farauta, kasuwanci, kiwon dabbobi, da ayyukan fata.

*** *** ***

Tana zaune a gurin har aka tashi yan makarantar masu siyen gid'ar suka siya, wanda tai saura sai ta dauki farantin ta dora akai ta nufi gida tare da kawar tafiyarta Rumaisa, suna tafe tana kirga kudin gidarta har suka kawo mararabar hanya (Hanyar da ta kasu hudu) a nan sukai sallama kowa ce ta nufi gidansu. Da sallama ta shiga gidan kamar yadda ta saba.

"Wa'alaikissalam yar Inna yar Albarka"

Inna ta fada tana juyowa ta kalleta fuskarta dauke da murmushi. Sanusi ya wara ido ya zubar da ruwan daya wanke tufafinsa.

"Mu da ba yan Inna ba a nuna mana bolar mu"

Aminatu ta kyalkyale da dariya kamar ba ita ba, tai saurin aje farantin dake kanta ta mikawa Inna kudin hannunta sannan ta karbi dawon (Fura) da Inna take da inna take kirbi (Daka) ta cigaba da yi tana fada mata ko nawa aka samu yau.

"Aminatu Auta, himma dai yar Audu"

Sanusi ya sake fada da fuskar zolaya, daman can indai yana gida ya fi kowa zolayarta kamar wata abokiyar wasarshi.

"Na ji dai ai ina aiki dai ni ba kamar sauran auta ba ne, kai da baka iya noma fa sai sana'ar tireda"

Ta masa gwalo. Sai Inna ta saka dariya.

"Fada masa dai yar auta gogar aiki, shi baya iya aikin karfi irin na maza sai sana'ar zama"

Aminatu ta wani yi warrr da ido tana jin kirarin da Inna tai mata har cikin ranta, ganin hakan yasa Sanusi sake tsokanarta.

"Eyee su igeee anji dadi, Igengen..."

Take ta turo baki gaba.

"Inna kin ga yana ce min Ige ko?"

"To maza nawa aka haifa kamin a haife ki? Kin zama Ige ai"

Aminatu ta kalli Inna da kwababbiyar fuskarta kamar zata fashe da kuka.

"Inna kina jinsa ko?"

"Dan Allah Sanusi ka gama ka fita ka bar mana gidanmu, ya zaka takurawa Auta"

Inna ta fada. Sai Aminatu ta gyada kai

"Atooo"

Dariya yai ya debi ruwa a babbar buta ya zagaya bandakin da ya kasance na kasa kuma iya tsawon habar mutum, (shoulder) domin idan ka mike tsaye gaba daya, za a iya hangoka.
Kamin ya gama wanka Aminatu ta gama kirba dawon har ta kwashe ta zuba wani, Auta ce amman ba kamar sauran ba, domin bata da ƙwiyar aiki, ita dai bar ta da shagwaba da yawan kuka idan an taba ba.

"Baka ma wanku ba tsami kake yi"

Ta fada tana yatsina fuska kamar gaske. Dariya yai ya shiga karamin dakin dake kusa da na Inna ya shirya cikin wata karamar shadda ta marasa karfi da ta gama shan jiki ya saka hullarsa taɓani ka ji Hadisi, sannan ya fito yana ta kwanbo da talkaminsa na roba.

"Wallahi ba kai kyau ba"

Cewar Aminatu tana dariya, sai Inna ta taya ta.

"Lallai kam kyau ai sai Auta hanci har baka (Baki) sai dai a gwada mata haske shi ma kadan"

"Inna Wallahi ki daina biyewa wannan yarinyar, idan ma ta samu miji irina ta more..."

Har Aminatu ta bude baki tai magana sai kuma tai shiru ta maida dubanta gurin yayanta Amadu, wanda take tsoro kamar mutuwarta domin idan yana a cikin gidan bata da sukuni ko wani motsin kirki bata yi. Na tsantsiyar yarinya ce, sai dai shigowar Amadu ya saka ta kara natsuwa ta yi tsit a gurin kamar babu ita. Amadu irin mazan nan ne da basa wasa da yara balle kuma ita da take kanwarsa ta biyar.
Wani tsohon babur dinsa Honda ya turo ya karaso inda suke, Inna na nashe dawon a tukunya, Aminatu kuma na zaune gaban turmin idonta kasa.

Inna ta daga kai ta kalleshi yana kokarin jingine babur din ta ce.

“Ka dawo?”

“Eh ya gidan?”

“Lafiya Kalau, ya kasuwa”

Ya dan yi jimm cike da damuwa sannan ya sauke ajiyar zuciya.

“Kasuwa da godiya Inna, amman abubuwan kasar nan sai hamdala, komai kara masa kudi ake, idan baka da wani babban jari yanzu sai kasuwancin ma ya gagareka”

“To ya za'ayi kasar ce ta zama abun da ta zama, Allah ya ba mu azzaluman shugaban ni, ba su da tausayi kansu kawai suka sani”

Cewar Sanisu yana nufo inda suke, Sai Amadu ya amsa masa.

“Wallahi ga rayuwar mutane an maida ta kamar ta dabba, kai har kara ma dabba a yanzu, kuma sun kasa daukar mataki basa ma son ana ji, Nigeria kam ban san yaushe zata gyaru ba”

“Allah ya kyauta, ni dai na wuce shago”

Sanusi ya sake fada, sai Inna ta bishi da addu'a.

“To Allah ya tsare ya bada sa'a”

Har ya fice Aminatu bata dago kanta ba, ko da wasa bata son ta hada ido da Amadu, ba ganinsa kadai ba ko muryarsa ta ji sai ta ji gabanta ya fadi.

“Inna Ina Lami kike neshen dawo da kanki? (Saka fura a tukunya)”

Amadu ya tambaya.

“Kai ma ai kasan bata nan, da tana nan ai ba zata bar ni nai wannan aikin ba, ta je ganin dan Kuidu (Kaciya)”

Ya shaf kansa.

“Na manta ta fada min, abubuwan ne sun yi yawa Wallahi”

Ya fada yana nufar bangaren da Iyalinsa suke. Domin irin katon gidan nan ne na kauye mai fili wanda yaya suke dibar bangare suna kafa na su iyalin, bayan shi da yake da mata daya, Musa mai mata biyu ma a gidan yake zaune, sai dai shi ya fitar da kofar gidansa ta can baya sai an zagaya za a iya shiga, Iro da Sanusi ma da ke shirin aure a cikin gidan suka gina gurin da za su aje matansu.

TALBA POV.

Yana zaune a dining din har Momy da Baaba suka gama hada abun karyawa. A hankali ya dago yana kallon yadda Baaba take jera kulolin, hannunsa suke da wayarsa. A hankali ya lumshe idonsa ya bude, cike da kasaita ya motsa bakinsa, yana maida dubansa gurin Momy wanda taja kujera ta zauna.

“Baaba a fadawa yaran nan su fito su karya”

Matar da aka kira da Baaba ta dan risinawa Momy cike da ladabi.

“To ranki ya dade”

Ya nufi upstairs da sauri, da ido Talba ta bita kamin ya maida dubansa gurin KB da ya fito a daya daga cikin kokafin da suke can dayan bangaren falon.

“Momy ina kwana”

KB ya fada yana kokarin jan dayar kujera ya zauna, sai Momy ta amsa masa ba yabo ba fallasa, sannan ya mikawa Talba hannu suka gaisa, ya shiga hadawa kansa tea. A tare Amal da Leila suka sauko downstairs din, kai tsaye suka nufu dinning area, Amal da far'arta kamar kullum, Leila kam sai wani sham kamshi take musamman da ta hango Talba a zaune a dinning din.
 Amal ce ta riga isa ta zauna tana fadin.

“Ya Talba Morning”

Ya kai dubansa gareta yana sakar mata murmushi as respond, irin murmushin nan da be saba zama a fuskarsa ba. Bayan ta gaishe shi ta gaishe da KB.

“Ya KB Morning”

“Morning Amal”

Ya amsa yana kai plantain a bakinsa. Leila na zaunawa Talba ya mike tsaye cike da izza, sai duk suka kalleshi.

“Ah ah ba karyawa za kai ba?”

Momy ta tambaya.

“Zan yi breakfast a waje”

Ya amsa kamar an amsa dole, already yayi nisa da dinning din. Sai da ya fice daga falon gaba daya sannan Momy ta kalli Leila.

“Kun sake yin fada ne?”

Leila ta kalleta cike da damuwa.

“Momy miyasa kullum ni ce mai laifi?”

Momy ta zare mata ido.

“Yes tun da ya dawo sallah asuba yake zaune a nan, idan har babu komai to babu abun da zai saka ya zauna tun 6:30 har 9:30 dan kawai kin zauna kuma ya tashi ya ce ya zai karya a waje, zan kaiwa Daddynku abinci yanzu, ki same ni daki anjima”

Momy na fadar hakan ta mike tsaye ta dauki wasu tsadaddun kuloli ta nufi kofar da zata sadata da bangaren Daddy.

“Ni ma ba zan karya ba”

Amal ta fada tana turo baki alamar ranta ya bace sai harara take watsawa Leila kamar ba yayarta ba, sannan ta mike tsaye ta fice daga gurin ta nufi upstairs.

“Munafuka, ai daman tun da Yayanki be ci ba ba zaki ci ba Mtschesss”

Cewar Leila tana binta da harara. KB ya bi Amal da kallo har ta shiga dakinta sannan ya kalli Leila.

“Da gaske fada kuka yi kenan?”

“Ai dole mu sake fada kuma mu yi ta fada, na gaji da halin Talba, na gaji, shi ba dan sarauta ba, ko yan sarauta ba su abun da yake, ba baiwarsa ba ce ni, and i hate nonsense”

Mikewa tai tsaye a fusace har tana jefa da empty cup din dake gabanta, a take ya fadi kasa ya fashe, kamar zata tashi sama haka ta nufi upstairs. KB ya wara ido.

“To ni ina ruwana, can ta matse muku, a takaice dai ni kadai zan karya a yau... Fine”

Ya sake bude wata kular ya shiga zubawa kansa ferfesu.

FARUQ POV.

Ya aje kofin garin dake hannunsa yana kallon dansa.

“Ka koshi ko?”

Sultan ya daga masa kai yana murmushi kamar yadda shi ma yake masa murmushin. Faruq ya dauke shi ya dora saman kafafuwanta sannan ya kalli Mahaifiyarsa cike da damuwa.

“Mama bari mu tafi kar dare yai mana”

“Kara ka tafi da wuri kam tun da a kafa zaka je”

Ya mike tsaye.

“To sai da safe ayi ta mana addu'a dai”

“Addu'a ai dole ce Faruq, Allah ya tsare, Sultan sai da safe ko?”

“Sai da safe Mama”

Sultan din ya fada da muryarsa da be gama kwarewa da iya magana ba. Daukarsa Faruq yai ya fice daga gidan, a kafa ya taka tun daga unguwar dallatu har Gadar Baga, ganin Sultan ya fara bachi sai ya dora shi a kafada Faruq, yana tafe gabansa na faduwa har ya iso gidansa. Sai da ya saka hannunsa aljihu ya lalaba garin kwakin dake cikin aljihun wandonsa da sugar ya tabbatar suna nan sannan ya kwankwasa kofar gidan. Yayi kusan rabin awa a tsaye sannan Rafi'a ta bude masa. Ganin babu komai a hamnunsa yasa ta ja tsaki.

“Mtcheesss”

Be ce mata komai ba ya saka kafarsa ya shigo cikin madaidacin gidan na zaman mutum daya, sannan ya maida kofar gidan ya rufe. Da sallama ya shiga cikin falon amman ta ki amsa masa sai latsar wayarta take kamar bata san da shigowarsa ba. Be damu ba domin in da sabo ya saba da halin matarsa. Dakinsu ya shiga ya kwantar da Sultan sannan ya dawo falo ya zauna kusa da ita, kana ya ciro garin da ba zai wuce gwangwani daya da rabi ba da surga ya mika mata.

“Ga dan abun da muka samu”

Daga shi har garin kallon uku saura kwata ta watsa masa.

“Gari fa nake gani Faruq?”

“Shi ne”

Ya amsa mata kamar wani yaronta.

“So kake jinina ya tsotse ne? Kara min jinin ma ya gagara? Haba Faruq, na wuni ban ci komai ba kuma yanzu ka shigo min da gari?”

Ta masa maganar kamar zata fashe da kuka, ya sauke ajiyar zuciya a hankali.

“Haba Rafi'a tun da kika ga na shigo miki da gari ai kin san ban samu komai ba ne, shagon na mu sabuwar unguwa ce ba a samun ciniki sosai, tun da na fita har babu wanda ya zo aski, wannan garin ma sai da na biya ta gida Mama ta siyo min aka jikawa Sultan ya sha sauran ne na kawo miki, Wallahi ni tun karin safe da na yi ban sake cin komai ba, kara ke na bar miki gwangwani biyu na wake...”

Be marasa ta mike tsaye tana masa ihu.

“Kai ka so Faruq kai kaso zama da talauci, sa'aninka suna can sun gina manyan gidaje wasu na da manyan motoci, su ci mai kyau su saka mai kyau, amman kai dube ka? Suturar kwarai ma ta gagareka, ni kaina da nake matarka ina kunyar a tararda ni a gidan nan, gida duk ya lalace, da an yi magana kace komai zai wuce sai yaushe zai wuce? Shekara biyar fa da aurenmu Faruq, ka dube ni ka gani tsabar kyau Baturiya ake ce min fa! Amman na kare a aurenka, auren kaddara auren cin garin kwaki, dan sunan mai dadi ma baka iya kirana da shi ba, Rafi'a Rafi'a, Fee'ah Fee'ah haka ake kirana ba Rafi'a ba”

Ta nufi dakinta a fusace, shi kuma ya lumshe idonsa yana jin zafin maganar da ta fada masa. Yana zaune a falon har 11pm na dare sannan ya tashi ya rufe kofar falon ya kashe wutar ya shiga dakin ya shiga bathroom yai fitsari ya wanke kafafunwasa da fuskarsa sannan ya dawo dakin ya kwanta bayanta, can kuma ya tashi zaune yai ma dansa addu'a sannan ya kashe wutar dakin, ya dawo bakin gadon inda ya saba kwanciya yai tasa addu'ar, ya ciro wayarsa ya aje a gefensa ya kwanta, a hankali ya kai hannunsa ya fara shafata sai ta buge masa hannun ta tashi zaune.

“Miye haka? Ka dawo min da garin dan jinina ya tsotse, kuma yanzu ka zo min na maka me? Da safe kuma dan ka ya dame ni da kayan fitsari tun da an gagara sai masa pampas, ga wannan tsinannen cikin wahala da yake jini, haba duk ni kadai? Wai kai baka da imani ne?”

“Rafi'a wai miyasa bakinki ba shi da linzami ne?”

Ya fada a fusace yana kokarin danne fushinsa.

“Shi bakin nawa ai haila yake, kai kudi ka gani idan zan maka duk wannan, su masu kudi ka ga matansu na musu haka ne? Saboda sun ba su komai gurin kwanciya ma dakin yara daban ake amman kai ka hade ni daki daya da yaronka, anjima kace min na taso muje falo ko? To ba zan je ba”

Sauka yai daga saman gadon gaba daya ya fice daga dakin, be tsaya a falo ba tsakar gidan ya fita gaba daya ya zauna saman turmi ya daga kansa sama.

“Kun faya kun sai kai Allah”

Ya fada yana kallon yadda taurari suka kawata samaniya.
Rafi'a na jin ya fitarsa tai azamar dauko wayarta touching, ta dauki keypad dinsa ta shiga contact list tana neman wata number.
MD Saleh a dai dai gurin ta tsaya ta bude sunan ta kwashe numbers din sannan ta maida wayar ta aje, sai tai saving number da Maryam Dahiru Sokoto, kana ta saka wayarta a silent ta kwanta.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata.
Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers please, idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -2□

“Akwai abubuwa da yawa da rayuwa bata iya tafiya sai da su, a ciki akwai numfashi ci da sha, da kuma soyayya. Bana jin zan iya rayuwa idan babu kai a kusa ni, zan iya rasa ci da sha kuma na rayu da soyayyarka”

Ta nade wasikar da ta gama rubutawa da hausar azami, tana murmushi sannan ta mike tsaye ta maida biron da littafin cikin jakarta ta islamiya ta rataya a jikin kusar dake gurin sannan ta saka hijabinta ta fito.

“Inna an gama?”

“Auta tun dazun na gama, kin yi sallah dai ko?”

Ta saka wasikar a cikin jikinta tana murmushi.

“Inna ke ma kin san bana wasa da sallah fa”

“Haka ne, Auta Allah ya miki albarka”

Inna ta fada Baba da ke zaune saman tarbarma yana sauraren redio ya amsa da Ameen yana murmushi. Sanusi ma dake aikin auna tuwon dawo a bakinsa ya so ma zolayarta kamar yadda ya saba.

“Ku na fasa mata kai da wannan kafafuwan nata kamar itace”

Aiko kamar jira take sai ta fara kukan shagwaba, musamman ganin duka gatanta suna nan Inna da Baba.

“Baba kana jinsa ko?”

Baba yayi dariya tare da kai hannunsa ya kashe redio dake gefensa, ya tofar da goron bakinsa. Yai mata alama da ta zo da hannu, kamar jira take sai ta karaso inda yake tana ta turo baki ita ala dole an taba ta.

“Auta Mamana, ki daina biyewa Sanusi, shi da yake ragon maza, ke da kike Jaruma, ki daina nuna musu rauninki, kin ga shi kin ga Rilwanu ki daina bari suna saka ki kuka, da an miki aure sai kun yi ta marmarinki”

Ta rufe ido da sauri cike da tsantsan kunyar irin ta ya mace bahaushiya. Hakan da tai sai ya kara saka Baba murmushi.

“Allah ya miki albarka ya nuna mana lokacin Autata”

Kasa amsawa tai da ameen domin Aminatu irin yan matan nan ne masu kunya da kawarda ido ga wasu abubuwan. Sai kawai ta mike tsaye har lokacin bata janye hannunta daga fuskarta.

“Wai kunya take, kunya kike kika yarda kina fita zance”

Sanusi ya fada yana dariya, a cikin hasken farin watan Aminatu ta watsa masa harara. Ta nufi inda kwallar tuwonta take ta nada ganwo ta dauka ta dora a kai sannan ta mika dayan hannunta ta dauki miyar dake cikin bokitin roba.

“Ni na tafi gurin sana'a ta”

Ta fada tana kara murda masa baki, Inna dai bata ce komai ba bayan murmushin da tai. Har ta kai bakin kofar fita daga gidan sai Baba ya kirata.

“Mamana”

Ta juyo.

“Na'am Babana”

“Allah ya miki albarka”

Sai ta amsa tana kallon gefen Sanusi.

“Ameen, yan bakinciki sai dai su mutu”

Ba Inna da Baba da Sanusi kadai ba, har Rilwanu da Iro da suka shigo yanzu sai da suka saka dariya, domin sun san tatsuniyar gizo bata wuce ta koki, inda Aminatu ta yi habaici ko shagube to ba zai wuce Sanisu ko Rilwanu ba take yi ma.

“Mai tuwo a bani na hansin”

Ko kallon Rilwanu ba tai ba ta saka kai ta fice tana cinno baki gaba kamar zai zazzago ya zubo kasa. Kusa da Baba suka zauna ko wane ya aje bindigar maharba da manyan wukaken dake hannunsu. Kana ganinsu ka ga zaratan jarumai, tun daga kirarsu har yanayin shigarsu da muryarsu. Domin suna daya daga cikin manyan yan saka na yanki, abu ne mai wahala ka ga gidan da ke da maza uku ko hudu baka samu yan sakai a gidan ba balle kuma gidansu Aminatu da suke da maza bakwai. Ba wuka ba ko bindiga bata huda mahaifinsu balle kuma su da suke shiga dajijikan kauyen neman barayi da kansu.

Tana yin nesa da gida kadan sai murmushi ya wanke mata fuska, a cikin abubuwan da tafi kaunar a rayuwarta akwai yan'uwanta, musamman Rilwanu

Sanusi da Musa, domin sun fi sauran sake mata, da kuma kyautata. Gashi basa yarda ko da wasa wani ya nuna mata yatsa a waje balle har a taba ta.
A natse take tafiya, tana ta mikawa mutanen data sani kuma suka santa gaisuwa cikin girmamawa, musamman abokan mahaifinta, sai da ta kusa dandali sannan ta rage saurin tafiyarta da alama akwai wanda take jira ko take son hangowa, can kuma ta ja ta tsaya ta juyo tana kallon hanyar data fito sai ta hango masoyinta tafe da saurinsa cikin shigar kananan kaya, murmushi ne ya cika fuskarta, sai ta sauke idonta kasa domin bata jin kunyarta zata barta tai ta kallonsa har ya karaso inda take.
Sai da yai wani gyaran murya ya waiga ya ga babu mai ganinsu sannan ya ce.

“Auta”

“Na'am barka da dare”

“Yau ina fitilarta?”

Sai da yai maganar ta tuna da zancen wata fitila, sam ta manta bata zo da ita ba, sai a yanzu ta suna ta bar fitilar a dakin Inna bayan ta gama rubuta wasikar.

“Wallahi na manta ta”

Ta fada tana dukawa ta aje bokitin miyar dake hannunta, sannan ta saka hannu a cikin zanenta ta dauko wasikar ta mika masa, ya karba da dayan hannunsa dayan hannun kuma ya mika mata tasa wasikar.

“Na je gida na karbo miki?”

Ta zaro ido.

“Kai Baba yana nan fa, ni ban saba aikin maza a gidanmu ba”

Yayi yar dariya yana kokarin magana suka ji muryar Sanusi.

“Auta...”

Ba karamin tsoro Aminatu ta ji ba, domin bata saba tsayuwa da maza har a ganta ba, duk kuwa da kasancewar ta kai munzalin da zata iya yin hakan, amman kunya da tsoron yayyunta ya hana ta yin haka, duk inda ta san idan ta tsaya da wani za a gani ayi mata magana ko fada bata yarda ta tsaya a gurin. Maniru ne ya soma wayancewa ya mikawa Sanusi hannu suka gaisa, Sanusi ya amsa yana musu dariya.

“Ka ce na zama yaya daga yanzu”

Maniru yayi dariya Aminatu kuma ta duka da sauri ta dauki bokitin miyarta daman tuwon yana saman kanta.

“Ga fitilar in ji Inna”

Ya mika mata yar karamar touch light din dake hannunsa, sai ta karba da sauri ta juya ta cigaba da tafiya cike da tsananin kunya gabanta sai faduwa yake. Sai da tai nisa sannan Sanusi ya kalli Maniru ya ce.

“Maniru idan kana son Aminatu ai gidansu ya kamata ka ta fi ba wai ka rika tare ta a hanya ba, amman irin wannan ai ba lallai ne kowa yai maka fahimta mai kyau ba”

“Wallahi Sanusi ina son zuwa, ita take hana ni, sai tace tana jin kunya kuma yayyunta za su iya mata fada”

Sanusi yayi dariya.

“Shirmen ta ne, ba a aure mu za mu yi, idan ka shirya kawai ka min magana zan sanar da Baba sai a komai cikin mutunci”

“Maa Shaa Allah, na gode sosai daman ni abun da nake nema kenan domin na gaji da zageye zageyen nan Wallahi”

“Inshallahu zan yi magana da Baba, duk yadda ake ciki zaka ji”

Sai da Maniru ya sake mika masa hannu suka gaisa sannan ya wuce yana ta jindadi abun nema ya samu.
Aminatu na daya daga cikin irin yan matan nan da suke da farin jinin siyarda sana'a musamman a dandali duk kuwa da kasancewar ba wani kula samari take ba, amman abu ne mai wahala ta je da tuwo ta dawo da shi sai ta saida kaf wani lokacin ma har ta karbi na wasu ta siyar musu, saboda tsabtarta da kuma dadin miyar Inna. Har ta gama sai da tuwon ta nade komai nata a guri daya Wasikar da Maniru ya bata tana cikin jikinta, a dayan bangaren kuma tana ta tunanin yadda zata shiga gida, domin ta san abu ne mai wahala ace Yayanta Sanusi be fada cewar ya ganta da Maniru ba, ba fada kadai ba wata kila har doka sai ta sha a gurin Yayanta Amadu. Da gangan ta ki yarda ta je gida da wuri duk kuwa da kasancewar ta siyar da tuwonta a cikin lokaci, sai ta zauna a gurin tana ta kallon mutane fuska ba yabo ba fallasa, ba zaka iya karantar damuwarta ba, sai dai hakan kuma be isa ka fadi cewar tana cikin farinciki ba.
Har kusan 11 na dare bata tafi gida ba tana zaune a gurin sai ta fakaici idon mutane sai ta matse yan kwalla da suke cika mata ido, sai kuma ta dan turo baki, sai kallon mutanen dandalin take sai ka rasa wa take turowa bakin. Ganin babu sarki sai Allah yasa ta mike tsaye ta dauki robar ta dora a kai tai ma abokan sana'arta sallama, ta fara tafiya kamar bata son zuwa, ta san inda bata je ba sai an aiko nemanta kamar yadda ake idan ta dade bata dawo ba, dan haka bata da wata mafita data wuce ta koma gida.

TALBA POV.

Yana shakimce cikin mota har Ali ya iso gurin motar ya bude front seat ya shiga ya zauna yana kallon abokin nasa

“Lafiya dai?”

Talba yaja wani dogon numfashi ya sauke sai huci yake, har ya bude baki zai yi magana sai kuma ya shiru ya maida dubansa wani gurin. Ali na ganin hakan yai dan murmushi.

“Leila ta tabo ka kenan?”

Talba ya kalleshi da idanuwan dake nuna bacin ransa karara kamar yadda fuskarsa ma ta kasa boye bacin ransa.

“Wai yarinyar nan ni zata wulakanta?”

Magana yake kamar wuta na fita a bakinsa. Ali ya masa kallon natsuwa.

“In I'm not mistaken ka sake mata maganar auren kenan?”

Shirun da Talba yai ne ya tabbatarwa da Ali eh ce amsar tambayar.

“Amman ta wace siga kai mata maganar?”

Talba ya watsa masa wani banzan kallo.

“Kamar wani karamin yaro zaka tambaye ni wace Siga nai mata maganar?”

“No baka gane ba ne Talba, su fa mata yan lalabawa ne, kai kuma sai kace komai da karfi da isa zaka yi ba haka ake ba”

Talba ya watsa masa wani kallo.

“Okay kamar ba baka san ni ba kenan? So kake na je na same ta ina lallashinta ta aure ni?”

“No kai baka gane ba, Talba wannan lokacin ya wuce da zaka dinga tirsasa mace ta yi maka abu any how, na san Leila tana sonka amman kai din ne wani iri”

“Kai Ali duk fa mace da zan aura alfarma zan mata, ba dai ita ta min ba, ina da kudi ina da kyau ina da ilmi ina da addinin da har a kasar waje za a iya bani aure balle a nigeria a nigeria ma a gidanmu”

“Ka ga matsalar ka ba, wani irin alfarma tun da har kuna son junanku? Kar fa ka manta Talba Leila a waje tai karatu kuma wayayyiyar mace ce mai son burgewa, Talba dan kalaman nan na soyayya baka san kai mata ba, dan morning text din baka tura mata, balle har ka kirata ku yi fira, ko ka dauke ta ku fita, mata suna son wannan”

“Ba zan yi ba, ina namiji zan wani zan wani rika lallaba mace, idan ma zan mata sai an yi aure, amman ba a yanzu ba ai sai ta raina ni, besides muna gida daya zan rika mata haka?”

“To miye a ciki, ai an san aurenta zaka yi tun da an muku baiko, kai komai sai kace na zafi zaka yi, idan ka sake mata ba shi yake nufin ka bata umarni ta ki bi ba, dan Allah ka kirata yanzu ka bata hakuri”

Kamar wanda aka cewa cire ranka ka bata haka Talba yai ma Ali wani irin kallo na mamaki da tsoro a lokaci daya.

“Ni Mu'azzam Auwal Shimkafi zan kira mace na ce dan Allah ki yi hakuri? Macen da ba uwata ba? Malam dan Allah fitar min a mota”

“Talba mata fa sai da haka, kuma ka canja hali dan Allah”

“Ita ma ai bata iya kalaman soyayya ba, bata san ta kira ni ta gaishe ni ba ko ta turon sakon soyayya, kai ni bana jin ma akwai ranar da Leila ta taba kallona tace kana da kyau simple word bata taba fada min ba, sai ni zan fada mata? Ba yi wannan macen da zan zauna ina bude mata sirrin zuciyata ba har ina rarrashinta”

“Wannan ji da kan babu inda zai kaika Talba, idan ka sake mata ka nuna mata kauna dole ita ma zata sauko fa”

“Malam na ce ka fitar min a mota...!”

Yanayin yadda yai maganar ya isa ya sanar masa ba da wasa yake ba, kuma ya san halin abokinsa idan ransa ya bace baya jin rarrashin sai dai hakan ba zai hana anjima ya kira shi yace yana son wani abu ba ko kuma su gadu a guri kaza. Salun alum ya bude motar ya fita yana murmushi da mamakin irin halin Talba.

“Ina fada maka matsalata kana wani kokarin ba ni laifi, an fada maka mata haka ake musu ne!”

Magana yake da kansa yana tukin cikin bacin rai, domin be san inda zai je ba a yanzu kasancewar yau weekend kuma gashi safiya ce be ma karya ba.

@12:44pm

Leila na zaune tool din mirror Momy tana zana mata abun da ya faru.

“Kawai sakonsa na gani a wayata wai na fito waje yana son magana da ni, Momy babu ko irin shaukin nan Wai Ke fito waje ina son magana da ke, haka dai na daure na fita, na same shi a balcony ya kusan 30 be ce min komai ba, sannan wai ki yi fixing date na auren mu, Imaging babu ko dan shauki sai wani ji da kai”

“Ke kuma kika ce masa me?”

Momy ta tambaya tana hararta.

“Na ce nasa ba zan yi ba, ni ban tashi aure yanzu ba”

“Ki ba shi hakuri”

Ta kalli Momy kamar tai magana sai dai ganin babu wasa a fuskar Momy yasa ta mike tsaye ba tare da tace komai ba ta fice daga dakin cike da bacin rai. Dakinta ta shiga ta dauki key din motarta da jakarta da wayarta, ta fito babu mayafi ta sauko kasa kamar zata tashi sama, daman ta saba fita babu mayafi abu ne mai wahala ka ganta da mayafi a jiki komai kankantarsa.
Tana fitowa ta nufi gurin da motarta take ta bude ta shiga tai yi warming dinta sannan ta danna horn da karfi mai gadin na ganin hakan yai saurin bude mata gate. Kamar wata mai gasar tsere haka ta fito daga cikin gidan da mugun gudu ta hau titi tana jin kamar ta fasa ihu. Sai da tai nisa sannan ta dauki wayarta ta kira Adam.

“Besty kana ina?”

“Ina gida ya akai? Kamar kina cikin damuwa”

“Ina ciki besty mun yi fada da Talba?”

“Mtssss wai me ke damun Talba ne?”

“Ina na sani, ban san abun da yake takama da shi ba, indai kudi ne ni ma ina da su, ilmin ina da shi kyau ba za a min gori ba, amman sai wani nuna isa da ji da kai”

“Wallahi kam yan kalaman soyayya ma ace ba zaka iya yi ma mace ba, idan an yi auren ya kenan?”

“Shine abun da nake magana a kai, ni kuma sai na nuna masa ina da tsada ni ba kamar sauran mata ba ne, dole na ja masa aji, yadda yake jin ba zai iya min kalaman soyayya ba ko ya dauke ni mu fita ko ba ni hakuri haka ni ma ba zan taba yi masa ba”

“Hakan shi ne daidai, kara ya san darajarki a dole ya sauko idan yana sonki”

“Shine ai, shi kawai abunda ya dauki mace ya mata umarni ta bi ya juyata yadda yake so, ni kuma sai na nuna masa na fi karfin haka Wallahi”

“Yanzu dai kwantar da hankalinki ki samu ruwa ki sha, ki fita waje ki sha iska zan zo na dauke ki mu fita”

“Har na ma fito gida amman bari na koma”

“Okay but ki yi murmushi pls”

Ta yi murmushin mai sauti kamar yadda ya bukata, sannan ta aje wayar, ta juya ta koma inda ta fito. Kamar yadda ta fito haka ta koma gidan da gudunta ba da damuwa da titi ko sauran motoci burinta dai ta aikawatar da abun da take so. Horn biyu tai kamin tai na uku Mai gadin ya bude mata gate ta shiga cikin gidan da mugun gudu ta faka motar a inda ranta ya so ta fito ta nufi kofar falon, door bell ta danna da karfi kamar zata balla shi sannan taja ta tsaya tana tsaki, shiru ba a bude ba har sai da ta sake danna door bell din sau biyu ta hada da knocking. Sannan Baaba ta bude mata.

“Wallahi tallahi kika sake barina a tsaye a waje ina knocking, abincin ki ya kare a gidan nan Baaba”

“Wanke wanke nake yi Leila shiyasa”

“Na dai fada miki”

Ta fada cikin tsawa, ba dan Baaba ta yi saurin kaucewa ba da Leila tureta zata yi ta wuce. Baaba ta maida kofar ta rufe sannan ta juyo cikin falon cikin rashin jindadi zata koma Kitchen din sai ta ji muryar Momy dake tsaye stairs.

“Baaba a rika kula mun dauke ku aiki ne kawai saboda mu huta, a daina batawa yarana rai”

Baaba ta daga kai ta kalli Momy sannan ta daga mata kai cikin da ladabi.

“To Hajiya Inshallahu za a kiyaye”

Sannan ta sadda kanta kasa ta nufi kitchen din cikin rashin kuzari.

FARUQ POV.

Kallonta ya tsaya yi da dayan biyu kamin ya amsa gaisuwar da tai masa, domin ba kasafai take gaishe shi da safe ba sai idan tana son wani abun ko kuma ta lura aljihunsa da dan nauyi.

“Lafiya Kalau an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah, sai yunwa da nake ta ji tun jiya”

“Toh Allah ya buda mana kofafin samu”

“Amin...”

Ta amsa tana kallon Sultan dake motsawa alamar zai farka daga bachin da yake.

“Na ce wai ba zaka kira abokin nan naka ba, ka roki shi dan wani abu?”

Ya girgiza mata alamar aa.

“Ba zan dauna kullum ina bin abokai ina rokonsu ba, bakin da Allah ya tsaga ba zai hana shi abun da zai ci ba, kuma ni ma na yi karatun idan mu kai hakuri komai zai wuce”

“Matsalar kenan Faruk girman kai, kana da girman kai, yanzu haka zamu zauna mu wuni da yunwa gashi idan ka fita baka dawowa sai dare? Ga ni da ciki ga Sultan?”

Yayi shiru yana jin yadda kansa yake sara masa saboda maganganun da Baturiya ta fara masa.

“Shiyasa na ce zubar da cikin nan zan yi na huta, kai ma ka huta domin na san ko ragon suna da wahala a samu a yanka masa wannan bakin talaucin da muke fama da shi”

Ta fada cikin kukanta na munafurci. Sai ya kalleta a raunane.

“Zubar da ciki ba zai kawo mana Mafita ba Rafi'a miyasa ba ki da tunani ne wai?”

“To ni dai gaskiya yunwa nake ji, tun jiya fa ban ci komai ba, kuma anjima na nan ga Sultan ma”

Wani dogon numfashi yaja ya sauke ya mike tsaye ya fice daga dakin cike da damuwa. Binsa tai da harara.

“Ni dai Wallahi na gaji da wannan bakar rayuwa, Allah kadai ya san yadda masu kudi suke ji, su kwanta a mai kyau a ci abun da ake so, ni ko na kare a nan duk kyau na”

Ta fada tana mikewa tsaye tare da bin bayansa, sai da ta tabbatar ya fita sannan ta dawo ta dauki wayarta ta shiga contact list dinta ta kamo number da tai saving jiya. Maryam Dahiru Sokoto ta aika mata kira, ringing tai har ta tsinke ba a daga ba ta sake kira nan ma ba a daga ba.

“Ka ji yan gayu sai ayi ta kira basa dagawa...”

Whatsapp dinta ta bude ta shiga gurin numbers ta kamo number wanda ke dauki da hoton wani matashin da ba zai wuce sa'an mijinta hakimce cikin mota. Sai da ta gama kallon hoton sannan ta shiga aika masa sako.

‘Assalamu Alaikum, ranka ya dade fatar an tashi lafiya, ya aiki ya Madam da yara. Ranka ya dade sunana Fee'ah matar Faruq abokinka, na kira baka daga ba shiyasa na yanke shawarar turo maka sako. Wallahi muna ciki matsala, yau kusan kwana nan mu hudu ba mu girka komai ba, shi ma idan ya fita haka yake dawowa saboda shagon da aka bude sabon gurin ne cikin wata sabuwar unguwa ba kowa yake ta aski ba, yanzu haka Sultan kuka yake, ni kaina dauriya kawai nai saboda da na, Dan Allah ka taimake mu kamar yadda Allah ya taimake ka, na duba na ga a cikin abokan Faruk babu mai tausayinsa da son taimaka masa irinka, na so Faruq yai maka magana da kansa amman yace nauyi yake ji, yanzu haka be san na dauki number ka ba, domin idan ya sani ina ciki matsala. Ka huta lafiya Allah kara rufa asiri’

A rarrabe ta tura sakon har tana gadawa da emoji din rokon da kuka. Sannan ta duba last seen dinsa tun jiya da dare, tana jin motsin turo kofar gidan tai saurin aje wayar ta kwanta kasa. Faruq ne ya shigo dakin rike da bakar leda har biyu a hannunsa. Ya aje mata dayar a gabanta ganin hakan yasa ta tashi zaune tana kallon 200 dari biyun da ya mika mata.

“Ina ka samo?”

“Ke dai ka bar”

“Dan girman Allah Faruq ka daina mana cin bashi kana kara mana kanskanci a unguwa kamar kan mu farau talauci”

“Ba bashi na ci ba wayata na bashi jingina”

Bata ce komai ba ta karbi dari biyu kana ta bude ledar tana duba taliya da makaroni dake ciki sai maggi da mangyada.

“To wannan ledar fa?”

“Mama zan kaiwa”

Yana fadar hakan ya juya ya kalli dansa dake sharar bachi sannan ya fice ba dan ranta ya so ba.

“Mu ba mu wadatu ba amman sai dauka ka kaiwa wasu, mtchhhh”

Ta karasa tana jan tsaki.

“Kuma Wallahi sai na zubar da cikin nan haka kawai zan zauna ga talauci ga wahala da kurciyata da kyauna”

Ta fada tana mikewa tsaye ta dauki ledar taliyar ta fito waje domin sarrafawa. Kallo daya zaka masa ka karanci damuwarsa abubuwan duniya sun taru sun masa turr kamar ya zagi arziki kamar komai yake juye masa, gashi yayi degree amman aiki ya gagara duk inda yai applying shiru ba wani motsi. Da tunani kala kala mai achaba ya sauke shi unguwar Dallatu wato gidan mahaifiyarsa, sai ta ciro naira dari a mika masa sannan ya ratsa cikin gidanje har ya isa kofar gidan ya tura ya shiga da sallamarsa. Kanensu biyu mata da suke tsakar gidan suka amsa masa suna masa sannu da zuwa, bayan ya amsa musu ya nufi dakin Mahaifiyarsa ba karamin faduwa gabansa yai ba ganinta a kwance domin ba al'adarta bace yawan kwanciya musamman a irin wannan lokacin.

“Mama lafiya dai? Ko jikin ne?”

“Da sauki ai Alhamdulillah”

Ta amsa masa tana murmushin karfin hali.

“Wani irin da sauki ga ki kwance? Kai Innalillahi Wa'inna illahirraji'un”

Jin furuncinsa yasa ta yunkura ta tashi zaune tana kallonsa.

“Ina Sultan?”

Kasa amsawa yai sai kallon mahaifiyarsa yake, yana jin kamar ace yana arzikin da zai iya kaita Asibiti, domin ba yau ciwon ya fara ba.

“Mama ko dai maganar auren Aisha da akai ne jiya ya tada miki hankali? Idan ma fasa aurenta zai yi ai ba wani abu ba ne zata samu wani”

“Har aure nawa za'ayi ta fashi ne Faruq? Haka zamu ta zama ana fashin aure saboda talauci? Kuma yaran nan sai girma suke, sai gulma ake mana a unguwa”

Ta tambaya idonta tab da hawaye, Faruq yayi saurin kawarda nasa idon yana sauke ajiyar zuciya, domin kukan mahaifiyarsa na daga cikin abun da ya fi tsana a rayuwarsa.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata.

Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers please, idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

https://www.wattpad.com/story/283871769?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_reading&wp_page=reading&wp_uname=KhadeejaCandy&wp_originator=ZCqcO2wXIv6pkkxIr3do4ng1%2BTHhzoVPTPFtpfDcb1ftHOVsldMflpG2lAwd5aYtrehJ12WEeerjWSVNDZunKAH9QpxhI0A%2BzJsYI6RrshbTOZsoLUXljeZDCPaDNtKr

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -3□

Shigowar Daddy ne yasa Momy ta cire farin gilashin idonta tana murmushi.

“Ranka ya dade an fito?”

Kusa da Amal ya zauna yana murmushi.

“Allah ya yarda”

Ya fada yana karewa katon falon kallo ganin Momy ce kawai sai Khadija da kuma Kabir, abun da ba kasafai yake gani ba, ya saba every weekend yana zuwa falon Momy ya zauna tare da ita da kuma yaransa, kowa ya fadi bukatarsa ayi hira a bawa juna shawara, ayi nishadi. Sometimes kuma shi zai kira su a bangarensa a tare a can.

“Daddy barka da wuni”

“Yauwa, Son”

Ya amsawa yana yi ma kowa kallon tsanaki, ciki har da yar autarsa Amal da ta wani hade rai.

“Hajiya ya ga falon ku kadai? Ina sauran yarana suke?”

Momy ta kalli Kabir dake kallonta sannan ta kalli Amal kamin tace komai Kabir ya tari numfashinta.

“Daddy yaranka biyu fushi suke da juna, kasan Angry Birds ne”

Daddy ya kalli Momy.

“Since when?”

Kabir zai sake magana Daddy ya dakatar da shi ta hanyar daga masa hannu, wanda hakan ke nuna kai tsaye Momy yake son ta amsa masa tambayarsa. Momy ta sauke ajiyar zuciya.

“Ni ma dazun nan na sani...”

A tsanake ta labarta masa abun da ya faru ciki har da fadan da tai ma Leila.

“Amman baki fada min ba? Taya zaki bar Mu'az ya fita ba tare da yayi breakfast ba? And baki dama ki san a wane hali yake ba?”

Momy ta lumshe ido ta bude tana murmushi.

“Wani lokacin kana maida Talba kamar wani karamin yaro, ya san yadda zai kula da kansa Alhaji”

“Ko da Mu'az zai shekara dari matukar ina raye to shi yaro ne a gurina, a shirya mana abincin rana tare”

“An gama ranka ya dade”

Ya mike tsaye sai Amal ta kalleshi.

“Daddy ni ma fa kaga ina fushin nan amman baka ce komai ba”

Sai a lokacin Daddy ya tuna da tana gefensa sai ya kalleta yana murmushi.

“Amal sorry wata taba ki?”

Ta nuna Kabir sai Kabir yai saurin daga hannayensa sama ya mike tsaye.

“Na ma bar muku falon”

Kamin Daddy yace komai ya nufi kofar fita daga falon da saurinsa yana murmushi.

“Mu yi masa uzuri amman yau kawai next idan ya sake tsokanarki zamu raba gari da shi”

Daddy ya fada yana kallon kyakkyawar yarsa. Sai ta sakar masa murmushi.

“Toh Daddy”

“Good”

Cewar Daddy yana ciro wayarsa ya kira Talba, ringing daya yai picking kamar daman can kiran yake jira.

“Hello Daddy”

“Mu'az kana Ina?”

Ya kalli katon office din da yake ciki kamar mai son tantance inda yake.

“Office Daddy”

“Me kake a office? Yau Weekend?”

“I don't know...Getting some fresh air”

“Baka fada min kana da damuwa ba, mu da kai ba abokai ba ne? Ba ma boyewa juna abu?”

Wani irin kasaitaccen murmushi ne ya bayyana a fuskarsa, ya mike tsaye daga inda yake zaune ya nufi windows.

“Daddy ba irin wannan ba you know dan crisis ne kadan”

Daddy ya tabe baki yana juya fuska kamar Talba na gabansa.

“Uhm.. Ka dawo gida yanzu zamu yi lunch tare”

“Okay Daddy Allah kara maka lafiya, i love you”

Daddy yayi murmushi ba tare da yace komai ba ya sauke wayar, sannan ya nufi wata kofa a dayan bangaren falon wanda zata sadashi da bangarensa.

“Ita Leila ba ya bace kenan? Da ba zaka kirata ka tambayi inda take ba?”

Daf da zai wuce Momy ta yi wannan maganar sai ya juyo ya kalleta, sannan ya dauke kai ya bude kofar ya fice.
Sai da ya rufe kofar sannan Momy ta tabe baki ta kai hannunta ta dauki wayarta ta kira Leila, sai da wayar ta kusa yankewa sannan Leila ta daga.

“Leila kina ina?”

“Gidansu Madina”

Ta amsa murya can ciki.

“Ki dawo da wuri, and make sure kin ci abinci”

“To Momy”

Momy ta sauke wayar sannan ta mike tsaye ta nufi kitchen.

Misalin 2:30pm Talba ya daka motarsa harabar Daddy, ya fito ya nufi bangarensa kai tsaye hannayensa duka biyu zube a alhaji, tafiya yake kamar wanda baya son shiga bangaren, haka yake idan yana fushi be cika son ya rabi mutane ba ko kuma mutane su rabe shi, a tunaninsa tare da kowa zasu ci abinci, domin Daddy ya saba zuwa bangaren Momy ya zauna a ci abinci rana tare ko na dare wani lokacin har da na safe, sai dai yana yin haka ne kawai ranar kun Assabar da Lahadi. Domin ranar weekend ba ya fita ko'ina sai idan fitar mai dalili ce kamar daurin aure ko wani abun, wannan al'adar ba shi kadai ba har yaransa sun saba da ita, every weekend zaka samu kowa a gida sai mai dalilin fita yake fita.
Ya samu kusan dakika 40 zuwa 50 sannan ya danna door bell din kofar falon Daddy, babu bata lokaci Amal ta bude masa kofar.

“Ya Talba”

“Lil Sis... Waye da waye a ciki?”

“Just me and Daddy”

Ya sakar mata murmushi sannan ta shiga cikin falon, tun da ya hango dinning din babu komai a kai ya tabbatar daga shi sai Daddy za su ci abincin. Kai tsaye ya wuce karamin Falon Daddy inda ya saba zama. Yana shiga ya samu Daddy zaune saman kujera yana amsa waya, sai ya zauna a inda aka jera manyan kuloli ya dauki plate biyu ya zubawa Daddy shimkafa, ya zubawa kansa a dayan plate din sannan ya bude miyar dake ta kamshin naman kaji ya zuba ma kansa kadan domin ba ya son miya tai yawa a abinci ya zubawa Daddy ta jera kofuna biyu ta zuba musu lemu ya hada komai sannan ya dauki na Daddy ya dora masa a dan karamin center table dake gefen kujera da Daddy yake kai. Sannan ya koma ya dauko na shi ya dawo kusa da Daddy ya zauna a kasa, ya soma cin abinsa yana kallon katuwar plasma dake karamin falon, Bayan Daddy ya gama wayarsa ya kalli Talba.

“Na lura har yanzu baka san ka girma ba Mu'az, ya kamata ka koyi hakuri da iya danne fushi, idan ina kiranka na damu da inda kake, wata rana bana nan, domin akwai rayuwa akwai mutuwa, na san kana kokarin ganin ka kawarda damuwa a zuciyar wasu musamman yan'uwanka, amman kai baka san yadda zaka yi ka cire kanka a damuwa ba, sai dai ka karawa kanka”

Talba ya dakatar da cin abinci da yake yana sauraren Daddy ba tare da ya kalleshi ba.

“Ka daina fushi da abinci idan ranka ya bace, And su mata ba a fushi da su, lallabasu ake, idan ka san wahalar da na sha kamin ya auri Amina sai ka ji ka tsani matar nan, amman haka na daure dan marayan Allah da ni har Allah ya ba ni ita”

Talba ya kalli Daddy yana murmushi mai sauki.

“Haba Daddy”

Daddy ya kalleshi yana dariya.

“I'm telling you my friend”

Daddy ya kai hannunss ya fara cin abinci.

“So haka zaka yi hakuri kai ta lallabata, mata soyayya suke so da kulawa, no matter how rich they are, anya ma kana kiranta da safe ka ji ya ta tashi? Like hello Baby how was your night?”

Talba ya saka dariya sosai har yana kwantawa jikin kujerar dake bayansa. Daddy ma Murmushi yai.

“Yes... Gida daya muke da Hajiya kuma a guri daya muke kwana amman kana gani kullum sai na gaishe, ni ban san abun da yake damun ku yaran yanzu ba, mu a da kunya da rashin wayewar addini ya saka iyayenmu da mu kanmu ba su yi wasu abubuwan na more rayuwar aure ba, amman ku a yanzu ga ilmin addini

da na zamani a arha ga wayewa amman kuke ta zaman matsalar zamantakewar aure, ban san miye matsalar matasan yanzu ba”

“So that's mean nine mai laifi kenan?”

“Kai ne mana, taya zaka samu mace kai tsaye da irin wannan maganar, bana jin yadda kake zaunawa kai hira da ni kana yi da ita ma, kawai kai gaka boss, gaskiya you're not romantic at all”

Daddy ya karasa yana wani yatsina fuska, wannan karon dariya sosai Talba yai har muryarsa tana fita kamar ba shi ba, dariyarsa ce ta saka Daddy murmushi mai sauti.

“Trust idan baka canja ba, za a iya kasa ka”

Ya daga kafadunsa alamar be damu ba.

“Then ai zan samu wata da gudu ma”

“Hakan na nufin ba wani son Leila kake ba, because idan kana son ta you won't said that”

Ya dan yi shiru kamar mai nazari.

“No i love her Daddy kawai dai ina sonta, but i won't tolerate nonsense”

Daddy yayi Murmushi yana dafa kafardarsa.

“Idan so ya zurfafa a zuciyarka, baka san lokacin da za ayi maka nonsense ba kuma ka dauka, a lokacin zaka zama wani stupid, fool, za a fada maka baka ga tana maka kaza ba, kace ka ji amman kana sonta ba zaka taba ganin laifin abun da take maka ba, mark my words”

Talba yayi murmushi irin murmushin nan dake nuna ban yarda ba, ranar ma ba zata zo ba.

“Yanzu ka gama cin abinci kaje ka samu Leila duk inda take ka dauko ta ka dawo da ita gida, kuma ka bata hakuri”

“No no no Daddy kasan ni bana ba wanda yake kasa da ni hakuri”

“Ba sai kace mata sorry abun da nai ban kyauta ba, no ka mata abun da zata ji farinciki sai ta manta da komai simple”

Ya dan yi jimm yana jin kamar an dora masa katon aiki.

‘Maybe i can try’

Ya fada a ransa a fili kuma sai ya amsawa Daddy da.

“Okay Daddy, for the sake of you”

Daddy yayi murmushi yana jinjina lamarin dansa.

FARUQ POV.

A gidan Mahaifiyarsa yai wanka sannan ya fito ya nufi gurin abokinsa, dake unguwar. He got lucky yana gida, yana sallama masa ya fito, bayan sun gaisa Faruq ya gabatar masa da abunda ke tafe da shi.

“Shamsu, na zo neman wata alfarma ne a gurinka”

“Allah yasa zan iya Faruq”

Faruq ya busar da iskar bakinsa.

“Wallahi ina cikin matsaloli ba ma daya ba, kasan matsalar kasar nan, mutum zai yi karatu amman aiki shiru, ga dan shagon da na kama sabuwar unguwa ce ba mutane sosai”

“Wallahi kasar ce har ka rasa yadda zaka misalta ta, abubuwan sai a hankali, idan baka yi karatu ba abun ya dame ka idan kuma ka yi aikin ya gagara”

“Shine nake son na fara koyon irin sana'arku, duk da ba iyawa nai ba amman dai idan nayi tare zan iya da yarda Allah”

Shamsu ya masa wani kallo na mamaki, a tunaninsa zai ranci kudi ne a hannunsa, sai ya ji yana masa maganar sana'arsu, ba Shamsu kadai ba kusan duk wanda ya ji mutum mai degree zai yi sana'ar gini zai yi mamaki, domin muna a zamanin da masu degree da kuma mutane suke ganin ba ko wane irin aiki ne ya dace da su ba, wani abun ana ganinsa kamar kaskanci ne, ace kana da degree kuma kai yi shi.

“Faruq zaka iya sana'ar gini kuwa? Kai da kai karatu? Kuma jikinka be saba da aikin wahala ba”

“Shamsu kenan, wanda ya tashi a area kamar wannan kuma dan talaka zai ce be saba da aikin wahala ba? Ya kake magana kamar ba san gidan da na fito ba?”

“To abun ne da mamaki Faruq naga kai ka yi karatu ka ni ban yi karatun ba”

“Ka aje komai a gefe ka duba bukatata idan zai yiyu”

“Inshallahu, sai dai ka san aikin mu tasowa yake ba wai kullum ba ne sai idan ta samu, inshallahu da mun samu zan kiraka a waya tun da ina da number ka”

“To na gode sosai sai na jika”

Ya mika masa hannu sukai musabaha, Shamsu ya koma cikin gidansa cike da mamaki, Faruq kuma ya nufi titi cike da damuwa.

FEE'AH POV.

“Gaskiya kina da kyau sosai”

“Thanks”

Shine reply din da tai ma mutumen da facebook bayan ta tura masa hotunanta masu kyau, kamar yadda ya bukata.

“A ina kike da zama a Gusau?”

Wannan karon tashi tai zaune tana tunanin irin karyar da zata masa, domin bata fada masa cewar tana da aure ba, duk kuwa da kasancewar bata dora hotonta a profile picture ba, sai hoton sunan Allah data saka as her profile picture dinta.

“Gida dari”

Ta bashi amsa.

“Na san gurin idan na shigo zamfara inshallahu zan neme ki mu gaisa”

“To Allah ya nuna mana”

Ta bashi amsa tana murmushi, kamin ta sake shiga profile dinsa ta duba komai nasa, ciki har da gurin da yake aiki da kuma hotunansa, kana ganinsa ka ga wani hamshakin mai kudi mai connection da yan siyasa, domin yadda ake masa fadanci a profile ma ya isa ya sanar da hakan. Murmushi ta sake yi sannan ta dawo inbox din ta duba tambayar da yai mata ta biyu.

“Are you on whatsapp?”

“Yeah”

Ta bashi amsa da sauri tare da rubuta masa number wayarta ta tura masa.

“Okay Thank You so much Baturiya”

Ta sake fadada fuskarta da murmushi tana jin sunan har cikin ranta. Sannan ta fita facebook din ta shiga whatsapp, few massage ta samu ciki har da reply din da MD Saleh yai mata, shi ta fara budewa da sauri jikinta har rawa yake kamin ta gama karantawa.

“Subhanallahi, Allah ya wadata, turo account number dinki”

Mikewa tai tsaye ta daka wani uban tsalle ta dire tsabar murna da jindadi sannan ta tura masa account din tana masa godiya.

“Alhamdulillah”

Ta furta sannan ta shiga group chat dinsu na makaranta, ta fita ta leka na matan aure ta fita ta shiga na novels nan ma bata dade ba ta fita ta bude chat din Ramlee.

“Kawata kin yi ciniki, wani ya ga Hotonki a wayata ya matsa na nemo masa ke”

Tana gama karanta sakon kawarta Ramlee ta zaro ido tare da sakin baki a lokaci daya, domin ta san sana'ar kawarta, tana da connection da manyan masu kudi tana hada su da mata kyakkyawa kuma masu siga kamar yadda ita ma take hulda da su, sai dai duk iskanci Baturiya bata taba aikata alfasha ba, za dai hadu da mutum har su gaisa ko kuma ta yi masa nata wayon ta waya ta samu yan

canji, amman bata san tai mu'alama da maza ba, bayan Faruq babu wanda ya taba saninta a ya mace.

“Gaskiya aa Ramlee ni dai ina jin tsoro ba zan iya ba, amman idan kin san irin wanda zan yi ma wayo ne na ci kudinsa ba sai mun hadu ba, ba matsala”

Ta mayar mata da amsa duk da kasancewar Ramlee tana Offline a lokacin, sannan ta kashe datan ta aje wayar ta mike tsaye ta fito waje.

“Sultan zo nan yau zamu ci kaza”

Ta fada tana zaunawa jikin kofar falon tana mikawa danta hannu fuskarta cike da murmushi kamar yadda zuciyarta take fal da farinciki saboda kudin da za a turo mata, Sultan din ya rugo da gudunsa yana murna.

“Abba zai siyo mana ne”

Ta shiga kabe masa riga tana fadin.

“Ba nace ka daina cewa Abba ba? Ka rika cewa Daddy, yayan talakawa ne suke cewa Baba ko Abba, yaran masu kudi kuma su ce Daddy ka ji?”

“To Daddy ne zai siyo mana?”

“Aa adashen zan kwasa yau sai na siyo mana, amman karka fadawa Daddy ka kaji? Har da lemun kwalba zan siyo mana”

Sultan din ya shiga murna yana jindadi yau za su ci kaji, rabon da su ci nama har ya manta.

AMINATU POV.

A bakin kofar shiga gidansu ta hadu da Sanusi tsaye yana latsar karamar wayarsa.

“Ya Sanusi”

Ya kalleta sai kuma yai dariya.

“Igee ai sai ki fada mana cewar kin fara fita zance, mu shirya yi miki aure”

Ta cinno baki gaba.

“Ni dai dan Allah ka daina, Allah yasa ba ka fadawa Inna ba ko Baba”

“Ban fada ba, amman dai zan fada masa, Baba ma baya nan”

“Ina yaje?”

“Gwaggo ta Makka aka aiko bata da lafiya sosai, shi ne suka je tare da Junaidu a babur”

“Yanzu?”

“No tun dazun”

“Allah ya bata lafiya shi kuma ya dawo da ita lafiya”

“Inna tace naje na dubo ki, idan kin shiga ki ce ni na zo da ke”

“Wallahi ba zan fada ba”

Ta fada tana nufar cikin gidan.

“Ni kuma zan fada mata cewar kin yi saurayi”

“To na bari”

Ta yi saurin fada har tana dawowa baya, sai ya saka dariya ya biyo bayan kanwarsa suka shiga cikin gidan tare. Kamar Kullum inna na zaune tsakar gidan tana jiran dawowarta, domin bata bachi sai ta saka yarta a ido.

“Oyoyo Auta yar albarka, an siyar ko?”

Aminatu ta aje kwallon tuwon da bokitin miyar da plates din roba a gaban ina tana sauke gajiya.

“Eh Inna wai Baba ya tafi gurin Gwaggo?”

“Eh an aiko bata da lafiya, aka ce mai rabon ganawa da ita ya zo”

“Allah ya bata lafiya”

Ta fada cike da damuwa, sannan ta ciro kudin cinikin ta mikawa Inna, sai da Inna ta kirga kudi ta ga sun cika sannan ta cire wadanda ta saba bata tana sakawa a asusu ta mika mata.

“Ga na ki”

“Na gode”

Ta fada bayan ta karba tana kallon Sanusi zuciyarta sai raya mata take zai fadawa Inna maganar, sai har sukai yar hira da zasu yi suka gama bata ci ya dauko zance ba, hakan yasa ta ji dadi sosai. Bata bude wasikar da Maniru ya bata, da fitilar da take zuwa talla ta haska wasikar da ya rubuto mata da hausar ajami, tana karantawa sai murmushi take tana jindadin yadda ya jera mata kalaman soyayya da kwantar da hankali.

Bayan ta gama karantawa ta rumgume wasikar a kirjinta, can kuma ta tashi ta saka a cikin littafanta na Islamiya kamar yadda ta saba, sannan ta gyara gurin kwanciyarta ta kwanta. Inna kam bata kwanta ba sai da ta gama komai ta kintsa komai kamar yadda ta saba sannan ta kwanta tare da rage fitilar kwai dake dakin, hasken ya rago sai dai bata kashe gaba daya ba saboda Aminatu na tsoron duhu sosai, bata bachi babu fitila a kusa da ita.

Misalin 12am gidan yayi tsit domin kowa ya nemi gurin kwanciya ciki har da yan awaki da tumakin da ake kiwo, can cikin bachi Inna ta soma jiyo hayaniya, tare da karar babura hakan yasa ta ta tashi zaune tana sauraren jikinta na bata ba lafiya ba, domin kowa ya san matsalar kasar a yanzu, balle kuma su da suke

kauye. Aminatu kam sharar bachinta kawai take bata ma san ana yi ba, jin ihu da kuma fadar Innalillahi a makota yasa Inna ta nufi inda Aminatu take ta shiga tashinta.

“Auta Auta”

Ta fada murya can kasa kasa, a hankali Aminatu ta bude ido ganin Inna yasa ta tashi zaune.

“Inna...”

“Shiiiii”

Inna ta mata alama da tai shiru. Wanda hakan yai daidai da banko kofar gidan ta kwano a shigo, ga wata uwar fitila mai shegen haske da suke ta hasken gidan da ita.

“Innalillahi Wa'inna illahirraji'un”

Inna ta furta gabanta na bugawa da mugun karfi, Aminatu ta mike tsaye da sauri kamar wanda ta rude, Inna ta shiga duba dakin tana jin kamar ace akwai wata hanya da zata bi ta fita, a rikice ta nufi gadonta.

“Shiga nan Auta shiga shiga”

Da sauri Aminatu ta nufi karkashin gadon na karfe ta shige, zuciyarta na wani irin zillo kamar zata fito, Inna ta nufi kofa domin duba sauran yayanta sai dai kamin ta isa kofar suka shuri kofar da mugun karfi ta cire suka shigo cikin dakin kamar an aikosu. Baya baya Inna tai tana fadin.

“Innalillahi Wa'inna illahirraji'u”

“Rufe mana baki dan ubanki”

Yanayin yadda yai maganar da karayar halshe kadai ya isa ya sanar da cewar gayu ne suka hauro garin a yau, wato bandits abun da ba a taba ba, domin duk wani hargitsi da ake fama da shi sai dai su ji a makotan kauyukan ko kuma a hanya abun ya rutsa da yan garin, amman ba a taba shigowa cikin garin ba. Ba Inna kadai ba har Aminatu dake karkashin gado sai da ta saka hannayenta ta rufe bakinta. Ta ko'ina jikin Inna rawa yake, ganin manyan makaman da ke hannunsu.

“Ina mijikin yake?”

Kasa magana tai bakinta sai rawa yake kamar jikinta ga wani gumi dake karyo mata.

“Wato ke ce uwar yaran ga yan iska ko?”

Nan ma Inna kasa cewa komai tai sai ambaton Allah take a zuciyarta, hannayenta duka biyu rike da bakinta.

“Innalillahi”

Inna ta jiyo muryar yayanta a tsakar gidan, wani irin abu ne ya ziyarci zuciyarta sai ta ji kamar ace akwai abun da zata iya yi ta ceci yaranta.
Dun dun dun ta ji tashin bindiga kamin ta tantance komai ta ji muryar Sanusi yana kuka.

“Wayyo Allah na, la'ilaha illahu, Innalillahi”

A lokacin ne hawaye ya cika idonta, irin hawayen da kowace uwa take yi idan ta kasa taimakon yayanta.

“Wayyo”

Ta jiyo ihun matar Amadu, bata san da inda kuzari ya zo mata ba har ta iya tambayarsu kamar ta rikice.

“Me muka muku?”

“Tambaya ma kike? Ba kun aje yan sakai a gidanku ba, wai masu yaya ko? To yau sai mun kashe su sai mun muku wulakanci”

Inna ta hade hannayenta biyu tana kuka tana rokonsu.

“Ku dubu girman Allah ku yi hakuri, ku kashe ni kar ku kashe yarana dan Allah...”

Bata gama rokon ba, wani ya karaso kusa da ita ta fisgi rigar jikinta.

“Cire wannan rigar ai har ke da kike uwarsu ba zamu bari ba”

Sai a lokacin Inna ta kara firgicewa, ta fara bin fuskokinsu da kallo tana ganin komai kamar a mafarki.

“Cire cire”

Sai ta rika jin kamar ba hausa suke mata ba, gaba daya ta rasa gane abun da suke nufi, bata fahimci manufarsu ba har sai da suka barge rigar dake jikinta suka kama zanen shi na suka fisge suka jefar da shi can gefe, suka mata tsirara a gabansu. Aminatu dake karkashin gado ta yi saurin kara rufe bakinta wasu irin zafafa hawaye na sauko mata, saurin rumtse ido rai hango mahaifiyarta tsirara a kwance yaron da be wuce sa'ar danta na biyar ba ya fara keta mata haddi!!
Ba mutum daya yai ba, ba biyu ba, ba uku ba, ba hudu ba, haka suka jera su goma sha daya suka yi mata yadda suke so, sannan suka fita suka barta kwance kamar tsumma. Abun ka da uwa suna fita ta yi karfin halin rarafawa ta isa inda zanenta yake da idanuwan da take jin kamar kukanta ya kare a yau. Ta dauki zanen da hannunta amman yadda zata sarrafashi ta daura ta suturta jikinta ne ta manta sakamon jin ihun Sanusi, cikin rashin kuzari zuci da na jiki ta isa jikin kofar tana kallon yadda yan bidigar majiya karfi, suka danne Rilwanu a kasa, dayansu ya kunna babur dinsa ya hau ta kan wuyansa ya tsaya.

“La'ilaha Illahu”

Inna ta fada da wata irin muryar da bata taba sanin tana da ita ba, tana mika musu hannu. Ba su kulata balle su fasa abun da suke, ba su saukar da babur din a wuyansa ba sai da suka tabbatar ransa ya rabu da gangar jikinsa, daman haka suke ma irin su Rilwanu masu aikin sa-kai domin kare rayuwarsu da kuma ta

al'ummarsu, idan suka halbeka da bingida suka ga bata tashi ba, sai su gwada adda, idan ita ma ba tai ba sai su saka dutse ko babur. Bayan sun kashe Rilwanu suka fashe rumbun hantsen dake gidan suka saka Iro a ciki suka kunna masa wuta, tare da hatsin. Wani irin ihu yake yana neman ceto amman babu wanda zai iya kawo masa dauki.

“Kaico Kaico kaico”

Inna ta fada tana kallon yadda danta ke ci da wuta, ga kuma wani a kwance, wani irin shiga da fita numfashinta ya rika yi da karfi, tana jin wani abu na mata yawo a ciki, gaba daya sai ta nemi dan sauran kuzarin nata ta rasa, a bakin kofar ta fadi kwance yawu da majina suna zubo mata a lokaci daya, cikin karfin hali ta dan dago kanta ta juyo ta kalli Inna Aminatu take boye, sannan ta juya tana kallon yadda suka dauko katon dutse suka daga sama suka saki a akan Amadu da yake da wasu barayin suka danne a kasa ko motsi baya iya yi, kamar yadda sukai ma Amadu haka wadancan barayin da suka zagaya gidan Musa suka masa, domin duk wanda ya san yayan Mai Damma ya san wuka ko bindiga bata hudasu, ya sha kuma ba bawa yaransa, ba dan komai ba sai dan kariyar irin wannan ranar, sai dai ayau shan be amfana musu komai ba, ba su kadai ba har da sauran mazan gari da bindiga bata fasawa, sukan kashe su da babur ko dutse, balle kuma Rilwanu da Iro da sukai kwarin suna a garin saboda aikin sa-kai da suke.
Sanusi kam sai yai kamar ya mutum ganin nasa mai sauki ne, domin da babur sauka hau kafarsa dan kawai su gana masa azaba, baya ambatar komai sai Allah, ba a gidan Mai Damma kadai ba, a garin gaba daya haka suka ci suka shude babu wanda ya kawo agaji, suka ci karensu babu babbaka yadda ransu ya so sannan suka bar garin bayan su kwashi abinci da mata cikin har da matan Musa da matar Amadu.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata. Akwai dan wata bakwai.
Ga masu bukata za su iya tuntubar number nan 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers Please idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

I just published "04" of my story "BAKAR WASIKA".
https://www.wattpad.com/1188003519?utm_source=android&utm_medium=com.whatsapp&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=KhadeejaCandy&wp_originator=gvBvvJY%2Brh7%2BfdxLjDxcLbTx9rDGdNBA0sMHgr3XMPr%2FqwZ4sIWJ88oZCr4nOa%2BILP0eBQ%2FKRLIQm73M62araHO6%2BoJXjoYprLv7YGhRYyguc1ysae3vRDycS1qvuqiM

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -4□

“So yanzu ka yarda zaka bata hakuri kenan”

Talba ta girgiza kai.

“Kai no never ni fa ba zan taba ba wanda yake kasa da ni hakuri ba”

Ali ya kalleshi.

“Amman ka ce Daddy yace laifinka ne, kuma kaje ka bata hakuri”

Yayi shiru kamar ba zai ce komai ba, sai kuma ya shafa kansa ya sauke numfashi a hankali.

“Yeah ba wai yana nufin na ce tai hakuri ba, ni yanzu so nake ka kirata ka bata hakuri kuma ka dauke ta ku je yawo ta wayance Shikenan komai ya wuce, amman karka ce ni na ce ka bata hakuri fa”

Ali ya rausayar da kai yana kallon abokin nasa cike da mamaki.

“Miye a ciki dan kace tai hakuri? Ko kuma ka dauke ta kuje yawo, faduwa kai?”

Sai Talba ya amsa masa kai tsaye.

“Yes, taya zaka bawa mace hakuri macen ma wanda take kasa da kai, ni me fa Ali”

“To wai idan kuka yi aure kuka samu matsala, kuma kai kake da laifi...”

Kamin Ali ya karasa Talba ya tari numfashinsa.

“Sai ta ba ni hakuri”

Ta fada da iyakancin gaskiyarta, domin har ga Allah be ga dalilin da zai saka shi bawa wanda ke kasa da shi hakuri ba, kuma mace sai dai shi a ba shi. Ali yayi murmushi.

“Yanzu dai for the sake of Daddy zaka yi”

“For the sake of him na zo har ina rokonka da kai, idan ba haka ba babu abun da zai saka na roke ka ma”

“Look Talba I'm not her boyfriend, ban san kalaman da zan mata ba, kuma ba ni nai mata laifin nan ba”

Talba ya mike, ganin hakan yasa Ali ma ya mike tsaye.

“Fine, amman tare za mu je, kana driving ina baya”

Talba be ce masa uffan ba ya nufi kofar fita, wanda hakan ya tabbatarwa Ali cewar ya yarda kenan. Sai da Ali ya shiga yai sallama da Samira sannan ya fito ya samu Talba a cikin motarsa. A hankali Talba yake tukin har suka fita daga cikin gidan suka hau titi.

“Kirata ka tambaye ta tana ina”

Ali ya masa wani kallo.

“Kiran ma? Talba wai kai zaka bata hakuri ko ni? Just ka kirata ka tambayi tana ina ma you can't?”

Ko kallon gefen Ali Talba be yi ba balle ya tanka masa.

“Fine”

Ali ya fada sannan ya zaro wayarsa ya shiga contact dinsa ya nemo number Amal, domin baya son batawa kansa lokaci tambayar Talba number ta zai iya ce masa baya da ita ma. Ringing biyu ta dauka.

“Hello”

“Hello Lil Sis ya kike?”

Ta yi murmushi jin ya kiranta da sunan da Talba yake kiranta.

“Na'am Ya Ali ina lafiya”

“Good number Leila nake so”

“Okay zan turo maka yanzu”

“Thank You”

Ya aje wayar yana kallon abokinsa tare da mamakin halinsa. In few minutes Amal ta turo masa number, a take ya kira Leila, abun ka da mai jin kai sai da wayar ta yi ringing ta katse bata daga ba, har sai da ya sake kira, wannan karon ma sai da ta kusan yankewa sannan ta daga kuma tai shiru tana sauraren mai kiran, daman can haka take babu yadda za'ayi ka kirata kuma ka yi expecting ita zata fara maka magana, sai da Ali ya saka wayar a speaker sannan ya fara magana.

“Kanwata Leila kina lafiya?”

Jin muryar Ali yasa ta dan sake domin ta san waye shi.

“Ali ya weekend?”

“Alhamdulillah kina ina?”

“Ina gida dari gidansu Madina”

“Okay gani nan zuwa”

Be jira abun da zata ce ba, ya aje wayar ya kalli Talba.

“Idan munje ta fito kai zan bata hakuri sannan na baku guri ku yi magana”

Talba ya masa wani kallo irin really!

*** *** ***

Leila ta aje wayar tana tabe baki.

“Waye?”

Madina ta tambaya tana gyara kwanciyarta.

“Ali wai gashi nan zuwa?”

“To ko ya san abun da ya faru tsakaninku ne?”

“Maybe ai Talba baya boye masa komai”

“Kin gani na fada ya damu fa”

“Ya damu amman be kira ni ya bani hakuri ko ya aiko min da sako ba? Ni I don't think Talba yana so Madina”

“Yana son ki mana Leila”

Madina ta fada sannan ta sauka saman gadon ta kama hannun Leila.

“Zo nan let me show you something”

Gaban madaubin dakin ta nufa da ita ta tsayar da ita gaban madubin.

“Kalli kanki da kyau Leila ki fada min abun da kika rasa”

Leila ta kurawa kanta ido a madabin tana kallon irin baiwar da Allah yai mata ta kyau daidai gwargwadon.

“Kyau?”

Madina ta tambaya sai Leila ta girgiza kai.

“Kudi? Lafiya? Kima, gata ko kuma me?”

“Ba ko daya”

Leila ta amsa.

“Kina da kyau da babu namijin da zaki yi tayin kanki ya ce miki aa ko waye shi kuwa, mahaifinki na da arziki da zai iya siya miki rai idan ana saidawa Leila, kina da kima, ga gata ta ko'ina, kuma duk wannan tarin baiwar da take tare da ke sai zuciyarki ta raya miki Talba baya son ki?”

Leila ta juyo tana kallon Madina

“Za ki iya fada min dalilin da ya saka yake min haka?”

Madina ta yi murmushi ta koma saman gadon ta zauna.

“Saboda Talba, na daya daga cikin irin mazajen nan masu matukar tsada da wahalar samu, kin ga duk wannan abubuwan da kike da su, Talba na da damar da zai iya cewa ba ya son ki idan har baya son ki, kuma ta zauna, domin kin san mutun ne da baya boye abu a ransa idan be masa ba, kuma babu wanda ya isa ya cilastashi, idan har baya son ki kai tsaye zai fada, amman be amsa cewar baya son ki ba ya amince”

Leila ta dan yi sama da ido.

“Haka ne but...”

Madina ta tari numfashinta.

“But Talba yana da matukar tsada Leila, Talba wani irin murdadden mutum ne mai wahala sha'ani, yadda kike takama da kyau yana da kyau, yana da dukiya, yana da duk wani abu da ake so a jikin namiji, yana da arzikin da yake jin zai iya tankwara komai yadda yake so, yana ganin tun da yana da komai dole a bi shi”

“Shi ne matsalarsa ai”

Leila ta fada tana zaunawa kusa da kawarta.

“Yeah ya kasa yarda cewar akwai abun da kudi basa siye, a nan ne kawai yai kuskure”

Leila ta yi murmushi.

“Ni kuma zan gyara masa wannan kuskuren, sai na nuna masa banbanci da sauran mata, dole ne ya san cewar ina da kima da daraja, kuma dole ya koyi yadda zai yi rayuwa da ni, all those four years of dating, ni nake bashi hakuri ko da ni ce da gaskiya, ina binsa kamar wani sarki da baiwa, all those years ni nake masa text how are you, so so so this, idan ya bar kasar nan ni zan kira shi na tambayi lafiyarsa, ko na masa sako, amman ko da rana daya Talba be taba daga waya ya tambayi ya nake ba! Idan na yi kwaliya be taba ce min kyau ba, be taba replied sakona ba, be san yai min kyauta irin ta masoya ba, balle har ya dauke ni muje yawo, ba zan taba yarda na aure shi a haka ba, now it's my turn, dole ne ya canja”

Ta karasa yana yawo da idonta a dakin. Madina ta kama hannunta.

“No Leila mutane irin Talba suna da wahalar sha'ani, kuma suna da shaukin kai ga wanda ya iya zama da su, kar garin gyara ki ballo wata barnar, idan kin bashi hakuri a inda kike da gaskiya ai ba laifi ba ne”

“No dole ne ya gyara, yana son soyayya amman be san yadda zai nuna ta ba? Be san yadda zai biya ta ba? Ban taba kiran sunansa a gaban idonsa ba sai na sakaya, amman shi be taba gwada kirana da suna mai dadi ba”

Ta karasa tana murmushi.

“I'm such a fool”

Ta kai dubanta gurin wayarta da ta soma ringing. Hannu ta kai ta dauki wayar sannan tai picking.

“Hello?”

“Kanwata ga mu harabar gidan”

“Okay”

Ya mike tsaye ba tare da tunanin komai ba ta nufi kofar fita.

“Talba ne?”

“Ali dai Uhm Talba zai zo nan?”

Ta fada tana mere baki sannan ta fice, hango Motar Talba harabar gidan ba karamin mamaki ya bata ba, domin ko a mafarki bata taba saka ran zai zo ba, kuma bata zaton Ali ya aro motarsa ne. Tun kamin ta sauko entrance din ta canja tafiya, kamar wata hawainiya haka ta rika takawa kamar bata son karasawa kusa da motar.
Da gangan tai haka domin ta san a cikin abubuwan da Talba ya tsaya akwai jira, ko bata masa lokaci for nothing, mutum ne da yake daukar lokacinsa da muhimmanci sosai, dakika daya ko biyu idan ka kara, zai iya rushe ko miye a tsakaninku, hakan yasa yana girmama lokacin wani da ra'ayinsa.
Kamin ta iso Talba ya cika har ya kusan fashewa, ba karamin jihadi yai ba na bawa zuciyarsa hakuri har ta iso. Ali dake front seat ne ya sauke gilashin motar yana murmushi, Talba kam ko inda take be kallo ba sai taba wayarsa yake kamar his life depends on it. Kallo daya Leila tai masa ta dauke kai tana amsa gaisuwar da Ali yake mika mata.

“Lafiya Kalau”

Ta amsa tana kokarin juyawa. Sai Ali ya bude motar ya fita.

“Ina zaki je?”

“Ciki zan koma, baka fada min tare da wani zaka zo ba”

Kallon mamaki Ali yai mata, ganin ta yi abun da bata saba ba. Wani irin tafasa zuciyar Talba take kadan ya rage ta kone, bude motar yai ya fito a fusace ya zagayo inda take tsaye.

“Na zo nan ne, saboda Daddy ya saka ni, ba dan ra'ayina ba, na fi karfin daukar wulakancin mace ko wace iri ce, na fi karfi na bawa na kasa da ni hakuri wannan ranar ba zata taba zuwa ba...”

Ali ya rasa inda zai saka kansa, sai kawai ya koma cikin mota ya zauna, shi da ya zo sasanci sai kuma a sake yin fada a gabansa. Talba na gama fada mata haka

ya juyo ya dawo cikin motar yadda ya rufe ganbun motar kadai ya isa ya sanar da bacin ransa.
Kamar wanda akai wa gorin tuki haka yai ribas ya rika danna horn, Mai gadin ya bude masa gate da sauri, ya firgi motar kamar wanda ya shirya bakuntar lahira.

“Wannan wace irin soyayya ce Talba me ke damunka, wai anya kana son Leila kuwa?”

Da mugun karfi Talba ya taka burki, he got lucky babu motoci da yawa a titin.

“Fitar min a mota”

Ya fada ba tare da ya kalli Ali ba. Ba sabon abu bane gurin Ali ya saba nasa haka idan ransa ya bace ko suka samu tsabani, sai dai baya hana anjima ya neme shi.

“Kana da matsala Wallahi kana da matsala, wannan mugun fushin ban san inda zai kaika ba”

Ali ya fada cikin bacin rai.

“Ka san bana son ana min ihu”

“Mtsssss”

“And i hate tsaki”

“Ba zan fita daga motar ba”

Ali ya fada yana gyara zama. A take Talba ya bude motar ya fita ya barta kunne, ganin hakan yasa Ali yai saurin fita ya zagaya driver side ya cigaba da tukin yana mamakin rayuwar Talba.
Gefen Titi Talba ya dawo ya tsaya, a ganinsa kaskanci ne ya shiga napep balle kuma ya hau babur zuwa gida, not just that even tsayin da yake a gafen titi ba girmansa ba ne, wayarsa ya ciro ya kira direban gidansu.

“Ka zo ka dauke ni zan turo maka location ta whatsapp yanzu”

Shine kawai abun da ya fada ya kashe wayar ya kunna datarsa ya shiga whatsapp dinsa ya tura masa location din, sannan ya maida wayar aljihu yana kallon titi, har lokacin zuciyarsa zafi take masa saboda Leila ta kira shi da wani, how on earth zata kira shi da wani?
After like 15 min direban ya iso, da kalle kalle har ya hango inda yake ya faka masa motar, Talba ya bude ya shiga ba tare da yace masa komai ba, shi ma direban be yi kokarin yi masa magana ba domin ya san Talba baya son yawan gaisuwa da kuma kallo, idan kuma kana son bata masa rai to ka cika shi da surutu.
Suna isa gida ya bude motar ya fita ya nufi bangarensu, wato shi da Kabir sai dai kowa side dinsa dabam, kai tsaye bedroom dinsa ya shiga ya jefar da wayarsa kan gado ya cire rigarsa da agogo ya shiga bathroom, sannan ya ciri jean din dake jikinsa ya kunna shower ya tara jikinsa yana kallon kansa a katon madubin dake facing dinsa a bathroom din, kamin ya dukar da kansa yana kallon zanen sunansa da tattoo dake kirjinsa wanda babu wanda ya san da shi sai shi kadai, can kuma ya dago ya lumshe ido.

AMINATU POV.

Kusan ko wane gida dake garin an taba, wasu an kashe wasu an kwashe duka da dabobi, wasu an tafi da yayansu da mata, wasu kuma anyi ma matan fyade, sai dai ba kamar gidansu Aminatu ba, domin wulakancin da akai wa mahaifiyarta ya wuce na kowa mutum goma shadaya a lokacin daya, kuma aka kashe yayyayunta hudu, aka kona rumbun hatsinsu, aka raunata wasu, aka kora dabobinsu.
Ba gidan kadai ba garin gaba daya tsit yai duk kuwa da kasancewar barayin sun yi iya barnar da zasu yi sun tafi, amman tsoro ya hana kowa fitowa, sai kuke kuke kake ji a gidanje, sai dai gidansu Aminatu ya fita dabam da baka jin kukan kowa, har asuba Aminatu na boye karkashin gado, mahaifiyarta kuma tana zaune a bakin kofar idonta a bude amman bata iya komai kamar an zare mata lakka a jiki haka take ji, Sanusi kuma na tsakar gidan a sume. Kamar macijiya haka Aminatu ta fito karkashin gado, ta janyo zanen gadon dake kan gadon karfe dan bono na Inna ta nufi Inna dake kwance tsirara tana kawar da idonta tana kuka har ta karasa kusa da ita ta kulluba mata zanen. Sannan ta juya ta koma inda fitilar kwai take ta dauka ta kara haskenta, ta taka kamar mai koyon tafiya ta fito waje. Wani rawa jikinta ya fara yi hango rumbun abincinsu na ci da wuta, sai kuma ta juya a hankali ta sauke idonta kasa ta kalli gawar Iro, da ta Amadu, ga kuma Sanusi shi ma dake kwance, kafa na zubar da jini, gaba daya ilahirin jikinta ne ya fara rawa kamar yadda bakinta ma yake yi.

“Ya... Ya... Ya.. Ya..”

So take ta kira sunan daya daga cikinsu amman ta kasa, hawaye sai aikinsu suke a fuskarta. Ta saki fitilar numfashi na fitar mata da karfi, wani kuma na shiga da sauri. Juyowa tai ta kalli Inna dake kwance bakin kofar har lokacin idonta na zubar da hawaye, sai wulakancin da akaiwa mahaifiyarta ya fado mata a rai, komai ya zame mata sabo.

“Me muka musu?”

Ta tambayi kanta tana wani irin kuka na fitar hankali, sai kuma ta ruga da dugu gurin yayanta Sanusi ta taba shi. Sai kuma ta juya ta kalli yayanta Amadu dake kwance kai a fashe, take ta girgiza kai.

“Ba da gaske ba ne aa, wannan be faru ba, yan'uwana ba su mutu ba, ba ayi ma mahaifiyata fyade ba, wadandan nan mutanen ba su zo ba, komai be faru ba”

Ta tashi da sauri ta ruga da gudu daki ta koma gurin kwanciyarta ta kwanta taja abun rufa ta lullube ta kame guri daya ta runtse ido, da gaske so take ta farka daga bachin, so take komai ya zama mafarki. Sai a lokacin Inna ta samu kuzarin motsawa ta fashe da kuka.

“Allah ka isar mana ga bayinka Allah....”

Ta fada tana kara fashewa da wani irin kuka mai ban tausayi ta taba zuciya. Jin kalamanta ne yasa Aminatu ta saka hannayenta ta toshe kunnuwanta ta kara runtse ido ta kwara wani irin ihu da muryar da bata taba sanin tana da ita ba.

“Aaaaaaaaaaaaaaaaaaaa”

Ba makotansu kadai ba, har gidan dake tsakaminsu dashi gida biyar ne sai da suka ji ihun Aminatu.

>>>>>>>>>>
Anya Leila zata kai labari kuwa na cewar sai ta koyawa Talba darasi?

Nikan nace Ali yana hakuri da wannan aboki nasa mai wuyar sha'ani da jin Kai 😕😫😫

Allah sarki Aminatu, ko da yake mahaifiyarta ce abar tausayi. 😭😭😭

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata. Akwai dan wata bakwai.
Ga masu bukata za su iya tuntubar number nan 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers Please idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.
https://www.wattpad.com/story/283871769?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_reading&wp_page=reading&wp_uname=KhadeejaCandy&wp_originator=ZCqcO2wXIv6pkkxIr3do4ng1%2BTHhzoVPTPFtpfDcb1ftHOVsldMflpG2lAwd5aYtrehJ12WEeerjWSVNDZunKAH9QpxhI0A%2BzJsYI6RrshbTOZsoLUXljeZDCPaDNtKr

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -5□

Sai after sallah isha'i ya fito harabar gidan ya zauna a inda aka jera kujerun zama domin hutawa, kusa da garden, sai kamshin turare yake kamar sabon ango, fuskarsa cike da annuri, sai dai babu walwala ko kadan a tare da shi.
A hankali ya hade yawun bakinsa ya daga kansa sama yana kallon taurarin dake samaniya, kamin ya juyo yana kallon Amal dake sanye da kayan bachi tana nufo inda yake.

“Ya Talba”

Ya dan sakar mata murmushi kadan.

“Lil Sis ya kike?”

Ta zauna a kusa dake kusa da tashi tana amsawa.

“Lafiya kalau”

Sai kuma ta yi shuru tana kallonsa.

“Kina bukatar wani abu ne?”

Ta girgiza kai ta soma wasa da yatsun hannunta.

“Talk to me Lil Sis fada min damuwarki”

Ya fada yana kallon yanayinta dake nuna akwai damuwa a tare da ita.

“Yaya ka sake yin fada da Ya Leila ne?”

Fada suka yi? Ya zai fada mata? Abun da suka yi fada ne ko aa, shi be ma tabbatar ba, all what he know is ta kira shi wani shi kuma ya fada mata magana, sincerely speaking ma ya manta me yace mata.

“Yeah Maybe”

Ya fada yana dan tabe baki.

“Miya faru?”

“Ta dawo gida tana ta kuka tun dazun, yanzu kuma kuma Daddy ya shigo yai ma Momy fada ita ma kuka take?”

“Why?”

“I don't know, kawai dai na ji Daddy yana cewa babu wanda ya isa ya wulakanta masa d'a, kuma wai ya zaba maka Leila ne saboda kar kaje neman auren wata a wani gidan ace ba za a baka ba saboda yadda kake behaving, amman a gidansa yana da iko da Leila”

Talba ya cika ma bakinsa iska ya busar.

“Ina Momy?”

“Tana dakinta...”

Amal ta karasa tana kallon Kabir daya doso inda suke zaune ta kofar gaba, kana ganinsa ka san a fusace yake.

“Look Talba, ba zaka Leila kuka saboda bakin halinka and now ka saka Momy kuka ba okay? I won't tolerate this, dole ne sai ka auri Leila ne? Idan ba ka canja hali ba ba zaka taba aure ba a rayuwarka”

Daga inda yake zaune ya dago yana yi ma Kabir wani banzan kallo.

“Ka sani ba a amin tsawa ba a nuna ni da yatsa”

“To sannu ubana, sannu Sarkin Arewa, girman kai zai kashe Mtsssssssss”

Kabir ya karasa yana jan wani dogon tsaki. Amal ta yi saurin kama hannun Talba.

“Ya taso mu bar mishi gurin gaba daya”

Uffan Talba be sake cewa ba ya bi Amal dake rike da hannunsa, har sai da suka shigo cikin falon sannan ya saki hannunta.

“Je dakinki zan yi magana da Daddy”

“To amman karka ce masa ni na maka gulmar”

Yayi murmushi ya juya zuwa bangaren Daddy. Daman can duk wata gulmar gidan gurin Amal ake jinta. Cikin natsuwa da kamala ya shiga bangaren Daddy, yai sallama Daddy ya amsa masa tare da kai hannu ya dauki remote ya kashe plasma dake kunne. Talba ya zauna kasa kusa da kafafuwan Daddy.

“Daddy yau na kawo maka karar kanka”

Daddy yayi murmushi.

“Na taba Momy ko?”

“Eh Daddy ka san bana son hawayen Momy”

“To ai laifinta ne, taya Leila zata yi laifi na yi mata fada kuma tace zata shigar mata”

“Amman Daddy Momy tana kare Leila ne kamar yadda kake min, kuma tun da har Momy ta shigar mata na yarda ni ne ba ni da gaskiya, domin Momy kullum tana side dina ne”

Ya sauke ajiyar zuciya.

“I will try my best na ga na zama Romantic, zan zama yadda Leila take so indai hakan zai faranta ran kowa, yanzu abu daya nake so Daddy ka je ka bawa Momy hakuri?”

Daddy ya nuna shi da yatsa.

“Hey i talk to your mom na mata fada, kuma ita ya kamata ta ba ni hakuri saboda rai na ya bace”

“Amman Daddy ai kai kayi mata laifi”

“Really? Kasan da wannan amman idan kai ma Leila laifi sai ka sa bata hakuri”

Talba yayi murmushi.

“Daddy wacan yana da banbanci da wannan, ita Leila ai yarinya ce, wannan kuma ba zaka iya da yayanta ba, yaranta ba za su yarda kai mata haka ba”

“Leila ma wata rana uwar wasu ce, kuma yaranta ba za su dauki abun da kake mata ba, kamar yadda a yanzu kake jin rashin dadi, and tell me, you take your Mom side”

Talba ya sake yin murmushi.

“No Daddy kullum ai ina side dinka, amman dai ina son Momy ta daina bacin rai please”

“Shikenan zan kirata ta zo nan na bata hakuri”

“No Daddy ka tafi dakinta mana, zata fi daukar abun da muhimmanci Please”

Daddy ya masa kallon mamaki.

“So that's mean kasan yadda ake lallaba mace, duk abun da kake yi da gangan kake yi kenan?”

Talba ya mike tsaye yana dariya kamar ba shi ba, Daddy ma murmushi yai mai sauti yana binsa da kallo cike da kauna irin ta Uba da D'a.
Bangaren Momy ya dawo, kai tsaye ya nufo dakin Leila, be tsaya knocking ba ya tura kawai ya shiga, sai ya same ta zauna gaban mirror tana duba fuskarka. Tsaye yai cak kamar an dasa shi, ta ina zai fara? Me zai ce mata? Sorry? Shi da kansa? Yace mata sorry? After ta kira shi wani? Taya ma zai ce mata haka? For the sake of Daddy, wata zuciyar ta raya masa, but duk da haka be jin zai iya ce mata sorry.

“Idan wani abu ya faru a tsakaninmu, ki bar shi a tsakaninmu ba zai wani ya ji ba”

Ya fada sannan ya juya, sai kuma ya juyo.

“And if you need something, lemme know”

Yana fadar hakan ya juya ya fice ba tare da ya rufe mata kofar ba. Tabe baki tai ta mike tsaye ta isa gurin kofar ta rufe ta juyo ta dawo gaban madubin ta zauna. Har ga Allah tana son Talba, kuma ta san yana sonta amman abun da yake mata is yayi yawa, girman kansa da jin kansa yayi yawa, that's why dazun ta fadawa Daddy cewar bata shirya aurensa a yanzu ba sai nan gaba, Momy kuma ta goya mata baya ganin kullum ita ake kwaruwa, but this time around Momy ta goyi bayanta.
Jin wayarta ta yi kara alamar sako yasa ta mike tsaye ta isa gurin da wayar take ta dauka ta duba sakon.

“Good Night”

Shine rubuce da number Talba, ba shiri ta zauna tana mamaki. Da gaske shi ne ya turo mata sakon ko wani dai? Dan murmushi.

“Duk sai na rama abun da kai min, it's my turn”

Ta fada tana jin wani irin dadi, juya ido tai.

“Ya kamata ya san ina da tsada”

Ta fada sannan ta kwanta saman gadon.

*** *** ***

Kamar jiya Saturday, yau kuma Sunday, kowa yana zaune a teburin cin abinci ban da Daddy da zai karya bangarensa da kuma Leila da take dakinta.

“Ina Leila?”

Talba ya tambaya yana kallon Amal.

“Tace zai ba zata fito ba”

“Why?”

“Just”

“Hada nata breakfast din na kai mata dakinta”

Ba Momy da Kabir ba, ko Amal har Baaba mai aikinsu sai da ta kalleshi.

“Kamar dai ba kai Talba”

Kabir ya fada, sai Talba yayi murmushi kadan.

“Sounds funny, right?”

“No sounds new”

Momy ta yi murmushi.

“Ban fada muku ba? Wata rana Talba zai canja”

Ya mike tsaye ya shiga hada ma Leila nata abun karyawa.

“I didn't change, ina yi ne for the sake of you and Daddy”

“So na dan ra'ayin kanka kake ba, kenan baka farinciki da abun da kake, doesn't make sense”

Kabir ya fada yana tabe baki. Talba dai be sake ce masa komai ba har ya cirewa Leila komai ya dauka ya nufi upstairs. Amal ta mike da sauri ta bi bayansa ta rigashi karasawa gurin kofar ta bude masa saboda hannayensa duka biyu suna dauke da abu ne. Yana shiga Amal ya janyo kofar ta rufe, har gefen gadonta ya aje mata komai sannan ya dago ya kalleta.

“Good Morning”

Ya sake gaisheta duk da kasancewar ya aika mata da sakon gaisuwa da safe kuma bata masa reply ba, which is pain her. Bata amsa masa ba sai kallonsa take.

“Ga breakfast dinki, idan kina bukatar wani abu ki fada min”

Yana fadar hakan ya juya, sai da ya kusa isa kofa sannan ta ce.

“Anjima zaka kai ni shopping”

“Idan kin shirya ki kirani”

Ya fada ba tare da juyo ba, sannan ya fice ya ja mata kofar. Yana saukowa downstairs be koma dinning din ba sai ya nufi kofar fita, yana fitowa ya tsaya bakin kofar falon ya kira Ali. Kamin Ali yai picking Kabir ya fito ya tsaya daidai inda yake tsaye.

“Kasan mi ye Talba?”

Talba ya kalleshi yana kokarin yanke kiran Ali da yake.

“Kai dan'uwana ne, ba zan so ka cutu ba, kamar yadda ba zan so Leila ta samu matsala, ni shawarar da zan baka karka auri macen da baka so, domin zaku yi ta samun matsala ne kawai, ji abun da kake yi a yanzu saboda Momy da Daddy kake yi ba wai dan ka faranta ranta ba, kuma ba dan kana so ba, hakan kuma zai haifar da kiyayya da tsana a tsakaninku”

Talba ta saka wayar aljihu yana kallon Kabir.

“Ina sonta Kabir...”

“No, maybe dai kana sonta saboda baka san miye so ba, ko kuma kana sonta saboda baka son ka bawa Daddy kunya, ko kuma kana sonta saboda kana son ka yi aure, amman na san wata rana zuciyarka zata so wata wata kila Leila ce ko wata dabam, a lokacin da zata maka laifi kuma na bata hakuri Wallahi baka ko sani ba, wanda zaka so faranta mata a karan kanka, idan tana cikin damuwa kai ta kokarin ganin ka cireta, idan tana kuka karika jin hawayenta kamar mutuwarka ne, duk wannan shan kunun da kake yi ita zaka sake mata ka rika neman tai maka murmushi kana mata dariya, idan zuciyarka ta fara wannan son, duk son da biyayyar da kake yi ma Daddy ko Momy idan suka muzantata sai ka ji ba dadi kamar kai aka yi ma, daga lokacin ne rayuwarka zata fara canjawa...”

“Noo Kabir, you know i don't believe in love, so wannan daren ba zai taba zuwa ba balle har na kwanta na yi wannan kalar mafarkin, ku ne da kuke karance karance da kallo fina finai kuke dauka irin wannan soyayya gaskiya ce, even if gaskiya ce ma ni bana cikin irin wadannanhawayen mazan...”

Yana fadar hakan ya fara sauka entrance din. Kabir ya bishi da kallo yana murmushi.

AMINATU POV.

Sai da haske ya fara bayyana sannan mutane suka leko gidan, duk da kasancewar kowa yana fama da nasa jimamin. Duk wanda ya shigo ya tararda gawar su Amadu sai ya zubar da hawaye, daman can kowa ya saka ran sai ayi musu ta'asar da tafi ta kowa saboda suna da yan sa-kai har biyu da da barayin yankin suke matukar tsoronsu, domin basa yi ma barayi da sauki musamman idan sun hadu da su a wani gurin. Da taimakon yan tsirarun garin da suka rage aka dauko zage aka rufe gawarsu, Sanusi kuma aka dauke shi kan babur zuwa babbar asibitin shimkafi, a lokacin ne Inna ta fahimci har da Musa aka kashe, kuma aka tafi da matansa biyu bayan matar matar Amadu, cikin yaranta da suka tsira Aminatu ce kawai ita ma dan ba su ganta ba ne, sai kuma Isa da ya tafi kai Baba gurin ganin Gwaggonsu, sai kuma Bashiru dake kasuwancinsa a birni tare da iyalansa.
Karfe bakwai da yan mintuna Baba ya iso cikin gidan, domin labarin abun da ya faru ya same shi a can garin da yake gurin kanwarsa, yana shigowa cikin gidan ya kasa rike kansa, tsayi ma ya kasa duk da kasancewarsa namiji sai gashi ya zube kasa yana kuka da idonsa, Inna kam zaune kawai take tana kallon komai, hawayen sun dauke mata. Da dai daya Baba ya fara bin gawar yayansa har hudu yana dubawa, Isah ma kuka yake sosai, ya ga Amadu da ka fashewa kai, sai kuma Rilwanu, da aka takewa wuya da babur, haka Musa na da dutse aka fashe masa kai. Iro kam gawarsa bata wuce ta karamin jariri ba domin gawarsa ta kone kurmus daker aka samu aka hada dan abun da yai saura gudu daya aka lullube da zanen Inna.
Baba ta fadi zaune ya fashe da wani irin kuka yana dora hannu saman kai.

“Allah ka hana zalinci, Allah ka sani mutanen nan ba mu musu komai ba, Allah ka isar mana”

Baba ya fada cikin wani irin kuka mai ban tausayi da taba zuciya, sai kuma ya juyo ya kalli dansa Isah da shi ma kukan yake ya ce.

“Isah ka gani an kashe an yan'uwanka...”

Daga inda Inna take zaune ta amsa.

“An kashe su Malam, d'a hudu, ni na haifi yarana kuma a gaban idona aka kashesu, yaran da ba su wuce sa'an yayana ba suka keta min haddi har su goma sha daya, a gaban yata, suka kone muna abinci, suka kora mana dabbobi, saboda kawai zalinci, titin kwarai ba mu da shi a garin nan, ba mu damu da cigaban zamani ba, taki ma sai an ga dama a bamu, duk wani cigaba ko aikin taimako ba mu san shi ba, da hakkinmu muke tara komai, yanzu kuma zaman lafiya da farinciki ya gagaremu...”

Inna na gama fadar hakan ta mike tsaye da sauri jin kamar numfashinta zai fita, ta dora hannunta a kirji tana kuka tana neman agajin Allah.

“Innalillahi, shikenan sun raba ni da murmushi sun raba ni da dariya, kuma sun keta rigar mutunci na”

Safa da marwa ta fara yi cikin gidan hannunta akai tana kuka tana jijjiga. Duk abun da ake a kunnen Aminatu, domin bachin da take son ya dauke ta ta sake farkawa a rayuwar zahiri be dauke ta ba, har lokacin kuma jikinta be daina rawa ba, kamar yadda kunnuwanta ba su daina jin karar binga, haka idanuwanta ba su kawar mata da ganin da tai ana yi ma mahaifiyarta fyade ba.

“Ina Auta? Ko sun tafi da ita?”

Baba ya tambaya yana kuka sosai, sai wata matar dake tsaye kusa da Inna tana kokarin bata hakuri ta ce.

“Aa tana daki”

Duk wanda ya ji ko ya ga ba aje da Aminatu ba ya san da cewar ba su ganta ba ne, yadda suka kwashi matan garin suka tafi da su babu abun da zai hana su zuwa da Aminatu. Baba ya tashi da sauri ya shiga dakin, sai ya same ta a inda ta saba kwanciya tana lullube, ba jikinta kadai ba, har hakoranta kana jin kara yadda suke haduwa da juna tsabar yadda jikinta yake rawa. Baba ya kai hannu ya janye mayafin sai ta tashi da sauri idonta a kumbure ta kalleshi.

“Baba...Baba... Baba... Baba”

Baba ya sake fashewa da kuka.

“Baba wasu mutane ne suka zo.. Ba mu musu komai ba Wallahi, ba mu musu komai ba... Sun... Sun... Sun... ”

Ta kasa fada sai ta fashe da wani irin kuka ganin cewar da gaske ne komai ya faru ba mafarki ba.

Ba ko wace gawa ta samu sallah da sutura yadda ya kamata, saboda yawan gawarwakin, ashe ma samun sutura da masu yi ma gawa sallah da kuma binne ta kamar yadda addini musulunci ya tabadar wani abu ne da ba kowa yake samu ba, domin wasu da tufafin jikinsu ake saka su a cikin ramen, wani ramen kuma sai a hada mutum hudu guri daya.
Bayan an binne gawarwarkinsu ne, Bashiru ya iso, hankali tashe, yana shigowa shi ma ya fara nasa kukan, na rashin yan'uwa. Aminatu kam tana can gefe daya zaune ta ki yarda ta zauna cikin mutane ko kallon mutane bata so, kuma ta ki cin komai. Sai da ta ji Baba yana maganar zai tafi asibitin gurin Sanusi sannan ta mike tsaye da sauri.

“Baba dan Allah ka tafi da ni”

Ta fada cikin kuka, wani irin tsoro take ji ganin take kamar sake dawowa zasu yi, gaba daya a firgice take, a dayan bangaren kuma tana son ganin halin da dan'uwanta yake ciki.

“Aa Auta ki zauna a nan, asibi ce fa”

Ta yi saurin rike rigarsa ta fashe da wani irin kuka.

“Dan Allah Baba ka tafi da ni, ka taimaka min dan Allah Baba ka tafi da ni”

Idon Baba ya sake cika da kwalla.

“To saka talkaminki mu tafi”

Ta saka talkamin dake kusa da ita, bata tsaya neman nata ba, haka suka fito cikin gidan tana rike da rigar Baba, Baba ya nuna mata wani babur.

“Ki hau Babur din Buba, ni zan hau na Isah”

Sai ta girgiza masa kai tana kuka ta rumgume shi.

“Aa Baba Baba dan Allah karka sake yin nisa da ni”

Gani take kamar idan yana nan babu abun da zai faru, gaba daya ta rasa gane kan komai, kwakwalwarta ba zata iya dauka ba.
A dole babur daya suka hau ita da Baba, dan motsi kadan sai ta ji kamar zuciyarta zata fado tsabar tsoro, har suka isa idon a rufe yake domin ganin take idan ta bude ido mutanen zata gani.
Ko da suka isa sun tararda asibitin a cike, domin a kauyensu ko a gidansu kadai akai ta'asar ba, an kawo mutane da yawa, wasu sai ihu suke wasu kuma suna zaune suna jiran a gama da wasu a duba su. Baba da Aminatu waje suka tsaya Isah ya shiga ciki, ganin ya dade yasa Baba ya shigo cikin emergency tare da Aminatu, gaba daya ta kara firgicewa ganin yadda wasu ke zubar da jini. Kamin su karasa inda suke zaton dakin da Sanusi yake ne, Isah ya fito yana kuka.

“Lafiya?”

“Baba babu Sanusi, Sanusi ya tafi sai dai idan mun isko shi, Allah ya jikanka Sanusi...”

Ya fada yana kuka, sai ga gawarsa an fito da ita. Aminatu bata san lokacin data saki rigar Baba ba ta ruga da gudu gurin gawarsa, duk ita duk tsoron gawa da take yau ta manta da wannan.

“Wayyo Allah na shiga uku, Ya Sanusi”

Sai kuma ta juyo da gudu gurin Baba dake kuka ta rike shi.

“Baba kai yi wani abu dan Allah Ya Sanusi ya tashi”

Baba ya girgiza mata kai yana wasu irin hawaye masu zafi.

“Ba ni da rayuwa Aminatu, sai hakuri”

Sai ta sulale kasa ta fashe da kuka.

“Wayyo na rasa Yaya mai sani dariya, yayana mai tsokanata, Yayana mai so na”

Baba ya duka kamar zai mata magana sai dai shi ma bashi da zuciyar yin haka a yanzu, sai ya kara fashewa da kuka.

“Allah ya Isar mana Allah ka isar mana”

Isah ya fada yana kuka, duk wani mai sauran imani da tausayi sai da idonsa ya cika da hawaye saboda tausayi. Zunbur tai ta tashi tsaye.

“Baba ku duba kila be mutu ba...”

Rugawa tai zata tafi gurin gawar sai Isah ya riketa, wani irin tsalle tai tana son ta kwaci kanta daga rikon da yai mata amman ta kasa, ta fisgi kanta ta fisga ta

sake fisga ta sai fashe da tana jin kamar ace yau akwai abun da zata iya yi ta dawo da rayuwar Sanusi.

>>>>>>

If you want to subscribe pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith Bank, and send the evidence to 08036126660, zan yi adding dinki paid group In-sha-Allah.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata. Akwai dan wata bakwai.
  Ga masu bukata za su iya tuntubar number nan 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers Please idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Bakincikin mutuwa, da damuwar rasa rai, wani irin bakinciki ne da yake ma kansa muhalli a zuciyar bawa, baki yayi kadan ya bayyana yadda zuciyata take ji, haka zuciya ma ba zata iya daukar abun ita kadai ba har sai da taimakon idanuwa da gangan jiki.
Taya Aminatu zata fadawa kowa yadda take ji? Taya zata rasa yayyu biyar maza kuma ta kasa kuka? Taya za a maida garinsu da gidansu kamar kufai kuma ta kasa kuka? Taya za a keta haddi mahaifiyarta a gaban idonta kuma ta kasa kuka?
 A tsakanin rasa yan'uwanta da kone musu abinci da keta haddin mahaifiyarta bata san wani yafi wani zafi ba. Anya zata iya dauka?

“Duk ni kadai?”

Ta furta wasu hawaye mazu zafi na sauko mata, kana ganin yanayinta da kuma jin kalaminta kasan bata cikin hayyacinta, ruwan hawayen dake mata zuba har ya canja launin fatar idonta, ya kumbura mata ido, kwayar idon kuma ta mata ja sosai.

“Auta dan Allah ki yi hakuri, haba kowa ba yana da tabon mutane nan a garin nan”

Anty Aina'u matar Bashiru ta fada tana kai hannu ta dafa ta. Aminatu ta kalleta kamar tace mata shiga zuciyata ki gani, sai kuma ta dauke kai ta hadeye yawu. Har aka yi gaisuwar kwana uku aka watse Amintu bata daina kuka ba, kukan da ta sha ko Inna bata yi ba, domin Inna ta bar komai a zuciyarta ne, idan ta yunkurin kukan ma baya zuwa mata, sai dai bata iya komai ko bandaki zata zagaya sai an rikata. Idan kuma ta zauna ta sanda kai kasa bata iya dagowa sai an rika kan nata an dago da ita. Kana ganinta ka san kukan zuci take wanda ya fi na ido illa.
Washe garin Ranar da aka watse Aminatu na tsakar gida tana wanke wanken kayan abincinsu, sai kawai ta fashe da kuka, rayuwarsu take tunawa kwana hudu zuwa biyar da ya wuce, a da idan tai wanke wanke kowa zubawa ake, amman yanzu daga ita sai Isah da Inna da Baba kawai suke ci, ba kamar da ba. Tunawa da tai da maganganun da mutane suke mata cewar ta yi hakuri ko dan ta karfafawa mahaifiyarta guiwa yasa tai saurin share hawayen. Ta cigaba da wanke wanke bayan ta gama ta dauki kayan ta kai a inda suka saba ajewa ta aje. Sannan ta fara sharar gidan, tana yi tana ta ganin inda aka aje gawarwakin yan'uwanta, ta kasa daina ganin abun a idonta.
Bayan ta gama sharar ta dauko tabarma ta shimfida daga bakin kofar sannan ta shiga ciki ta riko Inna dake kwance.

“Inna muje waje ki sha iska”

Daman zaman dakin ya fara isarta, sai ta yunkura, Aminatu ta taimaka mata ta mike tsaye tana takawa a hankali har suka fito, Aninatu ta zaunar da ita a hankali, sannan ta koma ciki ta dauko filo ta jingina mata a jikin ginin na kasa, ta jinginata. Take Inna ta sauke wata irin sanyayyiyar ajiyar.

“Allah ya miki albarka”

“Amin”

Aminatu ta amsa hawaye na sauko mata ganin yadda rayuwata ta sauya mata ita da mahaifiyarta a lokaci daya. Inna ta sakar mata murmushi sannan ta soke kai kasa. Madafa Aminatu ta nufa ta kunna wuta ta dora tukunya ta zuba ruwa. Sannan ta koma ta auko shimkafar da yayanta Bashiru ya siyo musu ta fara tsinta.

“Ji dan Allah ko tsintar shimfar bata iya ba...”

Ta lumshe ido da sauri tunawa da yayanta Sunasi da tai, yana yawan tsokanarta komai take sai yace bata iya ba. A hankali ta daga kai tana kallon ginin da yai domin yana daf da aure shi da Isah. Duk yadda ta so ta tana kanta hawaye sai ta kasa, hannunta ta saka ta share hawayen tana jin kamar wani nauyi a zuciyarta.

“Ashe haka ake ji idan aka rasa rai”

Ta furta a hankali tana kokarin tsayar da kukanta, sai kuma tai murmushi da yafi kuka ciwo.

“Mutuwa bakin takobi mai raba uwa da daya, ta raba yan'uwa ta raba mata da miji, kin maida mana gida kamar kufai”

Ta damki shimkafar a hannunta wasu hawayen na sauko mata kamar ba gobe, a dole ta aje gyaran shimfara saboda hawaye ya hana ta ga komai.

“Auta...”

Ta juyo da sauri jin kamar muryar Inna ta kirata, sai dai ganin kanta a noce ya tabbarta mata ba kiranta tai ba, muryar dai ce take jin kamar ta Inna. A take ta fashe da kuka ta bar gaban murhun ta mike tsaye wanda hakan yai sanadiyar barewar shimkafar da ke jikinta ta nufo inda ta gudu ta fada jikinta tana kuka. Sai Inna tai saurin lumshe idonta da sauri tana jin kukan Aminatu har cikin ranta, tana son tace mata yi hakuri amman bakinta ya mata nauyin da take jin kamar maganarta ta kare a duniya, sai kawai ta daga hannunta ta dora a jikin Amimatu tana shafata alamar rarrashi.

“Miyasa wani zai ji bakinciki da farinciki mu? A kauye muke zaune amman muna jindadi rayuwarmu, miyasa za su ruguza farincikinmu? Na kasa saba da rashin Yaya Sanusi Inna, Inna yanzu waye zai sake tsokanata? Yaya Amadu mai min fada baya nan, yaya musu mai bamu abinci baya nan, sun kashe Yaya Rilwanu da Yaya Iro...”

Inna ta bude idonta ta saka hannu ta kama fuskar Aminatu.

“Zan tafi na barki Aminatu, yar Autana, ina son ki saba da hakuri, akwai kalubale a gaba, mace da ta tashi a cikin gata da soyayyar uwa da uba da yan'uwa irin ki, duniya ta sauya mata lokaci daya? Dole zata ji ba dadi kuma zata fuskanci kalubale, amman zan fada miki wani abu, ina son ki rike ki rika maimaitawa, a duk lokacin da kika tsinci kanki a damuwa ko kika ga wani abun tashin hankali bakinki ya saba da furta Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, ri rike wannan kin ji”

Aminatu ta kalli Mahaifiyarta hawaye na sauko mata.

“Inna idan kika mutu kuma zai ki yi tsammani ni zan rayu? Wannan wace irin magana ce?”

“Zaki rayu Autarta, dan na mutu ba shi yake nufi ki mutu ba, Allah be raya wani dan wani, kuma be kashe wani dan wani, da ya bar yayana dan ni, ko kuma ya bar su dan ke, yadda ya so haka yake”

“Inna maganar da kika fada min yanzu, ta fi min ciwo fiye da rasa rayuwar yan'uwana, kada Allah ya nuna min ranar da zaki tafi ki bar ni, sai dai ni na tafi na barki”

Ta fada cikin kuka sannan ta rumgumeta. Inna ta sake runtse ido tana jin wani kololon bakinciki yana mata yawo a zuciya. Suna haka Baba ya shigo rike da yar ledarsa ta dawo (Fura) ganinsa yasa Aminatu ta tsagaita kukanta ta daga jikin Inna tana fyace hancinta.

“Kukan dai ne be kare ba”

Ya fada yana zaunawa kusa da Inna kana ya aje mata ledar furar.

“Ga fura Auta ta dama miki na san ba iya cin wani abua kike ba”

Kallon furar kawai tai ta dauke ido.

“Baba sannu da zuwa”

Aminatu ta fada da muryarta ta kuka, wai Baba yai mata murmushi irin na su na manya domin shi kansa juriya kawai yake irin ta maza amman ya ji zafin mutuwar yayansa, da kuma keta haddi matarsa. Hannu biyu Aminatu ta saka ta dauki ledar furar ta nufi gurin da suke aje ruwa ta dauko kwanon ruwa ta zuba furar ta fara damawa da nono. Daga Inna har Baba kallonta suke, ta ba su baya amman hakan be hana ta jin abunda suke tattaunawa.

“Ko ya rayuwa zata kasancewa Aminatu idan bana raye?”

Baba ya kalleshi da sauri jikinsa yayi mugun sanyi, Aminatu kuma ta juyo ta kalli Inna hawaye na bin fuskarta.

“Rayuwa zata kasance mai wahala Inna, zan zama marar gata marar yanci, dan farinciki da yai saura a rayuwata zai tafi ya bar ni, iskar da zan shaka ma sai na yi kamar na mutu sannan na same ta, Baba dan Allah ka yi mata magana ta daina irin wannan maganar”

Ta karasa tana duban mahaifinta, Baba ya kasa cewa komai domin jikinsa yayi sanyi sosai idonsa har sun cika da hawaye, Inna ta kalleshi tana murmushi ita ma hawayen ne a idonta.

“Yayanka sun fika jarumta Malam”

“Wannan ba maganar Jarumta bace, magana ce marar dadi, kuma da na san abun da zaki fada kenan da ban shigo gidan nan yanzu ba”

Ya karasa yana kai hannunsa aljihu ya ciro wayarsa dake ringing. Ya kara wayar a kunne tare da sallama sai dansa Bashiru ya amsa ta dayan bangaren...

BATURIYA POV.

Tana tsugune gaban murhu tana suyar naman kajin suka ji an kwankwasa gida. Ta kalli danta shi ma ya kalleta.

“Ko Abba ne?”

A take ta daka masa tsawa.

“Ban ce ka daina cewa Abbah ba?”

Sultan yayi saurin rufe bakinsa.

“Daddy”

“Good”

Ta mike tsaye tana mita.

“Wata kila ma yaran nan su Saifu sarakan kwadayi tun da sun ji an soyar abu kamshi ya kawo musu, shiyasa zama irin wannan area ta talakawa sai dole Wallahi”

Ta kai hannu ta bude kofar sai arba tai da kawarta Ramlee, a take ta washe baki, Ramlee ta sakar mata murmushi tana wani irin kamshin turare irin na manyan masu kudi.

“Yau gidanmu?”

“Sai kace ban saba zuwa gidanmu ba”

Ta fada a yayinda Baturiya ta kauce mata ta shigo.

“Ki ce yau na shigo a sa'a kaji ma kuke ci, lallai Faruq yayi abun kai”

Ta fada ta zigar zolaya da bugun ciki tana kallon Baturiya. A take Baturiya da bata shaye rada ta tsire baki tace.

“Kina magana kamar baki san wa nake aure ba, Faruq din ne zai kawo min kaji?”

“Ah gaskiya idan fa yana da shi yana yi”

“Idan yana da shi kika ce, ke dai zauna na kawo miki ruwa”

Baturiya ta mika mata kujerar da take zaune dazun, ita kuma ta karba ta zauna tana karewa gidan kallo kamar bakonta, ko gaisuwar da Sultan yake mata bata ji.

“Baturiya kenan duk kyau nan naki kika kare a gidan nan”

Baturiya ta aje mata ruwan a cup tana fadin.

“To ya iya, kaddara rayuwa ta kawo ni nan”

“Kika dai kawo kanki, ke kika so ai”

“Hmmm Wallahi Ramlee babu irin cin mutunci da ban masa ba, amman yaki ya sake ni”

“Ina ko zai sake ki, tun da be da kudin auro wata, kuma ya san yadda kike da kyau nan kina cika idda wani mai kudi zai aureki”

“Da gudu ma, ni Wallahi ban taba zaton zan yi rayuwa a haka ba, bawan Allah nace masa idan mun yi aure zan cigaba da karatu yace ya yarda zai dauki nauyin komai, sai gashi abincin ma wannan wahala yake mana”

“To miya hana shi?”

“Ai lokacin da na aureshi karatu yake, ni na dauka, yana gama karatu zai samu aiki mu fancama yadda muke so, ashe ashe wahala ce ke kirana, gashi gurin auren ma sauki aka masa tun da auren gida ne, kawaye da muka gama

secondary school a tare daga mai aure wani shege sai mai aiki a guri kaza ni ina nan zaune a wani shegen gidan duk yabi ya rugube, kuma na haya”

Tana kai aya Ramlee ta saka mata dariya.

“Ke kika so Baturiya, tsabar kyau fa Baturiya ake ce miki, gashi manyan mutane suna son farar mace, Wallahi ba ki ga yadda mutumen ya haukace daga ganin hotonki ba”

Baturiya ta nufi namanta ta juya tana fadin.

“Ke ni fa Ramlee duk iskancina ba zan iya zina ba”

“Su kuma manyan mutane ai sun fi son matan aure saboda sun fi Sirri, wasu kuma ba sai kin fada musu cewar kina da aure ba, ki ga abun da be wuce 30-1hour ba an baki kusan 500k ko 300k”

Baturiya ta juyo tana kallonta tana zaro ido.

“Da gaske wai?”

“Wallahi kuwa, ke auren ma ba rufi asiri ba ne a gareki, wanda ta haihu har wani tsoron fadawa maza take ma, kara ma budurwa ace ko dan gaba, amman ke fa? Kuma ko kudi aka ganki da shi za a ce na mijinki ne”

“Tab humm ai sun san bakiri nake aure, shi kansa idan ya gan ni da wannan kudi sai ya tambaya ina a samo”

“Ki ce tallafi ne kika samu, daga nan sai ki kirkiri sana'a ki fara yi, kin ga idan ma wasu sun shigo ba za a zarge ki ba, Wallahi cikin Shekara daya Fee'ah har makka sai kin je, kuma duk abun da kike so zaki siya a duniyar nan”

Baturiya ta dawo kusa da ita ta zauna.

“Amman su wani irin kudin banza ne da su haka?”

“Masu kudi fa aka ce miki Baturiya, kina irin wannan area ko'ina kwata ai dole ki yi mamaki, da zaki yarda zan hada ki manya manyan yan kasuwa da yan siyasa, kuma ba haka nan ake zuwa musu ba ai, sai an gyara ki an shirya, ta yadda zai ji kamar be taba kusantar wata mace ba”

“To shi zunubin zaki daukar min?”

Baturiya tai mata tambayar rainin wayo. Sai Ramlee tai murmushi tana mikewa tsaye.

“Baki ji matsi ba ne yarinya, kin san da Allah kika chat da maza a facebook? Har kina haduwa da su kina karbar kudinsu”

“Wannan ai dabam, ban aikata ba sai dai na yi musu dadin baki”

“To yayi kyau ki cigaba”

Ta saka hannunta a jaka ta ciro 10k ta mikawa Sulta.

“Sultan a siye minti ka ji, ni bari a dauki naman tun da ba za a min ta yi ba”

Ta karasa gurin naman ta saka hannu ta dauka ta kai bakinta, Baturiya ta yi murmushi.

“To ai ke dince kika dauke min hankali ”

Bata sake ce mata komai ba ta nufi kofa, Baturiya sai kallo tsadadden lace dinta take, sai da ta fita sannan ta juyo.

“Ni baki ma fada min ina kika samu nama ba, ko wani aka yaudara”

“Wannan karon roka na yi”

“Uhm wata rana dai zasu roki abun da baki so”

“Ai da zarar na ga mutum da ruwan haka, sai na zubar da shi na kama wani”

Ramlee ta yi dariya ta juya ta kama Hanya Baturiya kuma ta rufe gidan ta nufo gurin yaronta Sultan ta karbe kudin da Ramlee ta bashi.

“Karka fadawa Daddy ka ji?”

“Toh”

Ya amsa ta yana kai hannu ya dauki cinyar kaza. Sai bayansa sallah isha'i Faruq ya shigo gidan, ba laifi ya samu masu haske har ya hada 500, tun da ya ji kofar gidan a bude ya tabbatar matarsa na cikin nishadi, domin idan tana jin rashin mutunci wani lokacin rufe gida take saboda yai ta wahalar kwankwasa a waje.
Bayan ya shigo ya maida kofar gidan ya rufe, kamin ya karasa falon ya so ma jin waka ya tashi, ko kwankwato babu matarsa na cikin nishadi a yau. Sallama yai ya shiga ta amsa masa kamar ba ita ba.

“Sannu da zuwa”

Ya dan tsaya kallonta kamin ya amsa.

“Yauwa, ya gidan”

“Alhamdulillah”

Ya zauna saman kujera yana kallonta.

“Mun samu wani abu ne kike ta nishadi haka?”

‘Tun da a sanadinka aka samu ai za a sammaka’

Ta fada a ranta a fili kuma sai ta mike tsaye tana fadin.

“Uhm wasu yan kudi ne na samu shi ne na siyo kaji na soya mana”

Daki ta shiga ta debo masa a platecikin wanda ta soya ta kawo masa ta aje a gabansa.

“Ina kika samu kudi?”

Ya tambaya yana kallon naman da zai rabin kaza.

“Allah ya ba ni”

Ta amsa masa bayan ta zauna.

“Haka kawai Allah zai baki kudi daga sama ba ta dalilin wani ba?”

“Allah ne ya ba ni”

“Ki dauke namanki, ki kawo min abinci, ba zan ci abun da ban san inda aka samo shi ba”

“Matsalar talaka kenan ai, ga talauci ga girman kai, yaushe rabon da mu ci nama a gidan nan?”

“Ba mu kadai ne a cikin wannan halin ba Rafi'ah, mutane da yawa suna ciki, mutane da yawa a da da kika san suna ci uku a wuni wssu yanzu biyu suke wasu daya, amman idan muka yi hakuri komai zai wuce, na san kina cikin hali Rafi'a, saboda kina ganin yan'uwanki da kawayenki a ciki wadata, hakan ba yana nufin Allah ya manta da ke ba, da ya ga dama da sai ya aura miki wanda yafi kowa kudi a duniya, amman ya jarrabaki miyasa ba zaki yi hakuri ba?”

“Faruq kenan, yanzu duk hakurin da na yi na shekara biyar baka gani ba?”

“Kin yi hakuri na sani, amman fadar sirrin gidana yafi komai yi min ciwo, idan na ci ko ban ci ba wani ya sani abun na min ciwo, bana son ki fada wani hali saboda halin da muke ciki dan Allah ki yi hakuri”

“Ai dole kace na yi hakuri kam, ban da hakuri me kake da shi da zaka ba ni Faruq? Yanzu dan na samu kudi na siye nama na ci ya zama laifi? Ka san ina da ciki ina kwadayin abubuwa amman kai zargina ma kake, ni wannan cikin ma zubar da shi zan yi Wallahi, dan ba zan haihu ba ka yanka min bunzuru, wata kila ma ba zaka yanka min komai ba ka bar ni kyari da ido kamar kwaruru baki salab kamar Salamatu ina kallon yan barka ayi ta mana tsigumi”

“Allah da yai masu kudi be manta da ni ba Rafi'a, ban san wace irin macece ke ba, idan na fita waje ina cikin damuwa da bakinciki a maimakon idan na dawo gida na samu nishadi sai na tarar bakinciki gida yafi na waje yawa, har fargabar shigowa nake”

“To ka sake ni mana, ko zama da ni dole ne? Kai wai kana ganin Allah ba zai hukuntaka yadda kake azabbatar da mu da yunwa?”

“Kika sake furta wata magana sai na mareki Wallahi”

Ya fada cikin bacin rai, da muryar dake nuna da gaske yake. Ganin hakan yasa dole tai shiru domin ta san halinsa idan ya fusata be iya ba.

TALBA POV.

Zaune yake saman carpet yaran na zagaye da shi, sai kallonsu yake yana murmushin. Farincikin yara musamman marayu na daga cikin abunda yafi komai faranta masa rai, hakan ne yasa shi bude gidan marayu, kuma yana kai ziyara lokaci zuwa lokaci, wani lokacin kuma yana zuwa gurin ya wuni tare da su, ko ya dauke su ya fita da su zuwa gurin shakatawa.
Ya kalli agogon hannunsa sannan ya daga yarinya dake cinyarsa da bata wuce 5 years ba ya mike tsaye. Sai yaran ma suka mike tsaye suka bi bayansa har zuwa gurin motarsa, ya saba musu idan zai tafi yana raba musu kudi ko alawa wani lokacin kuma chocolate. Sai da ya shiga cikin motar sannan ya mika hannunsa baya ya dauko ledar sweet ya bude ya fara raba musu, hannu biyu suke sakawa suna karba kamar yadda ya koyar da su, hayaniyar yaran yasa Ali dake driver side ya bude ya fita yana waya. Da dai daya Talba ya bisu yana basu, idan ledar ta kare sai ya bude wata, har sai da ya raba musu duka sweet din da ya zo da shi, sannan ya kwantar da kujerar motarsa ya kwanta yana jiran Ali dake waje yana waya.
Bayan Ali ya kare ya dawo cikin motar ya rufe yana kallon abokinsa.

“Ka gama da su?”

Talba ya kalleshi kamar be ji abun da ya tambaya ba.

“Har yanzu tunanin abun da kai ma Leila kake yi?”

“Saboda Daddy da Momy na yi, kuma zan cigaba da yin hakan matukar hakan zai faranta musu rai”

Yana rufe baki sakon Leila ya shigo wayarsa.

“Ka zo ka kai ni shopping yanzu”

Ya dauke idonsa bayan ya gama karantawa.

“Leila tana ganin hakan ba zai saka na tsane ta ba? Ina son girmamawa Ali, ai ya kamata tace Yallabai, but look how she text me kamar wani direbanta”

“Tana da gaskiya, ya kamata ka koyi girmama mace”

“Ba macen da take kasa da ni ba, wannan ranar ba zata taba zuwa ba, ba zan taba zama wawa akan mace ba, sauke ni gida”

Ali yayi murmushi yayi ma motar key, har suka isa gidan idon Talba a rufe, hannyensa kuma rumgume a kirji. Harabar gidan Ali yai farkin Talba be ce masa komai ba ya bude motar ya fita ya nufi kofar falon, kananan kaya ne a jikinsa, sai kamshin turare yake. Yana isa ya danna door bell din ya tsaya jikin kofar, cikin kankan lokaci aka bude masa kofar domin yanayin yadda yake danna door bell din dabam ne, da yasa ake gane shi ne. Dagowa yai a hankali ya kalli Baaba wanda ta bude masa kofar hawaye na sauko mata. Dan fuskar Mama yai domin ta saba idan ta bude masa zata masa sannu da zuwa angona, sai yai mata murmushi ranar da yan kwarai suke a kai kuma zai soma taba wasa da ita ko ya amsa mata. Shigowa yai cikin falon yana kallon Leila dake tsaye kusa da sofa ranta a bace, sai kuma ya juyo ya kalli Baaba.

“Miya faru?”

“Babu komai ranka ya dade”

Baaba ta amsa masa sannan ta fara tafiya. Binta yai da kallo kamin ya maida dubansa gurin Amal dake tsaye upstairs tana zayyana masa abun da ya faru.

“Ya Leila ce ta mareta”

Talba ta kalli Leila.

“Baaba ta ho dan Allah”

Baaba ta juyo ta dawo kusa da shi ta tsaya cikin damuwa.

“Bata hakuri”

Talba ya fada yana kallon Leila, wani irin kallon mamaki tai masa, Momy na jin haka ta fito daga kitchen.

“Ita fa tai min laifi”

“Kin sani sarai bana maimaita kalma”

“Baka san abun da ya faru ba”

“Bana son na sani”

Ya fada yana matsawa kusa da ita, kana kallon cikin idonsa ka san ransa ya bace. Sai da ta kalli Momy sannan ta kalli Baaba ta ce.

“Ki yi hakuri”

“Babu komai ya wuce”

Baaba ta fada sannan ta nufi kofar fita falon zuwa BQ inda dakinta yake. Sai da ta fice sannan Momy ta karaso inda Talba yake tsaye tana fadin.

“Wannan be kamata ba sam, taya zaka wulakanta yar'uwarka a gaban yar aikin?”

“Be kamata ta dauki hannu ta mareta ba Momy, no matter what Baaba tai mata, ta yi jika da ita”

“Gaskiya ka ci mutunci Leila, ka tauye mata hakki Talba, na yi shiru ne kawai saboda bana son na yi magana a gaban Baaba”

“Kin san inda na fito Momy? Gidan marayuna, yaran da suke can basu da uwa ba su da uba, wasu ma a titi aka dauko su aka kawo su nan, wasu kuma danginsu basa iya kula da su, amman Leila Allah ya ba ta komai, kudi, uwa, uba, ilmi, dukiya, sai dan na saka ta ba da hakuri ne zai zama cin mutunci?”

“Wannan kuma ai dabam ne, akwai tazara mai fadi mai tsawo tsakanin mai kudi da talaka, akwai abun da be kamata ayi agabansu ba, ko kuma a saka ayi musu, musamman inda muke da gaskiya”

“Wannan zarar da kike magana, ban tana ganinta ba, kuma ba zan taba ganinta ba, ban taba jin na fi wani dan yana talaka ina da arziki ba, sai dai na ji nafi shi saboda yana kasa da ni a aiki ko a shekaru, ko kuma saboda ni ina miji ita tana mata, amman ba zan taba iya cin mutuncin wanda ya haife ni ba, wasu talakawan sun fi mu a gurin Allah”

Yana gama fadar hakan ya nufi kofar fita a fusace. Momy ta bishi da kallo tana kada kai.

“Finally, gatan Daddynka ya saka har ni kana iya tsayawa ka fadawa magana... ”

Be juyo ba dan be ji akwai abun da zai sake ce mata. Balle kuma ta kuma ya kula Amal dake zayyana masa abun da ya faru daga can inda take tsaye.

“Ya Leila ce ta kawo mata ruwa shi ne, gurin mika mata carpet ya tadeta ruwan ya zuba a jikin Ya Leila sai ta mareta...Shi ne abun da ya faru Ya Talba ko baka tsaya ba na fada maka, Ya Leila ce bata da gaskiya”

Ta karasa ita da Leila suna watsawa juna harara, daman can haka suke kamar ba yan'uwa ba, basa shan inuwa daya.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata. Akwai dan wata bakwai, muna da kwalli mai karfin gaske (Mujarrabun sadidan) Akwai na farin jini for yan mata da Zaurawa. Akwai wanda ba a bawa mai kishiya, akwai na mazajen da kr neman mata, muna da rantse baki da kishiya, muna da back to virgin, for yan matan da kaddara ta fadawa, ko Zaurawan dake son zama yan mata, akwai jigida mai kyau, muna da man ayu 100% natural. Akwai na maza masu hannun Dambe.
Hajiya sai n gwada akan san na kwarai, ba cuta ba cutarwa, duk wanda kika siya sai kin dawo.

Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers Please idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Bayan Baba ya sauke wayar ya kalli Inna cikin yanayin damuwa yace.

“Bashiru ne yake mana maganar komawar mu can”

Inna ta girgiza kai.

“Babu inda zanje, ba a tserewa mutuwa a ko'ina take”

“Na san da haka amman dai ya kamata mu bar garin nan saboda ance akwai yiyuwar su dawo, kuma kina gani kullum mutane barin garin nan suke”

“Babu inda zanje Malam, na fi son mutuwata ta same ni a inda nake”

“Ai kaji matsalarki kenan, shi kansa abun da yake ta magana kenan a lallaba masa ke”

Inna bata sake cewa komai ba, har Baba ya ci ya shude. Duk abun da suke Aminatu na dama furar tana saurarensu, bayan ta gama ta kawo ma Inna ta zauna kusa da ita ta fara bata a hankali tana sha, Inna bata hana Aminatu shayar da ita ba, duk kuwa da kasancewar zata iya sha da kanta. Sai da ta tabbatar ta koshi sannan ta rufe furar ta koma gurin girkin da take. Har ta girka ta gama bata cikin walwala da sakewar zuciya, ba na rashin yan'uwa ba, na tunanin kalaman da Inna tai mata? Ta ya zata rayu babu Inna? A hannu waye zata zauna ma? Ba ita kadai ba Baba ma ya zai ji idan suka wayi gari babu Inna? Ko da ace tana da aure rayuwa ba zata taba mata dadi babu uwa ba, balle kuma a yanzu da take tare da ita, Saurayinta Maniru ma yana cikin mutanen da yan bindigar suka kashe, bayan ta gama ta zubawa Baba nasa ta zubawa Isah a inda ake saka masa sannan ta kwashe sauran a Samira babba, ta debi ruwa ta shiga bandaki. Sai da ta cire komai na jikinta sannan ta zauna saman dutsen da suke zama idan zasu yi wanka ta fashe da kuka.
Kuka tai sosai sannan tai wanka ta fito idonta a kumbure, ta dora alwala ta shiga dakinsu tai sallah, bayan ta gama ta d hannayenta sama tana rokon Allah.

“Ba ni da gata sai naka Allah, ka dauke yan'uwana a lokacin da ka so, ka sauya rayuwata zuwa yadda ka kaddara min, Allah ka yafe min ka jikan yan'uwana, ka ba mahaifiyata lafiya ka bar ni da ita Allah”

Ta karasa hawaye na sauko mata, sannan ta shafa addu'ar ta mike tsaye, ta fito waje, sai da ta zuba ma Inna ruwa a buta sannan ta rika ta, ta kaita bandaki bayan ta fito ta taimaka mata tai alwala sannan ta shimfida mata abun sallah.

“Allah ya miki albarka Auta”

Inna ta fada tana kokarin gyara zamanta, domin a zaune take sallah a yanzu. Aminatu ta kalleta kamar ba zata ce komai ba sai kuma ta amsa.

“Ameen”

Ta mike tsaye.

“Bari naje na yi itace yamma ta yi”

Kai kawai Inna ta daga mata, ita kuma ta shiga dakin ta dauko hijabinta ta saka ta ta dauki zaren da take daure itacen idan ta yi, sannan ta saka talkaminta ta fice, ba ita kadai ba kusan duk yan matan garin da ma matan aure suna zuwa daji ne su yi kara da yamma saboda dafa abinci, abu ne mai wahala ka ga gidan da ake siyen itace a yanki, yawanci duk a daji suke yin kara.
A da ta saba idan zata tafi yin kara akan biyo mata ko kuma ita ta biyawa wasu, sai dai tun bayan da aka tarwatsa rabin garin take tafiya ita kadai, saboda an tafi da wasu yan mata, wasu kuma sun yi gudun hijira, sauran da suka rage kadan ne. A gurin da ta saba tsayawa ta tsaya ta shimfida zanen sannan ta aje zaren a gefe, kana ta shiga tsintar karan, tana yi tana tuna yadda suke yi a da, ita da kawayenta, har tigengen suke cikin nishadi da walwala, sabanin yanzu da suka bar ta da kewa.
Sai da tai rabin sannan ta samu kanta da mugun faduwar gaba, marar misaltuwa, a take ta nade wanda ta tara a daure ta dauka ta nufo gida da gudunta, kowa sai kallonta yake, kamin ta iso har hawaye ya fara sauko mata, bakin kofa ta jefar da karan ta rugo da gudun gurin Inna da ke kwance tana bachi ta taba ta.

“Inna...Inna.... Inn”

Bata karasa ba, Inna ta bude idonta da sauri tana kallonta.

“Lafiya Auta?”

Sai ta fashe da kuka, wanda hakan yasa Inna ta tashi zaune.

“Tsoro nake ji Inna, gabana faduwa yake”

“Tsoron me? Miya faru?”

“Ban san ni ba, bana son na yi nisa da ke”

“Auta kenan, kin isa ki tare min mutuwa ne? Da wani na tarewa wani mutuwa ai da na tarewa Yayana, kin san babu uwar da za a kashewa yaya a gabanta kuma ta kyale alhalin tana da ikon yin wani abu?”

Maganar da Inna tai ya isa ya tabbatar da cewar ta fi jin bakincikin kashe mata yaya da akai fiye da keta mata haddi da aka yi. Aminatu ta yi kasa da kanta tana kuka sosai.

“Kina kuka da wuri, ki adana kukanki saboda gaba”

Ta kalleta.

“Miyasa kike min fatan kuka Inna?”

“Saboda zaki yi kuka mai yawa Aminatu, dole zaki yi kuka, ranar da zaki bude ido babu ni, ranar da zaki ga wata uwar idan kika tuna da taki dole ki yi kuka, ranar da kika ga wasu yan'uwa kika tuna da naki dole ki yi kuka, ranar da kika nemi wani abu kika rasa dole ki yi kuka, ni na riga na gama tawa rayuwar har na yi jikoki kuma na yi Auta, ke kuma yanzu rayuwarki take kan ginuwa, ta fara miki a

haka, me kika tsammani a gaba? Dadi? Dadin yana tafe bayan wuya amman, yanzu na fi tausayin rayuwarki fiye da ta kowa Aminatu”

Ta share hawayenta, ta kara matsawa kusa da Inna ta kwanta jikinta, ta lumshe ido, tana maida numfashi a hankali.

“Allah ga yata, Allah ka zame mata gata”

Inna ta fada a ranta hawaye na sauko mata, ba tana kalamai ba ne domin ta daga mata hankali, a a har ga Allah tana fadin abun da take jin ya kusa tabbatuwa a gareta ne, kuma tana jin nata mai kiran ya kusa kiranta, jikinta da mafarkanta suna bata haka, domin tana jin wani kalar yanayi na dabam a jikinta wanda bata taba jin irinsa ba, sai dai a kusa? Ko a nesa? Yau ko anjima? Shi ne abun da bata da tabbaci.
Bayan sallah Magariba, Baba da Isah suna daki sun saka Inna a gaba suna ta kokarin convinced din Inna akan ta amince da magabar Bashiru su ma su yi hijira su bar garin amman ta ki, Aminatu kam tana zaune waje sai kallon hadarin dake haduwa take, ita kanta bata san na yi ba, tafiyar ko zaman? Inna tana da gaskiya idan sun tafi ba za su tserewa mutuwa ba, sai dai barin garin zai taimaka Inna ta manta wata damuwar, domin a cikin abubuwan da suke bata mata rai har da zaman gidan da take ganin an kashe yayanta kuma tana ganin a kowa ne dare kamar za su shigo ne su yi mata sallama kamar yadda suka saba, yadda rayuwa take a baya.
Sai da akai kiran sallah isha'i sannan Baba da Isah suka fito waje, sukai alwala suka yi haramar zuwa masallacin.

TALBA POV.

Ya kusan minti ashirin a cikin motar sannan ta fito, kamin ta bude motar ta shiga ma wani aiki ne, ba karamin kufula shi tai ba, domin ya tsani jira ya tsani a bata matsa lokaci.
Sai dai ko kadan be nuna mata ransa ya bace ba, ya ja motar suka fita fuskarsa ba yabo ba fallasa.
Mai gadin be yarda ya tsaya jiran sai Talba ya danna horn sannan ya bude masa ba, tun a lokacin da ya ga ya shiga motar yai hanzari bude gate din ya tsaya, be bar gurin ba har sai da motar Talba ta fice daga gidan.
Be kalli inda take ba, tukinsa kawai yake yana sauraren fm din dake gabatar da wani program, sai dai ita lokaci zuwa lokaci tana satar kallonsa, duk kuwa da kasancewar bata son su hada ido gudun kar ya ga tana kallonsa.
A hankali ta sauke ajiyar zuciya ta lumshe ido ta bude ta maida dubanta gurin titi, ya zata yi ta canja Talba? Shine tambayar da ta zo mata a rai, gata a mota daya da shi amman baya nuna mata wata alamar kauna, Baya ma son kallon inda take kamar ba masoyinta ba.

“Na fasa zuwa shopping din take me home”

Sai a lokacin ya kalleta tare da kiran sunanta.

“Leila...”

Ta kalleshi Irin duban nan na fusata, sai dai kwarjininsa ya hanata nuna masa fushinta.

“I'm not your driver, and this should be the last time da zaki umarce akan wani abu”

“Amman ni dazun ka cilasta ni na bawa Baaba hakuri bayan kuma bata cancanci haka ba”

Ta fada idonta na cika da kwalla.

“Me ka dauke ni ne Talba? Baiwa?”

Be amsa ta ba, ya juya motar zuwa gida, kamin su isa hawaye da ya wanke mata fuska ya fi a kirga, yana yin farkin ta bude motar ta fita tana share hawayenta. Sai a lokacin ya juyo da fuskarsa yana kallonta har ta danna door bell din aka bude mata ta shige, sannan ya maida dubansa gurin Daddy dake tsaye jikin motarsa yana magana da Momy da gaba daya hankalinsu yake kan Talba. Bude motar yai ya fito ya rufe ya nufi gurin da Daddy yake tsaye yana wata irin tafiya kamar baya son taka kasa, kamin ya karasa ya zuba hannayensa aljihu kana ya sadda kansa kasa.

“Ranka ya dade baka burge ni ba, da baka tura Leila gida gurin Gwaggo ba”

Daddy ya fada yana kallon dansa, sai Talba ya kalli Daddy, kamin ya maida dubansa gurin Momy wanda hakan kr tabbatar masa da cewar Momy ta fadawa Daddy abun da yai ma Leila kenan.

“Momy ba zamu iya yin abu a tsakaninmu ba har sai Daddy ya ji?”

“Yes, ya kamata ya ji ne, saboda kana kokarin wuce guri”

“Just because...”

“It's just because? Tun ba yau ba Talba kana treating Leila kamar ba yar gidan nan ba, ya kamata ka sani ita ma tana da right fa!”

“Miyasa karamin Abu zai bata miki rai Momy?”

“Kai kaja komai, wacan yar aikin ma dana kora saboda kai na koreta Talba, saboda kana nuna kamar ta fi Leila gata a gidan nan, and now kana son na kori Baaba ko? Ka cigaba”

Tana kaiwa nan ta nufi hanyar da zata sadata da bangarenta, daga Daddy har Talba kallonta suke har ta shige, sannan Daddy Talba ya ce.

“Ka saba da halin Momy ka ba tun yau ba, kar hakan ya dame ka”

Talba yayi murmushi.

“Daddy fita zaka yi?”

“Yeah zan je gaisuwar Galadima ne”

“Lemme drive you”

“No tare da direba zamu je, go and rest”

Murmushi ya sake yi ya dan ja baya, ya budewa Daddy motar sai Daddy ya shiga yana fadin.

“Ance an kai hari Galadi, ya kamata A shirya wani abu a kai musu, mutanen nan suna cikin matsi”

“Inshallah Daddy, ban ji ba two days ban duba news ba”

“Sai na dawo”

“Allah ya kiyaye”

Ya fada yana rufe masa motar, sannan yaja ya tsaya har sai da driver ya ja motar Daddy suka fice daga gidan. Sannan ya nufi bangarensa, daga shi har Faruq da part dinsa yake kusa da nasa a kasa dakunansu suke, tsabanin bangaren Daddy da Momy da akai yi ma upstairs.
Dakin da yake aje tardunsa ya nufa ya bude ya shiga cikin natsuwa ya zauna a kujera ya bude system dinsa ya cigaba da wani aikin da be karasa ba, be bar dakin ba sai kusan 6pm.
Freezer ya nufa ya bude ya dauko ruwa ya zuba a cup ya surka da wasu sannan ya sha, bayan ya ajr cup din ya nufo kofar fita yana duba agogon hannunsa. Kai tsaye bangaren Momy ya nufa domin ya san izuwa yanzu ta huce fushin da take. Door bell din ya danna, yana dauke hannunsa Amal ta bude masa da sauri hawaye na sauko mata.

“Lil Sis?”

“Na'am?”

“Me ya same ki?”

Ya tambaya a yayinda ya saka kafarsa cikin falon yana dubanta.

“Baaba ce...”

Sai kuma tai shiru, shi dai kallonta kawai yake, as she knows ba zai sake tambayarta ba sai ta soma labarta.

“Tana mopping sai ruwa ya zame ta ta fado...”

Wani irin kallo tsoro yai mata.

“Ta fado ina?”

“Daga sama ta fado kasa!”

“You're kidding me”

“No Wallahi da gaske nake”

“Ina take? Ta ji ciwo?”

“Momy ta dauke ta sun tafi asibiti tare da Ya Leila tun dazu ba su dawo ba”

“Yaushe abun ya faru?”

“Lokacin da Daddy ya fita”

Ya juya da sauri ya fita zuwa bangarensa domin a can ya baro wayarsa, yana shiga ya koma dakin karatunsa ya dauki wayar ya kira Momy, ringing tai sai da ta kusa tsinkewa sannan ta daga.

“Momy kuna ina?”

“Gamu hanyar dawowa gida”

“Ina Baaba?”

Dan Jimm Momy tai kamin ta amsa masa.

“Yaranta sun zo sun dauketa, sun tafi da ita, daman ciwon ba sosai ba ne”

“Amman...”

Be karasa ya lumshe idonsa sosai jin Momy ta katse wayar, hakan nan jikinsa ya ba shi kamar ba iya haka ba ne. Idan har ba babban abu ba ne, babu yadda za ayi Momy ta kaita asibiti da kanta, kuma har Leila ta bi ta su tafi tare.

AMINATU POV.

Tun safe take ta wanke tufafin Baba da nata har kusan daya da tabi, abun ka da marar aiki da kuzari, bata da kuiyar aiki kam amman bata da sauri, sai wuni ta kwana tana abu daya.
Bayan ta wanke su fes ta matse ya daurewa ta soma sha shayawa, sannan ta bi tana kwashe wadanda ta shanya da farko suka bushe tana ninkewa, sai ta dora akai da haka har ta gama kwashe ta kai su daki, sannan ta fito ta shanya sauran. Ta dauke kayan da tai aikin da su cike da gajiya ta aje a inda suka saba ajewa.

“Inna tashi ki yi sallah”

Ta fada tana doso dakin, har zata shiga sai kuma ta juya ta dauki butar Inna ta cika da ruwa sannan ta nufo dakin, bata sake ce ma Inna komai ba har sai da jera tufafin Baba a inda ta saba saka masa sannan ta nufo inda Inna take zaune ta sadda kai kasa ta.

“Inna...”

Jin bata amsa ba yasa ta risina a hankali ta leketa, sai ta ga idonta a rufe, da sauri ta taba ta abunka da wanda yai nisan bachi sai ta zabura da karfi ta bude ido, da wanin irin karfi Aminatu ta hade yawu ta sauke ajiyar zuciya.

“Inna anyi sallah, yi hakuri na tashe ki da karfi tsoro na ke ji”

Sai Inna tai mata murmushi, sannan ta fara yunkurin tashi Aminatu ta kama ta ta mike tsaye, da taimakon Auta ta fito waje ta shiga bandakin, bayan ta fito ta rika mata butar tai alwala, sannan shimfida mata tabarma da abun sallah ta dauko mata hijabi.

“Allah ya miki albarka”

“Amin”

Ta amsa tana kokarin rikata ta zaunar da ita, domin a zaune take sallah, saboda bata iya dadewa a tsaye. Sai da Inna ta fara sallah sannan ta dauki butar ta shiga bandaki bayan ta fito tai alwala ta zo kusa da Inna ta yi sallah, babu komai a cikin addu'ar sai nemawa Inna lafiya, domin shi ne abun da yafi komai tsaya mata a rai a yanzu.

Kamar kullum bayan ta gama ta dora girki, sannan ta matsawa Inna furarta ta jiya ta bata. Baba be shigo ba sai bayan sallah isha'i.

“Sannu da zuwa Baba”

“Yauwa”

Ya amsa yana sauke gajiya, kamar wanda ya wuni yana aiki, daman can haka yake tun da tsufa ya kama dan abu kadan sai gajiya ta tarar masa. Aminatu ta tashi da sauri ta dauko masa abinci da ruwa ta aje masa.

“Allah ya miki albarka”

“Amin Baba”

Ta amsa tana jindadi albarka da suke yawan saka mata, ta san ko ba yau ba wata rana albarka nan zata bita.

“Baba na wanke kayanka fes na ninke maka”

“Eyeee Auta gayyar aiki, Allah kara miki albarka yar Baba”

“Amin”

Ta amsa tana murmushin data manta rabon da ya ziyarci kumatunta, Inna ma murmushin take tana kai hannu ta rage hasken fitilar dake kusa da ita.

“Yau da wuri za'ayi bachi ko? Dan a san akwai gajiya”

Cewar Inna tana kallon Aminatu, fuskarsa sai haske take duk da kasancewar dare ne, sai dai dan hasken farin wata daya haska ta da kuma fitilar dake kusa da ita yasa duk wanda ya kalleta zai yi arba da yadda fuskarta take ta haiba.

“Jikina yau Alhamdulillah ji nake kamar ba ni ba”

Baba yayi murmushi yana kallon Aminatu wanda ita ma murmushin take.

“Ai na ga alama ga annuri nan a fuskarki”

Ta sake fadada fuskarta da murmushi tana amsa sallamar da Isah yai, kusa da Baba ya zauna sannan ya aje mata ledar yalo a gabanta.

“Ga tsarabar kasuwa”

“Allah ya maka albarka”

“Amin”

Ya fada kamin ya dora da amsa tambayar da Baba yake masa.

“Wallahi kasuwa Baba taki ta koma kamar da, kowa a tsorace yake, saboda ana ganin mutanen nan kamar za su iya dawowa, kasan idan suka saka gari agaba sai sun ga bayansa, musamman garin da da suke da dade suna dafafe, tun da ba a taba shigo mana ba sai yanzu, gashi daman yan saka kai na yankin nan sun sha kashe mutane suna da haushin garin nan sosai”

“Allah dai ya tsare, abun da Bashiru yake ta ce min kenan kullum, ga shi tsohuwar ta ku ta ki yarda mu bar nan”

Cewar Baba.

“Ku bar ni na mutu inda uwaye na da kakanina suka mutu, ai ba a tsirewa mutuwa”

“Amman inna idan mu ka bar garin nan ke kanki hankalinki zai fi kwanciya fiye da nan”

Amina ta fada, a karon farko kenan da ta saka bakinta a maganar. Sai Inna ta girgiza kai.

“Babu inda zanje, kina ganina ko tafiya bana iyawa miya rage min Allah na tuba”

“Mai ciwo da mai lafiya, duk daya ne a gurin Allah, sai kaga mutuwar ta dauke mai lafiya ta bar mai ciwo ai”

Ta daga ma Baba hannu.

“Dan Allah ku daina min maganar nan, ni ban hana ku tafiya ba, amman ni kam ba zan bar garin nan ba”

“Allah ya kyauta”

Duk suka amsa da Amin har ita. Ko da goma tai duk sun kwanta Inna da Aminatu suna daki, Isah da Baba kuma suna waje saboda garin akwai alamun hadari hakan yasa zafi ya tsananta, sai dai hakan be saka Inna fitowa ta kwanta waje, Aminatu kuma duk inda Inna take tana nan. Kowa yayi bachi ban da Aminatu dake ta tunanin abubuwa da dama ciki har da wasikar ta ta karshe da ta bawa Maniru shi ma ya bata, babu yadda be yi ba akan yana son tai masa iso gurin iyayenta ta hana shi saboda tana jin tsoro, ashe ba rabon gaisuwa da shiga tsakaninsa da iyayenta. Sai a yanzu take jin zafin mutuwarsa, kuma take ganin laifin kanta na hana shi ganin Babanta da tai. Ba shiri tai firgigit ta tashi zaune

sakamakon kara bindigar da taji, a da can yan saka na yanki su kan harba bindiga idan dare yai, shi ma kuma ba kullum ba, sai dai tun bayan harin da aka kawo musu aka kashe wasu wasu suka tarwatse sai aka daina harbawar, ba ta hadda karar wacan bindigar da kuma ta yan ta'adda ba, balle ta iya banbanci ta su da kuma ta yan sa kai, sai dai yanayin yadda take ta jin tashin bindigar babu kakkautawa yasa hankalinta ya tashi sosai.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Daga waje ta ji muryar Baba yana neman agajin Allah. Kamin su soma jiyo hayaniyar mutane da alama gudu tsiratar da rai suke, Baba ya shiga dakin da sauri ya haske fitilarsa ya bude inda yake ajiyar kudi ya kwashe su ya saka aljihu.

“Aminatu rikata tashi mu tafi yan ta'adda ne”

Kamar an zare mata lakka haka Inna ta ji, sai jikinta ya kara nauyi, Aminatu ta shiga kokarin rikata da sauri amman ta kasa.

“Tu tafi Malam, ku gudu ko dan saboda Aminatu”

Aminatu ta girgiza mata kai da sauri tana kuka.

“Ba zan tafi na barki ba Inna...”

Ta shiga kama Inna da dukan karfinta tana jin kamar ace tana da karfin da sata iya daukarta ta dora akai, sai gashi tsaye ma ta kasa mikar da ita sai da Baba ta rika mata dayan bangaren, sun mikewa tsaye suka ji harbin kamar a bayan dakinsu, wani kuma a cikin gidansu.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Baba ya fada yana sako fitsari a wando sai kuma ya fara rawa yana tsalle kamar wanda ya tabu.

“Allah ka batar da ni, Allah ka batar da ni kar su gan ni”

A take cikinsa ya murda sai zawo, abun ka da mai tsoro sai yai cikin tufafinsa na sakawa ya tura kansa sauran jikin a waje, ga wandonsa sharkat da zawo da fitsari. Inna kam gaba daya hankalinta yana gurin Aminatu. Da hannu ta nunawa Aminatu karkashin gadon karfi alamar ta shiga domin bata ko ina magana. Da gudu Aminatu ta nufi karkashin gadon kamin ta karasa shigewa suka shigo dakin rike da magayen makamai, ga wata uwar fitila mai dan karen haske da suke haska ko'ina da ita kamar gulub. Dayan ya turo Isah cikin dakin da karfi, sannan ya karasa karkashin gado ya daga daga katifar ya jefar can gefe, sai ga Aminatu dunkule.

“Fito ko na halbe ki”

Dayan ya fada, da Aminatu ake sai dai tsabar tsoro yasa Baba ya ji kamar da shi ake, sai ya cire kansa cikin jakar kayan ya rarafo kusa da Isah yana ta kuka da karanta addur'ar da ta zo masa.

“Yanarukuna bardan wassalamu ala ibrahim”

Daga nan ya dora ta ayatul kursiyu, kamin su daka masa tsawa ya kama bakin ya rike jikinsa ta ko'ina rawa yake. Wani irin rawa jikin Aminatu yake tana ganin komai kamar ba gaske ba, yadda take fita da shigar da numfashinta kadai ya isa ya bayyana irin tsoron da take ji.

“Dan Allah karku taba ta, ku kashe ni ita ku kyale ta”

Inna ta fada, sai dayan ya saka bakin bindigarsa ya buga mata a kai, take gurin ya fara zubar da jini.

“A kyale ta ita tafi sauran yaya ne? Kuna son ta kuka ja mata masifa ba kuri kuke ku kuna da jarumai a gari ba? Yayanka sai kashe mu suke duk inda suka ga bahillace sai ku kashe shi, Wallahi yau ko wa ba mu bari garin nan”

Cewar wani tsukaken a cikinsu yana rike da ak47. Ko kamin ya karasa maganar har wani ya fara yaga tufafin Aminatu, a take ta fashe da kuka tana kiran sunan Inna tana jin kamar ace Inna ko Baba wani zai iya taimakonta.

“Dan Allah ku kashe ni, ba zan iya ganin wannan abun ba...”

Inna ta fada a rikece tana kallon Aminatu take ta kuka suna kokarin rabata da zanenta.

“Kai bata giďa”

Wani ya fada a take na kusa da kofa ya dauke ta da bindiga har harbi hudu. Wani irin ihu Aminatu ta saka jikinta na rawa idonta kamar zai zubo tana kallon gawar Inna dake kwance tana zubar da jini ido a bude, tassss wani ya dauke ta da mare wanda ya saka ta a take ta manta inda take, duniya ko lahira? Ba suma tai ma, sai dai jinta yayi karanci kamar yadda idonta suke ganin haske wutar marin da akai mata, sai dai ko kadan hankalinta be yi nisa da jikinta ba.

“Bar shi ya fara yi”

Dayan ya fada yana nuna Baba da ke jiran ace masa mutu ya mutu. Baba ya kalli Aminatu dake kwance tsirara sai kuma ya kalli mutane kamar be gane yarensu.

“Tashi ka yi aka ce ko mu kashe ka”

“Ya... Ya... Ya...ya.... Ya... Ta ce... Ce.. ”

Daker ya furta, sai dayan ya saka bindigar ya halbe Isah dake gurfane kamar mai neman gafara yana kuka, halbi biyu yai masa a kai.

“Ko ka yi ko mu kashe ka, ina ruwanmu da yarka ce, mu be dame mu ba...”

Aminatu ta runtse idonta da sauri tana jin kamar ta bude ta ganta a wata duniyar...!

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata. Akwai dan wata bakwai, muna da kwalli mai karfin gaske (Mujarrabun sadidan) Akwai na farin jini for yan mata da Zaurawa. Akwai wanda ba a bawa mai kishiya, akwai na mazajen da kr neman mata, muna da rantse baki da kishiya, muna da back to virgin, for yan matan da kaddara ta fadawa, ko Zaurawan dake son zama yan mata, akwai jigida mai kyau, muna da man ayu 100% natural. Akwai na maza masu hannun Dambe.
Hajiya sai n gwada akan san na kwarai, ba cuta ba cutarwa, duk wanda kika siya sai kin dawo.

Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers Please idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -8□

“Mutuwata zata fi min sauki fiye da aikata abun da kuka bukace ni da shi”

Abun da ya fito daga bakin Baba kenan. Wanda hakan ya saka Aminatu bude idonta duk kuwa da kasancewar bata da tabbacin idan ta bude idon zata ga mutane, domin kamin ta rufe idon haske ne kawai take iya gani.
Sai dai kallon be kare mata ma, domin ta yi arba da fuskar mahaifinta da suka haske da katuwar fitila mai haske.

“Kai ba shi giďa”

Idan suka ce aba wa mutum giďa yana nufin a halbe ka, take dayan ya daga bingida da zimmar harbin Baba sai bindigar ta ki tashi. Dayan ya sake daga ma ita ma taki tashi.

“Kaga wani tsohon shige... Sa mai wuka”

Dayan ya fada yana buga masa kan bindigar. Sai biyu suka kama shi suka kwantar da shi, dayan ya saka zabgegiyar wukarsa ya fara gagarawa a wuyan Baba, nan ma wukar bata kama ba.

“Shege, samo dutse yau ba maganin karhe ba ko maganin mutuwa ka kasha sai mun kashe ka”

Ban da kallon Baba babu abun da Aminatu take, ta kasa kuka hawayenta sun kafe, kamar yadda zuciyarta ta wanke tass, kwakwalwarta kuma ta zama fanko babu tunanin komai a ciki. Bata iya jin komai sai kalmar shahadar da Baba ke yi, duk yadda ta so ta kawar da kanta daga kallon yadda suke fasa kan Baba da katon dutse sai ta kasa ko da kwakkwaran motsi. Wani irin sanyi ne marar misaltuwa ya taso mata ya baibaye ilahirin jikinta, sai ta soma jin abu na mata yawo a cikin kai kamar hatsi.

“Baba...”

Ta furta daker tana kallon yadda suka rabe masa kai biyu a cikin dakin mahaifiyarta da suka harbe bayan sun kashe Ya Isah.

“Tashi ki saka tufafinki”

Dayan ya fada, sai ta kalleshi, duk da kasancewar hasken fitilar ba ya iya bari ya ta ga fuskokinsu, ba kuma dan ta fahimci abun da yake fada mata ba, sai dan hasketa da yai da fitila da yai, kana kallon kwayar idonta ka san bata cikin hayyacinta. Dayan ya kai mata mugun shuri a cinyarta.

“Saka tufafinki dan ubanki”

Maimakon ta saka tufafin sai ta juyarda fuskarta ta kalli inda ya shuri ta, ta kai hannu ta taba.

“Baba....”

Ta furta domin har yanzu tana jin sautin kalmar shahadar da yake a kunnenta, dayan ya fisgota sai ta mike tsaye sam ta manta a sirara take, yau ga ranar da bata kunyar siraicinta, ranar da dimauta da bakinciki suka saka ta manta babu sutura a jikinki.

“Wuce mu tafi”

Ta kalli inda mai maganar yake tana jin kamar ta taba jin kalmar. Tasss ya wanke mata fuska da wani irin mari mai zafi, sai ta rikice ta fara kuka.

“Inna.... Baba.... Wayyo Baba.... ”

“Saka tufafinki”

Ras ta ji abun da ya fada, kuma ta fahimce shi, hakan yasa tai saurin nufar inda tufafin suke ta dauka, sai dai a maimakon ta saka sai ta rike tufafin tana ganin komai kamar a mafarki. Dayan cikinsu ne ya fisgota ya turo keyarta waje, sai ta samu kanta da bin bayan wadanda suke gabanta, abun da bata sani ba ashe a sauran gidajen nan ma sun fito da sauran matan da suka rage, tafiya kawai take tana jin kamar ba kasa take takawa ba, hade ta sukai da sauran matan dake ta rawar jikin tsoro, domin sun kasu kashi kashi ne, suna shiga gidaje. Kamar wandanda suka fito yakin duniya, haka kowa ganinsu, karyar mutun yace ga iyakarsu sai dai ya kiyasta a kiyasinsa ya fadi iya abun da idonsa ya gane masa, babura ne ko wane da goyon mutum uku dauke da makamai, wasu kuma mutum biyu ne a kai, wasu kuma a kafa sun saka manyan samarin maza a gaba dauke da hatsin da suka kwasa.

Ba Aminatu ce kadai mace da suka tafi da ita ba, sai dai Aminatu ita kadai ce tsirara a cikin matan da suka kora zuwa daji, kamar sun kora dabbobi haka suka saka matan a gaba, wasu kuma suna daga gefe duk wanda yai kokarin guduwa daga cikin matan sai a halbeshi. Wasu mazan kuma suna bayan su Aminatu dauke da hatsin da suka dora musu, suna tafe suna dukan mazan a baya. Tafiya suke ta yi Aminatu na rumgume da tufafinta, bakinta kuma be daina furta Baba ba, da muryar da ita kadai zata iya ji, tana jin ta taka abu har ya huda fatarta ya shiga cikin kafarta, sai dai ko kadan tashin hankali be barta ta ji zafi ba, ko da ma ta ji bata isa ya tsaya cirewa ba, a cikin matan da suka tura gaba har da masu goyo, da kananan yan mata da matan auren, babu mai waiwaye balle ya taimaki wani, a cikin masu goyon wandanda yayansu suka fi takura musu da kuka sai su fige yaran su jefar, tsofafin da suka fara gazawa kuma sai su halbe su, masu sauran jini a jika kuma suna tafe suna dukansu. Zalincin da mutanen nan suke sai ka rantse da Allah ba zuciyar dan'adam ce a jikinsu ba. Ba su san wani abu tausayi ba, ba su ragowa ba, ba su san rai yana da muhimmancin ba, ba su wani abu imani ba, ba su san ragowa ba. Tun cikin dare suke tafiya a kafa suna ratsa wani irin jeji da Aminatu bata taba mafarkin gani ba, ba su isa inda za su je ba sai da hasken asuba ya fara ketowa.
Ba ita kadai ba mata da yawa idan ka duba kafafuwansa zaka tarar sun kumbura, saboda babu mai talkami a kafarsa, kuma da yawa sun taka kaya wasu kuma ice ya shiga kafar amman ba damar cirewa, sai dai kai ta taka kafar a haka.

Wani irin jeji ne da baka iya ganin iyakarsa, sai dai da alama mutanen kowa ne da dabarsa dabam, domin an raba matan ne wasu suka kora wasu zuwa yamma wasu kuma suka arewa, a cikin matan da aka kora arewa har da Aminatu dake rike da tufafinta.
Har ga Allah ba zata iya fadar inda take ba, har yanzu bata yarda ba rayuwarta ba mafarki bace, har yanzu kisan da akai Baba da Inna gani take kamar ba gaske ba ne. A wani kebantaccen guri aka tsayar da su, sannan wadanda suke manyansu suka taso da manyan fitilu suka haska matan, kamin su kalli mazan da su ma sun gama galabaita.

“Wadanda ku kashe su kawai”

Aminatu ta juya a hankali ta kalli mazan da bata iya tantance fuskar kowa a cikinsu saboda tana cikin nata tashin hankali. Kamar umarni suke jira a take suka budewa mazan wuta suka musu mugun halbi, wadanda bindiga bata kamawa kuma suka takasu da babur. Faduwa Aminatu tai durkushe ta fashe da kuka, domin a yanzu ta tabbatar ya baro duniyarta, ta shigo wata duniyar ta azzaluman mutanen da babu digon tausayi a zuciyarsu. Kukan da tai ne ya saka dayan sake haskata.

“Wai iyakar matan kenan?”

“Aa an raba dai, Daba... Ba ruwana ba zan fadi suna ba, sun dauki rabi, kai duk mun watse garin nan fa yau babu wanda muka bari, Wallahi yau mun aiki”

Dayan ya fada cikin mutanen da suka zo da su Aminatu, idan suka ce suna nufin gundu, domin akwai Babbar daba akwai karama, kuma daba kala kala ce, kowa da tashi, suna maganar yaron wata na kuka sai dayan ya ce.

“Kai wacan ya dame mu da kuka”

Wanda ke kusa da ita ya fisge yaron, sai ta rike masa kafafuwa tana kuka.

“Dan Allah kai hakuri yaro ne be san komai ba”

Ba su saurareta ba, sai suka aje yaron gefe suka halbeshi, da sauri uwar ta saka hannunta ta rufe bakinta saboda kar kukanta ya fito ita ma su halbeta.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Aminatu ta furta tana jin hawayen ya tsaya mata cak. Sai dayan ya haskata daga masa zuwa kasa.

“Ku daure wadanda”

Kamar dabbobi haka aka turasu zuwa wani gurin da babu wanda zai iya tantance shi, suka fara dauresu da sarka. Wasu kuma da igiya irin yadda ake yi ma dabbobi, idan an daure sai a saka igiyar a turke. Sauran da aka baro a garin suna da suke kan babura ba su iso ba sai kusan 6:30am daman can haka ake, idan za a saka mata to wadanda za su kura matan su zasu fara tafiya da su a gaba, su kuma sauran su biyo bayan idan sun gama na su aikin. Sai da haske safiya ya baibaye ko'ina sannan Aminatu ta tabbatar da ba ita kadai take ba, domin a gabansu wasu mazan ne aka daure masu yawan gaske, gafensu kuma akwai mata, gana ganin su kasan sun dade a gurin domin sun galabaita tufafin jikinsu sun yi datti sosai, mazan kuma wasu har gemu ya tarar musu, wasu gashin kai yayi musu yawa, a cikin wadanda suke daure akwai marasa lafiya. Sai dai wayewar gari zuwa karfe takwas an kashe mutun biyu a gaban idonta saboda sun cika tari, wai suna gudun kar su saka musu cuta, da zarar ka fara tari yayi yawa sai su ce a kashe ka kar ka saka musu cuta. A lokacin ne Aminatu ta samu kuzari da karfin zuciyar daura zanen dake hannunta ta suturta jikinta.
A wani kebantaccen guri aka fito da abinci, aka fara bin wadanda suka dade a gurin ana zuba musu 3 Spoon na shimkafa fara babu mai babu gishiri babu komai a ciki, kowa aka zubawa jiki na rawa yake cinyewa yana hadeye yawu, ba a baka abinci wadataccen, kuma baka isa ka yi magana ba. Bayan an gama da su aka biyo gurin su Aminatu aka zuba musu a hannu, ita kam rike nata tai a hannu tana ta kallon abinci kamar wanda bata san abun da ake kira da shimkafa ba. Suna zaune a gurin har rana ta fara dukansu, daga ita sai ireirenta ne suke ta murkususun zafin ranar da ya tsanata, sauran wadanda suka tarar a gurin kam da alama sun sab da zafin rana domin ko motsi basa yi. Wadansu mutanen ne dabam suka nufo inda Aminatu take suka kwance ta tare da wasu matan suka zaga da su zuwa bayan wata zana da aka kafa aka kare ta kamar katanga.

“Kwanta nan”

Ya nuna mata wani karamin duhu dake shimfide a gurin. Sai ta kwanta kamar daman can an halittota ne kawai dan ta bi umarninsa, da kansa ya kama zanenta ya cire, ya bude kafafuwanta, sannan ya kwance wando ya kwanto samanta ya ratsa cinyoyinta yana kokarin ratsa jikinta, runtse ido tai, ta ja wani dogon numfashi kamar zata shude, sannan ta fashe da kuka.
Har cikin kwakwalwar kanta take jin yadda yake ratsa cinyoyinta yana kokarin shigarta da karfi, zabar da ta ji ne yasa ta fasa ihu, sai ya rika kanta ya buga da kasa, a take ta ji kan ya sara mata.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Take ta maimaitawa tana tuna nasihar da Inna tai mata. Bayan ya gama abun da zai yi ya tashi, sai wani ya shigo ya saka zanenta ya shafe gabanta, sannan shi ma ya kwanta jikinta ya aikata irin abun da mutumen farko ya aikata, bayan ya gama wani ya shigo, suka suka bi layi, tun tana iya ambaton Allah tana kuka har ta kai bata iya yin komai, Wallahi sun keta haddi Aminatu tun tana cikin hayyacinta har sai da hankalinta ya bace gaba daya, babu komai a tsakanin cinyoyinta sai jini da fatar gabanta data zazzago tana rawa, bayan sun gama suka janyota kamar shara suka fito da ita suka kawo ta a inda sauran matan suke suka barta nan kwance galala sai zanenta da suka rufa mata a jikin.
Ba Aminatu kawai sukai ma ba, kusan duk macen da suka dauko sai sun mata haka, suna yi ma mata fyade har sai sun fita hayyacinsu, ba matan kadai ba har da mazan suna keta musu haddi, sai dai ba kowa ce Daba ce suke haikewa mace kamar Dabar da aka kai su Aminatu ba, ta haka ne mazan da aka kama suke gane an ketawa mace haddi, ko kuma namiji, domin idan sun gama suna barin mutun a wulakance.

LEILA POV.

“So kike ki tonawa kanki asiri ne?”

Momy ta tambaya tana kallon Leila, sai Leila ta girgiza kai tana share hawayenta.

“To na ce ki yi shiru ya isa, babu abun da zai faru, amman wannan kukan da kike zai saka Talba ko Daddynku ya zargi wani abu, bana son tashin hankali kin sani”

Kai ta daga mata, sannan ta kai hannunta ta dauki tissue ta goge hancinta, a daidai lokacin da Momy ta faka motar a harabar gidan. Kusan a tare Talba da Amal suka fito har ma da Kabir da ya shigo bangaren ba da dadewa ba.
Amal da Kabir suka karasa gurin Motar ban da Talba da ya tsaya jikin kofar yana kallon Momy da Leila da ta kasa hada ido da shi. Abun da Momy ta fadawa Talba shi ta fadawa Kabir, sannan ta nufo inda kofar falonta take wato inda Talba yake tsaye yana jiran karasowarsu.

“Sannu da zuwa Momy”

“Yauwa”

Ta amsa masa sannan ta ratsa gefensa ta wuce cikin falon. Yana tsaye a gurin har Leila ta iso, idonta yayi ja sosai kana ganinta ka san ta ci kuka ba kadan ba, uffan Talba be ce mata ba, bayan kallonta da yake har ta shige cikin Falon.

“Me Leila take yi ma kuka?”

Ba Kabir daya tambaya ba, har Amal dake tare da Kabir din sai da ta Kalleshi, sai dai bata ce komai ba ta wuce cikin falon. Kabir ya saka hannayensa biyu aljihu yana kallon Talba da mamaki.

“Really? Ina ce matar da zaka aura ce, miyasa ba zaka same ta da kanka ka tambaye ta damuwarta ba?”

Talba ya dan daga kansa sama ya sauke.

“Kabir Leila tana da matsala you know it”

“Tana da matsala ko kana da matsala? Simple tambaya ba zaka iya ba”

“No baka gane ba ne, ina son na san idan tana kuka ne saboda abun da ya faru da Baaba or not, saboda ban gansu da abun da Momy ta fada ba”

“So Momy ta yi karya kenan?”

Kabir ta tambaya yana masa wani kallo. Shiru Talba yai domin be san me zai sake ce masa ba. Ganin hakan yasa Kabir kai hannunsa ya tura kofar falon ya shiga ciki, Talba kuma ya sauke ajiyar zuciya sannan ya nufi bangarensa.

“Momy miyasa za ku dage sai Talba ya auri Leila ne? Ba ku tunanin kamar za ku takura masa ne?”

Momy dake kokarin yaye mayafinta ta juyo ta kalli Kabir dake tsaye bayanta.

“Ya maka wata maganar ne?”

“No kawai ina ganin kamar Talba ba sonta yake ba”

“Idan ba sonta yake ba wa yake so? Tun da kake a gidan nan ka taba jin ya yi maganar wata yarinya? Be taba yin maganar aure ba, sai da Engineer ya gabatar masa da Leila, kuma ya amsa yace yana son ta, idan kuma har baya son ta ai ba zai ce yana so ba”

Kabir ya kwanto jikin kujerar yana fadin.

“Ina ganin kamar ya amince ne saboda kar ya bawa Daddy kunya... ”

Momy ta daga masa hannu.

“Yana sonta baya sonta, saboda Engineer ya amince what so ever, ba damuwar mu bace, tun da ita Leila tana sonsa, daman shi ai be san so ba”

“Amman tsakani da Allah fa zai cutu nan gaba, kuma ita ma....”

“Kabir....!!!”

Momy ta daka masa tsawa, tare da mikewa tsaye.

“Ka daina yin abu kamar ciki daya kuka fito, kai yana tausayinka ne ko ya raga maka? Ba zaka gane hakan ba sai nan gaba, kullum maganar Talba kake baka duba yar'uwarka, baka tunanin idan aka fasa aure ita Leila zata iya shiga damuwa?”

“Kara ta shiga damuwa a yanzu, da wanda zata shiga nan gaba... Domin abu ne mai wahala Talba ya canja rayuwarsa, imagine yanzu fa ni yake tambaya miyasa Leila take kuka ba zai iya tunkararta ya tambaye ta ba”

“Zai canja, domin dole ya canja, dole ne mu gyara masa zama, idan ba haka ba zai wahala ne”

“Ko kuma ita ta wahala ba..”

Momy ta kalleshi da kyau.

“Wai Kabir ko so kake mu bar Talba ya dauko mana wata bare can daban? Bayan ga yar'uwarsa a gida?”

Ya dan tabe baki yana kallon Momy, domin ya san a yanzu ba zata fahimce ba. Daukar mayafinta tai da jakarta ta nufi upstairs rai a bace. Har zata shige dakinta sai kuma ta nufi dakin Leila ta murda kofar a hankali ta tura, sai ta same ta zauna tsakiyar gado hawaye shabe shabe a fuskarta wayarta makalle a kunne, da alama magana take da wani.

“Da wa kike waya?”

Momy ta tambaya with serious face. Sai da ta sauke wayar sannan ta kalli Momy.

“Madina”

Momy ta karasa shigowa cikin dakin gaba daya, tare da maida kofar ta rufe.

“Leila wannan sirrinki ne, duk amintar da kike da Madina karki fada mata sirrinki”

“Toh Momy”

Ta amsa tana share hawayenta.

“Ki dauka kuskure ne kowa ai yana kuskure, idan kina yawan kuka sai ki saka mutane su zargi wani abu”

Saukowa tai da kafafuwanta a kasa, tana kara share hawayenta. Momy har ta juya sai kuma ta juyo ta kalleta.

“And for the very last time, zan sake tambayarki kina son Talba?”

Leila ta daga kai.

“Wallahi ina son sa sosai Momy, ina son shi, miyasa kika tambaye ni?”

“Ba komai, ki kwantar da hankalinki”

Leila ta daga kai alamar gamsuwa, sannan Momy ta juya ta fice daga dakin zuwa dakinta. A hankali ta tura kofar dakinta ta shiga kai tsaye ta nufi gadonta ta sauke jakarta da mayafinta akai sannan ta zauna tana sauke dogon numfashi.

“Allah ka yafe mana...”

Ya furta tana lumshe ido, sai kuma ta busar da iskar bakinta.

FARUQ POV.

“Ina son anjima zan tafi kasuwa”

Ya juyo ya kalleta yana kokarin saka agogon hannunsa.

“Gurin me?”

“Tufafi zan siyo, kuma zan siyawa Sultan ma”

“Karki je ko'ina, kuma karki siyawa dana komai da kudin da ban san inda suka fito ba”

Yana gama fadar hakan ya saka talkaminsa ya fice daga gidan gaba daya. Wani dogon tsaki ta ja ta murguda masa baki.

“Wallahi sai na je, wato bayan talauci har da hassada tana damun talaka”

Ta fadi zaune saman kujera rike da wayarta tana tabe baki, Data ta kunna ta shiga facebook, sai da ta fara duba notifications dinta, ta shiga comments tana duba yadda maza ke yaba surarta kowa da yadda yake yaba sabon hoton da ta dora, murmushi take tana ta bin comments dinsu da like har cikin zuciyarta take jindadin yadda suke yabonta. Bata da fargabar komai domin ta yi blocking din Faruq da duk wani dan'uwanta na kusa da ta san zai iya ce mata ta gyara ko ta daina, daga familyn Faruq har nata yan'uwan. Bayan ta gama karanta comments din ta leka inbox dinta, sakonni ta tarar da yawa cikin har da bakin fuskar da basu saba mata magana ba, kamin ta yi ma mutun reply sai ta duba profile dinsa ta duba abokansa aikinsa hotunansa da kuma inda yake zaune, da zarar ta ga alamar mai rufin asiri ne sai ta sake masa idan kuma ta ga sabanin haka sai ta yi blocking dinsa a take.

“Ibrahim”

Ta furta sunan dake profile dinsa sai kuma ta shiga duba hotunansa, da inda yake aiki kana ganinsa kasan mai abun hannun ne. Komawa tai inbox din ta amsa masa da thanks akan yaba kyauta da yai. Kasancewar yana online a take ya maido mata da amsa.

“Babu godiya a tsakaninmu, wani ma yai rawa balle dan makadi”

“Uhmm haka kace”

“Haka ma yake, wani ya bawa mana matarmu balle kuma ni”

Ba shiri ta zaro ido gabanta ya fadi.

“Ya san ni kenan, ko kuma dai wasa ce”

Ta fada tana tashi tsaye.

“Matarku kuma?”

Ta tambaya domin tantancewa.

“Eh mana ba matar Faruq ba ce Rafi'ah?”

“Ka san Faruq ne?”

“Sosai ma tare muka yi makaranta da shi”

Ta kara zaro ido.

“Na shiga uku”

“Gaskiya abokinmu yayi dacen mata, kina da kyau”

Ya rubuto mata, sai ta koma ta zauna tana kokarin kwantar da hankalinta.

“Da alama shi ma shegen ne”

‘Allah sarki, ashe kun yi karatu tare’

Ta amsa masa.

‘Eh sosai ma, na zo har aurensa ai, kuma ko lokacin da kika haihu na so na zo ban samu dama ba, ya Babyn?’

‘Lafiya Kalau, ya naka iyalin?’

‘Ni kam da saura har yanzu ban yi aure ba, sai na samu mai kyau irinki’

‘Hmmm kana koda kyau na kamar gaske’

‘Da gaske ne mana, Faruq be taba fada miki kina da kyau ba’

‘Uhmmm’

Shine reply din da tai masa sannan ta kashe data ta aje wayar, ta nufi inda Sultan yake yana bachi ta tashe shi ta bashi ragowar kazar jiya ita ma ta ci ta koshi sannan ta shirya masa ita ma ta shirya ta dauki jakarta da mayafi ta riko hannun Sultan suka fito daga cikin gidan, sai da ta kulle gidan sannan ta nufi makontansu ta bada ajiyar Sultan ita kuma ta kama hanyar titi, ba yau ta saba satar hanya ta fita ba, wani lokacin idan ta tambaya ya yana ta ma fita take wani sa'in kuma bata ma tambayarsa, gashi idan ya fita baya dawowa sai dare, inda ba wani abun ya bijiro ba. Ko ma ya dawo ya tarar bata nan sai dai yayi hakuri ya danne abun a zuciyarsa.

“Malam tsohuwar kasuwa”

Ta fada bayan ta tsaya da mai adaidaita, kai kawai ya daga mata, sam bata lura da kofatun dake kafunsa ba ta shiga, sai da ta gyara mayafinta da face mask din dake fuskarsa sannan ta aje jakarta gefe. Kamar ance duba ki gani tana kallon bayan kansa sai ta ga kan kamar na tsuntsu har wani rawa yake kamar zai fado ga bayansa duk gashi kamar dabba.

“Malam tsaya na fasa zuwa...”

Ta fada da sauri tana runtse ido, sai mai Napep din ya faka gefen titi, tsabar tsoro yasa bata tsaya daukar jakarta ba ta fita da sauri tana haki, tana fita mai Napep din ya cigaba da tukinsa kamin ta rufe ido ta bude har ya bacewa ganinta, baya tai da sauri tana kara zari ido.

“Innalillahi”

Bata karasaba ta ji kamar ta taki abu, sai ta juya da sauri ta kalli Mahaukacin dake bayanta ya tara uban gashi ga tufafin jikinsa duk datti, wani irin tsalle ta daka ta ranta ana kare, wani irin gudun bala'i take mahaukacin na biye da ita shi ma da gudunsa. Wani shagon dake titi ta nufa kamin ta isa mutanen dake gurin suka watse da gudu domin sun san mahaukaci ba ya yi ma mutum da sauki, ita kanta bata taba sanin tana da gudu ba sai a yau, tana karya kwana ta samu wani gida ta shige ta turo kofar gidan da karfi ta rufe, tana ta haki kamar numfashinta zai fita. Mutanen gidan suka fito da sauri suna kallonta.

“Lafiya?”

Sun tambaya domin kama tai musu da mahaukaciya, kanta babu dankwali balle mayafi ga kafafuwanta babu talkami sai uban datti da suka yi, gashin kanta ma dake fake har ya yamutse, gumi sai sauko mata yake.

“Mahaukaci ya biyo ni....”

Ta fada daker tana haki, idonta har wani zurfin wahala sukai.

“Subhanallahi tsokanarsa kika yi?”

Dayar ta tambaya tana kokarin gyara goyonta, kamin ta amsa mata suka ji aka dukan kofar da karfi.

“Zai iya balla mana kofa fa”

Baturiya ya kauce jikin kofar da sauri ta dawo cikin mutanen tana kallon kofar.

“Ban tsokane shi kasuwa zan je sai mai Napep...”

Bata karasa ba tai shiru tsabar fita da numfashinta yake da karfi.

“Wallahi haka yake, ranar fa tun daga rijiyar zaki ya dinga bin Marwa har unguwa uku”

Baturiya ta kalli mai maganar, daman tun daga jin yanayin maganarsu ta ji ta banbanta data Zamfara, domin su kananci suke yi, gashi kuma an fadi rijiyar Zaki da unguwa Uku, wanda ta san ba a Zamfara unguwar take ba.

“Baiwar Allah nan kuma wani gari ne?”

“Kano... ”

“Kano....?”

Ta maimaita tana zaro ido, sai ta fadi a gurin zaune ta fashe da kuka.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata. Akwai dan wata bakwai, muna da kwalli mai karfin gaske (Mujarrabun sadidan) Akwai na farin jini for yan mata da Zaurawa. Akwai wanda ba a bawa mai kishiya, akwai na mazajen da kr neman mata, muna da rantse baki da kishiya, muna da back to virgin, for yan matan da kaddara ta fadawa, ko Zaurawan dake son zama yan mata, akwai jigida mai kyau, muna da man ayu 100% natural. Akwai na maza masu hannun Dambe.
Hajiya sai n gwada akan san na kwarai, ba cuta ba cutarwa, duk wanda kika siya sai kin dawo.

Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers Please idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -9□

If you're not living around these people, you will never know what they are going through, fiye da haka ma yana faruwa, kawai dai Allah ya tsare mu su kuma yai musu mafita.
Tun daga jin sunan Labarin kun san abun da ya kunsa. Ban san abun da readers suke so ba, idan an saka kudi da luxury life sai ace writers suna bude idon mutane, and when we're talking about reality kuma ba mu tsira ba, anyway if you don't like the story you can quit it.

*** *** ***

Har past 12am Talba yana zaune bangaren Momy doing nothing, haka nan kawai yake jin yanayinsa sai a hankali. Idan zaka tambaye shi damuwarsa ba zai ce maka ga matsalarsa ba. Mikewa yai tsaye ya isa gaban plasma ya kashe sannan ya wuce kitchen domin samu abun da zai sakawa cikinsa, rabonsa da abinci tun da rana, ko lunch din Momy ta hada be ci ba. Tea ya fara hadawa kansa sannan ya bude freezer dake kashe ya dauko cake ya kunna oven ya saka shi a ciki, sannan ya dauki tea ya rike a hannunsa yana ta kallon harabar gidan ta windows kitchen din, ko ina haske ne kamar rana.
Juyowa yai a hankali jin kamar shesshekar kuka a falo, aje cup din dake hannunsa yai ya tako a hankali zuwa bakin kofar kitchen din ya tsaya. Sai ya hango Leila zaune a bakin stairs din sanye da kayan bachi riga da wando sai kuma safar dake kafarta, kanta ba dankwali sai hawaye take tana kallon wani bangare na falon, sam bata lura da shi ba har sai da ta juyo tana cigaba da rera

kukan a hankali. Suna hada ido sai tai sauri share hawayenta ta dauke kai sannan ta mike tsaye ta juya a hankali zata hau stairs din.
Har tai rabi ban da kallon mamaki babu abun da Talba yake mata.

“Leila...”

Ya kira sunanta kamar wanda baya son magana, tsayawa tai cak gabanta na mugun faduwa, domin har ga Allah bata dauka yana zaune a falon har lokacin ba, da b zata fito daga dakinta ba, juyowa tai a hankali sai dai bata yarda ta kalleshi, sanin kanta ne ba zai tambaye ta me take yi ma kuka ba, kiran sunanta kawai da yai ya isa ya sanar da ita cewar tambayar damuwarta yake.

“Na yi mafarkin tsoro ne...”

Ta fada tana wasa da yatsun hannunta, bata tsaya jiran abun da zai ce mata ba ta juya da sauri ta haura sama. Da kallo ya bita har ta bace masa sannan ya juyo ya dawo cikin kitchen din, mamaki karara a fuskarsa.

‘Mafarki tsoro?’

Ya maimaita aransa, idan mafarkin tsoro tai me zai saka ta fito a nan ta zauna ita kadai?

“Ko dai saboda ni ne?”

Ya tambayi kansa yana kokarin kai hannunsa ya dauki tea, domin ya san abun da zai tashi hankalin Leila ba karami ba ne, and bayan shi ba ya ji akwai wani abu da zai saka Leila ta yi kuka ko ta shiga damuwa. Kamar wanda baya son bude baki haka ya kai cup din a bakinsa ya soma sha a hankali, dayan hannunsa ya saka a aljihu yana kallon oven din sai dai gaba daya tunaninsa ba a nan yake ba.
Sai da ya sha rabin tea sannan ya kashe oven din ya ciro cake din daya dumama ya aje, ya dauki tissue ya saka a hannunsa sannan ya fara daukar cake din yana ci. Bayan ya gama ya kashe wutar kitchen din ya fito falo ya kashe wutar sannan ya wuce bangarensa. Shirt din jikinsa ya fara cirewa wanda hakan ya bawa kyakkyawar surarsa da murdaden kirjinsa bayyana, a kafadarsa ya dora rigar sannan ya nufi wani madaidaicin daki dake hannunsa na dama, a hankali ya murda kofar ya bude ya shiga, kai tsaye ya nufi teburinsa ya ja kujera ya zauna ya bude system dinsa yana duba sakon da Jahid ya turo masa na adadin kudin da za a kashe wannan watan na gidan marayu.

“Okay”

Ya furta sannan ya rufe system din ya saka hannunsa aljihu ya ciro wayarsa ya kunna data ya shiga WhatsApp.

‘Zan rubuta maka cheque gobe, after that, ka bincika abun da yan gudun hijira suka fi bukata ka kirga ko nawa za akashe na mutun 300’

Bayan ya gama rubuta masaya kashe data ba tare da ya duba sako ko daya da yake shigo masa ba, balle har ya amsa. Fitowa yai daga dakin ya nufi Bedroom dinsa yana shiga ya aje rigar dake kafardarsa a muhallinta ya cire jean din jikinsa ya nufi bathroom ya jika jikinsa da ruwa ba tare da ya saka sabulu ba yai alwala

ya fito, sai da ya tsane jikinsa sannan ya nufi closet din ya dauko kayansa na bachi.
Wando kawai ya saka domin abu ne mai wahala ya kwana da riga komai tsananin sanyi, sai dai ya rufa da bargo, riga na cikin abun da ke takura shi ta hana shi sakewa idan zai yi bachin dare.

BATURIYA POV.

“Wallahi tun da nake a rayuwata ban taba zuwa Kano ba, ni fa ban taba barin Zamfara ba”

Ta fada tana fyace hancinta daya cika da majina tsabar kukan data sha.

“To ya akai kika zo nan?”

“Agwagwa da buje na shiga nace ya kai ni tsohuwar kasuwa sai na ga kansa yan rawa kamar dan tsuntsu, bayansa kuma da gashi shine nace ya sauke ni yana sauke ni na fito da sauri, sai wannan mahaukacin ya biyo ni”

“Minene kuma Agwagwa da buje?”

Ta kalli wanda tai tambayar da idanuwanta da sukai ja abun ka da farar mace.

“Keke Napep”

“Oh Allah na wata kila aljanine ya dauke ki, kin san fa ance suma suna yin Napep din”

“Ga zahiri na gani, wata kila da bance ya tsaya ba da yanzu na tsinci kaina a Russia ko Iraq”

“Lallai kuwa abun na su ba wuya, to yanzu kina da waya a tare da ke?”

Sai a lokacin ma ta tuna da jakarta, domin wayarta da kudinta har da makullin gidanta suna cikin jakar.

“Na shiga uku Wallahi jakata na cikin napep din aljani nan kuma ya tafi da ita”

A take ta fashe da sabon kuka, domin ta san samun wata wayar ma agareta yanzu abu ne mai wahala.

“Subhanallahi, to kina da number wani akai ko mijinki ko Baba?”

“Babana ya mutu sai dai mijina kuma shi ma ya siyar da wayarsa, yau ina cikin ukuba”

Ta kara fashewa da kuka.

“Baki da number kowa akanki”

“Akwai ta yayata da Mamana”

Sai da ta share hawayenta sannan ta karbi wayar ta saka number Mama tana shiga aka dauka.

“Hello Sallamu Alaikum”

“Mama ina cikin matsala Mama gani a Kano”

“Kano kuma Rafi'a? Gurin me?”

A nan ta labarta mata abun da ya faru, cikin labarin tafi nanatawa Mama cewar wayarta na cikin jakarta kuma ya tafi jakar, da alama ma batan wayarta yafi mata zafi fiye da ganin kanta da tai a Kanon cikin kankanen lokaci, yan kudinta ma duk suna ciki. Kamar wata sabuwar mahaukaciya haka Baturiya ta zama har wani yamutsar kai take.

“Wallahi Takauci be yi ba, daman ance idan mutum ya kwana arba'in be ci nama ba idan yai maka baki zai ya kama ka, gashi nan ai laifin Faruq ne”

“Wanene kuma haka?”

Sai tai shiru bata fada ba, domin bata son tace mijinta ace bata jin magana tun da har ya hanata fita kuma ta fita duk kuwa da kasancewar ba wannan ne karo na farko da ya hanata kuma ta fita ba.
Account din mai POS din unguwar aka karba aka turawa Mama ta turo mata kudin mota, aka ciro mata sai dai tafiyar ba zata yi a yau ba domin yamma ta yi gashi kuma hanyoyin nigeria babu kyau a dole ta hakura sai gobe da safe ta kama hanyar dawowa Zamfara.

Kamar kullum sai bayan sallah isha'i Faruq ya dawo gida. A bakin kofar gidan ya tsaya ya kwankwasa yana sauraren ta bude masa amman shiru bata bude masa ba, ya sake kwankwasa nan ma ba a bude masa ba, yayi haka kusan sau hudu sai a na biyar ya saka makullin hannunsa ya murda ya bude kofar daman can a tunaninsa ko ta rufe kofar ne daga ciki kamar yadda ta saba, sai dai tun a yanayin yadda ya tararda gidan ya tabbatar masa da matarsa bata nan. Yayi sa'a akwai wutar nepa sai ya kunna gulob din waje dana falo ya shiga daki ma ya kunna, tsaye yai yana karewa dakin kallo komai a watse kamar yadda ya fita ya bar shi, daman yana fita ta shirya ta fita bata tsaya gyaran komai ba. Gashi kuma be tararda ita ba, ajiyar zuciya ya sauke.

“Rafi'a Allah ya shirya ki”

Ya furta cikin yanayin dake nuna alamar be jidadin daya sami gidan a haka ba, babu abun da ya fi bakanta masa rai ma kamar tararda ita da be yi ba a gidan, ko da yake halinta ne ko da ba zuwa unguwa ba takan fita makota tai taje can tana hira ko ta rika musu aiki alhalin ga nata aikin na gidanta ta bari, sai dai shi ya kasa sabawa da wannan halin, domin duk mai mata baya son ya shigo gida ya tarar matarsa bata cikin gidan idan ba da wani dalili ba, babu irin fadan da be mata ba amman bata canja ba, har ya gaji ya saka mata ido.
Gadon ya fara gyarawa sannan ya kwashe kayan data bari ya aje su a guri daya, ya gyara shimfidar Sultan ya dauko tsintsiya ya share dakin har zuwa falo, sannan ya zauna saman kujera ya daga kansa sama yana tunanin halin damuwar daya samu mahaifiyarsa a ciki, kusan kullum uwarsa bata rabuwa da damuwa domin idan babu na abinci akwai na rashin lafiyarta, sai dai a yanzu ta fi shiga damuwar fiye da koyaushe, a da tunanin na yadda zamu samu abun da za su

sakawa bakinsu ne ko kuma na maganinta tsabanin yanzu da tunanin aurarda yarta wanda kanwace a gurin Faruq ya hanata sakat, ba Mahaifiyarsa kadai ba, idan aka fasa auren nan shi kansa zai shiga damuwa balle kuma ita kanwar tasa, domin mijin yace ya gaji da daga auren da ake ta yi, su kuma ba su da wani abun aurar da ita a yanzu, sadakin da suka karba da dadewa Mama ta saka shi a cikin kasuwancin da take ta zimmar zata dan juya ko zata samu riba, sai gashi ba wan ba kanen wato ba uwa balle kuma riba, daman sana'ar talaka sai Allah, balle kuma irin nata sana'ar da ake ci ciki.
Bayan matsalar kanwarsa ga matsalar kudin hayan da ke jiransa next week, gashi ba shi da mafitar kudin a halin yanzu, dan aikin da yake ta applying shi ma shiru kamar wanda ya zagi gobnati.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ya furta yana dafe kansa.

“Allah ka kawo min sauki Allah ka yi min mafita”

Ya fada yana mikewa tsaye ganin har goma ta kusa matarsa bata dawo ba, duk yawunta bata wuce tara na dare sai idan biki ake ko kuma wani abu ke saka ta kai dare, ko da makota ta shiga bata wuce 9pm.

‘Ina tunanin tafiya nijar zai fi min gurin ginar zinari, sai dai shi ma ai dole sai ka samu kudi, samun wanda zai baka rance ma a yanzu ai aiki ne’

Ya nufi kofa yana ta sake-sakensa da tunanin inda zai samu mafita. Babu waya a hannunsa balle ya kira ya tambayi inda take domin ya bada wayar jingina tun shekaran jiya ya karbo musu abinci, hakan yasa ya fara nufar gidansu Maman Amira makociyarsu domin Baturiya tafi zuwa can ta wuni saboda suna da rufin asiri daidai gwargwado, ba shi ma ko mutanen unguwar sun shaidi Baturiya da son shigewa masu kudi, idan ka ga tana shiri sosai da mutum to mai rufi asiri ne. Cikin almajiran dake zama bakin kofar gidan ya kira daya ya aike shi cikin gidan ya kira masa Rafi'a, almajirin na shiga ya fito dauke da Sultan dake bachi ya mikawa Faruq.

“Ance wai bata nan, tun dazun da ta shigo bar Sultan tace zata je kasuwa bata dawo ba, kuma ta kira wayarta a kashe”

Cikin fargaba Faruq ya karbi dansa ya juya yana yi ma almajirin godiya ya koma gida, kwantar da shi yai ya fito waje zuwa gurin mai shagon daya bada jinginar wayarsa.

AMINATU POV.

Sai da yamma lis ta farka, ta dade da farkowa daga suman da tai sakamakon ruwan da suka zuba mata ga kuma zafi rana dake dukanta. Kana kallon kwayar idonta zaka karanci gajiya, da wahala dake tattare da ita. Gaba daya jin take kamar babu mararta zuwa kasan cinyoyinta, ko motsasu ta kasa yi, hakoranta kuma sun dantse gam kamar a hade aka haliccesu, a kwance take amman jiri sai dibanta yake tana ganin hadarin dake haduwa yana juyawa. Ba ita kadai ce a cikin wannan halin ba, sai dai wasu sun fita juriya domin suna da aure wasu kuma sun yi har sun fa ra warkewa. Kamar jira suke ta farko sai wani yaja hannunta ayayinda sauran jikinta yake kasa zuwa gurin turken da suke daure

matan, a kafa duka daureta kamar sauran matan, sai dai har lokacin a kwance take ta lumshe ido tana sauraren yadda numfashinta ke fita a hankali, babu tunanin komai a kanta tana son tai tunanin amman ta kasa, tana tai kuka ta kasa sai a yanzu ta gane ashe yin kuka ma wani babban gata ne, yin tunani ma wata baiwa ce, yau ta rasa ta ina zata fara tunani balle ya gayyato kukanta.
Sama sama take jin kafarta na mata zogi, saboda tafiyar data sha da kuma Kayoyin da suka taka, ba ita kadai ba kusan kowa yana fama da ciwon kafafuwan wasu sun taka kusa wasu kaya, sai dai basa jin zafi a lokacin sai a yanxu, wasu kuma daurin da akai musu ne yake musu ciwo, domin na da wasa suke daure mutum ba.
Kamar dazu da safe haka aka biyo su ana ba su abinci a hannu cibi biyu wasu uku, kowa aka zubawa sai yai sauri ya cinye saboda yunwa ta ci su har ta galabaitar da su, daman idan suka ci cibi biyu ko uku da rana ba za su sake ci ba sai kuma dare, wani lokaci ma ci daya ake a rana.
Komai tsananin zafin rana ko sanyi ko ruwa ba a basu abun rufa ko gurin fakewa, sai dai sanyi ya kare akansu, haka ma idan ruwa ne sai dai ayi ruwa a gama ya jika musu kaya kuma tufafin ya bushe a jikinsu, idan rashin lafiya ta same su sai dai su mutum domin babu zancen basu magani balle kuma akai su asibiti.

“Dan Allah ku kwance mu yi sallah magariba ta yi”

Daya daga cikin mutanen dake daure ya fada, kusan wannan shi ne karo na barkatai da yake rokon su barshi yai sallah. Sai wasu kananan samari suka nufo inda yake suka kwance shi suka ware shi gefe suka saka bulala mai kyau suna dukanshi.

“Wato kai shege ko, baka daddaraba”

Duka suka masa ba na wasa ba, daman jikinsa da sauran bulala da suka masa dazun saboda yace su bar shi yai sallah, a kullum sai yayi magana kuma a kullum sai sun masa duka.

(As I'm writing this mutumen da yake cewa su bar shi yai sallah is no more, Wallahi sun kashe shi neighbor din mu ne, and they sent his friend wanda aka kamasu tare ya fadawa iyalinsa bayan an biya kudin fansar karbo shi)

Bayan sun gama dukansa suka maida shi gurin da yake suka sake daure shi yana ta kuka, ga wahalar yunwa ga na dukan dazu dana jiya ga shi yanzu kuma sun kara masa da wani.
Ana gama sallah magariba ruwa ya fara sauko, ta yanayin garin suke iya gane magariba ko azahar da la'asar domin babu masallaci balle su ji kiran sallah balle kuma agogo. Yan bindigar ne suke ta gudu suna neman gurin fakewa, mutanen da aka ma kuma suna daure aka fara ruwan kama da bakin kwarya yana sauka a kansu, iyakar abun da suke shi ne su dukar da fuskarsa saboda kar ruwan ya taba fuskarsu, wasu kuma su saka hannu su kare fuskar tasu, sai dai hakan be hana ruwa ya jika su.
A cikin mutanen da ruwan saman ya jika har da Aminatu, dake kwance galabaice kamar sauran matan da basa da kuzarin yin komai, abincin da aka bata ma bata karba ba, komai ganinsa take kamar ba shi ba, har yanzu bata yarda mutanen da suka kashe mata uwaye da yan'uwa suka kawota daji suka keta haddinta yan'adam ne masu zuciya da jini a jikinsu ba. Ta kasa yarda a duniyar da ta sani take, gani take kamar daukarta akai aka jefata a wata duniyar ta dabam mai cike da azzalumai, kuma marasa tausayi da tsoro Allah.

Haka suka kwana a cikin sanyi cikin kwabon ruwa har safe, sam ita ko yunwar bata ji, sauran da suka dade nan kuma suna fama da yunwa domin sun sabu da gurin ya zame musu kamar gida, wasu sun yi wata uku wasu biyu wasu hudu har biyar ma.

*** *** ***

MONDAY MORNING 9:21am.

“I wonder what wrong with our country? Kashe mutane ya zama kamar abinci?”

Cewar Kabir yana kallon hotunan da aka turo na harin da aka kai a garinsu Aminatu, abun ya kazanta kuma yayi muni sosai, musamman harin nan na biyu yafi na farkon ma, domin a yanzu an bar garin ba kowa, tun a lokacin da abun ya faru suka kashe na kashewa suka tafi da wasu, sauran da sukai rai suka gudu zuwa wasu garuran gudun Hijira!
Talba ya kalleshi yana kokarin gyara agogon hannunsa. Ba al'adarsa ba ce yin breakfast a bangaren a week days sai dai weekend, idan har zai karya to sai dai ya karya bangaresa ya sha tea ko kuma ya tafi office dinsa ya karya, sai dai ya zame masa al'ada shigowa ya gaisa da Momy kamin ya tafi aikin, sanadin hakan yasa suka sabu da Baaba idan ya shigo tana masa kirari ko da ba zai amsa mata ba zai mata murmushi ya gaishe ta sannan ya fita.
Yau sai ya ji dabam domin ya saba idan ya shigo zai tarar ita take shirya abun karyawa sai idan weekend ne Momy take tayata su hada komai a tare.

“Wai ya ake son talaka yayi ne? Su fa suke noma, yanzu an hana su noma wadanda sukai kuma a kone kuma a ashe su a dauke matansu kai jama'a wannan abun yayi yawa, nan gaba abinci ma sai yayi wahala”

Momy ta kalle tana kokarin aje flakes din ruwan zafi a dinning.

“Shiyasa ga su nan sun bi sun cika mana gari da bara kamar za su kwata da karfi”

“Haba ai dole Momy, ki duba yadda mutumem kauye yake alfahari da noma amman su bar komai nasu su dawo inda babu kowa suna bara, abun tausayi ne Wallahi”

“Su ma ai sun so, tun da su suka fara kashe Fulanin”

“No wannan ba hujja bace Momy idan ma da gaske ne”

Tabe baki tai ta cigaba da abun da take, har suka ci suka shude Talba be ce komai ba, daman shi ba komai ke saka shi magana ba, ko da kuwa abun ya dame shi.

“Momy zan tafi aiki”

“Yau da wuri?”

Ya daga mata kai.

“Allah ya tsare”

“Ameen”

Ya amsa sannan ya fito daga bangaren yana wani irin kamshi turare mai jan hankali yan mata da saukar da natsuwar mai shakarsa. Kai tsaye bangaren Daddy ya nufa sai da yai knocking sannan ya tura kofar sai ya jita a rufe, door bell din ya danna sannan yaja ya tsaya. After few minutes aka bude masa kofar. Sai da suka gaisa da Amal da ta bude masa kofar sannan ya karasa can ciki gurin Daddy. Sai ya same shi zaune rai a bace yana kallon wayarsa, domin labarin harin da aka kai ya karadi kafofin sada zumunta musamman Facebook.

“Wa'alaikassalam”

Daddy ya dago yana amsa masa sallamarsa, Talba ya zauna kusa da shi yana karantar bachin ran daya bayyana a fuskarsa.

>>>>>><<<<<<
Sauran page daya mu gama free page, if you want to subscribe pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank and sent the evidence via 08036126660. Yan nijar kuma za ku biya ta wannan number +227 90 16 59 91 sai na yi adding dinku a group.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata.
Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers please, idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

□ BAKAR WASIKA □

By Khadeeja Candy

Page -1□0□

Talba ya mikawa Daddy wayar bayan ya gama dubawa.

“Daddy ku da kuke kusa da gobnati ya kamata ace kuna fada musu halin da ake ciki mana, mutanen nan suna cikin bala'i, kamar ni ne, kana zaune kana rayuwarka sai a iskoka a koreka daga gidanka a akashe yayanka kuma a keta haddin matanka, Wallahi tausayi suke ba ni matuka”

Cewar Talba cikin wani irin bacin rai da jin zafin abun da yake faruwa. Daddy yayi murmushi yana gyara zamansa.

“Mu'az kenan, waya fada maka gobnati bata san halin da ake ciki ba? Sun san komai, wannan matsalar tsoro tana kawo kudi sosai, fiye da yadda kake tunani, duk jihar dake fama da matsalar tsaro kudin da ake ware mata dabam, idan har aka magance matsalar to abinci wasu zai tsaya, kuma duk jihar da kaga suna fama da matsalar tsaro to suna da cigaba da ake bukata”

“Amman Daddy basa tsoron hakkin rai?”

“Wannan kuma ai sai lahira, Allah dai ya kyauta kawai amman matsalar tsoro a yanzu abu ne mai wahalar magancewa, domin an fi samun kudi ta gurin tun daga manya har kanana, na mu dai addu'a ne, da kuma taimaka musu da abun da Allah ya ba mu”

A hankali Talba ya busar da iskar bakinsa ya kalli Amal data doso inda suke sanye da uniform dinta na makaranta.

“Na yi magana da PA zai yi list din abubuwan da zamu siya mu kai musu soon”

“Maa Shaa Allah, hakan na da kyau”

“Wa za a kaiwa? Baaba?”

Amal ta tambaya tana aje fular abinci. Daga Daddy har Talba kallonta su kai, ta san ba maganar Baaba ake ba, kawai ta dauko maganar ne saboda tana son fadawa Daddy abun da ya faru ne, daman ita ce yar gulmar gidan komai akai a bakinta za aji.

“Wace Baaba kuma? Yan gudun hijira ake magana”

“Au na dauka Baaba za a kaiwa, Allah yasa dai ta ji sauki”

“Miya same ta?”

Daddy ya tambaya, a nan Amal ta zauna gefensa ta labarta masa irin abun da ta fadawa Talba.

“Taya Doctor zata yanke wannan hukunci bs tare da sani na ba? Tafi ki kirata”

Daddy ya fada rai a bace. Sai ta mike tsaye gabanta na faduwa.

“Ya sai ka ce ni kai ka fada”

Talba yayi murmushi, ita ma murmushin tai ta fice, bayan ta wuce Daddy ya kalli Talba.

“Ka san da maganar ne?”

Talba yayi shiru ba tare da ya amsawa Daddy da eh ko aa ba. Wanda hakan ya tabbatarwa da Daddy cewar ya sani kenan, domin idan be sani ba kai tsaye zai fadi cewar be sani ba.
Daddy be sake cewa komai ba har sai da Momy ta shigo dauke da wasu manyan kulolin abinci ta aje a gabansa, sai da Momy ta kalli Talba sannan ta kalli Daddy tana karantar yanayinsu.

“Lafiya dai engineer?”

Daddy ya kalleta irin duban da ke fassara mata bacin ransa.

“Baaba ta fado, har kun kaita asibiti amman baki sanar da ni ba”

Dagowa Momy tai ta kalli Talba da kansa ke kasa.

“Ina ganin kamar karamin abu.... ”

“Karamin abu? Da gaske? Amina kin san abun da kike fada kuwa? Mutum ya fado daga sama zuwa kasa ki kira shi karamin abu? Idan har karamin abu ne yayanta zasu dauke ta su tafi da ita ne? Ko da ma karamin ciwo ne tun da har a nan ta samu matsalar ai ya kamata ki sanar da ni, kuma be kamata a bar yayanta su tafi da ita ba, a nan ya kamata a dauki nauyin komai na ta, shekara biyu tana aiki tare da mu”

“Ranka ya dade, ba wani ciwo ne sosai ba, kuma na kaita asibiti sun bata magani sai ta kira yayanta tace zasu tafi da ita, babu yadda ban yi ba amman suka ki yarda, kuma ina da niyar fada maka anjima da dare idan ka natsu”

“Yanzu idan wata ce a cikin yayanki ta fado zaki mata haka ne? Balle tsohuwa? Sometime kina abu kamar damuwar wani ba damuwarki ba ce”

“Allah ya huci zuciyarka Engineer, amman be kamata damuwar wani ta dame mu ba, mu ma yanzu idan muka shiga cikin wata matsalar babu wanda zai damu da halin da muke ciki”

“Okay, yayi kyau daga yau ba zan sake biyan mai aiki ba, indai zan dauki mai aiki ta taya yaranki aiki ne ba za a sake ba, idan har damuwar wani be kamata ya dame mu ba, karki sake gabatar min da wata matsalar yan'uwanki balle kawaye”

Yana kaiwa nan ya mike tsaye a fusace ya nufi hanyar dakinsa. Momy ta rutse ido ta bude ta kalli Talba da shi ma kallonta yake domin ya san shi zata dorawa laifi.

“Karamin abu ma, sai ka tasa mahaifinka a gaba kana tsegunta masa? Talba wacce irin rayuwa ce wannan? Mun yi fada hankalinka ya kwanta? Kuma zai fita be karya ba, ina tunanin haka kake so ai? Kai na ya fara kwnacewa da lamarinka”

Uffan Talba be ce ba, har tai ta gama ta mike tsaye ta fice, mikewa yai tsaye ya ciro wayarsa dake ringing.

“Ali”

Ya fada bayan ya danna picking.

“Talba ka fita office ne?”

“No ya akai?”

“No ina son magana da kai ne, na dauka kana office na biyo”

“No yanzu zanje, yau da wuri zaka je aiki kenan?”

“Eh muna da patients da aka kawo mana, kasan sojoji sun samu kwato wasu daga cikin wadanda yan bindiga suka tafi da su, akwai wadanda suka samu rauni sosai an kawo mana su”

“Eh na ji an kai hari abun ba dadi Wallahi”

“Sosai an kawo wasu shekaran jiya wadanda suka harba abun ya kazanta”

“Allah ya kyauta, We can talk later”

Ya sauke wayar, sannan ya nufi kofar fita yana kiran Jahid.

AMINATU POV.

Labarin harin da aka kai ya karade ko'ina a Nigeria, gidanjen jaridu da kuma kafofin sada zumunta. Hakan yasa aka turo jirgin sojijin tun daga jihar Lagos har zamfara.
Kwashe gari aka bi su da danyen dankalin hausa a hannu duk wanda aka gutsawa sai yai sauri ya cinyewa, bayan sun gama ci kuma sai a bisu duka musamman wadanda aka akai maganar kudi da yan'uwansu ba su kawo ba. Sun fi dukansu fiye da kowa, duk abun da ake Aminatu na kwance bata iya komai ba, har yanzu bakinta a nauyaye yake, idanuwanta ne kadai abun da suke aiki a jikinta sai numfashi. Tana kwance galala ta daga kanta sama tana kallon jiragen sojoji guda biyu da suke shawagi a sama, kararsu kadai ta isa ta kurmantar da mutu, sun yi kasa kamar zasu saki wuta sai dai ba su saki wutar ba suka gangara can nesa da damarsu suka saki wutar a inda babu mutane.
Bayan ya wuce barayin suka fito daga gidanjensu na bukka dake can nesa da inda aka daure su Aminatu, suna da yaya da mataye a cikin bukokin sai dai akwai tazara mai yawa a tsakaninsu.
Suna isowa inda suke mutunen jiya ya sake rokon su bar shi yai sallah, sai suka hau shi da zagi.

“Kawo shi nan”

Dayan ya fada, sai sauran suka kwantoshi daga inda yake suka nufi wata bushiya inda mutunen yake, suka daureshi jikin icen suka sako kansa kasa kafafuwansa a sama yana ta lilo.
Tun yana kuka yana rokon su kwance shi har ya gaji ya fara kalmar shahada, majina ta fara fitowa ta hancinsa tana zazzagowa kasa tare da hawayensa.
Ba su kwance shi ba sai da su suka tabbatar rai ya bar jikinsa, sannan suka sauke shi kasa, lumshe ido Aminatu tai wasu hawayen suka cika mata ido.
Bata sake bude idon ba sai da ta sake jin karar jirgin, wannan karon da fatan mutuwa take kallon jirgin burinta ya sako wuta kowa ya kone har ita, domin tana da tabbacin babu wata rayuwar jindadi a tare ita ko da rayu! Ta ina ma zata rayu? Taya zata fita a nan? Idan ma ta fita gurin wa zata je? Da wa zata zauna? Wa zai rike ta? A kashe mata kowa, yayyu da iyaye, idan zata nemi yan'uwan uwa ko na uba ta ina zata fara nemansu? Ina zata gansu? Zata fita a nan ma?

‘Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un’

Ta maimaita a cikin ranta, domin bakinta ya mata nauyin da bata iya saka komai ta tauna balle har ta furta wani abu, wata kila kalamanta sun kare wata kila kuma har da rayuwarta, farinciki kam ta tabbatar da ya barta. Bayan sallah isha'i ta dan unkura ta tashi zaune tana jin kamar ba zata iya zaman ba kuma gashi ta gaji da kwanciyar. Hannunta ta kai ta damki kasar gurin ta junke a hannunta da wani irin karfin zuciya, sai dai na jiki kam babu shi ko kadan a kusa da ita, a galabaice ta dago kai tana kallon mutanen da suka doso inda suke da manyan fitulu suna haske su, matasan yan bindigar ne suka kwance matan kusan shiri maza takwas, a cikin mutanen da aka kwance har da Aminatu.

“To ku fadawa sauran dabobi an yi diyya kar sai mun kama hanya su bude mana wuta”

Wanda yai maganar fuskarsa a nade take da rawani babu ta inda zaka iya ganinsa balle ka shaida shi, sauran yan bidigar kuma wasu na sanye da rigar soja wasu kuka wandon suka saka wasu kuma duka biyu sai dai dukansu suna dauke da manyan bindigogi.

“Ai dai hanyar da suka biyo zaku bi karku kuskura sauya hanya, idan ba haka ba zaku hadu da wata dabar, kuma za mu aika musu”

Dayansu ya fada, sannan aka fara dukansu da bulala aka korasu kamar dabbobi.

“Ku wuce yan iska, ni na tsani kado Wallahi”

Cewar dayan yana dukansu, masu kuzarin cikinsu suka tashi suka fara tafiya ban da Aminatu da sauran da akai ma fyade kamar ta, ganin hakan yasa mutumen ya roki a dorasu akan babur, a fitar da su sauran da suke iya tafiya a kafa kuma a korasu a kasa. Wadanda aka kora a kasa suna tafe suna jin tsoro saboda daukin ba dadin da ake da babbar daba, daman can sun fi kowa dauka da zafi, karama daba kudin fansarsu ba su da tsada kuma ba da taurin kai kamar babbar daba, kasancewar karamar daba matasa ne masu tasowa wasu ma duk yara ne, babbar daba kuma manya ne wadanda suka dade a cikin harkar.

Su Aminatu sun riga isa kusan da bakin dajin saboda an dauke su a babur, sai dai zubesu akai a kasa suka zauna a gurin har sai da na kasan suka karaso sannan aka hadasu aka nuna musu hanya. Sauran wadanda sukai musu rakiya kuma suka juya suka koma ana kusan kiran sallah asuba suka fiton daga dajin, Aminatu na tafiya daker tana hawaye, idan ta gaji da tafiyar sai ta zauna a kasa ta yi rarrafe idan ta gaji sai ta unkura ta mike tsaye ta fara tafiya.. Da haka har suka iso bakin gari a inda motocin sojojin suke. Da farko sun tsorata duk kuwa da kasancewar an fada musu akwai sojoji a gaba, sai dai ganin a cikin barayin ma akwai masu uniform din sai ya saka wasu suka tsorata, sai dai kana ganin wadandan sojojin kasan zaratan sojoji ne ba kamar yan bindigar ba. Karasowa sukai suka dauki mutanen a mota, Aminatu kuma da ire irenta suka daukesu suka saka a motarsu, suka kama hanyar gari da su.

Ko da tara na safe ta yi, labarin nasarar da sojojin suka samu a kokarinsu na kwato mutanen da akai garkuwa da su ta kwarade ko'ina, labarin barin wutar da akai ya shiga lungu da sako na nigeria, ya leka gidan jaridu ya cika social media.

Masu lafiya aka tafi da su inda za a buka fuskarsu ayi ado da su a jaridu, marasa lafiyar kuma aka wuce da su asibiti a sirrance.

A tsakanin iskar dake dajin dana cikin gari zuwa na asibitin da aka wace da su Aminatu ko wane dabam, na dajin na tawaya ne da damuwa da bakinciki, shigowa garin kuma samun iskar yanci ne, sai dai shiga asibiti kuma na fata ne, wata kila ta rayu wata kila kuma rayuwar ta zaba mata mutuwa.
Mutanen da suka zo da gudu suka karbeta a hannun sojan daya dauko ta, sai su ka yi mata kama da wata halittar da taban kasancewar suna cikin farin uniform ne na aikinsu. Lumshe ido tai tana sauraren yadda aka dagata sama aka dorata saman gadon asibiti ana turata.

FARUQ POV.

A gurin mai shagon ya karbi wayarsa, ya saka line sa ya kira number Baturiya ya jita kashe. Hakan ya saka ya kira ta kanwarta sai da ta kusa tsinkewa sannan ta yi picking.

“Hello Raliya ya kike?”

“Lafiya Kalau Ya Faruq”

“Yayarki ta zo?”

“Aa, tana Kano fa”

“Kano?”

Ya maimaita cikin tsananin mamaki.

“Eh Napep ta hau shi ne...”

Ajiyar zuciya ya sauke bayan ya gama sauraren abun da Raliya ta fada masa, sannan ya sauke wayar yana jin babu dadi. Ya sani ba dan komai Baturiya take masa haka ba sai dan talauci, da yana da arziki da bata isa ya mata umarni ta saba ba, daman ai ta fada idan yana da kudi ba zata taba gujewa umarninsa ba, tabbas da yana da arziki da iyayenta sun nemi inda yake sun fada masa halin da matarsa take ciki, sai dai ba su yi hakan ba saboda ba kowa ba ne a idonsu, wannan dalilin ya saka a duk lokacin da ya kai kararta akan abun da take masa sai du bata gaskiya su goyi bayanta. Cire line yayi ya ya mika masa wayar ya juyo ya dawo cikin gida cikin yanayi na rashin dadi ya maida gidan ya rufe.

BATURIYA POV.

Washe gari mutanen gidan suka bata wani tsohon Hijab ta saka ta talkami, Bayan ta karya suka rakota har bakin titi suka tara mata Napep zuwa tashar mota. Su suka biya mata na napep din, tana ta musu godiya, idonta har yanzu be warware daga kukan da tasha ba, babu abun da take ji kamar wayarta, domin samun wata wayar a gareta yanzu abu ne mai matukar wahala a halin da suke ciki, har kara ma a gidansu wata kila mahaifiyarta zata iya taimaka mata da wani abu, yayanta ya cika mata sauran ta siye wata wayar, amman ba daga bangaren Faruq ba kam.
Tun daga yanayin hausarta suka gane yar zamfara, abun ka da kanawa sai dariya suke mata ita kam bata ma bi ta kansu ba gaba daya hankalinta yana kan

wayarta data bata yadda zata samu wata wayar kawai take tunani, gashi hanyar samun kudinta ta facebook ne inda take yaudarar maza, yanzu kuma babu wayar yaudara ma.

“Kai Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ta furta wasu hawayen na cika mata ido.

‘Dan Allah aljanuna idan kuna jina ku taimaka min da wayata ku dauki kudin na bar muku’

Wannan karon a cikin zuciyarta tai maganar hawaye na sauko mata.

“Malama Lafiya dai?”

Wani matashin saurayi dake kusa da ita ya tambaya yana kallonta. Banza tai masa ta ta juya masa fuska, sai yai murmushi ya cigaba da danna wayarsa. Sai da motar ta cika sannan suka kama hanyar Zamfara suna tafe suna addu'a saboda yanayin hanyoyin nigeria kowa ya san yadda tafiya take a yanzu. Sai da tafiya tai nisa sannan aka kira saurayin a waya, Baturiya ta kashe kunne tana sauraren yadda yake amsa wayar a cikin har da amsar da yake fadawa cewar motar haya ya shigo saboda motarsa ta tsaya ya barta a nan Kano.
Baturiya na jin haka sai ta juya ta kalleshi sai a lokacin ma ta lura da shaddar jikinsa babbar shadda ce, haka zalika wayarsa ma.
Tun da suka kama hanyar direban be tsaya ba har suka iso Zamfara.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Baturiya ta fada da muryar kasa kasa tana fashewa da sabon kuka. A nan ma kallonta yai ya tambayeta.

“Lafiya...?”

Kai ta girgiza ta share hawayenta ta fada masa abun da ya faru da ita, sai dai ta canja cewar tana da aure, sai ta fada masa cewar mahaifitarta ta aiketa.

“Subhanallahi, ki gode Allah ma be kai ki wata kasar ba”

“Haka yan gidanmu suka ce, ni daman Allah ya sani gidanmu bama hawan Napep duk inda zamu je a mota ake kai mu yanzu ma tsautsayi ne”

Ta fada kamar gaske, kallon lace din dake jikinta yai kamin ya kalli kyakkyawar fuskarta.

“Allah ya tsare gaba”

“Amin”

“Amman miyasa kike kuka?”

“Haba Malam dubi tufafin dake jikina fa? Ban taba kwana a irin gidan dana kwana ba sai jiya, yanzu kuma motar haya na biyo tun daga Kano har Zamfara abun da ban saba ba”

“Ba dadi gaskiya, ni ma ban saba hawan motar haya ba sai dolen dole”

“Ba dadi ai”

“Gaskiya”

Daga haka be sake cewa komai ba sai da suka isa cikin tasha. Bayan sun fito ta jero ita da shi suka fito titi, fitowarsa tai daidai da fakawar wata bakar mota mai kyau har wani sheki take tsabar sabuntaka.

“If ba wani matsala zan iya sauke ki a gida ai”

“Aiko da naji dadi Wallahi domin tsoron Napep nake yanzu.”

Murmushi yai ya bude mata baya ta shiga, shi kuma ta bude front seat ya shiga ya zauna.

“Ku gaisa da abokina”

Ya fada yana juyowa ya kalleta.

“Sannu ya aiki”

“Alhamdulillah ya hanya”

“Da godiya”

Ta amsa sai ta maida dubanta gefen titi tana kallon motocin dake kai kawo.

“Wace unguwa ma?”

“Gada biyu”

Ta amsa masa ba tare da ta kalleshi ba, ko kadan tsoro be kamata ba balle ta ji faduwar gaba, ta saba shiga motar maza duk kuwa da kasancewar tana da aure, sai dai bata barin wanda ya santa ya ganta, wannan karon ma bata haufin ganinta ne saboda ta san yayanta ya san labarin bata tan idan ya ganta da wani ba zai mata fada ba.
Har kofar gidan yayanta suka sauketa, kato gidan mai kyaun gaske, sai da tai musu godiya sannan ta bude motar zata fita.

“Ga katina maybe zamu iya gaisawa”

“Okay thank”

Ta fada tana karbar katin sannan ta fice ta maida motar ta rufe sannan ta tura gidan ta shiga.

“Ina ka hadu da wannan?”

“Ta sha kuma ta min”

Ya fada yana murmushi.

“Tana da kyau gaskiya”

Dukansu dariya sukai sannan abokin nasa yaja mota suka juya.

LEILA POV.

Tsaye take jikin windo tana kallon garden din dake cike da itatuwa, fuskarta dauke da hawaye, haka ma zuciyarta babu dadi ga rashin natsuwa da samun sukuni da take.
Hannu ta saka ta share hawayenta tana jin wani irin nadama da bakincikin abun da ta aikata.

“Why? Sometimes I'm very selfish”

Ya fada tana kai hannunta ta shafa wuyanta, bakinta ta cika ma iska ta busar sannan ta juyo ta baro jikin window ya nufi kofar fita har yanzu jin take babu dadi, tsaye tai tana kallon bakin kofar dakin a daidai inda Baaba ta tsaya sannan ta dauke kai ta fara tafiya, sai da ta leka dakin Momy ganin bata ciki yasa ta sauko kasa gaba daya sai ta same ta zaune akan sofa tana amsa waya. Wucewa tai dinning taja kujerarta ta zauna tana ta kallon abincin dake gabanta kamar mai wani nazarin.

“Leila...”

Momy ta kira sunanta bayan ta gama wayar, sai Leila ta juyo ta kalleta da idanuwanta dake nuna alamar bata samu bachi da yawa ba. Tasowa Momy tai tana karantar damuwar yarta, a take ta nemi bacin ran dake tare da ita ta rasa, hannu ta kai ta rika fuskar Leila.

“Dear ba ki bachi ba?”

“Wallahi Momy na kasa bachi kamar yadda na saba, Wallahi dana rufe ido matar nan nake gani”

Momy taja kujera ta matsa kusa da yarta sosai ta zauna.

“Leila ki kwantar da hankalinki babu abun da zai faru, babu wanda zai san wannan abun even if ma sun sani ba su isa su yi komai ba, they're poor ba su isa su ja da mu ba, kuma wannan abun ai kaddara ce, ki dauka haka Allah ya rubuta”

Ta gyada kai cike da gamsuwa. Sai Momy tai mata murmushi ta share mata hawayenta.

“Ko kadan bana son na ganku a damuwa, ku kenan uku Allah ya bani bana son kuna samun kanku a damuwa, wannan matsalar ma ta Talba zata wuce inshallah sai ya sauke duk girman kan nan”

“Anya Momy Talba zai ce?”

“Dole ya canja, sometime lamarinsa har daure min kai yake, yanzu maganar nan ta Baaba har ya kai ta gurin mahaifinki, simple abu Talba ya rika yinsa kamar wani mace ko karamin yaro, gashi na je Mahaifinku yace ba zai sake biyan mai aiki ba”

“Ba zai rika dafa abinci kenan?”

“Dole a aljihu zan rika biyansu, ai na yi magana da Hajiya Samira ta nemo min wasu yan aikin, a dole mu dauki wasu amman da ni zan biya su”

“Ban san miyasa Talba ya fita dabam a gidan nan ba, ni na rasa gane wane irin mutum ne”

“Shiyasa nake son ki kwantar da hankalinki, domin bana son ya fara zarginki, ni kam ba dan kin matsa kina son Talba ba....”

Kamin Momy ta karasa Leila tai saurin tare numfashinta tana rike hannunta.

“Wallahi Momy ina son Talba, ina mugun sonsa, Wallahi idan ba shi ba ba zan iya auren kowa ba”

“Shikenan ai ba zamu bari ya dauko mana bare ba, amman halin nan nasa ina ganin kamar zaki wahala idan akai auren nan”

“Momy ba zan aure shi ba sai ya canja, zan canja shi inshallah na san yana son mu yi aure ai zan yi amfani da wannan damar na canjan shi”

“Allah yasa yanzu dai sai ki karya”

Ta daga mata kai ta kai hannu zata fara bude kular akai knocking, kusan a tare ita da Momy suka kalli kofar falon sai dai ta riga Momy mikewa tsaye ta karasa gurin kofar ta bude.

“Madina...”

Suka sakarwa juna murmushi, sai kuma Madina ta juya tana kallon Talba dake kokarin shiga mota, kamin ta juyo ta kalli Leila.

“Fita zai yi?”

“I think”

“Kamar ya you think zai fita baki sani ba”

“Kina abu ke ma kamar baki san Talba ba”

“Ke ce ya kamata ki canja ba shi ba”

Madina ta fada tana sake juyawa ta kalli motarsa, ajiyar zuciya ta sauke a sirance sannan ta shiga cikin falon gabanta na mugun faduwa, irin faduwar gaban da take yawan samun kanta a ciki a duk lokacin da tai arba da Talba.

Alhamdulillah a nan na kawo karshen free page duk page din da zai biyo bayan wannan na kudi ne.

If you want to subscribe Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660. Yan Nijar zaku biya ta wannan number +227 90 16 59 91.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle I'm on Instagram as ramla_incense. Install the app to follow my photos and videos. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

---

“Madina ce”

“Eh Momy ya gida?”

“Lafiya Kalau ya Maman ki?”

“Lafiya Kalau take”

Ta amsa tana murmushi, sai Momy ta mike tsaye ta nufi hanyar dakinta dake kasa. Daga Leila har Madina binta su kai da kallo sai da ta shige sannan Madina ta kalli Leila.

“Wai da gaske baki san inda Talba za shi ba?”

“Ba zai wuce Office ba”

“Amman ya karya kamin ya fita?”

Ta daga fadunta alamar bata sani ba.

“Sometime a office yake karyawa wani lokacin kuma a bangarensa”

“Wani lokacin kina bani mamaki Leila, idan an yi magana ki ce kina son Talba, amman baki san abun da yake so ba, da wanda baya so, ba ki kokarin kiyaye bacin ransa”

“Shi yana kokarin kiyaye nawa ne? Yana son a rika masa sakon soyayya ana tambayar Lafiyarsa an damuwa da shi, amman shi be damu yai min ba, ni fa macece be kamata na zubar da kai a kansa ba”

“I know amman idan kin kula haka rayuwarsa, then why ba zaki bishi ku tafiyar da rayuwarku a haka ba, I'm sure idan kuka yi aure komai zai canja”

“Zamu yi aure, amman sai na gasa masa gida a hannu tukuna, and kina bukatar sanin wannan, Talba wanda zan aura ne ba wanda na aura ba, me yace me zai ci rayuwarsa for now bata dame ni ba”

“Haka dai kike gani, amman matakin kulawa daga yanzu ne, ni ina ganin ya kamata ma ki fara aiki ta haka zaku samu fahimtar juna sosai”

Rausayar da kai Leila tai.

“Madina, miyasa kike yawan damuna da maganar Talba ne? Ban shirya aiki yanzu ba sai na yi masters”

“Ina tsoron kar ya kubuce miki ne!”

“Really….”

Leila ta fada tana dariya.

“Ke a tunaninki akwai abun da zan nema na rasa a rayuwata? Haba Madina, ai Talba ko daga wani tsatson ya fita Daddy da Momy za su tsaya min na same shi, ballr kuma a jinina Talba ya fito, ba wai rasa shi ba, soyayyata ma ya hada da ta wata ma be isa ba, balle har ya hada ni da kishiya, haufi daya ne akan halayyarsa”

Madina ta yi murmushi.

“Leila kenan, na san kina da gata ta ko'ina, amman Talba yafi gaban yadda kike tunani, kar fa ki manta shi namiji ne”

Leila ta juya ido.

“Please My friend mu aje maganar Talba a gefe, kin san wai ko jiya na yi mafarki matar nan?”

Madina ta zaro ido.

“Da gaske?”

“Wallahi, ina ganin kamar ko yawan tunaninta da nake ne yasa nake mafarkinta”

Madina ta yi shiru tana kallonta kamin ta ce.

“Amman kin san fa hakkin jini...”

“Hakkin jini Madina sai kace wanda na kwantar na yanka? Kamar yadda Momy tace mistake ne, kuma kowa yana iya yin laifi ai dan adam ajizi ne ko?”

“Yeah.. Amman wannan kamar da banbanci Leila... ”

Ganin Leila zata yi mata wata maganar ta daban yasa Leila kawarta maganar ta hanyar dauko wata maganar.

“Ya aikin ki?”

“Alhamdulillah, ni aikin ma ya fara isata Wallahi”

“Kamar ya?”

“Ayukan ne basa karewa kuma gashi bama tashi da wuri, kuma zuwa kullum ne, ni da zan samu wani aiki ai da na aje wannan”

“Kamar ya zaki samu? Kin fa yi karatu ne Madina”

“Na sani amman idan ba irin kamfaninku ba ne da suke biyan ma'aikata da kyau kin san ba ko wane aiki zan iya ba”

“Idan kina son aiki a kamfaninmu ai zaki iya samu”

Madina ta wara ido tana murmushi.

“Da gaske?”

“Haba dai kina kawata ki nemi abu a gurina kuma ki rasa samu? Ki kawo takardunki kawai zan yi ma Daddy magana”

Da sauri Madina ta bar inda take zaune ta rumgume Leila tana wani irin murna. Leila ta yi dariya.

“Are you kidding me? Ai ko mahaifinku kika yi ma magana zai canja miki aiki domin su ne manya a gobnati, amman kina ta kewaye kamar wanda bata da kowa”

“Ba haka bane, Leila na dade ina mafarkin aiki a kamfaninku Wallahi”

“Amman shi ne baki fada min ba? Haba dai Madina ina ganin kamar mun zama daya ni da ke?”

“Ai da nauyi, amman dai yanzu komai ya wuce na gode sosai zan kawo takardun anjima ko gobe Inshallah na gode sosai dear ina kaunarki”

Leila ta yi murmushi.

“Karki damu, i trust you”

“Bari na tafi kar na yi latti”

Ta fada tana daukar jakarta ta rataya, sai Leila ta rakota har gurin motarta sai da ta shiga ta bar gidan sannan Leila ta juya ta koma ciki.

BATURIYA POV.

Har ta huta ta ci abinci yayanta be dawo ba, daman idan ya fita gurin kasuwancinsa baya dawowa sai dare. Batan ta yi wanka ta fito ta tari Napep ta nufi family house dinsu.
Tana shiga cikin gidan kannenta da mahaifiyarta suka hau murna kamar su hade ta. Ko minti talati ba ta yi da zama ba, Sultan ya shigo cikin gidan da gudunsa, kanwarta ta fara tare shi ta daga shi sama yana dariya.

“Sultan kaga Mama ta dawo?”

“Tace a daina cewa Mama sai Mommy”

Ya fada da yar siriyar muryarsa yana kallon Baturiya dake zaune falon.

“Kai da wa ka zo nan?”

“Daddy yana waje”

Wani tsaki taja ta dauke kai.

“Zuwa zai yi ya fara min bakar masifar nan Ko?”

“Aa ya isa? Ai Raliya ta fada masa halin da kike ciki, ko ma haka be faru da ke ba tun da ya ga baki dawo gida ba ai ya san ba lafiya ba, dole ya daga miki kafa”

“Uhm Umma baki san halin Faruq ba, Wallahi ni da nake tare da shi kawai na san ukubar da nake sha a gidansa, zai iya zuwa a nan ya nuna babu komai sai mun koma gida ya fara min masifa”

“Bayan duk hakurin da kike da shi? Cikin yan'uwanki ke kadai ce baki dace da daki ba Rafi'a, ba mu yi zaton haka ba”

Wannan maganar da Umma tai sai ya saka Baturiya ta kara bata fuska.

“Wallahi Umma ni kadai na san azabar da nake sha a gidan Faruq, bayan yunwa ga rashin sutura da kwadayi, ga masifarsa kamar ni na dora masa talauci”

Umma ta sauke ajiyar zuciya tana kallon yarta cike da tausayawa.

“Shiyasa tun farko ni bana son auren nan na zumunci, mahaifinku ne ya dage sai an yi gashi nan ya tafi ya barki da wahala, haihuwa daya kenan nan gaba idan an tara yara me kike tunani”

“Ni ma tsorona kenan Umma, haihuwa daya, rayuwa tana ta mana haka balle nan gaba, kullum dai dai tai ta min karyar aikin zai fito amman shiru”

“Ni abun nasa har mamaki yake ba ni, wai ko dai be yi karatu mai kyau ba ne”

“Ni ina na sani, tun da ba fada zai yi ba, ni Wallahi makaranta ma nake son komawa, kar na bata nawa future na zama irinsa”

“Aiko da kin yi ma kanki abu mai kyau, sai ayi ma yayanku magana ya biya miki”

A take murmushi ya cika fuskarta.

“Da gaske Umma?”

“To miye a ciki idan ma be biya miki ba, ai ni zan biya miki”

Umma ta fi tausayin Baturiya fiye da kowa a cikin yayanta, domin ita kadai ce take auren matalauci talaucin da abun da zasu ci ma sai ya gagaresu wani lokacin. Ba wasu masu arziki ne can sosai ba sai dai suna da rufin asirin irin na yayan da suka dace da daki, domin kusan duk abun da ake ci a gidan yayyun Baturiya ne dake aure suke kawowa, sauran dawainiyar kuma babban yayansu ne yake yi, domin yana da rufin asiri irin na wanda kasuwanci yai ya aura.

“Sultan je kace Daddy ya shigo kar ya ce an barshi a waje”

Baturiya na fadi hakan Sultan din ya sauka daga kafafuwan kanwar mamansa ya nufi kofa da saurinsa, ko da ya fito Faruq na tsaye bakin karamin gate din gidan rumgume da hannayensa.

“Daddy ance ka shigo”

Faruq ya sakar masa murmushi sannan ya kama hannun dansa suka shiga cikin gidan, cike da nauyi ya shiga kasancewar baya samun riko musu komai idan zai zo, ba kamar sauran surukan ba da har mararin zuwansu ake saboda suna da rufin asiri, Baturiya ma ta sha fada masa shi kadai ne baya kawo komai idan ya zo, hakan yasa idan ba da wani babban dalilin ba baya son shiga cikin gidan duk kuwa da kasancewarsa dan'uwa, shi kansa ya san baya samun sakin fuska a gurin mahaifiyarta yadda ya kamata.
A bakin kofar falon ma tsayawa yai sai da aka matsa iso, sannan ya shiga cike da kunya ya nemi guri kusa da matarsa ya zauna bayan ya gaishe da sarakuwarsa kuma matar Kawunsa.

“Yanzu kika iso ne? Na dauka gida zaki wuce ai”

“Ko naje gida me zan yi tun da ba abinci ke akwai ba, yunwa kawai zan sha”

Juyowa yai da kyau ya fuskance ta.

“Rafi'a wannan wane irin magana ce? Idan ma kasa kike ci naga ai gidan aurenki ne”

“To karya na fada? Ni yanzu ga shi na rasa waya da sauran canjina”

“Rashin jinki ne yaja miki ai”

“Kaji ba bakar fata kawai yake min, shiyasa ai baka ma damu ka san inda nake ba sai yanzu”

Uffan be sake cewa ba ya kama hannun dansa yana wasa da shi.

“Ya kira ni ai ya tambaye ni”

cewar Raliya kanwar Baturiya. Sai mahaifiyarsu ta tashi ta nufi dakinta tana fadin.

“Allah ya kyauta”

Bayan ta wuce, Faruq ya kalli Baturiya.

“Tashi muje gida”

“Yanzu yanzu fa na shigo, sai na huta zan tafi gida”

Ta fada tana turo baki gaba tana hararsa kasa kasa.

“Rafi'a me ke damunki, sai ki rika min abu kamar ba mijiki ba, danki ne ni?”

“To idan naje gidan me zan maka? Yanzu fa na dawo ai sai ka bar ni sai na huta sannan anjima zan koma ai ban ce nan zan zauna ba”

Sanin cewar idan ya biye mata za su siyar da hali ne a gidan da ba a ganin mutunsa da kimarsa ne yasa be sake ce mata komai ba ya saki hannun Sultan ya mike tsaye.

“Raliya ki fadawa Umma na wuce”

“Okay”

Raliya ta amsa tana kallon Baturiya cike da jin haushin abun da yar'uwarta take yi a gabanta. Sai da ya fice sannan ta kalli Baturiya ta ce.

“Wallahi Rafi'a baki kyautawa, talauci ba fa ba hauka ba ne, baki san budin da Allah zai masa nan gaba ba”

Baturiya taja wani shegen tsaki.

“Ki dauki arziki ki ba shi, idan mun zauna mu kadai kin san iya abun da yake min ne? Kin san yadda yunwa take halaka mutum kuwa? Dan Allah karki kara min da wata damuwar ki bar ni na ji da wanda nake ciki”

Tana fadar hakan ta mike tsaye ta nufi dakin mahaifiyarta, Sultan ya bi bayanta.

Family house dinsu ya nufa cikin rashin jindadi, daman ta saba masa a gaban yan uwanta, yan'uwansa kam daman sun san irin zaman da suke, hakan yasa kanensa basa sha'awar zuwa gidan sai da wani babban dalili, domin bata musu tarbar arziki.
Mai achaba na sauke shi kofar gidan ya ciro kudinsa ya mika masa sannan yai sallama ya shiga cikin gidan, tun daga yanayin yadda ya ga gidan ya san ba su girka komai ba, domin murhunsu a bushe yake, a take ya ji ransa ya kara baci domin baya son ganin mahaifiyarsa a hali na yunwa, ga kuma damuwar halin da suke ciki na neman kudin aure. Da sallama ya shiga cikin dakin kanwarsa Aisha ta amsa ciki yanayi na damuwa. A bakin kofar dakin ya tsaya yana kallon mahaifiyarsa dake lullube da wani tsohon zanen gado tana ta rawar sanyi.

“Jikin ne?”

Ya tambaya da muryar dake bayyana tsananin damuwarsa.

“Haka ta kwana”

Aisha ta amsa.

“Miyasa ba a kira ni ba?”

“Ita ce kar a kiraka kar a tayar maka da hankali”

Runtse ido yai ya sauke ajiyar zuciya, ya dade a haka kamin ya bude idon ya nufi inda mahaifiyarsa take kwance ya zauna daf da ita, sai ta yaye mayafinta ta kalleshi da idanuwanta dake fassara irin tsananin zazzabin da take.

“Faruq”

“Mama damuwar nan ce kika dauka kika saka a ranki ko? Allah shi yake yin komai, kuma daman na yi tunani zamu hutar ta da kanmu da wani lefe ya bada kudin kawai a siya mata kayan daki da su”

“Ko ya bada kudin ai ba zai wuce 100k ba kuma ba zai isa a siye kayan daki ba, ko kujeru kanana yanzu sai an siye su 60k ko fiye ma”

“To ai sai a kara da wani abun idan Allah ya mana fatahi, dan Allah ki cire damuwa a ranki, Mama so kike ke ma mu rasa ki? Haba Mama”

“Damuwa dole ce Faruk bayan ta auren yaran nan akwai ta yau da kullum, yanzu ga shi abun da zamu karya ma ya gagaremu sai da na ba Asiya ta siyar da tufafina sannan zamu samu su karya, tun safe har la'asar ace bawa bai saka komai a bakinsa ba”

“Allah be manta da mu ba Mama, bayan wuya sai dadi, kuma idan ka ga tsanani yayi yawa sauki na tafe, Inshallah komai zai warware kamar ba a taba yi ba”

“Allah yasa muna da rabon jindadi ko kadan ne Faruq, lokaci tafiya yake baya jiran kowa”

Ta karasa tana runtse ido da karfi sakamakon bugawar da zuciyarta tai da karfi. Daga Aisha har Faruq hankalinsu tashi yai.

“Sannu Mama”

Kai ta daga musu cike da karfin hali har lokacin idonta na rufe saboda azabar ciwon da take ji. Ajiyar zuciya Faruq ya sauke ya mike tsaye ya bar dakin cikin damuwa, ji yake kamar ace yana da halin da zai magance damuwar mahaifiyarsa, kuma ya kaita asibiti a duba lafiyarta, amman ina? Talauci ya saka shi a gaba kamar wanda ya zagi arziki.

LEILA POV.

Rike da takardun Madina ta shiga dakin Momy ta zauna gefen gadonta.

“Momy Could you do me a favour?”

Momy ta aje plate din abincin dake hannunta ta kalli Leila dake sanye da doguwar rigar shadda ta sha aiki kamar sabuwar amarya.

“Minene?”

“Kin san kawata Madina ai...”

“Har sai kin sake gabatar min da ita? Madina ai ta zama yar gida”

“No Momy ina son ki gane cewar maganar da zan miki tana da muhimmanci ne, Wallahi ta min magana tana son aiki a kamfanin Daddy and i promise her zan saka a dauke ta”

“And....?”

Momy ta bukata tana tsattsage hakoranta na makka.

“So daman dazun na mata magana ta kawo takardunta shi ne ta kawo, da na zo naje na samu Daddy kai tsaye da maganar amman na san zai ce na bawa Talba ne, Talba kuma zai iya cewa ba zai dauke ta ba, kuma kin san be kamata na kasa yi mata haka ba, ko da ba ita ba ma a kamfanin mahaifina ya kamata ace zan iya yin komai ina da ikon yin komai”

Momy ta yi dariya.

“Leila kenan, kina abu kamar ke ce Amal, idan za a dauki wani aiki ta dalilinki har sai kin tsaya wani kame kame? Ki same yayanki Talba da maganar mana”

“No Momy ni fa bana son magana da shi sai idan wani babban abu ne, yadda yake jin kansa haka nakr jin kaina, kuma kin san zai iya amfani da wannan damar ya wulakanta ni ko ya fada min wata maganar marar dadi, idan kuma na rama ke da Daddy ni zamu dorawa laifi”

“Wannan ai da ne Leila, amman yanzu na fahimci halin da kike ciki, halin Talba sai mai hakuri da kai zuciya nesa ni kaina yanzu ya fara min ai”

“Shiyasa nake son ki saka shi ya dauke ta... ”

Tana rufe baki Talba ya kwankwasa kofar dakin sannan ya murda kofar ya turo ya shigo, juyowa tai ta kalleshi, a take annurin dake fuskarsa ya auri idanuwanta, duk yadda ta so ta dauke kai daga barin kallonsa sai ta kasa har ya karaso inda Momy take ya zauna a saman kujera, lumshe ido tai tana ta yaki da numfashinta dake ta kokarin sauya mata kamshin dakin Momy zuwa na turaren Talba da ya cika daki.

“Momy barka da dare”

“Yauwa”

Yanayin yadda Momy ta amsa masa ne yasa shi murmushi domin ya san har yanzu bata gama hucewa daga laifin da be aikata mata ba.

“Allah yasa dai ba fushi kike da ni ba har yanzu Momy?”

Uffan Momy bata ce masa ba, hakan ya saka shi kara yin Murmushi sai dai wannan karon be ce komai ba.

“Abun da kake dai ba abu ne mai kyau ba, mata aka sani da tsegumi ba maza ba”

“To ayi min afuwa ba zan sake ba, Leila...”

Ya karasa yana kiran sunanta, sai ta bude idonta a hankali ta kalleshi ba tare da ta amsa ba, daman shi ma he called her name ne kar Momy tace ta ganta be mata magana ba, duk kuwa da kasancewar ita ya kamata ta fara masa magana a lokacin daya shigo a matsayinta na kanwarsa kuma wacce zai aura, ko ba komai ai ita ce karama.
Mikewa yai tsaye sai Momy ta dauki takardun da Leila ta aje mata gefenta ta mikawa Talba. Sai da ya kalli takardun sannan ya mika hannu ya karba ya bude yana dubawa.

“Ba mu fara daukar ma'aikata ba, muna da enough”

Ya fada bayan ya dauke idonsa daga fararen takardun zuwa ga Momy.

“Na sani, saka iya replacement dinta da wani ai”

“Na dauka Madina tana aiki da ma'aikatar Alhazai ai”

“Tana yi, yanzu nan take so kuma umarni ne so nake ka dauke ta”

Ya hade yawun bakinsa, sannan ya kalli Leila da ita ma kallonsa take ya rufe takardun ya juya ba tare daya sake cewa komai ba ya fice, binsa Leila tai da kallo har ya fice sannan ta juyo ta kalli Momy.

“Thank Youu Momy”

“Karki damu, je ki samu abun da kika sakawa cikinki”

“Okay”

Ta mike tsaye ta fice daga dakin cikin jindadi. Ko da Talba ya fito Kabir na zaune kan center carpet tare da Amal suna shan kankana. Saman kofa Talba ya zauna rike da takardun yana kallon plasma.

“Malam bismilla karka ce mun maka rowa”

Kabir ya fada yana kallonshi, Talba kallonsa kawai yai ya dauke kai fuska ba yabo babu fallasa. Amal ta kalli Kabir sannan ya kalli Talba ta ce

“Ya Talba Momy ta maka fada dazun?”

Gira ya daga mata, wanda hakan yai daidai da saukowa Leila sai ya mike tsaye ya fice daga falon gaba daya.

“Strangers, ban taba ganin masoya irinku ba, wai a haka zaku yi aure?”

“Miye damuwarka ne Kabir? As long as yana so na miye ruwanka ne?”

Yayi dariya ya mikawa Amal hannu suka taba.

“Hi five Baby”

Dinning ta nufa ta bude manyan kulolin tana duba abun da Momy ta dafa, wayar dake hannunta ta aje a gefe ta dauki karamin plate ta dauka ta fara zubawa, abun ka da wanda baya son cin abinci sai ta zuba kadan ta ja kujera ta zauna. Kamar zaman ake jira tai sai ga sako ya shigo wayarta.

‘Good Night Dear’

Wani irin kasaitaccen murmushi tai bayan ta gama karanta sakon dake dauke da hoton zuciya.

“I love you”

Ta furta a zahiri, sannan ta aje wayar ta juya ta kalli Kabir dake ta rigima da Amal akan waye zai karasa shanye watermelon din da suka raga mai tawa, sai kuma ta juyo ta kalli abinci.

“Talba kana da wuyar sha'ani, wannan girman kan naka yana bani mamaki, ban taba ganin mai tsoro ko jin nakasu akan nuna soyayya ba kamar kai... But i love you..”

Ta furta tana kara jin shaukin kaunarsa na ratsa zuciyarta.

_____

Na zo muku da albishir guess what? A have alot of kayan mata masu kyau gaske, akwai na infection, akwai maida tsohuwa yarinya, akwai set din da ake hadawa

for matan da basa gane kan mazajensu, akwai na mallaka kala kala, muna kaza mai magani, tantabaru, akwai kaza mai Yasin, akwai na mallaka sirrine mai karfin gaske. Ina masu son zama madubi a gurin mazanje su? Ina matan dake cewa na gwada ban dace ba? Muna da gumba da garin magani kala kala da na tsarki ga Humra da turarunka kala kala amman fa na kayan mata.
Ga masu bukata za su iya tuntubar number na 08036126660 zan saka miki a mota na aika miki har inda kike da yarda Allah.

Serious Buyers please, idan ba ki shirya ba kar mu batawa juna lokaci.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

_____

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Seven days later...

FARUQ POV.

A gabanta ya dire kofin dake dauke da koko ya dora mata suga a saman murfin.

“Ga abun da muka samu”

Wani banzan kallo tai ma kofin ta dauke ido tana turo baki gaba.

“Koko kuma? Ni bana son shan koko gaskiya”

Kallonta kawai yai ya dauke kai ya shiga dakin ya cire tufafin jikinsa ya daura wani tsohon tawul ya fito ya nufi inda ya jona ruwan zafi a electric a juye a karamin bokitin wanka ya fita waje ya sirka ruwan sannan ya dawo falon.

“Ni fa bana son koko”

“Wani yana can yana nema be samu ba”

“Wallahi babu, ba dai sa'ata ba, sai dai tsofafi sa'o'ina kyawawa kam suna can suna neman arziki”

Uffan be sake ce mata ba ya nufi hanyar dakin.

“Ni fa ba zan sha koko ba, waina nake so da nama”

Juyowa yai ya kalleta.

“Idan ina da halin siya miki ita kin sani, kuma babu abun da zai hana na siya miki, idan kuma babu sai ki yi hakuri har Allah ya kawo”

Sai ta mike tsaye.

“Tsakani da Allah Faruq kana cutar da ni, yanzu haka zan yi ta zama cikin matsi? Kamar mu muka fi kowa? Duk wani abun da nake so baka iya siya min sai idan na siyawa kaina ko kuma an aiko min daga gidanmu, ni gaskiya na gaji kana cutar nan kuma na san Allah zai saka min domin baya son zalinci”

“Gaskiya ne, Rafi'a baki da tunani ko kadan, kan mu farau talauci? Ko kuma mutum yana yi ma kansa arziki ne? Halin nan naki ya ishe ni..!”

“Da ya isheka da ka sauwake min, da ya isheka da ka samawa kanka mafita, tsakani da Allah Faruq idan ba kaddarar aure ba babu abun da zai hada ni aurenka, daman can na dauka zaka samu aiki rayuwa ta tafi mana da kyau, ashe hauka nake, gashi na gagara samun abun da zan ci ma”

“Saki kike so?”

“Eh saki nake so, ka sake ni Faruq ka sake ni idan ka haihu”

“Zan nuna miki na haihu”

Yana fadar hakan ya wuce cikin dakin da bokitin ruwan ya shiga bandaki ya watsa ruwan ya fito ya shirya cikin kananan kaya ya dauki makullin shagonsa ya saka aljihu, dayan aljihun kuma ya saka wayarsa, ko da ya fito tana zaune falon tana jiran ya mika mata takardar sakinta, tana ganinshi gabanta yai mugun faduwa.
Be kulata ya nufi kofar fita daga falon yai ficewarsa rai a bace.
Sai da ya fita sannan ta tashi ta fita ta rufe gidan ta dawo falo ta zauna, can kuma ta tashi ta fita ta dauko ludayi ta zo ta zauna ta bude kokon ta mutsa.

“Ba zan saka sugan ba”

Ta fada tana wurgar da kullin sugan ta fara shan kokon lami ba suga, ludayi biyu tai sai gata ta tashi ta nufi inda kullin sugan ya fashe ta kwaso a hannun ta nufo

kokon ta zuba, ta zauna ta fara sha. Rabi ta sha ta bar ba Sultan dake bachi rabi, domin ta san bayan ya sha yanzu da rana ma zai iya nema.
Tashi tai ta koma saman kujera ta zauna, ta mika hannu ta dauki keypad din da Umma ta siya mata kamin ta siya mata smartphone, tsaki tai bayan ta shiga contact dinta ta fito ta shiga inbox dinta, nan babu komai domin sabun line ne da tai welcome back, hakan yasa ta ji babu dadi domin wanda ya saba rika babbar waya yana chatting idan ya rasata zai ji kamar ya koma a wata karamar duniya.

“Allah tsinewa Aljanin nan, ya dauke ni ya kai ni Kano kuma gashi nan ya rasa wayata da atm dina da yan kudina, Allah kasa min, Wallahi Faruq be da kashin arziki gashi nan na rasa komai”

Ta fashe da kuka. Kamar jira ake ta fara kukan sai ga kiran Ramlee ya shigo wayarta, share hawayenta tai sannan tai picking call din ba dan ta gane mai kiran ba domin number babu suna.

“Hello”

“Baturiya ya kike?”

“Lafiya kalau Ramlee ce?”

“Ni ce fa baki gane ni ba?”

“Number ba suna wayata ta bata ne na yi welcome back kuma numbers din ba su dawo ba”

“Garin ya? No wonder na yi ta kirankin number ki ban samu ba, na yi mamaki domin na san baki kashe waya”

A nan Baturiya ta labarta mata abun da ya faru, sai Ramlee ta saka mata dariya.

“Farin jininki yayi yawa Baturiya abun har da su Malam aljani? Shiyasa na ji muryarki wani iri kuka kike ne?”

“Ba dole ba Ramlee ina cikin matsala, ina son na ci da dadi na saka mai kyau amman abu ya garara, yanzu ko wayar nan tawa da ta bata ai daidai ne ya siya sabuwa amman sai da Umma ta siya min karama”

“Fee'at kenan, wannan fa duk kika so, da kin yarda da yanzu kin dangwali arziki har ma ki raba mijinki ciki, Wallahi Baturiya da zaki sake jiki yadda kike da kyau nan da har kyautar gida sai kin yi ma wasu”

“Ramlee ina fa da aure har da”

“Mace nawa ce mai yaya uku hudu har biyar take biyawa kanta bukatar da jikinta? Ke ko a unguwarku idan aka ce za a bude wasu matan auren ki ga sirrinsu zaki sha mamaki Wallahi, ba ki san cewa aure yana rufa miki asiri ba? Ko da kin samu wani abu ba za a zargeki ba? Yadda kike da kyau nan Baturiya ba ke ba ko ni da maza suke ganin hotunanki a wayata suna hauka sai na samu arziki, wai kin san ma dalilin daya saka na kira ki?”

“Sai kin fada”

“Wallahi wani ne ya sake ganin hoton ki yace kina cikin irin matan da yake so, na fada masa ke ba irin mu bace amman ya saka ni gaba wai na lallaba masa ke dan Allah, kuma babbar mutum ne dan siyasa, yanzu haka haka 100k ya bani wai na baki na wankan hoton da kika yi”

Baturiya ta mike tsaye tana dokan kirji idonta kamar za su fito.

“Dubu dari fa kika ce Ramlee”

“Wallahi ga su nan, tun shekaran jiya ya bani su jiya ma daker ya bar ni na yi bachi sai damuna yake da maganarki a waya kamar zai min kuka, shiyasa ma na kira ki da safen nan, Allah yasa ma mijinki baya nan”

“Baya nan ya aje min wani shegen koko ya fita”

“Kin gani yanzu da kina da kudi sai abun da ranki yake so zaki ci, idan kina free anjima zan zo na dauke ki a motata muje na siya miki sabuwar waya”

“Da kudin?”

“Aa da kudina dai, wacan kudin a cewa yai a baki kuma zan danka miki abun ki a hannu, amman ki yi tunani idan kika bada kai me kike ganin zaki samu? Bayan shi ma akwai maza da yawa musamman ace kina samun sakewa ana zuwa da ke hutu abuja ko kasar waje? Hmmmm Hajiyata ai kin take”

“To zunubin fa?”

“Allah gafurun raheem ne, kuma ban ce zaki dauwama a haka ba idan kin yi kin samu dan abun da kike so, sai ki daina amman ki yi tunanin future dinki dana yaronki koma nace yayanki na nan gaba Baturiya”

“Shikenan zan yi tunani”

“Yauwa Tawan haka nake son ji, ki yi tunanin kamin na zo kin ji? Yau ko wayar 500k kike so zan siya miki ita da yardar Allah”

Baturiya ta yi murmushin jindadi.

“Na gode kawata Allah ya bar min ke”

“Ameen Allah ya bar mu tare”

“Ameen”

Ta sauke wayar tana ta murna.

“Bari na yi sauri na gyara gidan kamin ta zo”

Ta dauki zane ta fara kabe kujerun, sai ta ji an kwankwasa kofar gidan, saurin saving number Ramlee tai sannan ta goge kiran da tai mata domin a tunaninta Faruq ne ya dawo. Sannan ta nufi kofar gidan ta bude sai tai arba da Malam Musa dilalin, cikin mutunci suka gaisa duk da kasancewar babu mayafi a jikinta sai hullar dake kanta.

“Mai gidan yana nan kuwa?”

“Aa ya fita”

“Oh dan Allah idan ya dawo ki ce masa na zo maganar kudin hayar nan, masu gida sun matsa, ko jiya da dare masifa yake ta min domin ganin yake kamar an bani kudin na kashe ne”

“Idan ya dawo zan fada masa, dazun ma yake cewa da ya ganka da ka saka masa number mai gidan domin yana son yai magana da shi”

“Indai maganar haya ne kar ma yayi domin Alhaji Sule be da mutunci ko kadan”

“Aa karka ce haka Malam Musa, bari na dauko wayar”

Kamin ya sake cewa wani abu ta juya da sauri ta koma cikin gidan ta dauko wayarta ta mika masa.

“Saka masa number a nan”

Be karbi wayar ba, ya ciro tasa wayar ya karanta mata number ta saka a wayarta.

“Idan ya zo zan fada masa sai na ba shi number”

“To yayi na gode”

Ta rufe gidan tana murmushi ta dawo falonta tana kokarin saving din number.

“Ba Alhaji Sule kake ba ko Alhaji lule kake sai na ci ubanka, talauci ya matsa shi ne kai kuma zaka kunno mana wata wutar dan kana da shegen tsohon gida”

Ta fada tana ƙwafa.

FARUQ POV.

Ya lalaba aljihunsa ya ciro naira 100 da ta rage masa ya mikawa Aisha.

“Je ki siyo koko ku sha”

Aisha ta saka hannu biyu ta karba.

“Yaya Wallahi ko jiya Mama ba tai bachi ba, yanzu ma jikinta zafi yake”

Ajiyar zuciya ya sauke.

“Jarabawa ce, ga rashin kudi, ga rashin mata ta gari, ga rashin lafiya Alhamdulillah”

Ya fada yana kallon mahaifiyarsa dake lullube bata ma san ya zo ba, karasa yai kusa da ita ya yaye mayafin data lulluba da shi ya taba jikinta sai ya ji shi da zafi sosai.

Mikewa yai tsaye ya fito daga dakin cikin wani irin yanayi na rashin jindadi. Hannunsa ya saka aljihu ya ciro wayarsa ya rike a hannu yana kallo, ya san ko siyar da ita yai kudin ba zai isa ya kai Mama asibiti ba, jinginar daya bada ma daker ya samu ya biya mutumen ya karbo wayar. Bakin kofar dakin ya zauna ya dafe kansa, yana mamakin lamarinsa wani lokacin shi kansa abubuwa suna daure masa kai, ga karatu yayi kuma ya fito da kwali mai kyau amman aiki ya gagareshi, wadanda sukai karatu tare wasu duk sun samu aiki har sun bar kasa, wasu kuma suna Abuja wasu a manyan mukana gobnati wasu a manyan bankuna da kamfani amman shi ya kare a shagon Barber, shi ma daker ya samu wani kawunsa ya bude masa shagon.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Allah ka kawo mana sauki”

Ya furta yana dago kansa ya shiga contact dinsa ya nemo number abokinsa kuma amininsa Nura.
Wayar bata dade tana ringing Nura ya dauka.

“Hello Faruq”

“Na'am Nura ya gida?”

“Lafiya kalau kwana da yawa”

“Sai godiya, ina su Sakina”

“Lafiya kalau”

“Wallahi Nura ina cikin matsala”

“Subhanallahi miya faru?”

“Abubuwa da yawa, yanzu dai wanda ya fi damuna rashin lafiyar mahaifiyata, kudi nake so rance idan zan samu na kaita asibiti”

“Kash.... Wallahi Faruq yau da 500 na tashi na basu su karya, ka san abu ga ma'aikaci idan ba albashi akai ba, ba mu da kudi, kuma gashi albashin na jihar zamfara sai a hankali anki a gyara mana, ga kayan masarufi sai tashi suke, abun da zaka siya da 20k yanzu sai 40k shiyasa albashin baya mana auki”

“Haka ne, Allah ya sauwake”

“Ameen, amman da zaka iya da kaje gidan Alhaji Mu'azu Shimkafa ance suna da Foundation na taimakon marayu da mabukata, amman idan baka jin kunya kasan wasu basa son zuwa irin abu na neman taimako”

“Haba Nura ina zancen kunya ga mai nema, suna nuna mutun a tv ne?”

“No babu ma wanda zai san an maka, amman ance Dattijon yana taimako sosai gaskiya, ban san yadda ake bi ba, amman dai idan kaje can gidansa ba rasa taimakon da zai maka ba, har aurarwa suna yi ga marayu su masu komai”

“Ai ban sani ba, ina dai jin ana fadarsa Tsohon Minister kudi ko? Ban san yana taimakom nan ba Wallahi, amman zan je yanzu Inshallah na gode sosai”

“Allah yasa a dace, ya bata lafiya anjima zan shigo na dubata Inshallah”

“Okay”

Ya dauke wayar daga kunnesa ya mike tsaye da sauri sai a lokacin ya tuna da be tambayi unguwar da yake ba. Hakan yasa ya sake kiran number Nura.

“Baka fada min sunan unguwar ba?”

“Shimkafi Road, kana shiga unguwar kace gidan Alhaji Mu'azu Shimkafi kake nema, za a nuna maka”

“Okay”

Ya saka wayar aljihu be ma koma cikin gidan ba ya nufi titi, da kafa ya taka tun daga gadar gaba har unguwar Shimkafi road, akwai tazara amman a haka yai ta cin kasa saboda babu ko naira aljihunsa.
Kamin ya karasa shiga cikin Quarters din wayarsa tai ringing, yana ciro wayar ya duba, a take gabansa ya fadi ganin number Malam Musa Dillali, hakan nan dai ya daure ya dauka.

“Hello”

“Hello Faruku haka ake daga karbar number sai ka ba matarka ta ciwa mutun mutunci?”

Tsaya yai daga tafiyar da yake fuskarsa da mamaki.

“Wane mutum kuma?”

A nan Malam Musa ya fada masa yadda sukai da Baturiya dazun sannan ya dora da abun da mai gidan ya fada masa.

“Wata kila kiransa tai ta ci masa mutunci, yanzu ya kira ni yana ta masifa wai wata ta kira shi Baturiya ta zage shi, ya baku daga yau zuwa gobe ku tashi ku bar masa gidansa”

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Wallahi Malam ban san Matata zata yi haka ba, kuma Wallahi ban ce zan karbi number sa ba”

“To yanzu dai sai ku san abun ba, Baturiya ko balaraba ta ja maka”

Malam Musa na fadin haka ya kashe wayar, Faruq ya dafe kansa.

“Na shiga uku wai me ke damun Rafi'a ne? Ta sake janyo mana wata fitinar kuma? Ina ruwanta da mai gida?”

Wani irin kololon bakinciki ne ya taso masa, sai ya ji kamar na runtse ido ya bude a gansa a kabari ya huta, yana fama da wasu matsalolin yanzu kuma ta ballo masa wani.

“Wallahi yau sai na miki mugun duka, Rafi'a sai kin dawo hayyacinki in ma baki da hankali sai kin yi shi”

Ya fada rai a bace, duk abun da take masa na bacin rai bata taba mata masa rai irin wannan ba, domin be san inda zai je ba idan ya bar gidan haka nan ya cigaba da tafiya ransa a bace. Da tambaya ya aka nuna masa kofar gidan Alhaji Mu'azu Shimkafi, Gate din gidan kadai a abun kallo ne, balle kuma farar ginar da aka kawata da farin fenti ga shuke shuke itatuwa da fulayoyi, idan ka daga kanka kuma sai ka hango gidan sama daga can cikin gidan an kawata ko'ina da gilasai komai a tsare kamar ba za a mutu ba. Faruq ya girgiza kai.

“Allah man yasha'u, ka baiwa bawa ba dan kana son shi ba, kuma ka hana Bawa ba dan baka son shi ba, Allah ka bamu na mu arzikin na halal, yanzu nan gidan mutum daya ne”

Ya fa da yana mamakin tarin dukiyar dake gidan. Karasa yai bakin gate din yana kallon security cameras daka laka hagu da dama na gidan sannan ya kwankwansa kofar gate din. Ba dade wani police ya bude masa yana sanye da uniform dinsa.

“Malam Lafiya?”

Faruq ya mika masa hannu suka gaisa cikin mutumci.

“Dan Allaj ina son ganin mai gidan ne matsala ce da ni”

“To ganin mai gidan a yanzu ai, sai an jira domin be fito ba, idan zaka iya jira a nan wajen idan ya fito sai ka tare shi da matsalarka, duk dai baya son a ana mishi haka amman karka nuna masa na san da zuwan ka”

“Ba Matsala na gode sosai”

Faruq ya nemi wani gurin ya zauna a nan kusa da gate din, shi kuma police din ya koma cikin gidan ya maida gate din ya rufe. Be yi minti talatin da zama ba, aka sake bude gate din sai dai wannan karon gate din gaba daya aka bude ganin mota zata fito yasa yai saurin mikewa tsaye a zatonsa mai gidan ne sai ya nufi motar da sauri, ganin ya nufota yasa ta tsaya ta sauke gilashin motar tana kallonsa.

“Ya akai?”

“Daman na dauka mai gidan ne shi nake son gani”

“Saboda me kake son ganinsa?”

Ya tambaya tana kare masa kallon from head to toe.

“Taimako nake nema”

Hannu ta saka ta cire katon gilashin idonta.

“Okay idan ana neman taimako sai azo har kofar gidan mutum a takura masa? Baka san yadda zaka bi ta Foundation ba? Ba ma taimako a gida sai ta karkashin kungiya, kaje can ka samu kungiya karka sake zuwa nan, Talauci ba hauka ba ne”

“Haka ma Arziki ba hauka ba ne malama, karki nemi fada min maganar banza saboda na zo nema a gidanku, ni ba wulakantaccen ba ne”

“Really”

Ta bude motar ta fito tana masa wani banzan kallo.

“Dubi ka! Ka zo nema a gidanmu kuma kana cewa kai na wulakantacce ba ne? To waye kai? Kai kama isa ka zo nema a gidanmu kuma fada min maganar banza?”

“Maganar banza ana furtata ne a lokacin banza kuma ga mutanen banza irinki”

“Ni…”

Ta nuna kanta Faruq ya daga mata kai cikin bacin rai daman be gama wankewa daga na matarsa ba ita kuma tana neman kara masa wani, hannu ta daga zata mare shi sai ya rike hannun da mugun karfi ya jefar da shi.

“Kika kuskura kai hannunki a fuskata sai na illataki, dan ina neman taimakonku ba shi zai baku damar wulakanta ni ba”

Bata sake ce masa komai ba ta juya da sauri ta isa gurin gate din ta buga da karfi, daman Police din ya rufe gate din a lokacin daya bude mata ta fita, da sauri ya bude sai ta nuna masa Faruq.

“Ku rike mutumen can”

Da sauri ya fito shi da wasu Police din biyu suka nufi inda Faruq yake tsaye suka rike shi, ita kuma ta nufi cikin gidan da saurinta kamar zata tashi sama, Talba dake kokarin tashin motarsa yana kallonta ta danna door bell din kofar be kula ta ba ya ja motarsa zuwa gate ya hanna horn, dai dayan Police din ya dawo ya bude masa gate din ganin suna rike da Faruq ga kuma motar Leila dake bude a kunne yasa shi tsaya ya sauke gilashin motarsa.

“Lafiya?”

“Wallahi ba mu san abun da ya faru ba, Hajiya Leila ce tace a rike shi”

Talba ya kalli Faruq daga sama har kasa, be masa kama da yan ta'addaba, kuma ya san halin yar'uwarsa mafi akasari fadan da take da mutane ita ce bata da gaskiya. Hakan yasa shi tambayar Faruq dake kokarin fisge kansa daga rikon da Police din suke masa.

“Malam Lafiya?”

“Lafiya ce zata saka Police rike ni? Daman idan za ku taimaki mutum sai kun wulakanta shi”

Faruq ya fada cikin fusata, hakan yasa Talba ya bude motar ya fito ya nufo inda suke tsaye.

“Ku sake shi”

Ya fadawa Police din sai suka saki Faruq, Talba ya saka hannayensa aljihu yana kallon Faruq.

“Bari na fada maka wani abu, ba a min tsawa kuma ba a fada min bakar magana, amman na maka uzuri saboda na fahimci kana cikin bukatar taimako ne, and bana son na yi ma mutun wani abun ta dalilin taimako, da ace a hanya na hadu da kai da zan iya maka cin mutunci fiye da kima, now tell me miya faru”

Kalaman da Talba yai yasa Faruq sasautawa zuciyarsa domin ya fahimci ba fada Talba yake son yi da shi ba, idan ma sun yi fadan ba riba zai ci ba.
Cikin bacin rai Faruq ya fadawa Talba abun da ya faru, sai Talba ya girgiza kai ya lumshe ido ya bude, ba dan baya iya bawa kowa hakuri ba, da sai ya bawa Faruq, domin ya fahimci halin da
yake ciki.

“Ka manta da abun da tai maka yanzu fada min wani iri taimako kake so?”

“Mahaifiyata ce ba lafiya”

Faruq ya fada domin yana jin cewar shi ne kawai abun da zai iya fada a halin yanzu, kasancewar shi ya fi damunsa. Talba ya juya ya koma cikin motarsa ya bude ya shiga ciki ya zauna, wani karamin diary ya dauko yai rubutu akai, sannan ya bude wani guri a cikin motar ya dauko 100k ya fito ya nufo Faruq.

“Ga wannan Allah ya bata lafiya, and idan kana neman taimako a foundation din Mahaifina ka tuntubi wannan number, su za su tantance komai su sanar mana”

Ya mika masa number bayan ya bashi kudin. Faruq ya saka hannu biyu ya karba cikin jindadi.

“Na gode sosai Allah ya saka da alheri, ya kara sutura”

Uffan Talba be ce masa ba balle har ya amsa da Ameen, sai juyawa yai ya nufi motarsa, yana kokarin shiga yaji dayan police din na fadin.

“Hajiya tace a rike shi, ku rike shi”

Juyowa Talba yai ya kalli Police din, sai suka fasa rikon Faruq.

“Hajiya Babba ba Leila ba ita ta kira ni yanzu”

Da kai Talba yai ma Faruq alama daya wuce sannan ya shiga motarsa ya danna horn suka sake bude masa gate din yai ribas ya shiga cikin gidan. A harabar Entrance din ya faka motarsa sannan ya fito ya nufi kofar falon kamin ya karasa sabuwar mai aikin Momy ta bude kofar da sauri da alama fitowa za ta yi.

“Yauwa ranka ya dade Hajiya tace na kira ka”

Shiga yai cikin falon hannayensa zube a aljihu sai kamshi turare yake zubawa, tsaye ya samu Momy Leila na gefenta dayan mai aikin Momy Zulai tana tsaye nesa da su, domin wannan karon har masu aiki biyu Momy ta dauka. Yana kallonta ya san ranta a bace yake, can kuma ya kalli Leila da ke hawaye, kamin ya kalli Kabir dake zaune rike da waya yana kallonsa.

“Talba haka zamu zauna mutane suna ci mata mutunci kana daukar side dinsu”

“Ta fada miki Abun da tai masa?”

“I don't care, amman komai tai masa ai be kamata ya rike hannunta ba, har ya fada mata bakar magana alhalin shi yanzo nema a gidansu, har kuma ka bar shi ya tafi”

Talba be ce komai ba, har Mairo ta shigo tare da police din da Momy tasa ta kira daman shi da Talba ta ce ta kira. Yana shigowa Momy ta nuna shi da yatsa.

“Wannan ya zama na karshe da wani zai zo ya takura mana kofar gida, karka sake barin kowa ya shigo mana ba tare da saninmu ba, idan makamancin haka ya sake faruwa a bakin aikinka, ba wai a gidan nan kadai ba, no ka daina saka Police Uniform kenan har a bada mark my words”

“Ayi hakuri ranki ya dade Inshallah zan kiyaye”

Cewar police din sannan ya juya ya fita. Da ido Talba yai ma Mairo da Zulai alamar su fice daga falon sai suka fice da saurinsu.

“Wannan abun yayi yawa Momy, ya kike Leila ta zama? Ba fa Amal bace, taya Leila zata raini yara masu tarbiya idan tana wannan halayyar? Saboda wani ya zo nema daga abun da Allah ya wadata mu da shi sai ya zama abun wulakantawa? And ji yadda kike fadawa Police din nan magana kamar wanda yai wani babban laifi”

“To ya kake son na yi? Haka zamu yi ta zama Leila bata da yanci a gidan nan? Haka zaka rika mata idan kun yi aure ka bar ko wane kare da biri suna cin zarafinta? Shi ne jindadinka?”

Talba ya kalli Leila cikin yanayi na rashin jindadi.

“I wonder what kind of woman zan aura! Akwai karamci tarbiya a tare da ke, ba zan iya daukar wannan halin na ki ba kina bukatar ki canja rayuwa Leila...”

“Kai kake bukatar canja rayuwa ba ni ba...”

Ta fada mishi kai tsaye sannan ta nufi upstairs. Momy ta kara da nata.

“Kana fada min Leila bata da tarbiya ko? An maka dole ka aureta ne? Ko kuma kana son ci min fuska ne Saboda ba ni na haife ka ba?”

Talba ya kalleta da sauri, Kabir ma mikewa yai tsaye sai a lokacin ya saka bakinsa a maganar.

“No haba Momy... ”

Momy ta daga masa hannu.

“Na san abun da yake nufi, duk abun da kake kana yi ne saboda ba ni na haife ka, kuma na sani, daman tsintacciyar mage bata taba zama mage ba, amman karka manta ni na raine ka, ko da ka bude ido baka san mahaifiyarka ba ni ka

sani, na raine kamar uwa, so weather you like it or not I'm still your mother, karka manta da wannan...!”

Tana kaiwa nan ta nufi upstairs ya bita da kallo kalamanta na ratsa kowane lungu da sako na zuciyarsa. Leila ma da bata karasa hayewa ba juyowa tai ta kalleshi cikin yanayin da ke nuna bata jidadin kalaman Momy ba, balle kuma Kabir da ya tsaya kamar hoto yana kallon dan'uwansa cikin yanayi na rashin jindadi.

<<<<<>>>>>

Na ce ba? Baturiya ko ba indiya ta taro mach da Faruq yau

Anya Leila zata ga Annabi kuwa? 😊

Momy ta kyauta a kalaman da tai ma Talba saboda Leila?

Wai ina Aminatun mu ne?

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Juyawa Talba yai ya fice daga falon, sai Leila ta sauko da sauri zata bi bayansa, kamar wanda ta tuna wani abu sai kuma taja ta tsaya cikin yanayi n rashin jindad

“Yanzu ai kin jidadi ko?”

Kabir ya tambaya yana gyara shirt din jikinsa. Sai ta kalleshi cikin yanayin damuwa domin har ga Allah bata son Talba ya shiga damuwa duk kuwa da irin son da take ya canja bata son ace saboda ita Momy ta yi masa Wani abun bacin rai domin ba su saba haka.

“Wane irin dadi kuma? Kana jin kalaman da Momy ta fada masa fa”

“Eh ai ke kika ja, ke dai burinki wulakanta mutane”

Yana kaiwa nan shi ma ya nufi kofar fita falon cikin bacin rai, duk irin rashin jituwar da suke samu da Talba baya son wani abun bacin rai ko damuwa ta same shi, kamar yadda Talba ma baya son ganin bacin ran Kabir sai dai dukansu sun san cewa ba a komai na rayuwa suke shan inuwa daya ba, musamman ma Talba da yafi kowa girman kai a gidan.
Juyawa tai ta hau stairs din ta nufi dakin Momy, ko knocking bata tsaya yi ba ta tura kofar ta shiga kamar zata fasa kuka.

“Haba Momy wannan abun har ya kai ki fadawa Talba irin wannan maganar ne?”

Momy dake zaune gaban madubi tana kokarin cire awarwaron hannunta ta juyo ta kalleta da mamaki.

“Ba ki kalmar da yake jifata da ita ba?”

“Da ni yake ba da ke ba”

“No cewa yai baki da tarbiya, kai tsaye na fahimci inda kalamansa suka dosa, tun ba yau ba ai na lura da yadda ya canja kamar mai son yai kishi da ni”

“Haba Momy Talba ne zai yi kishi da ke?”

“Eh mana, bakisan wasu yayan suna tsanar iyayen da ba su haife su, Idan ba haka ba ai ba zai min kalaman banza ba, ko ba komai ni surukarsa ce right”

“Momy yanzu zai ji babu dadi Wallahi ransa zai bace”

“Ran nasa ya dade be bace ba, wannan wane irin so ne kike ma Talba wai? Shi fa baya son ki kamar yadda ke kike sonsa, kuma naga ke ma ai kina bata masa ran”

“Eh amman Momy wannan ai matsalar mu ce ta dabam ba wai akan ba”

“I don't care, idan ke baki san zafin abun da ya fada ba ni na sani”

Mikewa tai tsaye cikin yanayin damuwa ta fice daga dakin tana ta sake sake, ko ta kira ta bashi hakuri akan abun da Momy tai ko kuma ta kyale shi, sai dai idan ta tuna cewar saboda ita komai ya faru sai ta ji wani iri.
Dakinta ta shiga ta dauki wayarta ta kira Madina ta labarta mata abun da ya faru, daman komai na duniyar ba zata iya boyewa Madina ba, no matter how Momy ta kwatseta akan abu sai ta fadawa Madina.

“Amman Leila baki taba bata min rai irin yau ba, wai miyasa kike barin zuciyarki tana aikata abun da Talba baya so? Ke baki san yadda zaki faranta masa rai ba? Haba Leila ni kam da baki labarta min wannan abun ba da ban shiga damuwa ba Mtchssssss ”

Ta yanayin yadda Madina take mata responding kadai ya isa ya karantar da ita cewar Madina ta fita shiga bacin rai ma.

“Ni ma fa ban jidadi ba, that's why na kira ki ko zan samu mafita”

“Mafitar me? Ni Wallahi kin bata min rai, i don't think i can eat today, kin bata ran bawan Allah, na sha fada miki haka rayuwarsa take ki bishi a haka mana sai ku samu zaman lafiya amman kin gagara daukar shawarata”

“Look Madina na yarda a nan ina da laifi daya janyo aka fada masa magana marar dadi, amman maganar Allah ban ga laifi a abun da na yi ba, Talba yana shigar min hanci da yawa fa”

“Yanzu dai na ji, idan kina son mu shirya da ke kije ki bashi hakuri”

“Na bashi hakuri fa? Gaskiya ba zan iya ba”

“To miye a ciki, ke fa kika ja komai, kuma ba akan abun da yai miki fada zaki bada hakuri ba, akan abun da Momy tai masa”

“Zan ga idan zai yiyu”

“Please do this for me, tsakani da Allah ko kadan bana son na ji ran Talba ya bace, Mutumen yana son ki Leila kin kasa ganewa ne, kina raina yadda rayuwarsa mata da yawa suna can suna sonsa a haka, ki bi a hankali”

“Na ji”

Ta fada tana juya ido, bata tsaya jiran abun da kawarta zata sake fada ba ta yanke wayar ta wurgar saman gadonta, sannan ta fadi kwance.

TALBA POV.

A lokacin daya fita daga falon cikin motarsa ya nufa ya zauna, ba karamin taba shi kalaman Momy sukai ba, duk yadda ya so ya ga laifin kansa kan abun da yai ma Leila sai ya kasa, zuciyarsa nata raya masa a daidai yake, hannu ya kai ya dauki wayarsa ya kira Ali.

“Hello”

“Kana ina?”

“Office ya akai?”

Iskar dake bakinsa ya busar ya kashe wayar ya aje gefensa sannan yai ma motar key yai reverse ya danna horn, tun kamin ya isa gate suka bude masa sai da ya fito ya ga motar Leila dake waje har lokacin sai dai wannan karon an kullenta amman motar tana kunne, horn ya danna har sau biyu wanda hakan ya saka

Bello Police lekowa ya nufo motarsa da sauri, sai ya sauke gilashin motar ya nuna masa motar Leila, Bello na ganin ya nuna motar ya san abun da yake nufi na sai ya masa magana ba. Sai ya nufi motar Talba kuma ya hau titi, driving yake kamar wanda be san inda zai je ba, kadan kadan yake lafiya har ya isa asibitin FMC a inda ya saba fakin ya faka motarsa ya fito yana jin kamar ya juya ya tafi gurin aikinsa sai dai ya san he need someone to talk to, a duk lokacin daya shiga wata damuwa komai kankantarta Ali yake fara fuskanta ya fada masa damuwarsa duk kuwa da kasancewar wani lokacin za su rabu a fada ce ne. Kai tsaye office dinsa ya nufa and he got lucky Ali yana ciki sai dai office din ba shi kadai ba ne tebur biyu ne na dayan abokin aikinsa. Ko kallon gefen da abokin aikin na Ali yake be yi ba ya nufi teburin Ali ya zauna a kujerar baki. Ali na kallon abokinsa ya fahimci akwai damuwa.

“Leila ce ko?”

Talba ya dago ya kalleshi, sai kuma ya juya ya kalli teburin abokin aikinsa sai a lokacin ya lura da be shigo ba

“No”

Ya amsa masa cikin yanayin damuwa.

“Na san dai abu ne mai wahala yadda Daddy yake ji da kai abu ne mai wahala ya bata maka rai, sai dai idan wata damuwa ce ta dame shi a san zata iya shafarka”

Ajiyar zuciya Talba ya sauke, sannan ya labatawa Ali abun da ya faru. Ali ya kwanta jikin kujerarsa yana kallon Talba duk kuwa ya san kallo na daga cikin abun da abonkinsa ya tsana.

“Momy dai ta fusata ne, kuma kai ke da laifi”

“Amman Ali ban yi dan taji haushi ba, ba ina nufin bata bawa Leila tarbiya ba, kawai bata fahimci ni ba”

Yana fadar hakan ya mike tsaye ya nufi windows din office din.

“Kuma na ji babu dadi, na san ba ita ta haife ni ba, amman ban taba mata wani kallo na dabam na bayan uwa, ita ta raine ni a hannunta na tashi na girma”

“Kai ka ji zafin abun da ta fada maka balle ita? Yanzu dai ka manta da komai ka dauka cewar kuskure ne irin wanda kowa yake yi”

“And seriously ba zan iya zama da Leila da wannan halin ba”

“Kai da za a bibiya zata ce ba zata iya zama da kai saboda halinka ba, Talba dan adam duk tara ne be cika goma ba kowa ka ganin yana da inda be cika ba, abun da zai fi kawai ka dauke idonka daga gareta, musamman a yanzu da ka fahimci idan ka taba ta ran Momy yana baci, ka bita a yadda take sai a samu zaman lafiya”

“And… ”

“And ka koyi bada hakuri Talba, ba zaka ragu ba, mata rarrashi suke so, yanzu duk wannan abun daya faru idan ka koma gida ka yi kamar komai be faru ba, ka samu Leila ka lallabata ka bata hakuri”

“Ba a hallici wannan macen da Talba zai bawa hakuri ba, ba ayi mace da zan yi ma yar murya ina lallabata akan tai hakuri ba, matukar tana kasa da ni”

“Ya kamata ka sauke wannan nauyin daka dorawa kanka Talba life is very simple”

Talba ya juyo ya kalleshi.

“Ko?”

Sai Ali yai dariya domin ya san halin abokin nasa yanzu zata iya bare musu su fara siyar da hali.

“Yanzu dai forget about it, akwai maganar da nake son mu yi da kai”

Talba ya juya ya cigaba da kallon harabar asibiti da yadda mutane suka zirga zirga sai dai hankalinsa da ears dinsa suna gurin Ali.

“Akwai wata yarinya da aka kawo last week, tana cikin mutanen da yan bidiga suka raunata”

Yana tsaka da maganar sai kuma yai shiru yana duba wata takarda dake gabansa.

“To ta ina alakarta ta shafe ni?”

Talba ya tambaya ba tare da juyo ba, jin Ali ya dauko masa wata maganar da be san ta inda zata masa amfani ba. Murmushi Ali yai yana jinjina halin abokin nasa.

“Tana bukatar taimako ne sosai gaskiya”

Juyowa Talba yai ya rumgume hannayensa yana kallon Ali.

“Kai ina zuciyar taimakonka ta tafi ne? Ko baka taimako?”

Ali yayi dariya.

“Talba kasan irin taimakon da na yi mata? Tun da aka kawo su ba Gobnati bata sake waiwayarsu ba, babu wani tallafi da ake kawo musu, mostly yan uwa da iyaye ne suke daukar nauyinsu, sisin kwabo babu daga gobnati komai daga alijunsu dana yan'uwansu yake zuwa, wasu an sallame su sai dai wadanda albarushi ya shiga jikinsu ne kawai suke nan suna jinya har yanzu”

Ya hade yawun bakinsa sannan ya cigaba.

“But yarinyar har yau babu wanda ya taba zuwa nemanta, babu wani da yazo yace shi babanta ne ko yayanta, komai da ake biya daga aljihuna ya fita na taimaka mata saboda ta bani tausayi sosai”

Ganin Ali yana maganar babu alamar wasa a tare da shi yasa shi tambayar abun da yake son ji daga gareta.

“Miya same ta?”

“Na farko dai she can't walk, she can't talk tun da aka kawo ta bata taba magana ba, idan dare yayi sai na yi mata allurar bachi sannan take iya bachi, kuma na yi na yi da ita ta ki tai magana, babu wata alama data nuna yarinyar tana magana, idan ma kaga ta motsa to na matso kusa da ita ne da allura, sai ta fara kallon allurar tana hawaye, and the most sadness part is an yi mata fyade sun lalatata ko mai haihuwa iyaka kenan”

Kusan a lokaci daya komai dake aiki a zuciya da jinin Talba ya tsaya cak na dakiku. Kalmar fyade wata irin babbar kalma ce mai razanarwa da muni a kunnuwan tsabtattacin mutane irin Talba, shi din namiji ne ba mace ba, amman ya tsani jin duk wani abu daya shafi fyade balle kuma fyaden kansa, be taba ganin Aminatu ba, labarin wanzuwarta be taba ziyartar kunnensa ba, kamar yadda zuciyarsa da tunaninsa ba su hasaso masa mai irin rayuwarta ba, wani abu daga cikin cikin tausayinta ya kusa zuciyarsa ya samu guri a kusa da kirjinsa ya zauna, hankalinsa ya kara tashi sosai a lokacin da Ali yake kara fada masa halin da yarinyar take ciki.

“I don't think kurma ce, domin idan na ce kee zata kalleni amman bayan haka bata yin komai, na sha jera sunaye ina kiranta da su amman bata taba min wata alama da zan gane sunanta ba, kuma kafanta ya kumbura wanda hakan ke nuna ta yi tafiyar da ta wuce kima kuma ta taka abubuwa da yawa gaskiya yarinyar tana bukatar taimako”

“Ta ina ya kamata na taimaka? Irin mutanen kamata yai ace gobnati tana daukar nauyin maganinsu fa”

“Wallahi kuwa ni ma abun da nake fada kenan amman sai kaga an barsu kara zube ba a kula su. Yanzu dai tana bukatar a duba lafiyar duka jikinta, a kula da kafafuwanta, private part dinta dai yana samun sauki sai dai da zata samu wanda zai kula da ita da zata fi samun sauki”

Ali na kaiwa nan ya mike tsaye.

“Zo muje ka ganta”

“No ba sai na ganta ba, kasan akwai mutane sosai a gurin nan”

“Haba dai irin abubuwan nan suna karawa mutum tsoron Allah, Allah kadai ya san halin rayuwar data shiga, ni ba abun da ya fi bani tsoro kamar rashin maganar ta, kuma gashi har yau babu wanda ya taba zuwa nemanta, and bata kallon mutane idan zan shiga inda take har na yi abun da zan yi na gama ba zata kalleni ba sai idan na dauko allura, and wani lokacin sai kaga hawaye na sauko a idonta, idan aka aje mata abinci bata ci yadda ka bar shi haka zaka zo ka tararda shi, idan ka danka mata abu a hannu bata rikewa”

“Ya ake take rayuwa bata cin komai?”

“Ta hanyar allurar da maganin da muke saka mata a drip”

Talba ya lumshe ido ya bude.

“Mutanen nan suna ganin rayuwa, farincikin da suke so, kadan ne amman ya gagaresu, a kashe su, a kwashe dukiya a kune kuma wandanda aka raunata a bar su da daukar nauyin kansu, Allah kadai ya san abun da akai mata ko ta gani”

“Wallahi ai mu muna ganin abubuwa sosai”

Ali ya nufi kofa Talba ya bi bayansa sai suka fito tare suka jera zuwa gurin da ake aje marasa lafiya, suna tafe Ali na masa hirar wasu da aka kawo da yadda sukai ta fama da su, Talba dai be ce Uffan ba har suka shiga female ward din suka doshi gado na 36 da inda Aminatu take kwance. Ko da suka isa sun tarar an ja mata lalube gurin da take, an rufe ta ta ko'ina ta yadda bata ganin kowa kuma kowa baya ganinta. Ali ne ya fara daga labulen ya shiga sannan Talba ya shiga. Kwance suka same ta idonta a rufe hawaye na saukowa ta gefen idonta. A zatonsa babbar mace ce sai da ganinta yarinya mai kananan shekaru yasa jin tausayinta ya karu da kashi talatin cikin dari, domin ya san fyade na daga cikin abun da yake lalata rayuwar ya mace, kuma yana daga cikin abun da mace tafi tsana balle kuma wannan da take karamar yarinya. Ali ya saka hannu ya dauki safar dake gurin ya saka a hannu sannan ya taba kafarta sai ta bude idonta da suka yi ja da alama ta dade tana hawayen ta sauke su akan Talba dake kallonta fuskarsa cike da haiba da annuri. Shi ma kallonta yake ba yabo ba fallasa, daga can cikin zuciyarsa cike take da tausayinta sai dai jinkai da rayuwarsa daya daukarwa kansa ya saka ya kasa barin hakan ya bayyana a kyakkyawar fuskarsa.

“Da son samu ne, a ware mata daki daya ita kadai saboda halin da take ciki, so that ta samu kulawa ta musamman kuma tana bukatar ayi mata gwaje gwaje, tana ma bukatar jini”

Ali ya fada yana kama hannunta ya tabawa. Har lokacin Aminatu Talba take kallo ji take kamar ta taba ganinsa a wani gurin sai dai bata san ko'ina ba ne, ji take kamar ta bude baki tai magana sai dai bara da kuzarin yin haka, kamar yadda take jin jikinta be da kuzarin riketa balle har hannunta ya jimke wani abu, tabbas yanzu kam ta tabbatar da kalamanta sun kare, kamar yadda take jin komai na rayuwarta a yanzu ya zama tarihi, bata yarda ita ce dai wacan Aminatun dake rayuwa a karkara tare da iyayen da yan'uwa ita ce a nan ba.
Da ace zata iya bude zuciyarta ta sun yi arba da tarin bakinciki da duhu zuci, wanda idan suka karanta wata kila likitan zai tausaya mata ya daina bata taimakon da yake bata na drip da allurar so that ta samu ta huta ita ma tafi sahun yan'uwanta da iyeyenta. Har gobe tana jin karar bindigar da aka kashe mahaifinta da mahaifiyarta a cikin kanta, ta kasa manta yadda yan ta'addan suka rika yawo a jikinta a lokacin da suke kokarin keta rigar mutuncinta, idanuwanta sun ki su goge hoton fyaden da akai ma mahaifiyarta a gaban ido wai shin miya rage mata? Miyasa take a raye har yanzu?

Ali ya kalli Talba dake tsaye ya kalli Aminatu data kafe Talba da ido, a zahiri shi take kallo, a badini kuma rayuwarta bayan take hange a cikin idanuwan mutumen da take jin kamar ba a yau ta taba arba da shi ba. Har lokacin hawaye ba su daina zubar a idonta ba.

“Kallon mutane ba dabi'ar bace ko dai ta san ka ne?”

Ali ya tambaya, kallonsa kawai Talba yai ya dauke kai.

“Kin san shi ne?”

Bata dauke ido daga kallon Talba da take ba balle har ta kali Ali ta amsa masa. Ali ya kalli Talba dake kallonta shi ma har lokacin.

“Ka yi mata magana wata kila zata amsa”

“A canja mata daki idan kana ganin hakan ya dace, idan ka yi list din ko nawa za a ashe sai ka fada min”

Shine abun da Talba ya fada sannan ya sakar ma Aminatu murmushinsa mai tsada kadan wanda yafi kama da na yake ya juya ya fice. Yana fita sai ta lumshe idonta kamar mai bachi sak rayuwar da take a gidansu ita da iyayenta da yan'uwanta ya soma kawata idonta dake rufe. Juyawa Ali yai ya fice yana kokarin cire safar hannunsa.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min. Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

BATURIYA POV.

Bayan ta gama zazzagawa Alhaji Sule rashin mutunci ta shiga tai wanka. Ta shirya cikin farin lace sai aikin gogawa fuskarta powder take, can kuma ta mike tsaye tana kallon kanta a madubi, sai ta ji ana kwankwasa gidanta, jiki na rawa ta aje soson hodar dake hannunta ta fice daga dakin da sauri taje ta bude gidan domin ta san da zuwan Ramlee.

Rumgume juna sukai ita da Ramlee kowa ne na murnar ganin wani kamar wadanda suka shekara basu saka junan a ido ba.

“No no ba dai lace din nan kika saka ba? Ai yanzu kuma kin wuce saka kananan kaya”

Ramlee ta fada tana yatsina fuska

“Ke mai tsada ne fa, yayata ta ba ni shi, mai kudi take aure fa”

“Baturiya kenan yanzu ai kin wuce wata ta kwance ta baki ki daura, sai dai ke ki kwance ki bawa wata ta saka, ga wata abaya nan na zo miki da ita kamin mu fara zuwa siyayen tufafi masu tsada”

Ta karashe tana mika mata jakar dake dauke da abayar, wani irin tsalle Rafi'a tai ta dire tana murna.

“Amman Wallahi kina da zuciya mai kyau, kamar kin san ina mararin abaya”

Ta karba da sauri ta nufi cikin dakinta sai Ramlee ta bi bayanta tana murmushi, a falo ta zauna har sai da Rafi'a ta canja tufafin jikinta daga lace zuwa sabuwar abaya, ita kanta ta yaba yadda bakar abayar tai mata kyau kasancewarta fara, cikin zumudi ta nufo falo.

“Allah ya miki sura Baturiya Wallahi kina da kyau”

Ramlee ta fara tana kallonta.

“Wallahi zaki sha kudi, manyan masu kudin nan suna son fararen mata amsu kananan shekaru”

“Da gaske?”

“Uhm har sai na rantse miki ma, a ciki ma zaki samu wanda zai ce miki aurenki yake so, ko ma be ce ba idan kin ga ya miki sai mu bada sunansa kawai a kama mana shi, dube ki gani fa Wallahi ke matar manya ce Baturiya”

Baturiya ta yi murmushi tana jin wani irin dadi, sannan ta koma ciki ta dauko. Jakarta da karamar wayarta da makulli ta fito.

“Ina Sultan”

“Tun dazun na tura shi makota”

“Aiko kin kyauta, domin yara akwai sa ido zai iya fadawa Babansa na zo”

Suka yi dariya sannan suka fito daga falon kamin su fita daga gidan gaba daya Baturiya ta kulle gidan. Sannan suka nufi bakin titi inda motar Ramlee take, front seat Baturiya ta shiga Ramlee kuma ta ja motar suka kama hanya, suna tafe suna hira har suka shigo cikin gari, gaban wani katon shagon siyar da wayoyi Ramlee ta faka motar, kusan a tare suka fito ita da Baturiya, tana kokarin rufe motar ta hango Alhaji Garba jikin mota yana waya.

“Ramlee bari na gaisa da mijin yayata ga shi can”

“Ba zai ce wani abu ba?”

“Zan ce ke na rako ai, ban sani ba ko zai ba ni wani abun yana da alheri ai”

“Shikenan bari na jira ki daga ciki”

Kai ta daga mata sannan ta nufi gurin da yake tsaye jikin motarsa yana waya, ganinta yasa yai hanzarin yanke wayar da yake ya kalleta yana murmushi.

“Baturiya ina kika fito?”

“Ai kai zan tambaya na sani ko wata budurwa ka rako”

Yayi dariya.

“Zaki bari ne? Ai kin tare kowa ya gida ya kowa ina mijinki?”

“Kowa lafiya kalau, ina Anty”

“Lafiya Kalau take, me kika zo yi nan?”

“Wallahi wayata ta bata kwanan baya shi ne na zo siyen karama”

“Oh haka fa, Yayarki ta fada min Allah maida alheri, ai da na san da zuwanki da na riko miki wani abu gashi bani da enough a mota”

“Uhm Alhajina kenan ai kai babba ne, kuna da kudi sai dai idan ba ayi niyar ba mu ba, tun da alherin zuwa zuwa ne”

Ya sake yin dariya yana kallonta.

“Haka yayarki ta fada miki?”

“Aa yayata bata fada min komai ba, haka dai na gani da idona”

Ya bude motarsa yana dariya.

“Baturiya sarkin rigima ashe dai mijin naki yana fama”

“Kana dai fama zaka ce, ko ka bawa wani ne?”

Yayi dariya mai sauti.

“Zankadediyar mata irinki zan kyautar na dai ara masa shan miya, yanzu dai bari na siye bakin nan naki dan karki je ki fadawa yayarki kin gan ni a gurin siyen waya”

Ya fada bayan ya zauna cikin motar, sannan ya ciro bandir din yan dari dari 10k ya mika mata.

“Gashi na rufe bakin nan kar yayarki ta ji”

Murmushi tai ta karba.

“Karka damu Alhajin Allah, ai ko mutum ka yanke agabana ka bani wadannan ka rufe bakina babu wanda zai ji”

“Da gaske? Ashe za a iya siye ki da kudi?”

“Ba wai za a iya ba, ana ma yi ne”

Ta fada tana wani irin kashe masa ido kamar wata tsohuwar karuwa. Binta da kallon da shi kadai ya san manufarsa yana murmushi har ta shiga cikin gurin. A bakin kofa ta samu Ramlee tana jiranta.

“Yayarki tana da miji kamar wannan kike zaune a talauci?”

“Uhmm yan uwa yanzu ai babu ruwansu da son zumunci idan sun samu daga su sai yayansu”

“Shiyasa nake son ki gina kanki ki yi naki arzikin”

“Wallahi kuwa, babu abun da yake burge ni kamar katon gida da katuwar mota da kayan sakawa da na ci masu kyau masu tsada, Wallahi ko hoto ake turowa a group zaki ga ko wace shegiya da katon falo, haka nake ta ganin friends dina a gida masu kyau da sutura mai tsada, ki duba ko yan'uwana kowa tana auren mai rufin asiri amman ni kullum abushe ko abunda zamu ci wani lokacin gagararmu yake”

“Karki damu kin warke yarinya ke dai ki goge kawai ki iya dadin baki da kwarkwasa da jan hankali”

Haka suka cigaba da nisawa cikin shagon suna ta hira, an tsara shago gwanin sha'awa camera a ko'ina ga gilashi da haske gulob kamar ba rana ba,.kana ganin gurin kasan na manyan mutane ne.
A tare suka jera da Ramlee suka nufi gurin da aka jera wayoyin techno. Ramlee ce ta fara dubawa sannan ita ma ta kai hannu zata dauki wata sai ta ji an riko hannun nata, saurin kallon gefenta tai da tsoro sai tai arba da mutumen daya rage mata hanya a wacan lokacin da ta sauka tasha daga Kano, murmushi ta sakar masa kamar yadda yake mata murmushin shi ma, sai ta janye hannunta.

“Sarki alkawari”

Ta watsa masa wani irin kallon irin na masoya.

“Daman na yi alkawari?”

“Ba ki yi ba amman dai ai ya kamata ki ce min na isa gida lafiya ko?”

Ta yi murmushi, shi ma murmushin yai ya gabatar mata da yarinyar dake gefensa.

“Ku gaisa da kanwata, ya kamata ku san juna tun yanzu ai”

“Sannu”

Baturiya ta fada. Sai ita ma yarinyar dake kama da saurayin ta maido mata.

“Yauwa sannu, sunana Salima”

“Ni kuma Rafi'a amman anfi kirana Baturiya”

“Yeah kin fi turawan kyau ai”

Cewar saurayin sai duk suka yi dariya har shi.

“Me kika zo yi nan?”

“Waya na zo siya kasan wayata ta bata”

“Oh haka ne, amman kin san na tashi koma gidan nan sai kuma wata zuciyar ta bani hakuri ashe rabon zan hadu dake ne a nan, gaba daya na kasa samun natsuwa tun da muka rabu Wallahi nake ta mamarin ganinki har Hajiya na bawa labarinki”

Ta yi murmushi.

“Gashi yanzu, ai mun hadu katin daka bani ya bata ne”

“Ayyah”

Ya fada sai kuma ya kalli Ramlee dake ta duba wayoyi.

“Ko zaki bani aron kawar nan taki mu zagaya gurin masu IPhone”

“Yeah ba matsala, zan jiraki a mota”

Ramlee ta fada tana murmushi, sai Baturiya ta daga mata kai.

“Okay”

Bayan Ramlee ta wuce ya bawa kanwarsa key din motar.

“Je ki jirani a moto”

“Okay sai anjima in-law”

Budurwar ta fada sai duk suka yi dariya, sannan ya nuna mata hanyar da zasu bi su bullo gurin da aka jera iPhone din.

“Fahat sunana duk dai baki tambaya ba”

Ta kalleshi ta yi murmushi, da kansa ya zaba mata iPhone mai kyau, sannan ya nufi wajen biyan kudi ya mika atm dinsa, kamar ance ta juyo, tana juyowa tai arba da Nura tsaye gurin biyan kudin, da alama wani ya rako, suna hada ido tai saurin dauke kai gabanta ya shiga faduwa da mugun karfi. Bayan ya biya ya rakata har gurin motar Ramlee ya sake ciro katinsa ya mika mata.

“Ki tausayawa zuciyar nan tawa ki kira wayata ko zata samu sukuni”

“Karka damu zan kiraka, na gode sosai”

“Nine da godiya yau zan yi kwanan farinciki”

Ya fada sannan ya rufe mata motar Ramlee yaja suka bar gurin.

“Ina kika san shi? Baturiya Allah ya miki farin jini”

Dariya tai kamin ta labarta mata yadda akai ta sanshi, sannan ta dora da na ganin da Nura tai mata abokin mijinta kuma amininsa.

“Ke kar ya dame ki, idan ma ya fada masa ki bururuce ki ce ki kam sam ba ke bace, idan ya dage ke din ce kice tare da yayanki kika je siyen waya”

“Kuma fa kin kawo shawara, idan ba haka ba kam zai iya fusata sosai domin dazun na ci mutun mai mana maganar kudin haya na san kuma za su fada masa”

“Saboda me? Ai ba haka ake ba, nawa ne kudin hayar?”

“80k”

“Just 80k? Yanzu zan baki 100k da mutumen ya baki sai ki nemi inda mai hayar yake ki bashi gaba daya, wayar da ban siya miki ba zan baki kudin daman na yi niyar kashe miki 50k akan wayar dan haka zan baki su a hannu, gobe kuma zan kawo miki kayan mata masu kyau ki fara shirya kanki kamin lokacin da saku gana da Alhajin”

“Har da wani shan kayan mata?”

“Eh mana, kuma idan kika fara sha karki yarda ki bar Faruq yaje kusa da ke”

“Ni daman bana shan kayan mata ai, mutum yana fama da talauci ko a sha kayan mata me zan samu? Shiyasa ba ruwana da shan su, kuma ba kullum nake barinsa yana damuna ba”

“To ki dai kiyaye, yanzu kina isa gida ki fara neman mai kudin hayar ki bashi hakuri ki bashi kudinsa, kin ga idan ya dawo zai rage jin zafin tun da kin biya kudin hayar”

“Haka zan yi Inshallah na gode sosai kawata”

“Allah dai ya bar mu tare”

“Ameen”

A inda ta faka motarta dazun ta sake tsayawa, ta ciro kudin ta bata sannan sukai sallama, Baturiya ta fita ita kuma ta juya ta hau titi.

FARUQ POV.

Kamin ya isa gida sai da ya kira abokinsa Nura ya fada masa yadda sukai da abun da ya samu kana yai masa godiya. Ya isa gida cikin farinciki, ba zai ce be taba rika 100k ba amman ba kasafai ba, rabon daya rika 10k tashi ta kanshi ma ya manta.
Yana isa ya zare dubu biyu ya bawa Asiya ya ta girka abinci, sannan ya shiga daki ya taba mahaifiyarsa dake zaune tana maida numfashi a hankali.

“Mama ya jikin na ki?”

“Alhamdulillah, Aisha tace ka zo dazun ina bachi”

Ta amsa tana kallon yanayinsa dake bayyana irin farinciki da yake ciki.

“Eh na zo na tararda jikin na ki ne sai a hankali...”

Ya dora mata da labarin yadda komai ya faru ciki har da abun da Malam Musa ya kira shi yana fada masa Rafi'a ta yi, kamar wanda aka cirewa ciwo sai Mama ta nemi ciwon ta rasa zuciyarta tai fal, daman ciwon nata hawan jini ne na tunanin auren Aisha da kuma yunwar da suke wuni da ita su kwana da ita, abu ga talaka bawan Allah kadan ya ishe shi.

“Amman Allah ya saka masa da alheri, Allah ya faranta rayuwarsa ya daummawar da farinciki a cikin zuciyarsa kamar yadda ya faranta ranmu”

“Ameen, ni kaina ina tafe a hanya ina ta masa addu'a, Wallahi na jidadi sosai, domin rashin lafiyar nan naki ya dame ni, yanzu ki tashi ki shirya mu tafi asibiti”

“Aa wace asibiti kuma Faruq? Ai ni yanzu na ji sauki, daman ciwon ai na rashin kudin ne”

Wata kalar dariya Faruq yai wanda ya manta rabon da yai irinta har ya manta.

“Haba Mama saboda ciwon ki fa naje karbo kudin nan, kuma har ga Allah ni asibitin nai niyar kaiki”

“Aa ai ciwo kuma ya warke, da aje a kashe kudin a banza ai kara a kara ayi hidima, Idan aka karbi kudin lefe aka rage wani abu cikin nan ai sai a dan kara, in yaso sai ka dauki rabi ka ba mai hayar ka bashi hakuri”

“Ai ba za su isa ba, 80k ne muke biya shekara”

“Eh ka bashi ko 50k ne dai ka bashi hakuri kamin Allah ya budo mana wata hanyar samu sai ka cika masa”

“To Allah ya sa ya yarda, wannan matar ta kira min ruwa, Wallahi na gaji da halin Rafi'a Mama kullum da kalar fitinar da take bullo min da ita, bata da wata magana sai ta na sake ta”

“Ka kara hakuri tana maka haka ne saboda tana ganin baka da kudin yin wani auren, da ace ta san kana da kudi da ba zata maka haka ba, koma na rayuwa dan hakuri ne wata rana zaka ga komai ya wuce kamar ba ayi ba”

“Allah ya kara min hakurin domin har ga Allah ta kai kulu, ba wai zan sake ta ba ne bana son shiga hakkinta ne”

“Yanzu dai tashi ka tafi gurin sana'arka in yaso gobe sai ka samu mai hayar na san zuwa lokacin ya huce sai ka ba shi hakuri ka bashi dubu hansin din, Allah ya warwareka yai maka albarka, zuwa da yamma zan tafi gidan Kanen mahaifinku na fada masa yayi ya aiko da kudin lefen sai a hada da dan abun da aka samu”

“Toh Allah ya taimaka ni zan tafi”

“Ka dai baro mata abinci ko?”

“Eh akwai Taliya da wake, da cefane, idan na koma anjima zan siya mana abinci ina son na cire 5k a ciki”

“To Allah ya taimaka yai maka albarka”

“Amin Mama Allah kara miki lafiya”

Ya fada yana mikewa tsaye sai ta bishi da kallo ina na uwa da da tana jin kaunarsa na karuwa a ranta, ta fi kowa sanin cewar idan Faruq yana da mafita da tuni ya share mata hawayenta.
Kudin ya ciro ya cire 50 na mai haya sannan ya cire 5k ya mika mata 43k da suka yi saura, sannan ya fito ya nufi gurin aikinsa.
A hanyarsa ta tafiya ya saye waina sannan ya karasa shagon daman yana da plate da spoon da dan copinsa a shagon bayan ya bude ya wanke plate din sannan ya zuba wainar ya ci, ya siyo ruwa ya sha, tukuna ya hau gyaran shagon kamar yadda ya saba.
Be tashi ba sai 7:30 daman haka yake tashi kamin ya isa gida 8 tayi sai ya tsaya yai sallah a massallacin unguwarsu sannan ya shiga gida. A duk lokacin da zai shiga gida da tunani da fargabar abun da Baturiya zata masa, amman a yau haushin shiga gidan ma yake ji, har be san ta inda zai fara mata ba idan ya shiga.
Kamar kullum sai da ya tsaya yai sallah, sannan ya biya gurin mai siyar da balangon unguwarsu ya siye na dubu daya, ya biya shago ya siye shimkafa da sauran kayan masarufi sannan ya nufi gidansa.
Yayi mamakin ganin kofar gidan a bude domin bata saba barin kofar a bude ba, rufewa take wai a cewarta masu kudi ma basa barin gida bude sai takawa, hakan yasa duk wanda ya zo sai ya kwankwasa mata sannan ta bude. Sai dai yau kofar a bude ya same ta, sai ya shiga rike da ledodin a hannu nan ma sai ya samu kofar falon a bude, be yi sallama ba ya shiga saboda ransa a bace yake. Sultan kadai ya samu a falon zaune yana shan bobo, Sultan na ganin mahaifinsa ya sauko daga saman kujerar da sauri ya nufe shi.

“Daddy sannu da zuwa”

Sai da ya aje ledodin hannunsa sannan ya dauki Sultan yana murmushi.

“Sultan ya keke?”

“Lafiya”

“Me kake sha?”

“Bobo Momy ta siya min Bobo”

Jimmm Faruq yai sannan ya sauke dansa ya bude masa ledar naman daya siyo ya aje masa a gabansa.

“Zauna ka ci”

“To”

Ya zauna da sauri ya fara ci yana ta murna.

“Momy ma ta siya min kifi dazun”

Faruq be sake ce masa komai ba ya nufi kofar dakin tana tabawa ya ji a rufe, sai ya juyo ya kalli dansa.

“Sultan ina mamanka?”

“Tana ciki”

Kwankwasa kofar ya fara yi.

“Rafi'a ki bude kofar nan”

Sai ta amsa masa daga can ciki.

“Wallahi ba zan bude ba, ai na san dokana zaka yi”

“Kin san abun da kika yi kenan?”

“Eh mana, haka kawai muna fama da talauci zai zo ya kara mana da wata damuwar kudin haya shiyasa na karbi number sa na zage shi ai”

“To kin jawa kanki ya bamu kwana daya mu tashi mu bar masa gidansa, Rafi'a mi yake damunki ne wai? Miyasa ke baki son zaman lafiya? Duk wani abu da zai tayar min da hankali shi kawai kike nema”

“Ai na bashi 100k yau, na biya shi kudinshi kuma ya bada takardar ya yarda mu zauna”

Natsuwa yake kokarin yi wai ko zai fahimci inda kalamanta suka dosa, ta bashi kudi haya?

“Rafi'a”

Ya kiranta a hankali, sai ta amsa daga jikin kofar da take, rike da sabuwar wayarta.

“Na'am”

“Maimaita abun da kika fada min”

“Na ce na bashi kudin hayar har na kara masa da 20k sama”

“Ina kika samu kudi?”

“Yaya ne ya ba ni Umma ta cika min sauran”

“Bude kofar nan mu yi magana”

“Ba fa zan bude ba, tufafin ka nan a falo na fitar maka, kuma abinci ka yana nan kusa da kujera, kai da Sultan ku kwana a falo ba zan bude ba”

Ba dukan abun da tai kawai take tsoro ba, har da na sabuwar wayar data siya da kuma kudin data biya hayar domin ta san abu ne mai wahala ya yarda da ita.

“Ki bude kofar nan Rafi'a ba zan dake ki ba, na taba dukanki ne? Duka ai ba halina ba ne ina son nai magana ta fahimta da ke”

Shiru tai masa kamar bata gurin.

“Na samu 100k yau”

“Da gaske? Ko dai dan na bude ne”

“Wallahi da gaske ne, Rafi'a i need to talk to you seriously ki bude kofar nan ko kuma na tafi na barki ki kwana a gidan ke kadai...”

“Wallahi Faruq dukana zaka yi idan na bude ni na san abun da na yi, duk abun da na yi ai dai ina sonka ka san dai ina sonka, bakin talaucin nan ne bana so, saboda farar kafa ce da kai Faruq, aurenka be karbe ni ba, da yanzu na yi arziki”

Ta fada da muryar dake nuna tana daf fashewa da kuka. Murmushi jin yadda ta juya abun zuwa kansa, wato shi ne mai farar kafa ba ita ba.

“Na ji bude mu yi magana”

Ta dade tana tunani sannan ta nufi karkashin filonta ta saka wayar, ta nufo kofar ta bude cike da tsiro sannan tai baya ta haye saman gado, shi kuma ya shigo cikin dakin yana kallonta, yana bude baki yai magana sai wayarta tai ringing, yanayin yadda ta razana kadai ya isa ya nuna bata da gaskiya, saurin nufar inda wayar take ta yi ta dauka ta kashe ta gaba daya.

“IPhone? Ina kika samu IPhone Rafi'a?”

Ta yi shiru sai kallonsa take. Shi ma kallon tsoro yake mata domin lamarinta a yanzu ya fara bashi tsoro ta fara wuce tunaninsa.

“Ko yaya ya siya miki?”

Nan ma shiru tai, at first ya fusata sai dai a yanzu kwakwalwarsa cike take da tunani kala kala. Karasa yai kusa da gadon ya zauna gabansa n mugun faduwa, yana ta kokarin ganin ya kawarta yaye yayen da zuciyarsa take son masa akan Rafi'a. Zaunawa yai bakin gadon yana kallonta.

“Rafi'a ki saka tsoron Allah a ranki, ina son ki san cewa duk abun da aka samu a duniyar nan a nan ake barinsa, ba a zuwa lahira da komai sai aiki da mutum ya aikata, Rafi'a dan Allah ki zama mai tunani ki duba future din Sulta da abun da yake cikinki, na san ni talaka ne ba zan iya miki komai yadda kike so ba, amman

da ki je ki aikata wani mummunan abu da aurena kuma kina uwar yayana kara na sauwake miki ki auri mai kudi idan har hakan zai kawo miki mafita”

Yana maganar idonsa ya cika da hawaye, domin har ga Allah be fatar matarsa ta aikata abun da zuciyarsa take raya masa.

“Ina son ki Rafi'a amman Wallahi zan iya sauwake miki saboda yayana da aurena”

“Ni fa ba iskanci na yi ba, Wallahi ban taba iskanci ba”

Ta fada tana soshe soshe kamar mai kuraje.

“To ina kika samu wannan kudin da wannan wayar?”

“Yaya”

“Kin yarda na tambaye shi?”

“Eh na yarda”

Ido ya kura mata domin ya san karya take, yayanta yana da rufi asiri amman ba zai iya siya mata iPhone ba, duk be san ko wace irin iPhone bace amman ya san tana da tsada tun daga yanayin wayar da kuma yadda yake ganinta ga yan mata. Kasa yai da kansa ya lumshe ido be isa yace ba zata rika wayar ba tun da har ta danganta cewar yayanta ne ya siya mata, ya san idan ya hana mahaifiyarta zata saka baki ko kuma tace zata yi fushi ta tafi gida, ko ma suce ya rabu da ita.

“Ina da ciki idan ka dake ni ka daki cikinka”

Dagowa yai ya kalleta.

“Saboda ban da kudi shi ya baki damar yin duk abun da kike so?”

“To Faruq kai ma kasan ni ba ajin ka bace amman...”

“Haka ne...”

Ya fada sannan ya mike tsaye.

“Bari ki sauke abun da yake cikinki, labarin rayuwarki da tawa zai canja komai zai zo karshe”

“Da gaske?”

Ta tambaya cikin farinciki har ga Allah babu abun da take so kamar Faruq ya sake ta ta auri mai kudi, tana sonsa kan amman tafi son ta tafi inda zata huta. Kallonta kawai ya dauke kai ya fice daga dakin, falo ya dawo ya zauna yana kallon dansa cike da damuwa.

“Dady ba zaka ci ba?”

“Aa Sultan ci ka ragewa Momynka”

Ya fada yana shafa kansa cike da so da kauna, haihuwar da Allah ya bashi kadai ya san wani babban arziki ne.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

AMINATU POV.

Daga jiya zuwa yau da aka canja mata daki sai ta ci kadaicin ya karu, domin a can tana jin hayaniyar mutune a wannan dakin komai babu kowa sai ita kadai, sai duk ta ji tana kewar gidansu da rayuwarta ta baya.
Bata san dalilin daya saka aka canja mata daki ba, bata san ranar da wani zai zo nemanta ba, bata san ranar da rayuwarta zata koma daidai ba, har yanzu ji take kamar komai mafarki ne.
Tana fara tunanin ta ji wani irin tsoro ya taso mata, sai ta ji wani abu yana mata yawo a cikin kai karar bindigogi ya dawo mata hayaniyar mutane da rokon da Baba yake musu ya dawo mata kamar lokacin yake faruwa. Wani irin abu ta rika ji kamar kanta ba zai iya dauka ba, gashi tana son ta yunkura ta sauka saman gadon amman dama domin kafafuwanta basa iya komai a yanzu, bakinta ma ya dantse gam duk yadda ta so tai ihu ko kuka sai ta kasa. Ji tai bata bukatar komai a lokacin sai tafiyar da babu dawowa. Da wani irin karfi ta tashi zaune ta fisgi robar ruwan dake hannunta wanda hakan ya bawa jini hanyar fita ya fara zuba, jiki na rawa ta fisgo robar da karfin da bata taba sanin tana da shi ba sai karfen ya fado gefen gadon, bata tsaya komai ba ta hada robar a wuyanta tana kokarin aika kanta da kanta inda take ganin kamar idan ta tafi ta huta da komai.

Wannan karon ta samu sukunin bude baki, sai dai ko kadan hakan be bawa muryarta damar fita ba, hawaye kawai take babu kakautawa tana ta yaki da numfashinta, kamar an zare mata lakka haka ta ji wani abu ya sauko mata wanda ya zare duk wani sauran kuzari dake jikinta. Tun tana kallon kofa tana numfashi a hankali har numfashin nata ya fara nisa ta komai ya fara mata dishe dishe alamar ta fara ban kwana da duniya, ga jinin hannunta sai zuba yake.

TALBA POV.

As usual every weekend a falon Momy ko Daddy ake karyawa tare da kowa ciki har da Daddy da matarsa, sai dai mafi akasiri an fi cin abincin safe a bangaren Momy, Daddy zai zo bangarenta aci tare da shi, idan an gama ko kamin a fara duk wani mai wata bukata zai gabatar masa.
Sai dai wannan karon a bangaren Daddy Momy ta saka masu aikinta su kai komai wanda hakan ke nuna cewar a bangarensa za a karya.
Duk abun da ake Talba na zaune dinning yana lasa wayarsa, be dago ba har sai da ya ji saukowa Momy, sannan ya dago ya kalleta.

“Momy ina kwana?”

“Lafiya kalau an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah”

Ya amsa yana tashi tsaye sai da ya bar dinning din ta kira shi.

“Talba”

Juyowa yai ba tare daya amsa ba.

“Ka yi hakuri da abun da ya faru jiya, raina ne ya bace”

“Babu komai Momy, ke ai uwata ce Wallahi ban rike ki da komai a rai ba”

Wannan maganar da yai sai ya saka Momy ta dan ji nauyinsa, kasa hada ido tai da shi har ya juya ya fice daga falon. Kai tsaye bangaren Daddy ya nufa a bude ya samu kofar shiga falon, hakan yasa be yi sallama ba kamar yadda ya saba ya nufi gurin da suke karyawa.
Leila kadai ya samu zaune a dinning din ta saka plantain a gaba tana ci, tana sanye da wani jan yadi kanta sanye da bakar hula, fuskarta ta ji hoda sosai sai dan janbakin data shafa, ta yi kyau sosai abu ne mai wahala mace ma tai mata kallo daya ta dauke ido balle kuma namiji. Talba yaja kujerar dake facing dinta ya zauna yana kallonta, shi kansa ya san ta yi kyau, sai dai ba al'adarsa bace fadawa mutum cewar yayi kyau ko yana da kyau, musamman mace, no matter yadda take da kyau ba zai taba iya bude baki ya furta cewar ta yi kyau ba, kuma ba zai zake da yawa gurin kallo ba gudun kar a ankara da shi.
Dauke idonsa yai bayan ya zauna, sai a lokacin ya tuna cewar yau be tura mata sakon barka da safiya ba, kuma ba zai iya tura mata a yanzu ba gudun kar tace saboda ta yi kyau ne.
Gaba daya ya tattara hankalinsa ya maida gurin wayarsa, sai yai kamar be san da zaman Leila a gurin ba, ita kam daman gaisuwa ba halinta ba ne bata saba gaishe da mutane ba bayan Momy da Daddy, balle kuma shi duk kuwa da irin sanin da tai na son a girmama da yake, sai dai ta kasa dauke idonta daga barin

kallonsa duk kuwa da irin bugawar da zuciyarsa take after every blink. Har ga Allah bata iya fadar irin son da take yi ma Talba, da ace ta dauki biro da zayyano irin kaunar da take masa da alkalumman rubutu da takardun duniya sun kare bata gama rubuta irin kaunar da take masa ba. Sai dai har yanzu ta rasa gane manufarta a kanta, miyasa ba zai dauki rayuwa da sauki ba? Ya sauko da kai su yi soyayya kamar sauran masoya? Har yaushe zata yi ta jiran ya canja rayuwarsa? Anya ma zai canja din? Bata raba dayan biyu ba ta ji yana amsa waya, bata iya fadar cewar kiransa akai ba ko kuma shi ya kira domin wayarsa a silent take.

“Yeah ni ma na kwana da yarinyar nan a raina”

Furucinsa ne yasa ta kara tattara hankalinta tana saurarensa.

“Okay”

Shine last abun da ya fada sannan ya sauke wayar, ya daga kansa yana kallo Amal data nufo inda suke sanye da riga da wando yan patistan.

“Good morning Ya Talba”

“Morning Little Sis”

Ya amsa yana aikawa PA sa sakon kar ta kwana.

‘Ka yi magana da wannan number zai fada maka ko nawa yake bukata sai ka tura masa’

Aje wayar yai bayan ya aika sakon. Leila bata fahimci komai a wayar ba, sai dai ta fahimci da Ali yake magana domin yanayin yadda ya amsa wayar ya tabbatar mata da hakan. Sai da kalmar da ita na kauna a raina ya fi tsaya mata a rai.

“Wace yarinya ce?”

Ta tambayi kanta tana kallonsa, a take ta ji zuciyarta ta buga da mugun karfi, har sai da numfashinta yai sama, da sauri ta dauki cup din dake saman teburin ta zuba ruwan sanyi ta sha, sannan ta mike tsaye ta fice daga gurin zuwa karamin falon Daddy.
Zaunawa tai tana haki, ji take kamar taje ta tambaye shi wace yarinya ce sai dai ba wannan damar domin ba ya hira da ita, da ma dai Amal ce ita kam har sirri yake da ita.

“Wace yarinya ce Talba zai kwana da ita a ransa? Ban gane ya kwana da ita a ransa ba, as how?”

Wannan karon a fili tai tambayar tana hade yawun bakinta, sai kuma ta mike tsaye.

“Ko dai yayi ne dan na ji haushi? Amman kuma be taba min haka ba”

Ta dafa kanta tana jin kirjinta kamar zai rabe biyu, ita kamta da akai musu baiko bata tana jin yace ya kwana da ita a rai ba sai wata? Wacece ma? Ba kasafai yake saka mutane a rai ba balle har ya kwana da su amman yace da yarinyar na kwana a raina.

Haka ta sake sake a ranta, wani irin zafi ta ji zuciyarta na mata, irin zafin da bata tana jin irinsa ba, wata kila sabida bata tana jin Talba yana maganar wata mace a gabanta ba, hasali ma ba zata ce ga wata mace da yake so ko take burge shi ba, ko akwai be tana nunawa ba balle har ya fada.

“What if wani abun bacin rai tai masa?”

Ta sake tambayar kanta tana cire hular kanta, sam bata taba sanin wani abu wai shi kishi ba sai yanzu, domin Talba be taba yin maganar wata mace a kusa da ita ba, shiyasa kullum hankalinta a kwance yake bata da haufin komai, sai dai a yanzu tana jinta a cikin wani irin yanayi marar misaltuwa saboda ya furta ya kwana da wata a ransa.

“Ko dai bata masa rai tai, ai be kamata ya kwana da ita a ransa ba, Indai har macece ko yaya ne be kamata Talba ya kwana da ita a ransa ba”

Ta fada tana wasa da wayar hannunta, can kuma ta busar da iskar bakinta ta shiga contact dinta ta nemi number Ali ta kira shi. Kara wayar tai a kunne ta fara safa da marwa, kamin yai picking har ta matsu.

“Hello Leila”

“Ali ya weekend?”

“Alhamdulillah”

“Am akan maganar da kuke da Talba ne yanzu”

“Okay...”

Yayi shiru yana jiran yaji abun da zata ce, sai ta rasa ta inda zata fara ta san duk irin wayon da zata yi ba zai taba fada mata sirrinsa da Talba ba, sai dai idan ba sirri ba ne.

“Ban fahimci abun da kuke magana akai ba, kuma na ga kamar ransa a bace”

“Leila”

“Na'am”

“You should feel free to ask when ever kika ga Talba a damuwa ko matsala, shi ne fa mijin da zaki aura a tare zaku gina rayuwa idan kuna irin wannan zaman rayuwarku ba zata taba yin dadi ba”

“Na sani, amman ka san halin abunka, zan iya tambayarsa ya ki fada min ni kuma na damu ne kawai”

“Ki saka a rayuwarki ba ki da wanda yafi Talba, idan har kin damu da damuwarsa ya kamata ki tambaye shi”

“Zan yi haka, amman for now ina jin akan wata yarinya ce da na nuna masa jiya tana bukatar taimako, yar gudun hijira ce”

Shiru tai kamar mai tunani.

“Subhanallahi, tana ina yanzu?”

“Asibitin mu”

“Okay Allah ya bata lafiya, amman idan ana bukatar taimako Ali kai na gida ne, ka san yadda komai a Foundation din mu yake, ba sai ka sake yi masa magana ba, domin ba zan taba lamunta Talba ya kwana da tausayin wata a ransa ba, an yi na farko kuma na karshe, bana son ya kwana da kowa a cikin ransa sai ni”

“Ameen”

Ya amsa addu'ar da tai a farko yana murmushi, sannan ya aje wayar ba tare da ya sake ce mata komai ba domin ya san kishi ne.
Sai ta sauke ajiyar zuciya tana dan jin sauki a ranta.

“Ranki ya dade, Hajiya ta ce a kira ki”

Ta juyo da sauri ta kalli Mairo, sai kuma ta rufe da masifa domin ba karamin razana ta tai ba.

“Wai miyasa komai ba ku iya yinsa a cikin natsuwa ne? Mi yake damunku ne? Wannan ya zama na karshe da zaki sake kira sunana da karfi I'm not your mate”

Ta karasa tana jan tsaki sannan ta nufi hanyar shiga babban falon, bata ko tsaya kula Mairo b dake aikin bata hakuri. Ko da ta isa dinning din kowa ya hallara har sun fara cin abinci.

“Ina kika je?”

Momy ta tambaya tana kallonta.

“Waya na amsa”

Ta fada sannan taja kujera ta zauna tana mikawa Daddy gaisuwa. Sai da suka nisa da cin abincin sannan Daddy yai gyaran murya ya ce.

“Ina son na yi wata magana mai muhimmanci, Shiyasa na bukaci a shirya mana abun karyawa a nan, musamman mahaifiyarku”

Jin hakan tasa kowa ya kalleshi har Momy.

“Allah yasa ba laifi na yi ba”

“Laifi kika yi kuma babba, laifin da ban saka ran zaki yi ba a matsayinki na uwa, sam ban tsammaci haka daga gareki ba, ban yi zaton rana zata zo da zaki dubi dana ki fada masa cewar ba ke kika haife shi ba...”

Talba ya tsaya da cin abinci ya dago ya kalli Daddy dake maganar cikin tsananin bacin rai, Momy kuma tana kallon Talba a tunaninta shi ya fadawa Daddy abun da ya faru.

“Again?”

Momy ta tambaya tana cigana da kallon Talba rai a bace.

“Ba shi ya fada min ba wacan karon ma ba shi ya fada min ba...”

Kamin Daddy ya karasa Amal ya karba tana kallon Kabir.

“Ni na fadawa Daddy, ni kuma Ya Kabir ne ya fada min”

Momy ta kalli Amal kamin ta kalli Kabir.

“Na ji na yi laifi amman Amal bata fada maka danka yana wuce gona da iri ba?”

Da wani irin karfi da fusata Daddy ya daki teburin cin abinci.

“Da na be yi komai ba Amina... Wannan dalilin ne yasa na tara ku duka anan, saboda Leila ba zan yarda ki rika batawa Mu'azz rai ba, ko da rana daya bana jin ya taba miki wani abu da zai banban taki da uwar data haife shi, akan me zaki zabi raba kan yarana? Ko bana da rai shi zai yanke hukunci a gidan nan kuma shi zai dauki dawainiyar komai, na tara ku a nan ne saboda na ja miki kunne kuma. Yaranki su daina kokarin wuce guri ko da mafarki ban tsammaci zaki iya furta kalaman da kika furtawa dana ba, saboda abun da Amal ta fada min jiya ban samu bachi da kyau ba, ko kadan bana son abun da zai raba kan yayana kuma bana fatan Allah ya nuna min ranar da Talba zai ji bakincikin rashin uwa”

Yana kawai nan ya mike tsaye a fusace ya nufi dakinsa, kowa shan jinin jikinsa yai har Talba din da Daddy yake masifa saboda shi, domin ya san indai akansa ne tsab Daddy zai iya fushi da shi ko yai masa fada. Amal ma tashi tai da sauri ta bi bayan Daddy, domin ta san sakamakonta gurin Momy.
Momy da hawaye ke sauko mata ta kalli Talba tace.

“Mutum baya kuskure ne? Ni kaina na ji cewar ban kyauta ba, na ji cewar be kamata na furta kalaman nan ba”

Talba yayi saurin girgiza mata kai.

“Haba Momy kamar baki san halin Daddy ba? Yanzu zai hau kuma yanzu zai sauko, be kamata wannan ya dame ki ba, kin mu sanin Daddy fa, muma a tare muka bude ido muka ganku please ki yi hakuri dan Allah”

“Ka yi hakuri kai ma, ban kyauta ba na sani, Allah ya muku albarka”

Ameen. Duk suka amsa har Leila sannan ta mike tsaye ta nufi hanyar bedroom din Daddy, hakan yasa Leila ma ta tashi ta nufi hanyar fita daga part din gaba daya.

“Daddy's Boy?”

Kabir ya fada yana kallon Talba, sai Talba yai murmushi kadan.

“Har yanzu Daddy be yarda na girma ba, yana ganina kamar jariri”

“Maybe sai ka yi aure ka haihu ya ga ka fara bawa yayanka kulawa”

Ya dan tabe baki kadan.

“Ni ma ina son ganin haka, you know i love children alot, but before then ya kamata ka iya bakinka, Amal parrot ce ba komai ake fada mata ba, yanzu kaga abun da taja mana”

“Da gangan na fada mata ai, saboda na san zata tseguntawa Daddy, sincerely speaking Momy bata kyauta ba, she shouldn't say that, we're one family be kamata tai haka ba, rai na be taba baci irin jiya ba”

Cewar Kabir with serious face. Talba ya dauki tea gabansa ya sha kadan.

“You know mata suna da rauni Kabir, kuma tunaninsu gajere ne, shiyasa ba a zure musu kuma ba a kuresu, idan bama dauke kai ga wasu abubuwan zamu yi ta ji da ganin abun da bama so, ya kamata ace muna yafiya da manta kuskure, no body above mistake”

“Yeah wani lokacin kuma muna yin abu saboda ya zame mana darasi so that kar mu sake aikata shi nan gaba”

Murmushi kawai Talba yai be sake cewa komai ba, ya cigaba da cin abinci har sai da ya koshi sannan ya mike tsaye ya dauki wayarsa ya nufi kofar fita yana jin wani irin kaunar Daddy, ji yake yafi kowa sa'a a duniyar domin ba kowa ke samu uba kamar yadda shi ya samu nasa ba, kaunar da Daddy yake masa bata misaltuwa shi kansa ya sani.

Fitowa yai daga bangaren gaba daya ya nufi bangarensa, yadda ya tsaya yana kallon harabar gidan sai rantse da Allah yau ya fara ganin gidan, sai hankalinsa na can wani gurin daban ya dade a tsaye sannan ya karasa entrance din ya murda kofarsa ya bude. Yana shiga yai wanka ya fito ya shirya cikin shadda milk color ya saka hula sannan ya saka wallet dinsa da wayarsa aljihu da ya fito rike da makulli mota ya ja kofar.
Leila na tsaye jikin window dakinta tana kallonsa da murmushi a fuskarta har ya shiga motarsa ya danna horn aka bude masa ya bar gidan.
Sai ya fara biyawa ta shagon da yake siyen sweet da chocolate din da yake zuwa da su gidan marayu sannan ya wuce gidan abokinsa Ali domin a tare suka saba zuwa, wani lokacin Ali zai zo ya dauke shi wani sa'in kuma shi yake zuwa ya dauki Ali kamar dai yau. A bakin gate din gidan ya faka motarsa sannan ya ciro wayarsa ya kira Ali, Ali na yin picking sai ya kashe wayar ya aje. After like 5 minutes Ali ya fito ya bude motar ya shiga, Talba yai reverse sannan suka hau titi.

“Ina yara?”

“Lafiya Kalau Gwauro”

Ali ya amsa masa yana kallonsa fuskarsa da dariya. Talba be sake cewa komai ba har suka kusa isa sannan Ali ya dauko masa zancen Aminatu.

“PA ka ya turo kudi dazun Allah ya saka da alheri”

Nan ma Talba be ce komai ba, har sai da Ali ya dauko masa zancen kiran da Leila tai masa dazun yana murmushi, sannan ya kalleshi.

“Da kai tai waya da safe kenan?”

“Yeah kishi take wai ba zata iya daukar ka kwana da wata a rai ba”

“And...”

Ali ya kalleshi.

“And she's right”

Tabe baki Talba yai be sake cewa komai ba har suka isa gidan marayun, tun kamin ya karasa harabar yaran suka nufoshi a guje suna murna da zuwansa, murmushi ne ya cika fuskarsa farinciki marayu na daga cikin abun da yake faranta ransa, musamman kananan domin Talba mutum ne mai matukar son yara. Da sauri ya bude motar ya shafa kansa yana tambayar lafiyarsu, sannan ya mika hannunsa ya dauko alawar daya siyo musu ya bude ya fara raba musu.

“Uncle ni dai chocolate nake so”

Wata yar karamar yarinya ta fada, sai ya amsa mata in a funny way yana dariya kamar ba shi ba.

“Noooo chocolate dai anjima idan zan tafi”

Ali ya bude dayan side din ya fita yana amsa waya.

“Subhanallahi gani nan zuwa”

Ya fada sannan ya saka wayar aljihu ya zagayo side din da Talba yake zaune a motar.

“Zan barka nan na tafi asibiti”

Wani kallo Talba yai masa wanda ke nuna alama ce ta tambayar lafiya.

“Wai yarinyar nan aka samu ta suma hannunta nata zubar da jini kuma robar karin ruwa murde a wuyanta kamar an shaketa”

Shiru Talba yai fuskarsa da mamaki sannan ya fito cikin motar gaba daya.

“You can go with my car”

“Thank you”

Ali ya fada sannan ya shiga motar da sauri, Talba ya bude baya ya dauko ledar chocolate din sannan ya rufe har lokacin fuskarsa dauke take da mamaki, bin motar yai da kallo har sai da Ali ya fita gate din sannan ya maida dubansa gurin yaran sai dai gaba daya hankalinsa ya tafi akan dalilin da zai saka yarinyar ta aikata haka, he don't even think zata ma iya aikatawa kanta haka sai dai idan wani ne ya kashe ta ko kuma yake kokarin kasheta.

Be wani dade sosai kamar yadda ya saba yi ba domin hankalinsa gaba daya ya tafi gurin yarinyar, and baya son azahar tai masa a nan saboda a tare suke cin abincin rana da duka Family kamar yadda suke yi da safe on every weekend sai dai idan akwai wani uzuri. After like 2 hours da wucewar Ali ya turawa direbansa

sakon inda yake. Sannan ya bude chocolate din ya shiga raba musu yana Murmushi kamar ba shi ba.
Bayan ya gama yai musu bankwana suka rakoshi har gurin da direban ya faka motar, domin ya dade a zaune cikin motar yana jiran Talba. Kamin ya karaso direban ya fito ya bude masa motar bayan ya shiga ya rufe, ya ya zagaya da gudunsa ya shiga driver side ya ja motar suka nufi gida.
Tafiyar minti talatin suka iso unguwar
shimkafi Quarters, Talba na hakimce cikin motar har direban ya faka motar a kusa da entrance din kofar Momy. Kamar ya bude baki ya ce ma direban ba bangaren Momy zai fara shiga ba, sai kuma ya ji ba zai iya ba, sai da direban ya bude masa motar sannan ya fito ya nufi bangarensa.
Yana shiga ya bedroom dinsa ya bude bathroom yai alwala ya fito yana rike da agogon hannunsa, a inda ya saba aje shi ya aje sannan ya nufi inda Capet dinsa ta sallah take shimfide yai ikama ya fara gabatar da sallah nafila. Kamin ya sallame limamin gidansu ya fara kiran sallah hakan yasa yana sallamewa ya fito daga bangarensa ya nufi masallaci gidansu inda dukansu suke sallah da kuma ma'aikatan gidan.
Bayan saukowa daga sallah azahar ya nufi bangaren Momy sai kamshi turare yake kamar wanda ya lullube jarkar turaren a jikinsa. Sai da ya danna door bell din sannan kuma yai knocking sai ga Zulai da gudunta ta bude masa.

“Sannu da zuwa ranka ya dade”

Kai kawai ya daga mata sannan ya nasa kafarsa cikin falon, saman sofa ya zauna yana kallon Plasma dake ta aikinta, babu kowa a falon sai Leila dake zaune a dinning rike da waya, yana shigowa sai duk hankalinta ya tattara ya koma kansa. Be yi minti biyar da zaman ba aka sake danna door bell din, Mairo dake kitchen ta fito da gudu ta nufi kofar ta bude, daman idan ba yan aikin gidan ba ko Kabir sai Amal sune kawai suke iya bude kofa idan ana kwankwasa, Leila tana ganin ta fi karfin haka, Talba kuma jin kai ba zai bar shi ba.

“Baaba na nan?”

“Ban santa ba gaskiya”

Shiru yai yana kallon sabuwar yar aikin domin be taba ganinta ba, duk kuwa ba da yawan zuwa yake gidan ba amman dai akan aikoshi daga kauye gurin Kakarsa Baaba dake aikin gidan, hakan yasa police din dake gadin gidan suka san shi basa hana shi shiga a duk lokacin da ya zo.

“To Hajiya fa?”

Ya sake tambaya, sai Mairo ta amsa masa.

“Eh tana nan wa za a ce mata?”

“Ki ce mata Shamsu ne jikan Baaba”

“Toh”

Ta saki kofar falon dake bude ta nufi hanyar upstairs. Leila a hango shi ta mike tsaye da sauri.

“Ki ce masa Baaba bata nan”

Ta fada kamar wanda ya rikice. Mairo ta juya da sauri da zimmar fada masa, sai Talba ya dakatar da ita ta hanyar daga mata hannu. Mikewa yai tsaye ya nufi kofar Leila na ganin haka ta nufi upstairs da gudu.
Shamsu na ganin Talba ya dan risina masa yana gaishe shi.

“Shamsu”

“Na'am ranka ya dade ya gida?”

“Alhamdulillah, lafiya dai?”

“Lafiya Kalau, daman daga can gida ne suka ce na zo na duba Baaba ko lafiya kwana biyu ba a samun wayarta”

Kamar an dasa ice haka Talba ya tsaya jikin kofar yana kallon Shamsu da mugun mamaki, kwakwalwarsa ta cika da tarin tambayoyi, sai ma ya rasa abun da zai ce wa Shamsu.
Yawun bakinsa ya hade a hankali yana kallon Shamsu har ya bude baki zai yi masa magana sai ya ji muryar Momy dake saukowa tana kiran sunan Shamsu da far'arta, abun da bata saba yi ma talaka ba musamman wanda yake karkashinta.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

“Shamsu ne?”

“Eh Hajiya ina wuni?”

“Lafiya kalau shigo mana”

Talba ya juyo tana kallon Momy dake amsa masa da far'arta kamar ba ita ba. Sai kuma ya juya ya kalli Shamsu dake kokarin shigowa.

“Baaba ka zo nema...?”

Kamin Shamsu ya ce komai Momy ta daka masa tsawa.

“Talba ka barshi ya huta ya sha ruwa mana, Mairo akai shi karamin falo a kawo masa ruwa”

Momy ta karasa tana kallon mai aikinta Mairo, sai Mairo ta amsa a ladance.

“Toh Hajiya”

Ta wuce gab Shamsu ya bi bayanta, Momy ta gyara tsayuwarta tana kallon Talba.

“Bangaren Mahaifinku zaku yi lunch”

Ya gyada mata kai yana bin Shamsu da kallo.

“Zulai ta kai komai a can Engineer kai kawai yake jira”

Ta fada tana juya wayarta a hannunta, yanayin yadda tai maganar yana nuna masa son take ya bar mata falon. Ya san ba zai iya nufar falon ta ce akai Shamsu ba, idan ma yaje ba zata bari yai magana da shi ba, idan kuma ya ce zai musa mata zata yi korafi.
Juyawa yai ya fice daga falon gaba daya zuciyarsa cike da tambayoyi kala kala, a entrance ya tsaya yana kallon harabar gidan, sai kuma ya nufi gate din ya fice daga gidan gaba daya.
Yana fita falon Momy ta rufe kofar da kanta tana sauke ajiyar zuciya. Lumshe ido tai ta bude tana kai hannu ta dafa kirjinta dake mugun bugawa da karfi, sannan ta bar jikin kofar ta nufi karamin falon inda Shamsu yake zaune, yana ganinta sai ya sauka daga kan kujerar ya zauna a kasa abun ka da mutunen kauye akaai girmama mutane.

“Shamsu ya gida ya kowa?”

Ta tambaya bayan ta zauna.

“Lafiya kalau Hajiya”

“Maa Shaa Allah, fatar su Baaba ma suna lafiya?”

“Eh... Ai ita aka ce na zo na duba, kwana biyu an ta kiran wayarta baya shiga”

“Ah ah Subhanallahi, Baaba ai yau kwananta tara ko takwas da tafiya gida”

Shamsu ya kalleta da sauri.

“Gida Hajiya? Wallahi bata je gida ba”

“Subhanallahi Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, lallai tabbas ni ma nayi ta kiran wayarta bayan tafiyarta ban samu ba, amman ban saka ran komai ba saboda na san kauye wani lokacin akwai matsalar network ko nepa, kaga ai shiyasa binciken yake da dadi Allah yasa ba mugun hannu ta fada ba, amman ka bincika aka ce bata je ba?”

“Wallahi bata je ba, ai idan tana can dole zan sani saboda a gidan nake, kuma bata fada miki dalilinta na zuwa ba”

“Eh to gaskiya bata fada min ba, na san dai kamin ta tafi tana dan jin jiki, domin da kaina ma na dauke ta muka je asibiti aka ce zazzabi ne da hawan jini, bayan mun dawo da kwana biyu tace min tana son taje kauye ta ga kowa hankalinta ya koma can a yanzu, ta inda nai kuskure ban tambaye ta me take tunani ba, domin hawan jini baya tasowa haka siddan sai da damuwa ko bakinciki har ma nake cewa ba zata kira ta fada a kauye ba tace bata son ta tashi hankalinsu”

Wani kalar tashin hankali ne ya cika Shamsu, jin cewar Baaba bata gidan ga wayarta ma idan an kira ba a samu, Momy kuma ta fada masa cewar yau kwananta tara da tafiya. A gabansa Momy ta nemo number Baaba ta kira ta saka wayar a speaker, daga ita har Shamsu suka ji cewar wayar a kashe take. Shamsu ya mike tsaye

“Wallahi haka nima suke ce min idan na kira, su ma can haka suka ce wayar a kashe take, amman yanzu zan kira na fada musu halin da ake ciki”

“Gaskiya kam kara a dage da addu'a kuma a saka cigiya, ni ma Inshallah zan bada sanarwa gidan radio ko Allah zai saka a dace”

“Zan tafi Hajiya”

“To Shamsu bari na baka number na duk yadda kake ciki sai ka kirani”

Ta fada tana karanto masa number ya saka sannan ita ma ta mike tsaye.

“Bari na kawo maka wani abu ka hau mota”

Tsaye a falon cikin tashin hankalin kamin Momy ta kawo masa 5k din har ya matsu domin hankalinsa gaba daya ya koma gurin inda yake tunanin Baaba zata iya zuwa. Ya karbi dubu biyar din data bashi yana godiya ya fice da saurinsa kana ganinsa kasan bayan cikin natsuwa. Har bakin kofar babban falon Momy ta raka shi tana ta masa addu'ar Allah yasa a gane ta ya amsa da Ameen sannan ya fice ta maida kofar ta rufe. Sannan ta hau sama da sauri ta nufi dakin Leila, Momy na turo kofar Leila ta zabura ta mike tsaye da sauri tana hawaye jikinta har rawa yake.

“Miye haka? So kike idan ya gani ya fara zargin wani abu”

Leila ta kama hannayen Momy ta rike tana kuka.

“Momy tsoro nake ji”

“Ki daina jin tsoro, babu abun da zai faru, idan kina nuna irin wannan hallayar sai ki tonawa kanki asiri, amman idan kika cire komai a ranki sai ki samu kwanciyar hankali”

“Momy har yanzu ina mafarkinta Wallahi, kuma ina jin kamar asirina zai tonu”

“Idan ma asirin ki ya tonu sai mu zuba miki ido akaiki gidan yare? Ko ayi miki wani hukunci? Noooo babu abun da zai same ki, je ki kwanke fuskarki ki shafa hoda ki same ni a bangaren Daddynku”

Ta gyada kai wasu hawayen na sauko mata.

“Momy akwai CCTV a gidan nan, Talba zai iya bincikawa, kuma idan ya gane zai iya cewa ba zai aure ni ba”

“No kul bakinki ya daina furta wadannan kalaman, Talba ba shi da mata sai ke, ki kwantarta hankalinki zan saka a cire CCTV cameras din, je ki wanke fuskarki”

Ta saki hannayen Momy ta nufi bathroom dinta Momy kuma ta fice daga dakin, tana saukowa ta nufi kofar da zata sadata da part din Daddy.

Kamar zai tashi sama haka Shamsu ya nufi gate yana ciro karamar wayarsa ya ciro karamar wayarsa domin kiran yan'uwansa ya sanar musu halin da ake ciki, police din dake gadin gate din ya bude masa ya fita hankali a tashe. Talba dake tsaye wajen gate din ya kalleshi yana karantar irin tashin hankalin da yake ciki.

“Ka fito”

“Eh ranka ya dade, zan je can gida na fada musu halin da ake ciki”

Talba ya masa kamar ya san abun da yake magana akai.

“Oh ba su sani ba”

“Eh Wallahi shiyasa suka ce na zo na bincika ai, ita ma Hajiya tace tana ta kiran wayar sai ta jita a kashe, Allah yasa dai ba mugun hannu ta fada ba”

“Ameen”

“Yanzu zanje can na fada musu, Hajiya ma tace yau kwananta tara da tace mata zata je ganin gida, ka ga ita bata san bata isa ba, mu kuma ba su san da zuwanta ba”

“Haka ne, Allah ya bayyanata”

Shine abun da Talba ya fada zuciyarsa na bugawa kamar zata fasa kirjinsa ta fito saboda bacin rai, zuciyarsa na ta dawo masa da abun da Ali ya fada masa akan halin da aka samu Aminatu.

Bayan Shamsu ya amsa da Ameen Talba ya kwankwasa karamar kofar gate din suka bude masa, ya doshi cikin gidan, Momy na shiga bangaren Daddy Talba ya danna door bell din, Mairo ta zo da gudunta ta bude masa, kana ganin yanayinsa kasan ransa a bace yake, kai tsaye ya nufi stairs sai dai kamin ya karasa hawa Leila ta fito fuskarta cike da ruwa ko hodar da Momy ta ce ta shafa bata shafa

ba, tana ganin Talba ta hade yawu da karfi ta dauke numfashi na tsawon dakika uku.

“Yanzu zan iya sanin abun da kika yi ma Baaba?”

A karo na biyu ta sake hade yawu da karfi a tana kallonsa kamar wanda bata fahimci abun da yake magana a kai ba. Ya kara matsowa kusa da ita cikin wani irin bacin rai sai ta koma baya da sauri tana kallon kofar da Momy ta fito.

“Lafiya na shiga can ban ganku ba, Daddynku yana jira zamu ci abinci”

“Answer me...!!!”

Talba ya fada a tsawace yana Kallon Leila. Cikin karfin hali tace.

“Ni ban gane abun da kake magana a kai ba”

“Miya faru?”

Momy ta tambaya daga downstairs din da take tsaye. Sai Leila ta amsa mata.

“Tambaya yai wai zan iya sanin abun da ya faru da Baaba”

“What? Me kake kokarin cewa Talba?”

Talba be kula Momy ba ya kara yin sama ya matsa kusa da Leila.

“I hope ba ke kika shakari yarinyar can ba, kike kokarin kasheta, saboda zafin zai zame miki biyu wahalar zata miki yawa...”

Hawaye ne ya fara saukowa Leila.

“Talba wace irin magana ce wannan? Me kake son fada?”

Juyowa yai ya kalli Momy.

“Momy kin san me nake magana a kai, I'm not a fool na fahimci komai, and i do hope Leila bata da hannu a kokarin kashe yarinyar nan...!”

Yana kawai nan ya sauka a fusace ya fice daga falon gaba daya, Momy ta bishi da kallo, Leila kam ban da hawaye babu abun da take.

“Wace yarinya yake magana akai?”

Zubewa Leila tai a gurin ta fashe da kuka.

“Momy....”

Sai kuma ta kasa karasa, Momy ta hau saman da sauri ta rika Leila suka nufi dakinta.

TALBA POV.

bangarensa ya nufa wayarsa makalle a kunnensa yana ta kiran Ali, sai dai har wayar ta gaji da ringing ta katse Ali be daga ba, zaunawa yai saman kujera ya sake kiran wayar, wannan karon ma Ali be daga ba. Hakan yasa ya dauki keys dinsa ya fito ya shiga motarsa ya fito ya ja motar da karfi, suna ganin ya kunna motar suka bude masa gate. Cikin saurin ya fice daga gidan, yana driving zuciyarsa na raya masa Leila zata iya yin yunkurin kashe yarinyar saboda ta tambayi Ali akan ta, wata kila zata iya zargin wani abu ne a tsakaninsu idan ma bata yi da kanta ba zata iya saka wani yai.
Yana isa asibitin ya faka motarsa ya fito ya mufi hanyar da zata sada shi da office din Ali, kamin ya karasa Office din Ali ya fito daga ward din, yayi mamakin ganin Talba sai dai kamin yace komai Talba ya ce.

“Ali ya yarinyar take?”

“Ba dadi, but she's still alive”

Wani deep breath Talba yai sannan ya bude office din suka shiga.

“Ya akai abun ya faru?”

Ali ya rufe kofar yana fadin.

“Nurse Karima dai ta fada min cewar tana shiga dakin ta same ta a sume, robar a zagaye da wuyanta kuma an fisge robar hannunta jini ya zuba, yanzu haka sai da muka saka mata robar jini, daman jinin be isheta ba”

Talba ya zauna saman kujera yana dan tunani kaminnya kalli Ali daya kai hannu ya dauki wayarsa yana dubawa.

“Ali lokacin da Leila take tambayarka akan yarinyar nan ta tambaye inda take?”

“Tace dai wace yarinya ce na fada mata tana asibitin mu”

“Ka fada mata number dakin?”

Alinya dago ya kalleshi.

“No miya faru?”

“Ali Leila can do this yarinyar nan bata da zuciya mai kyau....”

“Noooooooooooooooo”

Ali yayi saurin dakatar da shi yana daga masa hannu, domin maganar ta masa nauyi sosai har sai da ya runtse ido ya bude ya kalleshi.

“Look Talba yanzu na fahimci baka son Leila, and it fine, ka ji baka son mutum normal ne amman kokarin dora mata sheri ba zai amfana maka komai ba”

“Na san dalilin daya saka na fad....”

Talba be kasara Ali ya daka masa tsawa.

“Baka da wani dalili, and karka manta Leila yar'uwarka ce ko da babu alakar kauna a tsakaninku be kamata ka jefe ta da wannan ba”

“Ali ba zaka gane ba ne, Leila can do this”

Talba ya sake maimaitawa with full confidence, abun da ya kara fusata Ali.

“Enough Talba, enough. Leila tana da damar da zata yi kishi, ta nuna bakincikinta ko bacin rai akan ka damu da wata, amman for now ka bar Leila ta ji da damuwarka karka kara mata wata”

Ali ya fada cikin tsawa jijiyar wuyansa har tashi take. Talba ya mike tsaye yana kallon Ali cikin wani irin zafin nama.

“So you're shouting at me...?”

“Yes me ke damunka Talba? Why Leila? What if ita tai kokarin kashe kanta? What if kila ta akan wani abu dabam ake kokarin kasheta?”

Talba ya matsa kusa da shi yana kallon idonsa.

“Don't fool me, haka nan kawai zata yi kokarin kashe kanta saboda bata son kanta? Bayan ta samu ta fito daga daji? And you already told me babu wanda ya taba zuwa ganinta how could someone know tana a nan? Ali Let me tell you this, zan bincike yarinyar nan and if i find out Leila ta aikata abun nan, sai na bata mamaki”

“And before you do this let me show you something, daga yau ba zan sake kula yarinyar nan ba, and i swear sai ta bar asibitin nan yau, ba zan zuba maka ido ka bata alakarka da matar da zaka aura ba kuma yar'uwarka saboda wata bare ba, kuma a dalilina ka san yarinyar nan and now na fahimci halin da Leila take ciki akanka”

Talba yayi murmushi irin murmushin na bacin rai da mamaki a lokaci daya.

“And remember you said yarinyar bata da kowa”

“I don't care, idan ma mutuwa zata yi tai mutu, she's not my responsibility...”

“And for now on she's my responsibility har sai ta dawo hayyacinta ta fada min komai... And believe me with or without you yarinyar nan zata rayu Doctor Aliyu Muhammad Bukar...”

Talba na fadar hakan ya juya ya nufi kofa a mugun fusace, da mugun karfi yake taka kasar kamar zai fasata tsabar bacin rai, rabon da ya samu kansa cikin irin wannan bacin rai har ya manta. Har ya fito daga ward din sai kuma ya juya ya koma ciki, kai tsaye ya nufi gurin da sauran nurses din suke, mostly sun sanshi domin yana yawan zuwa asibitin gurin Ali kuma gashi sanannen mutum kuma dan babban mutum wato Alhaji Mu'azu Shimkafi, sai dai ba zai iya shadar sunansu duka ba musamman a yau da yake weekend ne ba faces din daya sani ba ne a gurin.

“Who's Karima a nan?”

“Ni ce”

Ta amsa tana kallonsa.

“Ali ya ce ki dauko yarinyar ki saka a motana zan canja mata asibiti”

“Okay”

Ta mike tsaye ta kira mutun biyu da za su rika mata ita, a gurin ya tsaya har aka fito da ita suka turota a kujera idonta a rufe. Yana gaba suna Karima na biye da shi wata mai aikin shara da dauko files tana rike da file din Aminatu, suna isa gurin Motar Talba ya bude gidan bayan Nurse din da matar suka rikata suka sakata ciki sannan suka rufe motar. Shi kuma ya karbi file din ya bude side dinsa ya shiga ya aje file din a front seat, hakan kawai ya samu kansa da juyawa ya kalli fuskarta, sai tausayinta ya kara kama shi, abun da Ali ya fada masa akanta ya dawo masa, ga kuma wanda yake tunanin Leila na kokarin kara mata.

“Leila...”

Ya furta bayan a dauke kansa daga barin kallon Aminatu, yana jin tsanar Leila na kokarin dasuwa a ransa. Key yai ma motar yai reverse, ya kama hanyar ficewa daga asibitin.
Wata expensive private hospital ya nufa da ita, yana shiga ya nufi emergency, duk da kasancewar yau weekend ne ya samu ma'aikata da yawa a asibitin saboda private hospital ce da suka san aikinsu, sai dai ba kowa yake iya kai kansa ko wani nasa a can ba, sai ya tsaya da kafafuwansa.
Sun karbi Aminatu da gaggauwa da kuma kulawa suka shiga da ita ciki domin bata taimakon da take bukata.
Shi kuma ya tsaya daga waje ya ciro wayarsa dake aljihunsa tana ringing, ganin number Daddy yasa shi saurin picking.

“Hello Daddy”

“Mu'az kana ina? Mun ci abincin rana ba tare da kai ba?”

Ya daga jikin motarsa yana kallon harabar asibitin.

“Daddy ina asibiti”

Sometimes idan yana gurin Ali a asibitin ya kan cewa Daddy yana asibiti, hakan yasa Daddy yai zaton ko yana tare da Ali ne?

“An bata maka rai ne? Could we talk?”

“No Daddy ina wata magana ne mai muhimmanci, bata shafe ka tsakanina ne da Ali”

“Okay”

Daddy ya fada sannan ya kashe wayar, Talba ya cikawa bakinsa iska ya busar a hankali yana kallon Nurse din data doso inda yake.

“Dan Allah kai ne mijin yarinyar nan? Ko dan'uwanta?”

Tsaye Talba yai kamar an dasa shi ya kasa amsa mata.

“Tana bukatar jini da gaggauwa”

“A ina zamu samu?”

“Lab amman for now za mu bincika mu ga ko za'a samu jinin da zai dace da nata”

Ya gyada mata kai a hankali cike da natsuwa, sannan ya bi bayanta suka nufi cikin ward din, ita ta nuna masa dakin da suka saka Aminatu. Ita ta fara shiga shi kuma ya bi bayanta ya tsaya jikin kofar yana kallon fuskar Aminatu dake ta bachi kana gani kasan bata san inda take ba. Nurse din ta yi abun da zata yi ta fita Talba yana tsaye jikin kofar idonta akan Aminatu, takawa yai a hankali ya karasa kusa da gadonta still ya kasa kauda idonsa akanta.

“You need to survive”

Ya furta yana jin kamar ya tashe ta ya tambaye ta waya mata haka, kuma ayi sa'a ta amsa masa cewar Leila ce. Yana tsaye akanta har na kusan mintuna talati, sai ga nurse din ta dawo tare da likitan daya karbi Aminatu a dazun.
Sake dubawa yai sannan ya kalli Talba.

“Ba mu da kalar jininta a yanzu, sai kaje babbar asibiti ko kuma ka samu wani daga familynta idan zai iya bada jinin”

Uffan Talba be ce ba har sai da Likitan ya nufi kofar fita.

“Ko zaka iya gwada nawa? O ne”

Likitan ya juyo ya kalleshi.

“Yes why not amman zamu fara maka test mu tabbatar baka dauke da kowace irin cuta gudun samun matsala”

Ya daga masa kai kamar an masa dole, sannan ya bi bayan Nurse din dake nuna masa kofa.

“Bismillah Malam”

LEILA POV.

Wani irin kuka take wanda ita kanta ba zata iya fadar dalinlinta na yin kukan a yanzu ba, na zargin da Talba yake mata ne ko kuma na laifin ne da yake kokarin dora mata? Taya zai zarge da da abun da bata san wanzuwarsa ba? Miyasa ma zai yi maganar wata yarinyar a gabanta? Ko kuma dai tana kukan ne saboda zuwan Shamsu? For now she can't tell, all what she know is dukansu is painful, daga zargin har zuwan Shamsu har zancen yarinyar da Talba yake.

“Tun dazun kike ta kukan nan? Haka zaki yi ta yi a gaban mutane ki daure kanki?”

Momy ta fada cike da tausayin yarta.

“Wai wace yarinya ce ma yake magana akai?”

A take ta amsawa Momy hawaye ma sauko matan

“Wata ce, wata yar gudun hijira ce”

“Yar gudun hijira kuma? Shine har zai zarge ki da kashe ta? Ke kin santa ne?”

Ta daga kai tana goge hancinta.

“Na santa amman Wallahi ban ma taba ganinta balle har na yai yunkurin kasheta? Miyasa zai zarge ni?”

“Ke kika bashi fuska ai! Kina ta son bada kofar da za a zarge ki, koma dai miye ai be kamata yai wannan tunanin ba, and ko da kin aikata be kamata ya sameki kai tsaye da maganar ba!”

Momy ta fada a fusace, sannan ta mike tsaye yana wani kashe ido.

“Karki fito cin abinci, saboda Daddynku zai tambaye dalilin danuwarki, so ki zauna a nan zan fada masa kanki yana ciwo”

Leila ta daga kai, sai Momy ta juya ta fice daga dakin tana mamakin yadda Talba yake son sauyawa.
after like 40 minutes da fitar Momy wayar Leila tai ringing, hannu ta kai ta dauka tana duba number Ali dake kiranta, da kamar ba zata daga ba sai kuma ta daga wayar ta kara a kunnenta tai shiru tana sauraren abun da zai fito daga bakinsa.

“Kuka kike yi ko?”

Ta daga masa kai kamar yana gabanta, wasu hawayen na sauko mata. Be damu da yaji abun da zata fada ya sauke ajiyar zuciya daga can cikin wayar.

“I know na san abun da ya faru, can we talk? Gani a hanyar gidanku akwai maganar da nake son fada miki, please ki daure ki fito zan tsaya a gate”

“Okay”

Ta amsa masa tana jin wani sabon kuka na taso mata, sannan ta aje wayar ya lumshe ido, fuskar Baaba ce ta fara mata gizo, hakan yasa tai saurin bude idon ta mike tsaye ta nufi gurin windows din dakinta dafe kai wasu hawaye na sauko mata.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji

Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Madina ta jimmm bayan da Leila ta gama labarta mata abun da ya faru, gaba daya sai ta ji jikinta ya mutu.

“Yanzu dai ki fita ki ji abun da Ali zai fada miki”

“Zan je yanzu”

“Ki kwantar da hankalinki komai zai wuce, amman da zaki dauki shawarata da kin fadawa Talba gaskiyar komai, barin kashi a ciki baya maganin yunwa Leila, kuma yanzu zaki yi ta samun rashim fahimta a tsakaninku ne”

“Madina wannan sirina ne, Momy ma bata san na fada miki ba, amman na fada miki ne saboda na yarda da ke”

“Babu wanda zai taba jin wannan maganar daga gareni Leila, amman ina baki shawara ne akan abun da nake ganin zai zame miki masalaha”

“Yanzu dai bari na tafi Ali yana jirana”

“Okay”

Leila ta aje wayar sannan ta sauka saman gadon ta dauki wani karamin mayafi ta rufe kanta, sannan ta saka talkaminta ta nufi kofar fita idonta a kumbure saboda kukan da ta sha.
Ko da ta sauko falon babu kowa, dukansu suna bangaren Daddy, yan aikin Momy kuma Momy bata basu damar zama a falonta hakan yasa idan ba wani aikin zasu ba abu ne mai wahala ka gansu a main house din kullum suna BQ. A hankali ya bude kofar falon ta fita gabanta na faduwa, domin ji take kamar zata yi arba da Talba ne, domin a yanzu bata son ganin fuskarsa, ba dan bacin rai ba sai dan bata da amsar tambayar da zai mata. Tun kamin ta karasa gurin gate din police din ta bude mata karamar kofar ta fice, tana fitowa ta ga motar Ali fake sai ta nufi inda motar take. Ali na zaune cikin motar yana kallonta har ta karaso gaba daya sai ya ji tausayinta ya kama shi, a da can yana bata laifi kamar yadda yake

bawa abokinsa sai dai a yanzu ya fahimci abokinsa ne mai matsala ba ita ba. Bude motar tai ta shiga sannan ta rufe ta kalleshi da idonta da suka kumbura.

“Ali”

Sai da ya sauke wani dogon numfashi sannan ya amsa mata.

“Na'am Leila, ya kike?”

Tambayar ya take da yai sai ta ji kamar ya tsokano mata kukanta, a take hawaye ya cika idonta.

“Ba Kalau ba Ali, ba Kalau ba”

“Na sani, abokina yayi rashin tunani, amman ban dauka zai miki magana ba, a thought ya bar abun a ransa ne kawai, sai dai faga lokacin dana kira ki na ji yanayinki, sai tausayinki ya kama ni, and now na fahimci irin halin da kike ciki”

Ya karasa yana kai hannu ya ciro tissue ya mika mata, sai ta karba ta share hawayenta.

“Sometimes ina kasa fahimtar waye Talba, abokinka yana da wahalar sha'ani Ali, taya wanda zaka aura zai zarge ka da kisa? How? And Why? Saboda na nuna kishina? Talba be dadin zama wani lokacin”

“Na sani, amman ban dauka abun zai kaishi haka ba”

Cewar Ali yana kallonta gaba daya zuciyarsa ta cika da tausayinta, domin gani yake Talba baya sonta ita ce kawai sonsa ke dawainiya da ita.

“And i respect your decision na cewar ba zaki auri Talba ba har sai ya canja”

Juyowa tai ta kalleshi da kyau.

“Dan Allah zaka fada min abun da ta faru da yarinyar?”

A takaice ya labarta mata komai na yadda aka samu yarinyar, sai dai be fada mata cewar Talba ya dauke ta daga asibitin ba, haka ma be fada mata cewar sun samu tsabani ba, domin yana ganin kamar sirrinsa ne da be kamata kowa ya ji ba.

“Amman me zai saka wani yai mata haka?”

“Ni ma ban sani ba, kuma a iya binciken da na yi wani be shigo ba, so dole dai sai ta farka zata iya fada mana yadda komai ya faru”

“Yanzu tana asibitinku?”

“No na canja mata asibiti, and i am here to apologize saboda ni na janyo komai, Talba be san yarinyar nan ba, ni na hada shi da ita da neman ya taimaka mata saboda yarinyar tana bukatar taimako, amman ban yi tunanin abun zai zama na rigima haka ba”

“Baka da laifi, na san ka yi ne da kyakkyawar niya, be kamata ka bada hakuri ba”

Yayi shiru na wani lokacin kamin ya kalleta ya ce.

“Amman Leila kin yi wani abun ne da zai saka Talba ya zargeki da taba yarinyar nan?”

“Ban yi komai ba, amman kasan a gurin abokinka kullum nice mai laifi, kawai dai na fahimci wani abu... Talba baya so na ni ce kawai na mutu da kaunarsa, wanda yake sonka ba zai maka haka ba, ko da gaske na aikata zai nemi hanyar kare ni ne, ba ya tunkare da wannan laifi mai girma ba, abun akwai ciwo”

Ta karasa wasu hawaye masu zafi na sauko mata, har cikin ranta tana fadawa Ali abunda ta fahimta ne akan zamantakewarta da Talba. Ali ya kawar dai yana jin irin tausayinta na kara kamashi.

“Ada can na dauka miskilancinsa ne ya saka yake min abun da yake min, amman a yanzu na fahimci kauna ta ce babu abunsa, kawai ya amince ne saboda ba zai iya cewa Daddy a a ba”

Ta runtse tana kokarin fashewa da kuka.

“Kabir yana da fada min gaskiya amman na kasa ganewa, saboda kaunar Talba ta cika min zuciya amman yanzu na fahimta...”

Ali yayi saurin daukar ruwan dake cikin motarsa ya mika mata.

“Please sha ruwa”

Sai kuma ya dauko tissue ya mika mata.

“Ki daina damuwa dan Allah, kukan nan yayi yawa idonki har ya kumbura, me yasa zaki damar kanki akan Namiji?”

Sai ta kalleshi hawaye na sauko mata

“Talba be taba min haka ba, na gode”

Ta fada sannan ta karba ya share hawayenta ta bude ruwan ta sha.

“Ki je ki huta, karki saka damuwar komai a ranki komai zai wuce, kin san idan ya fusata yana aikata abubuwa amman zai sauko and ina tabbatar miki zai baki hakuri”

Ta dan yi murmushi irin na bakinciki da kuma kin yarda da maganar Ali cewar zai bata hakuri domin ta san waye Talba, sai dai bata ce masa komai ta bude motar ta fita, Ali ya bita da kallo cike da tausayi har ta shige cikin gidan, sannan ya kai hannu ya dauki wayarsa dake carji a jikin motar ya kira Talba, wayar tai ta ringing har ta gaji ta katse be daga ba ya sake kiransa nan ma shiru, haka ya jera masa kusan 4 miss calls a na biyar ya ji wayar a kashe alamar ya gaji da kiran da yake masa kenan kuma ba zai yi picking ba.

“Talba....”

Ali ya fada yana jin kamar ace yana kusa da shi yai masa dan banzan duka a yau saboda kukan da Leila ta sha akasa.

‘Ina ka kai yarinyar nan?’

Shine sakon daya tura masa sannan yai reverse ya kama hanyar gidansa.

TALBA POV.

Be dawo gidan ba sai dare, domin bayan an gama diban jininsa sai ya fito asibitin ya koma gidan marayun, daman can yakan je idan yana cikin bacin rai ko damuwa ya wuni a can, sai ya ji damuwar tasa ta ragu saboda yara suna rage masa kewa, and ko ba komai zai ji cewar ba shi ne kadai a damuwa ba, su ma sun rasa iyaye da yan'uwa amman sun zaune a inda Allah ya tsara musu rayuwarsu kuma suna farinciki, balle kuma shi da Allah yai ma ni'imar aje su da ciyarda su, bayan tarin lafiya da ni'imar yan'uwa da kuma ta uba kamar Daddy da Allah yai masa.
A can yai sallah magaba a can yai isha'i, be dawo gida ba sai ba tara saura, wunin yau bayan abincin safe be sake saka komai a cikinsa ba sai ruwa. Yana shigowa ya faka motarsa kusa da entrance din Momy sannan ya fito ya nufi kofar falon cikin yanayin da ba zai iya fada ba, kawai misaltawa yake idan har da gaske Momy da Leila suna da hannu a mutuwar Baaba ko batanta ya iyalanta za su ji? Yayanta da jikokinta? And ya ma akai komai ya faru? Idan ma kasheta sukai ina suka kai gawarta. Sau biyu yana danna door bell din sannan Amal ta bude masa kofar.

“Ya Talba welcome”

Ya amsa mata ta kai fuska ba yabo ba fallasa, sannan ya shigo cikin falon, hakan ta nuna alamar baya cikin walwala. karasa yai kusa da Kabir dake zaune a sofa yana cin tuwon samun miyar gayye ya zauna. Kallo daya yai ma tuwon ya dauke kai domin shi ba ma'aboci cin tuwo ba ne, wayarsa dake aljihu ya ciro ya kunna sai ga sakon Ali ya shigo wayarsa.

‘Ubanta ne kai?’

Shine reply din da yai ma Ali sannan ya aje wayar ya busar da iskar bakinsa. Kabir ya kalleshi sannan ya kalli Amal dake zaune tana kallonsu dama haka take idan ta lura da ba a zaune kalau, so that ta samu abun tseguntawa Daddy.

“Amal je ki yi bachi mana”

Kabir ya fada, sai ta make kafada.

“Bana jin bachi yanzu”

A take ya zare mata ido, hakan ke nuna ba da wasa yake ba, ya saba wasa da ita sosai sai dai a duk lokacin da yake serious magana da ita ta san yanayinsa. Mikewa tai tsaye tana kallon Talba.

“Ya sai da safe”

Ta murgudawa Kabir baki sai ya kyalkyale da dariya yai mata gwalo.

“Daddy's noy could we talk?”

Talba ya kalleshi.

“Leila ta fada maka ne?”

“Nooo Amal dai ta shinshino ta shinshina min”

Talba ya dan yi murmushi kadan yana kallon hannunsa.

“Na bada jinina yau”

Kabir ya duba shi duba na mamaki, ba zai ce ya san dukan abun da Talba yake yi ba, amman be taba jin yace zai bada jininsa ga kowa ba.

“Something new...”

Talba yayi murmushi.

“Yeah.... I feel like..... ”

Sai kuma yai shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

“I feel honour.. I mean it was a great joy.... to do....something like this”

A rarrabe yai maganar and he is very excited, he can't tell why amman yana jin yayi abu mai kyau.

“Yeah at least wani zai rayu da jininka, and mutumen nan ba zai taba manta ka idan ya sanka, idan kuma be sanka ba, kai zaka ji cewar wani yana can yana rayuwasa saboda ka taimaka masa da jininsa ko da kuwa siyarwa kai balle kuma ace kyauta ka bada, more especially ace mutumen nan yana cikin yanayi na bukatar jini tsakanin rayuwa da mutuwa...”

Talba yayi shiru yana sauraren kalaman Kabir, sai kuma ya soma tuna abun da ya faru a yau. Juyowa yai ya kalli Kabir.

“Idan mutum ya suma zai dauke ki awa nawa kamin ya dawo hayyacinsa?”

“Is depend on yanayin suman, ko kuma irin kulawar daya samu, but most wadanda tsoro yake saka su suma ko damuwa, ba su cika farkawa da wuri ba kamar wanda rashin lafiya ta saka shi suma, kuma ya danganta da kalar suman da mutum yai”

Shiru Talba yai alamar nazari sannan ya sake tambayar Kabir.

“Amman me ke saka mutum baya kuka da murya sai hawaye, kuma ba ya magana, baya cin abinci baya ma bude bakin”

Kabir ya aje spoon din da yake cin abinci da shi ya dauki ruwa ya sha.

“Depression... Damuwa tana saka wannan har fiye ma, tana saka hauka, rashin lafiya and so on, indai har ba wai mutum ya daman can haka aka haife shi ba, daga baya ne ya sauya gaskiya damuwa ce, tana tsoro tana saka mutum ya rika ganin abu yana imagination ko kuma zuciyarsa ta raya masa ya aikata ko ta saka shi hauka ko ya rika abu kamar mai aljannu, tana saka yawan mantuwa ko surutu ba akan abun da ake magana akai ba, you know komai n jikin dan'adam yana da limit din abun da yake iya dauka, so idan abun yai yawa ko yai kadan zaka tarar akwai irin illar da yake haifarwa”

Silently Talba ya sauke ajiyar zuciya.

“Idan mutum yana son yayi magana da mai irin wannan abu kamar ya tambaye shi wani abu ya zai yi?”

“Ya zai yi kuwa? Most important thing is ka yi kokarin cire wannan mutumen a damuwa, idan wani abu yake so ka sama masa, idan tsoron wani abu yake ka nuna masa babu abun da zai same shi kuma zaka bashi kula, ka sake jikim da shi kana bashi kulawa kana nuna masa far'a da walwala kana dauke masa hankali daga damuwar, kai ta kokarin ganin ka faranta masa rai, da haka da haka zaka ga ta saki jiki da kai, ka yi ta cusa kanka kana bata abinci tun bata ci har ta fara ci”

“Idan kuma ya ki fa?”

“Taki dai... Zata ma ci idan ta ji yunwa, idan ana saka mata maganine a ruwa na abinci ko kuma ana bata ta hanci a daina, as long as zata iya tashi zaune ko ta kwanta bata bukatar irin wannan maganin, a kyaleta ta wuni da yunwa idan ta ji babu komai a cikinta zata karbi abincin idan an bata, da haka zata saba ta rika ci, amman a yanzu ai an hanata jin yunwa ne, kuma ace ana son ta ci abinci?”

“But he cant walk fa”

“That one is different, maybe damuwar ce ta haifar mata da hakan ko kuma wani matsalar dabam, amman rashin lafiyarta ba zai zama da matsala a cin abincin ta ba, indai ba wai tana kan wani magani da aka dorata ba ne, shi ma kuma sai dai ace ba zata ci wani ba wani zata ci”

Talba ya yunkura da zimmar tashi sai Kabir ya kalleshi ya ce.

“Ita ce yarinyar?”

Da ido Talba yai masa alamar question mark, sai ya karansa tambayarsa.

“Yarinyar da kake zargin Leila tana kokarin kashewa?”

Talba be ce masa komai ba ya fara tafiya.

“And do you really think Leila zata iya wannan abun?”

Tsayawa Talba yai ya juyo ya kalli Kabir.

“Amal ta baka labarin Baaba?”

“No amman Momy ta fada mana yan'uwanta sun zo sun dauke ta right?”

“Yes amman dazun nan jikanta ya zo nemanta, so kai tunani akai”

A take Kabir ya cika da tsananin mamaki, Talba kuma ya juya ya fice daga falon. Bangarensa ya nufo kamin a karasa ya cire agogon hannunsa, sannan ya kai hannunsa na hagu ya bude kofar ya shiga, tafiya yake kamar baya son taka kasa ya karasa bathroom dinsa ya jefar da wayarsa saman gado, ya cire tufafin jikinsa ya daura tawul. Samun kansa yai da karasawa gaban katon madubin dake dakin wanda ke nuna iya tsayin mutun. Tsaye yai yana kallon kansa kamin ya kai hannu ya shafa kirjinsa zuwa cikinsa sai kuma ya dawo da hannun saitin inda zanen kirjinsa yake yana tabawa.
Motsin shigowar mutum da yaji ne yasa shi juyowa da sauri domin ya san ba kasafai ake shigowa bangarensa ba, Momy ba tai musu wannan tarbiyar ba, ta shiga dakin juna barkaita sai dai idan da wani dalilin. Takawa ya fara yi kamin ya isa bakin kofar Bathroom din Leila ta shigo, tsaye tai cak tana kallonsa daga kasa zuwa sama, wani irin bugawa zuciyarta tai da karfi a lokacin da idanuwanta sukai arba da faffandan kirjinsa. Tun da take a rayuwarta bata taba ganin Talba babu riga ba sai yau, duk kuwa da kasancewar a gida daya suka tashi sai dai baya bayyana mata siraicinsa kamar yadda ita bata taba nuna masa nata ba sai dai dan abun da ba a rasa ba, kamar saka damammen kaya ko wando da riga, sai dai rika hannunsa ko taba shi ba wani abu ba ne a gurinta kamar yadda shi ma be dauke shi komai ba.

“Ya akai?”

Ya tambaya yana kallonta, ba karamin jihadi tai ba na ganin ta daidaita natsuwarta, sai dai hakan be hana numfashinsa yin nisan kiwo ba na tsawon dakiku, ta dauken kai tana kokarin dawo da numfashin a hankali.

“Yarinyar ta fada maka wanda yai mata haka?”

“Kina da wata maganar ne bayan wannan?”

Juyowa tai ta kalleshi.

“Ita wannan maganar ba mai muhimmanci ba ce?”

“Mai muhimmanci ce a lokacin da ta fada min cewar ke ce ko ba ke ba ce, and kuma idan na gane gaskiyar komai a game da Baaba”

“Duka biyun ban aikata ba, miyasa baka yarda da ni ba? And me zai saka ka zarge ni da kisan yarinyar da kai ma basan san ta ba”

“She can't walk she can't talk, depression yana damunta, and now idan na gano da hannunki a ciki, i swear ba zan raga miki ba, you have no idea what she's going through”

Ta kara matsowa kusa da shi tana kallon idonsa.

“I don't care, she can't talk or walk is not my business, ta mutu ko ta rayu be dame ni ba, ina ta fito ina zata je me ya faru da ita duka ba matsala ta ba ce, all what i care is us....we... I mean us... Just us...”

Yanayin yadda tai maganar ya bayyana bacin ran dake tare da ita, shi ma kallonta yake ido cikin ido yana kokarin hana zuciyarsa tsanarta. Sai da ta gama yawo da idanuwanta a fuskarsa sannan ta juya ta fice daga dakin a fusace. Tana dawowa dakinta ta dauki wayarta ta kira Madina ta san is late amman tana son ta yi magana da ita mai muhimmanci.

“Hello Leila”

Madina ta yi picking.

“Madina fada yadda ake mantawa da mutum”

“Ban gane ba”

“So na ke na manta da Talba, na cire shi a raina gaba daya na manta da shi”

Wani irin murmushi ne ya kawata fuskar Madina, ta yi saurin aje kofin ruwan dake hannunta.

“Amman miyasa?”

“Na gaji ba zan iya ba, sai na nuna masa ni din mai tsada ce kuma na nuna masa he is nothing to me”

“Shikenan zan zo da safe, wannan maganar ba ta waya ba ce”

“Okay ina jiranki”

Leila ta katse wayar, sai Madina ta rike wayar tana kallo, rabuwar masoya ba abu ne mai kyau ko dadi ba, sai dai ita ya zo mata a dabam domin ta samu kanta cikin farincikin jin abun da Leila take kokarin aikatawa.

BATURIYA POV.

Kamar yadda Ramlee tai mata alkawarin kawo mata kayan mata da zata sha a jiya, ta kawo mata su cike kamar wanda zata sara ta kai su wani gurin, ita ma kanta ta yi mamakin tarin hakin mayen da Ramlee ta kawo mata, wanda za a hado da madara ko zuma a sha duka ta siyo mata madarar da zumar, yadda ta ware kudi ta siye mata kayan matan sai ka rantse da Allah yarta ce.
Hakan yasa ta bude wardrobe dinta ta saka su ta rufe da makulli, idan zata sha sai ta bude ta debo ta sha ta rufe, ko Sultan bata yarda ya gani ba balle kuma Faruq uban gayya.

Bayan ta gama gyara gidan yayi tsab ta dora girkinta da wuri, sannan ta shigo falonta ta dauki wayarta ta kunna data ta fara chat. Zata yi reply wani sako kiran Fahat ya shigo wayarta, da sauri tai picking ta kai wayar a kunnenta.

“Hello”

“Yan mata ya kike?”

“Lafiya kalau, sai marmarinka”

“Uhm mmn Marmari kamar gaske, ke da kin ki bari ma na zo mu gaisa, sai kwana kwana kike min”

“Ai na fada maka gidamu ba za a bar ni ba, ba a barin mu zance gaskiya”

“Amman ai kin yi girman da ya kamata ace ana barinki zance Fee'at”

Ta lumshe ido tana jindadin yadda ya kira sunanta, daman haka take so ba kamar yadda Faruq yake kiranta da Rafi'a ta yi complain har ta gaji, sai yace mata shi ba ba ta soyayya yake ba, ta neman kudi yake da abun da zasu ci.

“Ba zaka gane ba ne”

“Na gane, kuma suna da gaskiya, wasu iyayen basa barin yayansu su na kula samari barkatai, amman idan kin amince min zan iya sakawa a zo a nema min izinin magana da ke har mu fahimci juna”

“Da gaske?”

Ta tambaya tana tashi zaune daga kwance da take.

“Wallahi kuwa, Fee'at ni fa da gaske nake aurenki zan yi, ba da wasa na zo ba”

“Uhmm”

“Allah kuwa, Momyna ta dade tana min maganar aure, ansha kai ni gurin yan mata da yan'uwa amman wallahi ban taba jin wanda tai min ba, amman ke ina ganinki na ji wani abu akanki Fee'at you're different...”

Ba karasa maganar da yake ba ta yanke wayar ta kasheta gaba daya sakamakon jin ana kwankwasar gidan. Fitowa tai ta isa gurin kofar ta bude sai tai arba da Faruq yana dauke da Sultan.

“Har kun dawo”

Sai da yai kamar kar ya amsa mata sai kuma ya amsa.

“Eh, Sultan shiga ciki”

Ya karasa yana sauke Sultan dake rike da ledar kifi kasa. Sannan ya juya ya

“Zan tafi shago”

“Allah ya tsare”

Ta fada kamar ba ita ba har sai da ya juyo ya kalleta, rabon da tai masa addu'a har ta manta.

“Ameen”

Ya amsa sannan ya juya ya cigaba da tafiyarsa, ita kuma ta maida kofar ta rufe taja hannun Sultan suka nufi cikin gidan tana tunanin maganar da Fahat yai mata.

‘Amman da gaske yake zai aure ni? Ko kuma dai wasa yake? Amman ai be san na taba aure ba, idan na fada masa gaskiya zai yarda ya auri bazawara?’

Ita kadai take ta haukanta ta saka wannan ta kwance wacan, gaba daya sai hankalinta ya tattara ya koma gurin Fahat tana ta ayyana irin rayuwar da zata yi, kasancewar sa mai kudi kuma dan masu kudin.

“Momy Mama tace a gaishe ki”

Sultan ya fada yana zaunawa ya bude ledar kifin.

“A hanya Dady ya siya min, yace na ci rabi na baki rabi”

Ba ta ma kula, gaba daya hankalinta yana gurin Fahat.

“Amman fa na masa karyar arziki, wata kila yana min kallon yar masu kudin ne”

Sultan ya kalleta.

“Momy waye?”

Sai a lokacin ta lura da a zahiri tai maganar ba a badini ba.

“Ba kowa ba ci kifinka, ga abinci can akan wuta idan yayi zaka ci kaji”

Ya fada mata kai ita kuma ta shiga uwar daka ta dauki wayar ta kunna, sai ga sakon Ramlee ya shigo mata.

‘Ki sha kayan nan da yawa, yace yana son ku hadu da gobe, na kira wayarki ban samu ba, idan kin gama karantawa ki goge sakon’

Dundundun ta ji gabanta yayi duka uku uku, ba dan bata saba haduwa da mazan da ba muharramanta ba, sai dai wata kila saboda wannan haduwar ta daban ce, saboda zata aikata sabo ne alhalin tana da aure da kuma da, ga kuma karamin ciki a jikinta.
Saurin goge sakon tai kamar yadda Ramlee ta bukata, sannan ta mike tsaye ta isa bakin kofar dakinta ta tsaya tana kallon Sultan dake ta aikin cin kifinsa hankali kwance, damuwa ce ta bayyana a fuskarta, duk wani dauki da take na son a bata kudi sai ta ji ya ragu, domin bata taba aikata alfasha ba, sai a wannan karon ne zata gwada. Juyawa tai ta koma cikin dakin tana busar da iskar bakinta.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji

Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

LEILA POV.

Sam bachi ya gagari idonta saboda yunkurin da take a zuciyarta na naki da soyayyar Talba. Sai ta kasa samun hadin kan sassan jikinta ciki har da idanuwanta, da kuma zuciyar datai mata garkuwa da kaunar Talba. Sai yanzu ta gane ashe abun ba shi da sauki, daman taya zai zame mata mai sauki? Ta rayu da kaunarsa na tsawon lokaci a dare daya ta ce zata cireta?
A maimakon ta ji kuzarin cirewar ta karfafawa kanta guiwa, sai ta samu kasala tana jin kamar ba zata iya rayuwa idan babu Talba ba.
Sai dai tana jin ajinta da martaba da kimarta ta wuce Talba yai mata haka kuma ta cigaba da sonsa ko waye shi kuwa?

“Na girmi wannan... Amman why?”

Ta furta tana jin kamar ba zata samu hadin kan zuciyarta ba.

“Allah karka min jarawa da kaunar mutumen nan”

Ta furta ta saka hanayenta biyu ta share hawayen da suka zubo mata. Mikewa tai tsaye ta nufi gurin window ta bude window ta tsaya a gurin tana kallon taurarin da suka kawata samaniya.

“Do i deserve this? It's painful...”

Ta fada wasu hawayen na sauko mata, a rayuwarta bata san zafin rashin ba, bata san ta nemi wani abu ta rasa, wata wani abu painful irin na wannan daren ba, a damuwarta akan halin Talba ne, amman a yanzu abun ya ninku tana jin kamar ba zata iya yakar kaunarsa a zuciyarta ba, kuma ba zata iya barin kaunar ta zauna ba then me zata yi?
Ta yi kasa da kanta wasu hawaye na sauko mata, ta fashe da kuka marar sauti, sai kuma ta soma murmushi.

“Ni Leila ina kukan namiji? Wannan ba ajina ba ne, at least na san Talba be isa yace ba zai aureni ba, amman ni din ai be kamata na aure shi bayan duk wannan abun da yai min ba, be kamata na damu ba”

Ta share hawayenta, sai magana take da kanta tana kallon harabar gidan kamar wani bakonta. Can kuma ta rumgume hannayenta tana tuna kalaman Kabir cewar Talba yana son ta, sometimes akwai kamshin gaskiya maganarsa, amman idan har Talba baya son ta waye zai so? Dole dai ita din ce.

“Akwai maza da yawa da suka fi Talba komai a duniyar nan, kudi, kyau, aji da komai ma, idan zan ba wa maza da yawa dama zan samu wanda zan so fiye da Talba ma”

Wannan karon with full confidence tai maganarta tana jin cewar zata iya. Ba laifi ta dan samu karfin guiwa da dakiyar zuciya, hakan yasa ta rufe window ta dawo saman gadonta ta hau ta kwanta ya rumgume filo ta lumshe ido tana son bachi ya dauke ta.
A nan ne bachi ya ce mata fir ba dai shi ba a yanzu, tunanin abun da Talba yai mata sai ya dawo mata a rai ya zauna, idonta zuciyarta kuma a bude, har kusan karfi uku na dare, Leila ba mace ce ma'abociyar karatu ba balle ma har tai tunanin raya daren da nafila.
Bata yarda ta bude idon ba duk kuwa da kin bata hadin kai da bachin yai. Sai kusan asuba bachi yai gaba da ita.
Washe gari Sunday kamar jiya kowa ya hadu a gurin cin abinci ban da Leila, sai dai a yau bangaren Momy aka zauna ba kamar jiya ba da aka karya bangaren Daddy.
Daddy ya gama duba kowa be ga Leila, hakan ya saka ya kalli Momy.

“Doctor ina Leila?”

“Tana dakinta i think”

Daddy ya yi mata wani kallo da kyau.

“So you think? Lafiya take na lafiya tana dakin ma ko bata ciki baki da tabbaci?”

“Uhm wani lokacin kana bani mamaki Alhaji, yaran nan fada wayansu ya kamata idan muka gan su a wani yanayi da suke son kebancewa mu bar su a yanayin da suke ciki”

“Amman idan suna da damuwa fa? Har kullum wanda ka haifa kana masa kallon yaro ne ko da kuwa ya girmi duniyar nan, irin wannan abun shi yake haifa da depression mutum yana da damuwa kuma a kasa maganance masa ita ko a ki kula da shi, wannan be dace ba, ko jiya bata ci abinci safe tare da mu ba”

Momy ta tabe sannan ta kwalawa Mairo kira, Mairo dake kitchen tana wanke kayan da sukai amfani da su, ta amsa tana fitowa da sauri.

“Shiga dakin Leila ki kirata”

“Hajiya Wallahi ko dazun dana shiga gyara dakin fada tai tayi tace idan a sake shiga dakinta ba tare data fito ba ko kuma na tashe ta bachi sai ta mare ni”

Mairo ta fada a ladabce. Sai Daddy ya kalleta.

“Ta mare ki? Yarta ce ke?”

“Wata kila fada dakin ne ba sallama ko knocked”

Momy ta amsa.

“No wannan ba dalili ba ne, at least ai ta girmamasu sun gurme ta nesa ba kusa ba”

“Wallahi Daddy haka take musu, ko magana cikin tsawa take yi”

Amal ta dora da nata, sai Daddy ya kalleta sai dai be ce komai ba ya cigaba da cin abincinsa, Daddy mutum ne mai matukar son yayansa, ko kadan baya son ya ga wani abun bacin rai ko n damuwa ya same su, sai dai hakan be taba saka shi ya kyalesu a inda ya kamata ya gyara musu ba kuma ya saka musu ido.
Sai da Daddy yai rabin cin abinci sannan ya kalli Momy ya ce.

“Yawan fushi ko tsana yana nuna akwai abun da yake damun mutun ne, musamman a kwana biyun nan da bata fitowa cin abinci, idan akwai wani abu da yake damunta ki sama mata mafita, akwai abun da ke ya kamata ki yi a matsayinki na uwa, zata fi sakewa da ke kuma ta bude miki cikinta ta fada miki damuwarta, and to you my friends idan akwai wanda yake mata wani abu da zai sakata a damuwa ko bacin rai dan Allah ku daina, ya zama tsintsiya madaurinki daya, idan dayanku yana cikin damuwa ku yi kokarin ganin kun kawar masa Allah ya hada kanku yai muku albarka”

Duk suka amsa da Amin, sannan Daddy ya mike tsaye yana fadin.

“idan kin yi magana da ita, ki fada mata ina son ganinta”

“Okay”

Momy ta amsa tana watsawa Talba harara kasa kasa domin har ga Allah yanzu haushinsa take ji, saboda yana kokarin wuce gona da iri. Sai da Daddy ya fice daga falon sannan Momy ta dakawa Amal tsawa

“Amal... Wallahi idan na sake jin bakinki akan fadawa Daddy magana any how sai na baki mamaki, sai na miki hukuncin da baki taba mafarkin zan miki ba, cigaba karki fasa”

Momy ta karasa tana dukan burin dinning din sannan ta mike tsaye ta bar gurin a fusace. Amal ta bata fuska kamar zata fashe da kuka, Kabir ya saka mata dariya. Talba ya kalleshi.

“Kabir?”

Ya sake bushewa da dariya yana yi ma Amal gwalo.

“Sai a hana ni dariya? Yarinyar tafi kowa iya gulma, bata gidan amarya bata gidan ango ai maganinki kenan”

Dariyar ya cigaba da yi mata yana cin abincinsa, ita kuma ta kara bata fuska kamar zata fashe da kuka.

“Karki biye Kabir kin san halinsa ai, daman so yake ki yi kuka, karki yarda ki masa kuka”

“Ai ba zan masa kuka ba, na fi karfin na yi masa kuka”

Ta fada tana matse hawayen dake son fito mata. Kabir kam ban da aikin dariya babu abun da yake mata, daman shi haka yake gurin dariya da keta shine a gaba gaba.
Talba be bar dinning din ba sai da cikinsa ya cika, sannan ya tashi yana handala da muryar da shi kadai zai iya jin kansa ya nufi bangarensa.
Tufafin jikinsa ya cire ya saka gajeren wando sannan ya hau gadonsa ya kwanta, da zimmar bachi amman ya ji kamar ba zai iya bachin ba, hannunsa ya mika ya dauki wayarsa dake gefen gadon, sai ya tararda miss calls har hudu daga Ali.
Ganin kiran na Ali ne ya tuna masa da Aminatu, sauka yai saman gadon ya nufi bandakinsa, ta bata minti talati yana jika jikinsa sannan ya dauki man wanka ya zuba ya soma gogawa a jikinsa. Bayan ya gama wankan ya fito daure da tawul dayan kuma a hannunsa yana goge jikinsa da shi, gaban madubin ya zo ya tsaya da alama dai kallon kansa a madubi abu ne daya zama masa al'ada, domin yana jindadin tsaya a madubin yana kallon kansa.
Sai da ya tsane jikinsa sannan ya dauki wani mai ya shafa a jikinsa ya feshe jikinsa da turare, ya murza wani a shafa a jikin, sannan ya shirya cikin kananan kaya ya dauki turaren tufafi ya saka sannan ya murza wani a hannunsa, sai ya juya ya nufi gurin da yake aje agogonsa ya dauki wanda yake ganin ya fi dacewa da tufafin jikinsa ya saka, ya saka talkaminsa sannan ya dauki wayarsa ya da wallet dinsa ya saka aljihu ya dauki wata Jacket milk color ya dora sama. Sannn ya fice dakin rike da makullinsa na mota. Sai da ya isa gurin motarsa sannan ya daga kansa yana kallon windows din dakin Leila, bakinsa ya cika ma iska sannan ya bude motar ya shiga. Ko kamin ya juya motar har sun bude masa gate, kamar dominshi kadai aka shimfida titi, haka ya fige mota ya hau titi yana driving. Kiran Ali ne ya sake shigowa wayarsa, sai ya saka hannunsa ya dauko wayar daga aljihunsa yai piciking.

“Hello”

Ali ya fada daga dayan bangaren sai Talba ya amsa masa kamar baya son magana.

“Ya akai?”

Ali yayi dariya.

“Kar kace min har yanzu fushi kake, Ni da n kira na fada maka ka ya kamata ka bawa Leila hakuri, sai kuma na ji ka a fushi har yanzu”

“Ali taya na kusa da ni zai wulakanta dan adam ya muzanta shi kuma ka tsammaci abun nan zai wuce da sauri? Kawai fatan da nake ya zama na babu hannun Leila a taba yarinyar nan, and zan binka matsalar Baaba na tabbar idan akwai hannunta ko babu”

“Wace Baaba kuma? Talba are you in sense? Miya samu Baaba and why za kai blaming Leila? Ban taba yarda baka son ta sai...”

Ali be karasa Talba ya yanke kiran ya aje wayar ya cigaba da tukinsa, ya san idan zai bata lokaci yana ma Ali bayani a yanzu ba zai fahimta ba saboda yana ganin tausayin Leila kuma yana ganin kamar Talba yana mata haka saboda baya sonta.

Be sake bin ta kan wayar ba har ya isa asibitin ya faka motarsa a inda aka tana domin aje motoci, sannan ya dauki wayar ya bude motar ya fita.

Kai tsaye ya dauki hanyar da zata sada shi da dakin da aka kai Aminatu, so kawai yake ta farka ya tambaye ta, idan ta amsa masa da eh zai dauki mataki akan Leila idan kuma ya zama tsabanin haka zai bata taimakon da take bukata be kuma zama lallai ta sake ganinsa ba. Ba dan wannan abun daya faru ba wata kila ma da ba za zai sake sakata a idonsa ba har abada.

A hankali ya kai hannunsa ya tura kofar dakin, sai kuma ya tsaya daga bakin kofar yana kallonta, kwance take idonta a rufe hawaye na sauko mata, an cire mata robar jinin an saka mata ta ruwa, sai kuma ledar pure water dake saman dan karamin tabur din dake kusa da gadonta. Silently ya shiga cikin dakin ya maida kofar ya rufe, sannan ya isa gurin gadonta yana kallon fuskarta, ko kadan bata ji motsin bude dakin ba balle kuma shigowarsa ba, sai dai kamshin turarensa ya dawo da ita duniyar tunanin da tafi, hakan yasa ta bude idon a hankali a karo na biyu ta sake saka idonta cikin nasa, bayan wacan karon da suka zo tare da Ali, sai dai yanayin fuskarta sa ya tsorata, da alama ba mutum ne alaka da sakin fuska da murmushi ba. Sai dai kallonta yake kamar yadda ita ma take kallonsa hawaye na cigaba da sauko mata.

“Can you talk?”

Ta tambaya domin burinsa ta amsa masa da eh ko aa. Sai ta maida idon ta rufe.

“Keeee.!!!”

Ya daka mata tsawa, sai ta bude idon a zarane ta tashi zaune jikinta na rawa ta fara dube dube, domin ta tsorata matuka, abu kadan sai zuciyarta ta fara bugawa tana ganin kamar abun da ya faru ne a baya zai sake faruwa.

“Mi na yi, kashe ni za ayi?”

Tsayawa yai kallonta a ransa yana jinjina irin tsoratata da Leila tai. Be ankaro ba ya ji ta fashe da wani irin kuka mai taba zuciya, hakan ya saka shi matsowa kusa gadon.

“Ba komai za a miki ba tambayarki kawai zan yi”

Ta kalleshi jikinta na cigaba da rawa hawaye na sauko mata kamar ba gobe.

“Me zaka tambaye ni? Inna? Ko Baba? Ko kuma yan'uwana?”

Shiru yai yana kallon yadda idonta yai ja tsabar kukan da take, ya hade yawun bakinsa tare da maida numfashi a hankali.

“Ki kwantar da hankalinki babu abun da za a miki, kawai ina son na tambaye ki ne ko akwai wanda yai kokarin kasheki kamar makura, saboda an samu hannunta yana zubar da jini kuma roba zagaye a wuyanki”

Kokarin natsuwa take tana son tuna abun da ya faru, sai ta daga kanta tana kallon dakin, sai a yanzu ta tuna akwai banbanci tsakanin wannan dakin da wacan.

“Zaki iya tunawa?”

Ya sake tambaya.

“Ban manta komai ba, komai yana cikin kaina, idanuwana suna ganin komai har yanzu”

Ta amsa masa cikin rashin kuzari.

“Good fada waya kika gani kamin su suma?”

Ta kalleshi.

“Ban ga kowa ba”

“Wa yayi kokarin kasheki?”

“Babu”

“Amman an tarar da hannu da jini...”

Be karasa ba ta bashi amsa, bakinta a bushe kana ganinta kasan yunwa da ciwon sun mata mugun kamu.

“Ni ce ni na aikata”

Kallonta yake irin kallon nan dake nuna so yake ya gano idan tana cikin hayyacinta ko akasin haka. Sai ya ware mata hannunsa.

“Miye wannan”

Ta kalli hannun nasa, sai kuma ta koma zata kwanta.

“Keeee!”

Sai ta zaburo masa kamar ba ita ba.

“Miye? Me kake so? Me zan maka? Dan Allah ka bar ni da damuwata, ka bar na ji da abun da yake damuna”

“Ni ma ba damuwa ba ne, i just want to ask miyasa kike son ashe kanki..”

Shi ma a tsawace yai mata tambayar zuciyarsa na bugawa da karfi yana jin kamar ya dake ta saboda ta masa tsawa.

“Saboda na mutu, na huta, na tafi inda yan'uwana suka tafi na tararda mahaifiyata da mahaifina, ta tafi inda ba a zalinci inda ba a danne hakkin kowa, na tafi inda....”

Ta kasa karasawa sai numfashinta yai sama ta fadi kwance saman gadon wuyanta a lankwashe, da sauri ya kai hannunsa ya rikota ta gyara mata wuyanta.

“Baba.... Baba.... Baba.... Baba...”

Shine kawai abun da take ta fada tana kallon Talba da idanuwanta da suka fara rufewa. Fita yai dakin da sauri ya nufi inda likitoncin suke ya fada musu sai likita da nurse uku suka taso a guje suka nufo dakin, zai shiga wata nurse din ta dakatar da shi.

“Malam ka tsaya a waje...”

Sai yaja ya tsaya gabansa na faduwa, kalamanta sun ratsa shi ga tausayinta, a yanzu kan ya tabbatar tana da babba damuwa wanda zata iya haifar mata da matsala kamar yadda Kabir ya fada. Yana tsaye a wajen har suka fito. Likitan ne ya tsaya yana tambayar Talba yayin da nurses din suka wuce.

“Ya kake da wannan mai rashin lafiyar?”

Talba yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

“Kanwata ce”

“Dan Allah bismillah akwai bayanin da zan maka”

Likitan na fadar haka ya wuce gaba, Talba ya bi bayansa har suka shiga cikin Office. Talba ya zauna ba tare da jiran likitan yai masa izini ba.

“I'm sorry ban sani ba, ko an maka bayanin cewar yarinyar nan an mata fyade, fyaden da ya wuce na hankali, da alama ba mutun daya ba ne ko biyu, domin abun yayi effecting kwakwalwarta, tana jin tsoro gaskiya, so ya kamata ka kiyaye bacin ranta damuwa, kuma kai kokarin kwantar mata da hankali, and karka dame ta da tambaya ko son sai ta tuna abun da ya faru, domin a yanzu ta kai matakin da zuciyarta zata iya bugawa, kuma be zama lallai idan ta buga ta rayu ba, za a iya rasa ta”

Ya karasa tare da mika hannu ya dauko wata takardar yai rubutu akai, ya mika masa.

“Ka siyo wannan maganin ba mu da shi a nan”

Talba ya kai hannu ya karba yana kallon takardar maganin.

“And zata fara cin abinci daga yanzu, domin na ga a file dinta an rubuta cewar bata ci, sai dai jiya na gwada bata ruwa ta sha kuma ta sha, so from now on zata fara cin abinci”

Talba ya gyada masa kai. Sannan ya juya ya fice daga office din jikinsa a mace, tafiya yake yana tuna kalaman da tai masa da kuma na likitan, and the most important part is fyade. Kamar marar kuzari haka ya bude motar ya shiga ya zauna.

“She's too young for this, maybe sun ashe Mamanta Babanta and su kai raped dinta... Wow.... ”

Ya furta yana runtse ido, yana ayyana yadda abun yake da mugun ciwo. Wayarsa ya ciro ya nemi number Kabir ya kira shi.

“Ranka ya dade”

“Kabir wane chemist ko pharmacy zan samu magani ko wane iri a yanzu?”

“Wa zaka siya wa?”

“Kai... ”

Kabir yayi dariya. Sannan ya fada masa, Talba ya kashe wayar ba tare da sake ce masa komai ba, sannan yai ma motar key yai reverse ya fice daga asibitin. After ya siye maganin ya siyo ayaba da kankana da lemu a hanya sannan ya dawo asibitin, kamar wani barawo haka ya shiga dakin without making a sound, har gaban gadonta ya karasa ya aje ledodin.

“Waye kai?”

Ta tambaya a hankali idonta a rufe, kallon mamaki yai mata a zatonsa bachi take but maganar da tai ya tabbatar masa da tsabanin haka, sai dai idonta a rufe yake.

“Talba, you can call me Talba...”

Ya samu kansa da amsa mata yana kallon fuskarta. Sai ta bude ido a hankali ta kalleshi, ta sake maida idon ta rufe.

“Idan kina bukatar wani abu ki fadawa likitan zai sanar da ni, kuma idan zaki iya fada zamu so sanin inda yan'uwanki suke sai a bincika so that su san kina raye kuma ki samu mai kula da ke”

“Da rayuwata da mutuwa ta duka daya ne, saboda ba ni da kowa a yanzu”

“Shiyasa kike kokarin kashe kanki? Ko kuma dai wani ne yake kokarin kasheki?”

Ta bude idon ta tashi zaune cikin rashin kuzari tana kallonsa, idonta har ya yi baki yayi ja kamar tsabar damuwar da kuka.

“Idan baka ci abinci ba akwai mai damuwa? Wani yana damuwa idan baka da lafiya? Idan ka shiga damuwa akwai mai kokarin faranta maka rai? Akwai wanda zai so abun da kake so, ya guji abun da zai bata maka ra?”

Yayi shiru yana kallonta, kamin ya hade yawun bakinsa, ya daga mata kai alamar eh akwai.

“Ni duk na rasa wannan, a cikin dare daya rayuwata ta sauya, a tsakanin awannin da dakiku aka min katanga tsakanina da iyayena, farincikina yana tare da yan'uwa kuma duka an kashesu, a ciki wuni guda aka juya duniyata, aka nesanta ni da farinciki, a kusanto da bakinciki, a cikin daren nan aka raba ni da martaba da, na kasa manta komai, hoton komai ya gagara goguwa a idanuwana, a tsakanin wacan daren da dararen da suka biyo bayansa bakinciki ne da tashin hankali, sum rusa duniyata, sun tarwarsa shirina...”

Kallonta Talba yake a tsakanin hawayenta da duniyarta da take labarta masa sai ya rasa wane ne yafi tsaya masa a zuciya. Kujerar dake gefen gadon ya ja ya zauna yana kallonta.

“Likita yace ki daina damun kanki, saboda yanayinki yawan tunani da damuwa zai iya haifar miki da wata matsalar...”

“Akwai matsalar data wuce ta rashin uba da uwa? Rayuwata ta riga ta sauya, bana tsoron mutuwa....”

“Amman baki yi tunanin miyasa mutuwa take gudunki ba? Na san kin shiga a gurin da za a iya kasheki amman ba a yi ba, kika samu kanki a nan kuma kika yi kokarin kashe kanki, still hakan be faru ba, rayuwata tana ta zabenki ke kuma kina neman mutuwa baki yi tunanin ya kamata ki rayu ba?”

Ta lumshe ido tana jin bachi na son daukarta saboda allurar da akai mata.

“Na rayu a inda ba a rufa idan akwai sanyi, ba a fakewa a idan ana ruwa, ba a gusawa idan rana ta kawo, a hannu ake raba mana abinci, idan an bada da safe ba za a sake ba badawa ba sai da dare, na ga wa ana dukan wasu, kuma a kashe da yawa a gabana, sun keta haddin mahaifiyata a gabana, sun yanka yan'uwana, sun kona abincin mu, suka akashe babana saboda ya ki yarda ya keta haddin ni, sanadin tafiyar da muka yi kafafuwana basa iya komai a yanzu, sun yanka yan'uwana sun fasa kan wasu da dutse, a haka kuma kake ganin rayuwata tana zabata? Wata kila saboda tana son na yi taraiyya da bakinciki ne”

Hawaye ya sauko mata sai bachi yai baga da ita, ido ya sakar mata kalamanta na taba zuciyarsa, misali yake da kansa idan shi ne ya zai ji? Yana rayuwa cikin jindadi lokaci daya ace komai ya tarwatse! Shi kansa maraya ne, amman be san zafin rashin iyaye ba, be san zafin rashin yan'uwa ba, idan wani abun ya same shi da gudu za a kawo masa agaji, tsabanin it. Takurewa tai gurin daya ta jikinta na dan rawa alamar tana jin sanyi ga kuma hawayen har yanzu ba su daina zuba ba, murmushi mai sauti ne ya biyo bayan hawayen.

“Inna....”

Ta furta tana cigaba da murmushi, sai kuma tai fuskar kuka wasu sabbin hawayen suka zubo mata. Mikewa yai tsaye ya cire Jacket din jikinsa zai lulluba mata sai jikimta ya fara, tana numfashi da karfi ta kara rumgume kanta kana ganinta kasan a tsorace take, a hankali ya lullub mata jacket din sai kuma ya tsaya yana kallonta har lokacin hawayenta zuba suke, wani dogon numfashi yaja ya sauke sannan ya juya ya fara tafiya a hankali zuwa gurin kofar.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un... Taya zan tafi na barki? Ko na gudu harbina zasu yi, ba zan tafi ba tare da ke ba...”

Juyowa yai ya kalleta, kana ganinta ka san wani tashin hankalin ne take mafarki, da alama abun da ya faru ya shiga ranta sosai ya zauna, ya kusan minti biyar a tsaye yana kallonta sannan ya fice yaja mata kofar a hankali ya rufe.

Dan Girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

FARUQ POV.

Mama ta sauke ajiyar zuciya tana jinjina lamarin Rafi'a.

“Faruq ka saka mata ido, duk abun da take tana yi saboda ta bata maka rai ne, kuma komai na rayuwar duniya jarabawa ne, ko da arziki ne Allah ya baka ya ga yadda zaka iya rike su, balle kuma talauci, da muguwar mata”

“Wallahi Wani lokacin Rafi'a tana bani mamaki, ita kamar bata san Allah ke yi ba? Shi zai yi ma kansa arziki ne? Sai ta rika abu kamar ba yar'uwa ba?”

Aisha ta dana da nata. Sai Faruq ya kalleta.

“Wani lokacin ina jin kamar na sake ta na huta, sai dai idan na tuna irin wahalar da mahaifinta yai da ni a karatuna kuma ya dauki yarsa ya aura min duk da a lokacin bana da komai, sai na kamar idan na sake ta ban kyauta masa ba”

“Haka ne, wani abu dole a daga mata kafa saboda mahaifinta, domin mutumen kwarai ne, kuma na tabbatar da yana raye Rafi'a ba zata maka wani abun ba, kasan Umma daman ba son auren take ba tun farko shiyasa komai tai bata ganin laifinta, amman kai hakuri Inshallah sauki yana tafe”

Ya ja wani dogon numfashi ya sauke.

“Ni da har na yanke shawarar na bi Yusufa mu tafi nijar gurin ginar zinarina nan”

“Nijar kuma?”

Cewar Mama ciki damuwa.

“Eh kin ga masu zuwa suna samowa ba laifi, kuma ba kasan inda rabonka yake ba, amman zama haka ba zai yi Mama, hausawa sun ce idan hagu ta ki sai a koma dama”

Mama ta girza kai.

“Wallahi bana son tafiyar nan nesa Faruq, da dai ka hakura mu ga abun da Allah zai yi”

“Mama duk inda rabonka yake sai ka tararda shi, ko kuma ya nemeka, kuma abun da Allah ya rubutawa bawa ko a ina yake zai same shi, na san dai ba zai wuce ki ce kina jin tsoron hanya ba ko abunda zai faru da ni, kawai ki min addu'a”

“To Allah ya zaba mana abun da yafi zama alheri, idan tafiyar Alheri ce Allah ya shige maka gaba”

“Ameen idan Allah yasa naje ko na siyen fili na samu ai na samu”

“Haka ne, amman kudin motar zuwa can fa?”

“Har cin abinci da komai zan iya kashe 20k haka Yusufa ya fada min, kuma yace ana kwana uku kamin a samu isa, wannan kudin da ban biya haya ba zan iya cire na mota ciki sai kuma sauran kuma na siya ma Rafi'a abinci na bar mata kamin mu tafi kuma mu ga abun da Allah zai yi”

“Toh Allah ya shige maka gaba”

“Ameen”

Ya fada yana mikewa tsaye sai kanwarsa ta kalleshi.

“Ya Faruq ance fa rame ake shiga, ko. Kwanan baya na ji ance rame ya rusga da wasu”

Murmushi yai.

“Allah shi ke tsarewa ai, ku dai kui ta mana addu'a”

“Toh Allah ya tsare, yasa arzikinka na can”

“Ameen ya Rabb”

Ya amsa sannan yai musu sallama ya fice, ko da ya isa gida har ta gota, a bude ya samu kofar gidan, sai ya shiga da sallama ya maida kofar ya rufe sannan ya shiga falon, sai ya same ta tana waya sai dai ganinsa yasa ta sauke wayar ta kalleshi.

“Sannu da zuwa”

“Yauwa, ya gidan?”

“Alhamdulillah”

Sai ta tashi ta nufi inda abincinsa yake ta dauko masa ta aje masa tare da ruwa.

“Ina Sultan?”

“Yayi bachi”

Ta amsa sannan ta zauna kusa da kujerar da yake zaune, kallonta yake har ta zauna din, gaba daya yau ta canja, daman can fara fes amman haskenta and yau ya karu sai wani sheki take tana ta kamshin hummura mai tsada. Dauke kansa yai ya maida dubansa gurin abincin data aje masa yana hade yawu, rabon da wata mu'amalar aure ta shiga tsakaninsu har ya manta, domin bata yarda idan ma ya neme ta, idan ya matsa sai tace ga ciki ba zata iya ba, shi kuma baya son yi mata da karfi hakan yasa ya dauke mata kai ta wannan bangaren ba dan baya bukata ba sai dan ba zai iya ja'inja da ita ba.

“Rafi'a ina ta shawara da kuma neman zabin Allah”

Ta kalleshi da sauri a tunaninta ko zai fada mata cewar daya faga cikin aikin da yake Applying ne wani ya fito.

“Na me? Aikin ka samu ne?”

“Aa, ina shawarar zuwa nijar ne?”

Wani irin yatsine fuska tai kamar wanda tai arba da abun kyama.

“Nijar fa kace? Ba dai gurin ginar zinari ba ko?”

“Can mana”

“No nonono, Wallahi ba zan yarda ba, so kake ka ja min abun magana a gari? Ace mijina ya tafi gurin ginar zinari? Talaucin har ya kai nan? Aa Wallahi ba zaka je ba”

“Shi zuwa ginar zinari zunubi ne? Wace irin magana ce wannan nan?”

“Kana tafiya za a ce talauci ya matsa mana har ka bar gari ka tafi nema nijar, ka ja min abun magana, kawaye na mazajensu daga masu aiki a kamfani sai banki sai ma'aikatun gobnati, ni kam ba zan iya ba Wallahi”

“To sai na fasa saboda ke nan? Ni na riga na yanke shawara, kuma na zo na fada miki ne saboda na baki hakkinki”

“To Wallahi ba zan yarda ka je ba, Wallahi sai dai ka sake ni ka tafi na san ba mu tare”

Dubanta yai irin duba na mamaki.

“Rafi'a me kike son ki zama? Ke kin isa ki yi ma kanki arziki ne, da abu kadan zaki fara cewa talauci?”

Sai ta mike tsaye domin ya fahimci da gaske take.

“Wallahi Faruq, na rantse da Allah ba zaka tafi nijar ginar zinari da aurena ba, sai dai idan tafiya ce zaka yi ta har abada, wanda babu dawowa, wai kai baka da zuciya ne? Baka san Annabi ya faku ba, na gaji da abun kunya Faruq, na gaji, aurena dole ne? Ni kadai ce mace a duniya nan ne? Ba zan iya ba, ga danka nan yayi wayo amman ka kasa saka shi makaranta, wannan da zan haifa ma na san dan taure zaka yanka min”

“Sai ki saki kanki ai, ba saki ba? Ba zan saki ba kuma sai na tafi nijar din ki mutu, ina hakuri ne dake kawai saboda Mama da kuma mahaifinki”

Ya fada yana mikewa tsaye, sai ta sa gabansa.

“Wato ka fito gurin bakar tsohuwa ta kitsa maka abun da take so a kai...”

Bata karasa ba ya wanke mata fuska da mari sai da ta fadi zaune. Ta fashe da kuka.

“Faruq ni ka mara?”

“Har abun da yafi mari zaki samu, matukar iskancinki da rainon wayo ya kai ki ga taba mahaifiyata, ai ko da ba ta hada komai dake ta cancanci girmamawa saboda tana sarakuwarki balle tana a matsayin kanwar mahaifinki”

“Ita bata san da zumuncin bane ta barka kana ta cutar da ni? Ba zan iya ba, na ce bana so ka sauwake min mana”

Har yayi kamar Ya bude baki yace na sakeki sai kuma wata zuciyar ta hana shi. Be sake kulata ba ya shiga bedroom din, bakin gado ya zauna yana kallon Sultan dake ta bachi ya kai hannu ya shafa shi, makomar dansa yake zubawa idan har ya sake ta rayuwarsa zata zama abun tausayi, domin zaman zai zame masa a tsakanin gida biyu, gidan mahaifinsa da kuma inda Mahaifiyarsa. Tsabar bacin rai da tunani be ci abincin ba ya kwanta kusa da dansa, Baturiya kuma ta kwana a falo.
Washe gari waina ya siyo musu abun kari kasancewar aljihunsa da dan nauyi irin na masu nema yau da gobe, bata gaishe ba tun da garin Allah ya waye, sai dai hakan be hana shi ce mata zai fita ba, da harara ta bishi babu Allah ya tsare balle addu'ar alheri.

“Allah yasa kai hadari ka mutu..”

Ta fada bayan ta ji karar rufe gidan, sannan ta tashi ta bude wainar ta zubawa Sultan, ita kuma ta nufi wayarta ta dauka ta kira Fahat, ringing biyu ya dauka.

“Fee'at”

Sai ga murmushi a fuskarta kamar ba ita ba, bata kula da Sultan ba ta cigaba da wayarta tana masa kalaman soyayya kamar yadda shi ma yake mata. Sun kusa awa daya suna abu daya sannan sukai sallama tana masa kiss a wayar, duk abun da take Sultan na kallonta sai dai ita bata lura da hakan ba. Fitowa tai waje ta fara gyara gidan domin Ramlee ta fada mata karfi goma za su hadu. Ko da tara tai Baturiya ta gama komai har ta shiga ta yi wanka. Sai da ta shirya sannan ta kai Sulta makota ta dawo gidan ta kara daukar wasu kayan matan ta sha daman Ramlee ta nuna mata wadanda zata sha idan tana kusan tafiya.

Tara da rabi kiran Ramlee ya shigo wayarta, jiki na rawa ta dauka kamar ba ita ce ta gama jin tsoro ba a jiya.

“Madam hop kin shirya”

“Na shirya, ke kawai nake jira”

“Haka na ke so, ba wasa ganin nan nima na kusa karasowa”

“Sai kin iso”

Ta aje wayar tana murmushi, ita ma kanta ta san ta yi kyau, sai kamshi take zubawa kamar sabuwar amarya, kamin Ramlee ta iso ta shafa hoda ya kai sau shida, turare kan ba adadi irin feshin da take masa.
Tana jin sallamar Ramlee ta dauki wayarta da jakarta ta fito waje da sauri.

“Wow yanzu kika fito da sunanki n Baturiya, amman mutumen idan ya ganki sai ya rude”

Baturiya ta yi dariyar jindadi.

“Da gaske”

“Wallahi kuwa, sam sam baki dace da Faruq ba, ke din matar manya ce, amman fa karki fada masa cewar kina da aure domin na ce masa ke din bazawara ce”

“Ke ma dai da wata magana, ya za'ayi na fada, Allah dai ya sa inda zamu je ba public place ba ne, domin akwai wadanda bana son su gan ni”

“No guest house dinsa ne, muje dai kar mu bata lokaci”

“Amman kin san me? Idan na fita da kwaliyar nan haka ina kamshi mutanen unguwa za su fara saka mana ido”

“To ya zamu yi? Ke dai ina ruwanki da mutane ne wai?”

“Aa bari dai a saka hijab da nikab idan na je can sai na cire a motarki”

“Haka yayi yi sauri”

Ta juya ta koma dakinta da sauri ta dauko katon Hijab ta saka tare da niqab sannan fito ta rufe gidan.
Tun daga yanayin ginin unguwar da shuke shuken zaka san cewa unguwar manyan mutane ce, a gaban wani katon gate suka faka Ramlee tai horn Mai gadin ya leko tai magana da shi sannan ya bude mata ta shiga, a harabar gidan tai fakin ta ciro wayarta ta kira shi.

“Alhaji mun iso”

“To yayi Kyau Hajiya Ramlee a barta ta dan huta gani a hanya, garin sauri ma na kade wasu amman dai na gama komai zan iso yanzu”

“To yayi Alhaji sai ka iso”

Ta aje wayar sannan ta labartawa Rafi'a abun da ya faru da shi.

“Kuma ki sake jikinki ki kwashi arziki, domin yana son ki Wallahi na fada miki hotonki kawai ya gani amman duk yabi ya rufe balle kuma ce ya yi arba da ke”

“Inshallah ba zan baki kunya ba”

“Yayi kyau, haka nake son ji, yanzu mu shiga ciki na nuna miki falonsa sai n fito na bar ku ku sha shagalinku”

Ramlee ta fada tana murmushin jindadi. Sai Baturiya ta cire Hijab din da Niqab ta kai hannu ta bude motar wayarta tai kara.

“Allah yasa ba mijin nan naki ba ne”

Cewar Ramlee tana tabe baki, fasa fitar Baturiya ta yi ta ciro wayar daga jakarta ta duba.

“Shi ne kuwa, ban san mi zai ce min ba, ko kuma ya dawo gida ne oho”

“Karki dauka dan Allah zai wargaza mana shiri ne”

“Ai ba zan dauka ba”

Ya fada tana kallon wayar dake ta ringing har ta gaji ta tsinke, sai gashi ya sake kira sai dai wannan karon ta ji gabanta ya dan fadi.

“Kai wannan miji na ki da ci yake, gaskiya ki kashe wayarki kar ya zo yana damunki da kira ya lalata mana shiri”

“Wallahi kiran Fahat kawai nake jira, saboda yace zai kira ni anjima bana son na kashe wayar ya kira ya jita a kashe zai damu ne”

Ramlee ta mata wani kallo.

“Da alama dai shi ma dan hannu ne”

“Aa Wallahi shi ai son aure yake min da gaske, na nuna Masa ni Budurwa ce”

“Amman ke yar banza ce, ya zaki yi da Faruq?”

“Haba Ramlee kina min fatar zama da shi? Ai rabuwa zamu yi, kin ga idan ya sake ni ina zubar da cikin nan na cika idda zai na yi aurena”

“Kina ganin Faruq zai sake ki ne?”

“Dole na idan na bude masa shikashikan rashin mutunci ai dole ya sake ni”

“To dan fa ki yi yaya da shi? Ai kin san za a bincike ki musamman yayan manyan mutane basa aure zai sun zurfafa bincike”

“Ai idan na fita zan bar Sultan a gurin Faruq ne, ba da shi zan je ba, kuma shi Fahat din ai yace min a Lagos yake aiki, kin ga zamanmu a can zai kasance ba a nan ba, zan iya boye komai”

“Ki ce kema kin iya bala'i

Sai duk suka saka dariya, kiran Faruq ne ya sake shigowa wayar, wannan karon wani tsaki taja ta kashe wayar gaba daya.

TALBA POV.

Sai da yai sallah azahar sannan ya karaso gida, tun kamin yayi fakin idonsa suka sauka akan Leila dake zaune a daya daga cikin kujerun da suke balcony rike da wayarta sai cup din lemu a gaban kujerarta tana taunar cingan har wani kis kis take. Yayi kusan five minutes a motar sannan ya bude ya fito ya nufo inda take zaune ya zauna ba tare da yace da ita komai ba, hakan ya bata damar dauke kai daga gefen da yake ta maida wani gurin tana cigaba da taba wayarta.

“Can we talk?”

Ya fada ba tare da ya kalli inda take ba, sai ta juyo ta kalleshi.

“Ta fada maka ba ni ba ce ba kenan?”

Shi ma juyowa yai ya kalleta fuska ba yabo ba fallasa.

“Daddy ya damu dake ne i want us to talk”

“Da gaske?”

Sai ta mike tsaye ta dauki cup din lemun ta wuce ta bar masa gurin. Tana kokarin kai hannu ta danna door bell din kofar falon sai ga Kabir ya fito, ko kula shi bata yi ta shige, da kallo ya bita kamin ya juya ya kalli Talba dake kallon harabar gidan, har lokacin tunanin Aminatu yake. Karasa Kabir yai ya zauna a inda Leila ta tashi.

“Ya jikinta?”

“Da sauki...”

Talba ya amsa ba tare daya kalleshi ba.

“Ka yi magana da Leila ne?”

Ya girgiza masa kai.

“Wani lokacin baka sanin damuwar mutane idan baka kusantar su, you see yan gudun hijirar nan da kake gani a hanya wasu a fankon guri, suna da labaruka masu taba zuciya”

“Ita ma tana daya daga cikinsu ne?”

“Tana daya daga cikinsu ne?”

“Yeah they raped her, killed her Father, mother suka gona musu gida, suka kashe yayyunta and raped her mother in front of her, labarinta akwai tsoro da taba zuciya, yanzu haka she can't walk saboda wahalar data sha gurin mutanen nan, and bata da kowa kuma tana bukatar kulawa sosai”

Talba ya fada cikin yanayin dake nuna zuciyarsa ta tabu sosai da labarin Aminatu.

“You know a lokacin da kake raina ni ni'imar da Allah yai maka, wasu da yawa suna can suna neman kadan, a yadda na fahimta now yanzu farinciki take bukata, saboda ya cire rai daga shi har tana neman kashe kanta, and Ali and wannan likitan sun fada min abun nan ya taba ta”

Kabir ma saurarensa yake cike da tausayin Aminatu duk da kasancewar ba taba ganinta ba, sai dai ya san waye Talba duk abun da zai saka shi a damuwa ko tunani ba abu ne kadan ba.

“Yanzu a wane matsaya take”

“Tana samun kula a asibitin, amman babu mai kwana a inda yake kuma kasan da ace tana uwa ko wata yar'uwa a raye zata fi samun kulawa, tana jin tsoro sosai har magana take idan tana bachi, and likitan ya fada mim idan tana yawan damuwa zuciyarta zata iya bugawa, yarinya ce karama kamar Amal, bata san inda zata je ba”

“Haka ne mutane suna cikin hali, sai dai idan baka shiga cikinsu baka sani”

Talba ya mike tsaye yana saka hannunsa aljihu. Ya nufi bangarensa, Kabir ya bishi da kallo yana murmushi.

LEILA POV.

Tana shiga dakin ta dauki wayarta ta kira Madina ta fada mata abun da ya faru, a ciki har da kudinta na son ta fadawa Daddy cewar ta fasa auren Talba.

“Anya idan kika yi haka baki yi kuskure ba? A Maimakon ki ta wannan haukan ba kara ki nuna masa kina son yarinyar ba ko da a munafunce ne”

“Lallai Madina baki gama sanina ba, ke a tunaninki zan iya share miji ko saurayi da wata? Har sai na nuna ina son ta bayan duk abun da yai min, ni fa na san ba sonta yake ba kawai yana amfani da ita ne ya cusa min bakinciki?”

“Idan har haka ne, ke me zai hana ki yi amfani da abokinsa ki rama abun da yai miki?”

“Waye kenan?”

“Ali mana, ta hanyarsa ma zaki iya tabbatarwa idan Talba yana sonki da gaske”

“Kin kawo shawara, tabbas zan iya rama abun da yai min ta hanyar Ali”

“Yes amman ina fatar hakan ba zai janyo matsalar da zata hana a dauke ni aiki ba, kin san fa ina nan ina ta jira”

“Aiki ai dole a dauke ki, bari anjima ma zan yi ma Daddy magana, ki kwantar da hankali cikin kwana biyun nan za a dauke ki aiki”

“Alhamdulillah, na gode sosai yau zan yi kwana farinciki ko ba komai ai hakan zai kara kusantar da alaka ta da ku”

“Haba ai mun fi haka dake, zan kira ki anjima”

“Okay thank you”

Ta sauke wayar tana murmushi, har cikin ranta take jin cewar Madina ta sama mata mafita na bata shawarar ta yi soyayya da Ali, ta san idan tai haka zata Talba sosai kuma zai gane irin zafin da take ji ita ma.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Khadeeja Candy

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe

Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Zaunawa yai saman gadon yana goge ruwan jikinsa. Sannan ya kai hannu ya dauki wayarsa dake ringing.

“Ali ka dame ni fa”

“Ai dole na dame ka Talba, ka bawa Leila hakuri?”

“Na yi maka kama da wanda zai yi wannan?”

“Seriously Talba baka kyauta ba, kuma ya kamata ka bata hakuri, be kamata alakarku ta lalace saboda wata bare can da baka san inda ta fito ba”

“Leila ta yi abun da yake bani mamaki ne, so dole na zargeta akan halin da yarinyar nan ta shiga, lastly karka sake min maganar bada hakuri”

“Really kana ganin ka kyauta kenan? And me yarinyar ta fada maka?”

Can sama sama Talba ya fada masa abun da Aminatu ta fada masa.

“Yanzu ina yarinyar take?”

Ali ya tambaya yana sauke ajiyar zuciya.

“King's and queen's hospital”

Cewar Talba sannan ya mike tsaye yana shafa fuskarsa.

“Labarinta be taba ka ba?”

“Kai ya taba ka kenan?”

“Yeah, duk wani mai imani ne dole ne labarin yarinyar nan ya taba shi”

“Kar tausayinta ya saka ka manta da yadda kake da Leila, tsakani da Allah yarinyar nan tana sonka kuma tana azabtuwa da irin abun da kake mata”

“We can talk later”

Yana fadar haka ya kashe wayar ya jefa saman gado, sannan ya shiga dan karamin dakin da aka tanada domin ajiyar tufafi ya saka riga da wando na suit blue sannan ya fito ya dawo gaban madubi yana duba kansa. Komawa yai ya dauki turare ya murza a hannunsa na fesawa kuma ya fesa a jikinsa. Sannan ya dauki abun da ya kamata ya dauka ya fice daga dakin yana kokari saka wayarsa aljihu.
Ya fito bangarensa ya nufi bangaren Momy sai dai turarensa ya riga shi isa bangaren Momy saboda karfin kamshinsa, yau kam a bude ya samu kofar falon Zulai nata aikin mopping tana ganinsa tai saurin risinawa ta gaishe shi, sai dai be ma kalleta ba balle har ya amsa mata. Motsin da yaji a kitchen ne yasa ya nufi kitchen din, sai dai be karasa ciki ba saboda ya hango Leila a tsaye kusa da Momy da alama yau kamar a tare suke hada abun karyawan.

“Momy ina kwana?”

Momy ta juyo ta kalleshi, sai ta amsa fuska ba yabo ba fallasa.

“Lafiya Kalau an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah”

Ya amsa sannan ya juya da zimmar ficewa, sai Momy tai masa tayin abun kadyawan.

“Ba zaka tsaya ka karya ba?”

Kamar zai ce a a sai kuma ya juyo.

“Idan an gama a saka min a kula zan tafi da shi”

“Okay”

Momy ta amsa sannan ta dauki abu ta shiga zuba masa dukan abubuwan da suka hada, yana ganin haka ya fice daga kitchen din, ko da ya fito Zulai ta gama mopping din sai ta bude masa kofa da sauri, ya fice yana addu'ar fita daga gida, sannan ya nufi inda Motarsa take fake, tun kamin ya karasa ya danna remote din hannunsa motar tai kara ta bude kanta daga lock. Hannunsa ya mika ya bude motar ya shiga ya zauna yana warming dinta, yana kokarin yin reverse da Motar, Mairo da fito da gudunta rike da kwadon abinci ta nufo inda yake, after yayi reverse din ta bude gidan baya ta saka masa sannan ta rufe motar tana masa addu'ar Allah ya tsare.
Kamin ya isa gate ya daga wayarsa ya kira Daddy, domin ba al'adarsa ba ce ficewa ba tare da ya gaisa da Daddy ba, sai idan Daddy na bachi ko kuma baya garin, ko kuma wani ne, shi kadai ne ke saka shi fita ba tare da yayi ido biyu da Daddy ba. Har ya hau babban titi Daddy be dauki wayar ba, as usual idan ya kira sau daya ba a dauka ba zai sake kira ba.
Sai kawai ya aje wayar ya cigaba da tukinsa, a gogon hannunsa ya duba a daidai lokacin daya faka motarsa harabar asibitin, sannan ya bude motar ya fito ya bude baya ya dauki abinci ya nufi ciki, akwai jama'a sosai a asibitin ba kamar jiya da shekaran jiya ba da suke ranakun hutu, yau kam Monday mutane sai hada hada suke, kamar bako haka ya tura kofar dakin ya shiga. Zaune ya same ta tana ta kallon kofar kamar mai jiran shigowar wani, hawaye suna mata zuba, sai da ya maida kofar ya rufe sannan ya karasa kusa da ita ya aje abinci.

“Ya jikinki?”

Sai ta juyo ta kalleshi, ta kasa amsawa.

“Ya sunanki?”

Ya tambaya yana cigaba da kallonta.

Nan ma bata ce komai ba, sai ya matsa kusa da inda aka aje file dinta ya bude yana dubawa Ramlat Ibrahim ya ga an rubuta.

“Ramlat...?”

“Aminatu...”

Ta amsa tana kallon wani wajen tare da kai hannu ta share hawayenta.

“Mamana, ba ki gajiya da kuka?”

Sai ta sake kallonsa a karo na biyu tana murmushin da ya fi kuka ciwo.

“Baka san yadda nake ji ba, yanzu ba ni da mai damuwa da ni, babu wanda ya rasa kamar yadda na rasa komai a lokaci daya, yanzu bara zan koma a titi, ina zan kwana? Me zan ci ko na ci babu ruwan kowa, ni kadai na rage.... ”

Kamar fada take maganar tana kuka mai karfi, sai kuma ta saka hannayenta ta rike kanta tana lumshe ido. Kallonta kawai Talba yake har ta fara yunkura sauka saman gadon.

“Zauna karki sauka”

Dagowa tai ta kalleshi, sai ta zauna din kamar yadda ya bukata ta rumgume kanta tana hadiyar yawun bakinta da ya bushe. Dukawa yai ya fara bude abincin yana dorawa a saman gadon da take sannan ya duba fruits din daya kawo mata jiya, domin tun jiya da ya kawo mata fruit din ya fita be sake dawowa ba.

“Baki ci komai ba?”

Ya tambaya yana kallonta. Sai ta daga masa kai.

“Ina jin yunwa amman bana iya cin komai, kuma hannuna baya kaiwa”

Be sake ce mata Uffan ba, ya bude mata abinci.

“Zaki iya cin wannan?”

Ta kalli abinci sai ta girgiza masa kai, alamar aa domin komai na duniyar baya burgerta. Zai sake yin magana likitan daya karbeta ya shigo dakin rike da takardu da wata Nurse a bayansa.

“Yauwa, daman ina son magana da kai”

Likitan ya fada sannan ya mika masa hannu suka gaisa. Sai kuma ya shiga duba Aminatu.

“Kina jin wani ciwo ne?”

“Kirjina yana ciwo sosai ksmar zai cire, kuma idanuwana ma suna ciwo suna kai kayi”

“Ki daure ki rage tunani, da yawan kuka damuwace ke saka haka, ita kuma damuwa bata da magani kamar a gusar da abun da yake rai”

Ya fada yana rika hannunta ya saka mata abun hauna bp ya aunata, bayan ya gama ya kalli Talba dake tsaye ya ce

“Tsakani da Allah yarinyar nan na bukatar kulawa, akwai maganin daya kamata ace ana shafa mata a kafa kuma ana bata lokaci zuwa lokaci, and tana yawan kuka wanda hakan yana kara mata damuwa, kamata yayi ace akwai wani abu da zai dauke mata hankali, ka ga ko shiga bandaki ya kamata ace akwai mai rikata domin jiya ma a nan tai fisari sai da aka gyara gurin, sannan tana zaman kadaici ne kawai babu kowa a tare da ita a nan”

Talba ya kalleta cike da tausayi, shi kansa ya san tana bukatar mai kula da ita, domin tufafin jikinta ma sun yi datti duk da kasancewar Ali ya saka an canja mata wasu tufafin tun a lokacin da take asibitinsa.

“And jiya ma ance bata yi bachi ba sai magana take ta yi da kanta tana kuka, be kama ace kullum sai an mata allurar bachi sannan zata iya bachi ba, domin ita kanta allurar yawan yinta yana haifar da wata cutar ta dabam”

“Ba ni da wanda zai kula da ita a yanzu gaskiya”

“Ko da a gida?”

Yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

Aminatu ta kalleshi da idanuwanta da suka sha kuka har suka canja kala.

“A yanzu ba mu da gida, idan kun gaji da ni, to ku kai ni gurin da yan gudun hijira suke zama, ko kuma gidan marayu ko gidan nakasassu, ba ni da kowa...”

Talba ya risina kusa da gadonta yana kallonta cike da tausayi.

“Ba nasasa kika yi ba, ciwo kika ji, kuma zaki warke soon ko Likita?”

Sai likitan ya daga mata kai yana murmushi.

“Bata da kowa ne?”

“I can take care of her zan kai ta gida...”

Talba ya fada, sannan ya mike tsaye.

“Okay, idan zaka kaita gida, za ta fi samun kulawa gaskiya, domin a yanzu damuwarci kawai ciwonta sai kuma kafafuwan. Amman a shawarce zai fi kyau ka

samu likitan da zai rika zuwa yana dubata, ko kuma ka rika kawota time to time asibiti ana duba kafar”

Talba ya daga masa kai alamar gamsuwa, Likitan ya kai hannunsa ya rika kan Aminatu ya bude idonta.

“Ki daina yawan kuka kina daga idonki sama saboda kar glass din idonki ya samu matsala”

Ita dai bata sake ce masa komai ba har yai abun da zai yi ya fice. Sai da ya fice sannan Talba ya zauna a saman kujerar dake facing din gadon yana kallonta.

“Ki zama mai jajircewa da hakuri, komai da kika gani na rayuwar duniya baya zuwa da sauki, kuma kowa da kalar jarabawarsa, and ina tunanin Allah ya hada ni da ke saboda na taimakeki, wata kila da dace da wani kika hadu shi ba ni ba, da yanzu wani labarin ake ba wannan ba, so ki dauki haduwa ta dake a matsayin kaddara, akwai wani karon magana da ake cewar when life gave you hundreds reasons to cry, show life you have thousand reasons to smile, ina da tabbacin zaki zama jaruma, ki hade komai ki rayu ko dan iyayenki”

“Kuka ya zame min dole baka san yadda nake ji ba, rashin iyaye yan'uwa abu ne mai matukar ciwo, lokaci daya na rasa komai”

Ajiyar zuciya ya sauke yana kallonta, hawaye nata wanke mata fuska kamar ba gobe.

“Na san yadda kike ji, ni ma maraya ne kamar ke ba uwa ba uba, banbancina da ke shine, ni ban taba kukan maraici ba, ban taba neman wani abu na rasa ba, ke ma kuma za ki samu kulawa Daga yanzu har karshen rayuwarki, kamin ki gane danginki, zan sama miki wasu dangin da zaki zauna tare da su, su rika debe miki kewa, na san ba za a rasa wani daga familynki da yake raye ba, From now on babu abun da zaki nema ki rasa Inshallah, babu abun da ya dace da ke a yanzu sai farinciki!”

Ta yi kasa da kanta tana hawaye.

“Da gaske na rasa kowa kenan! Da gaske ni kadai zan rayu? Taya farinciki zai zama a tare da ruhin da bakinciki ya zagaye, kuka da damuwa suka masa masauki? Har yanzu na kasa yarda a duniya na ke, an raba ni da kowa”

Ta fashe da sabon kuka tana jin wani irin bakinciki mai taba zuciya yana ratsata.

“Faranta ran mutane na daga cikin abun da yake saka ni farinciki, musamman irinki, ta ya mutum mai imani zai same ki a irin wannan halin kuma ya kasa taimakonki? Ki saka a ranki daman can haka Allah ya rubuta kuma akwai irinki da yawa”

Haka ya dage yana ta kokarin kwantar mata da hankali kamar na shi ba. So yake ta ji cewar ba ita kadai bace a cikin halin damuwa, so that ta kwantar da hankalinta, gudun kar abun yai mata yawa.

“Ki ci abinci yanzu sai na yi ma likitan magana, ya ba ku takardar sallama”

Wannan karon har dan guntun murmushi a fuskarsa.

“Bakina akwai datti da yawa”

Ya dan wara ido yana jin haka yasa mai tsabta ce.

“Okay bari muje gida gaba daya sai ki wanke bakinki a can ki karya”

Ta yi shiru bata ce masa komai ba, sai ya rufe abinci ya mike tsaye ya fice daga dakin. Be dade ba ya dawo rike da wata takardar sai wasu nurse biyu bayansa, su suka dauke ta suka saka ta a Wheelchair. Shi kuma ya dauki abincin kadai ba tare da ledar fruit din daya kawo ba sai kuma magani. Nurse din ce ta turo ta, shi kuma yana gaba har suka isa gurin motarsa, back seat ya bude musu suka saka ta sannan ya bude bayan motar suka saka masa wheelchair din, after ya rufe ya nufi driver seat ya bude ya shiga ya zauna.

“Yanzu zaki ga sabon gidanku da kuma yan'uwanki”

Ya fada ba tare da ya juyo ya kalleta.

“Na gode Yallabai”

Ta fada da muryar kuka, domin a yanzu ko kalma yan'uwa ta ji sai ta tuna da nata.

“Talba sunana, daga yanzu ni yayanki ne, kin zama kanwata gashi kina da sunan Momy kin zama Shalele”

Bata ce komai ba, har ya fara tukin motar ya fice daga asibitin, yana hawa babban titi ya fara gudu kamar yadda ya saba, sai jikinta ya fara rawa ta fara tsorata, abun da ya faru ya taba mata zuciya kuma ya shiga kwakwalwarta ya zauna, abu kadan sai hankalinta ya tashi.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ta furta da karfi tana runtse idonta. Hakan yasa shi juyowa ya kalleta sai ya rage gudun da yake, sai dai be ce mata komai ba, ita kuma bata yarda ta bude idon ba har suka isa gidan da bata san yadda yanayinsa da tsarinsa ba. Harabar gidan ya faka ya motarsa sannan ya fito ya dauko Wheelchair ya aje ya bude back seat din yai ma daya daga cikin mai aikinsu hannu, sai gashi ya zo da gudunsa.

“Ka dora Wheelchair din nan a kofar falo, sai ka saka yarinyar nan ciki, ka dauko abinci yana ciki Motar”

Ya fada yana kallon motar Daddy dake fake, hakan ke tabbatar da Daddy be fita ba kenan. Wayarsa ya ciro daga aljihu da zimmar kiransa sai ya hangoshi ya fito direbansa na rike da jakarsa, da sauri ya nufi inda yake Daddy na hango shi sai ya tsaya jikin motar yana jiran karasowarsa.

“Daddy good morning”

“Morning Mu'az har na fita?”

“Yeah muna da meeting a office, amman ka rasawa na dawo na fada maka wani abu”

Daddy ya masa irin kallon nan dake nuna ina saurarenka. Tun daga biri har wutsiya ya fedewa Daddy komai, ba karamin tausayin yarinyar Daddy ya ji ba.

“Yarinyar tana ina?”

“Gata acan na zo da ita, ina neman amincewarka, idan kuma hakan be maka ba, zamu iya duba wani gurin sa zamu iya ajeta, saboda gida marayunmu yawanci kanana ne ba su kai kamar ta ba, idan ma na aje ta a can zata sake shiga kadaicin ne”

Daddy yayi murmushi jindadi ya kai hannunsa ya dafa kafadar Talba.

“Ina alfaharin da kai Mu'az ka ci sunana kuma baka rago komai daga halina ba, mu gidan nan ai kullum muna marhabun da baki ne, kuma ni uban marayu ne karka manta da wannan, ko da ace tana da kowa nata a raye ta so zama da mu zan dauke ta kamar ya balle ma tana marainiya, ka yi tunani mai kyau ka ga yanzu kun zama ku biyar, Allah ya muku albarka”

Talba yayi murmushi.

“Thank you Daddy, amman Momy ba lallai ta yarda ba”

Daddy yai masa wani kallo.

“Momy ke da gida ko ni?”

“For now ita ke da gidanta...”

“Really to bari mu ga idan kai aure kai ne da gida ko matarka”

Talba yayi murmushi.

“Wannanai dabam, ni Talba ne kai kuma Daddy ne”

Daddy ya girgiza kai yana murmushi tare da zolayarsa.

“Za'a min izinin ganin yarinyar?”

Ban da dariya babu abun da Talba yake, ya wuce gaba Daddy ya biyo bayansa, sai dai hakan be hana su isa kofar falon a tare ba.

Talba ya danna door bell ba dadewa aka bude masa sai ya matsa Daddy ya fara wuce sannan shi ma ya shiga. A tsakiyar falon ya hango Aminatu zaune a wheelchair ta sanda kanta kasa hawaye na sauko mata, Kabir na tsaye gabanta. Momy kuma na zaune a kujera daya ita da Leila suna kallon ikon Allah.

“Ita wannan bata magana ne?”

Kabir ya tambaya yana kallon Talba.

“Ka dame ta da surutun ne ko?”

Cewar Daddy. Sai Kabir ya ce.

“Sunanta kawai na tambaya, sai ta rufe ido ta fara min kuka”

Daddy ya karasa kusa da ita yana kallonta cike da tausayawa.

“Sannu Allah ya baki lafiya”

Bata bude idon ba har sai da ta ji kamshin turaren Talba, sannan ta bude ido ta kalli inda take jin kamshin na fitowa, ido biyu suka yi sai dai nata idon cike suke da hawaye.

“Ya sunanta?”

“Sunan Momy”

Talba ya fada, sai Daddy yai murmushi ya kalleta.

“Yar gata ce kenan, sunan matata kuma uwar yayana kin ga babu wanda zai taba ki a gidan nan! Ki kwantar da hankalinki ki dauki kowa kamar dan'uwanki ni kuma na miki alkawarin zama mahaifinki da yarda Allah, duk abun da zan iya yi ma yayana zan miki Inshallah”

Talba yayi murmushi, sai Kabir ya wara ido.

“Ji wannan daga zuwanki zaki karbe mana fada, bari fitinanniyar ta zo zata zalzaleki”

Daddy ya girgiza kai yana dariya.

“Aa yanzu ita ce auta, daga gani Amal zata girme ta ai”

Ya fada sannan ya dago ya kalli Momy.

“Hajiya karaso ki ga yar da muka samu kyauta daga Allah”

Momy ta taso daga inda take zaune tare da Leila suka karaso inda Aminatu, sai da Momy ta kare mata kallo sannan ta ce.

“Ya kamata a nemi izini na kamin a kawo ta, amman sai ganin musaka nai a falona, saboda ban isa da gidan ba”

“Na fara magana da Daddy ne, kamin na yi magana da ke, ni ma ban yi zaton hakan zai faru ba sai da likitan ya fada min sai na ga kamar hakan ya dace”

“To be dace ba, be kamata ka dauko min wata bare can ka kawo min a gida ba, yarinyar da ban san daga inda ta fito ba”

A hankali Aminatu ta dago ta kalleta sai ta maida kanta kasa.

“Momy karki tsorata mana, ba nan ya kamata ku yi wannan maganar ba”

Kabir ya fada. Sai Momy ta watsa masa harara.

“Idan na tsoratata sai ka saka zane ka goya ta ai”

Daddy ya hade rai yana kallon Momy cikin rashin jindadi.

“Bana son maganar nan, Danki zai fada miki komai”

Sannan ya kalli Aminatu dake hawaye.

“Aminatu ki kwantar da hankalinki kin ji, mu iyayenki ne”

Ta kasa dagowa ta kalleshi ma balle ta ce masa komai, har sai da Talba ya kirata da sunan da Inna take kiranta da shi.

“Auta...”

Sai ta kalleshi da sauri tana jin wani tsam a jikinta.

“Ki cewa Daddy kin gode”

Ya fada yana mata murmushi kadan kamar na dole. Sai ta kalli Daddy da idanuwanta da ke zubar da hawaye.

“Na gode...!”

“Oh Really.. Zai ka mata umarni zata yi magana kenan”

Kabir ya fada yana kallon Talba, murmushi kawai Daddy yai ya nufi kofar fita.

“Zan tafi kar na yi latti, sai a gyara mana daya daga cikin dakunan da suke kasa nan”

“Da a BQ na so ta zauna”

Talba ya fada.

“Why BQ ga dakuna a cikin gida? A bar ta nan BQ ai na amsu aiki ne, sai na dawo”

A karon farko Momy ta kasa ce masa Allah ya tsare balle har tai masa rakiya. Bayan Daddy ya fice Talba ya risina gabanta ya nuna mata Leila.

“Sunan wannan Leila kanwata ce, kuma matar da zan aura, akwai wata Amal tana makaranta, wacan kuma Momy mahaifiyarmu, muna da masu aiki biyu Mairo da Zulai idan kina bukatar wani abu ki fada musu za su miki. Wannan kuma Kabir, shine likitan da zai rika dubaki shi ma kuma kanena ne”

Talba na ajewa Kabir ya tari numfashinsa.

“No no no Malam shekara biyu ka bani ba, sai wani ji kake da kanka wai kanenka kar ta dauka da gaske”

Talba be ce komai ba, daman ba komai yake saka shi dariya ko magana ba, sai ya kalli Momy.

“Momy ina son zamu yi magana”

Momy ta dauke kai daga kallon Aminatu ta kalli Talba tana jin wani irin zafi a zuciyarta.

“Har a bada dan wani br taba zama nawa ba, nawa kuma be taba zama dan kowa ba”

Kusan wannan ne karo na biyu da wata kalmar ta fito daga bakin Momy da bata masa dadi ba, bayan wacan karo da shigarwa Leila.

“Momy yarinyar nan marainiya ce, ba uwa ba uba, kuma ban daukota na kawo ta nan ba sai dan nasan zamu iya kula da ita, kuma kin san muhimmanci rikon maraya, and ko dan ni ya kamata ki daga mata kafa...”

“Saboda gaka Ubana? Ko kuma saboda mu muka fi kowa son lada? Waya sani ko karya ta tsara maka? Idan ma da gaske ne mu muka kashe iyayenta ne da responsible din ta zai dawo kanmu?”

Da mugun mamaki Talba yake kallonta jin irin kalaman dake fitowa daga bakinta, sai dai be ce mata komai ya kalli Aminatu ya dauke kai ya kalli Kabir da yanayinsa ke nuna be jidadin kalaman Momy ba.

“Kabir kira Mairo”

Momy ta ja tsaki ta nufi upstairs ta bar Leila tsaye tana kallon ikon Allah.

“Mairo...”

Kabir ya kwala mata kira, ya san daga muryar ne ba zai iya ba shiyasa ya saka shi kiranta ba wai dan yana nufin ya tafi yaje ya kirata ba. Da gudu Mairon ta fito daga kitchen hannunta da kumfa.

“Gani ranka ya dade”

“A wanke mata baki, a bata abun karyawa, sannan a gyara mata dakin kasa, ki taimaka mata tai wanka sai dai kafarta na ciwo sai kin yi a hankali”

“To ranka ya dade”

Ta amsa da sauri, shi kuma ya juya ya fice daga falon ya bar Aminatu sai Kabir da Leila.

“Let me help you with brush and toothpaste”

Kabir ya fada sannan ya juya ya nufi upstairs. Leila ta bishi da kallo sai da ya haye gaba daya sannan ta kalli Mairo tana yamutsa fuska.

“Idan kika mata wanka, sai Momy ta ci ubanki”

Mairo ta kalleta da duba na rashin jindadi.

“Haba Leila kina ganina kin san na yi kanwa ta uku da ke, be kamata ki ce min haka ba, ko da kuwa kin san Hajiya zata yi fada ne, amman be dace ki zage ni ba”

“Okay miya dace na fada miki? Ki zo aiki gidanmu sannan ki yi tunanin zan girmamaki? Koya min magana zaki yi ko mai”

Yanayin yadda Leila ta rufe Mairo da masifa ne ya saka jikin Aminatu rawa, sai ta fashe da kuka.

“Mtssss munafuskar banza”

Leila ta fada tana hararar Aminatu, sannan ta nufi kofar baya ta falon tana danna waya.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

BATURIYA POV.

Sai da Ramlee ta shiga da ita har cikin falon sannan ta fita ta barta. Baturiya ta dade a falon sannan ta ji tsayarwar Mota harabar gidan, sai ta leka ta window ta hangoshi ya fito daga motar rike da wata karamar jaka, dayan hannunsa kuma rike da Makalle da waya a kunne. Babban mutum ne a haife ya haife ta kuma ya haifi yayunta, irin mazan nan ne da ake kira da sugar daddy.
Wani irin faduwa ta ji gabanta yayi, sai hakan be hanata daidaita natsuwarta, Ta gyara zamanta sannan ta kunna wayarta ta saka ta silent, gabanta ya tsanata bugawa ne a lokacin daya turo kofar falon ya shigo, abun ka da wanda be saba ba sai ta mike tsaye tana kallonsa, shi kuma ya kare mata kallon tun daga sama har kasa sannan yai mata alama data zauna, sai ta koma ta zauna tana kirkiro murmushi, a kujera dake kusa da kofar ya aje jakar hannunsa sannan ya karasa kusa da ita yana murmushi ya zauna. Ita ma murmushin ta sakar masa, sai ya kai hannu ya shafa fuskarta ya nuna mata fuskarsa alamar tai masa kiss, ba

musu ta mika bakinta ta sumbanci gafen fuskarsa sai ya rumgumeta yana shafa bayanta.

“Yanzu dai Hajiya ki bari idan na dawo gida hankali kwance sai mu yi maganar, kisan Muhammad baya jin maganar kowa a yanzu so dole lallabashi za ku yi, idan yaji yana son ta ya amince daman abun da muke nema ne tun da yar'uwarsa ce, idan kuma yace sai wacan sai mu masa addu'a”

Ya fada yana gangarowa da hannunsa ya cire mata zip din atamfar ya fara murza fatarta ta baya dake cike da taushi da fari.

“Yanzu muna da meeting, idan mun gama kuma zan je na ga gwana saboda maganar kudin kwangilar nan, ba zan dawo da wuri ba sai dare”

Baturiya ta yi shiru tana sauraren yadda hannunsa ke ta yawo a jikinta, Sai wani abu take ji na rashin jindadi, ta saba mu'amala da Faruq balle tace ko dan bata saba bane, wata kila kuma saboda wannan sabo ne tsabanin wacan da take samu lada.

“Eh ya same ni da maganar ai, shiyasa muka taho tare sai kuma na buge wani mai acha, sun tafi da shi su kai shi asibiti, idan ya dawo nace ya same ni a gida mu yi maganar, so zamu zauna gani ga ki gashi sai mu yi maganar, sai anjima”

Ya kashe wayar gaba daya yana kallon Baturiya.

“Yan mata ya kike?”

“Lafiya kalau ya aikin?”

Ta amsa cikin rashin sakewa, shi kam sai murmushi yake abun nema ya samu.

“Alhamdulillah”

Ya fada yana kokarin cire mata dankwalin kanta gaba daya, ya fara shafa gashin kanta, sannan ya kamo hannunta ya saka a kirjinsa.

“Ba za a taya ni cire tufafin ba agajiye nake fa”

Sai da ta hade yawun bakinta sannan ta rika babbar rigarsa ta cire masa, da haka wasan ya canja salo, sai dai duk inda ya taba a jikinta sai ta ji wani iri musamman ma daya raba ta da rigar jikinta yana shafa kirjinta.

“Taso mu watsa ruwa yadda zamu jidadin bachi”

Ta dan yi murmushi ta mike tsaye, sai ya rika hannunta suka bathroom dinsa, a tare sukai wankan, yana ta labarta mata karamar haukar data same shi a lokacin da Ramlee take nuja masa honta a wayarta. Bayan sun gama suka fito sai kallon tsiraicin yake yana yabawa, tare da kai hannu ya taba inda yake jin ya masa. Kusan duk abun da Ramlee ta karantar da ita sai da ta aikata masa har abun da bata taba yi ma Faruq ba da sunan ya samu gamsuwa sai da tai ma Alhaji Haroon, sannan ta biyewa son zuciyarta ta budewa kanta babban file daga cikin manyan manyan files din zunubai. Ba shi ba ita kanta kanta ta samu gamsu irin wanda bata taba samu ba, sakamakon kayan matan da Ramlee ta bata ta sha, balle kuma shi da yai kamar zai haukace.

Nan da nan bachi yai gaba da shi, ita kuma ta tashi zaune ta daura tawul ta fito falo inda ta bar wayarta ta dauka tana dubawa sai ta samu miss calls biyu daga Fahat, jiki na rawa ta mayar masa da kiran daman can yana cikin ranta tun da ta shigo gidan take jiran kiransa. Ringing daya yai picking

“Na yi fushi yau duk ban ji muryarki ba kuma na kira wayarki na ji ta a kashe, na sake kira baki daga ba”

“Bana kusa da wayar ne, kasan idan ina kusa da wayar babu abun da zai hana ni dagawa, ni ma ai tun dazun nake ta jiran kiranka”

“Miyasa baki kira ni ba? Anyway yanzu dai bari na miki wani albishir na yi magana da Daddy, na fada masa cewar na samu mata”

Hannu ta saka ta dafe kirjinta, farinciki da faduwar gaba suka zo mata a lokaci daya.

“Da gaske? Amman me ya ce maka?”

“Me zai ce min kuwa, daman ai sun dade suna jiran ranar da zan fada musu na samu wanda nake so, even though akwai yan'uwa da ake son hada ni da su, amman ni bana son auren zumunci gaskiya”

“Allah yasa ya amince dai”

“Zai amince ma, fatar ba zan samu matsala daga bangarenki ba”

“Aa babu wata matsala Inshallahu”

“Haka nake son ji, ya kike?”

“Lafiya kalau, kai fa?”

“Ni ma kalau nake”

Sama sama take amsa masa duk wata magana da yake mata saboda bata son Alhaji Haroon ya ji tana waya da wani, ko da be nuna mata baya so ba ta san be dace tan a guest house dinta tai haka ba, domin maza suna da kishi no matter how old and young they are.
Bayan sun yi sallama ta kashe wayar ta koma cikin dakin ta hau gadon ta kwanta, ba jimawa bachi yai gaba da ita. Sai da aka yi sallah azabar suka farka kowanensu ya gabatar da wanka sannan suka yi sallah.

“Baby Fee'at me zaki ci na aika yarona ya siyo mana?”

“Shimkafa jalof”

“An gama gimbiyar mata”

Ya fada har wani kashe ido yake, ita kuma tai murmushi, tana sauraren wayar daya dauka ya kira yaronsa fada masa abun da suke bukata. Yana aje wayar ya mika mata hannunsa.

“Ta so zo nan”

Babu kunya balle tsoron Allah haka ta sake zuwa ta biye masa suka sake tarawa kansu wani babban zunubin, suna gamawa yaronsa ya kira wayarsa ya fada masa ya siyo.

“Ka aje a falo”

Ya fada masa sannan ya aje wayar ya tashi ya fita, ko da ya fito yaron ya aje abinci yayi ficewarsa, daukowa kawai yai ya shigo da shi ciki.
Jalof kawai ta bukata amman ya hado mata da farfesun kayan ciki da naman kai, ga kuma lemu mai sanyi da soyayyen naman kaza, zaunawa tai ta ci ta koshi nas, sannan ta tashi tana jindadi, rabon da ta ci abincin hotel har ta manta.
Bandaki ta shiga ta sake yin wanka ta fito, sai ya kalleta da mamaki.

“Wanka kika yi? Ai bamu gama ba, ni fa wuni ake min ba zaki koma gida ba sai dare, Ramlee bata fada miki ba”

“Aa bata fada min ba, amman tun kai ka fada min ai ya wadatar”

Murmushi yai ya bude nasa abinci ya fara ci yana yaba yadda ya sake me, da kuma irin gamsuwar daya samuna jikinta, ba karamin dadi ta ji ba domin Faruq ba mutum ne mai yaba mata ba idan ma ta gyara masa shimfidar, baya daga cikin mazan nan dake nuna jindadinsu a gurin matansu, ba dan komai ba sai dai be dauki yabon a bakin komai ba.

Kamar yadda ya bukata haka ta biyewa sharholiyarsa suka wuni suna raya sabo, sai bayan sallah Magariba ya rabu da ita tai wanka ta shirya cikin tufafinta, tana kokarin daura dankwalinta ta dauko jakarsa ya bude ya kirga dubu dari hudu ya aje mata.

“Ga wannan, sai kuma yaushe?”

Juyowa tai ta kalli kudin, a take gabanta yai mugun faduwa, sai dai bata yarda ta nuna matsa yawan kudin sun tsoratata ba sai tai murmushi.

“Sai kuma ranar daka tashi Alhajina”

“Ni kullum ai ban ki mun hadu ba, idan son samu ne ma tafiyar nan da zan yi China naje dake, kin taba zuwa china?”

“Aa Wallahi”

“To ki shirya dake zamu je”

Ta yi murmushi tana jin wani kalar dadi ya sakota gaba, duk kuwa da bata da tabbacin zata amince ta bishi din ko kuma aa, saboda aure da kuma Fahat. Wayarsa ya mika mata..

“Saka min number ki a nan, ya kamata ace muna da number juna, ba dole sai mun biyo ta bangaren Ramlee ba”

Ta karbi wayar ta saka masa number, sannan ta dauki kudin ta saka a jakarta ta fito falo ta dauki wayarta ta saka mayafinta tai masa sallama ta fice tana

mamakin yawan kudin daya bata, wannan karom bata yi shakkar saka gyaren ba saboda dare ne kuma a yanzu bata da kwaliya kamar dazun.

FARUQ POV.

Sai da ya fara biyawa gurin Mama ya gaisheta suka dan taba hira sannan ya kama hanyar zuwa shagonsa. Ba su karasa ba wani mai mota ya bugu babur din da yake kai, shi da mai achaban suka fadi gefen titi. A take mutane suka yo kansu da gudu mutumen daya buge su ma faka motarsa yai gefe ya fito yana dubasu. Kana ganinsa ka san babban mutum ne, domin shaddar jikinsa ma kadai abun kallo ce balle kuma bakar motar data buge su, a tare da shi a akwai direba sai kuma wata jar mota dake bayan tasa da alama take masa baya take ko kuma a tare suke. Daga mai achaban har Faruq daya ji ciwo a kafa zaune sukai mutane na musu sannu.

“Akwai asibiti nan kusa?”

Mutumen ya fada yana kallon direbansa, sai saurayin dake tsaye kusa da shi ya amsa masa.

“No Abba ba kace kana uzuri ba, ka tafi kawai ni ni zan kai su”

“Okay Muhammad idan an dubasu ka samu abun aka basu, idan mun hadu gida anjima zamu yi magana, yanzu jirana ake”

“Okay”

Dan nasa ya amsa sannan ya rika Faruq da yafi jin ciwo ya mikar da shi tsaye.

“Muje ga motana can”

Ya nuna masa jar motar da take bayan ta mahaifinsa, kamin su karasa gurin motar har mahaifinsa ya shiga tashi motar direban yaja motar sun kama hanya. A front seat ya zaunar da Faruq sannan ya bude back seat din ya ce da mai achaban ya shiga.

“Aa kaje ka kai shi, ni ban ji ciwo ba”

“Ka tabbata?”

“Inshallah”

Sai ya rufe motar ya rufe inda Faruq yake zaune, ya zagaya mazaunin direba ya kirga dubu biyar ya mikawa mai achaban, sai ya karba yana godiya daman haka tafi masa dadi. Ya hau achabansa ya kama hanya shi kuma ya shiga motar yaja Faruq suka isa asibiti.

“Sannu ko kana da asibitin da kake zuwa?”

“Aa”

“Okay bari muje ta nan kusa, ai zaka iya jurewa ko?”

“Haba sai kace ba namiji ba”

Faruq ya fada yana murmushi, shi ma murmushin yai ya cigaba da tukin har suka isa asibitin, aka duba kafar aka bashi magani suka rufe ciwon. Sannan ya sake daukoshi a motarsa suka suka nufo unguwarsu, suna tafe suka hira kamar daman can sun saba, be yarda ya bar Faruq a bakin titin ba duk kuwa da kasancewar mota bata shiga har kofar gidansu, sai ya fito ya taka masa har kofar gidan yana masa wasa wai kar madan tace sun buge mata miji, Faruq murmushi kawai yai ya kai hannu ya taba gidan sai ya ji shi a rufe, key dinsa ya dauko ya bude ya shiga ciki.

“Ina jin bata nan, daman tace min tana da biki zata je”

Fada a kokarinsa na kare matarsa duk da kasancewar mutumen be san Rafi'a balle har ya munana mata zato.

“To a gaishe ta, kuma a bata hakuri ga kuma wannan ayi cefane”

Ya fada yana mikawa Faruq dubu goma.

“Aa haba ai abu ne da Allah ya kawo...”

Kamin Faruq ya karasa Mutumen ya saka rantsuwa.

“Wallahi sai ka karba, kai shedan kadai ke maida kyauta”

Murmushi Faruq yai a karo na barkatai ya karbi kudin yana masa godiya.

“Na manta ban tambayi sunanka ba”

“Faruq”

“Ni kuma Muhammad Fahat na gode sosai Allah ya tsare gaba”

“Ameen”

Daga haka Faruq ya karaso cikin gidan shi kuma ya juya ya kama hanyarsa. A falo Faruq ya zauna yana kiran Baturiya a waya domin jin inda take, sai dai bata dauka ba daga baya ma sai yaji wayar a kashe, hakan kuma ba karamin bata masa rai yai ba, ba yau ta saba fita ba tare da izininsa ba sai dai ya fi jin zafin fitarta fiye da koyaushe. Cikin karfin hali ya shiga uwar daka ya tube tufafin jikinsa yai wanka ya canja wasu kayan sannan ya kwanta, nan da nan bachi yai gaba da shi. Kiran Allah azahar ne ya tashe shi, ya tashi yai alwala ya fita masallaci a can ya hadu da dansa da yabi yaran makotansu suka tafi masallacin a tare. Kusan kowa da ya gaisa da shi sai ya masa sannu da fatar Allah ya tsare gaba, shi kuma ya amsa da Ameen bayan ya labarta musu abun da ya faru.

Sultan na ganin mahaifinsa ya rike shi suka dawo gida tare. Abun ka yaro yana shigowa ya fara tambayar Faruq ina mamansa.

“Dady Momy bata dawo ba?”

“Ina ta tafi?”

“Bata fada min ba, amman na ji tana ta waya da yawa tana ta waya har ta ce ummouy”

Ya nuna yadda tai kiss din da bakinsa. Faruq ya hade yawu yana jin wani bakinciki na taso masa. Haka ya wuni a gidan

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

AMINATU POV.

Daga jiya zuwa yau da aka canja mata daki sai ta ci kadaicin ya karu, domin a can tana jin hayaniyar mutune a wannan dakin komai babu kowa sai ita kadai, sai duk ta ji tana kewar gidansu da rayuwarta ta baya.
Bata san dalilin daya saka aka canja mata daki ba, bata san ranar da wani zai zo nemanta ba, bata san ranar da rayuwarta zata koma daidai ba, har yanzu ji take kamar komai mafarki ne.
Tana fara tunanin ta ji wani irin tsoro ya taso mata, sai ta ji wani abu yana mata yawo a cikin kai karar bindigogi ya dawo mata hayaniyar mutane da rokon da Baba yake musu ya dawo mata kamar lokacin yake faruwa. Wani irin abu ta rika ji kamar kanta ba zai iya dauka ba, gashi tana son ta yunkura ta sauka saman gadon amman dama domin kafafuwanta basa iya komai a yanzu, bakinta ma ya dantse gam duk yadda ta so tai ihu ko kuka sai ta kasa. Ji tai bata bukatar komai a lokacin sai tafiyar da babu dawowa. Da wani irin karfi ta tashi zaune ta fisgi robar ruwan dake hannunta wanda hakan ya bawa jini hanyar fita ya fara zuba, jiki na rawa ta fisgo robar da karfin da bata taba sanin tana da shi ba sai karfen

ya fado gefen gadon, bata tsaya komai ba ta hada robar a wuyanta tana kokarin aika kanta da kanta inda take ganin kamar idan ta tafi ta huta da komai.
Wannan karon ta samu sukunin bude baki, sai dai ko kadan hakan be bawa muryarta damar fita ba, hawaye kawai take babu kakautawa tana ta yaki da numfashinta, kamar an zare mata lakka haka ta ji wani abu ya sauko mata wanda ya zare duk wani sauran kuzari dake jikinta. Tun tana kallon kofa tana numfashi a hankali har numfashin nata ya fara nisa ta komai ya fara mata dishe dishe alamar ta fara ban kwana da duniya, ga jinin hannunta sai zuba yake.

TALBA POV.

As usual every weekend a falon Momy ko Daddy ake karyawa tare da kowa ciki har da Daddy da matarsa, sai dai mafi akasiri an fi cin abincin safe a bangaren Momy, Daddy zai zo bangarenta aci tare da shi, idan an gama ko kamin a fara duk wani mai wata bukata zai gabatar masa.
Sai dai wannan karon a bangaren Daddy Momy ta saka masu aikinta su kai komai wanda hakan ke nuna cewar a bangarensa za a karya.
Duk abun da ake Talba na zaune dinning yana lasa wayarsa, be dago ba har sai da ya ji saukowa Momy, sannan ya dago ya kalleta.

“Momy ina kwana?”

“Lafiya kalau an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah”

Ya amsa yana tashi tsaye sai da ya bar dinning din ta kira shi.

“Talba”

Juyowa yai ba tare daya amsa ba.

“Ka yi hakuri da abun da ya faru jiya, raina ne ya bace”

“Babu komai Momy, ke ai uwata ce Wallahi ban rike ki da komai a rai ba”

Wannan maganar da yai sai ya saka Momy ta dan ji nauyinsa, kasa hada ido tai da shi har ya juya ya fice daga falon. Kai tsaye bangaren Daddy ya nufa a bude ya samu kofar shiga falon, hakan yasa be yi sallama ba kamar yadda ya saba ya nufi gurin da suke karyawa.
Leila kadai ya samu zaune a dinning din ta saka plantain a gaba tana ci, tana sanye da wani jan yadi kanta sanye da bakar hula, fuskarta ta ji hoda sosai sai dan janbakin data shafa, ta yi kyau sosai abu ne mai wahala mace ma tai mata kallo daya ta dauke ido balle kuma namiji. Talba yaja kujerar dake facing dinta ya zauna yana kallonta, shi kansa ya san ta yi kyau, sai dai ba al'adarsa bace fadawa mutum cewar yayi kyau ko yana da kyau, musamman mace, no matter yadda take da kyau ba zai taba iya bude baki ya furta cewar ta yi kyau ba, kuma ba zai zake da yawa gurin kallo ba gudun kar a ankara da shi.
Dauke idonsa yai bayan ya zauna, sai a lokacin ya tuna cewar yau be tura mata sakon barka da safiya ba, kuma ba zai iya tura mata a yanzu ba gudun kar tace saboda ta yi kyau ne.
Gaba daya ya tattara hankalinsa ya maida gurin wayarsa, sai yai kamar be san da zaman Leila a gurin ba, ita kam daman gaisuwa ba halinta ba ne bata saba

gaishe da mutane ba bayan Momy da Daddy, balle kuma shi duk kuwa da irin sanin da tai na son a girmama da yake, sai dai ta kasa dauke idonta daga barin kallonsa duk kuwa da irin bugawar da zuciyarsa take after every blink. Har ga Allah bata iya fadar irin son da take yi ma Talba, da ace ta dauki biro da zayyano irin kaunar da take masa da alkalumman rubutu da takardun duniya sun kare bata gama rubuta irin kaunar da take masa ba. Sai dai har yanzu ta rasa gane manufarta a kanta, miyasa ba zai dauki rayuwa da sauki ba? Ya sauko da kai su yi soyayya kamar sauran masoya? Har yaushe zata yi ta jiran ya canja rayuwarsa? Anya ma zai canja din? Bata raba dayan biyu ba ta ji yana amsa waya, bata iya fadar cewar kiransa akai ba ko kuma shi ya kira domin wayarsa a silent take.

“Yeah ni ma na kwana da yarinyar nan a raina”

Furucinsa ne yasa ta kara tattara hankalinta tana saurarensa.

“Okay”

Shine last abun da ya fada sannan ya sauke wayar, ya daga kansa yana kallo Amal data nufo inda suke sanye da riga da wando yan patistan.

“Good morning Ya Talba”

“Morning Little Sis”

Ya amsa yana aikawa PA sa sakon kar ta kwana.

‘Ka yi magana da wannan number zai fada maka ko nawa yake bukata sai ka tura masa’

Aje wayar yai bayan ya aika sakon. Leila bata fahimci komai a wayar ba, sai dai ta fahimci da Ali yake magana domin yanayin yadda ya amsa wayar ya tabbatar mata da hakan. Sai da kalmar da ita na kauna a raina ya fi tsaya mata a rai.

“Wace yarinya ce?”

Ta tambayi kanta tana kallonsa, a take ta ji zuciyarta ta buga da mugun karfi, har sai da numfashinta yai sama, da sauri ta dauki cup din dake saman teburin ta zuba ruwan sanyi ta sha, sannan ta mike tsaye ta fice daga gurin zuwa karamin falon Daddy.
Zaunawa tai tana haki, ji take kamar taje ta tambaye shi wace yarinya ce sai dai ba wannan damar domin ba ya hira da ita, da ma dai Amal ce ita kam har sirri yake da ita.

“Wace yarinya ce Talba zai kwana da ita a ransa? Ban gane ya kwana da ita a ransa ba, as how?”

Wannan karon a fili tai tambayar tana hade yawun bakinta, sai kuma ta mike tsaye.

“Ko dai yayi ne dan na ji haushi? Amman kuma be taba min haka ba”

Ta dafa kanta tana jin kirjinta kamar zai rabe biyu, ita kamta da akai musu baiko bata tana jin yace ya kwana da ita a rai ba sai wata? Wacece ma? Ba kasafai

yake saka mutane a rai ba balle har ya kwana da su amman yace da yarinyar na kwana a raina.
Haka ta sake sake a ranta, wani irin zafi ta ji zuciyarta na mata, irin zafin da bata tana jin irinsa ba, wata kila sabida bata tana jin Talba yana maganar wata mace a gabanta ba, hasali ma ba zata ce ga wata mace da yake so ko take burge shi ba, ko akwai be tana nunawa ba balle har ya fada.

“What if wani abun bacin rai tai masa?”

Ta sake tambayar kanta tana cire hular kanta, sam bata taba sanin wani abu wai shi kishi ba sai yanzu, domin Talba be taba yin maganar wata mace a kusa da ita ba, shiyasa kullum hankalinta a kwance yake bata da haufin komai, sai dai a yanzu tana jinta a cikin wani irin yanayi marar misaltuwa saboda ya furta ya kwana da wata a ransa.

“Ko dai bata masa rai tai, ai be kamata ya kwana da ita a ransa ba, Indai har macece ko yaya ne be kamata Talba ya kwana da ita a ransa ba”

Ta fada tana wasa da wayar hannunta, can kuma ta busar da iskar bakinta ta shiga contact dinta ta nemi number Ali ta kira shi. Kara wayar tai a kunne ta fara safa da marwa, kamin yai picking har ta matsu.

“Hello Leila”

“Ali ya weekend?”

“Alhamdulillah”

“Am akan maganar da kuke da Talba ne yanzu”

“Okay...”

Yayi shiru yana jiran yaji abun da zata ce, sai ta rasa ta inda zata fara ta san duk irin wayon da zata yi ba zai taba fada mata sirrinsa da Talba ba, sai dai idan ba sirri ba ne.

“Ban fahimci abun da kuke magana akai ba, kuma na ga kamar ransa a bace”

“Leila”

“Na'am”

“You should feel free to ask when ever kika ga Talba a damuwa ko matsala, shi ne fa mijin da zaki aura a tare zaku gina rayuwa idan kuna irin wannan zaman rayuwarku ba zata taba yin dadi ba”

“Na sani, amman ka san halin abunka, zan iya tambayarsa ya ki fada min ni kuma na damu ne kawai”

“Ki saka a rayuwarki ba ki da wanda yafi Talba, idan har kin damu da damuwarsa ya kamata ki tambaye shi”

“Zan yi haka, amman for now ina jin akan wata yarinya ce da na nuna masa jiya tana bukatar taimako, yar gudun hijira ce”

Shiru tai kamar mai tunani.

“Subhanallahi, tana ina yanzu?”

“Asibitin mu”

“Okay Allah ya bata lafiya, amman idan ana bukatar taimako Ali kai na gida ne, ka san yadda komai a Foundation din mu yake, ba sai ka sake yi masa magana ba, domin ba zan taba lamunta Talba ya kwana da tausayin wata a ransa ba, an yi na farko kuma na karshe, bana son ya kwana da kowa a cikin ransa sai ni”

“Ameen”

Ya amsa addu'ar da tai a farko yana murmushi, sannan ya aje wayar ba tare da ya sake ce mata komai ba domin ya san kishi ne.
Sai ta sauke ajiyar zuciya tana dan jin sauki a ranta.

“Ranki ya dade, Hajiya ta ce a kira ki”

Ta juyo da sauri ta kalli Mairo, sai kuma ta rufe da masifa domin ba karamin razana ta tai ba.

“Wai miyasa komai ba ku iya yinsa a cikin natsuwa ne? Mi yake damunku ne? Wannan ya zama na karshe da zaki sake kira sunana da karfi I'm not your mate”

Ta karasa tana jan tsaki sannan ta nufi hanyar shiga babban falon, bata ko tsaya kula Mairo b dake aikin bata hakuri. Ko da ta isa dinning din kowa ya hallara har sun fara cin abinci.

“Ina kika je?”

Momy ta tambaya tana kallonta.

“Waya na amsa”

Ta fada sannan taja kujera ta zauna tana mikawa Daddy gaisuwa. Sai da suka nisa da cin abincin sannan Daddy yai gyaran murya ya ce.

“Ina son na yi wata magana mai muhimmanci, Shiyasa na bukaci a shirya mana abun karyawa a nan, musamman mahaifiyarku”

Jin hakan tasa kowa ya kalleshi har Momy.

“Allah yasa ba laifi na yi ba”

“Laifi kika yi kuma babba, laifin da ban saka ran zaki yi ba a matsayinki na uwa, sam ban tsammaci haka daga gareki ba, ban yi zaton rana zata zo da zaki dubi dana ki fada masa cewar ba ke kika haife shi ba...”

Talba ya tsaya da cin abinci ya dago ya kalli Daddy dake maganar cikin tsananin bacin rai, Momy kuma tana kallon Talba a tunaninta shi ya fadawa Daddy abun da ya faru.

“Again?”

Momy ta tambaya tana cigana da kallon Talba rai a bace.

“Ba shi ya fada min ba wacan karon ma ba shi ya fada min ba...”

Kamin Daddy ya karasa Amal ya karba tana kallon Kabir.

“Ni na fadawa Daddy, ni kuma Ya Kabir ne ya fada min”

Momy ta kalli Amal kamin ta kalli Kabir.

“Na ji na yi laifi amman Amal bata fada maka danka yana wuce gona da iri ba?”

Da wani irin karfi da fusata Daddy ya daki teburin cin abinci.

“Da na be yi komai ba Amina... Wannan dalilin ne yasa na tara ku duka anan, saboda Leila ba zan yarda ki rika batawa Mu'azz rai ba, ko da rana daya bana jin ya taba miki wani abu da zai banban taki da uwar data haife shi, akan me zaki zabi raba kan yarana? Ko bana da rai shi zai yanke hukunci a gidan nan kuma shi zai dauki dawainiyar komai, na tara ku a nan ne saboda na ja miki kunne kuma. Yaranki su daina kokarin wuce guri ko da mafarki ban tsammaci zaki iya furta kalaman da kika furtawa dana ba, saboda abun da Amal ta fada min jiya ban samu bachi da kyau ba, ko kadan bana son abun da zai raba kan yayana kuma bana fatan Allah ya nuna min ranar da Talba zai ji bakincikin rashin uwa”

Yana kawai nan ya mike tsaye a fusace ya nufi dakinsa, kowa shan jinin jikinsa yai har Talba din da Daddy yake masifa saboda shi, domin ya san indai akansa ne tsab Daddy zai iya fushi da shi ko yai masa fada. Amal ma tashi tai da sauri ta bi bayan Daddy, domin ta san sakamakonta gurin Momy.
Momy da hawaye ke sauko mata ta kalli Talba tace.

“Mutum baya kuskure ne? Ni kaina na ji cewar ban kyauta ba, na ji cewar be kamata na furta kalaman nan ba”

Talba yayi saurin girgiza mata kai.

“Haba Momy kamar baki san halin Daddy ba? Yanzu zai hau kuma yanzu zai sauko, be kamata wannan ya dame ki ba, kin mu sanin Daddy fa, muma a tare muka bude ido muka ganku please ki yi hakuri dan Allah”

“Ka yi hakuri kai ma, ban kyauta ba na sani, Allah ya muku albarka”

Ameen. Duk suka amsa har Leila sannan ta mike tsaye ta nufi hanyar bedroom din Daddy, hakan yasa Leila ma ta tashi ta nufi hanyar fita daga part din gaba daya.

“Daddy's Boy?”

Kabir ya fada yana kallon Talba, sai Talba yai murmushi kadan.

“Har yanzu Daddy be yarda na girma ba, yana ganina kamar jariri”

“Maybe sai ka yi aure ka haihu ya ga ka fara bawa yayanka kulawa”

Ya dan tabe baki kadan.

“Ni ma ina son ganin haka, you know i love children alot, but before then ya kamata ka iya bakinka, Amal parrot ce ba komai ake fada mata ba, yanzu kaga abun da taja mana”

“Da gangan na fada mata ai, saboda na san zata tseguntawa Daddy, sincerely speaking Momy bata kyauta ba, she shouldn't say that, we're one family be kamata tai haka ba, rai na be taba baci irin jiya ba”

Cewar Kabir with serious face. Talba ya dauki tea gabansa ya sha kadan.

“You know mata suna da rauni Kabir, kuma tunaninsu gajere ne, shiyasa ba a zure musu kuma ba a kuresu, idan bama dauke kai ga wasu abubuwan zamu yi ta ji da ganin abun da bama so, ya kamata ace muna yafiya da manta kuskure, no body above mistake”

“Yeah wani lokacin kuma muna yin abu saboda ya zame mana darasi so that kar mu sake aikata shi nan gaba”

Murmushi kawai Talba yai be sake cewa komai ba, ya cigaba da cin abinci har sai da ya koshi sannan ya mike tsaye ya dauki wayarsa ya nufi kofar fita yana jin wani irin kaunar Daddy, ji yake yafi kowa sa'a a duniyar domin ba kowa ke samu uba kamar yadda shi ya samu nasa ba, kaunar da Daddy yake masa bata misaltuwa shi kansa ya sani.

Fitowa yai daga bangaren gaba daya ya nufi bangarensa, yadda ya tsaya yana kallon harabar gidan sai rantse da Allah yau ya fara ganin gidan, sai hankalinsa na can wani gurin daban ya dade a tsaye sannan ya karasa entrance din ya murda kofarsa ya bude. Yana shiga yai wanka ya fito ya shirya cikin shadda milk color ya saka hula sannan ya saka wallet dinsa da wayarsa aljihu da ya fito rike da makulli mota ya ja kofar.
Leila na tsaye jikin window dakinta tana kallonsa da murmushi a fuskarta har ya shiga motarsa ya danna horn aka bude masa ya bar gidan.
Sai ya fara biyawa ta shagon da yake siyen sweet da chocolate din da yake zuwa da su gidan marayu sannan ya wuce gidan abokinsa Ali domin a tare suka saba zuwa, wani lokacin Ali zai zo ya dauke shi wani sa'in kuma shi yake zuwa ya dauki Ali kamar dai yau. A bakin gate din gidan ya faka motarsa sannan ya ciro wayarsa ya kira Ali, Ali na yin picking sai ya kashe wayar ya aje. After like 5 minutes Ali ya fito ya bude motar ya shiga, Talba yai reverse sannan suka hau titi.

“Ina yara?”

“Lafiya Kalau Gwauro”

Ali ya amsa masa yana kallonsa fuskarsa da dariya. Talba be sake cewa komai ba har suka kusa isa sannan Ali ya dauko masa zancen Aminatu.

“PA ka ya turo kudi dazun Allah ya saka da alheri”

Nan ma Talba be ce komai ba, har sai da Ali ya dauko masa zancen kiran da Leila tai masa dazun yana murmushi, sannan ya kalleshi.

“Da kai tai waya da safe kenan?”

“Yeah kishi take wai ba zata iya daukar ka kwana da wata a rai ba”

“And...”

Ali ya kalleshi.

“And she's right”

Tabe baki Talba yai be sake cewa komai ba har suka isa gidan marayun, tun kamin ya karasa harabar yaran suka nufoshi a guje suna murna da zuwansa, murmushi ne ya cika fuskarsa farinciki marayu na daga cikin abun da yake faranta ransa, musamman kananan domin Talba mutum ne mai matukar son yara. Da sauri ya bude motar ya shafa kansa yana tambayar lafiyarsu, sannan ya mika hannunsa ya dauko alawar daya siyo musu ya bude ya fara raba musu.

“Uncle ni dai chocolate nake so”

Wata yar karamar yarinya ta fada, sai ya amsa mata in a funny way yana dariya kamar ba shi ba.

“Noooo chocolate dai anjima idan zan tafi”

Ali ya bude dayan side din ya fita yana amsa waya.

“Subhanallahi gani nan zuwa”

Ya fada sannan ya saka wayar aljihu ya zagayo side din da Talba yake zaune a motar.

“Zan barka nan na tafi asibiti”

Wani kallo Talba yai masa wanda ke nuna alama ce ta tambayar lafiya.

“Wai yarinyar nan aka samu ta suma hannunta nata zubar da jini kuma robar karin ruwa murde a wuyanta kamar an shaketa”

Shiru Talba yai fuskarsa da mamaki sannan ya fito cikin motar gaba daya.

“You can go with my car”

“Thank you”

Ali ya fada sannan ya shiga motar da sauri, Talba ya bude baya ya dauko ledar chocolate din sannan ya rufe har lokacin fuskarsa dauke take da mamaki, bin motar yai da kallo har sai da Ali ya fita gate din sannan ya maida dubansa gurin yaran sai dai gaba daya hankalinsa ya tafi akan dalilin da zai saka yarinyar ta aikata haka, he don't even think zata ma iya aikatawa kanta haka sai dai idan wani ne ya kashe ta ko kuma yake kokarin kasheta.
Be wani dade sosai kamar yadda ya saba yi ba domin hankalinsa gaba daya ya tafi gurin yarinyar, and baya son azahar tai masa a nan saboda a tare suke cin abincin rana da duka Family kamar yadda suke yi da safe on every weekend sai

dai idan akwai wani uzuri. After like 2 hours da wucewar Ali ya turawa direbansa sakon inda yake. Sannan ya bude chocolate din ya shiga raba musu yana Murmushi kamar ba shi ba.
Bayan ya gama yai musu bankwana suka rakoshi har gurin da direban ya faka motar, domin ya dade a zaune cikin motar yana jiran Talba. Kamin ya karaso direban ya fito ya bude masa motar bayan ya shiga ya rufe, ya ya zagaya da gudunsa ya shiga driver side ya ja motar suka nufi gida.
Tafiyar minti talatin suka iso unguwar
shimkafi Quarters, Talba na hakimce cikin motar har direban ya faka motar a kusa da entrance din kofar Momy. Kamar ya bude baki ya ce ma direban ba bangaren Momy zai fara shiga ba, sai kuma ya ji ba zai iya ba, sai da direban ya bude masa motar sannan ya fito ya nufi bangarensa.
Yana shiga ya bedroom dinsa ya bude bathroom yai alwala ya fito yana rike da agogon hannunsa, a inda ya saba aje shi ya aje sannan ya nufi inda Capet dinsa ta sallah take shimfide yai ikama ya fara gabatar da sallah nafila. Kamin ya sallame limamin gidansu ya fara kiran sallah hakan yasa yana sallamewa ya fito daga bangarensa ya nufi masallaci gidansu inda dukansu suke sallah da kuma ma'aikatan gidan.
Bayan saukowa daga sallah azahar ya nufi bangaren Momy sai kamshi turare yake kamar wanda ya lullube jarkar turaren a jikinsa. Sai da ya danna door bell din sannan kuma yai knocking sai ga Zulai da gudunta ta bude masa.

“Sannu da zuwa ranka ya dade”

Kai kawai ya daga mata sannan ya nasa kafarsa cikin falon, saman sofa ya zauna yana kallon Plasma dake ta aikinta, babu kowa a falon sai Leila dake zaune a dinning rike da waya, yana shigowa sai duk hankalinta ya tattara ya koma kansa. Be yi minti biyar da zaman ba aka sake danna door bell din, Mairo dake kitchen ta fito da gudu ta nufi kofar ta bude, daman idan ba yan aikin gidan ba ko Kabir sai Amal sune kawai suke iya bude kofa idan ana kwankwasa, Leila tana ganin ta fi karfin haka, Talba kuma jin kai ba zai bar shi ba.

“Baaba na nan?”

“Ban santa ba gaskiya”

Shiru yai yana kallon sabuwar yar aikin domin be taba ganinta ba, duk kuwa ba da yawan zuwa yake gidan ba amman dai akan aikoshi daga kauye gurin Kakarsa Baaba dake aikin gidan, hakan yasa police din dake gadin gidan suka san shi basa hana shi shiga a duk lokacin da ya zo.

“To Hajiya fa?”

Ya sake tambaya, sai Mairo ta amsa masa.

“Eh tana nan wa za a ce mata?”

“Ki ce mata Shamsu ne jikan Baaba”

“Toh”

Ta saki kofar falon dake bude ta nufi hanyar upstairs. Leila a hango shi ta mike tsaye da sauri.

“Ki ce masa Baaba bata nan”

Ta fada kamar wanda ya rikice. Mairo ta juya da sauri da zimmar fada masa, sai Talba ya dakatar da ita ta hanyar daga mata hannu. Mikewa yai tsaye ya nufi kofar Leila na ganin haka ta nufi upstairs da gudu.
Shamsu na ganin Talba ya dan risina masa yana gaishe shi.

“Shamsu”

“Na'am ranka ya dade ya gida?”

“Alhamdulillah, lafiya dai?”

“Lafiya Kalau, daman daga can gida ne suka ce na zo na duba Baaba ko lafiya kwana biyu ba a samun wayarta”

Kamar an dasa ice haka Talba ya tsaya jikin kofar yana kallon Shamsu da mugun mamaki, kwakwalwarsa ta cika da tarin tambayoyi, sai ma ya rasa abun da zai ce wa Shamsu.
Yawun bakinsa ya hade a hankali yana kallon Shamsu har ya bude baki zai yi masa magana sai ya ji muryar Momy dake saukowa tana kiran sunan Shamsu da far'arta, abun da bata saba yi ma talaka ba musamman wanda yake karkashinta.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

“Shamsu ne?”

“Eh Hajiya ina wuni?”

“Lafiya kalau shigo mana”

Talba ya juyo tana kallon Momy dake amsa masa da far'arta kamar ba ita ba. Sai kuma ya juya ya kalli Shamsu dake kokarin shigowa.

“Baaba ka zo nema...?”

Kamin Shamsu ya ce komai Momy ta daka masa tsawa.

“Talba ka barshi ya huta ya sha ruwa mana, Mairo akai shi karamin falo a kawo masa ruwa”

Momy ta karasa tana kallon mai aikinta Mairo, sai Mairo ta amsa a ladance.

“Toh Hajiya”

Ta wuce gab Shamsu ya bi bayanta, Momy ta gyara tsayuwarta tana kallon Talba.

“Bangaren Mahaifinku zaku yi lunch”

Ya gyada mata kai yana bin Shamsu da kallo.

“Zulai ta kai komai a can Engineer kai kawai yake jira”

Ta fada tana juya wayarta a hannunta, yanayin yadda tai maganar yana nuna masa son take ya bar mata falon. Ya san ba zai iya nufar falon ta ce akai Shamsu ba, idan ma yaje ba zata bari yai magana da shi ba, idan kuma ya ce zai musa mata zata yi korafi.
Juyawa yai ya fice daga falon gaba daya zuciyarsa cike da tambayoyi kala kala, a entrance ya tsaya yana kallon harabar gidan, sai kuma ya nufi gate din ya fice daga gidan gaba daya.
Yana fita falon Momy ta rufe kofar da kanta tana sauke ajiyar zuciya. Lumshe ido tai ta bude tana kai hannu ta dafa kirjinta dake mugun bugawa da karfi, sannan ta bar jikin kofar ta nufi karamin falon inda Shamsu yake zaune, yana ganinta sai ya sauka daga kan kujerar ya zauna a kasa abun ka da mutunen kauye akaai girmama mutane.

“Shamsu ya gida ya kowa?”

Ta tambaya bayan ta zauna.

“Lafiya kalau Hajiya”

“Maa Shaa Allah, fatar su Baaba ma suna lafiya?”

“Eh... Ai ita aka ce na zo na duba, kwana biyu an ta kiran wayarta baya shiga”

“Ah ah Subhanallahi, Baaba ai yau kwananta tara ko takwas da tafiya gida”

Shamsu ya kalleta da sauri.

“Gida Hajiya? Wallahi bata je gida ba”

“Subhanallahi Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, lallai tabbas ni ma nayi ta kiran wayarta bayan tafiyarta ban samu ba, amman ban saka ran komai ba saboda na san kauye wani lokacin akwai matsalar network ko nepa, kaga ai shiyasa binciken yake da dadi Allah yasa ba mugun hannu ta fada ba, amman ka bincika aka ce bata je ba?”

“Wallahi bata je ba, ai idan tana can dole zan sani saboda a gidan nake, kuma bata fada miki dalilinta na zuwa ba”

“Eh to gaskiya bata fada min ba, na san dai kamin ta tafi tana dan jin jiki, domin da kaina ma na dauke ta muka je asibiti aka ce zazzabi ne da hawan jini, bayan mun dawo da kwana biyu tace min tana son taje kauye ta ga kowa hankalinta ya koma can a yanzu, ta inda nai kuskure ban tambaye ta me take tunani ba, domin hawan jini baya tasowa haka siddan sai da damuwa ko bakinciki har ma nake cewa ba zata kira ta fada a kauye ba tace bata son ta tashi hankalinsu”

Wani kalar tashin hankali ne ya cika Shamsu, jin cewar Baaba bata gidan ga wayarta ma idan an kira ba a samu, Momy kuma ta fada masa cewar yau kwananta tara da tafiya. A gabansa Momy ta nemo number Baaba ta kira ta saka wayar a speaker, daga ita har Shamsu suka ji cewar wayar a kashe take. Shamsu ya mike tsaye

“Wallahi haka nima suke ce min idan na kira, su ma can haka suka ce wayar a kashe take, amman yanzu zan kira na fada musu halin da ake ciki”

“Gaskiya kam kara a dage da addu'a kuma a saka cigiya, ni ma Inshallah zan bada sanarwa gidan radio ko Allah zai saka a dace”

“Zan tafi Hajiya”

“To Shamsu bari na baka number na duk yadda kake ciki sai ka kirani”

Ta fada tana karanto masa number ya saka sannan ita ma ta mike tsaye.

“Bari na kawo maka wani abu ka hau mota”

Tsaye a falon cikin tashin hankalin kamin Momy ta kawo masa 5k din har ya matsu domin hankalinsa gaba daya ya koma gurin inda yake tunanin Baaba zata iya zuwa. Ya karbi dubu biyar din data bashi yana godiya ya fice da saurinsa kana ganinsa kasan bayan cikin natsuwa. Har bakin kofar babban falon Momy ta raka shi tana ta masa addu'ar Allah yasa a gane ta ya amsa da Ameen sannan ya fice ta maida kofar ta rufe. Sannan ta hau sama da sauri ta nufi dakin Leila, Momy na turo kofar Leila ta zabura ta mike tsaye da sauri tana hawaye jikinta har rawa yake.

“Miye haka? So kike idan ya gani ya fara zargin wani abu”

Leila ta kama hannayen Momy ta rike tana kuka.

“Momy tsoro nake ji”

“Ki daina jin tsoro, babu abun da zai faru, idan kina nuna irin wannan hallayar sai ki tonawa kanki asiri, amman idan kika cire komai a ranki sai ki samu kwanciyar hankali”

“Momy har yanzu ina mafarkinta Wallahi, kuma ina jin kamar asirina zai tonu”

“Idan ma asirin ki ya tonu sai mu zuba miki ido akaiki gidan yare? Ko ayi miki wani hukunci? Noooo babu abun da zai same ki, je ki kwanke fuskarki ki shafa hoda ki same ni a bangaren Daddynku”

Ta gyada kai wasu hawayen na sauko mata.

“Momy akwai CCTV a gidan nan, Talba zai iya bincikawa, kuma idan ya gane zai iya cewa ba zai aure ni ba”

“No kul bakinki ya daina furta wadannan kalaman, Talba ba shi da mata sai ke, ki kwantarta hankalinki zan saka a cire CCTV cameras din, je ki wanke fuskarki”

Ta saki hannayen Momy ta nufi bathroom dinta Momy kuma ta fice daga dakin, tana saukowa ta nufi kofar da zata sadata da part din Daddy.

Kamar zai tashi sama haka Shamsu ya nufi gate yana ciro karamar wayarsa ya ciro karamar wayarsa domin kiran yan'uwansa ya sanar musu halin da ake ciki, police din dake gadin gate din ya bude masa ya fita hankali a tashe. Talba dake tsaye wajen gate din ya kalleshi yana karantar irin tashin hankalin da yake ciki.

“Ka fito”

“Eh ranka ya dade, zan je can gida na fada musu halin da ake ciki”

Talba ya masa kamar ya san abun da yake magana akai.

“Oh ba su sani ba”

“Eh Wallahi shiyasa suka ce na zo na bincika ai, ita ma Hajiya tace tana ta kiran wayar sai ta jita a kashe, Allah yasa dai ba mugun hannu ta fada ba”

“Ameen”

“Yanzu zanje can na fada musu, Hajiya ma tace yau kwananta tara da tace mata zata je ganin gida, ka ga ita bata san bata isa ba, mu kuma ba su san da zuwanta ba”

“Haka ne, Allah ya bayyanata”

Shine abun da Talba ya fada zuciyarsa na bugawa kamar zata fasa kirjinsa ta fito saboda bacin rai, zuciyarsa na ta dawo masa da abun da Ali ya fada masa akan halin da aka samu Aminatu.

Bayan Shamsu ya amsa da Ameen Talba ya kwankwasa karamar kofar gate din suka bude masa, ya doshi cikin gidan, Momy na shiga bangaren Daddy Talba ya danna door bell din, Mairo ta zo da gudunta ta bude masa, kana ganin yanayinsa kasan ransa a bace yake, kai tsaye ya nufi stairs sai dai kamin ya karasa hawa

Leila ta fito fuskarta cike da ruwa ko hodar da Momy ta ce ta shafa bata shafa ba, tana ganin Talba ta hade yawu da karfi ta dauke numfashi na tsawon dakika uku.

“Yanzu zan iya sanin abun da kika yi ma Baaba?”

A karo na biyu ta sake hade yawu da karfi a tana kallonsa kamar wanda bata fahimci abun da yake magana a kai ba. Ya kara matsowa kusa da ita cikin wani irin bacin rai sai ta koma baya da sauri tana kallon kofar da Momy ta fito.

“Lafiya na shiga can ban ganku ba, Daddynku yana jira zamu ci abinci”

“Answer me...!!!”

Talba ya fada a tsawace yana Kallon Leila. Cikin karfin hali tace.

“Ni ban gane abun da kake magana a kai ba”

“Miya faru?”

Momy ta tambaya daga downstairs din da take tsaye. Sai Leila ta amsa mata.

“Tambaya yai wai zan iya sanin abun da ya faru da Baaba”

“What? Me kake kokarin cewa Talba?”

Talba be kula Momy ba ya kara yin sama ya matsa kusa da Leila.

“I hope ba ke kika shakari yarinyar can ba, kike kokarin kasheta, saboda zafin zai zame miki biyu wahalar zata miki yawa...”

Hawaye ne ya fara saukowa Leila.

“Talba wace irin magana ce wannan? Me kake son fada?”

Juyowa yai ya kalli Momy.

“Momy kin san me nake magana a kai, I'm not a fool na fahimci komai, and i do hope Leila bata da hannu a kokarin kashe yarinyar nan...!”

Yana kawai nan ya sauka a fusace ya fice daga falon gaba daya, Momy ta bishi da kallo, Leila kam ban da hawaye babu abun da take.

“Wace yarinya yake magana akai?”

Zubewa Leila tai a gurin ta fashe da kuka.

“Momy....”

Sai kuma ta kasa karasa, Momy ta hau saman da sauri ta rika Leila suka nufi dakinta.

TALBA POV.

bangarensa ya nufa wayarsa makalle a kunnensa yana ta kiran Ali, sai dai har wayar ta gaji da ringing ta katse Ali be daga ba, zaunawa yai saman kujera ya sake kiran wayar, wannan karon ma Ali be daga ba. Hakan yasa ya dauki keys dinsa ya fito ya shiga motarsa ya fito ya ja motar da karfi, suna ganin ya kunna motar suka bude masa gate. Cikin saurin ya fice daga gidan, yana driving zuciyarsa na raya masa Leila zata iya yin yunkurin kashe yarinyar saboda ta tambayi Ali akan ta, wata kila zata iya zargin wani abu ne a tsakaninsu idan ma bata yi da kanta ba zata iya saka wani yai.
Yana isa asibitin ya faka motarsa ya fito ya mufi hanyar da zata sada shi da office din Ali, kamin ya karasa Office din Ali ya fito daga ward din, yayi mamakin ganin Talba sai dai kamin yace komai Talba ya ce.

“Ali ya yarinyar take?”

“Ba dadi, but she's still alive”

Wani deep breath Talba yai sannan ya bude office din suka shiga.

“Ya akai abun ya faru?”

Ali ya rufe kofar yana fadin.

“Nurse Karima dai ta fada min cewar tana shiga dakin ta same ta a sume, robar a zagaye da wuyanta kuma an fisge robar hannunta jini ya zuba, yanzu haka sai da muka saka mata robar jini, daman jinin be isheta ba”

Talba ya zauna saman kujera yana dan tunani kaminnya kalli Ali daya kai hannu ya dauki wayarsa yana dubawa.

“Ali lokacin da Leila take tambayarka akan yarinyar nan ta tambaye inda take?”

“Tace dai wace yarinya ce na fada mata tana asibitin mu”

“Ka fada mata number dakin?”

Alinya dago ya kalleshi.

“No miya faru?”

“Ali Leila can do this yarinyar nan bata da zuciya mai kyau....”

“Noooooooooooooooo”

Ali yayi saurin dakatar da shi yana daga masa hannu, domin maganar ta masa nauyi sosai har sai da ya runtse ido ya bude ya kalleshi.

“Look Talba yanzu na fahimci baka son Leila, and it fine, ka ji baka son mutum normal ne amman kokarin dora mata sheri ba zai amfana maka komai ba”

“Na san dalilin daya saka na fad....”

Talba be kasara Ali ya daka masa tsawa.

“Baka da wani dalili, and karka manta Leila yar'uwarka ce ko da babu alakar kauna a tsakaninku be kamata ka jefe ta da wannan ba”

“Ali ba zaka gane ba ne, Leila can do this”

Talba ya sake maimaitawa with full confidence, abun da ya kara fusata Ali.

“Enough Talba, enough. Leila tana da damar da zata yi kishi, ta nuna bakincikinta ko bacin rai akan ka damu da wata, amman for now ka bar Leila ta ji da damuwarka karka kara mata wata”

Ali ya fada cikin tsawa jijiyar wuyansa har tashi take. Talba ya mike tsaye yana kallon Ali cikin wani irin zafin nama.

“So you're shouting at me...?”

“Yes me ke damunka Talba? Why Leila? What if ita tai kokarin kashe kanta? What if kila ta akan wani abu dabam ake kokarin kasheta?”

Talba ya matsa kusa da shi yana kallon idonsa.

“Don't fool me, haka nan kawai zata yi kokarin kashe kanta saboda bata son kanta? Bayan ta samu ta fito daga daji? And you already told me babu wanda ya taba zuwa ganinta how could someone know tana a nan? Ali Let me tell you this, zan bincike yarinyar nan and if i find out Leila ta aikata abun nan, sai na bata mamaki”

“And before you do this let me show you something, daga yau ba zan sake kula yarinyar nan ba, and i swear sai ta bar asibitin nan yau, ba zan zuba maka ido ka bata alakarka da matar da zaka aura ba kuma yar'uwarka saboda wata bare ba, kuma a dalilina ka san yarinyar nan and now na fahimci halin da Leila take ciki akanka”

Talba yayi murmushi irin murmushin na bacin rai da mamaki a lokaci daya.

“And remember you said yarinyar bata da kowa”

“I don't care, idan ma mutuwa zata yi tai mutu, she's not my responsibility...”

“And for now on she's my responsibility har sai ta dawo hayyacinta ta fada min komai... And believe me with or without you yarinyar nan zata rayu Doctor Aliyu Muhammad Bukar...”

Talba na fadar hakan ya juya ya nufi kofa a mugun fusace, da mugun karfi yake taka kasar kamar zai fasata tsabar bacin rai, rabon da ya samu kansa cikin irin wannan bacin rai har ya manta. Har ya fito daga ward din sai kuma ya juya ya koma ciki, kai tsaye ya nufi gurin da sauran nurses din suke, mostly sun sanshi domin yana yawan zuwa asibitin gurin Ali kuma gashi sanannen mutum kuma dan babban mutum wato Alhaji Mu'azu Shimkafi, sai dai ba zai iya shadar sunansu duka ba musamman a yau da yake weekend ne ba faces din daya sani ba ne a gurin.

“Who's Karima a nan?”

“Ni ce”

Ta amsa tana kallonsa.

“Ali ya ce ki dauko yarinyar ki saka a motana zan canja mata asibiti”

“Okay”

Ta mike tsaye ta kira mutun biyu da za su rika mata ita, a gurin ya tsaya har aka fito da ita suka turota a kujera idonta a rufe. Yana gaba suna Karima na biye da shi wata mai aikin shara da dauko files tana rike da file din Aminatu, suna isa gurin Motar Talba ya bude gidan bayan Nurse din da matar suka rikata suka sakata ciki sannan suka rufe motar. Shi kuma ya karbi file din ya bude side dinsa ya shiga ya aje file din a front seat, hakan kawai ya samu kansa da juyawa ya kalli fuskarta, sai tausayinta ya kara kama shi, abun da Ali ya fada masa akanta ya dawo masa, ga kuma wanda yake tunanin Leila na kokarin kara mata.

“Leila...”

Ya furta bayan a dauke kansa daga barin kallon Aminatu, yana jin tsanar Leila na kokarin dasuwa a ransa. Key yai ma motar yai reverse, ya kama hanyar ficewa daga asibitin.
Wata expensive private hospital ya nufa da ita, yana shiga ya nufi emergency, duk da kasancewar yau weekend ne ya samu ma'aikata da yawa a asibitin saboda private hospital ce da suka san aikinsu, sai dai ba kowa yake iya kai kansa ko wani nasa a can ba, sai ya tsaya da kafafuwansa.
Sun karbi Aminatu da gaggauwa da kuma kulawa suka shiga da ita ciki domin bata taimakon da take bukata.
Shi kuma ya tsaya daga waje ya ciro wayarsa dake aljihunsa tana ringing, ganin number Daddy yasa shi saurin picking.

“Hello Daddy”

“Mu'az kana ina? Mun ci abincin rana ba tare da kai ba?”

Ya daga jikin motarsa yana kallon harabar asibitin.

“Daddy ina asibiti”

Sometimes idan yana gurin Ali a asibitin ya kan cewa Daddy yana asibiti, hakan yasa Daddy yai zaton ko yana tare da Ali ne?

“An bata maka rai ne? Could we talk?”

“No Daddy ina wata magana ne mai muhimmanci, bata shafe ka tsakanina ne da Ali”

“Okay”

Daddy ya fada sannan ya kashe wayar, Talba ya cikawa bakinsa iska ya busar a hankali yana kallon Nurse din data doso inda yake.

“Dan Allah kai ne mijin yarinyar nan? Ko dan'uwanta?”

Tsaye Talba yai kamar an dasa shi ya kasa amsa mata.

“Tana bukatar jini da gaggauwa”

“A ina zamu samu?”

“Lab amman for now za mu bincika mu ga ko za'a samu jinin da zai dace da nata”

Ya gyada mata kai a hankali cike da natsuwa, sannan ya bi bayanta suka nufi cikin ward din, ita ta nuna masa dakin da suka saka Aminatu. Ita ta fara shiga shi kuma ya bi bayanta ya tsaya jikin kofar yana kallon fuskar Aminatu dake ta bachi kana gani kasan bata san inda take ba. Nurse din ta yi abun da zata yi ta fita Talba yana tsaye jikin kofar idonta akan Aminatu, takawa yai a hankali ya karasa kusa da gadonta still ya kasa kauda idonsa akanta.

“You need to survive”

Ya furta yana jin kamar ya tashe ta ya tambaye ta waya mata haka, kuma ayi sa'a ta amsa masa cewar Leila ce. Yana tsaye akanta har na kusan mintuna talati, sai ga nurse din ta dawo tare da likitan daya karbi Aminatu a dazun.
Sake dubawa yai sannan ya kalli Talba.

“Ba mu da kalar jininta a yanzu, sai kaje babbar asibiti ko kuma ka samu wani daga familynta idan zai iya bada jinin”

Uffan Talba be ce ba har sai da Likitan ya nufi kofar fita.

“Ko zaka iya gwada nawa? O ne”

Likitan ya juyo ya kalleshi.

“Yes why not amman zamu fara maka test mu tabbatar baka dauke da kowace irin cuta gudun samun matsala”

Ya daga masa kai kamar an masa dole, sannan ya bi bayan Nurse din dake nuna masa kofa.

“Bismillah Malam”

LEILA POV.

Wani irin kuka take wanda ita kanta ba zata iya fadar dalinlinta na yin kukan a yanzu ba, na zargin da Talba yake mata ne ko kuma na laifin ne da yake kokarin dora mata? Taya zai zarge da da abun da bata san wanzuwarsa ba? Miyasa ma zai yi maganar wata yarinyar a gabanta? Ko kuma dai tana kukan ne saboda zuwan Shamsu? For now she can't tell, all what she know is dukansu is painful, daga zargin har zuwan Shamsu har zancen yarinyar da Talba yake.

“Tun dazun kike ta kukan nan? Haka zaki yi ta yi a gaban mutane ki daure kanki?”

Momy ta fada cike da tausayin yarta.

“Wai wace yarinya ce ma yake magana akai?”

A take ta amsawa Momy hawaye ma sauko matan

“Wata ce, wata yar gudun hijira ce”

“Yar gudun hijira kuma? Shine har zai zarge ki da kashe ta? Ke kin santa ne?”

Ta daga kai tana goge hancinta.

“Na santa amman Wallahi ban ma taba ganinta balle har na yai yunkurin kasheta? Miyasa zai zarge ni?”

“Ke kika bashi fuska ai! Kina ta son bada kofar da za a zarge ki, koma dai miye ai be kamata yai wannan tunanin ba, and ko da kin aikata be kamata ya sameki kai tsaye da maganar ba!”

Momy ta fada a fusace, sannan ta mike tsaye yana wani kashe ido.

“Karki fito cin abinci, saboda Daddynku zai tambaye dalilin danuwarki, so ki zauna a nan zan fada masa kanki yana ciwo”

Leila ta daga kai, sai Momy ta juya ta fice daga dakin tana mamakin yadda Talba yake son sauyawa.
after like 40 minutes da fitar Momy wayar Leila tai ringing, hannu ta kai ta dauka tana duba number Ali dake kiranta, da kamar ba zata daga ba sai kuma ta daga wayar ta kara a kunnenta tai shiru tana sauraren abun da zai fito daga bakinsa.

“Kuka kike yi ko?”

Ta daga masa kai kamar yana gabanta, wasu hawayen na sauko mata. Be damu da yaji abun da zata fada ya sauke ajiyar zuciya daga can cikin wayar.

“I know na san abun da ya faru, can we talk? Gani a hanyar gidanku akwai maganar da nake son fada miki, please ki daure ki fito zan tsaya a gate”

“Okay”

Ta amsa masa tana jin wani sabon kuka na taso mata, sannan ta aje wayar ya lumshe ido, fuskar Baaba ce ta fara mata gizo, hakan yasa tai saurin bude idon ta mike tsaye ta nufi gurin windows din dakinta dafe kai wasu hawaye na sauko mata.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji

Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Madina ta jimmm bayan da Leila ta gama labarta mata abun da ya faru, gaba daya sai ta ji jikinta ya mutu.

“Yanzu dai ki fita ki ji abun da Ali zai fada miki”

“Zan je yanzu”

“Ki kwantar da hankalinki komai zai wuce, amman da zaki dauki shawarata da kin fadawa Talba gaskiyar komai, barin kashi a ciki baya maganin yunwa Leila, kuma yanzu zaki yi ta samun rashim fahimta a tsakaninku ne”

“Madina wannan sirina ne, Momy ma bata san na fada miki ba, amman na fada miki ne saboda na yarda da ke”

“Babu wanda zai taba jin wannan maganar daga gareni Leila, amman ina baki shawara ne akan abun da nake ganin zai zame miki masalaha”

“Yanzu dai bari na tafi Ali yana jirana”

“Okay”

Leila ta aje wayar sannan ta sauka saman gadon ta dauki wani karamin mayafi ta rufe kanta, sannan ta saka talkaminta ta nufi kofar fita idonta a kumbure saboda kukan da ta sha.
Ko da ta sauko falon babu kowa, dukansu suna bangaren Daddy, yan aikin Momy kuma Momy bata basu damar zama a falonta hakan yasa idan ba wani aikin zasu ba abu ne mai wahala ka gansu a main house din kullum suna BQ. A hankali ya bude kofar falon ta fita gabanta na faduwa, domin ji take kamar zata yi arba da Talba ne, domin a yanzu bata son ganin fuskarsa, ba dan bacin rai ba sai dan bata da amsar tambayar da zai mata. Tun kamin ta karasa gurin gate din police din ta bude mata karamar kofar ta fice, tana fitowa ta ga motar Ali fake sai ta nufi inda motar take. Ali na zaune cikin motar yana kallonta har ta karaso gaba daya sai ya ji tausayinta ya kama shi, a da can yana bata laifi kamar yadda yake

bawa abokinsa sai dai a yanzu ya fahimci abokinsa ne mai matsala ba ita ba. Bude motar tai ta shiga sannan ta rufe ta kalleshi da idonta da suka kumbura.

“Ali”

Sai da ya sauke wani dogon numfashi sannan ya amsa mata.

“Na'am Leila, ya kike?”

Tambayar ya take da yai sai ta ji kamar ya tsokano mata kukanta, a take hawaye ya cika idonta.

“Ba Kalau ba Ali, ba Kalau ba”

“Na sani, abokina yayi rashin tunani, amman ban dauka zai miki magana ba, a thought ya bar abun a ransa ne kawai, sai dai faga lokacin dana kira ki na ji yanayinki, sai tausayinki ya kama ni, and now na fahimci irin halin da kike ciki”

Ya karasa yana kai hannu ya ciro tissue ya mika mata, sai ta karba ta share hawayenta.

“Sometimes ina kasa fahimtar waye Talba, abokinka yana da wahalar sha'ani Ali, taya wanda zaka aura zai zarge ka da kisa? How? And Why? Saboda na nuna kishina? Talba be dadin zama wani lokacin”

“Na sani, amman ban dauka abun zai kaishi haka ba”

Cewar Ali yana kallonta gaba daya zuciyarsa ta cika da tausayinta, domin gani yake Talba baya sonta ita ce kawai sonsa ke dawainiya da ita.

“And i respect your decision na cewar ba zaki auri Talba ba har sai ya canja”

Juyowa tai ta kalleshi da kyau.

“Dan Allah zaka fada min abun da ta faru da yarinyar?”

A takaice ya labarta mata komai na yadda aka samu yarinyar, sai dai be fada mata cewar Talba ya dauke ta daga asibitin ba, haka ma be fada mata cewar sun samu tsabani ba, domin yana ganin kamar sirrinsa ne da be kamata kowa ya ji ba.

“Amman me zai saka wani yai mata haka?”

“Ni ma ban sani ba, kuma a iya binciken da na yi wani be shigo ba, so dole dai sai ta farka zata iya fada mana yadda komai ya faru”

“Yanzu tana asibitinku?”

“No na canja mata asibiti, and i am here to apologize saboda ni na janyo komai, Talba be san yarinyar nan ba, ni na hada shi da ita da neman ya taimaka mata saboda yarinyar tana bukatar taimako, amman ban yi tunanin abun zai zama na rigima haka ba”

“Baka da laifi, na san ka yi ne da kyakkyawar niya, be kamata ka bada hakuri ba”

Yayi shiru na wani lokacin kamin ya kalleta ya ce.

“Amman Leila kin yi wani abun ne da zai saka Talba ya zargeki da taba yarinyar nan?”

“Ban yi komai ba, amman kasan a gurin abokinka kullum nice mai laifi, kawai dai na fahimci wani abu... Talba baya so na ni ce kawai na mutu da kaunarsa, wanda yake sonka ba zai maka haka ba, ko da gaske na aikata zai nemi hanyar kare ni ne, ba ya tunkare da wannan laifi mai girma ba, abun akwai ciwo”

Ta karasa wasu hawaye masu zafi na sauko mata, har cikin ranta tana fadawa Ali abunda ta fahimta ne akan zamantakewarta da Talba. Ali ya kawar dai yana jin irin tausayinta na kara kamashi.

“Ada can na dauka miskilancinsa ne ya saka yake min abun da yake min, amman a yanzu na fahimci kauna ta ce babu abunsa, kawai ya amince ne saboda ba zai iya cewa Daddy a a ba”

Ta runtse tana kokarin fashewa da kuka.

“Kabir yana da fada min gaskiya amman na kasa ganewa, saboda kaunar Talba ta cika min zuciya amman yanzu na fahimta...”

Ali yayi saurin daukar ruwan dake cikin motarsa ya mika mata.

“Please sha ruwa”

Sai kuma ya dauko tissue ya mika mata.

“Ki daina damuwa dan Allah, kukan nan yayi yawa idonki har ya kumbura, me yasa zaki damar kanki akan Namiji?”

Sai ta kalleshi hawaye na sauko mata

“Talba be taba min haka ba, na gode”

Ta fada sannan ta karba ya share hawayenta ta bude ruwan ta sha.

“Ki je ki huta, karki saka damuwar komai a ranki komai zai wuce, kin san idan ya fusata yana aikata abubuwa amman zai sauko and ina tabbatar miki zai baki hakuri”

Ta dan yi murmushi irin na bakinciki da kuma kin yarda da maganar Ali cewar zai bata hakuri domin ta san waye Talba, sai dai bata ce masa komai ta bude motar ta fita, Ali ya bita da kallo cike da tausayi har ta shige cikin gidan, sannan ya kai hannu ya dauki wayarsa dake carji a jikin motar ya kira Talba, wayar tai ta ringing har ta gaji ta katse be daga ba ya sake kiransa nan ma shiru, haka ya jera masa kusan 4 miss calls a na biyar ya ji wayar a kashe alamar ya gaji da kiran da yake masa kenan kuma ba zai yi picking ba.

“Talba....”

Ali ya fada yana jin kamar ace yana kusa da shi yai masa dan banzan duka a yau saboda kukan da Leila ta sha akasa.

‘Ina ka kai yarinyar nan?’

Shine sakon daya tura masa sannan yai reverse ya kama hanyar gidansa.

TALBA POV.

Be dawo gidan ba sai dare, domin bayan an gama diban jininsa sai ya fito asibitin ya koma gidan marayun, daman can yakan je idan yana cikin bacin rai ko damuwa ya wuni a can, sai ya ji damuwar tasa ta ragu saboda yara suna rage masa kewa, and ko ba komai zai ji cewar ba shi ne kadai a damuwa ba, su ma sun rasa iyaye da yan'uwa amman sun zaune a inda Allah ya tsara musu rayuwarsu kuma suna farinciki, balle kuma shi da Allah yai ma ni'imar aje su da ciyarda su, bayan tarin lafiya da ni'imar yan'uwa da kuma ta uba kamar Daddy da Allah yai masa.
A can yai sallah magaba a can yai isha'i, be dawo gida ba sai ba tara saura, wunin yau bayan abincin safe be sake saka komai a cikinsa ba sai ruwa. Yana shigowa ya faka motarsa kusa da entrance din Momy sannan ya fito ya nufi kofar falon cikin yanayin da ba zai iya fada ba, kawai misaltawa yake idan har da gaske Momy da Leila suna da hannu a mutuwar Baaba ko batanta ya iyalanta za su ji? Yayanta da jikokinta? And ya ma akai komai ya faru? Idan ma kasheta sukai ina suka kai gawarta. Sau biyu yana danna door bell din sannan Amal ta bude masa kofar.

“Ya Talba welcome”

Ya amsa mata ta kai fuska ba yabo ba fallasa, sannan ya shigo cikin falon, hakan ta nuna alamar baya cikin walwala. karasa yai kusa da Kabir dake zaune a sofa yana cin tuwon samun miyar gayye ya zauna. Kallo daya yai ma tuwon ya dauke kai domin shi ba ma'aboci cin tuwo ba ne, wayarsa dake aljihu ya ciro ya kunna sai ga sakon Ali ya shigo wayarsa.

‘Ubanta ne kai?’

Shine reply din da yai ma Ali sannan ya aje wayar ya busar da iskar bakinsa. Kabir ya kalleshi sannan ya kalli Amal dake zaune tana kallonsu dama haka take idan ta lura da ba a zaune kalau, so that ta samu abun tseguntawa Daddy.

“Amal je ki yi bachi mana”

Kabir ya fada, sai ta make kafada.

“Bana jin bachi yanzu”

A take ya zare mata ido, hakan ke nuna ba da wasa yake ba, ya saba wasa da ita sosai sai dai a duk lokacin da yake serious magana da ita ta san yanayinsa. Mikewa tai tsaye tana kallon Talba.

“Ya sai da safe”

Ta murgudawa Kabir baki sai ya kyalkyale da dariya yai mata gwalo.

“Daddy's noy could we talk?”

Talba ya kalleshi.

“Leila ta fada maka ne?”

“Nooo Amal dai ta shinshino ta shinshina min”

Talba ya dan yi murmushi kadan yana kallon hannunsa.

“Na bada jinina yau”

Kabir ya duba shi duba na mamaki, ba zai ce ya san dukan abun da Talba yake yi ba, amman be taba jin yace zai bada jininsa ga kowa ba.

“Something new...”

Talba yayi murmushi.

“Yeah.... I feel like..... ”

Sai kuma yai shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

“I feel honour.. I mean it was a great joy.... to do....something like this”

A rarrabe yai maganar and he is very excited, he can't tell why amman yana jin yayi abu mai kyau.

“Yeah at least wani zai rayu da jininka, and mutumen nan ba zai taba manta ka idan ya sanka, idan kuma be sanka ba, kai zaka ji cewar wani yana can yana rayuwasa saboda ka taimaka masa da jininsa ko da kuwa siyarwa kai balle kuma ace kyauta ka bada, more especially ace mutumen nan yana cikin yanayi na bukatar jini tsakanin rayuwa da mutuwa...”

Talba yayi shiru yana sauraren kalaman Kabir, sai kuma ya soma tuna abun da ya faru a yau. Juyowa yai ya kalli Kabir.

“Idan mutum ya suma zai dauke ki awa nawa kamin ya dawo hayyacinsa?”

“Is depend on yanayin suman, ko kuma irin kulawar daya samu, but most wadanda tsoro yake saka su suma ko damuwa, ba su cika farkawa da wuri ba kamar wanda rashin lafiya ta saka shi suma, kuma ya danganta da kalar suman da mutum yai”

Shiru Talba yai alamar nazari sannan ya sake tambayar Kabir.

“Amman me ke saka mutum baya kuka da murya sai hawaye, kuma ba ya magana, baya cin abinci baya ma bude bakin”

Kabir ya aje spoon din da yake cin abinci da shi ya dauki ruwa ya sha.

“Depression... Damuwa tana saka wannan har fiye ma, tana saka hauka, rashin lafiya and so on, indai har ba wai mutum ya daman can haka aka haife shi ba, daga baya ne ya sauya gaskiya damuwa ce, tana tsoro tana saka mutum ya rika ganin abu yana imagination ko kuma zuciyarsa ta raya masa ya aikata ko ta saka shi hauka ko ya rika abu kamar mai aljannu, tana saka yawan mantuwa ko surutu ba akan abun da ake magana akai ba, you know komai n jikin dan'adam yana da limit din abun da yake iya dauka, so idan abun yai yawa ko yai kadan zaka tarar akwai irin illar da yake haifarwa”

Silently Talba ya sauke ajiyar zuciya.

“Idan mutum yana son yayi magana da mai irin wannan abu kamar ya tambaye shi wani abu ya zai yi?”

“Ya zai yi kuwa? Most important thing is ka yi kokarin cire wannan mutumen a damuwa, idan wani abu yake so ka sama masa, idan tsoron wani abu yake ka nuna masa babu abun da zai same shi kuma zaka bashi kula, ka sake jikim da shi kana bashi kulawa kana nuna masa far'a da walwala kana dauke masa hankali daga damuwar, kai ta kokarin ganin ka faranta masa rai, da haka da haka zaka ga ta saki jiki da kai, ka yi ta cusa kanka kana bata abinci tun bata ci har ta fara ci”

“Idan kuma ya ki fa?”

“Taki dai... Zata ma ci idan ta ji yunwa, idan ana saka mata maganine a ruwa na abinci ko kuma ana bata ta hanci a daina, as long as zata iya tashi zaune ko ta kwanta bata bukatar irin wannan maganin, a kyaleta ta wuni da yunwa idan ta ji babu komai a cikinta zata karbi abincin idan an bata, da haka zata saba ta rika ci, amman a yanzu ai an hanata jin yunwa ne, kuma ace ana son ta ci abinci?”

“But he cant walk fa”

“That one is different, maybe damuwar ce ta haifar mata da hakan ko kuma wani matsalar dabam, amman rashin lafiyarta ba zai zama da matsala a cin abincin ta ba, indai ba wai tana kan wani magani da aka dorata ba ne, shi ma kuma sai dai ace ba zata ci wani ba wani zata ci”

Talba ya yunkura da zimmar tashi sai Kabir ya kalleshi ya ce.

“Ita ce yarinyar?”

Da ido Talba yai masa alamar question mark, sai ya karansa tambayarsa.

“Yarinyar da kake zargin Leila tana kokarin kashewa?”

Talba be ce masa komai ba ya fara tafiya.

“And do you really think Leila zata iya wannan abun?”

Tsayawa Talba yai ya juyo ya kalli Kabir.

“Amal ta baka labarin Baaba?”

“No amman Momy ta fada mana yan'uwanta sun zo sun dauke ta right?”

“Yes amman dazun nan jikanta ya zo nemanta, so kai tunani akai”

A take Kabir ya cika da tsananin mamaki, Talba kuma ya juya ya fice daga falon. Bangarensa ya nufo kamin a karasa ya cire agogon hannunsa, sannan ya kai hannunsa na hagu ya bude kofar ya shiga, tafiya yake kamar baya son taka kasa ya karasa bathroom dinsa ya jefar da wayarsa saman gado, ya cire tufafin jikinsa ya daura tawul. Samun kansa yai da karasawa gaban katon madubin dake dakin wanda ke nuna iya tsayin mutun. Tsaye yai yana kallon kansa kamin ya kai hannu ya shafa kirjinsa zuwa cikinsa sai kuma ya dawo da hannun saitin inda zanen kirjinsa yake yana tabawa.
Motsin shigowar mutum da yaji ne yasa shi juyowa da sauri domin ya san ba kasafai ake shigowa bangarensa ba, Momy ba tai musu wannan tarbiyar ba, ta shiga dakin juna barkaita sai dai idan da wani dalilin. Takawa ya fara yi kamin ya isa bakin kofar Bathroom din Leila ta shigo, tsaye tai cak tana kallonsa daga kasa zuwa sama, wani irin bugawa zuciyarta tai da karfi a lokacin da idanuwanta sukai arba da faffandan kirjinsa. Tun da take a rayuwarta bata taba ganin Talba babu riga ba sai yau, duk kuwa da kasancewar a gida daya suka tashi sai dai baya bayyana mata siraicinsa kamar yadda ita bata taba nuna masa nata ba sai dai dan abun da ba a rasa ba, kamar saka damammen kaya ko wando da riga, sai dai rika hannunsa ko taba shi ba wani abu ba ne a gurinta kamar yadda shi ma be dauke shi komai ba.

“Ya akai?”

Ya tambaya yana kallonta, ba karamin jihadi tai ba na ganin ta daidaita natsuwarta, sai dai hakan be hana numfashinsa yin nisan kiwo ba na tsawon dakiku, ta dauken kai tana kokarin dawo da numfashin a hankali.

“Yarinyar ta fada maka wanda yai mata haka?”

“Kina da wata maganar ne bayan wannan?”

Juyowa tai ta kalleshi.

“Ita wannan maganar ba mai muhimmanci ba ce?”

“Mai muhimmanci ce a lokacin da ta fada min cewar ke ce ko ba ke ba ce, and kuma idan na gane gaskiyar komai a game da Baaba”

“Duka biyun ban aikata ba, miyasa baka yarda da ni ba? And me zai saka ka zarge ni da kisan yarinyar da kai ma basan san ta ba”

“She can't walk she can't talk, depression yana damunta, and now idan na gano da hannunki a ciki, i swear ba zan raga miki ba, you have no idea what she's going through”

Ta kara matsowa kusa da shi tana kallon idonsa.

“I don't care, she can't talk or walk is not my business, ta mutu ko ta rayu be dame ni ba, ina ta fito ina zata je me ya faru da ita duka ba matsala ta ba ce, all what i care is us....we... I mean us... Just us...”

Yanayin yadda tai maganar ya bayyana bacin ran dake tare da ita, shi ma kallonta yake ido cikin ido yana kokarin hana zuciyarsa tsanarta. Sai da ta gama yawo da idanuwanta a fuskarsa sannan ta juya ta fice daga dakin a fusace. Tana dawowa dakinta ta dauki wayarta ta kira Madina ta san is late amman tana son ta yi magana da ita mai muhimmanci.

“Hello Leila”

Madina ta yi picking.

“Madina fada yadda ake mantawa da mutum”

“Ban gane ba”

“So na ke na manta da Talba, na cire shi a raina gaba daya na manta da shi”

Wani irin murmushi ne ya kawata fuskar Madina, ta yi saurin aje kofin ruwan dake hannunta.

“Amman miyasa?”

“Na gaji ba zan iya ba, sai na nuna masa ni din mai tsada ce kuma na nuna masa he is nothing to me”

“Shikenan zan zo da safe, wannan maganar ba ta waya ba ce”

“Okay ina jiranki”

Leila ta katse wayar, sai Madina ta rike wayar tana kallo, rabuwar masoya ba abu ne mai kyau ko dadi ba, sai dai ita ya zo mata a dabam domin ta samu kanta cikin farincikin jin abun da Leila take kokarin aikatawa.

BATURIYA POV.

Kamar yadda Ramlee tai mata alkawarin kawo mata kayan mata da zata sha a jiya, ta kawo mata su cike kamar wanda zata sara ta kai su wani gurin, ita ma kanta ta yi mamakin tarin hakin mayen da Ramlee ta kawo mata, wanda za a hado da madara ko zuma a sha duka ta siyo mata madarar da zumar, yadda ta ware kudi ta siye mata kayan matan sai ka rantse da Allah yarta ce.
Hakan yasa ta bude wardrobe dinta ta saka su ta rufe da makulli, idan zata sha sai ta bude ta debo ta sha ta rufe, ko Sultan bata yarda ya gani ba balle kuma Faruq uban gayya.

Bayan ta gama gyara gidan yayi tsab ta dora girkinta da wuri, sannan ta shigo falonta ta dauki wayarta ta kunna data ta fara chat. Zata yi reply wani sako kiran Fahat ya shigo wayarta, da sauri tai picking ta kai wayar a kunnenta.

“Hello”

“Yan mata ya kike?”

“Lafiya kalau, sai marmarinka”

“Uhm mmn Marmari kamar gaske, ke da kin ki bari ma na zo mu gaisa, sai kwana kwana kike min”

“Ai na fada maka gidamu ba za a bar ni ba, ba a barin mu zance gaskiya”

“Amman ai kin yi girman da ya kamata ace ana barinki zance Fee'at”

Ta lumshe ido tana jindadin yadda ya kira sunanta, daman haka take so ba kamar yadda Faruq yake kiranta da Rafi'a ta yi complain har ta gaji, sai yace mata shi ba ba ta soyayya yake ba, ta neman kudi yake da abun da zasu ci.

“Ba zaka gane ba ne”

“Na gane, kuma suna da gaskiya, wasu iyayen basa barin yayansu su na kula samari barkatai, amman idan kin amince min zan iya sakawa a zo a nema min izinin magana da ke har mu fahimci juna”

“Da gaske?”

Ta tambaya tana tashi zaune daga kwance da take.

“Wallahi kuwa, Fee'at ni fa da gaske nake aurenki zan yi, ba da wasa na zo ba”

“Uhmm”

“Allah kuwa, Momyna ta dade tana min maganar aure, ansha kai ni gurin yan mata da yan'uwa amman wallahi ban taba jin wanda tai min ba, amman ke ina ganinki na ji wani abu akanki Fee'at you're different...”

Ba karasa maganar da yake ba ta yanke wayar ta kasheta gaba daya sakamakon jin ana kwankwasar gidan. Fitowa tai ta isa gurin kofar ta bude sai tai arba da Faruq yana dauke da Sultan.

“Har kun dawo”

Sai da yai kamar kar ya amsa mata sai kuma ya amsa.

“Eh, Sultan shiga ciki”

Ya karasa yana sauke Sultan dake rike da ledar kifi kasa. Sannan ya juya ya

“Zan tafi shago”

“Allah ya tsare”

Ta fada kamar ba ita ba har sai da ya juyo ya kalleta, rabon da tai masa addu'a har ta manta.

“Ameen”

Ya amsa sannan ya juya ya cigaba da tafiyarsa, ita kuma ta maida kofar ta rufe taja hannun Sultan suka nufi cikin gidan tana tunanin maganar da Fahat yai mata.

‘Amman da gaske yake zai aure ni? Ko kuma dai wasa yake? Amman ai be san na taba aure ba, idan na fada masa gaskiya zai yarda ya auri bazawara?’

Ita kadai take ta haukanta ta saka wannan ta kwance wacan, gaba daya sai hankalinta ya tattara ya koma gurin Fahat tana ta ayyana irin rayuwar da zata yi, kasancewar sa mai kudi kuma dan masu kudin.

“Momy Mama tace a gaishe ki”

Sultan ya fada yana zaunawa ya bude ledar kifin.

“A hanya Dady ya siya min, yace na ci rabi na baki rabi”

Ba ta ma kula, gaba daya hankalinta yana gurin Fahat.

“Amman fa na masa karyar arziki, wata kila yana min kallon yar masu kudin ne”

Sultan ya kalleta.

“Momy waye?”

Sai a lokacin ta lura da a zahiri tai maganar ba a badini ba.

“Ba kowa ba ci kifinka, ga abinci can akan wuta idan yayi zaka ci kaji”

Ya fada mata kai ita kuma ta shiga uwar daka ta dauki wayar ta kunna, sai ga sakon Ramlee ya shigo mata.

‘Ki sha kayan nan da yawa, yace yana son ku hadu da gobe, na kira wayarki ban samu ba, idan kin gama karantawa ki goge sakon’

Dundundun ta ji gabanta yayi duka uku uku, ba dan bata saba haduwa da mazan da ba muharramanta ba, sai dai wata kila saboda wannan haduwar ta daban ce, saboda zata aikata sabo ne alhalin tana da aure da kuma da, ga kuma karamin ciki a jikinta.
Saurin goge sakon tai kamar yadda Ramlee ta bukata, sannan ta mike tsaye ta isa bakin kofar dakinta ta tsaya tana kallon Sultan dake ta aikin cin kifinsa hankali kwance, damuwa ce ta bayyana a fuskarta, duk wani dauki da take na son a bata kudi sai ta ji ya ragu, domin bata taba aikata alfasha ba, sai a wannan karon ne zata gwada. Juyawa tai ta koma cikin dakin tana busar da iskar bakinta.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball

Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

LEILA POV.

Sam bachi ya gagari idonta saboda yunkurin da take a zuciyarta na naki da soyayyar Talba. Sai ta kasa samun hadin kan sassan jikinta ciki har da idanuwanta, da kuma zuciyar datai mata garkuwa da kaunar Talba. Sai yanzu ta gane ashe abun ba shi da sauki, daman taya zai zame mata mai sauki? Ta rayu da kaunarsa na tsawon lokaci a dare daya ta ce zata cireta?
A maimakon ta ji kuzarin cirewar ta karfafawa kanta guiwa, sai ta samu kasala tana jin kamar ba zata iya rayuwa idan babu Talba ba.
Sai dai tana jin ajinta da martaba da kimarta ta wuce Talba yai mata haka kuma ta cigaba da sonsa ko waye shi kuwa?

“Na girmi wannan... Amman why?”

Ta furta tana jin kamar ba zata samu hadin kan zuciyarta ba.

“Allah karka min jarawa da kaunar mutumen nan”

Ta furta ta saka hanayenta biyu ta share hawayen da suka zubo mata. Mikewa tai tsaye ta nufi gurin window ta bude window ta tsaya a gurin tana kallon taurarin da suka kawata samaniya.

“Do i deserve this? It's painful...”

Ta fada wasu hawayen na sauko mata, a rayuwarta bata san zafin rashin ba, bata san ta nemi wani abu ta rasa, wata wani abu painful irin na wannan daren ba, a damuwarta akan halin Talba ne, amman a yanzu abun ya ninku tana jin kamar ba zata iya yakar kaunarsa a zuciyarta ba, kuma ba zata iya barin kaunar ta zauna ba then me zata yi?
Ta yi kasa da kanta wasu hawaye na sauko mata, ta fashe da kuka marar sauti, sai kuma ta soma murmushi.

“Ni Leila ina kukan namiji? Wannan ba ajina ba ne, at least na san Talba be isa yace ba zai aureni ba, amman ni din ai be kamata na aure shi bayan duk wannan abun da yai min ba, be kamata na damu ba”

Ta share hawayenta, sai magana take da kanta tana kallon harabar gidan kamar wani bakonta. Can kuma ta rumgume hannayenta tana tuna kalaman Kabir cewar Talba yana son ta, sometimes akwai kamshin gaskiya maganarsa, amman idan har Talba baya son ta waye zai so? Dole dai ita din ce.

“Akwai maza da yawa da suka fi Talba komai a duniyar nan, kudi, kyau, aji da komai ma, idan zan ba wa maza da yawa dama zan samu wanda zan so fiye da Talba ma”

Wannan karon with full confidence tai maganarta tana jin cewar zata iya. Ba laifi ta dan samu karfin guiwa da dakiyar zuciya, hakan yasa ta rufe window ta dawo saman gadonta ta hau ta kwanta ya rumgume filo ta lumshe ido tana son bachi ya dauke ta.
A nan ne bachi ya ce mata fir ba dai shi ba a yanzu, tunanin abun da Talba yai mata sai ya dawo mata a rai ya zauna, idonta zuciyarta kuma a bude, har kusan karfi uku na dare, Leila ba mace ce ma'abociyar karatu ba balle ma har tai tunanin raya daren da nafila.
Bata yarda ta bude idon ba duk kuwa da kin bata hadin kai da bachin yai. Sai kusan asuba bachi yai gaba da ita.
Washe gari Sunday kamar jiya kowa ya hadu a gurin cin abinci ban da Leila, sai dai a yau bangaren Momy aka zauna ba kamar jiya ba da aka karya bangaren Daddy.
Daddy ya gama duba kowa be ga Leila, hakan ya saka ya kalli Momy.

“Doctor ina Leila?”

“Tana dakinta i think”

Daddy ya yi mata wani kallo da kyau.

“So you think? Lafiya take na lafiya tana dakin ma ko bata ciki baki da tabbaci?”

“Uhm wani lokacin kana bani mamaki Alhaji, yaran nan fada wayansu ya kamata idan muka gan su a wani yanayi da suke son kebancewa mu bar su a yanayin da suke ciki”

“Amman idan suna da damuwa fa? Har kullum wanda ka haifa kana masa kallon yaro ne ko da kuwa ya girmi duniyar nan, irin wannan abun shi yake haifa da depression mutum yana da damuwa kuma a kasa maganance masa ita ko a ki kula da shi, wannan be dace ba, ko jiya bata ci abinci safe tare da mu ba”

Momy ta tabe sannan ta kwalawa Mairo kira, Mairo dake kitchen tana wanke kayan da sukai amfani da su, ta amsa tana fitowa da sauri.

“Shiga dakin Leila ki kirata”

“Hajiya Wallahi ko dazun dana shiga gyara dakin fada tai tayi tace idan a sake shiga dakinta ba tare data fito ba ko kuma na tashe ta bachi sai ta mare ni”

Mairo ta fada a ladabce. Sai Daddy ya kalleta.

“Ta mare ki? Yarta ce ke?”

“Wata kila fada dakin ne ba sallama ko knocked”

Momy ta amsa.

“No wannan ba dalili ba ne, at least ai ta girmamasu sun gurme ta nesa ba kusa ba”

“Wallahi Daddy haka take musu, ko magana cikin tsawa take yi”

Amal ta dora da nata, sai Daddy ya kalleta sai dai be ce komai ba ya cigaba da cin abincinsa, Daddy mutum ne mai matukar son yayansa, ko kadan baya son ya ga wani abun bacin rai ko n damuwa ya same su, sai dai hakan be taba saka shi ya kyalesu a inda ya kamata ya gyara musu ba kuma ya saka musu ido.
Sai da Daddy yai rabin cin abinci sannan ya kalli Momy ya ce.

“Yawan fushi ko tsana yana nuna akwai abun da yake damun mutun ne, musamman a kwana biyun nan da bata fitowa cin abinci, idan akwai wani abu da yake damunta ki sama mata mafita, akwai abun da ke ya kamata ki yi a matsayinki na uwa, zata fi sakewa da ke kuma ta bude miki cikinta ta fada miki damuwarta, and to you my friends idan akwai wanda yake mata wani abu da zai sakata a damuwa ko bacin rai dan Allah ku daina, ya zama tsintsiya madaurinki daya, idan dayanku yana cikin damuwa ku yi kokarin ganin kun kawar masa Allah ya hada kanku yai muku albarka”

Duk suka amsa da Amin, sannan Daddy ya mike tsaye yana fadin.

“idan kin yi magana da ita, ki fada mata ina son ganinta”

“Okay”

Momy ta amsa tana watsawa Talba harara kasa kasa domin har ga Allah yanzu haushinsa take ji, saboda yana kokarin wuce gona da iri. Sai da Daddy ya fice daga falon sannan Momy ta dakawa Amal tsawa

“Amal... Wallahi idan na sake jin bakinki akan fadawa Daddy magana any how sai na baki mamaki, sai na miki hukuncin da baki taba mafarkin zan miki ba, cigaba karki fasa”

Momy ta karasa tana dukan burin dinning din sannan ta mike tsaye ta bar gurin a fusace. Amal ta bata fuska kamar zata fashe da kuka, Kabir ya saka mata dariya. Talba ya kalleshi.

“Kabir?”

Ya sake bushewa da dariya yana yi ma Amal gwalo.

“Sai a hana ni dariya? Yarinyar tafi kowa iya gulma, bata gidan amarya bata gidan ango ai maganinki kenan”

Dariyar ya cigaba da yi mata yana cin abincinsa, ita kuma ta kara bata fuska kamar zata fashe da kuka.

“Karki biye Kabir kin san halinsa ai, daman so yake ki yi kuka, karki yarda ki masa kuka”

“Ai ba zan masa kuka ba, na fi karfin na yi masa kuka”

Ta fada tana matse hawayen dake son fito mata. Kabir kam ban da aikin dariya babu abun da yake mata, daman shi haka yake gurin dariya da keta shine a gaba gaba.
Talba be bar dinning din ba sai da cikinsa ya cika, sannan ya tashi yana handala da muryar da shi kadai zai iya jin kansa ya nufi bangarensa.
Tufafin jikinsa ya cire ya saka gajeren wando sannan ya hau gadonsa ya kwanta, da zimmar bachi amman ya ji kamar ba zai iya bachin ba, hannunsa ya mika ya dauki wayarsa dake gefen gadon, sai ya tararda miss calls har hudu daga Ali. Ganin kiran na Ali ne ya tuna masa da Aminatu, sauka yai saman gadon ya nufi bandakinsa, ta bata minti talati yana jika jikinsa sannan ya dauki man wanka ya zuba ya soma gogawa a jikinsa. Bayan ya gama wankan ya fito daure da tawul dayan kuma a hannunsa yana goge jikinsa da shi, gaban madubin ya zo ya tsaya da alama dai kallon kansa a madubi abu ne daya zama masa al'ada, domin yana jindadin tsaya a madubin yana kallon kansa.
Sai da ya tsane jikinsa sannan ya dauki wani mai ya shafa a jikinsa ya feshe jikinsa da turare, ya murza wani a shafa a jikin, sannan ya shirya cikin kananan kaya ya dauki turaren tufafi ya saka sannan ya murza wani a hannunsa, sai ya juya ya nufi gurin da yake aje agogonsa ya dauki wanda yake ganin ya fi dacewa da tufafin jikinsa ya saka, ya saka talkaminsa sannan ya dauki wayarsa ya da wallet dinsa ya saka aljihu ya dauki wata Jacket milk color ya dora sama. Sannn ya fice dakin rike da makullinsa na mota. Sai da ya isa gurin motarsa sannan ya daga kansa yana kallon windows din dakin Leila, bakinsa ya cika ma iska sannan ya bude motar ya shiga. Ko kamin ya juya motar har sun bude masa gate, kamar dominshi kadai aka shimfida titi, haka ya fige mota ya hau titi yana driving. Kiran Ali ne ya sake shigowa wayarsa, sai ya saka hannunsa ya dauko wayar daga aljihunsa yai piciking.

“Hello”

Ali ya fada daga dayan bangaren sai Talba ya amsa masa kamar baya son magana.

“Ya akai?”

Ali yayi dariya.

“Kar kace min har yanzu fushi kake, Ni da n kira na fada maka ka ya kamata ka bawa Leila hakuri, sai kuma na ji ka a fushi har yanzu”

“Ali taya na kusa da ni zai wulakanta dan adam ya muzanta shi kuma ka tsammaci abun nan zai wuce da sauri? Kawai fatan da nake ya zama na babu hannun Leila a taba yarinyar nan, and zan binka matsalar Baaba na tabbar idan akwai hannunta ko babu”

“Wace Baaba kuma? Talba are you in sense? Miya samu Baaba and why za kai blaming Leila? Ban taba yarda baka son ta sai...”

Ali be karasa Talba ya yanke kiran ya aje wayar ya cigaba da tukinsa, ya san idan zai bata lokaci yana ma Ali bayani a yanzu ba zai fahimta ba saboda yana ganin tausayin Leila kuma yana ganin kamar Talba yana mata haka saboda baya sonta.

Be sake bin ta kan wayar ba har ya isa asibitin ya faka motarsa a inda aka tana domin aje motoci, sannan ya dauki wayar ya bude motar ya fita.

Kai tsaye ya dauki hanyar da zata sada shi da dakin da aka kai Aminatu, so kawai yake ta farka ya tambaye ta, idan ta amsa masa da eh zai dauki mataki akan Leila idan kuma ya zama tsabanin haka zai bata taimakon da take bukata be kuma zama lallai ta sake ganinsa ba. Ba dan wannan abun daya faru ba wata kila ma da ba za zai sake sakata a idonsa ba har abada.

A hankali ya kai hannunsa ya tura kofar dakin, sai kuma ya tsaya daga bakin kofar yana kallonta, kwance take idonta a rufe hawaye na sauko mata, an cire mata robar jinin an saka mata ta ruwa, sai kuma ledar pure water dake saman dan karamin tabur din dake kusa da gadonta. Silently ya shiga cikin dakin ya maida kofar ya rufe, sannan ya isa gurin gadonta yana kallon fuskarta, ko kadan bata ji motsin bude dakin ba balle kuma shigowarsa ba, sai dai kamshin turarensa ya dawo da ita duniyar tunanin da tafi, hakan yasa ta bude idon a hankali a karo na biyu ta sake saka idonta cikin nasa, bayan wacan karon da suka zo tare da Ali, sai dai yanayin fuskarta sa ya tsorata, da alama ba mutum ne alaka da sakin fuska da murmushi ba. Sai dai kallonta yake kamar yadda ita ma take kallonsa hawaye na cigaba da sauko mata.

“Can you talk?”

Ta tambaya domin burinsa ta amsa masa da eh ko aa. Sai ta maida idon ta rufe.

“Keeee.!!!”

Ya daka mata tsawa, sai ta bude idon a zarane ta tashi zaune jikinta na rawa ta fara dube dube, domin ta tsorata matuka, abu kadan sai zuciyarta ta fara bugawa tana ganin kamar abun da ya faru ne a baya zai sake faruwa.

“Mi na yi, kashe ni za ayi?”

Tsayawa yai kallonta a ransa yana jinjina irin tsoratata da Leila tai. Be ankaro ba ya ji ta fashe da wani irin kuka mai taba zuciya, hakan ya saka shi matsowa kusa gadon.

“Ba komai za a miki ba tambayarki kawai zan yi”

Ta kalleshi jikinta na cigaba da rawa hawaye na sauko mata kamar ba gobe.

“Me zaka tambaye ni? Inna? Ko Baba? Ko kuma yan'uwana?”

Shiru yai yana kallon yadda idonta yai ja tsabar kukan da take, ya hade yawun bakinsa tare da maida numfashi a hankali.

“Ki kwantar da hankalinki babu abun da za a miki, kawai ina son na tambaye ki ne ko akwai wanda yai kokarin kasheki kamar makura, saboda an samu hannunta yana zubar da jini kuma roba zagaye a wuyanki”

Kokarin natsuwa take tana son tuna abun da ya faru, sai ta daga kanta tana kallon dakin, sai a yanzu ta tuna akwai banbanci tsakanin wannan dakin da wacan.

“Zaki iya tunawa?”

Ya sake tambaya.

“Ban manta komai ba, komai yana cikin kaina, idanuwana suna ganin komai har yanzu”

Ta amsa masa cikin rashin kuzari.

“Good fada waya kika gani kamin su suma?”

Ta kalleshi.

“Ban ga kowa ba”

“Wa yayi kokarin kasheki?”

“Babu”

“Amman an tarar da hannu da jini...”

Be karasa ba ta bashi amsa, bakinta a bushe kana ganinta kasan yunwa da ciwon sun mata mugun kamu.

“Ni ce ni na aikata”

Kallonta yake irin kallon nan dake nuna so yake ya gano idan tana cikin hayyacinta ko akasin haka. Sai ya ware mata hannunsa.

“Miye wannan”

Ta kalli hannun nasa, sai kuma ta koma zata kwanta.

“Keeee!”

Sai ta zaburo masa kamar ba ita ba.

“Miye? Me kake so? Me zan maka? Dan Allah ka bar ni da damuwata, ka bar na ji da abun da yake damuna”

“Ni ma ba damuwa ba ne, i just want to ask miyasa kike son ashe kanki..”

Shi ma a tsawace yai mata tambayar zuciyarsa na bugawa da karfi yana jin kamar ya dake ta saboda ta masa tsawa.

“Saboda na mutu, na huta, na tafi inda yan'uwana suka tafi na tararda mahaifiyata da mahaifina, ta tafi inda ba a zalinci inda ba a danne hakkin kowa, na tafi inda....”

Ta kasa karasawa sai numfashinta yai sama ta fadi kwance saman gadon wuyanta a lankwashe, da sauri ya kai hannunsa ya rikota ta gyara mata wuyanta.

“Baba.... Baba.... Baba.... Baba...”

Shine kawai abun da take ta fada tana kallon Talba da idanuwanta da suka fara rufewa. Fita yai dakin da sauri ya nufi inda likitoncin suke ya fada musu sai likita da nurse uku suka taso a guje suka nufo dakin, zai shiga wata nurse din ta dakatar da shi.

“Malam ka tsaya a waje...”

Sai yaja ya tsaya gabansa na faduwa, kalamanta sun ratsa shi ga tausayinta, a yanzu kan ya tabbatar tana da babba damuwa wanda zata iya haifar mata da matsala kamar yadda Kabir ya fada. Yana tsaye a wajen har suka fito. Likitan ne ya tsaya yana tambayar Talba yayin da nurses din suka wuce.

“Ya kake da wannan mai rashin lafiyar?”

Talba yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

“Kanwata ce”

“Dan Allah bismillah akwai bayanin da zan maka”

Likitan na fadar haka ya wuce gaba, Talba ya bi bayansa har suka shiga cikin Office. Talba ya zauna ba tare da jiran likitan yai masa izini ba.

“I'm sorry ban sani ba, ko an maka bayanin cewar yarinyar nan an mata fyade, fyaden da ya wuce na hankali, da alama ba mutun daya ba ne ko biyu, domin abun yayi effecting kwakwalwarta, tana jin tsoro gaskiya, so ya kamata ka kiyaye bacin ranta damuwa, kuma kai kokarin kwantar mata da hankali, and karka dame ta da tambaya ko son sai ta tuna abun da ya faru, domin a yanzu ta kai matakin da zuciyarta zata iya bugawa, kuma be zama lallai idan ta buga ta rayu ba, za a iya rasa ta”

Ya karasa tare da mika hannu ya dauko wata takardar yai rubutu akai, ya mika masa.

“Ka siyo wannan maganin ba mu da shi a nan”

Talba ya kai hannu ya karba yana kallon takardar maganin.

“And zata fara cin abinci daga yanzu, domin na ga a file dinta an rubuta cewar bata ci, sai dai jiya na gwada bata ruwa ta sha kuma ta sha, so from now on zata fara cin abinci”

Talba ya gyada masa kai. Sannan ya juya ya fice daga office din jikinsa a mace, tafiya yake yana tuna kalaman da tai masa da kuma na likitan, and the most important part is fyade. Kamar marar kuzari haka ya bude motar ya shiga ya zauna.

“She's too young for this, maybe sun ashe Mamanta Babanta and su kai raped dinta... Wow.... ”

Ya furta yana runtse ido, yana ayyana yadda abun yake da mugun ciwo. Wayarsa ya ciro ya nemi number Kabir ya kira shi.

“Ranka ya dade”

“Kabir wane chemist ko pharmacy zan samu magani ko wane iri a yanzu?”

“Wa zaka siya wa?”

“Kai... ”

Kabir yayi dariya. Sannan ya fada masa, Talba ya kashe wayar ba tare da sake ce masa komai ba, sannan yai ma motar key yai reverse ya fice daga asibitin. After ya siye maganin ya siyo ayaba da kankana da lemu a hanya sannan ya dawo asibitin, kamar wani barawo haka ya shiga dakin without making a sound, har gaban gadonta ya karasa ya aje ledodin.

“Waye kai?”

Ta tambaya a hankali idonta a rufe, kallon mamaki yai mata a zatonsa bachi take but maganar da tai ya tabbatar masa da tsabanin haka, sai dai idonta a rufe yake.

“Talba, you can call me Talba...”

Ya samu kansa da amsa mata yana kallon fuskarta. Sai ta bude ido a hankali ta kalleshi, ta sake maida idon ta rufe.

“Idan kina bukatar wani abu ki fadawa likitan zai sanar da ni, kuma idan zaki iya fada zamu so sanin inda yan'uwanki suke sai a bincika so that su san kina raye kuma ki samu mai kula da ke”

“Da rayuwata da mutuwa ta duka daya ne, saboda ba ni da kowa a yanzu”

“Shiyasa kike kokarin kashe kanki? Ko kuma dai wani ne yake kokarin kasheki?”

Ta bude idon ta tashi zaune cikin rashin kuzari tana kallonsa, idonta har ya yi baki yayi ja kamar tsabar damuwar da kuka.

“Idan baka ci abinci ba akwai mai damuwa? Wani yana damuwa idan baka da lafiya? Idan ka shiga damuwa akwai mai kokarin faranta maka rai? Akwai wanda zai so abun da kake so, ya guji abun da zai bata maka ra?”

Yayi shiru yana kallonta, kamin ya hade yawun bakinsa, ya daga mata kai alamar eh akwai.

“Ni duk na rasa wannan, a cikin dare daya rayuwata ta sauya, a tsakanin awannin da dakiku aka min katanga tsakanina da iyayena, farincikina yana tare da yan'uwa kuma duka an kashesu, a ciki wuni guda aka juya duniyata, aka nesanta ni da farinciki, a kusanto da bakinciki, a cikin daren nan aka raba ni da martaba da, na kasa manta komai, hoton komai ya gagara goguwa a idanuwana, a tsakanin wacan daren da dararen da suka biyo bayansa bakinciki ne da tashin hankali, sum rusa duniyata, sun tarwarsa shirina...”

Kallonta Talba yake a tsakanin hawayenta da duniyarta da take labarta masa sai ya rasa wane ne yafi tsaya masa a zuciya. Kujerar dake gefen gadon ya ja ya zauna yana kallonta.

“Likita yace ki daina damun kanki, saboda yanayinki yawan tunani da damuwa zai iya haifar miki da wata matsalar...”

“Akwai matsalar data wuce ta rashin uba da uwa? Rayuwata ta riga ta sauya, bana tsoron mutuwa....”

“Amman baki yi tunanin miyasa mutuwa take gudunki ba? Na san kin shiga a gurin da za a iya kasheki amman ba a yi ba, kika samu kanki a nan kuma kika yi kokarin kashe kanki, still hakan be faru ba, rayuwata tana ta zabenki ke kuma kina neman mutuwa baki yi tunanin ya kamata ki rayu ba?”

Ta lumshe ido tana jin bachi na son daukarta saboda allurar da akai mata.

“Na rayu a inda ba a rufa idan akwai sanyi, ba a fakewa a idan ana ruwa, ba a gusawa idan rana ta kawo, a hannu ake raba mana abinci, idan an bada da safe ba za a sake ba badawa ba sai da dare, na ga wa ana dukan wasu, kuma a kashe da yawa a gabana, sun keta haddin mahaifiyata a gabana, sun yanka yan'uwana, sun kona abincin mu, suka akashe babana saboda ya ki yarda ya keta haddin ni, sanadin tafiyar da muka yi kafafuwana basa iya komai a yanzu, sun yanka yan'uwana sun fasa kan wasu da dutse, a haka kuma kake ganin rayuwata tana zabata? Wata kila saboda tana son na yi taraiyya da bakinciki ne”

Hawaye ya sauko mata sai bachi yai baga da ita, ido ya sakar mata kalamanta na taba zuciyarsa, misali yake da kansa idan shi ne ya zai ji? Yana rayuwa cikin jindadi lokaci daya ace komai ya tarwatse! Shi kansa maraya ne, amman be san zafin rashin iyaye ba, be san zafin rashin yan'uwa ba, idan wani abun ya same shi da gudu za a kawo masa agaji, tsabanin it. Takurewa tai gurin daya ta jikinta na dan rawa alamar tana jin sanyi ga kuma hawayen har yanzu ba su daina zuba ba, murmushi mai sauti ne ya biyo bayan hawayen.

“Inna....”

Ta furta tana cigaba da murmushi, sai kuma tai fuskar kuka wasu sabbin hawayen suka zubo mata. Mikewa yai tsaye ya cire Jacket din jikinsa zai lulluba mata sai jikimta ya fara, tana numfashi da karfi ta kara rumgume kanta kana ganinta kasan a tsorace take, a hankali ya lullub mata jacket din sai kuma ya tsaya yana kallonta har lokacin hawayenta zuba suke, wani dogon numfashi yaja ya sauke sannan ya juya ya fara tafiya a hankali zuwa gurin kofar.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un... Taya zan tafi na barki? Ko na gudu harbina zasu yi, ba zan tafi ba tare da ke ba...”

Juyowa yai ya kalleta, kana ganinta ka san wani tashin hankalin ne take mafarki, da alama abun da ya faru ya shiga ranta sosai ya zauna, ya kusan minti biyar a tsaye yana kallonta sannan ya fice yaja mata kofar a hankali ya rufe.

Dan Girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

FARUQ POV.

Mama ta sauke ajiyar zuciya tana jinjina lamarin Rafi'a.

“Faruq ka saka mata ido, duk abun da take tana yi saboda ta bata maka rai ne, kuma komai na rayuwar duniya jarabawa ne, ko da arziki ne Allah ya baka ya ga yadda zaka iya rike su, balle kuma talauci, da muguwar mata”

“Wallahi Wani lokacin Rafi'a tana bani mamaki, ita kamar bata san Allah ke yi ba? Shi zai yi ma kansa arziki ne? Sai ta rika abu kamar ba yar'uwa ba?”

Aisha ta dana da nata. Sai Faruq ya kalleta.

“Wani lokacin ina jin kamar na sake ta na huta, sai dai idan na tuna irin wahalar da mahaifinta yai da ni a karatuna kuma ya dauki yarsa ya aura min duk da a lokacin bana da komai, sai na kamar idan na sake ta ban kyauta masa ba”

“Haka ne, wani abu dole a daga mata kafa saboda mahaifinta, domin mutumen kwarai ne, kuma na tabbatar da yana raye Rafi'a ba zata maka wani abun ba, kasan Umma daman ba son auren take ba tun farko shiyasa komai tai bata ganin laifinta, amman kai hakuri Inshallah sauki yana tafe”

Ya ja wani dogon numfashi ya sauke.

“Ni da har na yanke shawarar na bi Yusufa mu tafi nijar gurin ginar zinarina nan”

“Nijar kuma?”

Cewar Mama ciki damuwa.

“Eh kin ga masu zuwa suna samowa ba laifi, kuma ba kasan inda rabonka yake ba, amman zama haka ba zai yi Mama, hausawa sun ce idan hagu ta ki sai a koma dama”

Mama ta girza kai.

“Wallahi bana son tafiyar nan nesa Faruq, da dai ka hakura mu ga abun da Allah zai yi”

“Mama duk inda rabonka yake sai ka tararda shi, ko kuma ya nemeka, kuma abun da Allah ya rubutawa bawa ko a ina yake zai same shi, na san dai ba zai wuce ki ce kina jin tsoron hanya ba ko abunda zai faru da ni, kawai ki min addu'a”

“To Allah ya zaba mana abun da yafi zama alheri, idan tafiyar Alheri ce Allah ya shige maka gaba”

“Ameen idan Allah yasa naje ko na siyen fili na samu ai na samu”

“Haka ne, amman kudin motar zuwa can fa?”

“Har cin abinci da komai zan iya kashe 20k haka Yusufa ya fada min, kuma yace ana kwana uku kamin a samu isa, wannan kudin da ban biya haya ba zan iya cire na mota ciki sai kuma sauran kuma na siya ma Rafi'a abinci na bar mata kamin mu tafi kuma mu ga abun da Allah zai yi”

“Toh Allah ya shige maka gaba”

“Ameen”

Ya fada yana mikewa tsaye sai kanwarsa ta kalleshi.

“Ya Faruq ance fa rame ake shiga, ko. Kwanan baya na ji ance rame ya rusga da wasu”

Murmushi yai.

“Allah shi ke tsarewa ai, ku dai kui ta mana addu'a”

“Toh Allah ya tsare, yasa arzikinka na can”

“Ameen ya Rabb”

Ya amsa sannan yai musu sallama ya fice, ko da ya isa gida har ta gota, a bude ya samu kofar gidan, sai ya shiga da sallama ya maida kofar ya rufe sannan ya shiga falon, sai ya same ta tana waya sai dai ganinsa yasa ta sauke wayar ta kalleshi.

“Sannu da zuwa”

“Yauwa, ya gidan?”

“Alhamdulillah”

Sai ta tashi ta nufi inda abincinsa yake ta dauko masa ta aje masa tare da ruwa.

“Ina Sultan?”

“Yayi bachi”

Ta amsa sannan ta zauna kusa da kujerar da yake zaune, kallonta yake har ta zauna din, gaba daya yau ta canja, daman can fara fes amman haskenta and yau ya karu sai wani sheki take tana ta kamshin hummura mai tsada. Dauke kansa yai ya maida dubansa gurin abincin data aje masa yana hade yawu, rabon da wata mu'amalar aure ta shiga tsakaninsu har ya manta, domin bata yarda idan ma ya neme ta, idan ya matsa sai tace ga ciki ba zata iya ba, shi kuma baya son yi mata da karfi hakan yasa ya dauke mata kai ta wannan bangaren ba dan baya bukata ba sai dan ba zai iya ja'inja da ita ba.

“Rafi'a ina ta shawara da kuma neman zabin Allah”

Ta kalleshi da sauri a tunaninta ko zai fada mata cewar daya faga cikin aikin da yake Applying ne wani ya fito.

“Na me? Aikin ka samu ne?”

“Aa, ina shawarar zuwa nijar ne?”

Wani irin yatsine fuska tai kamar wanda tai arba da abun kyama.

“Nijar fa kace? Ba dai gurin ginar zinari ba ko?”

“Can mana”

“No nonono, Wallahi ba zan yarda ba, so kake ka ja min abun magana a gari? Ace mijina ya tafi gurin ginar zinari? Talaucin har ya kai nan? Aa Wallahi ba zaka je ba”

“Shi zuwa ginar zinari zunubi ne? Wace irin magana ce wannan nan?”

“Kana tafiya za a ce talauci ya matsa mana har ka bar gari ka tafi nema nijar, ka ja min abun magana, kawaye na mazajensu daga masu aiki a kamfani sai banki sai ma'aikatun gobnati, ni kam ba zan iya ba Wallahi”

“To sai na fasa saboda ke nan? Ni na riga na yanke shawara, kuma na zo na fada miki ne saboda na baki hakkinki”

“To Wallahi ba zan yarda ka je ba, Wallahi sai dai ka sake ni ka tafi na san ba mu tare”

Dubanta yai irin duba na mamaki.

“Rafi'a me kike son ki zama? Ke kin isa ki yi ma kanki arziki ne, da abu kadan zaki fara cewa talauci?”

Sai ta mike tsaye domin ya fahimci da gaske take.

“Wallahi Faruq, na rantse da Allah ba zaka tafi nijar ginar zinari da aurena ba, sai dai idan tafiya ce zaka yi ta har abada, wanda babu dawowa, wai kai baka da zuciya ne? Baka san Annabi ya faku ba, na gaji da abun kunya Faruq, na gaji, aurena dole ne? Ni kadai ce mace a duniya nan ne? Ba zan iya ba, ga danka nan yayi wayo amman ka kasa saka shi makaranta, wannan da zan haifa ma na san dan taure zaka yanka min”

“Sai ki saki kanki ai, ba saki ba? Ba zan saki ba kuma sai na tafi nijar din ki mutu, ina hakuri ne dake kawai saboda Mama da kuma mahaifinki”

Ya fada yana mikewa tsaye, sai ta sa gabansa.

“Wato ka fito gurin bakar tsohuwa ta kitsa maka abun da take so a kai...”

Bata karasa ba ya wanke mata fuska da mari sai da ta fadi zaune. Ta fashe da kuka.

“Faruq ni ka mara?”

“Har abun da yafi mari zaki samu, matukar iskancinki da rainon wayo ya kai ki ga taba mahaifiyata, ai ko da ba ta hada komai dake ta cancanci girmamawa saboda tana sarakuwarki balle tana a matsayin kanwar mahaifinki”

“Ita bata san da zumuncin bane ta barka kana ta cutar da ni? Ba zan iya ba, na ce bana so ka sauwake min mana”

Har yayi kamar Ya bude baki yace na sakeki sai kuma wata zuciyar ta hana shi. Be sake kulata ba ya shiga bedroom din, bakin gado ya zauna yana kallon Sultan dake ta bachi ya kai hannu ya shafa shi, makomar dansa yake zubawa idan har ya sake ta rayuwarsa zata zama abun tausayi, domin zaman zai zame masa a tsakanin gida biyu, gidan mahaifinsa da kuma inda Mahaifiyarsa. Tsabar bacin rai da tunani be ci abincin ba ya kwanta kusa da dansa, Baturiya kuma ta kwana a falo.
Washe gari waina ya siyo musu abun kari kasancewar aljihunsa da dan nauyi irin na masu nema yau da gobe, bata gaishe ba tun da garin Allah ya waye, sai dai hakan be hana shi ce mata zai fita ba, da harara ta bishi babu Allah ya tsare balle addu'ar alheri.

“Allah yasa kai hadari ka mutu..”

Ta fada bayan ta ji karar rufe gidan, sannan ta tashi ta bude wainar ta zubawa Sultan, ita kuma ta nufi wayarta ta dauka ta kira Fahat, ringing biyu ya dauka.

“Fee'at”

Sai ga murmushi a fuskarta kamar ba ita ba, bata kula da Sultan ba ta cigaba da wayarta tana masa kalaman soyayya kamar yadda shi ma yake mata. Sun kusa awa daya suna abu daya sannan sukai sallama tana masa kiss a wayar, duk abun da take Sultan na kallonta sai dai ita bata lura da hakan ba. Fitowa tai waje ta fara gyara gidan domin Ramlee ta fada mata karfi goma za su hadu. Ko da tara tai Baturiya ta gama komai har ta shiga ta yi wanka. Sai da ta shirya sannan ta kai Sulta makota ta dawo gidan ta kara daukar wasu kayan matan ta sha daman Ramlee ta nuna mata wadanda zata sha idan tana kusan tafiya.

Tara da rabi kiran Ramlee ya shigo wayarta, jiki na rawa ta dauka kamar ba ita ce ta gama jin tsoro ba a jiya.

“Madam hop kin shirya”

“Na shirya, ke kawai nake jira”

“Haka na ke so, ba wasa ganin nan nima na kusa karasowa”

“Sai kin iso”

Ta aje wayar tana murmushi, ita ma kanta ta san ta yi kyau, sai kamshi take zubawa kamar sabuwar amarya, kamin Ramlee ta iso ta shafa hoda ya kai sau shida, turare kan ba adadi irin feshin da take masa.
Tana jin sallamar Ramlee ta dauki wayarta da jakarta ta fito waje da sauri.

“Wow yanzu kika fito da sunanki n Baturiya, amman mutumen idan ya ganki sai ya rude”

Baturiya ta yi dariyar jindadi.

“Da gaske”

“Wallahi kuwa, sam sam baki dace da Faruq ba, ke din matar manya ce, amman fa karki fada masa cewar kina da aure domin na ce masa ke din bazawara ce”

“Ke ma dai da wata magana, ya za'ayi na fada, Allah dai ya sa inda zamu je ba public place ba ne, domin akwai wadanda bana son su gan ni”

“No guest house dinsa ne, muje dai kar mu bata lokaci”

“Amman kin san me? Idan na fita da kwaliyar nan haka ina kamshi mutanen unguwa za su fara saka mana ido”

“To ya zamu yi? Ke dai ina ruwanki da mutane ne wai?”

“Aa bari dai a saka hijab da nikab idan na je can sai na cire a motarki”

“Haka yayi yi sauri”

Ta juya ta koma dakinta da sauri ta dauko katon Hijab ta saka tare da niqab sannan fito ta rufe gidan.
Tun daga yanayin ginin unguwar da shuke shuken zaka san cewa unguwar manyan mutane ce, a gaban wani katon gate suka faka Ramlee tai horn Mai gadin ya leko tai magana da shi sannan ya bude mata ta shiga, a harabar gidan tai fakin ta ciro wayarta ta kira shi.

“Alhaji mun iso”

“To yayi Kyau Hajiya Ramlee a barta ta dan huta gani a hanya, garin sauri ma na kade wasu amman dai na gama komai zan iso yanzu”

“To yayi Alhaji sai ka iso”

Ta aje wayar sannan ta labartawa Rafi'a abun da ya faru da shi.

“Kuma ki sake jikinki ki kwashi arziki, domin yana son ki Wallahi na fada miki hotonki kawai ya gani amman duk yabi ya rufe balle kuma ce ya yi arba da ke”

“Inshallah ba zan baki kunya ba”

“Yayi kyau, haka nake son ji, yanzu mu shiga ciki na nuna miki falonsa sai n fito na bar ku ku sha shagalinku”

Ramlee ta fada tana murmushin jindadi. Sai Baturiya ta cire Hijab din da Niqab ta kai hannu ta bude motar wayarta tai kara.

“Allah yasa ba mijin nan naki ba ne”

Cewar Ramlee tana tabe baki, fasa fitar Baturiya ta yi ta ciro wayar daga jakarta ta duba.

“Shi ne kuwa, ban san mi zai ce min ba, ko kuma ya dawo gida ne oho”

“Karki dauka dan Allah zai wargaza mana shiri ne”

“Ai ba zan dauka ba”

Ya fada tana kallon wayar dake ta ringing har ta gaji ta tsinke, sai gashi ya sake kira sai dai wannan karon ta ji gabanta ya dan fadi.

“Kai wannan miji na ki da ci yake, gaskiya ki kashe wayarki kar ya zo yana damunki da kira ya lalata mana shiri”

“Wallahi kiran Fahat kawai nake jira, saboda yace zai kira ni anjima bana son na kashe wayar ya kira ya jita a kashe zai damu ne”

Ramlee ta mata wani kallo.

“Da alama dai shi ma dan hannu ne”

“Aa Wallahi shi ai son aure yake min da gaske, na nuna Masa ni Budurwa ce”

“Amman ke yar banza ce, ya zaki yi da Faruq?”

“Haba Ramlee kina min fatar zama da shi? Ai rabuwa zamu yi, kin ga idan ya sake ni ina zubar da cikin nan na cika idda zai na yi aurena”

“Kina ganin Faruq zai sake ki ne?”

“Dole na idan na bude masa shikashikan rashin mutunci ai dole ya sake ni”

“To dan fa ki yi yaya da shi? Ai kin san za a bincike ki musamman yayan manyan mutane basa aure zai sun zurfafa bincike”

“Ai idan na fita zan bar Sultan a gurin Faruq ne, ba da shi zan je ba, kuma shi Fahat din ai yace min a Lagos yake aiki, kin ga zamanmu a can zai kasance ba a nan ba, zan iya boye komai”

“Ki ce kema kin iya bala'i

Sai duk suka saka dariya, kiran Faruq ne ya sake shigowa wayar, wannan karon wani tsaki taja ta kashe wayar gaba daya.

TALBA POV.

Sai da yai sallah azahar sannan ya karaso gida, tun kamin yayi fakin idonsa suka sauka akan Leila dake zaune a daya daga cikin kujerun da suke balcony rike da wayarta sai cup din lemu a gaban kujerarta tana taunar cingan har wani kis kis take. Yayi kusan five minutes a motar sannan ya bude ya fito ya nufo inda take zaune ya zauna ba tare da yace da ita komai ba, hakan ya bata damar dauke kai daga gefen da yake ta maida wani gurin tana cigaba da taba wayarta.

“Can we talk?”

Ya fada ba tare da ya kalli inda take ba, sai ta juyo ta kalleshi.

“Ta fada maka ba ni ba ce ba kenan?”

Shi ma juyowa yai ya kalleta fuska ba yabo ba fallasa.

“Daddy ya damu dake ne i want us to talk”

“Da gaske?”

Sai ta mike tsaye ta dauki cup din lemun ta wuce ta bar masa gurin. Tana kokarin kai hannu ta danna door bell din kofar falon sai ga Kabir ya fito, ko kula shi bata yi ta shige, da kallo ya bita kamin ya juya ya kalli Talba dake kallon harabar gidan, har lokacin tunanin Aminatu yake. Karasa Kabir yai ya zauna a inda Leila ta tashi.

“Ya jikinta?”

“Da sauki...”

Talba ya amsa ba tare daya kalleshi ba.

“Ka yi magana da Leila ne?”

Ya girgiza masa kai.

“Wani lokacin baka sanin damuwar mutane idan baka kusantar su, you see yan gudun hijirar nan da kake gani a hanya wasu a fankon guri, suna da labaruka masu taba zuciya”

“Ita ma tana daya daga cikinsu ne?”

“Tana daya daga cikinsu ne?”

“Yeah they raped her, killed her Father, mother suka gona musu gida, suka kashe yayyunta and raped her mother in front of her, labarinta akwai tsoro da taba zuciya, yanzu haka she can't walk saboda wahalar data sha gurin mutanen nan, and bata da kowa kuma tana bukatar kulawa sosai”

Talba ya fada cikin yanayin dake nuna zuciyarsa ta tabu sosai da labarin Aminatu.

“You know a lokacin da kake raina ni ni'imar da Allah yai maka, wasu da yawa suna can suna neman kadan, a yadda na fahimta now yanzu farinciki take bukata, saboda ya cire rai daga shi har tana neman kashe kanta, and Ali and wannan likitan sun fada min abun nan ya taba ta”

Kabir ma saurarensa yake cike da tausayin Aminatu duk da kasancewar ba taba ganinta ba, sai dai ya san waye Talba duk abun da zai saka shi a damuwa ko tunani ba abu ne kadan ba.

“Yanzu a wane matsaya take”

“Tana samun kula a asibitin, amman babu mai kwana a inda yake kuma kasan da ace tana uwa ko wata yar'uwa a raye zata fi samun kulawa, tana jin tsoro sosai har magana take idan tana bachi, and likitan ya fada mim idan tana yawan damuwa zuciyarta zata iya bugawa, yarinya ce karama kamar Amal, bata san inda zata je ba”

“Haka ne mutane suna cikin hali, sai dai idan baka shiga cikinsu baka sani”

Talba ya mike tsaye yana saka hannunsa aljihu. Ya nufi bangarensa, Kabir ya bishi da kallo yana murmushi.

LEILA POV.

Tana shiga dakin ta dauki wayarta ta kira Madina ta fada mata abun da ya faru, a ciki har da kudinta na son ta fadawa Daddy cewar ta fasa auren Talba.

“Anya idan kika yi haka baki yi kuskure ba? A Maimakon ki ta wannan haukan ba kara ki nuna masa kina son yarinyar ba ko da a munafunce ne”

“Lallai Madina baki gama sanina ba, ke a tunaninki zan iya share miji ko saurayi da wata? Har sai na nuna ina son ta bayan duk abun da yai min, ni fa na san ba sonta yake ba kawai yana amfani da ita ne ya cusa min bakinciki?”

“Idan har haka ne, ke me zai hana ki yi amfani da abokinsa ki rama abun da yai miki?”

“Waye kenan?”

“Ali mana, ta hanyarsa ma zaki iya tabbatarwa idan Talba yana sonki da gaske”

“Kin kawo shawara, tabbas zan iya rama abun da yai min ta hanyar Ali”

“Yes amman ina fatar hakan ba zai janyo matsalar da zata hana a dauke ni aiki ba, kin san fa ina nan ina ta jira”

“Aiki ai dole a dauke ki, bari anjima ma zan yi ma Daddy magana, ki kwantar da hankali cikin kwana biyun nan za a dauke ki aiki”

“Alhamdulillah, na gode sosai yau zan yi kwana farinciki ko ba komai ai hakan zai kara kusantar da alaka ta da ku”

“Haba ai mun fi haka dake, zan kira ki anjima”

“Okay thank you”

Ta sauke wayar tana murmushi, har cikin ranta take jin cewar Madina ta sama mata mafita na bata shawarar ta yi soyayya da Ali, ta san idan tai haka zata Talba sosai kuma zai gane irin zafin da take ji ita ma.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Khadeeja Candy

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe

Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Zaunawa yai saman gadon yana goge ruwan jikinsa. Sannan ya kai hannu ya dauki wayarsa dake ringing.

“Ali ka dame ni fa”

“Ai dole na dame ka Talba, ka bawa Leila hakuri?”

“Na yi maka kama da wanda zai yi wannan?”

“Seriously Talba baka kyauta ba, kuma ya kamata ka bata hakuri, be kamata alakarku ta lalace saboda wata bare can da baka san inda ta fito ba”

“Leila ta yi abun da yake bani mamaki ne, so dole na zargeta akan halin da yarinyar nan ta shiga, lastly karka sake min maganar bada hakuri”

“Really kana ganin ka kyauta kenan? And me yarinyar ta fada maka?”

Can sama sama Talba ya fada masa abun da Aminatu ta fada masa.

“Yanzu ina yarinyar take?”

Ali ya tambaya yana sauke ajiyar zuciya.

“King's and queen's hospital”

Cewar Talba sannan ya mike tsaye yana shafa fuskarsa.

“Labarinta be taba ka ba?”

“Kai ya taba ka kenan?”

“Yeah, duk wani mai imani ne dole ne labarin yarinyar nan ya taba shi”

“Kar tausayinta ya saka ka manta da yadda kake da Leila, tsakani da Allah yarinyar nan tana sonka kuma tana azabtuwa da irin abun da kake mata”

“We can talk later”

Yana fadar haka ya kashe wayar ya jefa saman gado, sannan ya shiga dan karamin dakin da aka tanada domin ajiyar tufafi ya saka riga da wando na suit blue sannan ya fito ya dawo gaban madubi yana duba kansa. Komawa yai ya dauki turare ya murza a hannunsa na fesawa kuma ya fesa a jikinsa. Sannan ya dauki abun da ya kamata ya dauka ya fice daga dakin yana kokari saka wayarsa aljihu.
Ya fito bangarensa ya nufi bangaren Momy sai dai turarensa ya riga shi isa bangaren Momy saboda karfin kamshinsa, yau kam a bude ya samu kofar falon Zulai nata aikin mopping tana ganinsa tai saurin risinawa ta gaishe shi, sai dai be ma kalleta ba balle har ya amsa mata. Motsin da yaji a kitchen ne yasa ya nufi kitchen din, sai dai be karasa ciki ba saboda ya hango Leila a tsaye kusa da Momy da alama yau kamar a tare suke hada abun karyawan.

“Momy ina kwana?”

Momy ta juyo ta kalleshi, sai ta amsa fuska ba yabo ba fallasa.

“Lafiya Kalau an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah”

Ya amsa sannan ya juya da zimmar ficewa, sai Momy tai masa tayin abun kadyawan.

“Ba zaka tsaya ka karya ba?”

Kamar zai ce a a sai kuma ya juyo.

“Idan an gama a saka min a kula zan tafi da shi”

“Okay”

Momy ta amsa sannan ta dauki abu ta shiga zuba masa dukan abubuwan da suka hada, yana ganin haka ya fice daga kitchen din, ko da ya fito Zulai ta gama mopping din sai ta bude masa kofa da sauri, ya fice yana addu'ar fita daga gida, sannan ya nufi inda Motarsa take fake, tun kamin ya karasa ya danna remote din hannunsa motar tai kara ta bude kanta daga lock. Hannunsa ya mika ya bude motar ya shiga ya zauna yana warming dinta, yana kokarin yin reverse da Motar, Mairo da fito da gudunta rike da kwadon abinci ta nufo inda yake, after yayi reverse din ta bude gidan baya ta saka masa sannan ta rufe motar tana masa addu'ar Allah ya tsare.
Kamin ya isa gate ya daga wayarsa ya kira Daddy, domin ba al'adarsa ba ce ficewa ba tare da ya gaisa da Daddy ba, sai idan Daddy na bachi ko kuma baya garin, ko kuma wani ne, shi kadai ne ke saka shi fita ba tare da yayi ido biyu da Daddy ba. Har ya hau babban titi Daddy be dauki wayar ba, as usual idan ya kira sau daya ba a dauka ba zai sake kira ba.
Sai kawai ya aje wayar ya cigaba da tukinsa, a gogon hannunsa ya duba a daidai lokacin daya faka motarsa harabar asibitin, sannan ya bude motar ya fito ya bude baya ya dauki abinci ya nufi ciki, akwai jama'a sosai a asibitin ba kamar jiya da shekaran jiya ba da suke ranakun hutu, yau kam Monday mutane sai hada hada suke, kamar bako haka ya tura kofar dakin ya shiga. Zaune ya same ta tana ta kallon kofar kamar mai jiran shigowar wani, hawaye suna mata zuba, sai da ya maida kofar ya rufe sannan ya karasa kusa da ita ya aje abinci.

“Ya jikinki?”

Sai ta juyo ta kalleshi, ta kasa amsawa.

“Ya sunanki?”

Ya tambaya yana cigaba da kallonta.

Nan ma bata ce komai ba, sai ya matsa kusa da inda aka aje file dinta ya bude yana dubawa Ramlat Ibrahim ya ga an rubuta.

“Ramlat...?”

“Aminatu...”

Ta amsa tana kallon wani wajen tare da kai hannu ta share hawayenta.

“Mamana, ba ki gajiya da kuka?”

Sai ta sake kallonsa a karo na biyu tana murmushin da ya fi kuka ciwo.

“Baka san yadda nake ji ba, yanzu ba ni da mai damuwa da ni, babu wanda ya rasa kamar yadda na rasa komai a lokaci daya, yanzu bara zan koma a titi, ina zan kwana? Me zan ci ko na ci babu ruwan kowa, ni kadai na rage.... ”

Kamar fada take maganar tana kuka mai karfi, sai kuma ta saka hannayenta ta rike kanta tana lumshe ido. Kallonta kawai Talba yake har ta fara yunkura sauka saman gadon.

“Zauna karki sauka”

Dagowa tai ta kalleshi, sai ta zauna din kamar yadda ya bukata ta rumgume kanta tana hadiyar yawun bakinta da ya bushe. Dukawa yai ya fara bude abincin yana dorawa a saman gadon da take sannan ya duba fruits din daya kawo mata jiya, domin tun jiya da ya kawo mata fruit din ya fita be sake dawowa ba.

“Baki ci komai ba?”

Ya tambaya yana kallonta. Sai ta daga masa kai.

“Ina jin yunwa amman bana iya cin komai, kuma hannuna baya kaiwa”

Be sake ce mata Uffan ba, ya bude mata abinci.

“Zaki iya cin wannan?”

Ta kalli abinci sai ta girgiza masa kai, alamar aa domin komai na duniyar baya burgerta. Zai sake yin magana likitan daya karbeta ya shigo dakin rike da takardu da wata Nurse a bayansa.

“Yauwa, daman ina son magana da kai”

Likitan ya fada sannan ya mika masa hannu suka gaisa. Sai kuma ya shiga duba Aminatu.

“Kina jin wani ciwo ne?”

“Kirjina yana ciwo sosai ksmar zai cire, kuma idanuwana ma suna ciwo suna kai kayi”

“Ki daure ki rage tunani, da yawan kuka damuwace ke saka haka, ita kuma damuwa bata da magani kamar a gusar da abun da yake rai”

Ya fada yana rika hannunta ya saka mata abun hauna bp ya aunata, bayan ya gama ya kalli Talba dake tsaye ya ce

“Tsakani da Allah yarinyar nan na bukatar kulawa, akwai maganin daya kamata ace ana shafa mata a kafa kuma ana bata lokaci zuwa lokaci, and tana yawan kuka wanda hakan yana kara mata damuwa, kamata yayi ace akwai wani abu da zai dauke mata hankali, ka ga ko shiga bandaki ya kamata ace akwai mai rikata domin jiya ma a nan tai fisari sai da aka gyara gurin, sannan tana zaman kadaici ne kawai babu kowa a tare da ita a nan”

Talba ya kalleta cike da tausayi, shi kansa ya san tana bukatar mai kula da ita, domin tufafin jikinta ma sun yi datti duk da kasancewar Ali ya saka an canja mata wasu tufafin tun a lokacin da take asibitinsa.

“And jiya ma ance bata yi bachi ba sai magana take ta yi da kanta tana kuka, be kama ace kullum sai an mata allurar bachi sannan zata iya bachi ba, domin ita kanta allurar yawan yinta yana haifar da wata cutar ta dabam”

“Ba ni da wanda zai kula da ita a yanzu gaskiya”

“Ko da a gida?”

Yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

Aminatu ta kalleshi da idanuwanta da suka sha kuka har suka canja kala.

“A yanzu ba mu da gida, idan kun gaji da ni, to ku kai ni gurin da yan gudun hijira suke zama, ko kuma gidan marayu ko gidan nakasassu, ba ni da kowa...”

Talba ya risina kusa da gadonta yana kallonta cike da tausayi.

“Ba nasasa kika yi ba, ciwo kika ji, kuma zaki warke soon ko Likita?”

Sai likitan ya daga mata kai yana murmushi.

“Bata da kowa ne?”

“I can take care of her zan kai ta gida...”

Talba ya fada, sannan ya mike tsaye.

“Okay, idan zaka kaita gida, za ta fi samun kulawa gaskiya, domin a yanzu damuwarci kawai ciwonta sai kuma kafafuwan. Amman a shawarce zai fi kyau ka

samu likitan da zai rika zuwa yana dubata, ko kuma ka rika kawota time to time asibiti ana duba kafar”

Talba ya daga masa kai alamar gamsuwa, Likitan ya kai hannunsa ya rika kan Aminatu ya bude idonta.

“Ki daina yawan kuka kina daga idonki sama saboda kar glass din idonki ya samu matsala”

Ita dai bata sake ce masa komai ba har yai abun da zai yi ya fice. Sai da ya fice sannan Talba ya zauna a saman kujerar dake facing din gadon yana kallonta.

“Ki zama mai jajircewa da hakuri, komai da kika gani na rayuwar duniya baya zuwa da sauki, kuma kowa da kalar jarabawarsa, and ina tunanin Allah ya hada ni da ke saboda na taimakeki, wata kila da dace da wani kika hadu shi ba ni ba, da yanzu wani labarin ake ba wannan ba, so ki dauki haduwa ta dake a matsayin kaddara, akwai wani karon magana da ake cewar when life gave you hundreds reasons to cry, show life you have thousand reasons to smile, ina da tabbacin zaki zama jaruma, ki hade komai ki rayu ko dan iyayenki”

“Kuka ya zame min dole baka san yadda nake ji ba, rashin iyaye yan'uwa abu ne mai matukar ciwo, lokaci daya na rasa komai”

Ajiyar zuciya ya sauke yana kallonta, hawaye nata wanke mata fuska kamar ba gobe.

“Na san yadda kike ji, ni ma maraya ne kamar ke ba uwa ba uba, banbancina da ke shine, ni ban taba kukan maraici ba, ban taba neman wani abu na rasa ba, ke ma kuma za ki samu kulawa Daga yanzu har karshen rayuwarki, kamin ki gane danginki, zan sama miki wasu dangin da zaki zauna tare da su, su rika debe miki kewa, na san ba za a rasa wani daga familynki da yake raye ba, From now on babu abun da zaki nema ki rasa Inshallah, babu abun da ya dace da ke a yanzu sai farinciki!”

Ta yi kasa da kanta tana hawaye.

“Da gaske na rasa kowa kenan! Da gaske ni kadai zan rayu? Taya farinciki zai zama a tare da ruhin da bakinciki ya zagaye, kuka da damuwa suka masa masauki? Har yanzu na kasa yarda a duniya na ke, an raba ni da kowa”

Ta fashe da sabon kuka tana jin wani irin bakinciki mai taba zuciya yana ratsata.

“Faranta ran mutane na daga cikin abun da yake saka ni farinciki, musamman irinki, ta ya mutum mai imani zai same ki a irin wannan halin kuma ya kasa taimakonki? Ki saka a ranki daman can haka Allah ya rubuta kuma akwai irinki da yawa”

Haka ya dage yana ta kokarin kwantar mata da hankali kamar na shi ba. So yake ta ji cewar ba ita kadai bace a cikin halin damuwa, so that ta kwantar da hankalinta, gudun kar abun yai mata yawa.

“Ki ci abinci yanzu sai na yi ma likitan magana, ya ba ku takardar sallama”

Wannan karon har dan guntun murmushi a fuskarsa.

“Bakina akwai datti da yawa”

Ya dan wara ido yana jin haka yasa mai tsabta ce.

“Okay bari muje gida gaba daya sai ki wanke bakinki a can ki karya”

Ta yi shiru bata ce masa komai ba, sai ya rufe abinci ya mike tsaye ya fice daga dakin. Be dade ba ya dawo rike da wata takardar sai wasu nurse biyu bayansa, su suka dauke ta suka saka ta a Wheelchair. Shi kuma ya dauki abincin kadai ba tare da ledar fruit din daya kawo ba sai kuma magani. Nurse din ce ta turo ta, shi kuma yana gaba har suka isa gurin motarsa, back seat ya bude musu suka saka ta sannan ya bude bayan motar suka saka masa wheelchair din, after ya rufe ya nufi driver seat ya bude ya shiga ya zauna.

“Yanzu zaki ga sabon gidanku da kuma yan'uwanki”

Ya fada ba tare da ya juyo ya kalleta.

“Na gode Yallabai”

Ta fada da muryar kuka, domin a yanzu ko kalma yan'uwa ta ji sai ta tuna da nata.

“Talba sunana, daga yanzu ni yayanki ne, kin zama kanwata gashi kina da sunan Momy kin zama Shalele”

Bata ce komai ba, har ya fara tukin motar ya fice daga asibitin, yana hawa babban titi ya fara gudu kamar yadda ya saba, sai jikinta ya fara rawa ta fara tsorata, abun da ya faru ya taba mata zuciya kuma ya shiga kwakwalwarta ya zauna, abu kadan sai hankalinta ya tashi.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ta furta da karfi tana runtse idonta. Hakan yasa shi juyowa ya kalleta sai ya rage gudun da yake, sai dai be ce mata komai ba, ita kuma bata yarda ta bude idon ba har suka isa gidan da bata san yadda yanayinsa da tsarinsa ba. Harabar gidan ya faka ya motarsa sannan ya fito ya dauko Wheelchair ya aje ya bude back seat din yai ma daya daga cikin mai aikinsu hannu, sai gashi ya zo da gudunsa.

“Ka dora Wheelchair din nan a kofar falo, sai ka saka yarinyar nan ciki, ka dauko abinci yana ciki Motar”

Ya fada yana kallon motar Daddy dake fake, hakan ke tabbatar da Daddy be fita ba kenan. Wayarsa ya ciro daga aljihu da zimmar kiransa sai ya hangoshi ya fito direbansa na rike da jakarsa, da sauri ya nufi inda yake Daddy na hango shi sai ya tsaya jikin motar yana jiran karasowarsa.

“Daddy good morning”

“Morning Mu'az har na fita?”

“Yeah muna da meeting a office, amman ka rasawa na dawo na fada maka wani abu”

Daddy ya masa irin kallon nan dake nuna ina saurarenka. Tun daga biri har wutsiya ya fedewa Daddy komai, ba karamin tausayin yarinyar Daddy ya ji ba.

“Yarinyar tana ina?”

“Gata acan na zo da ita, ina neman amincewarka, idan kuma hakan be maka ba, zamu iya duba wani gurin sa zamu iya ajeta, saboda gida marayunmu yawanci kanana ne ba su kai kamar ta ba, idan ma na aje ta a can zata sake shiga kadaicin ne”

Daddy yayi murmushi jindadi ya kai hannunsa ya dafa kafadar Talba.

“Ina alfaharin da kai Mu'az ka ci sunana kuma baka rago komai daga halina ba, mu gidan nan ai kullum muna marhabun da baki ne, kuma ni uban marayu ne karka manta da wannan, ko da ace tana da kowa nata a raye ta so zama da mu zan dauke ta kamar ya balle ma tana marainiya, ka yi tunani mai kyau ka ga yanzu kun zama ku biyar, Allah ya muku albarka”

Talba yayi murmushi.

“Thank you Daddy, amman Momy ba lallai ta yarda ba”

Daddy yai masa wani kallo.

“Momy ke da gida ko ni?”

“For now ita ke da gidanta...”

“Really to bari mu ga idan kai aure kai ne da gida ko matarka”

Talba yayi murmushi.

“Wannanai dabam, ni Talba ne kai kuma Daddy ne”

Daddy ya girgiza kai yana murmushi tare da zolayarsa.

“Za'a min izinin ganin yarinyar?”

Ban da dariya babu abun da Talba yake, ya wuce gaba Daddy ya biyo bayansa, sai dai hakan be hana su isa kofar falon a tare ba.

Talba ya danna door bell ba dadewa aka bude masa sai ya matsa Daddy ya fara wuce sannan shi ma ya shiga. A tsakiyar falon ya hango Aminatu zaune a wheelchair ta sanda kanta kasa hawaye na sauko mata, Kabir na tsaye gabanta. Momy kuma na zaune a kujera daya ita da Leila suna kallon ikon Allah.

“Ita wannan bata magana ne?”

Kabir ya tambaya yana kallon Talba.

“Ka dame ta da surutun ne ko?”

Cewar Daddy. Sai Kabir ya ce.

“Sunanta kawai na tambaya, sai ta rufe ido ta fara min kuka”

Daddy ya karasa kusa da ita yana kallonta cike da tausayawa.

“Sannu Allah ya baki lafiya”

Bata bude idon ba har sai da ta ji kamshin turaren Talba, sannan ta bude ido ta kalli inda take jin kamshin na fitowa, ido biyu suka yi sai dai nata idon cike suke da hawaye.

“Ya sunanta?”

“Sunan Momy”

Talba ya fada, sai Daddy yai murmushi ya kalleta.

“Yar gata ce kenan, sunan matata kuma uwar yayana kin ga babu wanda zai taba ki a gidan nan! Ki kwantar da hankalinki ki dauki kowa kamar dan'uwanki ni kuma na miki alkawarin zama mahaifinki da yarda Allah, duk abun da zan iya yi ma yayana zan miki Inshallah”

Talba yayi murmushi, sai Kabir ya wara ido.

“Ji wannan daga zuwanki zaki karbe mana fada, bari fitinanniyar ta zo zata zalzaleki”

Daddy ya girgiza kai yana dariya.

“Aa yanzu ita ce auta, daga gani Amal zata girme ta ai”

Ya fada sannan ya dago ya kalli Momy.

“Hajiya karaso ki ga yar da muka samu kyauta daga Allah”

Momy ta taso daga inda take zaune tare da Leila suka karaso inda Aminatu, sai da Momy ta kare mata kallo sannan ta ce.

“Ya kamata a nemi izini na kamin a kawo ta, amman sai ganin musaka nai a falona, saboda ban isa da gidan ba”

“Na fara magana da Daddy ne, kamin na yi magana da ke, ni ma ban yi zaton hakan zai faru ba sai da likitan ya fada min sai na ga kamar hakan ya dace”

“To be dace ba, be kamata ka dauko min wata bare can ka kawo min a gida ba, yarinyar da ban san daga inda ta fito ba”

A hankali Aminatu ta dago ta kalleta sai ta maida kanta kasa.

“Momy karki tsorata mana, ba nan ya kamata ku yi wannan maganar ba”

Kabir ya fada. Sai Momy ta watsa masa harara.

“Idan na tsoratata sai ka saka zane ka goya ta ai”

Daddy ya hade rai yana kallon Momy cikin rashin jindadi.

“Bana son maganar nan, Danki zai fada miki komai”

Sannan ya kalli Aminatu dake hawaye.

“Aminatu ki kwantar da hankalinki kin ji, mu iyayenki ne”

Ta kasa dagowa ta kalleshi ma balle ta ce masa komai, har sai da Talba ya kirata da sunan da Inna take kiranta da shi.

“Auta...”

Sai ta kalleshi da sauri tana jin wani tsam a jikinta.

“Ki cewa Daddy kin gode”

Ya fada yana mata murmushi kadan kamar na dole. Sai ta kalli Daddy da idanuwanta da ke zubar da hawaye.

“Na gode...!”

“Oh Really.. Zai ka mata umarni zata yi magana kenan”

Kabir ya fada yana kallon Talba, murmushi kawai Daddy yai ya nufi kofar fita.

“Zan tafi kar na yi latti, sai a gyara mana daya daga cikin dakunan da suke kasa nan”

“Da a BQ na so ta zauna”

Talba ya fada.

“Why BQ ga dakuna a cikin gida? A bar ta nan BQ ai na amsu aiki ne, sai na dawo”

A karon farko Momy ta kasa ce masa Allah ya tsare balle har tai masa rakiya. Bayan Daddy ya fice Talba ya risina gabanta ya nuna mata Leila.

“Sunan wannan Leila kanwata ce, kuma matar da zan aura, akwai wata Amal tana makaranta, wacan kuma Momy mahaifiyarmu, muna da masu aiki biyu Mairo da Zulai idan kina bukatar wani abu ki fada musu za su miki. Wannan kuma Kabir, shine likitan da zai rika dubaki shi ma kuma kanena ne”

Talba na ajewa Kabir ya tari numfashinsa.

“No no no Malam shekara biyu ka bani ba, sai wani ji kake da kanka wai kanenka kar ta dauka da gaske”

Talba be ce komai ba, daman ba komai yake saka shi dariya ko magana ba, sai ya kalli Momy.

“Momy ina son zamu yi magana”

Momy ta dauke kai daga kallon Aminatu ta kalli Talba tana jin wani irin zafi a zuciyarta.

“Har a bada dan wani br taba zama nawa ba, nawa kuma be taba zama dan kowa ba”

Kusan wannan ne karo na biyu da wata kalmar ta fito daga bakin Momy da bata masa dadi ba, bayan wacan karo da shigarwa Leila.

“Momy yarinyar nan marainiya ce, ba uwa ba uba, kuma ban daukota na kawo ta nan ba sai dan nasan zamu iya kula da ita, kuma kin san muhimmanci rikon maraya, and ko dan ni ya kamata ki daga mata kafa...”

“Saboda gaka Ubana? Ko kuma saboda mu muka fi kowa son lada? Waya sani ko karya ta tsara maka? Idan ma da gaske ne mu muka kashe iyayenta ne da responsible din ta zai dawo kanmu?”

Da mugun mamaki Talba yake kallonta jin irin kalaman dake fitowa daga bakinta, sai dai be ce mata komai ya kalli Aminatu ya dauke kai ya kalli Kabir da yanayinsa ke nuna be jidadin kalaman Momy ba.

“Kabir kira Mairo”

Momy ta ja tsaki ta nufi upstairs ta bar Leila tsaye tana kallon ikon Allah.

“Mairo...”

Kabir ya kwala mata kira, ya san daga muryar ne ba zai iya ba shiyasa ya saka shi kiranta ba wai dan yana nufin ya tafi yaje ya kirata ba. Da gudu Mairon ta fito daga kitchen hannunta da kumfa.

“Gani ranka ya dade”

“A wanke mata baki, a bata abun karyawa, sannan a gyara mata dakin kasa, ki taimaka mata tai wanka sai dai kafarta na ciwo sai kin yi a hankali”

“To ranka ya dade”

Ta amsa da sauri, shi kuma ya juya ya fice daga falon ya bar Aminatu sai Kabir da Leila.

“Let me help you with brush and toothpaste”

Kabir ya fada sannan ya juya ya nufi upstairs. Leila ta bishi da kallo sai da ya haye gaba daya sannan ta kalli Mairo tana yamutsa fuska.

“Idan kika mata wanka, sai Momy ta ci ubanki”

Mairo ta kalleta da duba na rashin jindadi.

“Haba Leila kina ganina kin san na yi kanwa ta uku da ke, be kamata ki ce min haka ba, ko da kuwa kin san Hajiya zata yi fada ne, amman be dace ki zage ni ba”

“Okay miya dace na fada miki? Ki zo aiki gidanmu sannan ki yi tunanin zan girmamaki? Koya min magana zaki yi ko mai”

Yanayin yadda Leila ta rufe Mairo da masifa ne ya saka jikin Aminatu rawa, sai ta fashe da kuka.

“Mtssss munafuskar banza”

Leila ta fada tana hararar Aminatu, sannan ta nufi kofar baya ta falon tana danna waya.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

BATURIYA POV.

Sai da Ramlee ta shiga da ita har cikin falon sannan ta fita ta barta. Baturiya ta dade a falon sannan ta ji tsayarwar Mota harabar gidan, sai ta leka ta window ta hangoshi ya fito daga motar rike da wata karamar jaka, dayan hannunsa kuma rike da Makalle da waya a kunne. Babban mutum ne a haife ya haife ta kuma ya haifi yayunta, irin mazan nan ne da ake kira da sugar daddy.
Wani irin faduwa ta ji gabanta yayi, sai hakan be hanata daidaita natsuwarta, Ta gyara zamanta sannan ta kunna wayarta ta saka ta silent, gabanta ya tsanata bugawa ne a lokacin daya turo kofar falon ya shigo, abun ka da wanda be saba ba sai ta mike tsaye tana kallonsa, shi kuma ya kare mata kallon tun daga sama har kasa sannan yai mata alama data zauna, sai ta koma ta zauna tana kirkiro murmushi, a kujera dake kusa da kofar ya aje jakar hannunsa sannan ya karasa kusa da ita yana murmushi ya zauna. Ita ma murmushin ta sakar masa, sai ya kai hannu ya shafa fuskarta ya nuna mata fuskarsa alamar tai masa kiss, ba

musu ta mika bakinta ta sumbanci gafen fuskarsa sai ya rumgumeta yana shafa bayanta.

“Yanzu dai Hajiya ki bari idan na dawo gida hankali kwance sai mu yi maganar, kisan Muhammad baya jin maganar kowa a yanzu so dole lallabashi za ku yi, idan yaji yana son ta ya amince daman abun da muke nema ne tun da yar'uwarsa ce, idan kuma yace sai wacan sai mu masa addu'a”

Ya fada yana gangarowa da hannunsa ya cire mata zip din atamfar ya fara murza fatarta ta baya dake cike da taushi da fari.

“Yanzu muna da meeting, idan mun gama kuma zan je na ga gwana saboda maganar kudin kwangilar nan, ba zan dawo da wuri ba sai dare”

Baturiya ta yi shiru tana sauraren yadda hannunsa ke ta yawo a jikinta, Sai wani abu take ji na rashin jindadi, ta saba mu'amala da Faruq balle tace ko dan bata saba bane, wata kila kuma saboda wannan sabo ne tsabanin wacan da take samu lada.

“Eh ya same ni da maganar ai, shiyasa muka taho tare sai kuma na buge wani mai acha, sun tafi da shi su kai shi asibiti, idan ya dawo nace ya same ni a gida mu yi maganar, so zamu zauna gani ga ki gashi sai mu yi maganar, sai anjima”

Ya kashe wayar gaba daya yana kallon Baturiya.

“Yan mata ya kike?”

“Lafiya kalau ya aikin?”

Ta amsa cikin rashin sakewa, shi kam sai murmushi yake abun nema ya samu.

“Alhamdulillah”

Ya fada yana kokarin cire mata dankwalin kanta gaba daya, ya fara shafa gashin kanta, sannan ya kamo hannunta ya saka a kirjinsa.

“Ba za a taya ni cire tufafin ba agajiye nake fa”

Sai da ta hade yawun bakinta sannan ta rika babbar rigarsa ta cire masa, da haka wasan ya canja salo, sai dai duk inda ya taba a jikinta sai ta ji wani iri musamman ma daya raba ta da rigar jikinta yana shafa kirjinta.

“Taso mu watsa ruwa yadda zamu jidadin bachi”

Ta dan yi murmushi ta mike tsaye, sai ya rika hannunta suka bathroom dinsa, a tare sukai wankan, yana ta labarta mata karamar haukar data same shi a lokacin da Ramlee take nuja masa honta a wayarta. Bayan sun gama suka fito sai kallon tsiraicin yake yana yabawa, tare da kai hannu ya taba inda yake jin ya masa. Kusan duk abun da Ramlee ta karantar da ita sai da ta aikata masa har abun da bata taba yi ma Faruq ba da sunan ya samu gamsuwa sai da tai ma Alhaji Haroon, sannan ta biyewa son zuciyarta ta budewa kanta babban file daga cikin manyan manyan files din zunubai. Ba shi ba ita kanta kanta ta samu gamsu irin wanda bata taba samu ba, sakamakon kayan matan da Ramlee ta bata ta sha, balle kuma shi da yai kamar zai haukace.

Nan da nan bachi yai gaba da shi, ita kuma ta tashi zaune ta daura tawul ta fito falo inda ta bar wayarta ta dauka tana dubawa sai ta samu miss calls biyu daga Fahat, jiki na rawa ta mayar masa da kiran daman can yana cikin ranta tun da ta shigo gidan take jiran kiransa. Ringing daya yai picking

“Na yi fushi yau duk ban ji muryarki ba kuma na kira wayarki na ji ta a kashe, na sake kira baki daga ba”

“Bana kusa da wayar ne, kasan idan ina kusa da wayar babu abun da zai hana ni dagawa, ni ma ai tun dazun nake ta jiran kiranka”

“Miyasa baki kira ni ba? Anyway yanzu dai bari na miki wani albishir na yi magana da Daddy, na fada masa cewar na samu mata”

Hannu ta saka ta dafe kirjinta, farinciki da faduwar gaba suka zo mata a lokaci daya.

“Da gaske? Amman me ya ce maka?”

“Me zai ce min kuwa, daman ai sun dade suna jiran ranar da zan fada musu na samu wanda nake so, even though akwai yan'uwa da ake son hada ni da su, amman ni bana son auren zumunci gaskiya”

“Allah yasa ya amince dai”

“Zai amince ma, fatar ba zan samu matsala daga bangarenki ba”

“Aa babu wata matsala Inshallahu”

“Haka nake son ji, ya kike?”

“Lafiya kalau, kai fa?”

“Ni ma kalau nake”

Sama sama take amsa masa duk wata magana da yake mata saboda bata son Alhaji Haroon ya ji tana waya da wani, ko da be nuna mata baya so ba ta san be dace tan a guest house dinta tai haka ba, domin maza suna da kishi no matter how old and young they are.
Bayan sun yi sallama ta kashe wayar ta koma cikin dakin ta hau gadon ta kwanta, ba jimawa bachi yai gaba da ita. Sai da aka yi sallah azabar suka farka kowanensu ya gabatar da wanka sannan suka yi sallah.

“Baby Fee'at me zaki ci na aika yarona ya siyo mana?”

“Shimkafa jalof”

“An gama gimbiyar mata”

Ya fada har wani kashe ido yake, ita kuma tai murmushi, tana sauraren wayar daya dauka ya kira yaronsa fada masa abun da suke bukata. Yana aje wayar ya mika mata hannunsa.

“Ta so zo nan”

Babu kunya balle tsoron Allah haka ta sake zuwa ta biye masa suka sake tarawa kansu wani babban zunubin, suna gamawa yaronsa ya kira wayarsa ya fada masa ya siyo.

“Ka aje a falo”

Ya fada masa sannan ya aje wayar ya tashi ya fita, ko da ya fito yaron ya aje abinci yayi ficewarsa, daukowa kawai yai ya shigo da shi ciki.
Jalof kawai ta bukata amman ya hado mata da farfesun kayan ciki da naman kai, ga kuma lemu mai sanyi da soyayyen naman kaza, zaunawa tai ta ci ta koshi nas, sannan ta tashi tana jindadi, rabon da ta ci abincin hotel har ta manta.
Bandaki ta shiga ta sake yin wanka ta fito, sai ya kalleta da mamaki.

“Wanka kika yi? Ai bamu gama ba, ni fa wuni ake min ba zaki koma gida ba sai dare, Ramlee bata fada miki ba”

“Aa bata fada min ba, amman tun kai ka fada min ai ya wadatar”

Murmushi yai ya bude nasa abinci ya fara ci yana yaba yadda ya sake me, da kuma irin gamsuwar daya samuna jikinta, ba karamin dadi ta ji ba domin Faruq ba mutum ne mai yaba mata ba idan ma ta gyara masa shimfidar, baya daga cikin mazan nan dake nuna jindadinsu a gurin matansu, ba dan komai ba sai dai be dauki yabon a bakin komai ba.

Kamar yadda ya bukata haka ta biyewa sharholiyarsa suka wuni suna raya sabo, sai bayan sallah Magariba ya rabu da ita tai wanka ta shirya cikin tufafinta, tana kokarin daura dankwalinta ta dauko jakarsa ya bude ya kirga dubu dari hudu ya aje mata.

“Ga wannan, sai kuma yaushe?”

Juyowa tai ta kalli kudin, a take gabanta yai mugun faduwa, sai dai bata yarda ta nuna matsa yawan kudin sun tsoratata ba sai tai murmushi.

“Sai kuma ranar daka tashi Alhajina”

“Ni kullum ai ban ki mun hadu ba, idan son samu ne ma tafiyar nan da zan yi China naje dake, kin taba zuwa china?”

“Aa Wallahi”

“To ki shirya dake zamu je”

Ta yi murmushi tana jin wani kalar dadi ya sakota gaba, duk kuwa da bata da tabbacin zata amince ta bishi din ko kuma aa, saboda aure da kuma Fahat. Wayarsa ya mika mata..

“Saka min number ki a nan, ya kamata ace muna da number juna, ba dole sai mun biyo ta bangaren Ramlee ba”

Ta karbi wayar ta saka masa number, sannan ta dauki kudin ta saka a jakarta ta fito falo ta dauki wayarta ta saka mayafinta tai masa sallama ta fice tana

mamakin yawan kudin daya bata, wannan karom bata yi shakkar saka gyaren ba saboda dare ne kuma a yanzu bata da kwaliya kamar dazun.

FARUQ POV.

Sai da ya fara biyawa gurin Mama ya gaisheta suka dan taba hira sannan ya kama hanyar zuwa shagonsa. Ba su karasa ba wani mai mota ya bugu babur din da yake kai, shi da mai achaban suka fadi gefen titi. A take mutane suka yo kansu da gudu mutumen daya buge su ma faka motarsa yai gefe ya fito yana dubasu. Kana ganinsa ka san babban mutum ne, domin shaddar jikinsa ma kadai abun kallo ce balle kuma bakar motar data buge su, a tare da shi a akwai direba sai kuma wata jar mota dake bayan tasa da alama take masa baya take ko kuma a tare suke. Daga mai achaban har Faruq daya ji ciwo a kafa zaune sukai mutane na musu sannu.

“Akwai asibiti nan kusa?”

Mutumen ya fada yana kallon direbansa, sai saurayin dake tsaye kusa da shi ya amsa masa.

“No Abba ba kace kana uzuri ba, ka tafi kawai ni ni zan kai su”

“Okay Muhammad idan an dubasu ka samu abun aka basu, idan mun hadu gida anjima zamu yi magana, yanzu jirana ake”

“Okay”

Dan nasa ya amsa sannan ya rika Faruq da yafi jin ciwo ya mikar da shi tsaye.

“Muje ga motana can”

Ya nuna masa jar motar da take bayan ta mahaifinsa, kamin su karasa gurin motar har mahaifinsa ya shiga tashi motar direban yaja motar sun kama hanya. A front seat ya zaunar da Faruq sannan ya bude back seat din ya ce da mai achaban ya shiga.

“Aa kaje ka kai shi, ni ban ji ciwo ba”

“Ka tabbata?”

“Inshallah”

Sai ya rufe motar ya rufe inda Faruq yake zaune, ya zagaya mazaunin direba ya kirga dubu biyar ya mikawa mai achaban, sai ya karba yana godiya daman haka tafi masa dadi. Ya hau achabansa ya kama hanya shi kuma ya shiga motar yaja Faruq suka isa asibiti.

“Sannu ko kana da asibitin da kake zuwa?”

“Aa”

“Okay bari muje ta nan kusa, ai zaka iya jurewa ko?”

“Haba sai kace ba namiji ba”

Faruq ya fada yana murmushi, shi ma murmushin yai ya cigaba da tukin har suka isa asibitin, aka duba kafar aka bashi magani suka rufe ciwon. Sannan ya sake daukoshi a motarsa suka suka nufo unguwarsu, suna tafe suka hira kamar daman can sun saba, be yarda ya bar Faruq a bakin titin ba duk kuwa da kasancewar mota bata shiga har kofar gidansu, sai ya fito ya taka masa har kofar gidan yana masa wasa wai kar madan tace sun buge mata miji, Faruq murmushi kawai yai ya kai hannu ya taba gidan sai ya ji shi a rufe, key dinsa ya dauko ya bude ya shiga ciki.

“Ina jin bata nan, daman tace min tana da biki zata je”

Fada a kokarinsa na kare matarsa duk da kasancewar mutumen be san Rafi'a balle har ya munana mata zato.

“To a gaishe ta, kuma a bata hakuri ga kuma wannan ayi cefane”

Ya fada yana mikawa Faruq dubu goma.

“Aa haba ai abu ne da Allah ya kawo...”

Kamin Faruq ya karasa Mutumen ya saka rantsuwa.

“Wallahi sai ka karba, kai shedan kadai ke maida kyauta”

Murmushi Faruq yai a karo na barkatai ya karbi kudin yana masa godiya.

“Na manta ban tambayi sunanka ba”

“Faruq”

“Ni kuma Muhammad Fahat na gode sosai Allah ya tsare gaba”

“Ameen”

Daga haka Faruq ya karaso cikin gidan shi kuma ya juya ya kama hanyarsa. A falo Faruq ya zauna yana kiran Baturiya a waya domin jin inda take, sai dai bata dauka ba daga baya ma sai yaji wayar a kashe, hakan kuma ba karamin bata masa rai yai ba, ba yau ta saba fita ba tare da izininsa ba sai dai ya fi jin zafin fitarta fiye da koyaushe. Cikin karfin hali ya shiga uwar daka ya tube tufafin jikinsa yai wanka ya canja wasu kayan sannan ya kwanta, nan da nan bachi yai gaba da shi. Kiran Allah azahar ne ya tashe shi, ya tashi yai alwala ya fita masallaci a can ya hadu da dansa da yabi yaran makotansu suka tafi masallacin a tare. Kusan kowa da ya gaisa da shi sai ya masa sannu da fatar Allah ya tsare gaba, shi kuma ya amsa da Ameen bayan ya labarta musu abun da ya faru.

Sultan na ganin mahaifinsa ya rike shi suka dawo gida tare. Abun ka yaro yana shigowa ya fara tambayar Faruq ina mamansa.

“Dady Momy bata dawo ba?”

“Ina ta tafi?”

“Bata fada min ba, amman na ji tana ta waya da yawa tana ta waya har ta ce ummouy”

Ya nuna yadda tai kiss din da bakinsa. Faruq ya hade yawu yana jin wani bakinciki na taso masa. Haka ya wuni a gidan

daga shi sai dansa girkin rana ma shi ya girka duk da kasancewar akwai ciwo a kafarsa, tun yana tunanin zata dawo da la'asar bata dawo gidan ba sai bayan magariba ana daf da kiran sallah isha'i wani gurin ma har an fara kiran. Sannan ta shigo da dan faduwar gaba, ganin cewar Faruq ya rigata dawowa, ta shigo falon da sallama, ya amsa mata ya mike ya fice ya bar mata falon, sai ta bishi da kallo kamin ta kalli danta.

“Sultan yaushe Dadynka ya dawo?”

“Tun da rana har ma ya ji ciwo a kafarsa”

Bata sake cewa komai ba ta nufi dakinta ta aje jakarta a inda ta saba ajewa sannan ta fita tsakar gidan da saurinta saboda kashi ya matseta. Ko da ta fito ta dauki buta ta shiga bandakin yana tsakar gidan yana alwala, bayan ta shiga bandaki ya shigo falo daga inda yake tsaye ya hango Sultan na ciro kudi mai yawa a jakar Baturiya, da sauri ya karasa ya kara bude jakar da kansa yana duba kudin. Bandir din yan dubu daya ne har guda hudu sai kuma karamin canji dake kasan kudi.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ya furta cikin wani irin yanayi na tsoro da bakinciki. Kamar an dasashi haka yai tsaye a gurin har ta fito daga bandakin ta shigo dakin, tana ganinsa tsaye kusa da jakarta sai ta yi tsaye a bakin kofar tana kallonsa. Tsayin da tai ya bashi damar kare mata kallo, lace din dake jikinta tsadadden lace ne da karfinsa be kai ya siya mata shi ba, sai dai ba zai munana mata zato ba saboda tana da yayyun dake auren masu rufin kudi, sai dai bata saka irin wannan tufafin sai zata je guri na musamman.

“Ina kika samu wannan kudi?”

“Ajiya aka ba ni”

Ta amsa kai tsaye kamar da gaske, sai ya watsar da kudin ya daka mata tsawa.

“Karki raina min hankali mana, wa ye zai baki ajiyar kudi mai yawa haka? Ina kika je?”

“Gida gurin Umma”

Ta amsa tana hade fuska.

“Rafi'a kin wuce gona da iri, ban taba tunani zaki iya aikata abun da kika aikata ba, kuma abun bakinciki da jinani a jikinki”

“Faruq.. Zarkina kake yi kuma? Zargi fa yana kashe aure”

“Waya baki ajiyar wannan kudin?”

“Ba zan fada ba, tun da zargina kake ai sai ka cigaba kuma Allah sai ya saka min, ka cutar da ni kuma yanzu ka fara bina da kazafin zina”

Ta fashe da kuka.

“Juya ki koma inda kika fito

Ya fada yana nuna mata kofa.

“Wallahi ba inda zan je sai idan sakina kai”

“Tafi na sake ki saki daya, kuma duk kika cutar min da yaya Allah ya isa tsakanina da ke”

Ta dora hannu biyu akai tana zaro ido kamar za su fado.

“Faruq ka sake ni fa kace...?”

Be bi ta kanta ba ya rika hannunsa dansa ya ratsa gefenta suka fice a fusace zuciyarsa na masa zafi.
Zaune tai a bakin kofar dakin tana kallon kudin, ba kuka take ba, bata jin ma kuka ko bakinciki yana kusa da ita, farinciki kudi data samu sai ya koma mata ciki.

AMINATU POV.

A tsakar falon aka barta babu wanda ya sake bi ta kanta Mairo ta koma kitchen bayan ta karbi brush din da Kabir ya kawo mata ya fice, Leila kuma ta haye sama ta shige dakinta ya sauki wayarta ta kira Madina ta labarta mata abun da ya faru.

“Leila wata mace da ba yar kowa ba, ba zata taba samun gurbi a zuciyar Talba ba, saboda yana ji da kansa sosai ba zai yarda ya auri wanda ba yar kowa ba, balle kuma yar gudun hijira”

“Ni ma ai ban ce sonta yake ba na san ai ba zai taba sonta ba, amman ina jin zafin abun da yake mata, taya zaka tsinci yarinyar ka kawota gidanku shi yafi kowa tausayi ne”

“Yanzu yarinyar tana nan gidanku?”

“Eh, tana nan yace Mairo tai mata wanka ta bata abinci ni kuma na hana, kuma ko ban hana ba Momy ma b zata bari tai ba”

“Gani nan zuwa yanzu, zan zo na ganta”

“Okay”

Ta kashe wayarsa sannan ta kira Ali tana fada masa abun da ya faru.

Ba'ayi minti talatin ba, Madina ta iso gida, tana faka motarta ta nufo entrance din da saurita, kamin a bude mata kofar ta danna door bell din kusa sau uku, sannan Zulai ta bude mata.

“Sannu da zuwa”

“Yauwa sannu da gida, ina Momy?”

“Tana sama”

Ta shigo cikin falon tana rabon ido, sai ta hango Aminatu zaune a wheelchair kanta a kasa, karasa tai kusa da ita ta duka tana kallon fuskarta, wannan karon ba kuka take ba sai dai idonta a rufe yake ba kuma bachi take ba.

“Hey...”

Madina ta fada, sai Aminatu ta bude idonta a hankali ta kalli Madina. Sai Madina ta sakar mata murmushi.

“Sannu Sunana Madina ke fa?”

Aminatu ta maida idon ta rufe. Sai Madina ta mike tsaye ta kalli Zulai.

“Ina Mairo?”

“Tana kitchen Mairo”

Ta karasa tana kwala mata kira. Sai ta fito tana amsawa. Sai da suka gaisa da Madina sannan tace.

“Ba a mata wankan ba?”

“Leila tace kar na yi, har buroshin da Kabir ya bani ban mata ba”

Madina ta yi murmushi.

“Amman Mairo baki san waye Talba ba, da zai baki umarni ki bini ki bi na Leila, ina brush din?”

“Na aje shi a dakin da daya ce a ware mata?”

“Wane daki?”

Mairo ta nuna mata hanyar corridor dake kasa inda dakunan uku suke.

“Na farkon”

Zagayawa Madina tai ta fara tura wheelchair din, ta nufi corridor da ita, suna isa ta tura kofar dakin ta sannan ta sake turata suka shiga ciki. Bandaki ta nufa da ita ta kunna fanfo ta zuba makilin din ta a brush ta cire karamin gyarenta ta aje gefe tare da jakarta ta fara wanke mata baki, bayan ta gama ta taimaka mata ta cire tufafin jikinta ta daura mata tawul ta murza nata inda zata iya a jikinta ta bar mata ragowar ta karasa wankewa sannan ta dauraye mata jikinta. Ba tare data raba ta tawul din dake jikinta ba, bayan sun gama ta fito da ita, sannan ta fita

dakin ta nufi kitchen abun da ya rage na safe ta dauko ta dawo da shi dakin ta dora saman karamin gadon ta fara bata.

“Zan iya ci da kaina”

Aminatu ta fada ganin tana kokarin kai mata abincin a baki, sai ta girgiza mata kai tana murmushi.

“No bari na baki da kaina”

Ta shiga bata abincin a hankali, kamar daga sama Talba ya shigo dakin Zulai na biye da shi rike da jakar Candy Collection, tsaye yai bakin kofar yana kallon Aminatu dake kan Wheelchair Madina kuma na zaune a bakin gado suna facing din juna tana bata abinci ga tawul din jikinta a tsike, wani irin dadi ne ya lullube Madina daman abun da take nema kenan Talba ya shigo ya sameta tana aikin da bana Allah ba.

Khadeeja Candy

Ko kin san kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin sa kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya domin siye ko sari ku tuntu Ramla incense ta wannan number +234 703 839 2576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Dan girman Zatin Allah karki karanta idan baki biya ba. Masu sharing Allah yai muku yadda kuke min! Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Ta yi saurin aje abincin ta mike tsaye tana kallon Talba.

“Sannu da zuwa”

Aminatu ta juya a hankali ta kalleshi, sannan ta kalli Madina, yadda ta ga yanayinta ya sauya tana kokarin shiga natsuwarta kadai ya isa ya saka ta fahimci cewar Madina tana tsoro Talba sosai. Shigowa yai cikin dakin fuska babu

annuri, ba dan komai ba sai dan ya san irin amintar dake tsakaninta da Leila. Juyawa yai ya kalli Zulai.

“Ba na ce Mairo tai mata wanka ba?”

“Eh ranka ya dade, Leila ce ta hana ta”

A take yaji ransa ta bace domin ya tsani ya saka mutum wani abu be yi ba, musamman ma ace wani ya hana shi, wanin ma wanda shi ma zai iya controlling dinsa kamar dai yadda Leila tai.

“Ya kai tawul din jikinta ya ke da ruwa?”

Ya tambaya yana kallon Madina.

“Na taya ta wanka ne, to bata yarda ta cire tawul din ba shi yasa ya jike, kuma bata da wani tufafin da za a canja mata, kuma a san idan na tambayi Leila ba lallai ne ta bata ba”

Talba ya kalli Aminatu sai kuma ya sake kallonta.

“Waya ce ki mata wanka?”

“Babu, ko da na shigo tana falo ne, sai na tambaya Mairo ta fada abun da ya faru, sai na yanke shawarar taimaka mata, amman ka yi hakuri idan hakan ya bata maka rai ba zan sake ba”

Ta karasa tana risinawa a gabansa kanta a kasa, kamar wanda take a gaban sarki tana neman yafiya. Da hannu Talba yai mata alama data tashi tsaye, sai ta mike tsaye.

“Zan iya cigaba da bata abinci?”

Ta tambaya cike da ladabi kamar mai tsoronsa, Talba ya kalleta da duba na mamaki irin da gaske? Kamin ya kalli Aminatu da idonta ya cika da kwalla tana girgiza masa kai.

“No”

Ya amsa mata still yana kallon Aminatu. Kamin ya juya gurin Zulai.

“Aje tufafin a can, ki taimaka mata ta saka”

Da sauri Aminatu ta sake girgiza kai hawaye na sauko mata. Hakan ya saka Talba yai saurin dakatar da Zulai dake kokarin bude kayan.

“Bar shi kawai tafiyarki”

“To ranka ya dade”

Ta amsa sannan ta fice da sauri, kana ya kalli Madina dake tsaye tana kallonsu.

“Excuse me”

Murmushi ta sakar masa alamar okay sannan ta fice da saurinta. Sai Talba ya karaso gurin Aminatu.

“Idan kina son wani abu, ko kuma baki bukatar wani abun, ba sai kin yi kuka ba zaki iya yin magana ko ki yi alama da hannu ko da ido ko da kai, ba wai kullum ki yi ta kuka ba”

Ta saka hannu ta share hawayenta.

“Ki ce to zan yi haka”

Ta maimaita abun da ya bukata da muryar kasa kasa kamar mai rada, hakan yasa shi risinawa ya kai kunnensa kusa da bakinta.

“Fadi na ji”

Ta sake maimaitawa saitin kunnensa.

“Good, ki dai kuka ba komai ake yi ma kuka ba”

“Ni ma ji nake kuka ya zo min”

Ta fada a nan sai da ya sake kai kunnensa sannan ya ji abun da ta fada.

“Okay na fahimta, yawan kuka zai iya zame miki matsala ne shiyasa, zaki iya canja tufafin da kanki?”

Ta daga masa kai.

“Okay ki duba tufafin da kike so sai ki canja”

Nan a kan ta daga masa. Sannan ya mike tsaye ya fice daga dakin yaja mata kofa, hannu ta kai ta dauki jakar ta bude ledar sama ta fara daukowa ta budewa sai tai arba da doguwar rigar abaya ash color, warware rigar tai ta soma sakawa daga zaunen da take, sannan ta cire tawul din ta aje a gefe ta daga kadan ta ja rigar zuwa kasa. ta daura mayafin ayabar a kanta sannan ta maida hankalinta gurin kofar tana sauraren shigowar wani, kusan kamar ta yi sara akan gaba ne, domin a tsakanin lurawa kofar ido da kuma kwankwasa kofar da akai ba zaka iya fadar wanda ya riga wani ba. A hankali ya turo kofar dakin ya shigo idonsa a rufe alamar ba kallonta yake ba, domin bashi da tabbacin ta gama kintsawar ko akasin haka, duk da kasancewar ya bata mintuna daya kamata ace ta gama, ba kuma zai iya kiranta daga can wajen kofar ba ya tambaya idan ta gama.

“Na gama”

Ta fada kamar ta san manufarsa, sai ya bude idon ya sauke su akanta.

“Ki karasa cin abincin, Zulai zata fitar da ke waje ki sha iska, ni zan tafi gurin aiki”

Ta gyada masa kai, sai ya juya ya fice, ido kawai ta kurawa abinci ta kasa kai hannu ta dauka balle ta ci, ko dazun ma saboda yunwa ta matsa mata ne kuma Madina ta dage sai ta bata abincin.

Ko da ya fito falon Madina na zaune a kan sofa, Leila kuma na saukowa downstairs. Kallo daya yai mata ya dauke kai ya maida gurin Zulai.

“Idan ta gama cin abincin ki fito da ita ta sha iska”

“To ranka ya dade”

“Mairo da Zulai ni suke yi ma aiki, idan kana son a kula maka da wacan kazamar sai ka dauki mai aiki”

Ya juyo ya kalli Momy dake tsaye dinning tana maganar, sai dai be ce uffan ya sa kai ya fice. Madina ta bishi da kallo cikin rashin jindadin furucin Momy, sannan ta kalli Leila.

“Yar gari”

“Kin ga abun mamaki a gidanmu ko?, gaba daya gidan nan neman hargitsewa yake”

Madina ta kama hannu Leila ta zaunar da ita kusa da ita tare da rage murya.

“Kina daina bari Momy tana ma Talba fada ko nuna be isa akan abu ba a gaban yan aiki, saboda kar su raina shi, ke ma kuma ki daina pls?”

“Raini kuma na nawa? Ai ni na dade da raina wayonsa Wallahi, duk yadda yake ji da kansa yana wani mazurai ace zai dauko wata ya kawo a gidan nan har yana mata yar muryar mtsss”

Ta karasa tana jan tsaki, sai Madina ta yi murmushi.

“Leila kenan ba zaki gane ba, idan kan son mutum, lallaba shi kake kana nuna masa kauna, musamman Talba daya zama watsentsen mutum, yadda ya dauko yarinyar nan ya kawo sai ki nuna masa kin fi shi sonta, idan Momy tai masa abu ki nuna kin fi jin zafin abun...”

“Uhmmm Madina kamar baki san wacece ni ba, kina tunanin zan iya wannan bautar? Ai ko aurensa nake sai ni na juya shi ba wai shi ya juya ji baki daina fada min magana kamar kin fini wayo”

Madina ta sake yin murmushi a karo na biyu tana kallon Leila.

“Ai na fiki wayo! Kuma very soon zan baki mamaki, ina fada miki gaskiya saboda baki da kawa kamar ni, nima kuma bani da kawa kamar ke, amman ba zan haramtawa kaina abun da Allah ya halattamin ba, kuma ba zan zabi cutar da zuciyata akan abun da nake ganinsa magani a gareta ba, ni da ke yake ne muke tsakanin zuciya da zuciya waye zai ci nasara? Allah shi ya bar wa kansa sani”

Leila ta yi mata kallon rashin fahimta.

“Ban gane ba?”

“Ina yakar zuciyata ne ta fada miki gaskiya kuma ta nuna miki ita, ke kuma kina yakar zuciyarki ki hana ta daukar gaskiya”

Ta karasa tana mikewa tsaye tare da daukar jakarta ta rataya.

“Baki shiga kin ga yarinyar ba”

Har ta yi kamar tace mata ai na ganta, sai kuma wata zuciyar ta hana ta, domin ko da suka sauko sun same ta zaune, babu wanda yaga shigarta ko fitowarsa a dakin.

“Okay muje na ganta”

Leila ta nufi hanyar corridor Madina ta bi bayanta dakin kofar suka fara budewa sai suka hangota zaune a kan wheelchair din ta juyo tana kallonsu.

“Kin ga musakar can, daya dauko ya kawo mana”

Leila ta fada tana yamutsa fuska, sai Madina ta karasa kusa da Aminatu tana mata murmushi, sai da ta kawar da murmushi a fuskarta sannan ta juyo ta kalli Leila.

“Ki daina haka, ke ma baki wuce Allah ya jarrabe ki ba, abun da Talba yayi abu ne mai kyau, kamata yayi ki taya shi sai ku ci ribar tare, taimakon maraya abu ne mai kyau ni kaina ba abun da nake so kamar wannan”

Leila taja tsaki ta saki kofar dakin ta juya ta fice domin ta fahimci Madina ba zata gane abun da take nufi ba. Sai da ta fice sannan Madina ta rage murya ta kalli Aminatu.

“Idan Talba ya dawo ki fada masa abun da Leila tace miki, da kuma wanda nace kin ji?”

Uffan Aminatu bata ce mata ba, kuma bata nuna wata alama dake nuna ta ji ko bata ji ba. Madina ta mike tsaye tana sakar mata murmushi.

“Zan dawo gobe na gyara miki kanki, wata kila ma anjima na sake dawowa, Allah baki lafiya”

Ta fada sannan ta juya ta fice. Ko da ta fito Leila na zaune a inda suka zauna dazun tana tabin wayarta.

“Ina Momy?”

“Ta hau sama”

Ta amsa mata ba tare data kalleta ba.

“Tana sama”

“Idan ta fito ki fada mata na tafi”

Leila ta mike tsaye ta bi bayanta, rakata tai har gurin motarta, Bayan Madina ta bude motar ta shiga ta zauna ta kalli Leila ta ce.

“Ina ganin kamar Talba ba zai iya son yarinyar nan ba, amman komai zai iya canjawa”

Leila ta bushe da dariya.

“Madina baki da hankali”

“Really? Ai tausayi ne silar soyayya tun da har ya fara tausayinta, ba ki ga yadda yake son a kula da ita ba?”

Wani irin zafi zuciyar Leila ta fara yi, ba dan ta yarda da maganar Madina ba, sai dan danganta alakar so da tai da Talba.

“Madina kamar baki san waye talwba ba, yaran masu arziki basa aure sai masu arziki, amman duk wanda ya gaji arziki ya taso a cikinsa ya ginu a cikinsa ba zai taba son rabar talaka ba, a littafai ne ake wannan ko a fina finai, amman talaka sai talaka mai arziki sai dan arziki kaddara ma yana sonta kina tunanin Momy da Daddy za su saka masa ido yana aureta? Ni kuma yayi ya da ni?”

Madina ta yi dariya.

“Waya ga Leila da kishiya”

“Har abada ba zan taba zama da kishiya ba”

“Ko da ni ne?”

Ta fada tana dariya, sai ita ma tai dariya.

“Kin san wani abu? Taimako daya zan miki, ki yi yadda zaki iya yarinyar nan ta dawo karkashin kulawata”

“Ya za'ayi haka ta faru? Kin san yanzu Talba ba yarda yake da ni ba, balle na bashi shawarar ya kai ta gurinki, tsaya ma me zai saka ya kaita gurinki?”

“Saboda ya nisanta da ita, ki kuma ki samu kusanci da shi, amman idan tana gidan nan, kullum sai kun samu matsala da shi, hakan kuma zai ta lalata alakarku ne har ya kai inda ba a so”

Leila ta yi shiru tana nazarin maganar, ta san gaskiya Madina ta fada sai dai tana ganin hakan kamar a dabara ba ne.

“Kawai ki bari sai ina nan shi m yana nan, ki yi mata wani abun da zai zama na magana, daga nan sai ki yi rantsuwa ba zata zauna ba, sai ki bar min sauran aikin”

Ta karasa tana kanne mata ido daya, Leila dai ta bita da kallon badan ta gamsu ba, har ta rufe motar tai reverse ta bar gidan.

BATURIYA POV.

Kamar an dasata a bakin kofar haka ta zauna tana jin kamar ba da gaske ne Faruq ya saketa ba, idan taje gida tace saboda yaga kudi a jakarta ya sake ta? Ai

suma za su tambaya ina ta samu kudin, sai tace musu me? Kawarta ta bata ajiya ba lallai ne su yarda ba.
Tana zaune a gurin har ya gama sallah masallaci ya shigo gida, tana jinsa sai ta saka kuka.
A maimakon ya shigo dakin sai ya zauna falo yana bitar karatu da dansa. Ganin be kula ta yasa ta taso daga bakin kofar dakin ta dawo kusa da shi ta duka tana kuka.

“Dan Allah Faruq kai hakuri, ka gafarta min, wannan kudin ajiya aka ba ni, Ramlee ce ta bani, kuma san zaka yi fada saboda baka son tarenmu da ita, shiyasa nace Umma ce ta bani ajiyar kudin, ba zan sake ba karba ba na maka alkawari”

Ta hade hannayenta biyu tana rokonsa hawaye a fuskarta shabe shabe. Faruq ya sauke Sultan daga jikinsa ya ciro naira ashirin ya mika masa.

“Je ka siyo minti”

Sultan ya karba yana kallon mahaifiyarsa dake kuka cikin yanayi na rashin jindadi ya fice. Sai da Faruq ya tabbatar ya bar gidan sannan ya kalli Baturiya ya ce.

“Hakan ne ya kara tabbatar da kudin nan ba ta hanyar kwarai suka fito ba, tun yaushe na raba ki da yarinyar nan? Yarinyar da a yanzu haka ba gidan iyayenta take ba? Yarinyar da ake zargin har lesbianism tana yi? Rafi'a ban isa na ce kar yi abu ba sai kin yi? Ban isa nace ki yi ba ki yi? Yanzu ai komai ya kare, na riga na sake ki sai ki tattara kayanki ki fice daga gidan nan”

Mikewa tai tsaye ta share hawayenta tana watsa masa harara.

“To na rantse da Allah babu inda zan je, zaman dana zan yi, kuma ai ga wani cikin nan a jikina, sai na haife shi dan haka sai na gama idda zan bar gidan nan, ai daman ni na biya kudin hayan ko? Sai ka tattara komai naka ka bar min gida, kuma dole ne ka rika ciyar da ni, idan ba haka ba sai na kaika kotu, kuma Wallahi yau ba zaka kwanar min da gida ba”

Wani fusata Faruq yai be san lokacin daya kai hannu ya mareta, sai ta fadi a gurin ta fara masa ihu tana kuka, alaar mutane take son tara masa.
Be bi ta kanta ba ya tsallake ya shiga dakin sai ta tashi ta bi bayansa, ta bude wardrobe dinta ta watso kayanta kasa ta fara tumurmuza gadon tana ta ihu, tsayawa yai kallonta da mamaki ganin zata fara masa abun da bata saba ba.

“Wai kina da hankali kuwa?”

Bata ko saurareshi ba ta cigaba da ihun iyakar karfinta duk wanda ya ji sai yayi zaton ko dukanta yake.

“Dan Allah kai hakuri, Wayyo Allah cikina Faruq ina da ciki ka sani dan Allah kai hakuri”

Sai ta sake fashewa da kuka ta dawo falo ta fadi kwance tana ta ihun.

Makociyarsu ce ta fara shigowa tana fadin.

“Subhanallahi lafiya Baturiya?”

Kamin ta karaso cikin falon Baturiya ta tashi zaune da sauri ta nufi bakin kofar sai sukai karo da juna, takenta fada jikinta tana kuka.

“Maman Siyama ki min rai, Faruq ya doke ni kuma ya sake ni saboda budurwarsa na shiga uku Maman Siyama, ga karamin ciki ga Sultan ina zan kai shi?”

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un. Subhanallahi wannan abu be yi dadi ba”

After shigowar Maman Siyama makotansu uku suka shigo suna tambayar abun da ya faru. Cikin kuka Baturiya take tsara musu karya wanda ta shiga kansu ta zauna das.

“Tun kwana baya na ga Faruq ya canja, idan na tambaye shi miya faru sai yace na daina damunsa ko ya mare ni, yau kuma na fita ina dawowa ya samu yana waya da wata a kan gadona, saboda na yi magana ina cewa hakan da kake be dace ba Faruq, idan ma waya zaka yi ka fita can waje mana, amman ba a gaban idona ba, sai ya hau ni da masifa, wai ban isa na hana shi aure ba, na ce masa Faruq ba aure zan hana ka ba, amman ka duba halin da muke ciki muna fama da rashin abinci ga ni da ciki ga yaronka idan ka ce zaka yi aure dawainiyar ai sai ta maka yawa, Wallahi ko kudin hayar gidan nan sai daje gurin Yaya na samo sannan na biya, wani lokacin haka zamu wuni babu abinci sai wahala, dan Allah idan shi mai tunani har yayi zancen aure a wannan yanayin da muke ciki? Akan haka kawai ya hau ni da duka yana marena yana zagin iyayena ga tufafina can ya watsar a wai na tashi na bar masa gida ya sake ni”

Ta kara fashewa da kuka. Kusan kowa dake dakin sai da ya cika da mamaki, domin kallon mutumen kirki suke yi ma Faruq sai yanzu suka gane kallon kitse suke yi na rogo.

“Wannan maganar ta kai a duka ayi saki? Ya sake ki ne saboda ya kawo wata ne kawai amman in ba dan haka ba, ai gaskiya kika fada masa, kuma Wallahi kina da zuciyar imani, da wata ce ba zata yarda ta zauna a irin wannan talaucin ba, da kurciyarki? Har ki biya masa kudin haya? Haba kai Namiji dai be yi ba”

Maman Siyama sai masifa take ta inda take shiga ba ta nan take fita ba, Sai dai duk fadan da take ita da sauran makotan ba su san Faruq na cikin dakin ba domin a falo suke. Badiya ta tabe baki tace.

“Idan kana ganin mutum baka san halinsa ba, ni Wallahi a zatona Faruq ko hannu aka saka masa a baki a zai ciza ba”

“Wallahi ni kadai na san irin ukubar da nake sha a gidansa, ga talauci ga rashin dadin hali, shi yai min mahaifiyarsa da kanensa su min kamar ba yar'uwarsa ba, sam basa kaunata ban san abun da na tare musu ba”

“Ki yi hakuri jarabawa ce, yanzu ina Faruq din yake?”

“Yana daki”

Sai duk suka yi tsit kamar basa gurin, abun ka da mata yan gulma, Maman Siyama ce kawai tai karfin halin nufar dakin, kasancewar ta Babba domin tana da

yaya har da jikoki ma. Ta daga lalulen tana kallon yadda aka watsa kayan Baturiya a kasa sai.

“Baban Sultan taya zaka bari Sheidan ya shiga tsakaninku, shekara nawa kuna zaune a unguwar nan babu wanda ya taba jinku se yanzu?”

Kasa daga kai yai ya kalleta, balle har ya iya furta wani abu, ba zai iya kare kansa ba, ba dan ba shi da abun karewar ba, sai dan baya son tona asirinta ne a matsayinta na matar dansa, taya zai fada musu sanoda ta shigo da kudin da ya ke zargin na alfasha ne? Ba shi ko ita abun zai taba ba, dansa Sultan da kuma wanda zata haifa ne abun zai yi effecting. Dole ne ya rufawa yayansa asiri.

“Haba Faruq a rika sara ana duban baki gatari, ko dan yara”

Sai a lokacin ya kalleta yana kara tsinkewa da lamarin Baturiya domin a yanzu ta wuce da saninsa.

“Inshallahu hakan ba zai sake faruwa ba, an yi na farko kuma n karshe”

“To Alhamdulillah, haka ake son ji, a maida komai ba komai ba, daman shi zaman aure sai da hakuri, a rika kai zuciya nesa ko dan saboda yara, shi auren zumuncin idan ya lalace har zumunci yake tabawa, kuma duk yadda kake ganin kyau matar waje da tarbiya ba tai ta gidanka ba uwar yayanka, dan Allah a gyara kuma ayi ta hakuri”

“Inshallahu komai ya wuce, mun gode sosai”

“To Alhamdulillah Allah ya muku albarka ya ba ku zama lafiya”

“Ameen”

Juyowa tai ta dawo kusa da Baturiya dake sharbar kuka ta zauna saman kujera.

“Ki kwantar da hankalinki kar hawan jini ya kama ki, kuma cigaba da hakuri sakamakonki yana gurin Allah, Allah ya baku hakuri da zama lafiya, na masa magana kuma ya ji yace za a gyara, ke kuma ki kawarda idonki akan lamarinsa idan ma auren zai yi ya kawo ta a nan falonki ya aje sai ki saka masa ido ki kyale shi, kar na sake jin bakinki kin ji ko?”

“To Maman Siyama, Inshallahu ba zan sake ba, na gode sosai”

Dayar makociyarsu mai suna Rufa'atu ta tabe baki tana fadin.

“Idai kika biye namiji sai ki kashe kanki ya auro wata”

Maman Siyama ta bugi hannunta tana nuna mata kofar dakin alamar mijinta na ciki, sai ta daga kafada.

“Ina ruwana shi be ji kunya abun da yai ba”

Tana rufe baki Faruq ya fito ya nuna mata kofar waje

“Malama fata ki bar min gida”

“An dai ji kunya Wallahi, ana wulakanta matar gida saboda ta waje”

Ta fada sannan ta fice Mamam Siyama na watsarta. Badiya ma ficewa tai tana Allah ya bada hakuri, Maman Siyama kan sai da ta tsaya ta sake musu nasiha sannan ta fita tare da dayar makociyarsu. Komawa Faruq yai dakin ya dauki jakarsa ta littafai ya bude ya dauko takardar da biyu ya rubutawa Baturiya wani sakin sannan ya nufo falon ya jefa mata takardar.

“Dazu saki daya nai miki, yanzu kuma kin ja sakin ya zama biyu kuma a rubuce, ki je ki yi duk abun da zaka yi amman zama ni da ke ya kare, ba zan iya zama da mace da bata ganin mutuncina ba, macen da bata iya rufa asirin mijinta ko dan saboda yayanta, Wallahi Rafi'a na rufa miki asiri ne kawai saboda Sultan da kuma abun da ke cikinki, ba dan bani da abun fada ba, kuma wannan abun da kika yi ya kara fito min da halinki yanzu na gane wacece ke?”

Mikewa tai tsaye tare da takardar tana karantawa.

“To sai me? Ina ce dai ni na biya kudin hayar gidan nan, dan haka ka fice min a gida, kuma gobe goben nan idan na ga dama sai na zubar da cikin nan, daga kawai ka raba ni da wahalar talauci? Ina cika idda zan auri Saurayi, dan gidan masu hannu da miya har da manshanu, kuma ka zuba ido ka gani, sai na baka mamaki Faruq, sai n tabbatar maka cewar ni Baturiya ba ajinka ba ce”

Ta fada kamar ba ita ce ta gama kukan munafurci ba a dazun, dauke kai yai ya fice yana taka kafarsa mai ciwo da karfi saboda bacin rai, yana kokarin saka talkaminsa ya hango Sultan zaune bakin kofar bandakin dake tsakar gidan yana kuka. Ajiyar zuciya ya sauke ya saka talkamin ya nufi inda yake ya kama hannunsa, kana ganinsa kasan a tsorace yake, domin be saba ganin Faruq yana fada da Baturiya ba.

“Sultan kana son muje gidan Mama my kwana?”

Sultan ya daga masa kai, sai Faruq ya sakar masa murmushi ya dauke shi suka fice.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram

handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Aminatu na zaune a dakin har kusan la'asar sannan Amal ta leko tana kallonta domin bata nan komai ya faru sai dai Kabir ya labarta mata abun da ya faru, sai kuma ta fita ba tare da ce mata komai. Aminatu ta saka hannu ta share hawayenta sannan ta fara tura keken da nufi shiga bandaki sai taji abun ya mata karfi ba kamar yadda ta ji yana tafiya idan an turata ba, wata kila saboda bata enough kuzari ne, wata kila kuma idan an turo ta baya yake tafiya ne. Leken keken ta fara yi sai ta ji an bude kofar dakin an shigo, dagowa tai ta kalli Mairo dake dauke da plate din abinci da kofin ruwa ta nufota, kamin ta karasa Leila ta biyo bayanta.

“Ke waya saka ki?”

Mairo ta juyo ta kalleta.

“Babu gani na yi an zubawa masu aiki na su, kuma an debar muku na ku, ita ma yanzu ai ta isa jin yunwa”

“Okay ashibabba, yar neman suna, abincin na gidanku ne? Daga zuwa aiki har ki fara tunanin sarrafa gida yadda kike so?”

“Saboda na zubo mata abinci shine abun sarrafa gida? Haba Leila miyasa kike fadawa mutum magana any how ne? A haife dai kin san na haife ki amman duk maganar da ta zo bakinki sai ki fada min kamar wata yarki? Saboda kawai ina aiki gidanku?”

“Kawai ne? Kyauta kike aikin ne? Ba biyanki ake ba? Yanzu uban waye ya baki umarni kawo mata abinci?”

“Keeeee karki sake zagina, idan ina aiki a gidan mu to na gama, arziki ai ba hauka ba ne”

Mairo na kai aya Leila ta wanke mata fuska da mari.

“Mi zaki dakawa tsawa kina ce min ke?”

Mairo ta duka ta aje abincin sannan ta mike tsaye ta ware hannunta zata rama marin da Leila tai mata sai Leila ta rike hannunta ya wulgar.

“Karki kuskura ki ce zaki taba ni da karamin hannunki, wawuya kawai”

Mairo, ya girgiza kai.

“Ina tausayin yadda rayuwa zata maida ke nan gaba, ki taka a hannu duniya ba gurin zama ba ce, ban taba ganin mutum mai wulakanta mutune ba irinki”

“Wallahi idan baki wuce kin bar dakin nan ba sai na baki mugun mamaki”

Mairo ta kalli Leila kawai sannan fice da Mairo ake fadan amman Aminatu ce ta fashe da kuka jikinta ya fara rawa tana yi ma Leila kallon tsoro.

“Ke kuma me akai miki da zaki fara yi ma mutane kuka munafuka?”

Ta dauki ruwan da Mairo ta aje ta watsa mata a jiki, wani irin zabura Aminatu tai ta kalli jikinta da ruwa ya jika, sannan ta hayayakomawa Leila a fusace.

“Mahaukaciya wayuya, baki san darajar dan'adan, ki bar ni da abun da ya dame ni”

Ta fada kamar ba ita ba har wani numfashi take da karfi hawaye a sauko mata. Leila kamar mai jira sai tai cikinta ta chakumota ta jefar kasa.

“Ni zaki yi ma ihu dan ubanki”

Ta kama tsorayen kanta ta rike gam tana fisger kan nata. Wani irin ihu Aminatu ta saka iya kar karfinta tana jin zafin har cikin kanta, sai ta soma jin abu kamar na wacan lokacin yana dawo mata, wani irin ihu take babu kakakautawa irin na fita hayyaci, Leila na ganin haka tai saurin sakinta ta fice daga dakin, sai kuma ta dawo ta cire key din ta rufe kofar ta waje ta cire key din, sannan ta nufi kofar fita daga corridor da saurinta, bata karasa ba Kabir da Amal suka shigo.

“Lafiya?”

“Ban sani ba, ihu take ta yi kuma ta rufe kanta daga can ciki”

Ta amsa tana kallon Kabir, sai suka nufi kofar shi da Amal, hakan ya bata damar ficewa daga corridor. Sai da Kabir ya fara murda kofar ya ji ta a rufe sai ya shiga kwankwasawa.

“Bude kofar”

Ko saurarensa ba ta yi gaba daya ta fita daga hayyacinta sai ihu take. Duk yadda Kabir ya so ya bude kofar sai abun ya ci tura saboda an saka key.

“Je ki tambayi Momy idan akwai extra key”

Amal ta ja tsaki.

“Shiyasa bana son baki, gashi nan Ya dauko mana mahaukaciya”

Ta fito tana ta mita, domin Amina bata kwanta mata ba, musmman da taji cewar Momy bata sonta, ko bayan haka ma Amal bata son baki ko yan'uwa ne suka zo da sunan kwana biyu sai sun ga canji a gurinta balle kuma wannan da bata san inda ta fito ba, kuma bata san ranar barinta gidan ba. Upstairs ta nufa, sai da ta fara shiga dakinta ta canja tufafinta ta saka uniform din islamiya sannan ta fito ta nufi dakin Momy, daga bakin kofa ta tsaya.

“Momy wai ya Kabir yace kina da key din dakin corridor”

“Akwai key a jikin ko wane kofa”

“Eh yarinyar ta rufe kanta ne, daga ciki kuma tana ta ihu”

“Karki dame ni da maganar yarinya, ta kashe kanta”

“Momy miyasa Ya ya kawo mana ita wai?”

“Oho masa, neman suna mana”

Ta saki kofar dakin ta nufo downstairs, kamin ta karasa saukowa ta hango Talba ya shigo yana jin ihun Aminatu ya nufi corridor da sauri, gulmarta ya sakata saukowa da gudu ta bi bayansa.

“Miya faru?”

Shine abun da ya fara tambaya.

“I don't know, muna falo muka ji tana ihu, Leila tace rufe kanta tai daga ciki”

Talba ya murda kofar sannan ya kwankwasa.

“Auta... Bude kofar”

Bata saurarinsa kuma bata fasa ihun da take ba. Baya yai da karfi ya daki kofar da kafarsa ya ji ta gam domin ba irin kofofin nan ba ne masara karfi, ganin kofar ba zata bude ba yasa ya fito daga gurin ya nufi inda suke ajiyar abubuwan a gidan ya dauko wani karfi mai karfi ya dawo ya fara bugawa, karar yadda yake buga kofar ne ya saka Momy da Leila saukowa su nufi corridor tare da Zulai da Mairo.

“Talba me ye haka? fasa kofar zaka yi?”

Be ko saurari Momy ba sai bugun kofar yake, Kabir ne ya amsa mata.

“Idan ba a buge kofar ba babu yadda za'ayi a fito da ita”

“Waya aiketa rufe kofar tun farko? Gaskiya yarinyar ba zata zauna Tana gidan nan tana mana hauka ba, wannan ai iskanci ne”

Talba be saurara har sai da yai nasarar balla kofar sannan ya saki karfin ya shiga dakin da sauri, a kife suka same ta tana ta ihu, dago ta yai yana kokarin zaunar da ita sai ta fado masa a jikin jikinta nata rawa alamar tsoro still tana ta ihun. Girgiza ta yai kamin ya kai hannayensa ya rika fuskarta, ta yadda zata yi facing dinsa ta gane shi ne, amman ko kallonshi bata yi sai ihun take ta yi.

“Akwai abun da za a mata ta daina ihun nan ne?”

Ya tambaya yana kallon Kabir.

“Allura”

“Please”

Talba ya fada sai Kabir ya fice dakin da sauri, Momy taja saki ta juya ta fice tare da Amal yayinda aka bar Leila a tsaye tana kallon Talba, zuciyarta na bugawa da karfi saboda rikon da yai ma Aminatu.

“Shiiiiiiiiiii ya isa saurare ni, kina a cikin mutane ne ba daji kike ba”

Kamin Kabir ya dauko allurar har Talba ya matsu saboda ihun da take bana wasa ba ne, sai da ya saka audiga ya goge mata hannun sannan ya soka mata allurar. Tana jin karfin allurar a hannunta sai ta fashe da kuka ta kamkame Talba, ko minti daya ba ayi ba bachi yai gaba da ita, sai dai hannayenta duka biyu rike suke da rigar Talba, kanta kuma kwance a kirjinsa. Kabir ya mike tsaye yana kallon Leila da hawaye ya cika idonta sai ta juya da sauri ta fice daga dakin, shi ma kallon Amina yai sannan ya fice aka bar Talba rike da Aminatu tana ta bachi wahala a kirjinsa.
Ido ya kurawa fuskarta sai tausayinta ya kara kama shi, idonta rufe yake amman hakan be hana kumburinsu fitowa ba, ga hawaye a fuskarta shabe shabe, ta turo baki gaba lokaci lokaci sai ta sauke ajiyar zuciya.
Yanayi ya so ji na dabam sakamakon rikon da tai masa gashi rabin jikinta yana kirjinsa, domin ta kwanto masa ne. Wata kila saboda be saba rumgumar mata ba ne, wata kila kuma saboda lafiya ta masa yawa ne. Kokarin daga yai daga jikinsa ya dauke ta ya kwnatar da ita saman gadon, ya gyara mata mata kwanciyarta sannan ya kai hannunsa ya taba kafarta a hankali sai ta motsa alamar ta ji ciwon taba kafar da yai.

“Baba... ”

Ta furta tana turo baki gaba kamar zai fado, samun kansa yai da murmushi, yana ganinta ya san shagwababiya ce. Sai da ya karewa dakin kallo sannan ya juya ya fice zuwa bangarensa.

Kusan awa uku tai tana bachi bata farka ba sai tara na dare, kamin ta farka shogowar Talba biyu yana dubata, a na ukun ne ya same ta zaune tana hawaye. Shigowa yai ya zauna bakin gadon yana kallonta.

“Mamana baki gajiya da kuka?”

Sai ta dago ta kalleshi.

“Taya zan rabu da abun da ya zame min azimun? Miyasa kake tunanin rabuwa da iyaye da yan'uwa abu ne mai sauki, taya zan manta komai a take? Saboda ta mutanen da basa maraba da kai abu ne mai wahala! Har yanzu na kasa yarda cewar na rasa komai, ina ta marmari kauyena, da mutanen kirki masu karamci dake cikinsa, na yi kewar mahaifiyata da Babana, har abada ba ni da mai maye min gurbinsu”

Ta share hawayenta sannan ta soma wasa da yatsun hannunta wasu hawayen na sauko mata.

“A da, ina rayuwa ne cikin wani karamin gari, mai cike da albarkar manoma, duk da kasancewar ban samu ilmin boko ba, na samu na addini daidai gwargwado, kuma ina zaune da yayyuna cikin jindadi da farincikin rayuwarmu ta yau da kullum, ni kadai ce mace bayan mazaje bakwai da mahaifiyata ta haifa, hakan ya saka na zama yar gata, ina jin kamar babu wanda ya fini more rayuwa, abun da ban sani ba, ashe kaddara tana nan tana min wani tsari, a lokacin da mahaifiyata

take cikin rashin lafiya na bakinciki abun da akai ma yayanta kasan me ta fada min?”

Ta kalleshi sai ya girgiza mata kai alamar be sani ba.

“Tace kuka na yana nan gaba, sai na tambaye tana take ganin zan iya rayu idan bata raye? Tace min zaki rayu amman akwai kuka a gaba, a yanzu na gane abun da take nufi, tabbas zan rayu amman wace irin rayuwa zan yi? Ban sani ba, kuka da take fada min cewar zan yi na tabbatar shi ne na fara tun a yanzu, yanzu na fahimta wanda ya rasa uwa ya rasa ta har abada, wand ya rasa yan'uwa ya rasa su har abada, abu ne mai wahala farinciki ko murmushi ya sake kusantar fuskata...”

Ta fashe da kuka sosai, Talba ya ja dogon numfashi a hankali ya sauke.

“Baki taba tunani miyasa Allah ya hada ni da ke ba? Wata kila a yadda nake da rufin asiri idan na tare ki a hanya, ba zaki tsaya ba zaki ji tsoro, wata kila ni kuma ba zan taba jin a kamata na tsayar da ke na tambayi damuwarki ba, amman sai Allah ya kawo silar da zata saka na hadu dake cikin sauki kuma har na dawo dake da zama kusa da ni, idan Allah ya karbe wani abun sai ya maka hanyar wani, ki dauka duka wannan yana cikin jarabawarki, Annabi Muhammad Sallalahu Alaihi Wassalam yafi kowa gata a gurin Allah kuma Allah yafi kaunarsa da kowa, amman a haka Annabi ya girma babu mahaifiya babu mahaifi, ni da ke banbancin kaddararmu kadan ne, ni ma na tashi babu uwa ba uba, sai dai na zamu gata, irin gatan da nake kokarin baki a yanzu, ki dauke ni a matsayin yayanki, saboda ina ganinki kamar yar'uwata ne, duk abun da zan yi ma kanwata Amal ko Leila zan miki, ki sake jikinki, zan maida ke yar gata believe me zaki zama Shalele ta ko'ina”

Kanta na kasa tana hawaye har ya gama magana, sannan ta dago ta kalleshi, be yi mata kama da mai karya ba, kamaninsa da cikar kamalarsa be nuna akwai gazawa a tare da shi ba.

Sai dai me? Matar daya ambata da sunan cewar matar da zai aura ce zata yarda? Anya ma zata jure zama a gidan tare da ita?

“Ina da tabbacin ba duka aka akashe yan'uwanki ba, Inshallah idan hankali ya kwanta kin samu lafiya zan muje mu nemi inda yan'uwanki suke, yanzu taso muje ki ci abinci”

“Ina son na yi sallah, ban yi sallah ba ana biyana salaloli da yawa, dazun ma na fara tura keken naje na yi sallah sai.... ”

Daga haka ta labarta masa abun da ya faru ciki har da wanda Madina tace idan ya dawo ta fada masa. Be jidadin abun da Leila tai mata ba, sai dai be nuna mata ba.

“Okay amman yanzu bari ki fara cin abinci ki samu kuzari, sannan muje ki yi sallah okay?”

Ta daga masa kai.

“Zulai zata zo ta tura ki bathroom ki wanke bakinki sai ta fito da ke ki ci abincin ki yanzu”

“Aa bana so yanzu wannan zata zo ta fara min masifa, kuma zata hana su yi min komai”

Ta fada kamar zata fasa kuka.

“Kina son na tura ki?”

Ta daga masa kai, sai ya mike tsaye ya dauketa ya dora a wheelchair din. Ya turata da kansa har bathroom din ta wanke bakinta.

“Zaki yi fitsari?”

Ta girgiza masa kai alamar aa. Sai ya turo ta ya fito da ita sai da suka kawo gurin kofar sannan ta kula da kofar a balle take, sai dai bata ce komai ba tana ta kallon hanyar har ya fito da ita falon. Iyakar abun da ta sani Leila ta rika kanta tana ja da karfin tsiya, bayan baka bata san me ya faru ba, sai ganinta tai ta farka daga bachi.

“Waya kwantar da ni kan gado dazun?”

“Ni”

Ya amsa mata a takaice sannan ya tura kujerar har gurin dinning, babu kowa a falon daga shi sai ita sai katon Plasma. Da kansa ya shiga zuba mata abincin, sannan ya mika mata. Sawun takun talkami da taji ne ya saka ta waiga ta kalli Upstairs din sai ta hango Madina da Leila suna saukowa a tare, suna hada ido da Leila tai saurin maida kanta kasa cike da tsoro. Kallo daya Talba yai musu ya dauke idonsa, kusan a tare suka kalli juna, ba Leila kadai ba har Madina ta ji zafin ganin Talba na zubawa Aminatu abincin da kansa, sai dai ta dannewa zuciyarta bata yarda ta nuna ba, duk da kasancewar Leila ta fada mata komai daya faru dazun.

“Amman wannan wulakancin ne, haba Talba? Taya zaka zuba mata abinci a irin plate din da muke cin abinci? Kuma ka kaita har gurin dinning?”

Madina ta yi saurin rike ta.

“Haba Leila miye haka?”

“Ai dole na yi magana, dazu fa har rumgumar ta yai...”

Tana kokarin kai hannu ta taba Aminatu data make guri daya Madina ta yi saurin rike ta da karfi.

“Leila miye haka wai?”

“Wallahi sai ta bar gidan nan, na rantse da Allah ba zata zauna a nan ba”

Ta fada da karfi kamin ta kwalawa Momy kira tana ihu. Uffan Talba be ce mata ba, ko kallonta be yi ba sai aikin zubawa Amina ruwa yake a cup. Kamar da gangan Madina ta saki Leila ta karasa gurin dinning.

“Karki taba yarinyar nan”

Furucin da yai mata ne yasa saka ta tsaya cak, domin bata ji wasa a muryarsa ba kamar yadda fuskarsa ma bata nuna wasan ba. Aminatu ta yi saurin sakin plate din abincin dake hannunta idonta cike da hawaye. Hango Momy na saukowa tare da Amal da Kabir yasa Leila ta dauki ruwan da Talba ya zuba a cup ta watsawa Amina.

“Haba Leila miye haka?”

Madina ta fada tana zaro ido tare da saka hannayenta ta rufe baki.

“You should apologize ki bata hakuri yanzu nan”

Talba ya fada yana nuna mata Aminatu.

“No Leila ta yi kuskure, amman ba zata bata hakuri ba, you're just hurting her”

Kabir ya fada, Momy na karasa kusa da ita ta maida Leila.

“Ya isa haka Talba, ba zan yarda ka wulakanta Leila akan wata banza ba”

“Momy kin san abun da ta yi”

“Be dame ni, amman ta duka ta bawa wannan musakar hakuri ne ba zata tayi ba!”

Nan da nan jikin Aminatu ya fara rawa, Talba ya kalli Momy.

“Wannan ba daidai ba ne Momy”

“Miye daidai tana yar riga kace ta bawa wata banza hakuri? Wai gata ka fi leila ne ko kuma miye?”

“Kuma na rantse da Allah ba zata zauna a gidan nan ba, Wallahi Momy sai dai ku zaba ni ko ita...!”

Leila ta fada tana buga kafa a kasa. Leila ta ji wani irin dadi, komai ya faru kamar yadda take so, duk da kasancewar bata yi zaton da wuri haka komai zai faru ba, daman ta zo gidan nan kawai saboda Leila ta kirata tana kukan rumgumar da yai ma Amina, sai dai a yanzu komai ya yafi kamar yadda take son ya tafi. Da sauri ta nufi Aminatu dake kuka taja kujerarta.

“Madina ki kyale yarinyar nan a gurin nan?”

Sai ta girgiza ma Momy kai.

“Dan Allah Momy ki gafarce ni, be dace ku yi wannan fada a gaban yarinyar nan ba”

Bata jira abun da Momy zata sake cewa ba, ta tura Aminatu zuwa corridor, a azaton Momy Madina ta yi hakan ne saboda bata son su yi fadan a gabanta kasancewar su yan'uwa.

“Abun da kake ba kyautawa ba ne, Talba, be kamata ba, ko a dazun ka rumgume yarinyar nan a gaban Leila kuma kasan dole zata ji ba dadi ba, and now kana kokarim feeding dinta for what”

Talba ya nuna Kabir da yatsa.

“Don't you dare tell me what is right and wrong, don't you dare judge me, this is my life waye kai da zaka kalubalanci abun da na yi?”

“So baka isa ka kawo wata a gidan nan just to hurt my sister in front of us? And now ba zamu zabi wata akan Leila ba, take her away”

Wani irin kallon kallo suke tsakanin shi da Kabir ko wane zuciyarsa ta kawo kamar ya rufe dan'uwansa da duka yake ji. Daker Talba ya samu hade numfashinsa ya kalli Leila dake tsaye sannan ya nufi corridor da zai sada shi da dakin da Aminatu take ciki. Bakin kofar dakin ya tsaya yana kallon Madina dake rumgume Aminatu tana share mata hawayenta da dankwalinta, ita ma tana kuka.

“Dan Allah ki yi hakuri ki daina kukan nan, ban taba rasa kowa ba, amman na fahimci yadda kike ji, akwai ciwo sosai ki kwantar da hankalinki Inshallah Talba ba zai bari ayi miki komai ba, ni kuma zan kula da ke kamar kanwata Inshallah”

Yadda take hawaye sai ka rantse da Allah kukan gaske take, zaka yi zaton da gasken gaske take tausayin Aminatu. A badini kuma tana yin hakan ne saboda ta ji kamshin turaren Talba ta san yana tsaye bakin kofar dakin ko ma cikin daki. Aminatu na hada ido da Talba ta saki Amadina tana kuka.

“Dan Allah ka kai ni inda yan gudun hijira, ko wani gurin, bana son fada bana son fada dan Allah karka yi fada da su dan Allah...”

Karasowa yai cikin dakin ya risina gabanta yana kallon fuskarta, magana yake son yi mata amman ya rasa ta ina zai fara.

“Idan zamanta a nan zai kawo matsala, zan iya tafi da ita gidamu, Mamana bata da matsala kuma zan iya kula da ita, kamin Momy da Leila su sauko”

Madina ta fada muryar na rawa, a ranta tana ala ala ya amince, a hankali Talba ya juyo ya kalleta.

“You can trust me. Wallahi ba zan mata komai ba, tare na da Leila ba zai saka na cutar da wani ba, yarinyar nan ta cancanci rayuwa mai kyau...”

A nan ma Talba be ce mata komai, ya juya yana kallon Aminatu.

“Excuse us Madina”

Murmushi ne ya cika fuskarta, saboda ya kiran sunanta, kusan tun da take da Leila ba zata iya tuna rana daya ta taji sunanta a bakinsa ba.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud Sandal flakes

Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

“Kar abun da Leila tai ya dame ki, tana da zafi ne, amman a sannu zata fahimta ta daina”

Aminatu ta saka hannu ta share hawayenta, wasu a sauko mata.

“Komai be da sauki a rayuwar duniya, komai ka sara yana da wahala ka samu abun da zai maye maka gurbinsa, rayuwarmu da ta ku akwai banbanci, kuma tana da gaskiya, ni yar kauye ce marar gata wanda bata waye a komai ba, ba kamar ni ba talaka kuma yar kauye, be kamata na zauna a mazauninsu ba, ko kuma na ci abincin a inda suke so, muna da banbanci mai nisa a tsakaninmu”

“Ban taba ganin wannan banbanci ba, ban taba jin cewar Leila ko ni mun fiki ba saboda dukiya, ita ma kuma kurciya ce ke janta”

“Idan ita kurciya ce, Momy fa?”

Yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai ce mata.

“Momy tana goya mata baya ne saboda bata son bata kunya a gaban mutane, ko da ni zan yi fada da Leila wani lokacin zata iya shigar min ta yi ma Leila fada”

Ta yi shiru hawaye sai sauko mata suke.

“Kalleni”

Ta dago, sai idonta ta sauka cikin nasa, a karon farko ta ji kwarjininsa ya cika sa, akwai kalama a fuskarsa kamar yadda natsuwarsa take kara fito da siffar zatinsa.

“Zaki iya zama a gurin Madina ko kuma na kai ki wani gurin dabam?”

Ta kawarda fuskarta tana tunani.

“Ban sani ba, wata kila ita ma iyalan gidanta kamar na ka ne, ba lallai ne su karbe ni, amman ka min wani alkawari dan Allah”

Kallonta yake, ita ma kamar tasan ba zai tambayeta minene sai ta fada tana yawo da idonta a dakin.

“Ka min alkawarin, zaka nema min gurin da zan zauna cikin yan gudun hijira yan'uwa, ko kuma ka nema min wasu daga dangina kamar yadda kai alkawari”

Yayi murmushi kadan.

“Kina tunanin yan gudun hijirar suna shan dadi ne? Suna wata irin rayuwa ne mai ban tausayi da tada hankali, abun da za su ci ma wahala yake musu, ba su da muhalli, wasu na fakewa a kangon makaranta ko tsohon gida, wasu kuma suna zaunawa inda yan'uwa ne, amman su suke ciyar da kansu, wasu bara suke su ciyar da kansu, wasu kuma surfe suke su yi wankakau ko wani aikin karfi sannan su samu ciyarda kansu, idan sun shiga wani gurin za a nuna musu kyara ana kiransu da mayu, sadakar ma sai wanda ya ga Allah ya ga Annabi yake ba su, ba rayuwa suke mai dadi ba, ya kamata ki daina wannan tunanin”

“Ba jindadi nake so ba a yanzu, jindadi abu ne mai wahala a gareni, so nake na samu sakewa ina sonnna zauna da irin mutanen dake rayuwa kamar yadda nake, mutanen da basa kyamata, ina ma kasance tare da mutane masu irin rayuwata, wadanda suka san zafin rashi...”

“Ina daya daga cikinsu ai”

Ya fada yana mikewa tsaye. Sannan ya nufi kofar fita wa kusa da kofar ya samu Madina ta jingina tana jiran fitowarsa.

“You should go and talk to your parents first, idan sun amince sai ki sanar da ni”

Ta dago a hankali ta kalleshi.

“Iyayena basa da matsala, amman zan je na sanar da su, sai dai ban san inda zan same ka ba”

Tsayawa yai kallonta sannan ya mika mata hannunsa, tana ganin haka ta fahimci wayarta yake nufi sai tai saurin cire password din wayar ta mika masa. Yana saka number ya mika mata wayar sai ta karba da hannu biyu tana godiya.

“Na gode”

Be kula ta ya juya ya koma cikin dakin, sai ta yi tsalle ta dire a hankali ta kai wayar a hancinta tana shinshinar kamshin turaren Talba kamin ta kai wayar a kirjinta. Sannan ya fito corridor tana boye jindadinta, Kabir ta samu tsaye yana fada Leila.

“Kishi ba hauka ba ne, kowa ya san akwai zafi amman ya kamata ki rika controlling kanki, idan ma wani abu ne ai shi yai miki ba ita ba”

Madina dai bata ce komai ba har Talba ya turo Aminatu kam wheelchair ya fito da ita falon, kanta a kasa tana tsoron kallon mutane, shi ma kuma kofar fita daga

falon kawai yake kallo. Momy da Leila har ma da Kabir na tsaye ban kallonsa babu abun da suke har ya fita da ita.

“Aikin banza mtsssss”

Leila ta fada tana jan tsaki. Sai da Madina ta leka windows ta hango ya tashi motar yana kokarin yin ribas sannan ta kalli Momy ta ce.

“Momy zan tafi da yarinyar nan saboda anan zata haifar da fitana ne kawai, kuma idan tana tare da ni zata nisanta da shi ba kamar yanzu ba”

Momy ta kalli Leila sannan ta kalli Madina.

“Ke iyayenki za su yarda ta zauna ne?”

“Eh zan musu bayani kuma ai kin ga ba dadewa za ta yi ba, na dan lokaci ne”

“Shi zai yarda ki tafi da ita?”

“Eh na masa magana, amman yace min na fara zuwa na yi magana da iyeyena”

“Okay ba matsala”

Momy ta amsa ta tana kallon yanayinta, sai ta yi ma Leila sallama tana fadin sai sun yi waya. Momy ta bita da kallo har sai da ta fice sannan ta kalli Leila ta ce.

“Ki yi hankali da yarinyar nan, hankalina be kwanta da ita ba, idan b munafurci ba ta ya za ayi fada akan yarinya kuma ke ki ce zaki dauketa ki kaita gidanku?”

“Momy da sani na tai, sai da tai shawara da ni, plan ne muke hadawa, Madina bata da matsala, ba yau na santa ba fa Momy”

“Ki dai yi hankali, kuma ki san irin sirrin da kike fada mata”

Kabir ya mike tsaye yana kallon Leila.

“I hope plan din da kike hadawa ba cutar da yarinyar nan zaki yi ba, ba na goyi bayanki ba ne saboda ki samu damar wulakantata, no na yi hakan ne saboda na san kina jin kishin abun da Talba yake yi ma yarinyar nan”

“Ba wanda za a cutar kawai zan nisanta ta da shi ne”

“Dauketa za ki yi?”

“Haba Kabir? Idan ma na dauke ta zan yi ai shi ya ja mata...”

Uffan Kabir be sake ce mata ba ya fice falon. Ita ma tashi tau ta nufi upstairs aka bar Momy zaune tana kallon Leila har ta haye.

TALBA POV.

A entrance din ya bar ta, sai da ya fara isa ya bude motarsa sannan ya dawo ya saka hannunsa ya dauke ta ta saka a motar ya dawo ya dauki wheelchair din ya

saka a bayan motar, kana ya zagayo ya rufe side dinta ya shiga driver seat yaja motar suka ce daga gidan.
A hankali yake tuka motar yana kallonta, ita kuma tana ta kallon titi, da motocin dake kai da kawo har suka isa super market din da yake siyen chocolate da sweet da yake kaiwa a gidan marayu, fakawa yai a harabar sannan ya fita ya shiga ciki be dade ba ya fito ya dawo cikin motar, yaja suka dauki hanyar by pass.
Har suka isa aka bude musu gate din ya shiga ciki ya faka motarsa Aminatu bata kalli inda yake ba, sai da ya bude motar ya fito, sannan ya zagayo gefenta ya bude mata.

“Ina kujerar?”

Ta fada tana kallonsa.

“Ya kamata ki fara takawa”

Ta bata fuska tana turo baki gaba kamar zata fashe da kuka.

“Akwai zafi idan na taka”

“Idan baki taka ba, then yaushe zaki taka kafar? Kullum haka zaki yi ta zama fa”

“Ni dai ba zan iya takawa ba”

A dole ya bude ya dauko mata kujera ya aje mata.

“Ta so ki zauna”

Ta kalli kujera ta kalleshi sai ta kara bata fuska.

“Akwai nisa ai sai na yi taku har hudu”

“Idan ba zaki taka ba, zan tafi na bar nan”

“Sai na yi ta zama a nan ina ruwana”

“Ni ma ina ruwana ki yi ta zaman to”

Ya fara takawa kamar gaske, sai ta fashe masa da kuka.

“Ashe kin iya kuka... Ya miki kyau”

Ya fada ba tare daya juyo ba, hakan yasa dole ta fito da kafafuwanta ta taka kadan.

“Wash wash wash...”

Tana fada tana hannunta rike ta ganbun motar har ta karasa gurin kujerar ta zauna.

“To na zauna”

Ta fada cikin kuka. Sai ya juyo ya kalleta yai murmushi.

“Daga yau ba za a sake turaki a keke ba”

“Ni kuma ba zan yi tafiyar ba, ai saboda kasan akwai ciwon a kafata ne, idan kai ne Allah kadai ya san yadda zaka yi kuka”

This time around murmushi yake mai sauti. Ya dawo kusa da ita ya tsaya.

“Wato kukan zan yi, an fada miki ni rago ne kamar ke?”

Ya fada yana kai hannu ya lasa kumatunta, sai ta kara turo bakin gaba. Murmushi yai ya bude back seat din ya dauko abubuwan da suka siyo ya dora mata saman jiki sannan ya koma bayanta ya fara tura keken.

“Yaran da zan nuna miki yanzu, basa da uwa ba uba, ba yan'uwa ba kowa, amman sun zama kamar iyalai a nan, kuma suna farinciki, ba dan yau yana ranar karatu ba, suna makaranta da yanzu sun zo sun zagaye mota suna murna da ganina”

“Waya kawo a nan to?”

“Na yi miki karya?”

“Aa ka fada min gaskiya dai, Babba ba ya karya karya ba kyau”

Yayi murmushi.

“Ni na kawo su a nan”

“Amman da zaka yi karya me zaka ce min?”

“Sai na ce Babana”

“Babanka ba ya rasu ba?”

“Yeah tun ina ciki mahaifina ya rasu, amman Daddy ai shi ne Babana gatan da yai min ko da ace Babana yana da rai ba zai min shi ba”

Ya fada sannan ya turata har gaban ajijiwansu, yaran na ganinsa suka taso ta gudu suna masa oyoyo.

“Uncle Uncle”

Yayi murmushi ya duka yana tambayar lafiyarsu. Aminatu na kan kujerar tana kallonsu cike da burgewa, irin yadda yake sake musu ya saka suka saba da shi sosai har taba jikinsa suke wasu na tsokanarsa.

Mikewa yai tsaye ya dawo kusa da Aminatu ya dauki ledar sweet din ya bude ya mika mata.

“Ki ba su”

Ta kalleshi kamin ta kai hannu ta dauka ta fara mika musu duk wanda ya karba sai ya koma gefe, wasu kuma sai su dawo a kara musu, shi ma ya dauki daya ya

fasa ya saka a baki, bayan sweet din ya kare ya bude chocolate ya bata tana dauka tana ba su, sai ga murmushi a fuskarta. Sai da ya kare sannan yai musu sallama suka koma ciki, shi kuma ya turo Aminatu har gurin Motarsa.

“Yanzu ma ke zaki shiga da kanki”

Ta bata fuska.

“Wallahi akwai zafi tafiyar dazun ma daurewa kawai na yi”

“Yanzu ma daurewa kawai zaki yi”

“Yanzu ba zan iya daurewa ba”

Ta fara matsar hawaye sai yai murmushi kadan ya ciro wayarsa dake ring, sai da yai kamar kar ya dauka sai kuma yai picking.

“Ya akai?”

“Talba... Kana ina?”

Ya kalli harabar gurin.

“Ina wani guri”

“I need to see you akwai magana mai muhimmanci daya kamata ka sani”

“Idan na dawo zan kira ka”

Yana fadar hakan ya kashe wayar ya kalli Aminatu dake masa kallon tsoro.

“Momy ce?”

“Momy kike tsoro? Abokina ne”

“Wannan likitan?”

Ya daga mata kai, sannan ya duka ya saka hannunsa ya dauke ta ya saka a front seat ya rufe, ya nade kujerar ya saka ta a bayan motarsa, ya zagayo zai shiga motar wayarsa ta sake yin ringing, sai da ya zauna sannan ya duba wayar sai ya ga bakuwar number. Picking yai ya kara a kunne sai Madina ta yi masa sallama.

“Assalamu Alaikum, Madina ce”

“Ina ji”

“Ka kawota gidanmu Hajiya ta amince”

“Mahaifinku fa?”

“Shi ma ya amince, baya gidan amman na yi magana da shi ta waya”

Be sake cewa komai ba ya kashe wayar. Ya yi ma motar key yai reverse suka fice daga gidan. Be yi wata doguwar tafiya ba, suka iso gidansu Madina, horn daya

yai aka bude masa gate din ko kamin ya faka harabar gidan Madina da kanenta biyu mata sun fito da saurinsu suna tarbonsu, ko wanensu fuskarsa a sake alamar suna maraba da zuwanta.

“Ina fatar dai kina ra'ayin zama, bana son na cilasta ki, kuma zan rika zuwa kullum ina dubaki, idan kin ga wani abu na daman ki fada min”

Ta daga masa kai, sannan ya bude motar ya fita kamin ya zagaya ya bude gefen da Aminatu take, har Madina ta ta rumgume Aminatu a gabansa, hakan da tai kuma ba karamin dadi yai masa ba, domin a ganinsa ko ba komai ta nuna mata rashin kyama. Da kansa ya fito da wheelchair din ya aje ta nesa da inda motar take, ita kuma ta riko Aminatu suka ta fito.

“A matso da kujerar”

“Aa ki taka a hankali, ki isa gurin kujerar, ya kamata ki rika takawa”

“Akwai zafi sosai”

Ta fada kamar zata fashe da kuka, Madina ta yi dariya.

“Aiko kara ki saba, domin ni ba zan yarda ki yi ra zama kan kujera ba kullum dole ne ki fara tafiya”

Da wash wash ta karasa gurin kamin ta zauna har ta kagu, Madina ta fara tura kujerar Talba kuma yana dagawa kanenta dake gaishe shi kai, sai kuma yai tsaye sai har sai da suka karasa gurin kofar falon sai ta juyo ta kalleshi ya sakar mata murmushinsa mai kyau, Madina ta ji gabanta yayi mugun faduwa, sai yanzu ta tabbatar Leila ta fita juriya, domin bata jin zata iya jurewa Talba ya rika kula Aminatu a gabanta, saboda shi, yanzu ma ba dan tana neman kusanci da shi ba da ba zata yarda ta karbi Aminatu ba.

“Maraba maraba”

Hajiya ta fada da fuskar dake nuna dole Madina tai mata ba dan tana so ba.

“Ina wuni”

“Lafiya Kalau”

Tana amsawa ta kalli Madina sai kuma ta dan yi murmushi.

“Yanzu bari mu fara cin abinci sannan ki yi wanka, ki huta”

“Ina son zan yi sallah”

“Okay”

Ta turata har zuwa dakinta.

“Nan zamu zauna, nan ne dakina so yanzu mun zama mu biyu”

Aminatu dai bata ce mata komai ba, har gaban gadonta ta kaita ta fita ta debo mata abincin da aka girka shinkafa da miya. Da kanta tai feeding dinta sannan

ya kaita bandaki ta hada mata ruwan wanka ta fito ta baro ta a ciki, bayan ta gama ta koma ta turo ta suka fito, wata doguwar rigar ta dauko mata ta taimaka mata ta saka sannan ta nuna mata gabas ta bata hijabi.
Haka tai ta wuni tare da ita a dakin tana kunna mata tv can kuma ta jata da hira.

Da dare ma a tare suka ci abincin dare, sannan ta dauko mata daya daga cikin tufafin na kwana ta bata ta saka. Sannan ta dauko wayarta ta rike.

“Ko na kira miki Talba ki masa sai da safe?”

Aminatu ta yi shiru kamar mai tunani.

“Aa”

Sai Madina ta kai hannu ta dafa ta.

“Ai kara ki saba da gaisawa da shi, ai zai jidadi kuma zai ce kin damu da shi, kamar yadda shi ma ya nuna miki kulawa”

“Toh...”

Sai Madina tai murmushi ta nemi number sa ta kira shi.

“Idan ya dauka ki ce kina son ki ji muryarsa ne kamin ki kwanta”

“Toh”

Wayar ta yi ringing ta katse be daga ba, tasan Talba baya son hayaniya, hakan yasa bata sake kira ba.

“Be daga ba wata kila baya kusa da wayar”

Aminatu ta daga mata kai sannan ta kwanta saman gadon. Tara da yan mintuna Madina ta sake kiran Talba, rejecting call din yai ya kira jiki na rawa ta dauka.

“Hello”

“Madina bana son yawan kira”

“Ka yi hakuri dan Allah, ni ma ban so kiran ba, Amina ce tace tana son na kira mata kai”

Yayi shiru be ce mata komai ba, sai ta saka wayar a hands-free ta mikawa Amina.

“Fada yayi?”

Amina ta tambaya kamin ta karba.

“Ban yi fada ba, Shalele ba ki kwanta ba?”

“Eh”

“Akwai wata matsala ne?”

“Aa kawai ina son na ji muryar ka ne kamin na kwanta”

Yayi murmushi ya.

“Shalele sleep tight”

“Miye haka nan?”

“Ba ki san abun da hakan ke nufi ba?”

“Eh ni bana jin turanci”

“To za a koya miki, ki kwanta yanzu ki yi bachi da kyau”

“Toh sai da safe”

“Sai da safe”

Yanke kiransa yayi daidai ta sauke ajiyar da Madina tai yi, domin har ga Allah bata dauka tana kishin Talba har haka ba sai yanzu. A take yanayinta ya canja, ta kwanta ba tare da tace cewa Amina komai ba.

Washe gari a dakinta ta kawo mata komai a karyawa, sannan ta nufi wayarta dake ringing ta dauka.

“Hello”

“Madina ya kika?”

“Lafiya kalau, kamar Kabir”

“Ni ne baki da number ta, ni ai ina da taki”

“Uhm Ya aikin?”

“Alhamdulillah, Yarinyar nan tana gurinki?”

“Wai Shalele? Eh tana nan”

“Shalele kuma?”

“Eh haka na ji Talba na kiranta, na dauka haka kuke kiranta ne ai saboda tana da sunan Momy”

“Aa zan zo na dubata yanzu”

“Momy ta sauko kenan?”

“No tana da ciwo a kafarta, zan duba ciwon ne, kuma ga maganinta nan kin manta”

“Okay sai ka zo”

Ta sauke wayar tana kallon Aminatu.

“Shalele wai haka Talba ke kiranki ko a gida?”

“Aa”

Aminatu ta amsa mata a takaice cikin rashin sakewa. Tsayawa tai tana kallonta sannan ta fice tana kiran Leila a waya.
Harabar gidan ta fito tana labartawa Leila abun da ya faru.

“Yau fa be ma shigo nan ba, ko Momy ta waya ya gaishe ta, be leko bangaren nan gaba daya, kuma na san duk saboda na ce ba zata zauna a bangaren ba ne”

“Ni abun har mamaki, taya zaka hadu da yarinya a titi kace zaka fifitata sama da yar'uwarka kuma matar da zaka aura”

“Daman kin san bama sha inuwa daya, idan ba ganin yai raina ya bace ba hankalinsa ba zai taba kwanciya ba”

“Jiya fa bata kwanta ba sai da ta ji muryarsa”

“Da gaske?”

“Wallahi kuwa, kin ji yadda yake kiranta Shalele”

“Madina sai na ci uban yarinyar nan, me take nufi?”

“Me yake nufi dai shi, idan bata ga fuska ba ai ba zata soma ba, amman fa karki ce ni na fada miki”

“Ai ba zan fada ba, amman dole na dauki mataki?”

“Matakin me zaki dauka? Har a bada, Talba ba zai taba auren yarinyar nan ba, ko da yana sonta, Wallahi ba zan bari ba, sai dai ina ganin yana yi ne saboda ya musguna miki, shiyasa na baki shawarar ki kulla soyayya da Ali, so that ya ji yadda kike ji, amman ko dan rashin sanin asalinta da kuma fyaden da akai mata ai ba zai aureta ba, besides ita fa ba yar kowa ba ce”

“Na san da wannan, amman ko zai yi dan ya bata min rai be kamata yai da wannan yarinyar ba”

“Zan kira ki anjima”

Ta yi saurin katse kiran hango motar Kabir da tai, tana tsaye har ya iso kusa da ita ya faka motar ya bude.

“Hajiya Madina...?”

“Yau dai sai gaka gidanmu kamar wasa”

Yayi dariya.

“Na zo na goge laifina ne, kin san jiya ba mu kyautawa Talba ba, shiyasa na zo na goge laifina”

“Hakan ya kamata gaskiya, bari na fito da ita”

Ya mika mata maganin ta karba ta shiga ciki ba dadewa ta fito tare da Aminatu ta kawo masa har gurin motar.

“Tashi tsaye”

Ta girgiza kai.

“Ni bana ita tashi yana min ciwo”

Fitowa yai motar ya duka gabanta yana duba kafafuwan, sannan ya koma ciki ya dauko safa ya saka a hannunsa ya fara latsa kafafuwan.

“Akwai zafi fa”

Ta fada a shagwabe. Rikata ya mikar da ita tsaye, sannan ya saka dayan hannunsa ya janye kujerar yana kokarin sakinta.

“Aa aa aa akwai zafi”

“Haka zaki hakura ki tsaya idan baki tafiya ya za'ayi ya warke? Kin yi gudun daya wuce kima ne shiyasa amman kina fara takawa zai warke tun da an saka miki magani”

Ya saketa sai ta fara rawa can kuma ta kasa tsayuwar ta fadi, tsakanin Madina da Kabir aka rasa wanda zai rika ta har ta kai kasa.

“Kar a sake bari tai zauna, ku rika barinta tana tafiya”

“Ton”

Ya koma cikin motar ya dauko takardar yayi rubutu akai ya mikawa Madina.

“A nemo mata wannan maganin duka na shafawa ne”

“Okay”

Ta fada tana karba sannan ya rufe motar ya juya ya fice daga gidan. Sannan Madina ta nufi inda take da keken ta rikata ta zauna.

“Karki takura kanki da tafiya, idan ba zaki iya ba ki yi zamanki a nan kin ji?”

“Toh”

Ta fada idonta tab da kwalla. Suna shiga ciki Madina ta kalleta tace.

“Anjima zan kaiki gurin gyaran kai, kuma zan muje da ke ki zabo tufafin da kike so, amman kamin mu tafi zan kira Talba ki fada masa inda zamu je, sai ki ce masa kina son ya raka mu okay?”

“Toh”

“Good, kuma idan yace zai je aiki ki ce masa kina son zaman a gurin aikinsa kamin na dawo daga nawa aikin, saboda ni ma aiki zanje yanzu”

“Tohm”

Kamar hadin baki Madina na daukar wayar da zimmar kiran Talba sai gashi ya kirata, murmushi ne ya kawata fuskarsa tai picking call din ranta fes.

“Hello”

“Shalele na kusa”

“Eh”

Ta amsa tana hade abu mai daci na kiran Aminatu da yai da Shalele sannan ta mika mata wayar.

“Hello”

“Shalele kin tashi lafiya?”

“Lafiya kalau, yanzu zamu je gurim siyen kayan sakawa da kuma gyaran kai, idan kana nan ina son mu tafi tare”

Ya dan yi jimmm kamar mai sauraren wani gurin, har sai da ta dauke wayar daga kunnenta ta duba sannan ta sake maida wayar.

“Hello”

“Already ina Office, ba zan samu zuwa ba kuje tare da Madina ki zabo duk abun da kike so”

“Ita ma aiki zata je yanzu, ko ta kawo ni a nan idan ta tashi sai ta zo mu tafi tare”

“Miyasa kike son zuwa inda nake ne?”

Tayi shiru sai kuma ta ce.

“Ka yi hakuri”

“No ba zan cen na yi hakuri ba ne, bata wayar”

“Gashi yace a baki wayar”

Ta mikawa Madina.

“Ki kawo ta nan idan zaki je aikin, idan kin dawo sai ki zo ki dauketa kuje siyayyar”

“Wata kila zata fi sakewa idan muka je tare da kai, tun jiya bata da magana sai taka, tun safe take son na kiraka, ni kuma bana son ka ga kamar ina takura maka ne, and you know her situation duk abun da zai sakata farinciki shi ya kamata mu yi”

Tana kawai nan ya yanke wayar, sai tai murmushi.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Kamin su sai da ta kira ta fadawa Leila cewar zata je yi mata siyaya ita kuma tace sai anje da Talba kuma yana gurin aiki yace a kawo masa ita kamin ya tashi aikin. Sannan ta shiryawa Aminatu cikin atamfa mai kyau duk da kasancewar ta yi mata yawa domin tsawo da jikin Madina ba daya dana Leila ba, sai dai hakan he hana atamfar karbarta ta mata kyau sosai sannan ta saka mata hijab.

“Ba zamu je da kujera ba, daurewa zaki yi ki rika takawa”

“Ba zan iya ba akwai zafi”

“Zaki iya ma”

Madina ta rikota sai ta fara takawa a hankali da dan tsoro, tana jin zafi sai dai ba irin zafin da zai hanata takawan ba, wata kila dai da tsayin ne ba zata iya ba. Da taimakon Madina suka fito falon har da gaisa da Hajiya sannan suka nufi kofa ba laifi ta yi kokari domin da kafafuwanta ta isa isa gurin motar Madina, ta bude mata ta shiga ta zagaya bangarenta, dadi gurin Aminatu ba a magana, saboda ta taka da fafuwanta a zatonta ba zata iya ba. Sai da suka yi tafiyar rabin awa sannan suka iso Kamfani, wani irin shuki ne ya kama Madina ace wai mijinta ne ke da iko da katon kamfani kamar wannan, bayan kyau da cikar kalama da Allah yai masa.

“Hmmm Leila kina wasa da damarki”

Ta furta tana karewa kamfanin kallon, kalaman da ta yi ne suka saka Aminatu ta kalleta. Sai tai hade yawu ta ciro wayarta ta kira Talba ta mikawa Aminatu.

“Hello”

Jin muryar Aminatu ya saka ya amsa.

“Shalele”

“Na'am mun zo muna waje”

“Okay, zan aiko a shiga dake yanzu nan”

“Toh”

Ta mikawa Madina wayar, Madina ta kai wayar a kirjinta ta rumgume tare da lumshe idonta bude. Ba jimawa wata mace sanye da suit kanta babu mayafi tana sanye da sarkar cross ta nufi inda suke ta gaisa da Madina sannan ta nunawa Aminatu hanya.

“Malama Bismillah”

“Ba zata iya tafiya ita kadai ba, sai kin taimaka mata”

Matar ta rika Aminatu suka fara tafiyar a hankali har suka shiga ciki, sannan Madina ta koma motar ta tana ayyana irin kulawar da zata bawa Talba idan mafarki da take ya tabbata, sam bata hangowa kanta yadda taraiyar da Leila zata lalace idan har soyayya ta kullu a tsakaninta da Talba.
Aminatu na rike da hannun matar suna takawa a hankali har suka hau sama, daman kamfanin mai hawa biyu ne. Yadda take ganin mutane sai ya saka ta dan tsorata abun ka da bakauye, kamin su isa gurin office din Talba ya fito hannayensa duka biyu a aljihu, yana sanye da suit kala daya dana matar dake rike da ita, wato black color. Murmushi ya sakar mata sannan ya kalli matar ya ce.

“Chidima sake ta, tafiyarki”

“Okay Sir”

Ta sake ta kamar yadda ya bukata ta juya ta bi wata hanyar, har lokacin murmushi yake yi ma Aminatu.

“Tako ki zo nan”

“Akwai zafi idan wani be rika ni ba ba zan iya tafiya ba”

“To ni zan koma ciki idan ba zaki zo ba”

“Wash.. Wash... Wash... Akwai zafi”

Nan da nan har ta fara hawaye tana takawa a dolenta tana ta raki, hannunsa daya ya ciro ya miko mata alamar ta kama.

“To ka matso”

“Aa ki zo dai, Madina ta kyauta, ta gyara min ke kin yi kyau, kuma gashi har kina takawa”

Daker ta karasa inda yake ta rika hannunsa suka karasa shiga karamin office din mai dauke da wata macen bahaushiya, da alama sakatariyarsa ce, sannan ya wuce office dinsa dake hannun dama. Yana shiga da ita ta fara rabon ido sanyin ac na ratsata, har gaban kujerar dake taburinsa ya kaita ya zaunar da ita.

“Duk wannan katon office din naka ne?”

Ya daga kai yana kallon office din kamar yadda take, sai ya dan tabe.

“Ba Office dina ba ne”

Ta nuna masa hoton Daddy sai ya juya ya kalli katon haton dake manne.

“Abokin Daddyn ne mai kamfani shiyasa ya saka hotonsa, kuma yanzu yayi tafiya shi ne yace yana son na zauna a nan kamin ya dawo”

Ta yi murmushi sai shi ma yai murmushi.

“Murmushi na miki kyau, jiya ma kin yi shi da muna gidan marayun nan”

Sai tai kasa da kanta.

“Fada min me kika ci yau?”

Ta daga hannunta tana taba teburin shi kuma ya zauna a kujerar dake facin din ta yana kallonta.

“Da safe mun sha tea da birede kuma mun ci waina kwai, wannan kanenka ya zo ya duba ni, yana ta latsa min kafa yace wai Madina ta daina bari ina zaunawa, wai sai dai na yi tafiya”

Tana fadar hakan Talba ya gane Kabir take nufi.

“Ya kyauta, me kike son ki ci? Tea ko lemu”

“Bana jin yunwa”

Ya mike tsaye ya nufi firgin din ya bude ya dauko lemu ya zuba mata a lemu ya mika mata, sai ta karba da hannu biyu ta sha kadan ta rike raguwar.

“Mai office din nan fada yake idan wani ya sha masa lemu ya rage”

“Da gaske?”

Ta yi saurin kai ragowar bakinta ta shanye da sauri ta mika masa cup din.

“Na shanye duka”

Ya karbi cup din ya juya yana dariya ba tare da ta gani ba. Sai da ya aje cup din sannan ya juyo ya dauki wasu takardun yana kallonta.

“Mai office din nan baya son ayi masa bachi a office”

“To ai ba bachi zan yi ba”

“Ni ma ai ban ce bachi zaki yi ba, zan yi wani meeting ne kar na tafi ya shigo ya tarar kin yi bachi”

“Ba zan yi bachi ba”

Ya daga mata kai sannan ya dauki takardun ya fice a office din ya barta yaje meeting ko da ya dawo tana zaune tana kallon tv.

“Ba ki yi bachi ba?”

“Ai kai ce mai kamfanin bayan son ayi masa bachi, ban yi ba”

Yayi murmushi.

“Me kike son ki ci yanzu?”

“Bana son komai”

“To ni yunwa nake ji, bari mu kira Madina ta zo mu tafi siyayyar mu dawo na kaiku gida sai na je gida ni ma na ci abinci”

Ta daga masa kai sai ya dauki wayarsa dake nan ya kira Madina, ringing daya ta daga.

“Hello”

“Baki tashi aikin ba?”

“Ban gama ba, amman zan iya fitowa yanzu, tana bukatar wani abu ne?”

“No ina son na tafi gida ne”

“Okay gani nan zuwa”

Ya aje wayar, sannan ya zauna a kujerar dazun yana kallon Aminatu.

“Shalele, fada min me kika fi so lokacin da kina gida?”

Ta fara bashi labarinta da yadda take rayuwar a kauye da yadda yayanta Sanusi yake yawan tsokanarta har zuwa abubuwan da suka faru sai gata tana ta kuka hawaye na sauko mata.

“Ya Sanusi ai yana da gaskiya, ke raguwa ce abu kadan sai kuka, ungo wannan ki share hawayenki”

Ya mika mata tissue, sannan ya tashi ya dauko mata ruwa ya zuba mata a wani kofin ya mika mata, ta karba ta sha wasu hawayen na sauko mata.

“Shikenan komai ya wuce”

Ya fada yana jin wani irin tausayinta ma kara kamashi. After like 30 minutes Madina ta kira wayarsa ta sanar masa tana waje.

“Ta so muje ta iso”

Yana fadar hakan yai gaba sai ta ce.

“Yallabai ba zan ita tafiya da kaina ba”

“Raguwa”

Ya fada sannan ya dawo ya rika suka fita tare, yana rike da ita har suka sauka kasa yana fitowa direbansa ya janyo mota ya iso inda suke tsaye, sai Talba ya budewa mata front seat ta shiga ta zauna ya rufe sannan ya kalli Madina dake tsaye.

“Bismillah”

Ta bude motar ta shiga duk kuwa da kasancewar ba haka ta so ba, a zatonta zai barta ta shiga front seat din ya saka Aminatu a baya, shiyasa ta bar motarta a gurin aikin ta hau Napep zuwa nan. Key din ya karba ya shiga motar yaja suka kama hanya. A hankali yake driving har suka isa Wani babban super market dake cikin garin gusau, yana yin fakin Madina ta bude ta fito ta zagaya ta sauri saboda ta samu rika Aminatu kamin Talba ya rika ta, har ga Allah bata son rikon da yake mata zuciyarta tana sosuwa ba kadan. Ta bude side din Aminatu ta rikota ta fito, yana gaba suna baya suka shiga super maket din.

LEILA POV.

Har wani huci take tana fadawa Momy abun da Madina ta fada mata.

“Leila baki da wayo baki da tunani, yarinyar so take ta dora ki a keken bera, idan ba haka ba mi zai saka ta rika kiranki tana fada miki abun da yai ko yace? Ni fa gani nake kamar so take ta hada ku”

“Haba Momy kamar baki san Madina ba, Wallahi ba zata yi haka ba”

“Aman yadda take fada, ni na san Talba ba zai aikata hakan ba har da wani kiranta Shalele tana karawa abun gishiri kawai, zan dai iya yarda tace a kira mata shi, dan haka ki yi hankali da ita”

Har Leila ta bude baki zata yi magana sai ga Amal ta shigo sanye da uniform din makarantar boko har dan gudunta.

“Momy Daddy yana falo yana jiranki”

“Yana jirana? Kamar ya? Wani abun kika fada masa ne?”

Amal ta yi shiru tana kallon Momy, kamin Momy tai wani yunkuri har Daddy ya shigo dakin kana ganinsa kasan ransa a bace yake.

“Amina kina ji kina gani Mu'az ya fita da yarinyar nan gidan nan?”

Momy ta hade yawun bakinta ta kalli Amal.

“Wallahi ban dauka abun zai kai haka ba, ban dauka Daddy zai dauka da zafi ba, Momy ki yi hakuri ba zan kara ba”

Daddy ya kalli Amal sannan ya kalli Momy rai a bace ya ce.

“Okay hakan yana nufi hanata kike ta fada min idan wani abun ya faru ko? Taya Mu'az zai dauko yarinya ya kawo ta a gidan nan sannan ke da yayanki ku wulakantata ki saka ya fitar da ita gidan nan? Ni kuka wulakanta ba shi ba ko ita, a tunani ko kare Ma'az ya dauko ya kawo a gidan nan ya kamata ki mutuntashi”

“Ban ce ya fita da ita ba, Leila ta yi rantsuwa yarinyar ba zata zauna a gidan nan ba, tace sai dai ya zaba ita ko yarinyar, kuma ka san babu yadda za ayi na bar Leila na zabi yarinyar da ban san asalinta ba”

“Miyasa baki tura Leila waje ba kin bar yarinyar? Ke har kullum ba zaki nuna cewa danki ba na ki bane dan wasu shi ne naki? Idan kin tozarta Mu'az kin ci mutuncin ribar mika ce? Akan Mu'az zan iya batawa da kowa, kuma ba zan dauki raini akan jinina ba, ba zan taba yarda a nuna masa isa ko rashin galihu ba”

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, Engineer wannan soyayya da kake nunawa Talba ta yi yawa, idonka ya rufe ruf baka ganin komai sai shi, ko yayanka baka so yadda kake son yaron nan, tsintacciyar mage bata taba zama mage ba, ni fa matarka ce amman idonka ya rufe akanTalba kana fada min magana son ranka dan Allah ka...”

Momy bata karasa ba Daddy ya nuna kansa a razane.

“Amina? Ni kike fadawa Tsintacciyar mage bata mage? Mu'az ne tsintacciyar mage? Yaron da ubansa ne sanadiyar arziki da nake ci a yanzu? Yaron da dan'uwana ya yafe karatunsa saboda ni na samu ingantaciyar rayuwa? Yaron da soyayyar mahaifinsa ta saka ya saka shi barin wasiyar idan an haifi masa da a saka masa sunana? Saboda uban yaron nan na samu ilmi har na zama abun da na zama a yanzu, karki manta babu abun da Mu'az yake nema a duniyar nan, dan'uwana be mutu ba sai da ya bar masa abun da zai isheshi kula da rayuwarsa, yaron da ba uwa ba uba? Ai ko da dan'uwana yana raye ba zan dauka a musgun ma dansa ba balle kuma ba shi da rai, dan'uwana yayi min komai Amina, dan'uwa na zame min uwa ya zame min uba, a lokacin da kowa ya kyare mu, dan'uwana shi ne ci na shi ne sha na, idan ina ciwo shi ne, saboda ni dan'uwana ya rasa rayuwarsa, yanzu kuma kike kiran dansa da tsintacciyar mage? Saboda ni dan'uwa na rabu da matansa biyu amman yau kin aibanta dan dan'uwana a gabana”

Hawaye ya cika idon Daddy.

“Na gode, indai maganar dana da nake ne ya zame miki fitina da tashin hankali, to na sauwake miki ki tafi inda zaki zauna ki samu kwanciyar hankali da natsuwa, ni kuma zan kawo wanda ke son dana wanda zata so abun da ya ke so, domin na tabbatar da Kabir ba zaki yarda ki masa wannan wulakancin ba, ba zan jure ko maganar banza a fadawa Mu'az ba, Wallahi ka bata masa rai kara a bata min rai, kuma har a bada ba zan wulakanta jinina ba...”

Momy ta daki kirji da karfi tana fadin.

“Engineer sakina kai?”

Amal ta dora hannu akai ta fashe da kuka, Leila kuma ta yi sauri girgiza kai tana kallon Daddy daya juya zai fice daga dakin.

“Daddy no please be kamata kai haka ba, abun da ba ayi da kurciya ba be kamata ka yi shi a yanzu da girma ya kama ma...”

Juyowa Daddy yai ya kalleta.

“Ba ke kika ja komai ba? Akan dana, zan iya batawa da kowa you too should be very careful...”

Tsayawa tai cak tana kallon yadda ransa ya bace har wani huci yake irin ma su na manya. Sai da ya fice sannan ta juyo ta dawo gurin Momy dake tsaye tana ganin komai kamar a mafarki.

“Momy dan Alla... ”

Tassss Leila ta wanke fuskar Amal dake maganar da mari.

“Dan ubanki ba ke kika ja komai ba? Duk abun da akai a gidan nan yana bakinki, komai aka yi sai ki je kin fadawa Daddy, yanzu ai kin ga ribar abun ko?”

“Ya Kabir ne ya fada min, ni ban dauka abun zai saka a saki Momy ba..”

Momy ta zauna tana nuna kanta.

“Yau ni Alhaji zai saki saboda Talba? Abun da be taba min ba? Saki? Ni Aminatu?”

Leila ta yi saurin dafata tana hawaye.

“Momy dan Allah ki yi hakuri, zafin zuciya ne da bacin rai nasan anjima zai sauko ya gane cewar yayi kuskure”

“Kar ma ya sauko, awa daya ba zan kara a gidan nan ba, je ki kira min Mairo ta zo ta hada min kayana ke da Shi sai kun dandana zafin rashina”

Momy ta fada tana kallon Amal dake kuka.

“Momy idan kika tafi mu zaki bari a damuwa dan Allah ki yi hakuri”

Leila ta fada tana kuka.

“Duk bakar yarinyar nan ce taja komai, duk ita ta haddasa mana fitina a gida”

Amal ma ban da kuka babu abun da take, bata aikata wani abu taji ta yi nadamar aikata shi ba irin fadawa Daddy abun da ya faru. Momy ta mike tsaye a fusace ta sauka kasa ta nufi hanyar kitchen inda Mairo da zulai suke suna aikin hada abun karyawa.

“Mairo Zulai ku shiga dakina ku janyo akwatunana ku zuba tufafi da yake wardrobe”

“To Hajiya”

Suka bar kicin din da sauri suka nufi upstairs, sai ta sake nuna kanta.

“Ya sake ni? Lallai Engineer...”

Ta girgiza kai tana jingina lamarin.

FARUQ POV.

Ko kadan sakin da Faruq yai ma Baturiya be yi ma Mama dadi ba.

“Saki ba shi da dadi, amman halin yarinyar nan ya wuce inda muke tunani, sai dai bana son wannan abun ya taba zumuncin mu”

“Inshallahu babu abun da zai samu zumuncin mu Mama, gobe zan je na kwaso tufafina na dawo da su anan, zan bar Sultan a nan ni kuma nan da kwana biyu zan bar garin nan na tafi nijar, idan Allah ya buda mana sai na samo a can idan na dawo sai na ayi wani auren, ita kuma zan cigaba da kula da ita saboda cikin dake jikinta”

“Yaya ba za'a gyara ba?”

Cewar Aisha cikin damuwa sai Faruq ya girgiza mata kai.

“Bana son na yi uku, na riga na yi biyu kuma na riga na cire Rafi'a a raina, ba zan iya zama da ita a wannan sabon halin da ta fara ba, kuma duk wani cin mutuncin daya kamata ta yi min, ba ta inda ta raga min, nan gaba ban zan yadda abun zai zama ba”

“Allah yasa haka shi yafi alheri ya baka ta gari, ita kuma ya shirya ta”

“Amin, ranar alhamis din nan nake son tafiya inshallah, tare da Malam Sirajo”

“To Allah yai maka fatahi a tafiyar, mutane na samowa, ko dan gidan Amadu ya samu yana dawowa ya siye gida da babur, amman tafiyar ce abun tsoro gashi ance ramen yana rusgawa da mutane”

“Kawai ki min addu'a Mama dacewa kawai ake so”

“To Allah ya datar da mu”

“Ameen”

Ya amsa sannan ya kwantar da Sultan dake jikinsa yana bachi kan shimfidar Mama.

“Baka nan kenan za'ayi bikin Aisha”

Mama ta fada tana kallon danta cike da tausayawa.

“Bana son na kara sati a garin nan kam”

Ba dan neman halal kawai yake son tafiyar ba, har da gujewa Baturiya saboda abun da tai masa da kuma sakin da yai mata ya tsaya masa arai yana jin babu dadi musamman idan ya tuna cewar saboda talauci tai masa haka. A dakin ya bar Sultan saboda Mama ta kula masa da shi, shi kuma ya nufi dayan dakin da ba a karasa ginewa ba ya shimfida tabarma da zane ya shimfida, sannan ya kunna maganin sauro ya kwanta, sai dai ko kadan bachin be ziyarce shi ba, sai tunani yake kala kala har safe.

BATURIYA POV.

Bata bar gidan ba sai da safe, sannan ta saka wasu tufafin ta saka Hijab ta rufe gidan ta tafi gidansu.
Tun a Napep ta fara kirkirar kuka, sai dai kukan be zo mata har sai da ta sallami mai Napep din ta shiga cikin gidan, sannan ta fashe da kuka tana faduwa tana tashi hankali kowa sai da ya tashi a gidan. Cikin kuka ta fadawa Umma irin abun da ta fadawa makontata, a take ran Umma ya ace ta dauki waya ta kira Yayansu ta fada masa abun da ya fara sannan ta dada masa cewar tana son abi mata hakkin yarta.

“Aa Umma ba a haka ko dan saboda zumunci”

Cewar Alhaji Alfa daga can cikin wayar, sai Umma ta rufe shi da masifa.

“Shi be duba zumuncin ba yai mata abun da yai? Ga ta da ciki yai mata wannan duka haka ga kuma cin mutunci saboda wasu karuwan banza a waje, ba zan lamunta ba idan kai ba zaka iya ba ni zan dauki mataki da kaina, domin ba zan lamunta aci zalin yata ba bayan bakin talauci sannan kuma ya hadota da saki bayan ya mata duka”

“Zan yi wani abu akai Inshallahu, aman ita ma ki bincike ba zai yiyu haka siddan Faruq yai mata haka ba ba tare da wani dalilin ba, Faruq ba irin mazan nan ne ba Umma, amman yanzu zan yi wani abun inshallah”

Da haka suka yi sallama, sannan Baturiya ta tashi ta shiga dakin Umma tana kuka kamar gaske, tana shiga ta bude jakarta ta dauko wayarta ta akashe ta saka wayar karkashin gadon Umma.

“Kuma cikin nan Wallahi zubar da shi zan yi, ina zubar ba na cika idda na auri saurayi kai kuma kai ta fama da talauci auren ma sai ya maka wahala”

Ta fada tana wani cika, sai a yanzu take jin zafin sakin da yai mata kukan na gaske da gaske ya zo mata.

Shin kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji

Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Madina ce take ta mata zaben tufafin da zata saka, daga atamfa zuwa abaya da shadda da kuma lace ta daukar mata kusan kala 25, ban da talkami da hijab da veil. Suna zuwa gurin biya kamin su yi wani yunkuri ta mika atm dinta. Talba ya kalleta.

“i can pay”

“Dan Allah ka bari na yi wannan aikin ladar”

Be saki cewa komai ba, ya kalli Aminatu.

“Muje mu jirata a mota”

Ba musu Aminatu ta mika masa hannu ya rikata tana takawa a hankali suka fice, kamar dazun a yanzun ma front seat ya zaunar da ita sannan ya zagaya ya zauna a side dinsa.

“You got lucky ba yayanki kadai yake son hidima dake ba, har da Kawar Matata”

Kallonsa kawai tai ta sauke kai kasa, shiru ne ya biyo baya har Madina ta fito tare da masu rika mata ledodin kayan Talba ya bude musu bayan motar suka saka, sannan ta rufe ta bude back seat din ta zauna, yana kokarin yin reverse ta mika masa box din agogon hannu that worth 150k.

“Zan yi farinciki idan ka karbi wannan kyautar daga gareni”

Kallonta yai sai kuma ya kalli Amintu.

“Shalele karba min”

Aminatu ta karba ta rike ba tare data buda ba, har suka isa gidansu Madina be karbi agogon ya duba ba, balle yai mata godiya, hakan da yai sai yasa ta ji wani iri, yanzu kam ta tabbatar akwai babban aiki a gabanta, domin samun abun da zai burge Talba a take ko kuma ya dauki hankalinsa ba abu ne mai sauki ba.
A harabar gidan ya faka motarsa, ya mika hannu ya budewa Aminatu.

“Ki taka da kafarki ki fita, kuma ki rika tafiya ke kadai ba sai an rika ki ba”

Ta lake kafada tana dan turo baki, sai dai bata ce masa komai ba kuma bata yarda ta kalli inda yake ba. Shi kam sai kallonta yake yana ayyana irin shagwabar da take a gaban iyayenta domin kana ganinta ka san shagwababbiya ce, dan farin ma wani yai shagwaba balle auta autar ma ta maza.

“Yaya Madina zaki rika ni ko?”

Ta fada tana jiya fuska ta kalli inda Madina take tsaye tana mikawa hadiman gidan ledidin hannunta.

“Eh”

Ta fada sannan ta nufo inda Aminatu take zaune ta rikata, sai da Aminatu ta aje masa agogon sannan ta fita Madina ta rufo masa motar.
A tunaninta zai mata godiyar siyayyar da tai ma Aminatu amman bata ji hakan daga bakinsa ba, ta san kuma hakan ya masa dadi ko da ba a fada ba, sai a yanzu ta tabbatar da miskilacinsa ya wuce inda take zato.
Sai da suka shige cikin main house din sannan ya ja motarsa ya bar gidan, at first restaurant ya so ya tafi ya ci abinci even though baya son cin abinci a waje sai dole, but yana son ya kaurace ma cin abincin Momy saboda ta fahimci be jidadin abun da tai masa ba, sai dai hakan ba zai saka shi gaba da ita ba, kamar yadda dazun ma be kasa kiranta a waya yai mata barka da safiya ba, bayan kuma ya saba da shiga part din ko wace safiya ya gaishe ta. Kamin ya karasa restaurant din kiran Amal ya shigo wayarsa, sai yai picking call din ya saka wayar a hands-free ya aje ta kusa da shi.

“Lil Sis”

“Yaya”

Ta amsa masa cikin kuka, ya san halinta da shagwaba sometime kan sily abu sai tai ta kuka, hakan yasa be tashi hankalinsa ba.

“Waya taba ki me kike yi ma kuka?”

“Momy ce ta yi fada da Daddy, kuma har ya sake a ta debi wani tufafinta ta bar gidan, ta bar mu ni da Leila tun dazun sai kuka muke”

Wani irin faduwar gaba ne ya same shi, sai yai sauri sauka daga titi ya faka motar gefe, ya dauki wayar ya kai kunnensa.

“Ba a wasa da irin wannan maganar Amal”

“Wallahi da gaske nake”

“Miya faru?”

“Ni na yi komai, Ya Kabir ya fada min abun da ya faru ni kuma na fadawa Daddy, shi ya zo bangaren Momy yana ta masifa and Momy ta kiraka da tsintacciyar mage, shi kuma yace ba zai dauka ba, shi ne ya saketa...”

Be ce mata komai ba ya yanke wayar, ya shiga kiran Daddy, amman har wayar tai ringing ta gaji ta tsinke Daddy be daga ba, Talba ya sake kiransa nan ma the same thing, tun yana kira yana sa ran zai dauka har ya cire rai, hakan ya tabbatar masa da cewar ran Daddy ya bace sosai, domin abu ne mai wahala yai masa two miss calls be daga ba, amman a yau ya jera masa 11 miss calls be yi picking ba. Sai ya sake kiran Amal.

“Yana gida?”

“Aa ya fita”

Ya yanke kiran sannan ya duba agogon hannunsa biyu saura kwata ya gani, take hau titi ya fisgi motar kamar zai bar gari, cikin yan mintuna sai gashi Harabar ma'aikatar su Daddy, ko fakin din kirki be yi ba ya fito da sauri ya shiga cikin ma'aikatan, kusan ya san mutane da yawa a ciki kamar yadda mutanen gurin ma suka san shi saboda yawan fadarsa da Daddy yake da kuma zuwa gurin, sai dai be tsaya gaisawa da kowa ba daman ba gaisuwar yake so ba, saboda ta zame masa kamar ta dole ce kasancewar su abokan mahaifinsa. Kai tsaye ya nufi bangaren da office din Daddy yake yana ta zuba sauri. Sai dai yana shiga sakariyar ta hana Talba ganin Daddy.

“Yace baya son a dame shi kowaye ya zo kar a bari ya shiga ciki”

“Kin san waye ni kuwa?”

Talba ya nuna kansa.

“Na sani dan Allah kai hakuri, aikina nake yi”

Ta fada cikin damuwa, sai ya wuce ta ya karasa gurin office din ya bude ya shiga ita kuma ta biyo bayansa da sauri tana kokarin dakatar da shi.

“Duk kika yi kuskuren taba ni sai na mareki Wallahi”

Ya furta yana nuna ta da yatsansa, babu alamar wasa a fuskarsa. Daddy dake tsaye yana kallonsu ya ce.

“Amman na tabbatar da kai ne, korarta zaka yi, yanzu kuma kana kokarin hanata aikinta, you can go Hannatu”

Sai ta juya da sauri ta fice. Daddy ya kalleshi.

“Ya akai?”

“Haba Daddy miya saka zaka yi haka?”

“Hey my friend, control your tongue, I'm your father and you're my son, so ni zan tambayi dalilin da zai saka kai wani abu ba wai kai tambaye ni ba”

Talba ya karaso kusa da teburin Daddy cikin yanayin damuwa.

“Daddy please, be kamata ba Wallahi, da girmanku ace kun rabu? Mu ya kake son ku yi? Baka duba Amal da Leila ba? Baka duba ni yadda zan ji ba? Da wane ido zaka kallemu? And baka yi tunanin yadda Momy zata ji ba?”

“So a idonku nine mai laifi? Ni baku ayyana yadda zan ji ba?”

“Ni kullum a gurina kai ne mai laifi daddy, kai namiji ne ya kamata ka rika kawarda ido, amman sai ka rika biyewa Momy da take mace? Hankalinta da tunaninta ba daya ba ne da naka”

Daddy yayi murmushi ya nuna masa kujera.

“Have a seat my friend”

“No ni ban zo nan domin zama ba, kawai na zo na dauke ka ne mu tafi da kai ka bawa Momy hakuri ka dawo da ita”

“Have a seat”

Daddy ya maimaita wannan karon ya fada tare da zaunawa. Sai da Talba ya sauke ajiyar zuciya sannan ya zauna.

“Fada min gaskiya, ban san ka da karya ba Son, abun da Amina tai be bata maka rai ba?”

“I feel bad, amman be kamata ya saka ka yanke wannan hukuncin ba”

“Ban yanke hukunci saboda ta kori yarinyar daka kawo ba, na yanke wannan hukuncin ne saboda ta kira ka da tsintacciyar mage”

“Fushin zuciya... ”

Daddy yayi saurin dakatar da shi with serious face ta hanyar daga masa hannu.

“No, bari na baka wani labari da ban taba fada maka ba. A cikin wani babban gida mai rufin asiri mata har hudu, kowa a wannan gidan yana da manyan y’ay’a da kanana, ko wace mace a cikin matansa ta haihu shida wata tara wata goma sha daya, sai karamar matarsa ce kawai ta haifi yaya biyu maza wanda ta kasance karama ce kuma ita ce ta hudu, tana tsaka da rainon yayanta sai mutuwa ta sallamo mata, yaya da kanensa suna daji gurin noma, ka zo kiransu aka fada musu cewar mahaifiyarsu bata da lafiya, sai dai kamin su kawo rai yai halinsa, ita ce karama kuma ita ta riga tafiya ta bar kananan yayanta guda biyu, haka yaran biyu suka tashi cikin yan'ubanci da kuma kyara ta matan uba, idan uban ya dawo sai a nuna ana son su kamar za a hade su,

idan kuma ya saka kafa ya fita abinci ma sai sun yi bara su ci, wata rana kwatsan wannan mutuwar ta sake kwankwaso kofar mahaifinsu, kuma ta dage sai da ta tafi da shi, daga lokacin sai rayuwa ta kara zame musu abun tausayi, domin a gidan da suka taso gida ne da babu hadin kai a ciki, kowa kansa ya sani kuma ga kishi da nunawa uba aka hada ba uwa ba, idan aka dafa abinci masu ake bawa, ba marasa uwa ba, idan sallah ta tashi sai dai yan'uwa mahaifiyarsu su yi musu dinki, wani lokacin abinci ma a can suke zuwa su ci, suna cikin wannan rayuwarsa sai yayan ya fara bin shanu yana rakiyarsu zuwa inda ake saidawa sai masu shanun su biyashi, sai kuma ya shiga daji yai itace sai ya shiga gidaje ya bada itacen a bashi abinci sai kawo wa kanensa, kudin da yake tarawa kuma idan kanensa yana jin yunwa ko rashin lafiya ta kama shi, zai siya masa magani ne, da haka ya fara faskare, da duk wani aikin karfi da yan'uwan mahaifiyarsa

suka samu labari sai suka zo suka dauke su suka tafi da su gurinsu, sai dai hakan be kashe guiwar yayan ba, da yan kudin da ya samu ya saka kenansa a makaranta, kullum kokarinsa na yadda dan'uwansa zai gina kansa ne, da wannan tunanin ya tsallaka zuwa birni yana achaba, daga nan ya fara zuwa kudu, idan ya samu kudi sai yace a bawa Mu'azu, a siyawa Mu'azu abu kasa, a biya masa kudin makaranta, sannu sannu dan'uwansa yana ta karatu shi kuma yayansa yana ta neman kudi saboda rayuwar kanensa ta inganta, achaba da yake a can sai ya karbe shi har ya zamana yana zuwa siyen wasu abubuwa daga nan arewa ya kai can, wani abun kuma sai ya siyo ya zo da shi nan, kamin a ankaro kudi suka taso masa kofafin arziki suka bude masa, sai ya dawo a nan yai aure, ana zaune kalau kanensa yana zuwa makarantar kwana a birni idan hutu ya samu sai ya dawo gida, sai matar yayan ta fara nuna bata son kanensa tana hana shi yi masa wasu abubuwan daya kamata, ganin haka yace ba zai iya sake dan'uwa ba, amman zai iya canja mata, sai ya sake ta ya auro wata, ita ma da ta zo sai ta fara nuna wannan halin, a take ya sallame ta ya auro wata, bayan ya jaddada nata cewar shi kam a duniyar nan be da kamar dan'uwansa, sai matar nan ta rike kenan da mutuncin da amana, shi kuma ya maida hankali gurin kasuwancinsa, har ya zamana yayyunsa da suka wofintar da shi a wacan lokacin suka dawo suna neman ci a karkashin inuwarsa, wasa wasa ya fara siye gonaki da gidaje irin na kauye yana saidawa yana samun riba, kamin kace kwabo ya zama daya daga cikin masu kudin kauye na wacan lokacin duk da kasancewar yana da samarta ba tsoho ba ne, da haka ya fada siyasa sai kuma abun ya karbe shi kofofi suka bude masa, yai taraka kuma ya cinye, sai dai har kanensa ya gama karatu ya tafi jami'a Allah be bawa yayansa haihuwa ba, yana cikin karatun ya hadu da wata a jami'ar suka yi aure, yayan ya siya masa gida a birni suka zauna, ana wata na uku da saurensa ya samu aiki a babban gurin saboda yayansa babban dan siyasa ne na taraiya, a kuma wannan lokacin matar yayan ta samu ciki, a kullum wakensa idan ta haifa masa namiji za a saka sunan kanensa, idan kuma mace ta haifa za a saka sunan mahaifiyarsa, ashe Allah be yi ba zai ga abun da zai haifa, wata rana aka samu wani gurbi na babban matsayi a Lagos, sai ya dage akan sai kanensa za a bawa saboda yana da takardu da duk wani abu da ake bukata, sai dai abu na yan siyasa su ma wadancan suna so, bayan ya bada sunan kanensa da takardunsa, sai abokin hamayyarsa yace ya saurari abun da zai same shi matukar be janye kudirinsa ba, be fada masa baki da baki ba, amman ya fada ta inda zai iya ji kuma ya ji, amman be janye kudirin ba, abun ka da mutanen kauye ana zaune kalau kafarsa ta fara kumbura har ya zamana baya iya zuwa majalisa, har ta kai ko gidansa baya iya fita, cikin sati jikinsa ya kumbura kamin wani makon ya dawo ya ce ga garinku, haka muka ta jimamin rashinsa musamman ne kuma mutuwarsa bata hana Allah hukuncinsa ba na dora ni a wannan matsayin, ashe kuma wani kukan yana tafe a gaba, a lokacin da muke ta murna matarsa ta shiga watan haihuwarta zata haifa mana da ko ya, ashe ban kwana take ta mana ba mu sani ba, ranar da ta haihu aa fiti ana da lafiya kalau mahaifiyarsa kuma ta koma ga Ubangijinta... ”

Tun da Daddy ya fara bawa Talba labarin be mumfasa ba sai da ya kai aya.

“Ka san waye wannan yaya da kanen Mu'az...?”

Talba ya kalli Daddy hawaye na sauko masa, kamar yadda suke saukowa Daddy.

“Kai ne kanen Daddy shi ne Yayanka... ”

Daddy ya girgiza kai yana cige bakinsa da karfin sosai yake yakar zuciyarsa yana hanata kukan dake son gabato masa da shi, daya wuce na zuciya har yake neman muhalli a bakinsa.

“A haka kaka tunanin wata macen zata kalli kwayar idona ta kira dan 'uwana na jini da jini da tsintacciyar mage kuma na kasa fusata na kasa yin komai? Macen da take karkashin ikona da kulawata? Ina raye wata mace tana nuna min tafi son yayanta da dan'uwana na jini? Ina jin sonka a cikin jinina Mu'az, ina jin wani irin son a jini da zuciyata, bana jin akwai wani uba da yake son dansa kamar yadda nake sonka, ko kadan bana son na ji wani abu da zai bata maka rai, zan iya daukar komai ban da a taba ka”

Talba ya mike tsaye hawaye na sauko masa ya nufi windows din office din Daddy ya tsaya. Sai Daddy ya dauko tissue ya goge hawayensa yana kallon Talba.

“Ban taba baka labarin nan ba, saboda bana son ka ji a ranki cewar kai maraya ne, alhalin ina raye”

Talba kamar jiran kalaman Daddy yake, sai ya fashe da kuka marar sauti irin na maza ya jimke hannunsa zuciyarsa na sosuwa da labarin da Daddy ya bashi. Da hannunsa na dama ya share hawayensa sannan ya juyo ya kalli Daddy yana jin wani irin shaukin kaunarsa.

“Ka yi duk abun da ya kamata Daddy, shiyasa ban taba jin maraici ba, kuma ban taba tambayar labarin iyayena ba, ka bani gata ka nuna min kauna wanda ba ko wane mai uba ke samu ba”

“Abun nan akwai ciwo Mu'az, saboda ni ma na taso a maraici, kana ji kana gani abu ya gagareka, kana gani a nun maka abu nan ba naka ba ne, idan aka bata maka rai, babu uwa ko uba da zai rarrasheka ya baka hakuri, musaman ma uwa, shiyasa ba zan taba bari kai maraici ba, idan har kaga ka rasa sai idan bana raye, ko da ma ace na mutu na ginaka kuma na bar maka abun da zai taimaki rayuwarka ba zaka taba rasa komai ba, ba zaka taba kukan rashin uwa ko uba ba, musamman uwa”

Talba ya gyada kai wasu hawayen na sauko masa.

“Kamar yadda na ji a yanzu nan Daddy, amman duk da haka Ina rokon Alfarma a yafewa Momy, ita ma ta rike ni kamar danta, na taso ban ta wata uba ba bayan ita, dan Allah Daddy ka dawo da ita”

“Of course zan dawo da ita, do you think I can live without Amina? Zan dawo da ita amman sai ta karbi hukuncinta, ni ma ina fatar za a daga min kafa”

Talba yayi murmushi idonsa na cika da wasu hawayen.

“Ina kaunarka Daddy, Allah kara maka lafiya”

“Amin Allah ya maka albarka”

“Amin”

Ya amsa sannan ya dauki tissue ya gyara idonsa, sannan ya nufi kofar fita.

“Mu'az ina ka kai yarinyar nan?”

“Gidansu Madina”

“Ka dawo da ita gida”

“A can din ma ta fi sakewa, Madina tana sonta”

“Baka da inda yafi gida, kuma be kamata akaita ko'ina ba, bayan ga inda kake da iko”

“Na ji, amman sai ka fara dawowa da Momy”

Daddy yayi murmushi yana daga masa hannu alamar ya tafi, shi ma murmushin yai kadan ya fice yana jin zuciyarsa wani iri, samun kansa yai a motarsa yana ta sauke ajiyar zuciya, be taba jin irin yadda yake ji a yau ba. Sai dai babu wanda ta fado masa a rai sai Aminatu, shi da be taba ganin iyayensa ba, be san su ba amman a yau yaji yana marmarin ganinsu yana kewarsu balle ita data rayu da iyayenta ta girma tare da su ta san dadinsu ace an raba ta da su lokaci daya, kuma a gaban idonta, ya tabbatar abu ne da ba zata taba iya mantawa da shi ba, ba kuma zai gogu a zuciyarta da idanuwanta ba.

A masallacin gurin yai sallah azahar sannan ya fito yana ta tukin ba dan ya san inda zai je ba, baya tunanin zuwa gida a yanzu, dan baya jin zaman gidan zai masa dadi, but ina zai je? Office? No baya bukatar komawa can, gurin Ali? Nope zai fara damunsa da maganar Leila, haka yai ta yawo idan ya gaji da tukin sai ya saka motarsa ya zauna a motar, uku da rabi ya nufi gidan marayunsa be fito ba sai hudu da rabi. Kai tsaye ya nufo gidansu Madina domin zuciyarsa ta bukaci ganin Aminatu, be kira Madina ya fada mata gashi zuwa ba, balle ta san da zuwansa, he just want go ba tare daya sanar mata ba, sai da ya isa gate din gidan sai kuma ya ji wani iri, kar mutanen gidan su ce ya cika zuwa, tun da dazun ma ya zo, gashi yanzu baya cikin yanayin na walwala. Amman ya kamata ya koma b tare da ya ga Aminatu ba? Bayan ya kudurtawa kansa son magana da ita? Hannu ya kai ya dannn horn sau biyu mai gadin ya leko ya ganshi sai ya koma ciki ya bude masa gate din. Tun kamin ya karasa harabar gidan ya hango Aminatu zaune a parking lot sanye da daya daga cikin rigar da suka siyo dazun picking color, bakinta ya sha man lebe har wani sheki yake gashin kanta kuma ya sha gyara, an basa mata shi ya sauko har bayanta, sai wata yar karamar farar hula wanda ke bayyana gashin tsakiyar kanta da kasan gashinta, sai a lokacin ya tuna dazun be kaita gurin gyaran gashin ba, and now he think Madina ta kaita ko kuma ta gyara mata. Tana zaune kan kujera kusa da wata mota, sai dan karamin teburi a gabanta mai cike da littafai textbooks hannunta rike da biro. Ana bude gate din ta dago tana kallon motarsa har ya karaso kusa da ita ya faka motar ya sauke gilashin motar yana kallonta. Ita ma kallonsa take har ya bude motar ya fito ya rufe a hankali ya karaso kusa da ita cikin yanayi na damuwa.

“Ina wuni”

“Lafiya kalau, me kike a nan ke kadai?”

“Na gaji da zama ciki ne shi ne Ya Madina ta fito da ni tace wai na sha iska, ta bani abun rubutu”

“Kin iya rubutu ashe?”

“Ajami ba”

Ya kai hannu ya dauki littafin da take rubutu akai.

Ina samun natsuwa a kalamanka, kamar yadda ganinka ke kwantar min da hankali, rashinka yana nufin mutuwata, samunka kuma farincikina

Yayi murmushi bayan ya gama karantawa, sannan ya kalleta.

“Ashe kin iya kalaman soyayya”

Sai tai kasa da kanta tana murmushin daya kara bayyana kyauta da hasken bakar fatarta.

“Ina rubutawa wani saurayina shi kuma yana rubuto min, idan zan tafi talla sai ya ba ni ta shi, ni kuma na a shi tawa, duk da ajami muke rubutawa, kamin rayuwarmu ta canja, ni na dawo nan shi kuma ya tafi inda ba a dawowa”

Ta karasa idanuwanta na cika da kwalla. Sai ya risina gabanta yana kallon kyakkyawar fuskarta.

“Kin rasa abubuwa da yawa, kina da juriya na injina miki, yanzu fada min ya kike ji?”

Ta dago ta kalleshi.

“Ba dadi, sabawa da mutanen da baka sani ba, abu ne mai wahala, na kasa manta iyalina”

“Na fahimta”

Ya fada yana kallon wani gurin dabam, hakan ya bata damar kare masa kallo, fari ne fes irin farin nan mai kyau da daukar ido, ga wani dogon hanci da sauko masa gashin kansa ma sai sheki yake, abu ne mai wahala a iya yi masa kallo daya a kawar da ido. Ba kyaunsa ne kadai abun da idanuwanta suke nuna mata ba, har da damuwar dake fuskarsa domin bata taba ganinsa a haka ba.

“Kai ma kana da damuwa...?”

Ta tambaya cikin tsoro da fargabar irin amsar da zai bata, juyowa yai ya kalleta sai tai arba da kyakkyawan Murmushin daya fadada fuskarsa.

“Ya akai kika gane?”

Ta yi shiru tare da sauke idonta kasa.

“Ina ce miki Shalele kin cancanci sunan, saboda kin rayu da iyeyenki kin jin duminsu, kin san muryarsu, kin san farincikin da damuwarsu, a karon farko yau na ji ina kewar mahaifiyata duk da kasancewar ban taba ganinta ba, amman ina jin kamar na kirata ta amsa min, kamar tace Talba be dace kai wannan ba, wannan ya dace kai, ban san maraici ba amman ina jin son ganin mahaifiyata ko da sau daya ne a rayuwata”

Yanayin yadda kalaman suke fitowa daga bakinsa kadai sun isar da kewar dake zuciyarsa.

“To ai Daddy yana raye, ka rika kallon dabi'unsa da kamaninsa kamar na mahaifinka, mahaifiyarka kuma sai ka nemi hotonta ka rika kalla”

Murmushi yake yana kallonta kamar ba shi ba.

“Kina da wayo Shalele, kin fahimci damuwata a take kuma kin sama min mafita duk da karancin shekarunki”

Ya fada yana kai hannu ya taba halshen gashinta. Sai ta kai hannu ta sanye gashin.

“Waya gyara miki?”

“Ya Madina, gata can”

Mikawa tai tsaye daga ita har shi suka koma kallon entrance din da Madina ta fito sanye da dogon Hijab ta nufosu da saurinta.

“Sannu da zuwa”

Ta fada a yayinda ta karaso kusa da su, sai ya daga mata kai alamar ya amsa.

“Ban san ka shigo ba sai yanzu bari na kawo maka ruwa”

“Ka ci abinci dazun ka ce min kana jin yunwa?”

Aminatu ta tambaya, sai ya kalleta ya girgiza mata kai alamar a'a. Sai Madina ta kalleshi.

“Ko na dafa maka wani abu? Zama da yunwa be da kyau”

“Ruwa kawai”

“Okay”

Ta juya da sauri sai ya kira sunanta.

“Madina...”

Ta juyo da saurin gabanta na faduwa a zatonta ko zai ce ya fasa shan ruwan ne.

“Thank Youuuuuuuu”

Suma ne kawai ba tai a gurin ba, amman ta yi mutuwar tsaye har ta kasa yarda da ita yake. Ita fa? Madina yace wa Thank you after celled her name kuma yace mata ya gode, godiya fa yake mata...? Murmushi ta sakar masa duk da kasancewar babu murmushi a tasa fuskarsa ta juya ba tare da tace komai ba ta cigaba da tafiya, tana jin kamar ta zuba ruwa kasa ta sha dan murna da jindadi, yadda ya kira sunanta ma abun alfahari ne a gurinta, sai ta ji kamar ba a taba kiran sunanta da lafazi mai dadi irin na Talba ba, lastly zai sha ruwan hannunta.

Ko kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Yana tsaye a gurin kusa da Aminatu har ta fito da glass cup dayan hannunta dauke da gorar ruwa. Tana isowa ta mika masa cup din ya karba sannan ta bude ruwan ta zuba masa, sai ya sha kadan ya mika mata cup din, ya juya ya nufi mota ba tare da yace da ita komai ba, haka ma be yi ma Aminatu sallama ba, daga ita har Madina binshi sukai da kallo har ya shiga motar ya fice daga gidan. Sannan Madina ta kalli Aminatu.

“Idan kin gama ki min magana zan shiga dake ciki”

“Toh”

Ta juyo tana ta kallon gate din kamar ance mata Talba zai dawo, ta nufi kofar falon cikin wani irin farinciki, ta shigo falo, bata ko kula Hajiya dake falon ba ta nufi kitchen, cup din ta aje ta kara ruwan gorar hannunta sannan ta dauka ta saita bakinta a inda Talba ya sha, tana sha tana murmushi.

“Madina...”

Ta juyo da sauri ta kalli Hajiya hannunta rike da cup din.

“Na'am Hajiya”

“Waya zo yanzu?”

“Talba ne”

“Miyasa be tafi da yarinyar ba? Ba kin ce kwana biyu zata yi ba?”

Ta yi kasa da kanta.

“Hajiya gaskiya ba kwana biyu zata yi ba, kusan zata zauna a nan ne kamin abubuwa su daidaita a can gidan, yanzu haka Momy bata gidan sun samu matsala da Daddy har ya turata gida”

“Saboda yarinyar?”

Ta daga mata kai.

“Eh saboda abun da Momy tai ma Talba a kan yarinyar”

“Amman shi Talba ba yana da yan'uwa uba da uwa ba? Miyasa be kaita can ba sai a nan? Saboda mu ya raina mu ko kuma saboda me? Ke baki tunanin aje a nan zai lalata alakarku da Leila ko mahaifiyarta? Ni kaina sai ki ga abun ya shiga tsakaninmu da Hajiya dan mutuncin da muke ma mu daina”

“Bana fatar hakan Hajiya, kuma ba wai ya dauke ta kai tsaye ya ba ni ba ne, ni na bukata”

Hajiya ta yi mata wani kallo na mamaki.

“Saboda...”

“Saboda na faranta masa rai”

Ta amsa kai tsaye, sai kuma ta aje kofin hannunta ta karasa kusa da mahaifiyarta ta kama hannunta cikin yanayi na damuwa.

“Hajiya ke mahaifyata ce, na san ko ban fada ba kin fahimta, Wallahi ina matukar son Talba na rasa yadda zan yi”

Hajiya ta yi saurin janye hannunta daga rikon da Madina tai mata.

“Kul...!!! Karki yarda son zuciya ya debe ki ya kaiki ya baro karki, Aminiyarki? Kuma mijin da zata aura? Ki ce kina sonsa? To me kike tsammani zai juyo gurinki ya bar zabin iyayensa? Anya kin shirya yin takara da Leila? Hajiya bata has akan yayanta, karki kuskura dinke rigar kanki inda kai ba zai fito ba balle sauran jiki, domin wahala kawai zaki sha ki tashi a tutar babu kuma tutar kunya”

Hawaye ya cika idonta.

“Na yi iya yadda zan yi na yaki abun nan Hajiya, na yi iya yadda zan yi na kawarda idona daga Talba, amman na kasa, na yi ta hangowa kaina matsalolin dake tattare da hakan, amman zuciya na raya min zan iya dauka, na san kawance na da Leila mai zurfi ne, mun taso tare an girma tare mun zama kamar yan'uwa, be kamata na yi hakan ba, amman wata kila wannan ce kaddarata, Wallahi Hajiya ina matukar son Talba fiye da yadda Leila take sonsa”

Maganar take cikin kuka hawaye na sauko mata.

“Ki gaggauta cire shi a zuciyarki, kuma bana son yarinyar nan ta wuce yau, ki fada masa na ce ya zo ya dauke ta, daman ai na lura da take taken ki ba tun yau ba”

Hajiya na kaiwa nan ta juya ta fice, sai Madina ta durkushe a gurin ta fashe da kuka. Kuka tai sosai marar sauti sannan ta mike tsaye ta nufi dakinta tana shiga ta kulle kanta ta fara rusar kuka kamar wanda akai wa mutuwa, can kuma ya dauki wayarta ta shiga gallery wayarta ta kamo hoton Talba ta tisa a gaba tana ta kallo hawaye na yi mata sallama.
Wani irin abu take ji marar misaltuwa, da daske yanzu kam ta tabbatar sonsa take fiye da kima, tun da har sonsa zai saka ta kasa ganin Leila kuma kunnuwanta su toshe daga maganganun da mahaifiyarta tai mata. tashi tai ta shiga bandaki ta wanke fuskarta ta fito falon idonta har ya canja kala, sai da ta zauna sai kuma ta ji zaman baya mata dadi, sai kawai ta mike tsaye ta fice daga falon zuwa parking lot inda Aminatu take zaune. Tun kamin ta karaso Aminatu take kallonta da karantar yadda yanayinta ya canja daga far'a da jindadin da ta shiga da shi dazun, zuwa fitowa da damuwa da kumburarin idanuwa.
Zuwa tai ta tsaya akan Aminatu ba tare da tace mata komai ba. Aminatu ta tsayar da rubutun da take tana sauraren abun da Madina zata ce mata ammam shiru bata ce mata komai ba har na tsawo lokaci. Hakan yasa ta dago kai ta kalleta sai ta ga hawaye na sauko mata.

“Yaya Madina baki da Lafiya ne?”

Madina ta lumshe ido wasu hawayen na sauko mata.

“Ba ni da lafiya Aminatu, kuma ciwo ne da ba zan tana warke shi ba, ciwo ne da Allah ya dora min, kuma kowa ya kasa fahimtata”

“Me ke damunki?”

“Ciwon son, ciwon son wanda be san da wanzuwar son ba”

Aminatu kan kallonta kawai take ba dan ta fahimci inda kalamanta suka dosa ba, sai dai ta fahimci son wani take amman wanenen wanda be san da wanzuwar son ba? Dukawa tai gaban Aminatu kamar mai neman gafara.

“Hajiya tace dole ne na dauke ki daga gidan nan tsakanin yau da gobe, ni kuma bana son ran Talba ya bace, ban san yadda zan yi ba, daman na fada mata cewar zaki zauna na kwana biyu ne, bana son bata ran Talba, kamar yadda bana son tsabawa umarnin mahaifiyarta”

“Shine kike kuka?”

Ta girgiza kai.

“Aa abun da nake yi ma kuka dabam”

“Ki kirashi a waya Sai ki fada masa na ce bana son zama a nan”

“Zai iya zargin wani abu, bana son abun da zai nisanta ni da shi, ko ya saka ya ga kamar ni ce bana son zamanki a kusa da mu”

“Zan fada masa gaskiya ba amin komai ba”

Saaz ta fada tana Kallon Madina, sai Madina ta hade yawun bakinta ta saka hannunta ta share hawayen da suka zubo mata. Sai da ta kira Talba sannan ta kara wayar a kunne.

“Hello...”

Ta fada bayan ya dauki kiransa jin muryarta sai yai shiru be ce komai ba, bata damu ba ta cigaba da maganar.

“Aminatu ce, ta dame ni da kuka na tambaye ta me ke damunta bata fada ba”

“Tana ina?”

Ya tambaya daga dayan bangaren.

“Gata nan kusa da ni”

Ta mikawa Aminatu wayar, sai ta karba ta kara a kunne.

“Hello”

“Shalele lafiya kike kuka?”

Ta yi shiru tana kallon Madina.

“Ko saboda na tuna miki da baya ne?”

“Aa bana son zama a nan ne?”

“Ba ki son zama kuma? Miya faru?”

“Ba komai ni dai bana son nan ka zo ka dauke ni”

“Ana miki wani abu ne da baki so?”

“Aa ni dai ka zo ka tafi da ni”

“Okay zan zo”

“Yaushe?”

“Yanzu ko anjima”

“Toh”

Ta mikawa Madina wayar. Sai Madina ta karba ta kai kunnenta.

“Hello”

“Akwai abun da akai mata ne?”

“Wallahi babu, amman ban sani ba ko ita tana da abun da take son fada maka”

Ne sake cewa komai ba ya kashe wayar yana busar da iskar bakinsa. Ali ya kalleshi.

“Ya akai?”

“Shalele ce, wai ba zata zauna a gidansu Madina ba tana son na zo na dauke ta”

Ali ya masa wani kallon na mamaki.

“Ka kaita ina?”

Sai ya daga kafadunsa ya jingina da motarsa.

“Wannan abun yayi yawa Talba? Sunan ma da kake mata ka daina domin Leila ba zata jidadi ba idan ta ji, kuma karka dauko ta daga can”

“Idan kuma ana mata abun da bata so fa? Wata kila suna musguna mata ne, ba zata iya fada ba ne a gaban Madina”

“Okay let assume that ana mata wani abun, idan ka dauko ta gidanku zaka sake maida ta saboda Daddy yace ka kawo ta? Kana ganin tunani ne mai kyau ka dawo da ita bayan Momy bata nan kuma saboda yarinyar komai ya faru?”

“Ba gida zan kaita ba?”

“To ina zaka kaita? Talba ka yi tunani please... Gidan wata gwaggonka ko yar'uwarka? No suma ba su maka kallon mai hankali da tunani ba”

Ya mike tsaye yana kallon Ali.

“Okay then zan ajeta a gidana i think babu wanda zai takura mata a can kuma ina da iko da can ai”

Ali yayi dariyar mamaki.

“Like seriously? Talba kana magana kamar baka san illar abun da zaka aikata ba?”

“Idan na kaita can fyade zan mata? Saboda gani dan'iska ko?”

“No don't take it serious, amman dai kasan idan mace da namiji suka ke be a guri daya shedan ne na ukunsu, yarinyar kyakkyawa kamar wannan, kai kuma gaka lafiyayyen mai bukatar aure? Duk abun da musulunci ya hane mu da shi ya kamata mu nisance shi, And aje wannan ma a gefe baka tunanin wasu za su iya amfani da wannan damar su yi blackmailing dinka? Kuma ya kake tunanin Daddy zai ji idan ya san ka aje ta a gidan ka yarinyar da ba matarka ba”

“Me kake son yanzu na yi? Kai ma fa kasan halin da yarinyar take ciki! Bata da kowa sai ni sai Allah”

“Bata da kowa dai sai Allah, kai din miye hadinka da ita? Kana kokarin bata alakarka da kowa saboda wata yarinyar da baka san asalinta ba? Ka bata hakuri daman ba zai yiyu mutum ya samu abun da yake so dari cikin dari ba, idan tai hakuri da zaman a can sannu sannu sai mafita ta zo mata, idan ta samu lafiya sai ka kaita gurin yan'uwanta, idan kuma ta ki yanzu ka dauke ta ka kaita gurin da yan gudun hijira suke zama ka siya mata abinci da dan wani abu mai dama ka bata”

Talba ya rumgume hannayensa yana kallon Ali.

“Karka zama marar tausayi Mana, abun da ya faru da ita zai iya faruwa da kowa, kuma ina ce kai ka gabatar da min da yarinyar nan saboda kana ganin tana bukatar taimako”

“Amman ni ban yi tunanin zata haifar da matsala tsakaninku da Leila da kuma Momy da Daddy”

“Babu matsalar data haifar, domin bata ce dole a taimake ta ba, kuma ba zuwa tai ta hada su fadan ba, daman na san damuna zaka yi da maganar Leila shiyasa bana son zuwa gurinka yanzu”

Ali yayi murmushin takaici.

“Allah sarki Leila baiwar Allah, yanzu har baka son maganarta? Ni daman shawarar da zan baka kawai ya daure ka sake yi mata maganar auren ka lallabata, idan ta aureka hankalinku zai kwanta zata samu natsuwa kai ma kuma zaka samu?”

“That's the only solution, gidan zan kaita kuma wannan ya zama a tsakaninmu, ni Wallahi kasa ma na kara jin tausayin yarinyar nan, bata da gata ko kadan”

Yana kawai nan ya nufi driver seat. Ali ya bishi da kallo.

“Ya ina maka maganar Leila kana maganar wata yarinyar? Talba lafiyarka kuwa”

“No ban da lafiya zo ka kai ni asibiti”

Ya fada bayan ya shiga motarsa sai da yai mata key sannan ya rufe, yai reverse ya ja motarsa ya bar Ali tsaye bakin kofar gidansa.
Daga gidansu Ali family house dinsu ya nufa, sai da ya faka motarsa harabar gidan sannan ya soma jin wani yanayi na kadaici tunawa da Momy bata ciki. Ya dade cikin motar sannan ya bude ya fito ya nufi bangarensa, kamar wani bako haka ya shiga bedroom din ya zauna kan kujera yana maida numfashi, sai kuma ya dago wayarsa yana kallo kamar mai tunani, yawo ya fara yi da yatsunsa saman wayar har zuwa gurin number Madina sai dai be kira ba, kiran Amal ya shigo wayarsa saurin tashi yai zaune ya amsa kiran.

“Lil Sis”

“Ya ka yi magana da Daddy?”

Ya kai hannunsa ya shafa hancinsa zuwa kasan bakinsa.

“Yeah na yi magana da shi, kuma zai dawo da ita komai zai wuce, amman yana bukatar mu ba shi lokaci domin shi ma yana cikin bacin rai a yanzu”

“Amman dai ai zata dawo ko?”

“Eh dole ma ne Daddy ya dawo mana a ita, Ki kwantar da hankalinki”

“Toh”

Ya yanke kiran, ya mike tsaye ya fice daga idakin, motarsa ya nufa ya shiga tun kamin yai reverse ya danna horn, ko kamin ya isa gate din an bude masa.
Kai tsaye gidansu Madina ya nufa, sai dai wannan karon be shiga ciki ba ya faka bakin gate din, ya kirata a waya ya sanar mata yana waje.
Bayan kamar minti talati aka bude gate din ta fito rike da Aminatu, mai aikinsu kuma na rike da jakar tufafin Aminatu, daga cikin motar yake kallonsu har suka karaso sannan ya bude motar ya fito ya zagaya ya bude mata gidan gaba ta zauna ya rufe. Sannan ya juyo ya kalli Madina.

“Thank Youu, zan so wata rana nima n rama abun da kika yi min na karamci”

Murmushi take tana masa wani irin kallo mai cike da saukin so.

‘Ina ma zan iya buda maka zuciyata ka kalli irin kaunar da nake maka? Taya zan iya fada maka cewar kaunarka ita ce tukuicin abun da na yi maka?’

A ranta take ta wannan tunanin tana binsa da kallon da bata san tana yi ba, har ya bude back seat ya saka jakar tufafin ya rufe ya zagaya bangaren direba ya shiga ya ja motar, sai da yai horn sannan hankalinta ya dawo jikinta har ta zabura sai kuma ta lumshe ido tana maida mumfashi a hankali.
Sai da yai nisa sannan ya kalli Aminatu ya ce.

“Ana miki wani abu ne a gidan?”

“Aa”

“Miyasa baki son zama a can?”

“Ba komai”

Be sake cewa komai ba, sai dai duk bayan lokaci yana kallonta da karantar yanayinta.

“Yanzu zan kai ki gidana ki zauna, a can babu wanda zai takura miki”

“Gurin su Momy?”

Ta tambaya tana kallonsa nan da nan idonta har ya cika da hawaye.

“No gidana ni kadai ne a ciki nima kuma bana zama, yanzu ke kadai zaki fara zama a ciki”

Ta yi shiru bata ce komai ba, sai dai kuma bata gama fahimtarsa, ba mutane kamar ya? Gida ne da zata zauna ita kadai? Ko kuma da matarsa? Amman ai yace mata Leila ce matarsa kuma da alama be aureta ba. Haka tai ta jerowa kanta tambayoyi tana yi tana kallonsa har suka kusa isa gidan, each and every single kallo da take masa sai idanuwanta da na shi sun yi tarayya. Wata sabuwar unguwa ce mai dauke da manyan gidaje na Alfama, a gaban wani katon green gate ya faka, sai ya kalleta.

“Bari na bude gate din”

Bata ce masa komai ba, ya bude motar ya fita tare da keys din hannunsa ya saka ya bude gidan ya shiga ciki ya bude gate din gaba daya sannan ya dawo

yaja motar ya shiga da ita ciki, kato gidane mai matukar kyau da tsari, ya fenti ko'ina da golde color, ga manyan itatauwa da ko'ina daga bakin entrance din kuma flowers har harabar gidan. A inda ya faka motarsa guri ne da aka tanada aka kawata domin aje motoci kawai, a kusa da inda ya aje motar akwai mota biyu dake lullube. Sai da ya kashe motar sannan ya bude ya fito, ya isa gurin gate din ya rufe, ya dawonya bude bangarenta ya miko mata hannunsa.

“Fito”

Ta rika hannunsa ta fito, ya rufe motar ya da taimakonsa suka isa entrance din, sai dai a nan be tsaya jiran ta taka da kafarta sai ya sake ta ta isa gurin kofar falon ya bude, sannan ya dawo ya dauke ta cak ya shiga da ita cikin falon, babu komai a ciki sai dai an ware gurin yin komai kama daga dinning har zuwa gurin saka plama. Sai dai ba a saka kujeru ba, ba a masa kwalliyar komai ba. Bedroom din ya nufa da ita shi ma ba yi masa wani gyara ba sai dai an saka gado da standing mirror.
A saman gadon ya sauke ta sai ta fara rabon ido yana karewa dakin kallo, ko'ina yayi datti alamar an dade ba a zauna a gidan ba.

“Bari na kunna miki inji”

Har ya juya sai ta mike tsaye tana jin tsoro.

“Ni kadai zan zauna nan?”

Ya juyo ya kalleta, babu komai a cikin idanuwanta sai tsoro da tashin hankalin da be san inda ya samu asali ba.

“Kina jin tsoro ne?”

Ta daga masa kai idonsa na cika da hawaye.

“Ba zan iya zama a nan ni kadai ba”

“Amman idan ba a nan ba, babu inda zan kai ki, duk inda zan kaiki za a takura miki ne”

“Ni dai ba zan iya zama a nan ba”

Ta fashe da kuka, tunani ya soma dawo mara, tana ganin kamar a nan din ma wani abun zai same ta.

“Dan Allah karka bar ni a nan tsoro nake ji sosai”

Ta fada tana ta kokarin takawa ta isa inda yake.

“Ba zai yiyu na kai ki wani guri ba, kuma ba ni da inda ya fi nan, kuma ba zai yiyu na zauna a nan ba, saboda ni ba muharramin ki ba ne, taba ki ma da nake Allah kadai ya san zunubin da zan samu”

Yana kai Aya saibta fashe masa da kuka sosai jikinta ya fara rawa, ta fara daga masa murya zata masa irin kukan da tai a lokacin da Leila ta mari Mairo. Sauri karasa yai kusa da ita ya rikata, sai ta fada jikinsa, nata jikin yana karkarwa numfashinta har rawa yake.

“Ya isa ya isa ba zan bari ki zauna a nan ke kadai ba”

Ta runtse ido sosai jikinta nata rawa numfashinta ma kamar zai fita ya bar jikinta. Sai da ya tabbatar ta samu natsuwa sannan ta taka tana a jikinsa ya zauna bakin gadon tare da ita.

“Tsoro nake ji, bana son zama ni kadai”

“Ba zaki zauna ke kadai ba, amman we have to plan, ba zai yiyu mu zauna sheidan ya rijanye mu, be kamata na yi kusanci da ke haka ba...”

Ya fada yana sauke ajiyar zuciya, sai kuma ya dago ta a hankali sai ta kalleshi idonta har ya fada.

“Zan zauna tare da ke, amman sai idan zaki yarda da wani sharadi da zan gindaya miki”

“Minene?”

Ta tambaya bakinta na rawa, jikinta na amsawa wani sanyi ya taso mata. Buaar da iskar bakinsa yai ya mike tsaye yana ganin kamar be dace yai mata wannan maganar ba, ya zata kalleshi? Ya zata dauki abun? Besides shi dai ya san ba sonta yake ba, amman dole yai haka saboda masa wa kansa mafita da kuma ita. Wayarsa ya ciro ya kira line Momy ringing biyu kamin tai na uku ta daga, da sallama.

“Talba”

“Na'am Momy kina lafiya?”

“Lafiya kalau ya kuke?”

“Momy kina ina?”

“Ina gidanmu, ina zan je?”

“Haba Momy ko da ace saki uku Daddy yai miki ai be kamata ki bar gidan nan ba, saboda kin tara mu sai dai shi ya tafi ya barki”

“Uhm... Indai kuna lafiya ai shikenan zan dan yi wani aiki”

Be ce komai ba har ta kashe wayar, sai ya juyo ya kalli Aminatu, sai kuma ya juya ya fita, kamin ya kunna injin din ya dawo har ta kawo bakin kofar falo tana hawaye, da tana dafa gini, har ga Allah tsoro take ji bana wasa ba, yanayin gidan da yadda yake shiru ga shi da girma sai yai mata kamar wacan dajin.

“Har kin kawo nan?”

Ya fada bayan ya bude kofar falon ya shigo, da mamaki ya kalleshi.

“Ba zan zauna a nan ba, dan Allah ka kai ni wani gu....gu... rin...”

Kamin ta karasa tai baya ta fadi duk kokarin da yai na riko be yi nasara ba har ta kai kasa babu numfashi.

MG'S COLLECTION.

"Saudatu ki shirya zamu je gaishe da su Baba, kasancewar azumi ya yi nisa ya kamata ace sun samu wani tagomashi daga arziƙin haihuwa"
Ta faɗa tana nufoni da ƙunshin kayan da ta soma zazzagesu. Galala yaro da wayau, haka na saki baki ina kallonta.
"Amma Raulatu baki kyautamin ba, haka zan je gaishe da su hannu na dukan cinya bayan ke kin gama shiryawa?"
"Ban fahimta shiri ba? Kina nufin ki ce min baki da labarin ƙayatacen wajen da suka sahalce mana yin Ramadan package?"
"Ina kenan?"
"MG'S COLLECTION mana. Wajan da ya tanadar mana da sauƙaƙiyar hanyar kyautatawa makusantamu ta hanya me sauƙi. Ingantattun kayansu masu sauƙi da kuma inganci. Ɗangin Turare, Darduma, Jallabiya, Agogo, Jaka da Takalmi. Har ma da Alƙur'ani mai girma"
"Eh lalai ki ce sa'a tafi manyan kaya, da hanau gara manau"
"Tabbas kuwa ba su tsaya iya nan ba, sun saida ingantatun kayan ɗa'a masu maida tsohuwa yarinya shar washar da ita.sannan munada set n gyaranjiki me matukar kyau yasakiyi haske meban shaawa,munasaida daddaya,kuma Akwai frams na ƙawata ɗakin amarya da uwargida"
"Tabbas zan garzaya yɜar uwa domin kashe ƙwarƙwatar idanuna"
"Za kuwa ki godemin, zaki same su a adireshinsu dake
Kunemesu ta WhatsApp number nasu 07046881166, 08062991549
kan waɗanan lambobi. Ga sauƙi ga inganci ga kuma mutuntawa.

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Momy ta aje wayar tana murmushin takaici.

“Waya kira?”

Hajiya Yana ta tambaya, sai Momy ta kalleta.

“Talba ne”

“Bawan Allah, bayan duk abun da kike masa har kiranki yake”

“Uhm Hajiya kenan, ke da Alhaji sai dora min laifi kuke”

“Dole a dora miki laifi mana Amina, yaron da zai girma a hannunka be san wata uwa ba bayan ke, amman ya kawo wata ki masa haka saboda kawai ba ke kika haife shi ba”

Cewar Mahaifiyarta Hajiya Yana.

“Hajiya ni fa ba kamar ke bace, ni kam kaza ce mai son yayanta, ba zan iya yi ma yayana abun da kike mana ba, na nuna mana kin fi son yayan yan'uwa fiye da mu, yanzu fa zamani ya canja, Wallahi kowa kansa ya sani”

“Allah ya wadaran wannan canji na zamani Amina, mu kam a da ko dan makoci dan ka ne balle kuma dan dan'uwa na kusa da nesa”

“Hajiya ai ni ban hada jini da Talba ba”

“Ban ga ta inda Talba ya babanta ki da mahaifiyarsa ba, bibiyar da yake miki ko Kabiru da kika haifa be fishi yi miki bibiyaya ba”

“Babu wannan damar ne ai, da ace zai samu hanyar nuna min zai yi, ai ruwa be taba zama jini ba”

Hajiya Yana ta girgiza kai.

“Na yi tunanin sakin nan da Alhaji yai miki zai saka ki natsu ki gane kuskurenki domin yayi abun da ya dace, ya nuna miki jini ba abun wasa ba ne, ke kam dai halinki ya fita dabam dana yan'uwanki, ba ki dauko ni ba kuma baki biyo halin mahaifinki ba, sam wannan ba rayuwa bace”

Mikewa tai tsaye tana dariya.

“Hajiya idan kina min wani abun kamar ba ke kika haife ni ba, ni saki be tashi hankalina ba, amman ya saka na kara nazari da tunani da kuma fahimtar abubuwa, ina mai tabbatar miki sai Engineer yayi nadama sai ya zo da kansa yana neman afuwa yana kuka da hawayensa, abun da be min a kurciya ba yanzu zai min shi da tsufana? Da yaya? Ai duk wanda ya zama silar mutuwar aurenka a gidan mijinka da kake kauna kuma da yayanka manya ba kakana ba, ba masoyinka ba ne Hajiya...Hmmm”

Ta karasa tana kashe ido daya, sannan ta kai hannu ta dauki wayarta tare da plate din data gama cin abincin ta nufi bedroom, Hajiya Yana binta tai da kallo tana mamaki yadda zamani ya lalace har zaka fifita danka akan son zuciya, domin a iya abun da ta fada mata bata hango Talba ko Daddy da wata matsala ba, duk abun da ya faru ita ta janyo komai, ba tun yau ba halin Amina ya fita dabam a cikin yayanta.

“Allah ya kyauta ya shirya ki”

Addu'ar da Hajiya Yana tai kenan ta cigaba da jan carbinta, tana gama tasbihin jikanta Kabir ya turo kofar falon ya shigo, juyows tai ta bishi da kallo har ya zauna, bata ce masa uffan ba domin ta lura yana cikin yanayi na bacin rai, domin ba haka ya saba shigo mata ba. Idan zai shigo ya kan yi sallama kuma ya shigo yana wasa da ita tsabanin yau da ya shigo kamar wanda akai wa dole.

“Hajiya Yana Ina Momy?”

“Bacin ran da ubanku ya saka muku shi ne zaka zo ka sauke a kaina?”

Ya kalleta sai kuma ya hade yawu yana ta kokarin danne bacin ransa.

“Hajiya ki yi hakuri, ina Momy?”

Da hannu tai masa nuna da kofar dakin, har ya mike tsaye sai ta kira shi.

“Kabiru... Zauna”

Bayan ya juyo tai masa umarnin zama, sai ya koma ya zauna.

“Karka dorawa mahaifinka laifi, karka kuskura ka biyewa mahaifiyarka abun da tai da kai da ita Leila duk ba ku kyauta ba, hakan da kuka yi kun nunawa Talba rashin gata ne da galihu, domin na tabbatar idan kai ne Amina ba zata maka haka ba”

“Son da Daddy yake yi ma Talba yayi yawa Hajiya, ni ma sai yanzu na lura da haka, kuma da Talba ya dauki Momy a matsayin uwa ba zai tana yarda ta kawo yanzu a gidan nan ba, duk yadda zai yi ya saka Daddy ya maidata gidanta zai yi, saboda Daddy yana jin maganarsa kuma yana gudun bacin ransa, amman be yi komai ba, saboda ba mahaifiyarsa ba ce”

“Aa Kabiru kar fushi ya rufd maka ido, ka rika ganin daya a matsayin biyu, baka san abun da yake kasa ba, kuma ka san halin Mahaifinka sani murdanden mutum ne, ba lallai ne wani ya iya saka shi abun da be tashi ba, yanzu kuma Amina ta gama waya da Talba”

Kabir ya mike tsaye.

“Ke ma kina goyon bayansa kenan? Akan mahaifiyata bana ganin kowa da gashi Hajiya, ya sha saka ta kuka saboda Silly abu Daddy zai rufeta da fada har sai ta yi kuka ranta ya bace, amman yanzu mai gaba daya Daddy yai, be dubi ni ko Leila ko Amal ba, abun da be yi da kurciya zai aikata da tsufa saboda Talba? Ya duniya zata kallemu da girmanmu ace iyayenmu sun rabu”

Hajiya ta nuna shi da yatsa.

“Kabiru me mahaifiyarka ta fada maka? Ka zurfafa abun nan”

“Babu zancen zurfafawa Hajiya, ina fada miki gaskiya ne, har yanzu Talba ne kira ya min magana ba, kuma be saka kafarsa ya shigo gidan nan ba, that's mean ya jidadin abun da Daddy yai kenan? Yanzu na fahimci dalilinsa na kin nunuwa Leila kulawa wato baya son ta kuma ba zai iya cewa baya son ta ba, ai ya san kulawa tun da gashi nan yana nunawa yarinyar, and now da Leila ta kamu da kaunarsa ta saka a zuciyarta shi ne yake kokarin broken heart dinta and i won't let that happen, i will teach him a lesson”

Yana fadar haka ya nufi dakin da Hajiya Yana ta nuna masa sai wani cika yake fushinsa yana kara hauhawa.

TALBA POV.

Kallonta yake yana ta tunanin ta inda zai fara mata bayanin, zata fahimta? No wait ya ma dace yai haka? Amman idan be yi ba yana da wata mafitar ne? Idan yace zai kaita wani gurin zata zauna? Zata jidadin rayuwa? Idan kuma ya zauna da ita anya zai iya rike ba tare da shiga hurumin da Allah ya haramta masa ba? Ta dan sakar masa murmushi ganin kallon yayi yawa har ta soma tsarguwa, sai shi ma yai murmushi yana cigaba da kallonta.

“Kin san me?”

Ta girgiza kai alamar aa.

“Ina ganin kamar muna da mafita daya ni da ke? Ita kadai ta rage mana”

Kamar ya san ba zata tambaye shi minene mafitar ba, sai ta ya cigaba da maganar yana kallon cikin idonta.

“Idan muka zauna a haka zamu iya sabawa Allah, ba ina nufin mu aikata wani abu ba, no zan iya kula da kaina, amman rika hannunki taba jikinki ko taimaka miki da yin wani abu da zai saka na kai hannu a jikinki, idan kuwa har zamu zauna a gida daya a tare dole ne sai hakan ta faru, tsakani da Allah ban saba mu'amala da mata ba, taba mace kallonta ba halina ba ne, and duk abun da zan yi ina kokarin ganin ban shiga hurumin da ya haramta a gareni ba, ina kokari sosai wajen ganin n tsare mutuncina da na iyayena da yan'uwana, idan babu yan'uwa da iyaye kuma akwai Ubangijina, ban ce na fi karfin sheidan ba amman duk inda mace da namiji suka kebe na ukunsu sheida ne, haka ne?”

Ta daga masa kai, sai ya zauna gefenta yana kallon gefen fuskarta a yayinda take kallon kofar bedroom din.

“So ina son na yi wannan shawarar kuma na yanke wannan hukuncin akan yardarki da amincewarki, bana son na cilasta ki ko kadan bana son ranki ya bace akan komai, bana son ki cilasta zuciyarki ta karbi abun da baki bukatarsa a yanzu, ni kaina idan nace miki ina bukata na yi karya, domin zan jefa rayuwata a hadari ne da kuma na matar da zan aura Leila, kuma zamu yi wannan abun ne a bisa sharadi”

Ta juyo ta kalleshi.

“Minene?”

“Shalele...”

Sai kuma yai shiru yana tunanin dacewa da rashin dacewar aikata hakan, ita kanta ya zata kalli abun?

“Ina son mu yi aure ni da ke....”

Duk wani abu dake motsi a jikinta sai ya tsaya cak na tsawon dakika uku.

“Aure...”

Ta maimaita a raunane tana kallon wani gefen.

“Yes... Aure ba saboda ina son ki ba, ba saboda kina so na ba, kuma ba saboda mun dace da juna ba, zamu yi wannan abun ne a karkashin sharadi guda daya”

Ta sake kallonsa sai dai wannan karon hawaye har ya fara sauko mata.

“Zan aure ki ne saboda gudun aikata abubuwan dana fada miki a dazu, amman Wallahi ba dan ina son ki ba, sai dan ina tausayinki, kuma saboda hakan zai zame mana mafita ni da ke, domin na san ke ma ba sona kike ba! Amman na miki alkwari ni Talba zan sakeke da zarar rayuwarki ta inganta, ma'ana kin gane yan'uwanki ko kuma kin samu wanda zai aure ki, kuma wannan auren zai

kasance ne kawai a tsakaninmu, babu wanda zai san da wannan sirrin har mu rabu”

Dauke kai tai tana jin abun wani iri, an taba aure ba yan'uwa ba kowa? Daga ita sai shi?

“Zamu yi ne saboda tsare mutunci da gudun fushin Allah, kuma na rantse miki da Allah zan sake ki a duk lokacin da dayan biyun nan ya faru! Ko dai kin gane wasu daga danginki ko kuma kin samu wanda ke sonki tsakani da Allah zai aureki, karki damu da tunanin babu yan'uwa ko naki, zamu yi wannan auren ne saboda ke, domin ni ina da wanda zan aura, kuma mu yi wannan abun ne a rubuce kuma akan yarjejeniyar saboda ki samu natsuwa”

Ya fada kamar ya san abun da ke ranta. Da gaske aurenta zai yi saboda abun ya fada ko kuma dai saboda wani dalilin ne na dabam?

“Momy...”

“Karki damu da ita, ba zata taba sani ba na miki alkawari”

“Leila...”

“Taya zan barta ta sani bayan kuma ita zan aura? Ya kike ganin zata kalli abun? Wannan abun zai zama sirrine a tsakaninmu”

Ta girgiza masa kai.

“Ba zan iya ba”

Ya cikama bakinsa iska ya busar kana ya kai hannu ya shafa kansa.

“Daman bana son cilas ta ki, yanzu dole mu nemo wata mafitar ta dabam, zan memo miki wani gurin da zaki zauna tare da wasu mutanen, amman kamin na samu wannan dole ki zauna a nan kamin mu samu wata mafitar”

Sai ta rumtse ido wasu zafafan hawaye na sauko mata.

“Inna ta yi gaskiya, ta fada min zan yi kuka a gaba, sabowa da wata rayuwar ba abu ne mai sauki ba, fuskantar kalubale bayan wani kalubalen abu mai wahalar gaske, ina a tsakankanin rayuwa da mutuwa, farinciki da sabo sun min nesa, samun sukunin na zuciya da ruhi ya min tsada”

Har ya kai hannu ya kama hannunta, sai kuma ya maida hannun a cikin dayan hannunsa ya rike.

“Miyasa ba zaki yarda da kaddara ki karbi duk abun da ya zo miki da hannu biyu? Wata kila idan kika bi rayuwar a yadda ta zo miki sai ki samu sukuni da walwala a gaba?”

Ta bude idanuwanta da suka soma yin ja ta kalleshi.

“Kana ta karfafa guiwa a inda babu karfi, taya kake ganin komai zai zo min da sauki? Na rasa uwa a gaban idona suka kashe mahaifina, aka kashe yan'uwana a dare daya na rasa komai, a tsakanin wadancan ranaku da na yau na rasa wacece

ni, ina jin zafin abun a raina ina jin kamar zuciyata zata fasa kirjina ta fito babu abun da yake da sauki a gareni...”

Ta karasa tana ta shesshekar kuka jikinta na rawa, hawaye na sauko mata kamar an yi su ne kawai saboda wannan ranar.

Gaba daya jikinsa yayi sanyi sai tausayinta ya kara kama shi, ba tare da ya so ba ya kai hannunsa ya kama hannunta ya jimke sosai, sai kawai ta kara fashewa da wani irin kuka mai taba zuciya.

“Za ki iya yarda da ni?”

Ta daga masa kai tana kuka.

“Na miki alkawarin zan dawo miki da farinciki a rayuwarki, ban ce zan dawo da iyayenki da yan'uwanki ba, amman da yardar Allah sai na samo miki wadanda za su maye miki gurbinsu? Zan dawo miki da farincikin da kika rasa Amina i promise you this! Kin yarda da ni?”

Ta sake daga masa kai, sai ya sauke numfashi a hankali yana jin kamar ya rikata ya saka ta a kirjinsa ya rarrasheta. A hankali ya zare hannunsa ya mike tsaye yana nuna mata gadon.

“Kwanta”

Ta kalleshi daker tana kokarin tsayar da kukan da take.

“Ta.... Tafiya... Zaka yi....”

Kamar ya ce mata eh sai kuma wata zuciyarta ta hana shi, wata kila idan ya amsa mata da eh zata iya cewa ba zata zauna ba, idan kuma ya ce mata aa ta kwanta ta tashi bata tararda shi ba zata dauke shi makaryaci. Be ce mata komai ba ya nufi inda bargon yake aje gefen gado ya dauka ya rike.

“Kwanta, ki samu bachi”

Ta hau saman gadon gaba daya ta kwanta sai ya dauki filo ya mika mata ta karba ya rumgume, sannan ya lullube ta. Baka jin komai a dakin sai saukar numfashinta da karfi, gefen gadon ya samu ya zauna yana kallonta, zaman da yai sai ta ji natsuwa har ma ta samu damar lumshe idonta, ta kai hannunta a baki tana cizawa a hankali. Kallonta yake for so many reasons, na farko rayuwarta yake hangowa, da kuma tasa ta ina zai sama mata duka abubuwan da take bukata? A dayan bangaren kuma yana tunanin Momy. Lokacin lokaci take sauke ajiyar zuciya da karfi tana shakar numfashin a hankali. Sai da ya tabbatar bachin nata ya nina sosai sannan ya mike tsaye ya karasa inda take ya kai hannunsa ya janye hannunta daga bakinta ya kara jan bargon ya lulluba mata har gurin wuyanta, sai kuma ya tsaya yana kallon kyakkyawar fuskarta, samun kansa yai da murmushi kamin ya juya ya fara takawa cikin izza ya nufi kofar dakin, hannunsa ya kai ya kunna ac dakin sannan ya juyo ya sake kallonta, kamin ya sa kai ya fice ya ja kofar a hankali ya rufe, this is the first time da yake taba kofa a hankalin saboda gudun katsewa wani bachi, after Daddy. Fita kofar falon ma a hankali ya jata ya rufe saboda kar karar rufe kofar ya tashe ta, sannan ya saka key ya rufe kofar daga waje, sai da ya fara isa ya gurin gate din ya bude sannan ya dawo ya fita da motarsa sai kuma ya dawo ya rufe gate din

ya koma cikin motar. Kamin ta fita unguwar aka soma kiran sallah magariba, a kusa da wani masallaci ya faka motarsa ya fita yai alwala ya shiga masallacin yai sallah sannan ya dawo cikin motarsa yai mata key ya dauki hanyar gida.
Kamin ya isa ya kira Daddy a waya, sai dai har wayar tai ringing ta gama be daga ba, hakan ya saka shi rike wayar a hannu ya cigaba da tukin da hannu daya har ya isa gida, yana danna horn sai ya ji babu dadi tunawa da Momy bata cikin gidan, har yake jin kamar ya juya ya koma domin shiga cikin gidan yana masa nauyi a yanzu, ya kasa daina ganin laifin Daddy na yanke irin wannan hukuncin kuma yana ganin shi ne silar komai, tun da yake da Momy ko fushi be tana ganin ta yi ba, balle kuma har saki ya shiga tsakaninta da Daddy, idan ma an taba ta an yi ta sigar da su ba za su gane ba. Har ya isa harabar aje motocin ya faka motarsa be lura da Kabir dake jingine jikin mota yana waya ba, duk da kasancewar ko'ina na gidan haske ne irin hasken nan da ko allurarka ta fadi zaka iya gani, ko da yake hausawa sun ce hankali ke gani ba ido ba.
Sai da ya bude motar ya fito sannan ya kunnuwansa suka jiyo masa sautin muryar Kabir, rufe motar yai ya karasa inda Kabir yake jingine ya tsaya tare da zuba hannayensa aljihu yana kallon harabar gidan kamar bako.

“Ya akai?”

Kabir ya bukata ganin ya tsaya a inda yake da alama jiran yake ya kare wayar, kallonsa Talba yai jin wata bakuwar kalma da be saba furta masa ba ga fuskarsa a gade kamar bakin hadari.

“Come on.. Karka ce min ka zo nan ne saboda ka yi magana akan abun da ya faru? Kai da baka san zafin uwa ba? Taya za ayi ka ji wani abu?”

Talba ya kalleshi da mamaki.

“Kabir magana fa kake fada min kai tsaye”

“Yes ko ni ma zaka saka Daddy ya kore ni ne? But I'm grown up now ba yaro ba ne ni”

“Kabir me ke damunka?”

Talba ya tambaya da mugun mamaki.

“Babu abun da yake damuna, kawai ina fadar gaskiya ne da ace ka san wacece uwa da baka bari komai ya faru ba? And you won't be here standing in front of me, Momy ta raine ka for so many years amman a yau ka nunawa duniya cewar kai ba danta ba ne, and Thank you....”

Yana fadar hakan ya bar gurin ya nufi hanyar falo, Talba binsa yai da kallon yana mamakin kalaman da Kabir ya fada masa kai tsaye! Ta dayan bangaren kuma sai ya ji kamar an caka masa wuka a kirji, how could someone like Kabir zai ce masa be san zafin uwa ba? For the second time after wacan karon da Daddy ya ba shi labarin komai ya samu kansa da jin wani yanayi irin na Aminatu.

BATURIYA POV.

“Na kira ne kawai na yi miki barka da safiya”

Ta yi murmushi tana kara gyara kwanciyarta kan gadon Umma.

“Na yi fushi baka kira ni da wuri ba har rana ya fito sosai”

Ta fada tana ta zuba masa shagwaba kamar yana gabanta. Sai ya marairaice murya daga can cikin wayar yana bata hakuri.

“Haba Babyna kin san bana son bacin ranki fa, amin afuwa ba zan sake ba, kuma ina tafe da wani katon albishir”

“Na me?”

“Sai kin ba ni goro zan fada”

“Me kake so?”

“Komai ma kika ban ina so, ai ni komai ni so nake”

“To na baka kaina”

“Wow na gode ko da yake ke ma din ai tawa ce”

“To yanzu fada min”

“Abbana ya amince, zai fada min lokacin da yake free sai na fada miki ki duba idan na ki Abbah yana free sai su hadu su ga juna”

Ta dafe kirjinta gabanta na faduwa, ga wani irin tsoro da fargaba da suka rabeta a lokaci daya.

“Da gaske?”

“Haba ana wasa da irin wannan maganar ne?”

“Wow Alhamdulillah, amman ka san me? Ni fa a gidan mu ba a san da maganar ka ba”

“Yeah ai na fadawa Abbana, shiyasa ma nake son aje nema min aurenki so that na samu izinin magana da ke”

“Kana ta maganar Daddy ban ji ka tabo Momy ba?”

“Kin san Momy tana son na auri wata a familynsu ne, amman ita ma ta yi na'am saboda tana son abun da nake so, kuma Abbah ya bi bayana yace matukar suka yi bincike suka tabbatar babu wata matsala za su nema min aurenki”

“Alhamdulillah Allah ya amince mana”

“Amin kin san fa ni na gaji da wannan boye boyen da kike min kin hanani zance da ke, da na yi magana sai ki ce ana fada a gida, kuma ya kamata ace muna haduwa saboda mu kara fahimtar juna da kyau”

“Haka ne, ni kaina ina son haduwa da kai, idan na samu free time zan kiraka sai mu haduwa akwai abubuwa da yawa da ya kamata ka sani akaina ni ma kuma na sani akanka”

“Haka ne, idan kin samu sa'ar fita sai ki fada min inda zamu hadu”

“Inshallah, i love you so much”

Ta fada da muryar dake nuna farinciki take, sai dai a zahiri ba farincikin take ba, tsoron abun da zai je ya dawo ne a ranta.

“Na'am Umma gani zuwa”

Ta yi amsawar karya kamin ta ce.

“Ina zuwa Umma tana kirana”

“Okay i love you”

Tun kamin ya aje ya yanke wayar ta tashi zaune tana dudu da hannayenta.

“Kam uban nan, zubar da cikin nan ya zame min dole, amma...”

Bata karasa ba Umma ta daga labulen dakin ta shigo tana fadin.

“Rafi'a, ta so ga yayanki can yana nemanki”

“Toh”

Ta amsa sannan ta sauko saman gadon a ta dayan bangaren tana ala ala idan ba Faruk ya fada masa tsabanin abun da ta fada musu ba. Kamin ta karasa falo har ta fara tunanin irin karyar da zata yi ta kare kanta.
Gabanta na faduwa ta zo ta zauna a kasa kanta a kasa Umma dake bayanta ta zauna kan kujera.

“Yaya ina wuni?”

Ta gaishe shi tana dan kallon yanayinsa, sai ya amsa mata fuska ba yabo ba fallasa.

“Umma ta fada min abubuwan da suka faru, na kira Faruq har gida domin ji daga bangarensa, sai dai be fada min komai ba, kawai dai ya ce min ya gaji ne, yayi iya hakurin da zai iya da ke, yanzu kuma Allah ya kare abun, sai dai yayi ta jaddada min cewar ke yar'uwarsa ce kuma uwar dansa, ba zai fadi mummunna abu akanki ba, amman mu zamu fahimci komai da sannu, ina fatar babu abun da kike boyewa”

Ta dago kai ta kalli Yayanta idonta cike da hawaye.

“Haba yaya! A hannunka fa na tashi idan akwai abun da ba halina ba ai kai zaka fara sani”

Umma ta tabe baki

“Ai ni ba haka na so ba Wallahi, da ka biye ta tawa da police station zaka kai shi a lakada masa shegen duka kamar yadda shi ma yayi mata”

“Ai an daga kafa wani gangaren ko dan zumunci, shiyasa na kira shi a gida na yi magana da shi”

“Shi ai be duba zumuncin ba a lokacin da zai wulakantata haba”

“Yanzu dai ayi hakuri komai ya wuce, Allah shi zai saka mata ai”

“Aiko ya saurari abun da zai same shi domin hakkinta sai ya kama shi, kuma gobe gobe zan aika a kwashe mata kayanta duka da yardar Allah, daga ma ta huta da talauci da rashin abincin, kuma ba zamu rika masa dansa ba”

“Yace ma zai rika aiko mata abinci duk wata saboda cikin da take da shi, Allah ya sauwake”

“Ameen”

Ta amsa a tare da Umma sannan ta taso ta baro musu falon da dawo dakin Umma ta zauna tana ta tunanin maganar da Fahat yai mata! Da sauri ta kai hannu ta dauki wayarta ta kira Ramlee ringing daya ta dauka cike da far'arta.

“Yar gari yanzu fa nake son kiranki”

“Lafiya?”

“Lafiya sai alheri, Wallahi Alhajin nan ne ya fara damuna da maganar ki jiya, har yana ce min yana son ya leka chine da ke, bayan shi ma na samo miki wani Alhajin”

“Uhmm ai yanzu fita ma sai ta min wahala Ramlee, Faruq ya sake ni”

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un, ya sake ki fa kika ce Fee'ah”

“Wallahi kuwa yau kwana biyu....”

Daga can cikin wayar Ramlee ta sauke ajiyar zuciya bayan Baturiya ta gama labarta mata komai.

“Wato sai yanzu na gane kin ci ubana da iya makirci Fee'at”

“Uhmmm ni ma ai ba ta wasa ba ce, ni yanzu kin san ma miyasa na kira ki?”

“Sai kin fada”

“Cikin nan nake son zubawar kin ga ina zubar da shi na gama iddata”

“Haka ne, amman kar ki yi gaggawa Fee'at, saboda zai taba lokacinki a yanzu, maganar ba zai yi a waya ba, ina son mu hadu if possible”

“Karki zo gida, zan kira ki idan na samu sararin fita”

“Okay ”

Ya sauke wayar tare da sauke ajiyar zuciya.

MATAYEN KƙWARAI SARAKAN ADO DA KƙAWATA JIKI DA KWALLIYA KUNA INA NE?.

Maza ku garzayo da gudunku ga mutunuyar taku maida tsohuwa yarinya ta sake dawo muku da sabon salo, sabon sunfarin kayan gyaran jiki na mayika da sabulai yƴan gaske□□.

Kayan kwalliya na mg's skin care zasu maidaki shalele yƴar ƙwalisa tamkar wata ɗan daren sha biyar koda kina da kishiya yƴar Morocco bata girgizaki ba, balle saurayi ɗan son ƙyale-ƙyale da ƙawa ga burwallensa😂□□.

_Kayan mg's skin care nada matuƙar sirrika da inganci irin wanda sai an gwada akansan na ƙwarai.

MUNADA KAYAYYAKI KAMAR HAKA□□

Hajiyata shin menene matsalanki, pimples ne?
Spot? sunburn,acne, stretch marks, knuckle, wrinkles, Black head,ko kinshafa Maine yabatamiki jiki
Inamai shaidamiki cewa ynx ne lokacin dayakamata kiyake dukkan wadannan kema kidinga fita sakayau abunki baruwanki da kunshe fuska ko kice sekinyi makeup hjy fita zar abunki kinuna ainihin natural beauty dinki😍domin kayanmu gbdynsu organic ne babuna bleaching zssu sa ki haskaka fatarki tayi ta kyalli kamar madubi ze fiddomiki d ainihin natural beauty dinki ne😘kunaji barin fadamuku wani Abu billah wannan prdcts damuke dashi ynx Koda kudinki seda rabanki domin duk sunzarce nabaya ankaramasu abubuwa dayawa masu matukar anfani agyaran fata□Ina Wanda basasan shafa Mai koda sabulun kawai kike anfani dashi inamai tabbatar Miki zkg ynd jikinki zekoma luwai luwai😘
Soap:3k
Beauty kit:11k
Chat:08062991549
07046881166
07067210195
Call :07046881166
08064532391
Instagram:glow_with_mgs
Facebook:mg's skincare
amare inakara shaidamuku duk wacce tayi anfani d kayanmu Bata bukatar gyaranjiki sedai ra'ayi□
Masoya kunanan kauna yanda nakwashe aljihu domin nafarantamuku kuyi achieving goal dinku pls Nima kunanan kauna kufarantamin😩□aljihuna yafarfado hilis karnakoma kauyenmu□
Yar shawarmannan duk nasaba□ hilis kugarzayo arabani da kaya□
Nd guest what□
Duk Wanda yy siya 10k zuwa sama zesamu Karin gift😄
Pamper your skin♀
Shine like a bride□□
Glow

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Slowly ya shiga bangarensa ya zauna kan kujera, yana maida numfashi a hankali. Kokari yake ya gano laifinsa amman ya kasa, sai kokarin ganin ya hade maganar da Kabir ya fada masa nan ma ya kasa, abun is so painful. Sai da ya hade yawu sannan ya mike tsaye ya nufi windows dinsa. Ya jingina da windows din ya kai hannunsa ya bude curtains din kofar yana kallon harabar gidan, for the first time ya ji yana marmarin ganin kakarsa, rabonsa da ita tun shekara biyu da suka wuce ita bata zuwa shi ma kuma baya zuwa, sai dai ya san duk wata Daddy yana aika musu da kayan abinci, idan lokacin sallah tai kuma sai ya aika musu da abun layya da dinkuna, amman ko kiranta a waya sai ya kwashe watanin be yi ba, abun da ya damu ne da shi kawai rayuwarsa ta nan, sai kuma Daddy da Momy, ya manta cewar yana da wasu familyn na mahaifiya bayan na mahaifi, amman a yau ya tuna saboda Kabir ya fada masa maganar data hana numfashinsa tafiya daidai. Hannunsa ya saka aljihu ya ciro wayarsa ya shiga ma'adanar lambobi ya nemo number kakarsa, ya aika mata kira yana kallon wayar sai da ta dauka sannan ya kara wayar a kunnensa.

“Ashe ko yau za ayi ruwa, Mu'azu ya kira ni da kansa”

Yayi murmushi tare da kai hannu ya shafa kansa.

“Kaka kina lafiya?”

“Ina nan lafiya kalau, sai ciwon kafa ya matsa min har yanzu”

“Subhanallahi zan zo na kai ki asibiti Inshallah”

“Kuna can birni kuna ta kula da wasu kun bar mu a daji, kamar ba mu da kowa, sunayen ku ma sai a radio muke ji, idan ba mu dauki waya mun kira ba kiran ayi gaisuwa ma ba ku yi sai idan mu muka kira”

Talba ya runtse ido ya bude yana jin rashin kyautawa.

“Ayi hakuri Kaka inshallah gobe zan zo na duba ki, amman na san baki bukatar komai a yanzu shiyasa ban cika kira ba, kuma kin ga a nan aiki yana mana yawa”

“Ba ci da sha ne kawai abun da rayuwa take bukata ba, ba kai kadai na haifa jika ba, amman ka fi sauran kwanta min a rai, balle kuma ka tako kafarka garin nan, yau shekara daya da wata takwas Mu'azu, ni ma ai fushi na yi shiyasa na daina sakawa a kira min kai, kuma na ki na fadawa kowa na birni cewar ina fama da ciwo, idan na mutu ba sai ku zo ku tafi da gawata ba”

“Kaka ke din ce kin ki ki dawo a nan ki zauna tare da mu, kin da ciwon nan na ki zamu sani ai, gashi a nan muna ta bawa bare balle kuma ke”

“Ai daman haka masu arziki suke, ba kowa ne yake a cikin iyalansu yake cin amfaninsu ba, wani lokacin kamin na kusa ya ci sau daya sai na nesa ya ci sau dari, kuma ni ba zan baro kauye na dawo birni na zauna na ba, na fi son na mutu inda aka rufe uwayena da yan'uwana”

“Garuruwan ma babu kyau a yanzu bandits suna ta kai hari kauyuka”

“Toh mu dai har yanzu ba su shigo inda muke ba, kuma ina addu'ar Allah ya tsare mu”

“Ameen Kaka, Inshallahu gobe zan zo na duba ki, kuma zan dauke ki na kai ki asibiti”

“Toh Allah ya kaimu lafiya, Allah ya maka albarka ka yi marmarin matarka kenan”

“Allah ya kara miki lafiya”

Ya fada yana murmushi idanuwansa kuma suna cika da hawaye a lokaci daya, sai ya sauke wayar ya saki windows din ya juyo yana tafiya kamar wanda baya son taka kasa, bedroom ya shiga ya tube tufafin jikinsa ya daura tawul ya shiga yai wanka, sannan ya fito ya nufi wardrobe dinsa ya ciro jallabiya da gajeren boxer da vest ya saka sannan ya dauki wayarsa ya kira Line Leila ringing wayar tai har ta katse bata daga ba, saka wayar yai a aljihunsa ya nufi inda ya aje key din motarsa ya dauka ya saka aljihu tare da wallet dinsa ya nufi kofar fita yana ta sauri, kamar wanda ya manto wani abu a wani gurin. Bangaren Momy ya nufa kamin Mairo ta bude masa kofar ya danna door bell din ya fi a kirga.

“Sannu da zuwa yan ranka ya dade”

“Leila na ciki?”

“Aa tun kamin Magariba ta fita tare da kawarta Madina”

“Amal fa?”

“Ita ma ta fita tun dazun, Kabir ne kawai a gidan”

Kai ya daga mata ya juya ya nufi motarsa, sai da ya shiga ya zauna sannan ya kira sake kiran Leila, a yanzu kam sosai yake son jin muryarta domin ya san tana cikin damuwa, kuma be kamata ya kyale ta ita kadai tai ta fama ba, a nan ma ba ta yi picking call din ba, hakan kuma be han shi sake kiranta ba, abun da ba al'adarsa ba, idan yai ma mutun kira daya ba zai sake kiransa ba, not because saboda yana jin kansa no saboda ya san duk wanda aka kira be daga ba wata kila yana da uzuri ne. Sai da ya jera mata kira biyar sannan ya kira Amal.

“Hello”

“Amal kina ina?”

“Ina gurin Hajiya Yana”

“Gurin Momy kenan?”

“Eh”

“Amman kin san Daddy baya son kuna kaiwa waje da dare ko?”

“Ina tare da Momy ai”

“Leila tana tare da ke”

“Aa na bar ta a gida”

“Okay ki kula da kanki, kuma ki kira Daddy ki fada masa kina gidan Hajiya Yana”

“Toh”

Ya yanke wayar ya sake kiran Leila bata daga ba, sai ya yanke shawarar kiran Madina domin ya san suna tare a yanzu kamar yadda Mairo ta fada. Ringing daya Madina ta dauka tana wani irin kashe murya.

“Hello Ya Talba”

Be amsa ba, sai kawai ya gabatar mata da bukatarsa.

“Leila tana tare da ke?”

“Eh amman ni ina mota su kuma sun shiga vip”

Yayi shiru kamar ya tambaya ita da waye sai kuma wata zuciyar ta hana shi, sai dai hakan be hana Madina fada masa ba.

“Tare da Ali”

“Okay”

Ya fada a takaice ba tare da ya kawo komai a ransa ba, yana kokarin aje wayar ta dora masa da wata maganar.

“Ina ta son na kira na tambaya halin da yarinyar nan take ciki kuma ina tsoron kar na kira ranka ya bace, ka. Taimaka min dan Allah ka fada min ya lafiyarta take? Ko na samu hankalina ya kwanta”

“Lafiya kalau”

“Alhamdulillah, idan tana bukatar zama da ni ko kuma wani gurin dabam, zan iya sama mata inda zata samu aminci da kwanciyar hankali inshallah”

“No need”

Ya aje wayar feeling some how, ya aje wayar yana ta kallon screen din wayarsa dake dauke da hoton Daddy, sai ya sauke numfashi a hankali sannan ya kai hannunsa yai ma motar key ko kamin ya reverse mai gadi ya bude masa gate. Driving yake amman ya kasa natsuwa, sai ya rasa abun da ke damunsa, be yi nisa sosai ba ya faka kusa da wani masallaci yai fita yai alwala ya shiga masallacin yai sallah, after ya fito ya shiga motarsa ya sake daukar wayarsa sai dai wannan karon ba kiran Leila yai ba sakon kar ta kwama ya aika mata wato sms,

“If you need someone to talk I'm here”

Sai da ya tura mata sakon sannan ya kira Daddy.

“Hello”

“Daddy yanzu dai na san ka huce”

“Mace ne ni da zan yi yaji?”

Talba yayi murmushi.

“Daddy sarkin tsokana, ni dai yanzu na kira na sake rokon alfarmarka, kuma na tabbatar maka cewa dawowar Momy shi ne farincikina”

Daddy yayi shiru kamar ba zai ce komai ba.

“And Rashin Momy ya saka Leila da Amal za su kwana gidan
Hajiya Yana, ni ma zan tafi kauye gobe Inshallah”

Daddy ya tabe baki.

“Okay har da kai a masu yi min tawaye kenan”

“This time around Daddy bana tare da kai gaskiya, kuma abun da kai ya saka ni a wani hali”

“Karka damu komai zai wuce, amman ba sai kaje kauye ba saboda hanyoyin kasar nan basa da kyau”

“Allah shi ke tsarewa Daddy, zan dawo lafiya inshallahu”

“Sai mun hadu gida”

“Okay”

Yana aje wayar reply Leila ya shigo wayarsa.

“No need ina tare da wanda ya san darajata, wanda kukana yake zame masa damuwa, farinciki ya zama burinsa”

Ya karanta sakon sau daya sai ya ji kamar be gane ba har sai da ya sake karantawa. Yawu ya hade sannan ya aje wayar yai ma motar key, tafiya kadan ya tsaya ya shiga wani restaurant yai ma Aminatu take away na jalof da ruwa sannan ya dawo motar ya saka yi mata key, be faka ko'ina ba sai kofar gidansa, bude motar yai ya fita tare da takeaway ya rufe motar sannan ya doshi gate din ya saka key din hannunsa ya bude gate din ya shiga, kamar yadda ya saka key ya bude gate haka ya bude kofar ya shiga cikin falon silently.

Har yayi kamar ya aje ledar hannunsa a falo sai kuma ya zarce dakin kai tsaye, a hankali ya tura kofar ya shiga, duk kuwa da ya san ba lallai ne ya same ta har yanzu tana bachi ba, sai dai be yi zaton zai sameta a halin da ya same ta ba. Ta koma can karshen gado ta rakube kallo daya zaka mata ka karamci tsoron daya cika mata zuciya, har ya rabawa wani bangare a jikinta domin idanuwanta hawaye suke jikinta kuma yana ta karkarwa. Ya dade a tsaye yana kallonta sannan ya karasa kusa da ita ya risina a gabanta.

“Shalele miya faru?”

Kallonsa kawai take hawaye na sauko mata, me zata fada masa? Yana bukatar ta maimaita masa cewar tana jin tsoro? Bayan ya rufe kofar fita kuma ya barta ita kadai a katon gida? Har yanzu kukan rayuwar baya take ta rashin uwa da uba da family da kowa ko kuma dai tana kukan kalubalen dake gaba ne? Ta yadda zata saba da rayuwa ita kadai ba tare da kowa ba?

“I'm sorry uzurin fitar ne ya kama ni shiyasa na fita, kin yi sallah?”

Ta girgiza masa kai alamar aa jikinta har lokacin rawa yake. Kallon jikinta yai kamin ya kai hannunsa ya kama hannunta wai ko zata samu hankalinta ya kwanta.

“You're safe now, babu abun da zai same ki, and na sama mana mafita, zan tafi da ke gobe a kauye can gurin Kakata na san za ki iya zama a kauye ko?”

Ta yi shiru bata ce masa komai ba, kuma bata bar masa wata alama da zai gane tana so din ko akasin haka ba.

“Tana da son mutane sosai, na san zata rike ki hannu biyu zaki jidadin zama a can Inshallah, abun nan is not easy arika passing passing da kai amman idan kika danne sai ki rayuwar ta zo miki da sauki”

Ban da hawaye babu abun da Aminatu take.

“Zaki iya yin kukanki, ba komai na fahimci halin da kike ciki, ni ma da ban taba jin kamshin mahaifiyata ba na ji wani iri balle da kika saba da su”

Kamar jira take sai ta fashe da wani irin kuka, zaunawa yai a gurin yana ta kallonta tun tana kukan da karfi har ta gaji ta daina dan kanta, mikewa yai tsaye tare da ita ya nufi bandakin da ita, ya kai dayan hannunsa ya kunna fanfo ya tara hannun nasa ya debo ruwa ya wanke mata fuskarta sannan ya fito ya barota tai alwala. A nan ta samu damar karewa kanta kallo a madubin dake gabanta, a zahiri madubin take kallo a badini kuma rayuwarta take hangowa? Har mutum dubu nawa zata gani kamin ta samu wanda zai zame mata uwa da uba? Har guri nawa zata zauna kamin ta samu muhallin zama na dindindin, kalaman da Umma tai mata sai ya suka dawo mata sabin, jin take duk duniyar nan babu wanda zai fahimce ta, babu wanda zai gane damuwarta, tana jin wani irin yanayi mai wuyar sabo, ta kasa sabawa da rashin kowa! A rayuwarta bata taba ganin zalinci irin wannan ba, a kashe maka kowa kuma a keta maka haddi sannan a raboka da garin da ka bude ido kai wayo a cikinsa, yanzu kuma a barta a wahale tana neman sabawa da rayuwar da bata taba mafarki ba, yau ga ta a duniyar da bata san da wanzuwarta ba, hannu ta kai ta dafa gefen kanta tana shafa kan a hankali dishes dishe ta fara gani jiri ya fara dibanta sai ta fisgi numfashi da karfi tai Sulale kasa tana ambaton Allah, da gudu Talba ya turo kofar falon ya shigo ganinta a kwance kasa ya saka shi furta.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ya saka hannunsa ya dago ta ya taba kanta, ya bude ido be ga wata alama dake nuna tana motsi ba, ga fanfon daya kunna mata yana ta zuba, dankwalin kanta ya cire sai gashin kanta daya sha gyara a hannun Madina ya zubo, daukarta yai ya dawo ta ita saman gado ya koma ciki ya dauki dankwalinta ya jika da ruwa ya matse ya zo ya saka mata a gaban goshi amman be ji ta yi wani motsi ba, sai ya

kai hannunsa jikin hancinta, ya ji bata numfashi a take hankalinsa yai mugun tashi sai ya girgiza ta.

“Amina.... Amina... ”

Nan babu alamar rai a gangan jikinta, sake komawa yai ya jika dankwalin ya sake zuwa ya saka mata a goshi, ya sake girgirza.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ya furta gabansa na mugun faduwa, zuciyarsa na raya masa Aminatu ta mutu, saboda an fada masa zuciyarta zata iya bugawa ta rasa rayuwarta. Wayarsa ya ciro da sauri ya kira Ali, ya kara wayar a kunne yana ta safa da marwa sai yawo yake da hannunsa yana ala ala Ali ya daga, amman har wayar ta gaji da ringing ta katse be daga ba, aje wayar yai ya nufi Aminatu ya sake girgiza ta a karo na uku, sai dai babu alamun zata farka ya dauke ta gaba daya ya nufi kofar fita da ita kamin ya isa kofar falon numfashinta ya dawo da mugun karfi kamar an jefo mata shi, har sai da taja numfashin da karfi tana fito da ido waje, ita kanta ta san ta lula wata duniyar dake mantar da mai ita komai na rayuwa. Durkushewa yai bakin kofar ya sanda kansa kasa ya rumtse ido yana sauraren yadda zuciyarsa ke bugawa da mugun karfi. Dago ta yai ya rungume a kirjinsa.

“Kin zama daya daga cikin yan'uwana idan kika mutu a yanzu zan shiga wani hali, ki kasance mai karfin hali mana”

Ta hade yawu daker hawaye na fito mata har lokacin numfashinta da karfi yake fita bakinta har ya soma bushewa.

‘Ya kake tsammanin tsayuwar dakin da rufinsa ya yaye katangarsa ta zube? Taya zata iya yin karfi hali? Zata iya hana kanta tunani? Ko kuma zata mantar da kanta abubuwa da suka faru ne? Ko kuma dai zata daina hangen future dinta...?’

Ita da shi saka daya suke da kalar zare daya, domin tunanin da take a zuciyarsa irinsa Talba yake mata a zuciyarsa, bude idon yai sai ya yi saurin rabata da jikinsa ya ajeta kasa yana kallonta kamar yadda take kallonsa da idanuwanta dake wani lumshewa kamar mai jin bachi kana ganinta zaka san babu karfi a jikinta.

“Sannu...”

Ya furta, kallonsa kawai take ba tare da ta ce komai ba. Can kuma ta lumshe idon ta bude sannan ta fara yunkurin tashi kyaleta yai ta gwada tashin da kanta ko zata iya, cikin iyawar Allah kuwa sai ta tashi zaune sai dai ta yi ginshikai da hannayenta.

“Suma na yi?”

Ya dauki lokaci yana kallonta kamin ya daga mata kai alamar eh.

“Kin zufafa a tunani, kuma kin yi kankanta da haka, zuciyarki zata iya bugawa a ko wane lokaci kamar yadda likita ya fada”

Sai kuma yai shiru damuwa ta bayyana a fuskarsa.

“Kin tsorata ni sosai”

Ya fada yana mikewa tsaye.

“Zaki iya tashi ki yi sallah? Ga abinci can sai ki ci”

Ta yunkura ta gwada tashi sai ta kasa, dukawa yai ya dauke ta ya shiga da ita bandakin, wannan karon tsayawa yai bakin kofar har sai da ta gama tsoro yake kar ya barta ta ta sake yin na dazun.

“Ki gwada takawa mu ga”

Ba musu ta daga kafar ta fara dakawa a hankali, ciwon ya ragu sai dai jirin ne be gama sakinta ba. Yana ta kallonta har ta iso bakin kofar fitowa bathroom din sannan ya fito yana kallonta tana takawa a hankali har ta fito gaba daya, kamin ta isa bakin gado ya zauna har ta tsawwala saboda gajiya da tai da tafiyar, tana zaunawa sai ya nufi akwaitin kayanta ya bude ya dauko wani dankwali a ciki ya shimfida mata.

“Kin ga gabas nan”

Ya nuna mata sai ta kalleshi.

“Ban taba tsammanin mutane irinka suna da saukim rayuwa da arha har haka ba, ban tsammaci samunka a yadda ka zo min ba, na yarda Allah yana so na, kuma idan ya hana ka wani abun sai ya baka wani, shiyasa ya hada ni da babban mutum kamar kai kake ta hidima da ni, na gode Allah ya saka maka da alheri, ba ka dubi tazarar dake tsakanina da kai ba, kana ta hidima da ni kamar wata yar'uwarka”

Yayi murmushi sannan ya nuna mata hijabinta.

“Ki yi sallah a zaune idan ba zaki iya tsayuwa ba”

Bayan ya fadi haka ya nufi kofa.

“Ni kadai zan kwana a nan?”

Tsayawa yai sai kuma ya juyo.

“Aa zan zauna falo ne, a nan zan kwana, gobe da safe zamu kama hanyar Maradun zan kai ki gurin Kakata za ki zauna tare da ita, ina da tabbacin zata karbe ki hannu biyu”

Ya sakar mata murmushinsa mai matukar kyau da tsada sannan ya juya ya fice.

LEILA POV.

A tare suka fito da Ali, ba laifi ta samu sakewar zuciya ba kamar dazun da take a cikin damuwa ba. Da kansa ya bude mata mota ta shiga front seat ta zauna sai Madina ta dubeshi tana murmushi.

“Yayi kyau Aminin ango, lallai kasan ta kan amaryar nan ta ku, nan da nan har ka mantar da ita damuwarta”

Leila ta kalli Ali tana murmushi, shi ma murmushin yake yai yana ganin kamar da biyu Madina ta fada masa maganar nan.

“Dole ne na yi abun da zan iya na tare abokina kar ya fadi”

“Yayi kyau, ai ka fi abokinka sanin darajar mata shiyasa kake damuwa da kukansu, matarka da huta Ali, Wallahi da ni na aureka da more miji”

A zahiri da kanta take, sai dai a kasan zuciyarta tana ingiza mai kan tururuwa ne, saboda Leila ta soma dasa wani abu a zuciyarsa akan Ali.

“Kina da son zolaya Madina, yanzu dai kuje gida ku huta”

“Thank Youu Ali”

Leile ta fada sai ya gyada mata kai ya rufe mata motar, Madina ta tashi motar tana fadin.

“Angonki fa ya kira ni yana tambayar ina kike?”

“Ai ina ganin kiransa na share shi”

“Aa Leila be kamata ki yi haka ba ai sai ransa ya bace, kuma tun da har ya kira ai ya nuna miki kulawa”

Madina na rufe baki sakon Talba ya shigo wayar Leila, tsaki tai bayan ta karanta sannan ta nunawa Madina, Madina kam dariya tai ta rike wayar da hannu daya tana rubutawa Talba amsar da take ganin ta dace da shi, sai da ta tura sannan ta mikawa Leila wayar.

“Duba ki ga amsar da na bashi, ta nan zamu fara wana shi kuma mu gane irin son da yake miki”

Leila ta tabe baki.

“Ni yanzu ma ban sani ba, ina sonsa ko tsanarsa nake, bayan duk abubuwan da yake min, yanzu wannan abun da yai ya saka na fara jin tsanarsa a raina”

Madina ta yi saurin kallonta tana tukin motar.

“Da gaske? Wai kin bincika inda ya aje yarinyar nan kuwa?”

“Yace be san inda ya kaita ba, ki kai ni gurin Momy can zan kwana”

“Okay”

Daga haka bata sake cewa komai ba, sai dai a zuciyarta murmushin jindadi take, domin Leila ce kawai zata zame mata matsala a tarayyarta da Talba, idan kuma har Leila ta juyawa Talba baya burinta zai samu ciki, a tunaninta Talba zai iya neman maye gurbin Leila da ita ko dan ya batawa Leila rai, a iya tunaninta Aminatu ba matsala bace a gurinta, domin ta san waye Talba kuma ya dade tana karantar rayuwarsa fiye da Leila da suka taso a gida daya.

FARUQ POV.

Yana tsaye a tsakar gidan rike da yar karamar traveling bag, yana sanye da kananan kaya kansa a kasa yana furta

“Ameen”

Idonsa yar rine yayi ja sosai kamar wanda ya wuni ya kwana yana kuka.

“Allah ya baka abun da ka je nema Faruk, Allah ya shige maka gaba”

Mama ta fada tana fashewa da kuka, ji take kamar idan Faruq ya tafi gurin ginar zinari nan ba zai dawo ba, shi kansa yana jin wani yanayi na rashin jindadi wata kila saboda be saba tafiya mai hadari da nisa kamar wannan ba ne. Dukawa yai ya kama hannun dansa yana kallon fuskarsa sai ya ji kamar kar ya tafi ya bar Sultan.

“Dady yaushe zaka dawo?”

“Ba zan dade ba, kuma zan kira a waya na gaisa da kai ka ji”

“Momy fa yaushe zata dawo?”

Faruk yai shiru kamar mai tunanin abun da zai fada masa, ya san shi kansa dauriya kawai yake balle kuma Sultan da yake karami, an raba shi da uwarsa yanzu kuma zai tafi ya bar shi hannun Mama.

“Ita ma zata kira ka a waya ku gaisa, kuma idan zan dawo zan dawo tare da ita”

Sai kawai ya fashe da kuka, daman tun da ya bude ido ya ga Dadynsa na shirin tafiya yake ta son yin kukan, Faruk ya kama shi ya rumgume zuciyarsa tana sosuwa da kukan dansa.

“Dady zan bika, ka tafi da ni”

“Ba a zuwa da yara, amman kai ta ma Dady Addu'a, idan ya samu kudi zan siya maka komai kake so kuma zai dawo lafiya”

A take Sultan ya kara fashewa da kuka, sai Aisha ta zo ta kama hannunsa ta dauke shi ita ma hawayen ne kwance a idonta.

“Kyale Dady zamu je mu siyo minti mu sha ba zamu je da shi ba ka ji?”

“Dady zan bika zan bika Dady zan bika”

Shi ne abun da Sultan yake ta maimaitawa har Aisha ta fice da shi. Sannan Faruk ya mike tsaye yana duba agogon hannunsa, hudu da yan mintuna gashi kuma abokin tafiyarsa ya fada masa da biyar za su kama hanya. Karasawa yai gaban mahaifiyarsa ya risina gabanta yana rokon gafararta.

“Mama dan Allah ki yafe min duk abun da na yi miki na bacin rai wanda na sani da wanda ban sani ba, kuma yi min addu'a, Inshallahu da zarar na isa zan kira

ku, ga Sultan nn na bari a hannunki kuma a karkashin kulawarki, ko da Allah be kaddara min dawowa ba, Mama dan Allah karki bari Rafi'a ta dauke shi, kara yai ta zama a nan tare da ku da talauchi da ya koma karkashin kulawarta, ban zan iya abun da zata aikata nan gaba ba, kuma zan rika yi miki aike ke da ita saboda cikin dake jikinta Inshallahu”

Ya karasa hawaye ya sauko masa, sannan ya mike tsaye Mama ta bishi da kallo tana hawaye kamar wanda aka cewa idan ya tafi mutuwa zai yi ba zai dawo ba, har ya fara tafiya bata ce masa komai ba sai da saka kafarsa daya a waje zai fita.

“Allah ya maka albarka Faruk, Alhamdulillah ko Allah be ba ni arziki ba ya ba ni ɗa mai tarbiya, ni da kai ba a san gawar fari ba”

Juyowa yai ya kalleta ita ma ta kalleshi sannan ya juya ya fice ba tare da yace mata komai ba.

Ko kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

BATURIYA POV.

“Amman kina ganin idan n zubar da cikin ba wata matsala?”

“Wane irin matsala? Yau aka saba zubar da ciki ne ki rika yi ma kanki fata na gari mana”

“Tsorona nake ji Wallahi kin san abun da baka saba ba”

“Ba wata matsala kawai shawarar da zan baki karki yarda ki zubar da cikin yanzu, sai kin yi tafiyar nan da Alhaji kin dawo”

“Ni fa bana son zuwa ko'ina Ramlee, iya abun da zamu a nan ya ishemu, ba sai mun tsallaka mun bar kasar ba, ka shiga jirgi kai sama da sunan zaka je aikata sabo?”

Ramlee ta kalleta tana tabe baki.

“Kar dai ki ce min tsoro kike ji? Ashe a gaishe da masu zuwa saudiya su aikata fiye da abun da kike tsoron aikatawa, ke matan da suka kware suka waye har lesbians suke fa da matan manya wasu kuma ta baya ake yi da su”

Baturiya ta kwalo ido tana kallon Ramlee da mugun mamaki.

“Yanzu Ramlee mutun zai taka jirgi ya tafi maka ka aikata sabo? Wannan kuma ai ya zama ganganci da isgilanci”

“Babu ko daya Allah shi gafurun raheemun ne, ki rika kyautata zato mana, idan ka tara dan abun da ka tara kamin lokaci ya kure maka sai ka tuba ai, duk abun da zaki aikata wani yana can zai aikata fiye da abun da kika aikata na zubinu kuma Allah a cikin rahamarsa sai ya yafe masa ya saka shi aljanna, wani kuma zai aikata aikin lada mai yawa kuma daga karshe ya zama dan wuta”

Baturiya ta sauke ajiyar zuciya.

“Toh ai baka da tabbacin wuta zaka je ko aljanna, ni fa ina tsoron kar zunubin yai min yawa, ga kuma wani ina kokarin aikatawa yanzu cikin nan yanzu cikin wata na hudu yake”

“Masu haihuwa su kashe yayan fa? Balle ke da be ma zo duniya ba? Gaskiya Baturiya kina da matsala ana nuna miki hanyar arziki kina sanyi jiki, ni dai yanzu fada min yaushe za ki samu fita sai na fadawa dan gidanki ya shirya?”

“Fitar ce tawa yanzu zata zama aiki, idan ma cika fita za a fara saka min ido”

“Shiyasa ni ban jidadin da kika kashe aurenki a yanzu ba Wallahi saboda Faruq be da matsala kina fita duk inda kike so weather ya barki ko akasin haka, su kuwa wadannan iyayene abu kadan sai ka fara jin tsinuwa da baki kala kala”

“Wallahi kuwa, kuma kin ga za ayi saurin gane ni ce ba ni da gaskiya, domin ya ki fadawa Yaya abun da ya hada mu, sai cewa yai wai ko minene za su gani, shiyasa kudin ma na kasa kashewa, ina gudun na taba kudi Umma ta fara zargina”

“Baki da wayo ne, ai wata hanyar zaki bijiro da ita ta samu kudi, kamar sana'a ko kuma ki nemi wani aikin ma wanda zai rika baki damar fita ki ga daga nan sai ki samu kafa kina yin yadda kike so hankali kwance”

“Kuma fa da maganar ki, amman wace irin sana'a ce mai kawo kudi haka? Ni fa bana son zargi ko kadan”

“Wannan kuma sai kin yi tunani, ko kuma mu samu hanyar yin aiki zai fi mana sauki ma”

“Ssce ce da ni fa aiki zai samu da ssce? Na ga Faruq ma mai degree yana fama balle ni”

“Ai ke da Faruq akwai banbanci, ke fa mace ce kuma a cikin matan ma mai kyau da daukar hankali, shi kansa da zai bada kasansa ga irin mazan nan da suke neman maza Wallahi na aiki ba har abun da yafi aiki idan yana so sai ya samu, yanzu fa duniyar ta zama yi min na yi maka ne, ba ni girishi na baka manda”

“Ramlee kina da wayo Wallahi, ni kam sam irin wannan tunanin baya zuwa min”

“Ba ki waye ba ne a abun, idan kika gwane ni kaina sai kin fara min wani gani-gani”

“Uhm... Yanzu ki fadawa dan gidanki sai karshen satin nan za mu hadu”

“Ni fa ce min yai ki saka masa ranar da zai rika ganinki, Wallahi Fee'at kina da farinjini da sa'a, kin ga manyan mutanen nan su suke sakawa mutum lokacin da za a gansu amman ke ya yarda ki saka masa ranar da zai rika ganinki”

“Uhmmm yanzu ne zan tabbatar idan ina da sa'a ko akasin haka, sai idan na auri Fahat zan tabbatar da haka, duk kuwa da na san akwai kalubale mai yawa a gaba”
“Kina ji zai aure ki da da? Kuma anya ya san kin taba yin aure kuwa?”

“Be sani ba, kallon budurwa yake min, amman very soon zan fada masa na taba yin auren, sai dai ba zan nuna masa ina da da ba, kuma zan nuna masa cewar auren dole akai min, shi ma kuma saboda na ji yana cewa za ayi bincike gudun kar a binciko a gano wani abu”

“Kina son Fahat din nan sosai Fee'at”

“Uhmm ya hada komai ne da mace take so, kyau kudi, dan mayan mutane ga shi yana so na, jiya har tambayata yake wani kalar gida nake so yanayinsa da yadda zai kasance saboda yana son a fara gina masa gida irin tsarin da nake so”

Baturiya na rufe baki kiran Fahat na shigowa wayarta, a take murmushi ya wanke fuskarta farincika kuma ya cika ruhinta.

“Dan halak ka ƙi ambaton, kin ga shi ya kira”

Ramlee ta yi murmushi kamar yadda Baturiya ma take murmushin tana kara wayarta a kunne.

“I just call to say hi kin san idan ban kira ba hankalina baya kwanciya, bana gajiya da jin muryarki”

“Yanzu kuwa nake zancenka a raina ina ta waken ganinka”

“Da gaskiya ne ai da kin nemo mana hanyar da zamu rika ganin juna, amman sai rowar fuskarki kike min, muryar ma yanzu ba kullum nake ji ba”

“Wallahi Umman mu ce take yawan fada idan ta ga ina waya, shiyasa sai na fakaici idonta nake kiranka ko na amss kiranka, yanzu haka ma ina tare da wata kawata”

“Kin samu fitowa kenan? Amman shi ne baki kirani na zo mun gaisa ba? Ko shi ma Umma ta hana? Domin na lura Umma har yanzu bata san yarta ta girma ba”

Ta yi dariya cike da nishadi.

“Ai ba zata yarda na girma ba sai ranar da ka sace mata ni”

“Ai na dade da sace ki, dauka ce kawai ban yi ba ita ma very soon zan mai da kulawarki karkashina”

Kusan a tare suka saki murmushi ita da shi, kamin ya dora mata da.

“Yanzu kina ina? Ina son na biyo mu gaisa i miss your face and your smile”

“Ina nan bayan government house gidan wata kanwar Babana”

“Okay yanzu zan karbo wani sako a tasha idan na fito zan same ki a can sai mu gaisa, ki min kwaliya mai kyau kamin na zo”

“An gama Dear”

“I love you”

“I love you too”

Ya sauke wayar yana murmushi, a can kasan zuciyarsa yai ma Baturiya muhallin, son ta yake so bana wasa ba, shi kansa yana mamakin yadda ya zurfafa a sonta. Tuki yake da hannu daya, dayan hannunsa kuma wayarsa ce a rike ya saka ajewa, daya daga cikin hotunan data turo masa ne ya saka a wallpaper dinsa idan ya kalli hoton har wani sanyi yake ji a ransa, fuskarsa dauke da murmushi zuciyarsa wasai yau zai gana da masoyiyarsa bayan tsawon lokacin daya dauka be hadu da ita face to face ba.
Sabuwar ta sha ya nufa kamin ya isa ya kira direban ya sanar masa gashi ya kusa karasowa a ina zai karbi sakon.

“Kace gurin Iliyasu Mai gadi ka karba sai ka bashi kudin”

“Okay”

Sai a lokacin ya samu aje wayar ya faka motar gefen titi domin baya son shiga da motar cikin tashar, ya fito ya nufi gate din. Kamin ya shiga ya tambayi wani mai talkami dake kusa da gate din ya nuna masa teburin da Iliyan yake zama, sai yai masa godiya ya nufi gurin da Iliyan yake zaune kamin ya karasa shi da Faruq suka rika kallon juna, yana ta kokarin tuna inda ya taba ganin fuskar Faruq, Faruq kam yana ganinsa ya gane shi, hakan ya saka ya mika masa hannu suka gaisa.

“Kamar na sanka”

Cewar Fahat sai Faruq ya mike tsaye yana murmushi.

“Ni ai ina ganinka na gane ka, ka san ku manya ne ba ku saurin gane mutane, ni ne wanda ka kai asibiti lokacin da Mahaifinka ya kade ni”

“Anyi haka to ya lafiyar jiki”

“Alhamdulillah, gashi har muna shirin barin kasar”

“To kaga kai ne babban kenan kasa”

Kusan a tare suka yi dariya Faruq ya shafa kansa yana fadin.

“Dole ne ai tun da kasar ta zama sai a hankali idan hagu da kiya ba sai mu koma dama ba”

“Haka ne, Allah ya bada abun da aka je nema, koto zaku je ko togo?”

“Nijar zamu leka mu samu rabonmu”

“Nijar dai? Ba ku tsoron tafiya a mota kasar nan ba lafiya”

“To ya za'ayi, dole ne mu fita daman ba asan maza da zama ba, kamin mu samu abun da muka samu mu dawo tun da aikin ya zama sai wane da wane”

“Ka yi karatu?”

“Na yi karatu Wallahi degree na yi, amman aikin ya zama sai a hankali”

Da mamaki Fahat yake kallonsa domin this is the first time da ya taba ganin mai degree zai tafi nema a inda wasu suka ganin ko ba su yi karatu ba ba za su iya ba.

“Da gaske?”

Faruq yayi murmushi mai sauti. Sai Fahat ya ce.

“Na yi mamaki Wallahi ba kasafai masu irin kwalinka suke yarda su yi aikin da zaka je yi ba, indai da har kwalinka yayi kyau ka turo min cv na maka alkawarin aiki inshallahu”

“Da gaske? Allah yasa domin na raba cv gurare da yawa amman shiru ne har yanzu Wallahi”

“Karka damu wani rabon nesa yake, me kake yi yanzu?”

“Ina jiran abokan tafiyata ne”

“Okay bari na karbi sako, sai mu je motana na baka number na da mail ka turo min cv ka, kuma ka kira ni Inshallahu zan sama maka aiki, ko dan sharar gidanmu ne na san sai ba zaka raina ba”

Faruq yayi dariya sosai.

“Ai ba zaka fara ba, nan gaba kadan ma kai zaka fara goge min talkami”

Fahat ya kyalkyale da dariya.

“Aiko zaka ga keta, Allah ya nuna mana lokacin”

“Ameen ya Allah”

“Bari na karbi sako sai mu na baka ko? Iliyasu nake nema mai gadi”

“Gashi nan”

Faruq ya nuna masa shi, ba dan ya masa wani farin sani ba sai dan yawan kiransa da yaji mutane na yi a daman zaman jiran abokan tafiyarsa da yake a gurin. Fahat ya karasa kusa da shi ya gaisa ya ciro kudinsa ya mika masa sannan ya karbi sakon takardun, suka jero tare da Faruq zuwa gurin motarsa, shi ya fara budewa ya shiga ya zauna ya dauki diary ya rubuta masa addireshinsa na email a kasa kuma ya rubuta masa number wayarsa sannan ya kai hannunsa ya bude front seat.

“Bismillahi ban rike sunanka ba”

“Umar Faruq”

Faruq ya fada yana zama, sai ya mika masa takardar sannan ya bude ma'adanar kudi a motar ya ciro kudin da zai kai 20k ya mikawa Faruq.

“Wannan a kara a sha ruwa, mail dina yana jiki sai ka turo min Inshallahu zan yi ma iya kokari”

Faruq ya rasa da wane baki zai gode masa, ga wani uban mamaki daya cika shi na kyautar 20k a take.

“To ai ni ka daure ni gaba daya, Wallahi ban san me zance maka ba”

“Bana bukatar godiya, kawai kai min addu'a Allah ya cika min burina na auren wata yarinya da nake so”

“Idan aurenta alheri ne a gareka, kuma ita din matar ka ce Allah ya shige maka gaba ka aureta”

Fahat yayi dariya.

“Mutun ya taba auren matar da ba tasa ba”

“Sosai, zaka auri mace kai ta wahala da ita amman bata gani, kuma ku yi ta samu matsala ku kasa samun kwanciyar hankali saboda ba matar data dace da kai ba ce, kasan ance mata ta gari rabin jindadin duniya ce, I'm talking from experience, ko da yake kai kana da rufin asiri wata kila ba zaka samu irin matsalar da na samu ba”

“Ta gujeka saboda talauci kenan ko kuma tana azabtar da kai”

“Ba ma tare da juna yanzu, amman mace idan ba ta gari ba ce kuma ba alheri bace a gurinka kin aurenta shi yafi, duk da yake wani lokacin ba zamu san alheri ko sherin ba wani abu ba har sai mun kusancesu ko sun kusance mu”

“Haka ne, ni ma zan yi ta addu'a kamar yadda Hajiyata take ce min, kuma kai ma wata rana zata dawo gareka tana neman yafiyarka idan ta gane kuskurenta Inshallah hope dai ba ku haihu da ita ba?”

“Da daya, sai cikin dake jikinta yanzu”

Faruq na maganar idonsa har ya sauya kala yayi ja alamar bacin rai.

“Komai zai wuce, karki watsar da hakkin da yake kanka, ka yi kokarin ganin ka sauke duka nauyin dake kanka ba tare da ka zalince ba ko yaran, inshallahu Allah zai taimake ka, da kai yi zalinci kara azalince ka”

“Haka ne na gode sosai, Inshallahu zan yi kokarin yin haka, Allah ya saka da alheri ya biya bukata”

“Ameen nima na gode, Allah ya kaiku lafiya”

Fahat ya mika masa hannu sukai sallama.

“Ameen”

Faruq ya amsa sannan ya fita motar ya rufe, key Fahat yai mata ya hau titi jikinsa a sanyaye, maganar da Faruq ya fada masa ta saka ya tuna da yawan nanata masa da Hajiyar take cewa ya rika addu'a idan alheri, sai dai shi yana kallon kamar tana fada masa haka ne saboda bata son ya auri wata sai wanda ta zaba masa. Wayarsa ya dauka ya kalli hoton Baturiya dake shimfide gaban wayar.

“Ina fatar yadda kike da kyau nan, haka zuciyarki take, ko ma zuciyarki ta fi wannan kyau”

Ya fada da murmushi a fuskarsa sannan ya kai wayar a bakinsa ya sumbace ta, kana ya cire key din ya kira Baturiya ta fada masa daidai inda gidan yake, yana driving din yana waya da ita har ya isa kofar gidan.

“Gani kofar gidan”

“Gani fitowa Dear”

“I love you, sai kin fito”

“I Love you too”

Ya yi murmushi ya sauke wayar zuciyarsa cike da kaunarta.

TALBA POV.

A falon ya zauna kan karamin stairs din da kai ka sakiyar falon, domin ayi falon ne a kasa bedrooms da kitchen kuma a sama sai dai ba sama irin na gidan sama ba, wani tsari ne akai mai kyau. Yana zaune a gurin yana ta kallon falon da ba a saka komai a ciki ba sai farin fenti da kuma na'urar sanyaya daki, ya dauki enough time din da yake ganin ya kamata ace ta gama sallah sannan ya mike tsaye ya juyo da zimmar shiga bedroom din sai ya ganta zaune a bakin bedroom din tana kallonsa.

“Kin gama?”

Ta daga masa kai.

“Kin ci abinci?”

Ya sake tambaya yana karasawa kusa da ita.

“Aa”

“Ta so ki ci abinci sai ki kwanta”

“Ni kadai?”

“No nan zan kwana”

“Toh”

Ta mike tsaye tana dafa ginin ta koma ciki sai ya bi bayanta, a kasa ta zauna inda ledar abincin take shi kuma ya zauna kan gadon, da kanta ta bude ledar ta dauko takeaway din ta bude sai ta kalleshi.

“Bismillah”

“Ni na koshi, ci abincinki ki koshi”

Ta maida kanta kasa ta fara cin abincin a hankali, shi kuma sai ya ciro wayarsa ya shiga dannawa, sai ga kiran Ali ya shigo wayarsa, yana kallon kiran har ya katse be daga ba, sai da wani ya sake shigowa sannan yai picking.

“Ya akai?”

“Ka kirani wayar na silent ban sani ba, I'm sorry”

“Daman wata matsalar ce kuma yanzu ta wuce”

“Gani kofar gidanka”

Kai tsaye ya san a cikin gidansa yake nufi domin idan family house dinsu ne zai ce gashi a cikin gidansu, ba kamar yanzu da ya banbanta ta shi da gidansa ba.

“Bana ciki”

“Haba Malam ba halinka ba ne, ga motarka ka waje”

“Toh bana son ka shigo”

“Akwai maganar da nake son mu yi da kai”

Talba ya mike tsaye ya kashe wayar ta kalli Aminatu.

“Bari na budewa wani gate okay?”

Kallonsa kawai tai ba tace masa komai ba har ya nufi kofar fita.

“Karka ka dade tsoro nake ji”

Ya juyo ya kalleta sannan ya daga mata kai alamar okay. Ya fice cikin izza da isa yake tafiya har ya isa bakin gate din ya bude karamar kofar ya kalli motar Ali. Ali na ganinsa sai ya bude ya fito ya rufe ya nufo inda yake yana murmushi, a can abu ne mai wahala su yi kwana daya ba su ga juna ba, idan dayan yana da wata matsala zai kira dayan ya sanar masa amman ya lura da Talba ya canja gaba daya ko irin sakewar nan ya daina masa.

“Ya akai?”

Talba ya tambaya sound so serious domin idan babu abun da ya kawo shi zai koma ciki ne ba zai tsaya saurarensa ba.

“Ba zaka min tayin shiga ciki ba”

Talba ya sakar masa kofar, ya juyo ya dawo cikin gidan, sai da Ali yai murmushi sannan ya shigo yana ta kallon gidan, Talba ya rigashi isa gurin kofar falon dan haka ya rigashi ganin Aminatu dake tsaye bakin kofar rana tana jiran karasowarsa. Be bukatar ya tambayi dalilinta na fitowa bayan ya san ya baro ta tana cin abinci, idan ma ya tambaye ta ya san amsar ta ba zai wuce tana jin tsoro ba. Da hannu yai mata alama da ta shiga ciki sai ta juya ta koma sai dai bata yarda ta koma bedroom din ba sai ta tsaya a falon har ya shigo, Ali ma ya shigo. Kallonta yai sannan ya kalli Talba.

“What this?”

Uffan Talba be ce masa ba, kallonsa kawai yake.

“To be frank wannan abun be dace da kai ba sam, not because ina side din Leila but because I'm your friend, be kamata na ga abun da zai kai ka ga halaka ba ko ya taba mutuncin ka kuma ina gani na bari ka aikata, this is wrong very very wrong, kana tunanin idan Daddy ya gani ko Momy ko Leila da kanta za su jidadi? Haba Talba”

“Kana da wata magana mai muhimmanci ne? Bachi nake son yi”

“A nan zaka kwana kenan?”

“Ina kake tsammanin zan kwana?”

“Bana zarginka ko kadan Talba, amman sheidan mugun ne”

Talba ya nufi kofa ya bude masa alamar ya fita, wani mugun mamaki ne ya kama Ali, ya san Talba yana da zuciya sosai amman be saba masa abun da yake masa a yau ba.

“Okay”

Ali ya fada yana jinjina kansa, kamin ya juya ya kalli Aminatu data rakube guri daya tana masa kallon tsoro. Sai kuma ya juya ya fice.

“Kin ci abinci?”

Talba ya tambaya sai ta daga masa kai,

“Kin koshi?”

Nan ma kan ta daga masa.

“Shiga ki kwanta zan shigo da motata ciki”

A nan bata samu damar daga masa kan ba, balle har ta amsa masa da to ko ta shiga dakin kamar yadda ya bukata. Be kula ta ba ya shiga dakin ya dauko keys dinsa ya fito tana tsaye ya fice daga falon, sai ta sake dawowa bakin kofar falon kamar dazun ta tsaya tana kallonsa har ya bude gate din ya shigo da motar ya rufe motar ya nufo kofar falon. Sannan ta kauce masa ya shigo sai ya wuce dakin kai tsaye, ganin ya dade be fito ba yasa ta bi bayansa. Sai ta same shi zaune kan dankwalin da tai sallah tana ta taba wayarsa, bata bukatar yace mata ta hau ta kwanta daman tun dazun bachi ke kawo mata hari bayan wanda tai. Sai kawai ta nufi gadon ta hau ta kwanta ta juyo da fuskarta ta inda zata rika ganinsa. Ko da wasa be kalli inda take ba har bachi ya dauke ta, sai da ya tabbatar bachin nata ya nina ta hanyar numfashi dake ta fita da karfi yana bada sauti, sannan ya tashi ya nufo inda yake aje bedsheet ya dauki daya kana ya doshi inda switch din wutar yake ya kashe, gudun kar ta farka yasa be rufe kofar ba ya fito falon ya shimfida bedsheet din ya cire jallabiyarsa yar vest din dake jikinsa ma sai da ya cireta, domin abu ne mai matukar wahala ya kwana da riga, no matter how hot or sanyin sa ake a gari ko a waje, baya sakewa idan ya kwana da riga, sai da ya rage hasken falon sannan ya kwanta a kasa, can kuma ya tashi yai addu'a ya sake kwantawa ya rufe ido ba dan yana jin bachi ba, kuma ba dan yana tsammanin bachin zai bashi hadin kai ba, sai dai be bude idon ba har kusan daya na dare.

Yana jin motsin lokacin da Aminatu ta fito daga dakin ta tsaya bakin kofa, can kuma ta kwanta nesa da shi ba sosai ba tana facing dinsa, kamar dazun yanzu ma be bude idon ba sai da ya tabbatar da bachinta ya nina sannan ya bude idon ya tashi zaune. Fitilar wayarsa ya kunna ya haske fuskarta, sai ya hangeta tana bachi hankali kwance ta saka hannunta daya a cikin baki kamar mai tsutsar hannu.
He spend more than thirty minutes yana kallo kyakkyawar hallitar Allah, an tsara mata komai cikin kwarewa da hikima irin ta Ubangiji, hancinta ya tsayu, kana gani kasan gwanin baiwa da rahama ne yai halinci komai na fuskarta, a kasan hancin an yanka mata wani karamin baki gwanin sha'awa da burgewa, idanuwanta dake rufe suka kara bayyanar da gashin idonta daya cika kamar ta aro.
Fuskarta na ta sheki kana ganin fentin fatarta kasan ba dai mutum ba sai dai Allah, babu digon fari ko kadan a jikinta, sai dai hakan be rage ta da komai ba a kyau, sai ma kara bayyanar da godiyarta ga Allah na tsaya a yadda Allah ya yi ta.

“Unique”

Ya fada yana jin kamar a yau ya fara ganin bakar fatar da ta dara fararen mata kyau da aiba irin ta hallintar Allah Subhanahu Wata'ala. A yau ya tabbatar da akwai hikimar Allah na yin fararen mata da bakake, sai dai bakin mutum ya banbanta da kowa, domin ba a siyen baki.

Daukar rigarsa yai ya saka sannan ya dauki bedsheet din da ya shimfida ya karasa inda take ya lulluba mata, ya tsakala ta ya shiga dakin ya dauko matashin kai ya daga kanta ya saka mata, kana ya hanye mata hannun data saka a baki, sai ta turo bakin kamar mai shirin fashewa da kuka, sai dai ba kukan zata yi ba domin bachi take.

Ko kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Komawa yai cikin dakin yai alwala ya shimfida dankwalinta yai sallah nafila akai sannan ya cire rigarsa ya hau saman gadon ya kwanta. Misalin uku da wani abu ta farka, tana bude ido ta hango inda yake kwance babu kowa sai tai saurin tashi tana waige waige. Har ta yi kamar ta fara kuka sai ta hangoshi saman gadon hasken gulob din waje na hasko shi, tashi tai da sauri ta koma can kusa da gadon ta kwanta kasa ta takure kanta sosai kamar zata shige karkashin gadon. Bachi da bata farka ba kenan har sai da yai sallah asuba ya tashe ta. Sai ta farka a firgice duk da kasancewar a hankali yake tashinta.

“Tashi ki yi sallah”

Ta fara murza ido, sannan yunkura ta tashi ta nufi bandaki tana takawa a hankali kamar yadda take har ta shiga, bata sha wahala gurin kunna fanfo ba domin ta kula da yadda ya kunna mata fanfon jiya. Bayan ta gama alwala ta fito sai ta same shi zaune gefen gado yana karantu a alqur'ane da wayarsa, inda tai sallah jiya a gurin ta sake yin sallah asuba. Bayan ta gama ta daga hannunta ya yabi Allah ta miyar godiyarta a gareshi sannan ta yi salati fa Annabi Muhammad Sallalahu alaihi wassalam, kana ta bijiro da bukatarta na naman gafara ga iyayenta, sannan tai ma maka na neman mafita da madafa, sai kuma ta rufe tana yi ma al'ummar Musulmi, ta dora da salati. Jinginawa tai jikin gado tana ta sauraren karatun da yake da muryarsa mai dadi saurare, sai ta lumshe ido kamar mai bachi alhalin ba bachin take ba.

. Sai da ya kai karshen suratul Ibrahim sannan yai addu'a ya aje wayar ya kalli inda take jingine jikin gadon idonta a rufe. Hakan nan kawai ya ji yana bukatar gyara mata kwanciyar kanta jikin gadon domin bata aje shi yadda ya kamata ba, wuyanta zai iya ciwo. Tashi yai ya karasa gefen gadon a haka ya kai kyakkyawan hannunsa ya kama fuskarta da zimmar kwantar da ita sai ta bude. Idanuwanta da na shi suka sarkafewa juna, ko wanensu ya kasa yin kawaicin dauke nasa, a zahirin kyaun idanuwanta yake kallo, a yayinda fuskarsa da idanuwansa suke mata kwarjini.

“Ina kwana… ” “Ina kwana… ”

Suka furta a tare muryarsa ta muryarta sukai tarayya a lokaci daya, kamar yadda numfashinsu sukai auratayya da junansu, ta hanyar shiga da ita a tare. Ta kowace kusurwa a hancinta na shigar mata da kanshin turarensa, ya samu guri can kasan ruhinta ya kwanata. A yayin da shi shiga da fitar numfashin yake shiga tare da bugun zuciya mai tsanani. Ita ta fara dauke idanuwanta tana murmushi kadan, sai kuma murmushi ya cika bakinsa har ya kawata fuskarsa, mikewa yai tsaye yana kallon kofa.

“Kar mu yi latti, ki shirya sai mu tafi waje mu karya, sai mu kama hanyar”

“Toh Yallabai”

Ta amsa tana kokarin mikewa tsaye, sai ya nufi kofar dake kallon yana jin sunan wani iri wai Yallabai, sound so funny.

A falon ya dawo ya zauna har sai da ta fito sannan ya juyo ya kalleta he thought ko zata yi wanka ne ta canja tufafin jikinta.

“Baki yi wanka ba?”

“Baka ce na yi ba”

Ya wara ido.

“Komai sai na ce ki yi? Come on ba ki bukatar komai sai na fada miki fa”

Juyawa tai ta koma ciki bathroom din ta shiga bata ga soso sai sabulu da shower gel kusan kala uku. Bata san abun da ake da shower gel din ba hakan yasa ba tai karanbanin tabawa ba, sai kawai tai amfanin da sabulun tai wanka, bata yarda ta fito ba sai da ta leko ta ga baya cikin dakin sannan ta nufi inda akwatinta yake da saurinta kamar ba mai ciwon kafa ba, ta bude akwatin ta dauko doguwar riga ta saka tana kokarin daura dankwalin ya shigo sai tai saurin juyawa ta bashi baya, shi kuma sai ya fice yana jin wani iri.
Be sake dawawo dakin ba har sai da ta saka hijabinta ta fito falon.

“Na gama”

Juyowa tai ya kalleta ita ma kallonsa take kamin ta kalli jikinta ganin yadda ya kura mata ido. Sai ya mike tsaye ya shiga bedroom din ya hada tufafinta har Wadanda ta cire a cikin akwatin sannan ya janyo akwatin ya fito da shi, yana gaba tana binsa a hankali har suka fita falon, cikin karfin hali ta karasa gurin daya faka motarsa shi ya fara bude mata kasancewar ya rigata isa gurin motar

sai ta shiga gidan gaba ta zauna, bayan ya saka akwatin a mota ya koma ya rufe kofar falon sannan ya nufi gate ya bude ya dawo cikin motar yai mata key.

“Zan fara biya gida na yi wanka n canja tufafi sannan na tafi”

“Toh Yallabai”

“Talba, idan ba zaki iya ba ki kira ainahin sunana Mu'az”

Ya fada yana reverse sannan ya fita da motar gaba daya, ya dawo ya rufe gate din sannan ya sake komawa cikin motar ya ja suka dauki hanyar Shimkafi road.

A lokacin daya isa kofar gidan sai ya faka motarsa daga waje, sannan ya fita ya nufi gate din yai knocking aka bude masa, ya shiga ciki suna ta mamakin ganin motarsa a waje kuma a jiya be kwana gida ba. Be shiga bangarensa ba sai da ya fara shiga part din Daddy ya gaishe shi sannan ya fito ya nufi part dinsa, a gaggauce yai wanka ya fito be tsaya shafa komai ba sai turaren daya zame masa jiki sannan ya dauki abubuwna bukatarsa ya saka aljihun shaddarsa ya saka agogon hannunsa sannan ya fito yana ta sauri kar Daddy ya riga shi fitowa ya ga Aminatu a motarsa, gashi yayi sa'a Daddy ya manta be masa maganar tafiyarsa kauye ba kamar yadda ya sanar masa a jiya, wata kila Daddy ya dauka ko sai da rana zai tafi ko kuma ya fasa ne, yana ta sake sake ya mai gadin ya bude masa gate ya fita. Sai ya hango motar Leila kusa da tasa motar rage tafiyar da yake yai yana nazarin a gidan ta kwana ko kuma yau ta dawo? Ta dade a gurin.

“Miyasa kike zargina da abun da ba ni na aikatawa kaina ba? Ke kin fi karfin Allah ya jarabeki ne?”

Aminatu ta tambaya cikin wani irin kuka marar misaltuwa.

“Me ke faruwa”

Talba ya tambaya a lokacin daya karasa kusa da su, Leila da ta baro motarta ta zo gurin Aminatu ta tsaya ta kalleshi.

“Babu, kawai na tambaye ta ne ya ta ji a lokacin da mutum fiye da goma suka keta mata haddi? Kasan me? Kai nake kokarin tunawa cewa wannan gwanjo ce, wadanda wasu suka gama amfani da ita suka jefar wasu man kuma wulakantaccin mutane da basa wanka sai sun ga dama, basa sallah kuma kashe mutum ba ya musu wahala, amman ka dauko ta kake kokarin motsa kishi na da ita...”

Tana kai aya Talba ya wanke mata fuska da mari cikin wani irin zafin nama da bacin rai.

“Taya kina mace zaki aikatawa mace yar'uwarki haka? Allah ya wadaran halinki Leila”

Ta dafe kunci hawaye na sauko mata, Aminatu kuma ta duka a gurin dafe da zuciyarta tana jin wani irin zafi da tukiki na kalaman da Leila tai mata, sai ta fi jin zafin kalamanta fiye da abun da mutanen suka aikata mata, ashe haka ake ji? Tabbas jawabi ba shi da dadi, yanzu bayan duk abun da ya faru har akwai wanda zata yi kokarin koranta mata a halin rayuwar da ba ta zaba ma kanta ba?

“Ka mare ni Talba saboda wata bare? Ka dauko ka kawo har kofar gida, ban kwana a gida ba, yanzu na dawo amman ina da tabbacin ita ma din a tare da kai ta kwana! Ko kadai ne namiji daya rage a duniya na hakura da kai Talba...!”

Ta fada kai tsaye hawaye na sauko mata, tana kallonsa ido cikin ido.

“Idan ka haihu ga ta uba da uba, ka auri yarinyar Talba...! Ka aureta sai na san son da kake mata na hakika ne, sai na san ka cika ka tumbatsa da tausayinta, sai na san ka amsa sunanka Talba”

Ta fada tana nuna shi da yatsa hawaye na sauko mata. Hannu ya kai zai kama hannunta sai ta kauce ta nufi motarta ta shiga ta fasa shiga cikin gidan ta juya ta koma inda ta fito tana fisgar motar. Sai ya ji babu dadi kamar be kyauta mata ba, not because of tace ta fasa aurensa but because of ya san kishi babu abun da baya sakawa ya kamata yai mata uzuri, and be kamata ya zo da Aminatu kofar gidan ba first place har ta gani, ba ita ba ko Daddy ya gani ya san ba zai jidadi ba.

“Shiga mota mu je”

Ya fada yana kallonta, sai ta mike tsaye tana kallonsa tare da girgiza masa kai.

“Aa dan Allah kai yi hakuri, ba zan iya ba, ka taimake ni iya taimakon da zaka iya kuma na gode Allah ya biyaka, be kamata na shiga tsakaninku ba, karka yarda ka rasa yan'uwanka ba zaka taba samun mai maye maka gurbinsu ba, dan Allah ka bar ni na yi tafiyata”

Be bi ta kanta ba ya kai hannunsa ya rika cinyar hannunta ya saka a motar da karfi ya rufe sannan ya zagaya ya shiga bangaren direba yaja motar suka kama hanya.
Kuka take sosai cikin motar mai sauti, and what he hate the most is kuka, ko na yara ne baya so, yana tukin yana kallonta sai be ce mata yi shiru ba balle kuma ya tattara kalaman bada hakuri ya bata.

Sai da suka kusa fita gari sannan ya tsaya gurin wani restaurant ya siya mata abinci domin shi dai baya jin zai iya cin komai a yanzu bayan ruwan sanyi da riko ma kansa.
A gidan baya ya aje ledar abinci ya dawo driver side ya zauna tare da ruwan gora a hannunsa, sai da ya fara sha sannan ya mika mata ba tare da ya ce komai ba. Sai ta karba ta kai bakinta ta sha kadan ta mika masa sai ya karba ya rufe gorar ya ajera a muhallin da aka tanada domin ajeta a cikin motar, sannan ya cigaba da tukin. Suna hawa babban titi zuwa sokoto sai ya kara ac ya kwantar mata da kujera, nan da bachi ya dauke ta.
Har aka isa cikin garin maradun bata sani ba, har sai da ya faka gaban wani wadataccen gida dake unguwar gabas, ya kashe motar yana kallonta, sai kuma ya sake daukar ruwan ya sha ya rike gorar a hannunsa ya bude motar ya fita, kamin ya zagaya side dinta har ta bude idon ta tashi zaune tana kallon garin da yai yanayi da na su.

“Fito”

Ta fito tana kara kallon garin da take kyautata zaton ta taba zuwansa sau biyu zuwa sau uku a rayuwarta, sai dai ba zata iya kawo kanta ba. Rufe motar yai ya matsa key din hannunsa, shi kansa yana missing din garin da gidan da kuma

mutanen da suke cikin gidan. Yalwataccen gida ne da itacen dogon yaro suka kawata shi ta ko'ina daga ciki kuma irin dogon itacen nan ne da ake cewa bedin turawa, ko'ina na gidan ya sha simimti kamar ba kauye ba. Tsaye tai sai da ya fara wucewa ya shiga ciki sannan ta bi bayansa tana ta karewa gidan kallo.

“Tsohuwa... ”

Ta furta tana ta kara kallon gidan, Talba ya kalleta sai dai be ce komai ba ya cigaba da tafiyar har suka shiga cikin gidan, abun ka da family house a take gidan ya dauki ihu suna ta murna da ganinsa, wasu kuma na dan kallon Aminatu suna ganin kamar sun santa ita ma haka take ganin kamar ta taba ganin fuskokinsu.

Sai da Talba ya gaisa da su, tabasansa suka hau tsokanarsa suna masa wasa da ce masa baya son zumunci.

“Wannan fa ko ita ce matar ta mu ka zo ka nuna mana?”

Ya kalli Aminatu yayi murmushi.

“Aa”

Shi ne kawai abun da ya fada sannan ya nufi bangaren Kaka. Kamin ya shigo murmushi da farinciki ya cika fuskarta, sai dai ganin Aminatu a bayansa ya saka ta manta da komai tana kallon Aminatu. Aminatu ma Kallonta take sai ta fashe da kuka ta karasa inda take da sauri domin ta manta da wani ciwon kafa, sai ta fada jikinta tana kuka.

“Tsohuwa...”

Kaka ma fashewa tai da kuka ta rumgume Aminatu tana kuka sosai, sai kara nerkewa take jikinta kamar zata shige cikinta.

“Auta... Laaa sai yanzu na gane ta”

Wata babbar mace dake tsaye kusa da Talba ta fada, sai Talba ya kalleta ya sake kallon Aminatu dake rumgume da Kakarsa tana kuka, mamaki ya hana shi cewa komai.

“Aka ce an kashe kowa, ashe ba gaskiya ba ne”

Matar da tai magana dazun ta sake fada, tana hawaye cike da tausayi.

“Kun santa ne?”

Talba ya tambaya.

“Eh jikar kawo Bala ce dake Galadi”

Talba yayi shiru yana mamaki, ya san kawo Bala dai dai ba kowa ya sani ba a cikin yayansa balle ya har ya sheidi jikansa, daman a familyn Mahaifiyarsa ba kowa ya sani ba, da dai na Daddy ne ko Momy sukan kusan zai iya shaidar kowa.

LEILA POV.

Da kuka ta shigo gidansu Madina, ko gaisuwar da ta saba yi ma mahaifiyarsu Madina bata iya yi ba a yau saboda kukan da take. Cewar da tai ta fasa auren Talba ya fi komai daga mata hankali miyasa ta fada masa haka? Bayan ta san har ga Allah ba zata iya rayuwa babu shi ba?
Madina na ganinta ta kama hannunta suka shiga dakinta ta zaunar da ita gefen gadonta hankali tashe.

“Subhanallahi, Leila mi ke faruwa?”

Leila ta kama hannun Madina ta dora saitin zuciyarta da take jin kamar zata fashe.

“Talba Madina Talba...”

Madina ta fisge hannunta tana jan tsaki.

“Ba ki taba ba ni haushi ba akan Talba sai yau, akan Namiji kike wannan kukan Leila? Me kuma ya faru?”

Haka nan cikin kuka ta labarta mata abun da ya faru. Sai hankali Madina ya tashi fiye da na Leila, jin cewar Talba ya kwana gida daya da Aminatu, kuma har ya mari Leila akanta.

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ta fada tana mikewa tsaye.

“Bana son na je gurin Momy ne na tayar mata da hankali”

Leila ta fada cikin kuka tana jin zuciyarta kamar zata nerke.

“Leila kar fa abun da muke gudu ne zai faru, miyasa kika masa wannan furucin, kin san halin Talba da zuciya”

“Ba zaki ga laifin abun da yai min ba? Sai nawa kike gani?”

“Ba wai ban ga laifinsa ba ne, mafita nake nema mana”

Ta dawo ta zauna.

“Kin san me? Zan iya rantsuwa Talba ba zai auri yarinyar nan ba, amman kar shedan ya rinjaye shi ya fada a halaka mu kuma mu fada a komar da na sani”

Madina ta rika Leila tana kokarin tashinta tsaye.

“Kin san me? Je ki wanke fuskarki wannan lokacin ba na kuka ba ne, idan kalaman da kika yi zaki iya kiransa ki bashi hakuri”

Leila bata musa ba, ta shiga bandakin tai wanke fuskarta domin ta san Madina bata dorata a shawarar banza. Bayan ta fito ta tararda Madina ta kawo mata ruwan sanyi da cup dai ta dauka ta zuba ta sha, ta sake zubawa ta sha sannan ta aje kofin tana kallon Madina.

“Me minene mafita? Ni ba zan iya bawa Talba hakuri ba, yadda yake ji da kansa haka nake jin kaina, kuma shi ya kamata ya ba ni hakuri ai”

“Ba ta wannan ake ba yanzu, kin san abun da nake ganin shi ne mafita? Ki lallaba Momy ta dawo gidan nan idan ta dawo sai ki sake lallabata ta saka Talba ya dawo da yarinyar nan gidan nan”

Leila ta yi mata kallon rashin fahimta.

“Ta dawo gidan kuma? Idan ta dawo ai sai abun ya fi haka ma, kin manta yadda ya fara yi ne akan wannan banzar”

“Ai inda yake tare da ita a can yana kara kusanci da ita ne, amman idan aka dawo da ita a nan komai zai faru kina gani”

“Wannan ba mafita ba ce, domin zai iya disgani a gabanta idan na yi mata wani abun”

“Ai ba haka zamu samu wanda sai aureta, sai mu biya shi kin ga mun huta, ke kuma sai ki biro masa da maganar aurenki”

Leila ta yi shiru tana nazari kamin ta kalli Madina da murmushi a fuskarta.

“Haka yayi, amman Talba zai iya zargin wani abu”

“Zamu yi abun ne cikin hikima ba tare da kowa ya gane ba, ke dai ki bar komai a hannuna, kuma ki bincike Ali domin mu san inda yake aje yarinyar”

“Zan yi hakan, amman kina ganin Talba zai yarda”

“Dole ma ya yarda, idan yarinya ta kamu da son mutumen me zai iya yi? Kin ga mun dauketa cikin rayuwarmu cikin sauki”

Leila ta yi murmushi tana kallon Madina wanda ita ma murmushin take.

“Yanzu ki kira Ali ki fada masa abun da ya faru cikin, kuka daga nan sai ki bincike inda yarinyar take”

“Okay”

Ta amsa tana ciro wayarta a jaka ta kira Ali fuskarta da murmushi kamar ba ita ce ta shigo dazun fuska sharkab da hawaye ba. Yana yin picking ta fashe masa da kuka.

“Subhanallahi Leila lafiya dai?”

“Ali ina cikin matsala kana ina dan Allah?”

“Ina gurin aiki”

“Gani zuwa, zan so na same ka yanzu”

“Okay sai kin zo”

Ta sauke wayar tana kallon Madina, sai su kai murmushi a tare.

Ko kin san Kamshi na daga cikin abun da yake daga darajarki? Kamshi yana saka a ga kimar mutum a girmamashi musamman ma na Ramla incense, tana da turaruka kala ka kama daga na jiki dana daki da na tufafi, irin su Halud
Sandal flakes
Sandal wood
Signature
Kajiji
Damboun kajiji
Halud ball
Wardrobe ball
Coconut sandal
exclusive gowe
Black humra
Body milk
Kulaccam
Misik humra. Ramla Incense ta shirya tsab domin aika muku da turarenku har garin da kuke, da kudinki kalila ki samu turare mai kyau mai dadin kamshi da sanyaya zuciya, domin siye ko sari ku tuntubi Ramla incense ta wannan number 07038392576 tana aikawa har wajen Nigeria. You can check her Instagram handle ramla_incense. https://www.instagram.com/invites/contact/?i=1fl5k3wnc4opb&utm_content=43xtopa

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Tana daga waje zaune cikin mutanen gida, sai dai hankalinta ya tafi wani gurin dabam, domin kana kallonta ka san tana zaune a cikinsu ne kawai amman bata sauraren hiran da suke.

“Ai akwai makaranta mai kyau ko kaka?”

Kaka ta kalleshi tana jar carbin hannunta, idonta har ya sauya kala saboda kukan data sha na labarin da Aminatu ta bada.

“Akwai, akwai inda babu boko a yanzu? Ai sai dai idan mutum baya son saka dansa”

“Sai a sama mata makaranta mai kyau a saka ta, tun da gaki a kusa da ita”

“Karatu yana da kyau, amman ba karatu ne abun da Auta take bukata ba a yanzu, miji mai tsoron Allah wanda zai riketa da mana, domin a duk lokacin daka rasa uwaye, miji ne yake maye maka gurbinsu idan ka samu n gari, idan ni, ni ma ai ina kusa da mutuwa, wanda be tsufa ba ma ya jira mutuwa balle ni”

Kaka ta saka hannu ta share hawayen daya zubo mata.

“Mahaifin yarinyar mutumen kirki ne ga zon zumunci, ko dan'uwa be san shi ba shi sai ya san dan'uwa, zuwansa biyu da Auta zuwa na biyo ya dauke ni ya tafi da ni na ga iyalansa sannan ya sake dawowa da ni, ashe ganin karshe kenan na yi masa”

“Allah ya masa rahama, amman ya kike da shi?”

“Da ubansa da ni uban mu daya, ubanmu, ni an auro uwata daga nan aka tafi da ita can, a lokacin da Allah ya iyakance auren sai aka rabu, ta dawo a nan maradun tare da ni, shi kuma suka zauna can, wadannan Bandits sun hana yi kowa zaman lafiya, Allah ya isarwa yarinyar nan”

“Ameen, tana ba ni tausayi sosai, shiyasa ma na yanke shawarar kawo ta nan ta zauna tare da ke ashe ma yar'uwa ce”

“Ta fada min abubuwan da suka faru, ban jidadi ba mutum ko ba san inda ya fito ba ka ga yana bukatar taimako ai sai ka taimaka masa, balle har kai ka kawota, irin yarinyar nan ai bana jin ko bakar magana ta cancanci a fada mata”

Kaka ta sake share hawayenta.

“Ubanta be yi komai ba sai alheri, da shi ne da yanzu ya kame dan wani ya rumgume, amman ga tasa na watangaririya har ana wulakantata, mutane kwarai su ake ta kwashewa ana barin na banza”

Ta saka tsumman dake gabanta ta share majinar hncinta, sannan ta kalli Talba dake zaune kan gadonta.

“Da ace na isa da kai da na saka ka auri yarinyar nan...!”

Talba yayi saurin kallonta.

“Kaka ai... Ina da wanda zan aura kawai dai lokaci ne be yi ba”

“Ban sani ba, saboda ba a fada min ba, ni ai talaka ce shiyasa ba a sakawa da ni balle a kwance, ganina ma sai ka ga dama kake zuwa yi, yanzu ma ba dan kana neman inda zaka aje ta b ada ba zan ganka ba wata kila sai na mutu, saboda uwarka na haifa ba uba ba, shiyasa ban isa na saka ayi ba ko hana, ban isa na san komai ba”

“Ba haka ba ne kaka, idan kin kula Aminata ba aure take bukata ba a yanzu, kuma kin ga Daddy ya zaba min Leila taya zan zo masa da maganar wata kuma?”

“Ba aure take bukata ba? Saboda bata kai mizalin auren ba? Ko kuma saboda ita jinin talauchi ce kamar ni? Ko kuma saboda kana dan Boko ita tana yar kauye? Ko kuma saboda tsatsona ce? Ita wacan da yake bangaren ubanka ta fito ai ka aminta ko?”

“Ba haka ba ne Kaka kin yi min kuskuren fahimta, tun kamin yarinyar nan ta zo an tsayar da maganar auren mu da Leila, rana ce kawai ba a saka ba”

“Amman ai ba a taba fada min ba, saboda an maida ni talaka, wato da sau lokacin auren yayi sai a fada mana ka yi aure ko kuma zaka yi? Daman tun da aka haife ka suka saka hannu suka dauke ka, ba suke waiwayar inda muke ba, dangin ubanka ai babu wanda baka sani ba, amman na nan sai dai su suce sun sanka, ina matsayin mace data haifi uwarka amman sai ka share shekara biyu baka zo inda nake ba, na tabbatar da in da arziki da kullum sai ka ziyarce ni, Shi

wacan uban daya dauke ka be nuna maka ka so dangin uwarka ba, balle ya nuna maka ka bisu”

“Ba haka ba ne, Kaka dan Allah karki fadi wata mummunar magana akan Daddy, ba shi da laifi a nan”

“Daman ai ba zaka ga laifinsa ba, ba zaka yarda ka bata masa rai ba, amman ni da nake uwar data haifi uwarka a baka gudun bacin rai na, kuma baka damu da ni ba, to ni ma babu ruwana daga yau duk wani abu naka babu hannuna a ciki, ba aure ba ko mutuwa kai kar a fada min, kuma ni bance idan na mutu ka zo gaisuwa ba”

Kaka ta karasa a fusace, tana dauke kafafuwanta daga dayan bangaren ta maida dayan. Talba ya mike tsaye da sauri yana furta

“Innalillahi wa'inna ilaihirraji'un”

Ganin yadda karamar magana ta juye ta zame masa babba. Har ga Allah shi dai ba zai ce yana son Aminatu ba, ko a da can da yai yunkurin aurenta zai yi ne saboda gudun fadawa halaka da kuma tausayinta da yake amman ba dan yana sonta ba, a yanzu kuma yana ganin ta samu mafita na gaduwa da wasu daga cikin danginta yana ganin kamar komai zai zo masa da sauri ita ma ya zo mata, sai kuma Kaka ta zo masa da wani sabon zancen kamar saukar aradu.
Zuwa yai ya durkusa a gabanta ya dafa hannayensa yana kallon kakar tasa data dauke kai.

“Haba Kaka, ni ma ai abun tausayi ne, ina zan iya da mata biyu a yanzu? Kin san ni ba mai son rigima ba ne”

“Ban sani ba, ai baka tashi a gabana ba balle na sani, su isassu su suka san abun da kake so da wanda baka so, ni ba zan cilasta ka aurenta dole ba, daman ai ban isa na yi hakan ba, amman Wallahi Mu'azu wannan ne abu na karshe da zan roki ka yi min, har kasa ta rufe idona”

Ta karasa idonta na cika da hawaye.

For the first time da Talba ya aikata wani abu ya ji ina ma be aikata shi ba, a yau kam ya ji kamar ace be zo garin nan da Aminatu ba.

“Amman kaka yarinyar nan bata dade ba fa, yau yau muka zo sai kuma ki dauki min wata maganar aure? Ina laifin ma ki barta ta kwana biyu?”

“Yanzu nake da wannan damar, idan ka saka kafarka ka tafi ba zan sake ganinka ba sai nan da wasu shekaru, wata kila sai na mutu. Ka yi hakuri Allah zai bata wani ai ba kai ne kadai dan'uwanta ba, zata samu miji na gari inshallahu”

Gaba daya sai ya ji kalaman bakinsa sun kare, ya zai yi ya fahimtar da kaka sai ya rasa. Mikewa yai tsaye ya nufi kofar fita cikin yanayin damuwa. Fitowa yai daga cikin gidan gaba daya bakin kofa ya fara tsayawa sai kuma ya fara takawa ya nufi gurin daya aje motarsa, be karasa ba ya juyo yana kalle kallen neman mafita sai ya hango Aminatu zaune gindin wani icen dogon yaro, ta bashi baya. Sai da ya sauke ajiyar zuciya a hankali sannan ya juya ya doshi inda take, ta bayanta ya fara tsayawa jin motsin mutum yasa ta kai hannu ta share hawayenta. Sai ya zagaya gabanta ya zauna kusa da ita a saman dutsen dake

gurin, akwai hasken gulub a gurin amman haka be hana shi ciro wayarsa ya kunna fitilar ya haska fuskarta, arba yai da hawayen da take.

“Kuka dai? Bayan na kawo ki gurin Kakarki har kina neman ki fini gata”

Kallonsa tai wasu hawayen na sauko mata.

“Baka san yadda nake ji ba”

“Na sani, ni ma ai na rasa uwa da uba kin tuna?”

“Ka san yadda ake ji idan an rasa uwa, da uba, amman baka san yadda ake ji ba idan an rabaka da su a gabanka, baka san yadda mace take ji ba idan aka ci zafinta.. Shi ma na kasa mantawa... ”

Ta fashe da kuka.

Sai jikinsa yai sanyi shi din ba mace ba ne, amman kalmar daya fi tsana ita ce fyade. Shiru yai yana sauraren kukan da take rerawa a hankali can kuma ya dauke kai.

“Shi ma zaki manta nan gaba kadan”

Daga haka yai shiru yana ta kallon wani gurin zuciyarsa kuma tana masa wani iri saboda kukan da Aminatu take, a kokarinsa na dauke mata hankali ya ce.

“Kina son karatu?”

Ta kai hannunta ta sake share hawayen da suka ki tsaya mata.

“Da can, ina so ina da wannan mafarki”

Sai ya kalleta

“Yanzu fa?”

Ta girgiza masa kai alamar babu.

“A yanzu ina tafiya ne a yadda rayuwa ta zaba min na tafi, duka burina da mafarki ya ruguje”

“Idan na miki alkawarin wani abu zaki yarda?”

Ta daga masa kai tana kallonsa still hawaye na sauko mata.

“Na miki alkawarin farinciki, kuma na miki alkawari zan cika miki wannan burin na karatu da duk wani buri naki da be fi karfina ba”

Shiru tai bata ce masa komai ba, a yanzu kam tana ganin kamar cikin burinta ba shi da amfani, Domin an baro kyau ne tun a gurin wanka, ta rasa farincikinta dawowa da shi kuma ba zai yiyu ba.

“Akwai sanyi ki shiga ciki”

Ya fada bayan ya daga kansa yana kallon hadarin dake haduwa a samaniya. Ita ma kallon hadarin tai sannan ta mike tsaye.

“Kaka ta ce idan ka tafi zaka yi shekara baka dawo ba, gobe zaka tafi ko?”

Daga zaunen da yake ya sakar mata murmushi sannan shi ma ya mike tsaye.

“Haka dai take gani, amman fada min kin saba da ni ne, za ki yi marmarina idan na tafi?”

“Me zai saka ba zan yi marmarin mutum mai karamci da sanin darajar dan adam kamar kai ba? Yallabai wani ya taba fada maka kai mutumen kirki ne? Kana daya daga cikin mutanen da suke wahalar samuwaa wannan zamani, mutumen da baya duban dukiyarsa ko kyaunsa ko asalinsa yake nemawa wani musulmi dan'uwansa mafita!”

Wani irin kallonta yake cike da shaukin kalamanta.

“Wani ya taba fada maka zuciyarka mai kyau ce?”

Ya girgiza mata kai alamar aa.

“Ban taba haduwa da wani mutum mai karamci da mutumci da sanin darajar dan'adam kamar kai ba”

Yayi murmushi yana sanda kansa kasa.

“Da ace ko wane namiji zai zama kamar kai, da rayuwar mutane da yawa ta inganta, baki yayi kadan ya gode maka, ina fatar Allah ya tsare gabanka da bayanka ya shiga gaba a lamarinka ya zama gatanka ya haska lamurranka”

“Ameen”

Ya amsa yana mata wani irin kallo da shi kansa be san na minene ba, tun da yake a rayuwarsa ba a taba tsaya a gabansa a yabe shi kamar yadda Aminatu tai masa ba.

“Allah ya tsare hanya”

Ta fada tana jin babu dadi, dan zaman da tai da shi sai ta ji kamar ta saba da shi, ji take kamar kar ya tafi ya barta. A nan shi ma kasa amsawa yai sai ya bita da kallo har ta isa bakin kofar gidan ta shige ciki.

“Oopss”

Ya furta tare da busar da iskar bakinsa, sannan ya zauna baki dutsen. Ma'adanar lambobi ya shiga neman number Ali sai ga kiran Daddy ya shigo wayarsa. Da sallama ya amsa yana mikewa tsaye ya nufi gurin motarsa.

“Ranka ya dade idan zaka kwana a can ai sai ka fada mana, da zaka tafi ma baka fada mana ba, kuma ka san yadda hanyoyin nan suke”

Talba yayi murmushi yana shafa kansa.

“Ayi hakuri Daddy, ni ma ban dauka zan kwana ba, sai dai ganin na dade ban zo ba yasa na ce bari na kwana saboda Kaka”

“Hakan na da kyau amman a rika addu'a, Allah ya tsare, tana kusa da kai ka bata wayar mu gaisa?”

Sai da ya kalli kofar gidan sannan ya amsawa Daddy.

“Aa ina tunanin ta yi bachi”

“To a gaishe ta pls”

“Inshallah thank you”

Ya sauke wayar, sai kuma ya sake maida ita kunnensa bayan ya aikawa Ali kira.

“Hello”

Ali ya daga sai ya ji muryar yaransa a kusa da shi, da alama yana gida tare da iyalansa.

“Kana gida ne?”

“Yes gwaro kana da magana ne?”

“Yeah”

“Okay Ina jinka”

Ya fada yana tashi ya fita daga falon, sai da Talba ya daina jin hayaniyar yaran sannan ya biro masa da abun da ya faru tsakaninsa har zuwa abun da Kaka tai masa. Ba karamin mamaki Ali yai ba jin cewar Aminatu da Talba yan'uwan juna ne.

“I'm happy for her yanzu ta huta da rabe rabe”

“Seriously? Bayan kana ta hanani?”

“No bana son kana samun matsala da Leila ne, kuma ya zama ni ne sanadi, ba zan jidadi ba, kuma duk wani abu da zai taba mutuncinka ya zubar da kimar ka bana sonsa ka sani”

“Yanzu miye abun yi ina cikin matsala Wallahi”

“Kana da wata mafitar data wuce ka amince ka auri yarinyar ne?”

“Wasa dai kake, na yi yaya da mata biyu”

“Can da kai yi niyar aurenta ya zaka yi da ita?”

“Wannan ai dabam ne, daman zai aureta ne saboda gudun abun da zai je ya dawo, kuma ni ada niyata idan ta samu wanda take so zan rabu da ita ta aure shi, daga baya kuma tunanin kawota gurin kaka ya zo min ashe wani sabon fitina

ce zata bullo min, kuma ka san ban isa na ce zan yi auren sirri na munafucin Kaka ba, idan na yi haka zai zama akwai zalinci a ciki”

“Ka lallabata idan ta fahimta shikenan idan kuma bata fahimta ba, kawai a auri yarinyar nan Talba, tsakani da Allah kai kanka kana bukatar aure, kuma ga Leila bata shirya ba a yanzu, kuma kai da Leila kun kasa fahimtar juna, dazun ma ta zo nan tana bincikar gurin da ka kai yarinyar, abun nan fa ya dame ta, tana son ka kai da ita girman kai ya hana ku fahimta, amman yanzu na fi yarda kana son yarinyar nan fiye da Leila”

“Ali baka da hankali, miya kawo maganar nan?”

“Haba Talba ka damu da damuwarta, ka dauke ta ka kaita gidanku har ka yi fada da Leila a kanta, sannan ka kaita gidanka yanzu kuma ka kaita gurin kakarta domin kawai ka sama mata mafita, zaka iya yi ma Leila haka?”

“Me zai hana indai har zata shiga a halin da yarinyar nan ta shiga?”

“Bari na fada maka gaskiya Talba, idan ka auri yarinyar ba zan jidadi ba, saboda zaku samu matsala da Momy da kuma Leila, kara ma Daddy na san yana son abun da kake so, kuma yana da saukin fahimta zai maka uzuri. Abu na biyu wanda nake ganin shi ne mafita a gareka shi ne auren yarinyar nan, saboda ka farantawa Kaka rai, kuma ina da tabbacin yarinyar nan zata samu kulawa yadda ya kamata, saboda ka san halin da take ciki ba zaka yarda ta shiga wani hali ba, tsakani da Allah yarinyar nan ta shiga damuwa da yawa a yanzu farinciki kawai take bukata idan kasan zaka aurenta ta zo ta samu matsala karka yi”

Talba ya sauke ajiyar zuciya.

“Tsofun nan rigima ce da su Wallahi”

“Wata kila kuma lokacin auren ne yai, ka san komai yana da lokaci, ni yanzu ai ba za shiga tsakaninka da yar'uwarka ba, duk dai bana son a shiga hakkin Leila, ka fara fahimtar da ita idan ta ki sai ka yi magana da Daddy ka ji abun da zai ce, idan ya amince shikenan idan kuma ya nuna akwai matsala sai mu sake neman wata mafitar”

Talba ya sauke ajiyar zuciya.

“Ban dauka abun nan zai zame min haka ba, and ni dai ba sonta nake ba, ita ma bana jin tana so na”

“Karka damu da sai ta soka, kai ma kuma na san kana sonta, ka kai level din da ya kamata ace ka aje yaya Talba”

“Let me talk to Daddy first”

“Okay, Allah ya zaba maka abun da yafi alheri, kai ta addu'a”

“Abu kamar a film”

Ali yayi dariya.

“Haka Allah yake ikonsa, kaga zak taimaki yarinyar ta samu rayuwa mai kyau”

“Ko ban aureta ba, na mata alkawarin rayuwa mai kyau, zan yi duk abun da zan iya na ganin na faranta mata rai”

“Yanzu dai zabi ya rage naka”

Be sake cewa komai ba ya kashe wayar ya rumgume hannayensa yana tunanin kalaman da Ali yai masa. Ba zai ce yana son Aminatu ba, haka ma ba zai sheidi tsanarta a zuciyarsa ba, tausayinta ya bi jini da jikinsa ya tsaya masa a rai. And of course idan ya aureta ba zai cutar da ita ba, amman ya zata ji? Aurensa ma wani sabon kalubale ne a gurinta.

“Kaka...”

Ya furta yana runtse ido, cike da rashin samun mafita.

AMINATU POV.

Tana baro gurin sai ta tsaya a zauren gidan ta fashe da kukan da bata san dalilinsa ba, wata kila saboda Talba zai tafi gobe ya barta ne, gashi kuma Kaka tace idan ya tafi sai ya shekara yake dawowa. Dukewa tai a gurin ta dafa kasa tana ta kuka sai bakincikin ya dawo mata sabo. Sai da tai kukanta mai isarta sannan ta share hawayenta ta shiga cikin gidan, kanta a kasa tana ta boye fuska har ta shiga dakin Kaka. Tun daga yanayin sallamarta da tai da muryar kuka Kaka ta gane kuka tai.

“Wa'alaikissalam Auta”

Yanayin yadda Kaka ta kirata sai ta ji kamar Inna ce ta kirata, kallonta tai sannan ta karasa kusa da ita ta zauna.

“Kin ci abinci?”

“Bana son komai, Tsohuwa na kwanta a jikin dan Allah”

“Kwanta auta”

Kaka ta fada cike da tausayi, sai ta kwanta a gurin ta dora kanta a cinyar kaka ta lumshe ido kamar mai bachi.

BATURIYA POV.

“Wai yanzu can ba a bar masa Sultan?”

Babban Yayansu ya tambaya, sai Umma tai karaf ta ce.

“To me zamu yi masa? Daman idan aka saki mace ai uba ne yake rika yayansa, ni Wallahi bana son ma rika yayan Faruq”

“Aa Umma kar a zafafa, dan'uwa ne fa, kuma abun da ya faru baki san mai gaskiya a tsakaninsu ba, tun da shi dai be fadi laifinta ba yace ki minene zamu gani, ita ce kawai ta fadi na shi”

“Ita ma dai ai ba zata masa karya ba, bayan duk hakurin da tai da shi, ga talauci”

“Allah ya sauwake, wannan ai na Allah ne, ba ku san arzikin da Allah zai masa ba nan gaba”

Duk maganar da ake Baturiya bata saka bakinta ba, har sai wayarta tai ringing sannan ya mike tsaye tana fadin.

“Ranar Monday zan je asibiti Umma”

“Allah ya kaimu, idan an rubuto magani sai mu kai masa ya siya”

“A kawo dai na siya”

Ya fada yana kallon wayar dake hannunta, sai dai be ce komai ba har sai da ta shiga ciki.

“Waya siya mata wannan wayar?”

“Tace adashe tai”

“Wanda ke fama da talauchi ina zai samu kudin yin adashe? Idan har zata samu yin adashe a gidansa to karya take masa kenan na cewa yana barinta da yunwa!”

“Dan Allah ka daina ma wannan maganar, mace ai tana da hikima kuma talauchi ba ita kadai ta fada ba, jikinta ma ai ya nuna haka, ko zuwa yai gidan nan haka zai fita sisin kwabo ba zai ba ni ba, rabon da yai min alheri har na manta”

Mikewa yai tsaye yana sauke ajiyar zuciya.

“Allah ya sauwake, ni zan tafi idan an rubuta maganin sai a aika min da takardar”

“Toh Allah ya maka albarka, ya kara rufa asiri”

Sai da ya amsa da amin sannan ya gyara babbar rigarsa ya fice daga falon yana yi ma Umma sallama.
Mai da kofar dakin tai ta kulle sannan tai picking.

“Yan mata...”

A take ta ji gabanta ya fadi, domin muryar babban mutum ta ji ba saurayi ba, gashi bata san ta bawa wani number ta ba.

“Wake magana?”

“Nine dai da ake ta yi ma rowa bayan a lasa min zuma”

Murmushi tai domin ta gane mai maganar.

“Aa waya isa? Sai idan baka bukaci ganina ba”

“Aa wacan karon ma ni kadai na san wahalar dana sha kamin na samu ki amince min, yanzu kuma kin fara guduna, Ramlee tace wani saurayi ne yake dauke miki hankali, shiyasa na ce ta turo min number ki na yi rokon iri, ko za a laba ni na sha miya”

Ta yi wata shu'umar dariya.

“Alhajina kenan, ko dai a laba wasu su sha miya ba, kai ai ka wuce nan”

“Anya dai, gani sai bibiya nake, ko maganar zuwa chine da na miki, ba ki ce min komai ba, ko da yake haduwar ma ta yi wuya balle zuwa wata kasar”

Ta sake yin dariya sai dai wannan karon bata ce komai ba.

“Yanzu dai a fada min yaushe za a sake labani?”

“Fitar ce tana min wuya yanzu, amman dai ranar Monday za mu hadu”

“Zan iya jira har Monday? Na zaku fa”

“Haka nan dai zaka yi hakuri har Allah a kai mu, sauran kwana hudu ai”

“To ya na iya tun da abun ya zama na manya, ina saurarenki Gimbiyata”

“To yayi Alhajina zan maka shiri na musamman kuwa”

Dukansu dariya suka yi sannan ya kashe wayar, ita kuma ta zauna bakin gado tana nazari, kamin ta kai hannunta ta saka cikin riga ta fara shafa cikin tana jin tausayin cirewar da zata yi, wata zuciyar na raya mata karta aikata, a yayinda dayar take ayyana mata rashin mafita a al'amurranta matukar bata yarda da zubar da cikin ba.

‘Idan na zubar shikenan na gama idda, zan samu damar auren Fahat, amman kuma zai yarda ya aure ni as bazawara? Idan kuma na boye dole a gaskiya zata fito za a ji’

Haka dai take ta sake sakenta, ta kulla wannan ta kwance wacan. Sam zuciyarta bata kawo mata Sultan kusa balle har tai tunanin a wane hali yake ciki a yanzu, gaba daya ta shagaltu da soyayyar Fahat.

“Wallahi da na san zan hadu da shi, da ban auri Faruq ba”

Mikewa tai tsaye tana jin wani kalar bakinciki ina ma ace ita din budurwa ce ba bazawara ba, da yanzu burinta ya cika.

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

A dakin Kaka Aminatu ta kwana, kaka na kan katifa ita kuma tana kan gado, asubar fari ta farka ita da kaka sukai sallah. Kaka na jan carbi ita kuma tana azakar din data manta when last ta yi saboda rashin kwanciyar hankali da natsuwa. Bayan ta gama ta daga hannayenta ta mikawa Allah bukatar ta kuka kai kukanta.

“Tsohuwa ina kwana?”

Sai Kaka ta amsa masa da murmushi a fuskarta.

“Lafiya kalau Auta, an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah”

“Maa Shaa Allah, fatar dai idan kika yi sallah kina yi ma iyayenki addu'a domin mamaci babu abun da yake bukata kamar addu'a”

“Ina yi tsohuwa ina yi sosai”

“Toh Allah yai miki albarka, ya baki miki na gari”

“Amin ya rabb”

Ta amsa tana yin kasa da kanta, ba laifi tana jin sakewa a gurin tsohuwa fiye da ko'ina wata kila saboda tana jininta ne ko kuma saboda ta santa ne, ko kuma dai dan bata da kyara ne amman Madina ma ai bata da kyara sai da bata jin sakewa a can, duk kuwa da kasancewar kwananta daya a nan.
Misalin Bakwai na safe aka shigo da kunu da kosai. Kaka da kanta ta dauki karamin kofi ta zubawa Aminatu nata sannan ta dauko mata sugar dake cikin wani bowl mai murfi.

“Ki saka wanda ya isheki, anjima zaka kawo dumame sai ki ci, idan kuma indomie kike so ko kwai akwai a dakin ajiya sai a dafa miki”

“Aa wannan ma ya isa”

Ta fada tana jin marmarin kunun a ranta, rabon da tasha kunu tun lokacin da tashin hankali ya fara samunsu, daman mutumen kauye ba ka raba shi da kunu ko fura ba. Sosai ta zuba surgan ta motsa da karamin ludayin da Kaka ta saka mata sannan taja kunun gabanta ta fara ci tana cin kosan.
Kaka ta janyo radio ta kamo bbc sannan ta aje radio kusa da ita ta cigaba da jan carbin.

“Assalamu Alaikum”

Talba ya shigo da sallamarsa, sai Aminatu ta dago ta sauri ta kalleshi tana shan kunu, Kaka ma juyowa tai ta kalleshi sai ta dauke kai ba tare da ta amsa ba.

“Wa'alaikassalam”

Aminatu ta amsa masa, sai ya zauna kusa da ita can Center carpet din da take zaune yana sakar mata murmushi. Kallonsa kawai take cike da shauki tana jin kamar tace masa kar ya tafi, daman jiya da tunanin tafiyar ta kwana a ranta, kasa dauke mata ido yai har sai da ita ta kawar da nata idon tana sannan shi ma ya dauke nasa yana kallon Kaka zai mika mata gaisuwa a yayinda ita kuma ta dago zata mika masa nata gaisuwar.

“Ina kwana” “Ina kwana”

Sun fada a tare, shi yana kokarin gaishe da Kaka ita kuma tana mika masa nata gaisuwar, sai suka kalli juna ita da shi murmushi ya biyo baya, wanda ya karawa kowanensu kyau da haiba.

“Lafiya Kalau an tashi lafiya?”

“Alhamdulillah”

Ta amsa sannan tai kasa da kanta, shi kuma ya juya ya saka gaishe da kaka, kamar dazun yanzun ma bata amsa masa ba sai ta daga masa alamar amsawa. Murmushi yai ya kalli kunun da Aminatu take sha.

“Kaka ni ba za a bani kunun ba? Saboda ni ba dan gida ba ne ko kuma me?”

Kaka ta yi kamar bata ji shi sai jan charbinta take. Aminatu ta mikawa Talba nata.

“Ka sha wannan”

Ya mika hannu ya karba ba dan yana son sha ba, kusan zai iya cewa be taba shan kunu ba a rayuwarsa idan ma ta taba to ya manta, tashinsa Momy ta saba masa da tea ba kunu. Babu kyama ya kai kofin bakinsa ya kurba, sai yai saurin runtse ido, ba dan dadi ko rashin dadin kunun ba, sugar da Aminatu ta zuba ne ya ji shi har cikin kansa, saboda be saba shan suga da yawa ba, wani lokacin ma ya kan iya jika Lipton kawai ya sha ba tare da suga ba, idan ma zai saka sugar baya wuce one or two to three cube.

“Shalele haka kike shan zaki ko Kaka ce take son bata ki?”

“Ni na zuba”

Daukar kunun yai ya kara a cup din ya motsa sai zakin sugar ya ragu, sai dai hakan be hana shi jinsa har cikin kansa ba, haka dai ya daure yana shan kunun idan yayi ludayi daya sai ya mika mata ta sha daya a haka har suka shanye kunun.

“Idan baki koshi ba ki kara ki cika cikinki, sai ki kwanta kamin a kawo dumame”

Kaka ta fada tana janyo kwanon da take ajiyar goro ta bude ta balla kadan ta saka a baki tana taunawa.

“Na koshi”

Aminatu ta fada tana lashe baki.

“Kaka ni ban koshi ba”

Talba ya fada yana kallonta, sai tai masa banza kamar ma bata san da zamansa a gurin ba. Murmushi yai ya tashi ya kuma kusa da ita ya zauna ya kai hannunsa ya dafa ta.

“Haba Uwargida kin taba ganin matar dake son aljanna kuma tana fushi da mijinta”

“Kai Mu'azu babu wani abun da zaka min ka wanke kanka, kar nake kallonka, kuma ka gwada min yan'uwan ubanka sun fi na uwarka, ba zan manta da wannan ba, ka nuna wasu dangin sun fi wasu”

Saurin dauke hannunsa yai yana jin wani irin, har ga Allah ba manufarsa kenan ba, amman kaka ta kasa fahimtarsa. Kallon Aminatu yai.

“Shalele zaki iya zuwa waje? Zamu yi magana da Kaka”

“Toh”

Ta amsa tana kokarin tashi sai Kaka tai karaf ta ce.

“Babu inda zata je, ni ce uwarta ni ce ubanta a yanzu, bata da wasu dangin sai ni, idan zaka yi maganar kai a gabanta ko kuma ka je can gurin naka dangin kai magana ai kai kana da gata”

“Haba Kaka wannan wace irin magana ce kuma?”

Ta furta cikin rashin jindadi, sannan ya mike tsaye ya ciro kudin dake aljihunsa ya aje masa a gabanta.

“Gashi nan a ci goro ni zan kama hanya, kuma zan aiko mota a daukeki saboda ciwon kafafuwan a kai ki asibiti”

“Ai daman idan ka zo garin nan kamar ana tsikararka kake, shiyasa kowa baka sani ba na dangin uwarka, idan ka zo baka san kaje ko'ina ba, idan kuma ka tafi sai an sake ganinka. Ka dauki kudinka sisin kabo bana so naka Mu'azu, ai baka gan ni a wahala ba, komai bana so naka, kuma karka sake takowa garin nan da sunan zuwa ganina na yafe maka har na mutu”

Sai a yanzu ya tabbatar da gaske kaka take, domin babu alamar wasa a fuskarta sai ma fushin dake kara bayyana a maganarta.

Kallon Aminatu yai wanda ita ma kallonsa take tana mamakin yadda Kaka take masa magana da fushi, be ce komai ba ya dauke kai ya fice daga dakin cikin rashin jindadi.

“Auta dauki kudin nan ki kai masa”

Kaka ta fada tana nuna mata kudi, kamar marar kuzari haka Aminatu ta isa gurin kudin ta dauka ta fito daga dakin tana jin kamar ta tambayi kaka dalilinta na kin karbar kudin.
Ko da ta fito waje yana zaune cikin motarsa ya bar kofar a bude yana kallon kofar gidan kamar ya san zata fito, tafiya take kamar wata hawainiya har ta isa gurin motar ta ja ta tsaya, ya dade yana kallonta ita kuma ta kasa daga ido ta kalleshi saboda kukan dake son zuwa mata.

“Shalele ya akai?”

Ta mika masa kudin da hannu biyu. Sai yai murmushi.

“Kin ga na kawo ki nan amman kin fini fada, saboda ke Kaka take fushi da ni”

“Ko dai tana jin an dora mata lalura ne?”

Ta tambaya hawaye na cika idonta.

“Aa wani abun ne dabam”

Ta hade yawun bakinta.

“Zan koma Gusau”

Bata ce masa komai ba, kuma ta kasa daga idon ta kalleshi.

“Ba zaki ce min Allah ya tsare ba?”

Ya furta yana kallon yadda yanayinta ya sauya, shi kansa yana jin kamar kar ya tafi ya barta. Sai a lokacin ta kalleshi hawaye a sauko mata.

“Da gaske idan ka tafi sai bayan shekara zaka dawo?”

Ido ya kura mata sannan ya fito cikin motar ya tsaya a gabanta still yana kallonta.

“Ba ki son na tafi?”

Samun kanta tai da daga masa kai.

“Kina son na dawo?”

Nan ma kan ta daga masa.

“Zan dawo”

“Yaushe?”

Ta tambaya cike da shauki da kuma zakuwar ta ji yace mata gobe ko jibi.

“Yaushe?”

Ta sake tambaya.

“Ba da dadewa ba”

“Yaushe?”

Ya shafa kansa zuwa hancinsa.

“Cikin satin nan”

“Ya za'ayi na yarda zaka dawo”

“Saboda nace zan dawo, idan na ce zan yi abu, zan yi”

Ta dauki idonta hawaye na sauko mata sosai, sai take jin kamar shi ma din idan ya tafi ba zai dawo ba. Ya kara matsowa kusa da ita cike da tausayinta.

“Kina son na zauna ne?”

Ta daga masa kai sai ya saka hannunsa ya dago kafadarta.

“Idan kina son na zauna sai idan zaki yarda ki zauna da ni zama na har abada”

Ta masa kallon rashin fahimta, sai dai kuma ta kasa tambayarsa abun da yake nufi da haka. Ganin haka ya saka shi yin murmushi ya dauke hannunsa daga fuskarta ya dan ja baya kadan yana kallon harabar gidan.

“Kina son zama da ni?”

Ta sauke kanta k'asa ta kasa cewa komai. He just ask dan ya gane idan tana son zaman da shi ko akasin haka, domin Kaka tana kokarin hada aurensu ne kawai ba tare da lura da suna son junansu ba ko a'a, hadi ne kawai take son tai musu irin na kauye na zamanin baya.

“To ni ina son zama dake, shiyasa nake son Kaka ta bani ke...”

Sai kuma ya kasa karasawa yana ta kallon reaction dinta.

“Na aureki...”

Dagowa tai da sauri ta kalleshi gabanta ya buga da mugun karfi, zuciyarta tai wani uban zillo kamar zata fito daga kirjinta ta fado kasa.

Bata san miyasa take jin kamar kalamansa sun mata nauyi ba, alhalin ba a yau ya fara furta mata wannan kalmar cewar zai aureta ba, wacan karon ya ce saboda kar su sabawa Allah ne, har yace idan ta samu wanda take so ko yan'uwanta zai sake yanzu fa? Bayan gashi tana tare da kaka. Ganin ta yi shiru bata ce komai ba ya saka shi zaunawa cikin motar.

“Zan tafi”

Sai ta sake mika masa kudin a karo na biyu.

“Ki koma ki kai mata, idan bata karba ba ki dauka na baki”

Yaja motar ya rufe yai reverse tana tsaye tana kallonsa hawaye na sauko mata, sai da ya juya motar sannan ya sauke gilashin motar ya leko da kansa ya kalleta ya sakar mata murmushi sannan yaja motar ya kama hanya. Tsaye take tana kallonsa tun tana hangensa har ta daina hangosa, sai ta durkushe a gurin ta fashe da kuka ta saka kanta cikin guiwar hannunta tana kuka sosai. Sai da ta soma jin motsin mutane na wucewa sannan ta tashi ta share hawayenta ta shiga cikin gidan kanta a kasa tana tafiya kamar dazun.
Ko da ta shiga Kaka bata cikin dakin, sai kawai ta hau gadon data kwana a jiya ta rumgume kudin a kirjinta, can kuma ta juya baya ta fara kuka a hankali tana jin zuciyarta na mata mugun zafi.

TALBA POV.

Be taba rabuwa da wani abu ya ji yana marmarinsa ba so soon kamar Aminatu, baronta da yai a can har ya fara jin kewarta. Murmushi yai tunawa da tambayar da tai masa cewar yaushe zai dawo.
Wayarsa ya dauka ya kira Daddy, ringing daya ya daga.

“Ranka ya dade yanzu nake kokarin kiranka”

“Daddy barka da safiya”

“An tashi lafiya fatar ka kamo hanya”

“Gani a hanya Daddy, fatar Momy ta dawo”

“Kun fara damuna da zancen Momy fa, ni ma zan yi yaji na tafi Abuja na yi zamana”

Talba yayi murmushi cike da kaunar Daddy daman san shi da barkwanci.

“Haba Daddy idan ba Momy ai ba rayuwa, dan Allah kace min ta dawo”

“I think dai yau ko gobe zata dawo”

“Gani tafe, zan rakaka ka dauko ta akwai maganar da nake son yi da ku mai muhimmanci kuma ina fatar zaku fahimta”

“Allah ya kawo ka lafiya”

“Ameen”

Ya katse kiran, sannan ya kira Leila kamar yadda ya tsammata bata daga kiran ba, sai ya kira Amal ya gaisa da ita sannan ya kira Momy.

“Talba”

“Momy barka da safiya”

“An tashi lafiya”

“Lafiya kalau Alhamdulillah”

“Ance ka baka kwana a gida ba, ina kaje?”

“Waya fada miki?”

“Amal”

Yayi murmushi mai sauti.

“Allah ya shirya Amal ba zata daina gulma ba, naje kauye ne”

“Amman kasan hanyoyin nan ba su da kyau Talba”

“Nan ai da sauki abun be kawo ba, kuma gani hanyar dawowa, ina fatar kin dawo Momy”

Ta yi shiru.

“Rashinki ne ya saka muka bar gidan nan, gaba daya gidan baya mana dadi, kuma ina jin babu dadi idan na tuna cewar saboda ni komai ya faru”

“Zan dawo ai, kuma ba laifinka ba ne komai ya wuce”

“Zan zo anjima na daukeki”

“Aa sai next week”

“Momy do this favor for me dan Allah...!!!”

“Shikenan”

Yayi murmushi.

“Thank Youu Momy ashe kina so na”

“Wannan wace irin magana ce Talba? Bana son ka nake zaune tare da kai? Na taba cutar da kai a tsawon zaman da na yi da kai? Ta ya uwa zata zauna da tun yana jariri har ya girma a hannunta kuma ta ce bata taba son dan nan ba, bayan kuma yaron nan be mata komai ba? Engineer ya riga ya dasa maka wani mugun ice na kiyayata a zuciyarka shiyasa har kake min wani kallo na dabam”

“Ko kadan Momy, ban taba kallo wata mace a matsayin uwata ba sai ke, ban san wata uwa ba sai ke, kuma Daddy be shimfida min komai ba a zuciyata sai kaunarki, ke da shi kun kasa fahimtar juna ne kawai, kina ganin kamar ya zurfafa a so na, shi kuma yana ganin kamar baki so ni a yadda ya kamata ki so ni ba, kuma duka na fahimcinku, fatar za a yafe min”

“Baka yi komai ba, Allah ya maka albarka”

“Ameen”

Ya amsa da murmushi sannan ya kashe wayar, ya cigaba da tukinsa yana tunanin yadda zai gabatar da Daddy da Momy maganar Kaka.
Ko da goma tai har yayi wanka ya canja tufafi, be tarar da Daddy a gidan ba haka ma Amal tana makaranta Leila ce kawai a bangare sai Kabir dake karyawa a dinning.
Kallo daya Kabir yai masa ya dauke ido domin a yanzu be da makiyi kamar Talba, Leila kuma ta kura masa ido ta kasa daukewa har ya karaso kusa da ita ya zauna, sai gabanta ya buga da karfi, duk yadda take son hana zuciyarta soyayyar Talba sai ta kasa musamman ma idan yana kusa da ita wani lokacin har jin take kamar ta rumgume shi, sai dai gudun zubar da class dinta ya saka bata nuna masa haka, dauke idonta tai tana ganin wani uban kyau daya kara kamar an shafa masa hoda.

“Ya kike?”

Ta mike tsaye sai ya kalleta.

“Can we talk”

Tsayawa tai sai dai bata juyo ta kalleshi ba, kuma bata ce masa komai ba.

“Zauna mana”

Ta koma ta zauna.

“Akwai abun da kike so ne?”

Ya tambaya feeling some how kamar he's out of words, haka yake a duk lokacin da yake tare da Leila, duk kalmar da zai kama yai magana ta fahimta da ita sai ya ji kamar ba zai iya ba, except ta fada masa baka magana ne ko kuma ta masa wani laifi, on that point kam ya san abun da zai fada mata.

Mikewa tai tsaye ta nufi upstairs sai ya bita da kallo yana ta kokarin hada kalmomin da zai yi mata magana ta fahimta amman ya kasa har ta haye sama. Tashi yai ya nufi kofar fita Kabir ya bishi da wani banzan kallo har ya fice, bangarensa ya koma ya dauki keys dinsa ya fito ya shiga motarsa. Ko da ya isa gate har sun bude masa. Yana fita ya fisge motar da karfi ya dauki hanyar da zata kai shi gurin da Daddy yake aiki. A harabar ma'aikatar ya faka motarsa ya fito ya nufi ciki da saurinsa yana kiran Daddy a waya.

“Daddy gani shigowa zan muje mu dauko Momy yanzu”

“Bana gida”

“Yeah na sani office dinka nake nufi”

“Bana office, ina gidan Hajiya Yana, na yi marmarin abincin Doctor ne shi ne na zo na yi breakfast, amman idan na gama zamu dawo gida yanzu”

Talba ya tsaya cak yana mamakin yadda Daddy ya fishi hikima da wayo, wato a can ma ya karya a maimaikon ya jirashi su tafi tare, and yes yayi abun da ya dace, daman shi yana son saka Daddy a gaba ne saboda yana ganin kamar baya son dawowa da Momy ne.

“Fine sai kun iso”

Ya fada sannan ya juyo ya dawo yana murmushi ya nufo motarsa. A ranar be yi maganar da Daddy ba, duk da kasancewar Daddy ya tambaye shi amman sai ya dauko wani zancen, ba dan komai ba sai dan ganin a ranar Momy ta dawo be kamata yai maganar ba, washe gari ma be yi maganar ba, har sai da aka kwana uku da dawowar Momy a gidan. In all these three days yana kiran Kaka a waya idan ta daga ta ji muryarsa sai ta kashe, last kiran da yai mata ma ya bukaci ta bawa Aminatu wayar amman bata ko tsaya saurarensa ba ta kashe wayar.

Sai da Amal ta tafi makaranta Kabir ma ya fita Leila kuma ta koma dakinta, sannan ya kalli Momy ya ce.

“Momy ina son magana da ke da Daddy, ko zamu iya zuwa can?”

Momy ta kalleshi daman tun da suka zauna karin kumallon ta lura da babu abun da ya ci sai kofin tea yake ta juyawa.

“Miya faru?”

“Magana ce mai muhimmanci kuma ina son na yi ta ne tare da ke da Daddy”

“Okay gani zuwa”

Sai ya dauki tea din ya mike tsaye ya nufi kofar fita, Ta kofar gaba ya shiga bangaren Daddy a babban falonsa ya zauna yana shan tea a hankali. Sai ga Momy ta shigo ta kofar ciki,

“Baka shiga ciki ba?”

“I think yana karyawa”

“Let me talk to him”

Ta nufi hanyar karanin falon, sannan ta wuce bedroom dinsa. After like thirty minutes Daddy ya fito Momy tana bayansa, a karamin falo ya zauna sai Momy ta kira Talba.

“Talba...”

“Na'am”

Ya amsa sannan ya tashi ya nufi falon, a kasa ya zauna Momy kuma na zaune kusa da Daddy, dukansu sun tattara hankalinsu guri daya suna kallonsa musamman ma Daddy da ya fahimci akwai damuwa a tattare da dansa.

“Kana da wata matsala ne? Na ga ko breakfast ba ka yi ba”

Momy ta fada, sai Daddy ya cire gilashin idonsa.

“Mu'az akwai wata damuwa ne?”

Sai da ya hade yawun bakinsa sannan ya ce.

“Matsala ce kuma ba matsala ba”

“Wani abun ne?”

Momy ta sake tambaya. Sai Talba ya fere musu daga buri har wutsiya akan kudirin Kaka da kuma irin yadda ta dauki fushi da shi. Ba abun da kaka tai ne ya bawa Momy mamaki ba kamar jun cewar Aminatu yar'uwarsa ce, Daddy ya yunkuro yana kallonsa shi ma da mamaki.

“Wato baka rabu da yarinyar nan ba Talba? Har da daukarta ka kaita gurin Hajiya, da ba yar'uwarta ba ce acan zaka aje ta kenan?”

Cewar Momy cikin wani irin bakinciki na jin abun da Talba ya fada, sai Daddy ya daga mata hannu domin shi ba wannan ne damuwarsa ba.

“Taimako ai abu ne mai kyau, babu laifi a abun da Mu'az yai, ki tattara wannan abun ki aje gefe daya, ki bari mu ji da damuwarsa. Kai kana son yarinyar”

Daddy ya karasa yana kallonsa with serious face. Yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai ce.

“I don't know yet”

“That's mean baka son ta, and no one can forced you shikenan”

Daddy ya karasa masa domin yasan waye Talba idan yana son abu zai fito kai tsaye ne ya ce yana so, haka ma ida baya so zai fadi cewar baya so.

“Ya ma za'ayi ya so ta? Yarinyar ai bata dace da shi ba, imagine an yi raped dinta kasan iya mutanen da sukai mata wannan aika aikan? And waya sani ko tana dauke da wata cutar, lastly Talba ba mutum ne mai son hayaniya ba bana tunanin zai iya zama da mata biyu”

“Wannan ba matsala ba ce, da ace yana sonta za a iya bincikar lafiyarta kuma i will support him ya aureta, amman tun da baya son ta ba zai aureta ba”

Daddy ya fada, gaba daya sai jikin Talba ya mutu kalaman bakinsa suka kare, domin ya san duk juyin duniyar nan da za'ayi Daddy ba zai yarda ya aureta tun da har be nuna cewar yana sonta ba, and yes shi kansa be san yana sonta ba, all what he know is yana tausayinta.

“Amman... Kaka...”

Talba be karasa ba Daddy ya tari numfashinsa.

“Zan kirata zan yi magana da ita a waya, zan fahimtar da ita, yaushe rabon duniya da ayaraye, ai an daina wannan abu a wannan zamani, ko da ma ana yi ni ba zan bari ayi maka ba”

Daddy na kawai nan ya mike tsaye ya nufi bedroom dinsa, daga Talba har Momy binsa sukai da kallo sai da ya shige sannan Talba ya mike tsaye da zimmar tafiya sai Momy ta dakatar da shi ta hanyar tsayar kiran sunansa.

“Talba”

Mikewa tai tsaye ta karasawa gurinsa tana kallonsa fuska a hade.

“Karka kuskura ka bari Leila ta ji wannan maganar, domin akan 'ya'yana, bana da mutunci, bana da ragowa, bana son abun da zai daga musu hankali, idan ma ka fara son yarinyar nan ka bullo da maganar ta wannan hanyar to ka cireta a ranka tun wuri, kana gani ai, ni kadai nake a gidan mijina, haka ma yayana zasu zauna har karshen rayuwarsu, ko da wasa kar ka yi kuskuren hada soyayyar Leila da ta wata macen ko da ba wannan ba, balle kuma wannan kazamar da bandits suka gama wulakantawa, yarinyar da ingiyar aurena ta rabu saboda ita”

Kallonta kawai yake da mamaki, kamar ba ita ce ta gama fada masa cewar tana kaunarsa ba, and yanzu ya gane halin Momy tana sonsa but when it's comes to her children bata saurarawa kowa. She got lucky ita ce ta fada masa haka b Leila ba, da Leila ce zai iya fada mata bakar maganar da har ta mutu ba zata taba iya mantawa da ita ba, but Momy ce ya zai yi bayan ya saka mata ido. Har ta yi gaba sai kuma ta dawo ta sake kallonsa.

“And for the very last time karka sake shiga safgar yarinyar nan”

“Yar'uwata a yanzu, ko a da na taimake ta balle a yanzu da bata da kowa sai ni sai Kaka”

“I don't care, rayuwar kowa bata dame ni ba, ka haka rame ka binne maganar nan a inda aka yi ta, idan ba haka ba zan baka mugun mamaki Talba domin ba zan yarda a taba kimar yata ba...!!!”

A falon ta bar shi tsaye ta nufi babban falo cikin fushi ta karasa kofar fita falon wanda zata sadata da bangarenta, shi kam binta yai da kallo har ta shige ta turo kofar sannan ya fito babban falon ya zauna yana tunanin yadda zai fuskanci Kaka, anya zata fahimta kuwa? Idan ta fahimta falillahil hamdu, daman haka yake so, sai ya cigaba da daukar dawainiyar Aminatu, sai dai idan kuma bata fahimta ba fa? Ya zai yi? Ya shafa kansa yana sauke ajiyar zuciya.

Ya kusan awa daya a zaune, sannan ya tashi ya nufi bangarensa yana amsa wayar Ali, a tsanake ya labarta masa komai sannan ya nufi gadonsa ya kwanta ba dan yana jin bachi ba, sai dan ya rasa abun yi. Yana rufe ido wayarsa tai ringing sai ya kai hannu ya dauka ba tare daya bude idon ba, power button ya danna sai yai picking call din ya kara kunnensa.

“Na cilasta maka aurenta ne da zaka turo ubanta ya rufe ni da fada, yana kokarin nuna min cewar ina son yi maka auren dole ne? Lallai Mu'azu ka nuna min ban isa da kai ba, kuma yanzu na gane dalilinka na watsar da mu da kake, saboda mu talakawa ne ko? Toh na shata layi daga yau kowa ya tsaya matsayinsa, yarinyar da kake kyama har ubanka yana fada min akwai banbanci tsakaninka da ita gata can ana mata karin ruwa, idan ta mutu aikowa ya huta”

Sai a lokacin ya bude idonsa ya tashi zaune da sauri.

“Bata da lafiya ne Kaka? Zata iya magana?”

“Ban sani ba, na dai fada maka kar kaka sake turo min ubanka ya dame ni da wata maganar banza, idan abun da yake ganin yana bani ne yana daukar nauyina ban cilasta shi ba, kuma ba a yunwa ya gan ni ba”

“Kaka dan Allah ki kwantar da hankalinki, daman na yi magana da Daddy ne saboda ya fahimtar da ke, ban yi tsammanin abun zai kai ga haka ba, na yi alkawari zan aureta”

“Ba zan aura mata miji irinka ba, kaje can ka auri yar masu arziki, ai daman kishi yake taya yarsa, har yana nuna min cewar kuna da banbanci”

“Zan shigo garin Maradu yau ko gobe kuma Wallahi sai kin aura min ita”

Yana fadar haka ya ji ta mikawa wani wayar tana fadin.

“Karbi kashe min, waya sani ma ko zagina zai yi yanzu kuma, bayan ubansa ya gama nasa”

Dit... Ya ji ankashe wayar, sai ya mike tsaye ya fice daga dakin da zimmar zuwa bangaren Daddy, sai ya same shi waje direbansa ya bude masa mota yana

kokarin shiga. Sai dai hangoshi da Daddy yai ya saka ya dan jinkintar yana jiransa.

Ya karaso gaban Daddy a natse.

“Daddy aka yi magana da Kaka ne? Ta kira ni tana ta masifa”

“Na yi magana da ita, ina kokarin fahimtar da ita ta kasa fahimta, sai maganar take saboda anga ita talaka ce shiyasa nake mata haka, kuma wai ina taya yata kishi for god sake ya za'ayi na taya Leila kishi ni ba mace ba? Ba wai bana goyon bayan auren nan ba ne saboda Leila, Wallahi bana goyon bayan auren nan ne saboda baka so”

“Amman Daddy idan yin zai zama mafita why not...”

“No baka so ba za'ayi ba, that's it”

“Idan kuma ina so fa...”

“No baka saba yi min karya ba, ni kuma ban saba canja kalamaina ba, ba zan yarda kai abun da baka so ba, kuma ba zan bari ka yi abun da zaka zo kana nadamarsa ba, ba za'ayi auren ba karka sake yi min maganar nan”

Daddy na kaiwa nan ya shige motarsa, Direban ya zagayo ya rufe matsa sannan ya koma ya shiga driver side ya ja motar. Sai da Daddy ya fice daga gate din gaba daya sannan Talba ya koma bangarensa ya canja tufafin jikinsa ya dauki wallet dinsa da keys ya fito da sauri ya shiga motarsa sai da yai reverse sannan ya hango Momy dake tsaye a backyard tana kallonsa fuska a hade, dauke kai yai yaja motar yana danna horn da karfi kamar mai tsere. Sai da yai nisa da unguwar sannan ya kira Ali ya fada masa abun da ya faru.

“Yanzu miye abun yi?”

“Oho ni yanzu hankalina ma ya koma can gaba daya, saboda Kaka tace min gata nan ana mata karin ruwa waya sani ma ko wanda ke mata karin ruwan be wani kware ba, kuma wata kila ba a bincika ciwonta ba”
“If ka damu da ita da lafiyarta Talba, be kamata ka nunawa Daddy baka son aurenta ba, kasan Daddy ya fika son abun da kake so, kuma yafi ka tsanar abun da kake ki, yanzu ya zaka yi kenan?”

Talba yayi jimmm sai kuma ya sauke ajiyar zuciya.

“Aurenta zan yi, ba zan yarda zumuncin dake tsakanina da Kaka ya lalace ba akan abun da ina da iko da shi ba, kuma ba zan yarda Daddy ya samu matsala da Kaka ba”

“Then ya zaka yi convinced din Daddy ya yarda ka aurenta? Kasan ba zai taba yarda ba, aje maganar Daddy a gefe ma, ya zaka yi da Momy da Leila?”

“AUREN SIRRI no one would know, har sai komai ya daidaita, and i think Aminatu deserved a better life zan dawo da ita gidan nan”

Ali yayi saurin mikewa tsaye daga zaunen da yake yana girgiza kai.

“No karka yi haka Talba, zaka cutar da kanka kuma yarinyar zata cutu”

“Sai dai ni na cutar da kaina, amman ba zan bari a cutar da Aminatu ba, kuma ba zan cutar da ita ba”

“Maimakon haka, ai kara ka samo wani dabam ka aura masa Aminatu a matsayinta, saboda ba lallai ne ma idan a aureta ka iya zaman aure da ita yadda ya kamata ba”

Talba yayi murmushi yana tuna kalaman Momy na dazun.

“Saboda me? Saboda wasu mazan sun wulakantata? Ali bari na tambaye ka, idan kanwarka zaka so wani aureta? Ita ta kaddarowa kanta wannan abun ya faru da ita? Miyasa ake kyara mutanen da irin wannan kaddarar ta fada musu? Wallahi wannan abun ya fara min tausayinta kuma ya karfafa min guiwar aurenta, saboda ta cancanci zama da namiji irina, bayan ni a yanzu ban san wanda zai aureta ya zauna da ita da zuciya daya ba, and ba zan iya yaudarar Kaka tana kallon ni na aureta sai kuma na saka wani yayi? Ita kanta Aminatu ba zata ji dadi ba, and idan hawayen yarinyar ya zuba saboda ni ba zan taba yafewa kaina ba”

Ali yayi murmushi.

“Na taba fada maka lokaci zai da idonka zai rufe ka taka kaya ka jita kamar lad'a, kana son yarinyar nan believe me, zaka iya yaudarar Daddy da Momy da Leila amman ba zaka iya yaudararta ba, and you are telling me idan hawayenta ya zuba saboda kai ba zaka yafewa kanka ba... This is Love Talba, Welcome To the club”

Talba ya natsu yana nazarin abun da ya fadawa Ali, did he said something wrong? No gaskiya ya fada masa ai abun da ke ransa. A hankali ya sauke wayar ya cigaba da tukin yana tunanin halin da Aminatu take ciki.

LEILA POV.

Tana fitowa daga dakin ta shiga dakin Momy, bata same ta a ciki ba, sai ta sauko kasa ta shiga kitchen nan ma bata ciki.

“Ke Mairo ina Momy”

Ta tambaya tana wani yatsinar fuska kamar wanda tai arba da kashi.

“Tana sama”

Mairo ta amsa mata ba tare da ta kalleta ba.

“Wai Mairo har wani ji kike da kanki a gidan nan, Wallahi idan baki yi hankali ba sai na karya ki, ba ki san halina ba ne”

Kallonta kawai Mairo ta yi ta dauke kai ta cigaba da abun da take, ita kuma ta juyo ta fito daga Kitchen, kai tsaye ta nufi upstairs kamin ta karasa Momy ta sauko rike da atamfa.

“Momy ina kika shiga ban ganki ba”

“Ina backyard”

“Gurin me?”

Leila ta tambaya da mamaki domin ba kasafai take shiga can ba.

“Gurin kallon Talba, ashe har yanzu yarinyar nan tana ransa?”

“Me yace ne?”

“Ba komai kawai na lura da yanayinsa ne”

“Yauwa Momy daman ina son na yi miki magana akanta, ki bincikar mana shi inda ya kaita dan Allah ko ma ki saka ya dawo da ita gidan nan if possible”

“Saboda me?”

“Madina ta ba ni shawarar mu samu wani mu biya shi ya aureta, kin ga ai mun huta, to na yi da bugun cikin Ali be fada min komai ba, sai ma ya nuna min kamar be san inda Talba ya kai yarinyar ba”

Momy ta yi shiru tana nazari.

“Indai haka ne, Madina ta kawo shawara mai kyau, amman akwai wani sirri da baki sani ba”

“Minene?”

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

AMINATU POV.

Tana jin muryar Talba sai ta bude ido da sauri, domin tabbatarwa idan kunnuwanta daidai suka jiyo mata, tsaye ta ganshi a kanta yana ta kallon kyakkyawar fuskarta cikin damuwa. A take ta zabura ta tashi zaune.

“Ina wuni”

Sai ya zauna kusa da ita yana kallonta cike da kulawa.

“Ya jikin?”

“Alhamdulillah”

Ta fada tana jin kamar an yaye mata ciwon an aje gefe daya. Hannunsa ya kai ya taba wuyanta sai ya ji shi da dan sauran zafi. A nan ya kalli Kaka.

“Wane irin magani aka bata?”

“Wanda ka kawo mata”

Kaka ta fada masa tana wani tsuke baki, ta dauke kai kamar wata yar yarinya wai ita ala dole fushi take da shi.

“Haba Kaka”

Sai kuma ya kalli Aminatu.

“Shalele wani irin magani aka baki?”

“Mai dacin nan na malaria da na ciwon kai, sai kuma ya saka min ruwa, kuma ta min allura”

Ta fada a shagwabe idonta na cika da kwalla ji take kamar ta fashe masa da kuka tunawa da zafin allurar da akai mata gashi kullum yake mata safe da yamma.

“Kin gani ko? Ba ma wani kwararen ba ne, taya zaka baka maganin malaria da allura a lokaci daya, kuma ba a tsaya an auna mutum ba? Maybe ma hawan jini ne tun...”

Kamin ya karasa Kaka ta daka matsa tsawa.

“Can can ga kanka, sai dai idan kai ka shafa mata hawan jinin, dan dai ina da shi ne shine kake son murdowa ta nan kace ni na saka mata? Daman tun da ka tafi take ciwo tana kuka na kira dan Asabe ya dubata yace malaria ce”

“Ba a auna mutun ba za a gano ciwonsa? Ni ban ce kin laka mata ba, daman ya za'ai wani ya saka ma wani hawan jini?”

“Wai idan ma manufar ka kenan ai na san ba so na kake ba”

Da gaske take maganar, a kokarin juya maganar zuwa wasa yai dariya ya amsa mata da.

“Me zan yi da tsohuwa ga sabon jini na samu”

Ya fada yana kallon Aminatu. Kaka ma kallonsa take.

“Ko Shalele?”

Aminatu ta yi kasa da kanta gabanta n bugawa da karfi. Sai yai murmushi

“Kin ci abinci?”

“Bata ci abincin ba ai gidan yan yunwa ka kawo ta ko?”

Kaka ta amsa masa a fusace. Be kula ta ba ya cigaba da kallon Aminatu.

“Bari na fita na bincika idan akwai inda ake siyar da abinci mai kyau sai na siyo miki, hankalina ya dauku shiyasa ban tsaya a hanya na siyo miki komai ba”

Magana yake mata a hankali kamar mai kokarin fahimtar da ita. Sai ta daga masa kai a hankali tana kai hannu ta share kwalla da suka tarar mata.

“Good Girl”

Ya mike tsaye sai ta bishi da kallo har ya fice, Kaka kuma ta bita da kallo mamaki zuciyarta na raya mata wani abun.

“Ke Auta...”

Aminatu ta kalli Kaka da sauri, sai Kaka ta matsa kusa da gadon da take zaune.

“Fada min lokacin da kuna can, yana miki wani abu?”

Aminatu ta yi shiru domin bata fahimci inda Kaka ta dosa ba.

“Yana tabaki ko ya rike hannunki ko ya dan shafa ki”

Aminatu ta yi shiru tana tunanin irin amsar da zata bawa Kaka.

“Karki ji tsoro ko kunya, kin ganshi nan jikana ne, duk yafi soyuwa a raina amman wacan kanen uban nasa da tsinanniyar matarsa da bata nuna masa son yan'uwan uwarsa ba, sun canja shi sun maida shi wani kala, ba san manufarsa a yanzu, na lura sai son shige miki yake kuma bayan ya nuna min shi ba zai aureki ba, har yana wani kiranki Shalele, wannan sunan yan iska ne, karki yarda ya sake ce miki haka kinji ko?”

Aminatu ta daga mata kai, alamar eh sannan tai kasa da kanta tana tauna maganar Kaka ba cewar yace ba zai aureta ba, wa yai masa tayin auren tun farko? Amman miyasa zai aurenta bayan ita da shi akwai banbanci da tazara mai girma?

‘A'uzubillahi’

Ta fada a ranta tare da lumshe ido tana jin kamar ta yi banban sabo saboda zuciyarta na kusanto mata da aurenta da mutumen da ko a mafarki yafi karfinta. Taya mutum mai daraja da tarin dukiya da kyau da iyali kamar Talba zai yarda ya hada jini da irinta? Amman miye manufarsa ta yi mata furucin da yai mata a lokacin da zai tafi? Ta daga idonta ta kalli Kaka.

“Tsohuwa ke kika ce masa ya aure?”

“Eh, saboda ki samu rayuwa mai kyau, kuma kin ga dan'uwanki ne zai rike ki da amana, sannan ni bana son yarinyar can da zai aura, uwarta sau biyu kawai ta taba zuwa garin nan, ita yarinyar ma ban santa ba, amman suka zaba masa ita saboda sun ga yana da dukiya, sai juya shi suke kamar waina, ni bana son ya aureta ma, kara ya auri yar'uwarsa idan ma a nan zai aje ki ai kin ga dole ya rika zuwa yana duba ki mu ma muna ganinsa, kuma sai na nunawa wannan bakar matar ni ma na isa da shi, amman sai ya juya min baya harbda turo wannan uban nasa a waya yana fada min kabli da ba-adi da shika shikan kin aurenki”

“Yana da wanda zai aura Kaka, kuma ba ki ga zubinsa ba? Akwai banbanci rayuwata da dasa, ni fa a kauye na tashi, sannan na rasa abubuwa da yawa da be zama lallai ma wani namijin ya so ni ba, balle kuma shi”

“Ai ba wannan za a duba ba, hadin gida da zumunci ba ruwansa da wannan dan haka ki daina ma duba wannan”

Kaka ta karasa tana mikewa tsaye ta gyara daurin zanenta.

“Bari na yi fitsari”

Aminatu ta yi kasa da kanta idonta na cika da hawaye. Kaka na shiga bandakin Talba yai sallama ya shigo, Aminatu ta kasa amsawa kuma ta kasa dago kai ta kalleshi, har ya zauna kusa da ita ya kai hannunsa ya dago kansa sai yai arba da hawayenta.

“Kaka ta miki wani abu?”

Ta girgiza masa kai alamar no.

“Toh miya faru ko kina jin ciwon ne?”

Wannan karon ta samu damar amsawa.

“Aa”

Sai ya saka hannunss biyu ya share mata hawayenta.

“Idan ina kusa da ke, hawaye basa da muhallin a fuskarki, ki daina kuka kin ji Shalele?”

“Ka daina ce min haka dan Allah”

Ya daga kansa sama yayi murmushi ya sauke.

“Idan Kaka ta zo ki fada mata ba zan daina ba”

Ya fada domin ya san ita ta kitsa mata wannan maganar, domin bata taba masa korafin kiran da yake da Shalele ba sai a yau.

“Na bawa wani ya siyo miki abinci mai kyau, yanzu fada min Kaka ta miki gulma ta?”

Ta yi shiru kanta a kasa.

“Kaka tana fushi da ni, saboda na ce ta aura min ke taki”

“Aa ba sai ka boye min ba, ni bana son aure a yanzu kuma na san akwai banbanci a tsakanina da kai...”

Bata karasa ba ya kai hannunsa ya rufe mata baki.

“Wallahi ban taba ganin wannan banbanci ba, kawai abun da nake tunani yadda zamu fuskanci juna ni da ke, kuma yanzu wannan zuwan da na yi ba zan tafi ba sai da igiyar aurenki”

Ta sakar masa ido sai kuma ta matsa baya kamar mai tsoronsa.

“Kana da wanda zaka aura, Yallabai ka rufa min asiri bana son na sake shiga wata matsalar idan ma Kaka tana fushi da kai ne saboda ka ce ba zaka aure ni ba, na fahimta”

Yayi Murmushi ya kalli wani gefen sannan ya sake kallonta.

“Yan mata, idan ma kin yi karya zuciya bata iya karya ba, na riga na karance ki kina kokarin hana zuciyarki abun da take so ne, a miyasa kika rika tambayar yaushe zan dawo a lokacin da zan tafi?”

“Saboda na sabu da kai ne kawai na kwana biyu”

“Miyasa a lokacin dana tafi kika kwanta ciwo sai a yanzu dana dawo kika samu lafiya?”

Ta yi shiru.

“Kin san saboda me?”

Ta girgiza kai.

“Saboda na tafi da zuciyarki, a yanzu kuma da na dawo na dawo miki da ita, karki yarda zuciyarki ta raya miki banbanci tsakaninki da wata ko wani, karki yarda ki sake nisa da mutanen da suke da muhimmanci a rayuwarki, domin zuciyarki ba zata iya daukar wani ciwon ba”

Har lokacin kanta a kasa yake tana hawaye, shi kuma yana kallonta yana jin kamar ace yana da permission din rumgumarta ya rarrasheta. Kamar daga sama suka ji muryar kaka tana jan tsaki.

“Maye ne kai da ka tafi da zuciyata, ka ji wata maganar banza idan son ta kake da gaske ai aurenta zaka yi”

Runtse ido Talba yai ya bude ya kalli Kaka da be san tana cikin bandakin ba har sai da ta fito.

“Kaka labe kike mana ne?”

“Ina ce dai Dakina ne? Kuma ina jinka dazun kana min karya wai na hana ka Auta, ai ban mutu ba da rai na”

“Dakinki ne, amman ni ma ina da hakki da shi ko? Kuma ai ban fadi karya ba na fada miki a waya zan zo kika ce ba zaki ba ni ba, kin dauka wasa nake? Wallahi Kaka ba zan bar garin nan ba sai na auri Aminatu”

A take Kaka ta washe hakora, gaban Aminatu kuma yai dukan uku uku.

“Aa dan Allah dan Annabi Aa”

Aminatu ta fada cikin kuka, sai Kaka ta watsa mata harara.

“Ke Wallahi baki isa ba ke ma, idan ba haka ba ni da ke ne, wannan abun farinciki da jindadi haka zaki ce wani aa, Mu'azu da gaske kake yi?”

“Wallahi da gaske nake yi kaka, amman dan Allah karki cilasta mata ki barni zan yi magana da ita”

“Mu can da aka mana aure, zabi aka bamu ne? Ko mazan ma ba mu sani ba sai da aka daura auren, karka biye shashancinta yarinya ce karama bata da wayo”

Talba yayi murmushi yana kallon Aminatu dake hawaye. Kamin ya kalli kofar shigowa dakin Kaka na amsa sallamar Aminu baki har kunnen.

“Aminu”

“Na'am Tsohuwa ya jikin?”

“Aa ni ai na warke, abun farinciki ya samu kuma ai”

Har Aminu yayi kamar ya tambaya minene domin ya lura Kaka tana son labarta masa sai kuma wata zuciyar ta hana shi, sai ya karasa gaban Talba ya aje masa kular abinci da ledar lemu ya mika masa canji.

“No ka rike carjin”

“To na gode Allah ya kara sutura”

Aminu na fita Kaka ta bi bayansa domin labarta masa, abun da ya kasa boyuwa a ruhinta. Sai da suka fice sannan Talba ya kai hannu ya bude cooler kamshin ferfesun kayan ciki ya daki hancin Aminatu.

“Sauko ki ci”

“Aa”

Ta fada da muryar kuka, domin kukan ne ya zo mata da gasken gaske. Kallonta yai.

“Shalele? Kar dai ki ce min baki son auren nan?”

Ta daga masa kai.

“No please, kar mu yi haka da ke, ba wai zan aureki saboda Kaka ne kawai ba, zan aureki ne saboda na faranta miki rai, ina tunanin zaki so abun da zai faranta min rai kuma ya shirya tsakanina da yan'uwana, idan har ban aureki ba ina cikin matsala ba yar karama ba...”

From a to z ya zayyana mata komai ciki har da kudirinsa na boye auren na su na wani lokaci. A nan ne hankalinta ya kara tashi.

“Ina jin tsoron abun da rayuwa zata samar min a gaba, komai nawa ya banbanta dana kowa, rayuwata ta zama ba tawa ba, duhu ne ya fara bayyana a ciki, sai iska ya mamaye komai, kamin na ankara taurarin ciki sun tarwatse! Hakan ne silar rushewar duniyata... Talba ba ni da gata, ni fa yar gudun hijira ce kawai...! Ina jin tsoro abun da zai faru”

Ta share hawayenta. Yayi saurin kama hannayenta, a cikin yanayin da ke nuna tsantsan tausayinta, fararen idanuwansa masu kamar madara suka rine da ja tsabar bacin rai da bakinciki.

“Ashe ba ina kusa da ke ba? Ki daina tunani wannan tunanin Shalele da yarda Allah sai na mai da ke yar lele”

“Taya? Kana da wanda zaka aura, kana da rayuwarka da mafarkinka, miyasa zaka rusa komai? Baka tsoron halin da zan shiga? Abun da iyaye basa so akwai hadari a yinsa”

“Ki daina damuwa da iyayena ko Leila, ni mijin mace hudu ne, ba san ba zaki yarda alakar dake tsakanina da Kaka ta lalace ba akan abun da zaka iya yi min, zan sama miki wata rayuwar mai kyau mai inganci, zamu gina wata duniyar mai ciki da daula da jindadi mai cike da zuri'a”

Ta fisge hannayenta hawaye na ta zirya a fuskarta, mikewa tai tsaye tana masa kallon tsoro.

“Ta ya kake tunanin rayuwa zata zama mai sauki a gareni? Ya kake tunanin Leila zata ji idan ta san ka aure ni? Miyasa kake tunanin samun wasu Family a gareni mai sauki ne? Bayan na rasa kowa? Taya mace irina wanda ta rasa komai na kima da mutuncin mace farinciki zai rabeta, ta ya Yallabai...!”

Mikewa yai tsaye yana kallon cikin idonta.

“Kar bakinki ya sake furta irin kalamin nan, ina gargade ki a kan furucin... Ina son na roki ki wannan alfarmar Aminatu, dan Allah ki yarda ki aureni ba dan saboda kanki ba ko Kaka, saboda ni”

Ta runtse ido hawaye na sauko mata, a take ta ji zazzabin ya dawo mata sabo.

“Na san akwai wahala amman ki daure dan Allah”

Ta bude idon ta kalleshi sai kuma ta sake rufewa sakamakon jirin data ji yana dibanta.

“Ina son zan kwanta”

Ta fara lalaben gadon tana kokarin kwantawa idonta a rufe.

“Wannan maganar zata zama a tsakaninmu, bana son Kaka ta san cewa a boye zamu yi wannan aure”

Nan ma bata ce masa komai ba har ta zauna.

“Ki ci abinci sannan ki kwanta”

“Bana jin yunwa”

“Ba zan cilastaki ba, bana son na saka ki a cikin abun da zai haifar miki da damuwa, zan yi magana da Kaka”

Bata ce masa komai ba har ya fice daga dakin. Ta inda yake jiyo muryar Kaka ya nufi sai ya tsaya daga bakin kofar dakin yana sallama.

“Shigo Mana Mu'azu”

Kaka ta fada da far'arta, sai ya cire talkamin kafarsa ya shiga dakin ya zauna kusa da Kaka yana kallon matar kawon nasa dake da far'ar da alama ita ma abun ya mata dadi.

“Mu'azu yanzu nake jin abun alheri Allah ya tabbatar ya sanya alheri”

“Amin na gode”

Kaka ta kalleshi tana fadin.

“Salamatu ce ta zo da wata magana wai idan Alhaji ya ji zai iya hanawa, ko kuma ya cilasta sai ka sake ta”

“Kaka kar wannan na dame ki, da saninsa na zo nan, kawai dai yace babu ruwansa saboda na dage sai na yi auren, shiyasa nake son kamin ya canja shawara a daura mana aure da ita inya so idan tarewa ne sai a barshi har sai komai ya kamalla”

“Amman Mu'azu hakan ba zai haifar muku da matsala ba? Baka ganin hakan zai iya sakawa su can su tsane ta?”

Cewar Salamatu tana kallonsa.

“Idan ma sun tsane ta, ni dai ina son ta kuma ba zan tana yarda a cutar da ita ba ko kuma ni da kaina na cutar da ita, a kokarin sama mata wasu iyalin na kawo ta nan, a can ma abubuwa da yawa marasa dadi sun faru saboda ni da ita, ina tunanin ko da a mafarki aka ce muku zan cutar da ita ko kuma na yarda a cutar da ita ba zaku yarda”

“Wallahi ko kadan, ban kawowa raina Cewar zaka cutar da ita ba, ai babu wanda ya dace ta aura sama da kai, kai da kasan komai nata kuma kake tausayinta, kawai dai ina ji maka tsoron abun da zai faru ne a gaba, kasan za su iya fushi da kai”

Salamatu ta sake fada tana kallon Kaka dake jinjina kai.

“Wannan kuma ai mai sauki ne, komai zai wuce Inshallahu, ni dai yanzu ina son ku amince min ayi komai tsakanin yau zuwa gobe amman da idan har ta amince domin bana son na cilastata”

Kaka ta dafa shi.

“Karka damu ita fa bata san so ba, kuma ta sabawa kanta da kuka tun da ka tafi kullum kuka take sai ciwo, bata da wayo amman an mata auren zata yi hankali”

Yayi shiru ya sauke kansa kasa can kuma yaja numfashi a hankali ya sauke.

“Na yi magana da Kawo Hasan kuma ya nuna min cewar ba wata matsala, amman duk da haka ina son yi sake yin magana da shi, sai a yanka min sadaki

kuma idan son samu ne a daura auren nan yau ko gobe kamin Daddy ya canja shawara”.

“Ka yi gaskiya saboda bakar matar nan ma zata iya kitsa masa wani yace ya canja shawara ba zaka aureta ba, kuma dan be saka hannunsa ba, sai me ai mu masu yi maka komai ne, ba mu hana ka auri yarsa ba karawa kawai aka ce kai amman sai taya yarsa kishi yake, wannan abun da kai ni ka yi wa Allah ya maka albarka”

“Ameen”

Ya amsa sannan ya mike tsaye ya saka hannayensa aljihu.

“Idan kun yi magana da su, sai ki sanar min domin ina son komawa yau, idan kuma hakan be samu ba, zan jira har sai zuwa gobe idan an daura auren”

“To bari na nemo shi yanzu”

Kaka ta fada sai ya sa kai ya fice ya bar Kaka da Salamatu kadai a dakin. Salamtu ta kalli sarakuwarta cikin yanayi na damuwa ta ce.

“Inna baki ganin hakan zai iya haifa da matsala? Allah ya ma ba aurenta zai yi ya tafi ya barta ba sai an gansa”

“Aiko da sun ci ubansu, daga shi har uban nasa, be ma isa ba, idan zai tafi kafarta kafarsa haka zai tafi da ita, idan ma wayonsa kenan ba zan yarda ya barta ba”

“Toh sai dai haka nan, kam idan ba haka ba zai iya mana wani wayon kin san halin yaran nn na zamani, amman kam da ta yi miji yaro barakalla da shi gwanin kyau”

Kaka ta tashi zuwa neman danta Hassan. A lokacin da Talba ya fita daga dakin Salamatu sai ya koma dakin Kaka, daga bakin kofa ya tsaya yana kallon Aminatu dake kwance rairai idonta a rufe, sai dai jin kamshin turarensa yasa ta shakar kamshi bada ta san yan tsaye bakin kofar ba, idan yaja numfashin da karfi sai ta sauke a hankali.

“Kina son turarena amman baki son kusanci da ni”

Ta bude idon ta sauri ta juyo ta kalli gurin kofar sai ta ganshi a tsaye, wani irin kwarjini da haifa ya kara a idonta. Idan har tace bata son Talba to ta yaudari kanta kuma ta yi karya, amman tana sonsa? Anya akwai son sa a zuciyar dake cike da damuwa da bakinciki? Anya ma ta gama karantar minene son? Ko kuwa dai sabo ne irin wanda ta ji a wacan lokacin da tafi ya barta, a yanzu ma idan bata amince ba zata sake ganinsa ko kuwa zai tafi ne har a bada ba zai dawo ba?

“Tashi ki ci abinci idan ba haka ba zan kira wannan mutun ya zo yai miki allura”

Daga inda yake tsaye ya fada, sai ta tashi zaune tana turo baki tana masa wani kallo dake nuna alamar kiris ya rage ta fashe masa da kuka. Sai yai murmushi ya saka kafarsa cikin dakin ba tare da ya cire talkaminsa ba.

“Idan kika aminta kika zauna da ni, zamu rika ganin juna kullum, amman idan kika ki ni wata kila ba zaki sake ganina ba Aminatu, amman na san ba zaki bawa Kaka kunya ba ko?”

Ta yi shiru sai kuma ta fashe masa da kukan da bata san na minene ba. Cooler ya dauka ya sake budewa ya saka hannunsa ya rika dauko farfesun ya kai mata a baki.

“Bude baki”

Ta bude bakin daker tana ta kukan shagwaba. Sai ya kai mata a bakin yana kallon kyakkyawan lips dinta.

“Pretty girl”

Ya furta yana hade yawu, even though be taba kissing lips din wata mace ba, he like her pink lips, dan karamin bakinta nan ya dauki hankalinsa sosai da yadda take tauna abinci a hankali kamar ya mata dole. Da hannunsa yake bata har sai da wayarsa tai ringing sannan ya saka hannunsa na hagu ya karba kiran kawo Hassan sannan ya mike tsaye yana fadin.

“Okay gani zuwa”

Be ce mata komai ba ya fice daga dakin, a harabar gidan ya kunna bohore ya wanke hannunsa sannan ya nufi dakin wajen, ba Kawo Hassan Kawai ya samu a gurin ba har da wane kanen Hassan din wanda shi na kawo ne a gareshi da kuma Kaka, kusan abun da suka tattauna a dakin Salamatu shine suka sake tattauna da Uncles din nasa, sai da ya tabbatar musu da babu wata matsala sannan suka amince akan gobe idan an sauke Sallah azahar za a daura masa aure da Aminatu a Masallacin kofar gidan. Kawu Hassan sai nuna bacin ransa yake akan abun da Daddy yai yana ganin kamar ya wulakanta kuma ya nuna shi kadai yake da iko da Talba, be jidadin da za a yi komai ba tare da shi ba, amman be tsammaci haka daga gareshi ba, sai dai dukansu sun raja'ah ne aka ce maganar Kaka cewar saboda ya maida su talakawa ne shi kuma yan ganin shi mai arziki ne.
A garin Talba ya wuni har dare, sai guraren tara da rabi Daddy ya kirashi Saboda Momy ta fada masa Talba baya gidan, sai da ya fita waje can nesa da gidan sannan ya amsa kiran Daddy, ya fada masa cewar yana gurin Kaka.

“Amman kasan yanayin kasar nan ki? Musamman kauye idan sun ga bakuwar fuska har hada kai ake azo a dauke mutum, sannan taya zaka yi tafiya baka fada min ba?”

“Saboda zaka iya hanani da wannan hujojin naka daka zayyano a yanzu, ni kuma ina bukatar zuwa saboda na yi magana da Kaka ka san tana cikin fushin a yanzu”

“Na ji ka dawo da wuri, Allah ya tsare, kuma ka yi addu'a sosai Wallahi ina tsoron garin nan”

“Inshallahu Daddy babu abun da zai faru”

“Toh Allah dai ya tsare, amman ka daina wasa da rayuwarka irin haka”

“Inshallahu”

Daga haka sukai sallama sannan ya kira Momy ita ma ya sanar mata inda yake ya kuma fada mata ba zai samu dawowa ba sai gobe.

“Allah yasa dai ba gurin yarinyar nan ka tafi ba”

Momy ta fada cike da gadara.

“Momy kina manta cewar akwai zumunci a tsakanina da ita a yanzu, ko bayan ita kuma Kaka ta tana nan kuma tana raye dole ne na rika zuwa”

“Hmmm Talba kenan, a hannuna ka tashi karka ce zaka min wayo, ni dai n gargadeka, kuma na ja maka kunne ka fita sabgar yarinyar nan tun wuri indai har ka dauke ni uwa, ina tunanin zaka ji magana ta”

Ya sauke ajiyar zuciya ba tare da yace komai ba, Momy ma bata sake cewa komai ba ta kashe wayar, sai ya koma cikin gidan ya ari wayar Kaka da sunan zai duba wata number yai blocking din number Daddy a wayar Kaka sannan ya goge number gaba daya, gudun kar Kaka tai karabanin cewa zata kira shi.
Bayan ya gama abun da zai yi ya mika mata wayarta ya fita, Kawu Hassan ya shigo dakin Kaka ya saka Aminatu a gaba yana tambayar idan tana son Talba, sai dai Kaka bata bata damar amsawa da eh ko aa ba, duk inda Kawu Hassan yai sai a tare, tana cewa wai Aminatu bata da wayo bata san ciwon kanta ba, kuma ba san minene so ba. Ita kanta Aminatu da za a bata dama da bata san wace kalar amsa zata bawa Kawu Hassan ba, domin kanta a yanzu a duhu yake.
Daga ita har Talba bachinsu kadan ne, misalin biyu da rabi ta tashi ta shiga bandakin Kaka tai alwala ta fara raya daren na Laraba tana kaiwa Allah kukanta da neman zaba mata abun da zai zame mata alheri da kuma rokin daukinsa a dukan al'amurranta, ta bangaren Talba ma sallah nafila ya kwana yi, a da can sai dai yai raka'a biyu yai karatu da addua ta kwanta sai dai wannan karon har asuba yana zaune a saman carpet din da yai sallah yana karatun qur'ane, bayan ya kamalla ya fadawa Allah bukatarsa da neman daukinsa a abun da yake kokarin aikatawa.
Washe gari abun kari na musamman Kaka ta saka aka shirya masa, aka kawo masa har dakinsa, ruwan tea kawai ya sha ya kasa cin komai, sai abubuwan da suka faru a jiya suka rika dawo masa, ya sani akwai kalubale mai yawa a gabansa, sai dai yayi ma kansa alkawarin duk rintsi duk tsanana ba zai taba yarda ya cutar da Aminatu da saninsa ba.
Misalin Tara da yan mintuna Kawu Hassan ya same shi da maganar Sadakin da kuma wanda zai masa walicci domin shi zai dauki bangaren Aminatu ne.

“Na saka dubu ashiri Hajiya tace yayi kadan zai dai a saka arba'in”

“Ba matsala Kawu zan bada 100k, Inshallahu”

Kawu yayi murmushi yana mamaki.

“100k fa kace Mu'azu, aa yayi yawa”

“No be yi yawa ba, ita kanta Aminatun ina son ta ji cewar na dauke ta da kima”

“Duk da haka dai dubu dari yayi yawa”

“Be yi yawa ba Kawu, Allah dai ya tabbatar mana da alheri”

“To amin”

Talba ba mutum ne mai yawo da kudi mai yawa ba, haka ya saka dole sai da ya je POS ya cire wasu kudin sadakin ya bawa Kawu da kuma kudin da za a siye komai na al'ada na daurin auren. Bayan ya dawo ne ya kira Ali ya fada masa komai, at first Ali dariya ya fara masa kamin ya biyo da addu'a sannan ya tabbatar masa cewar da shi za a daura auren nan.
Haka kuwa akai, kamin lokacin daurin auren ya iso garin tare da sabuwar shaddda mai masifar kyau da tsada sai kyalli take kana ganinta kasan ta ci kudi, fara ce sol zagenta ya fito kwar gwanin sha'awa, not just shadda hula da Talkamin da Ali ya siyo masa ma abun kallo ne.

Misalin karfe biyu da yan mintuna aka daura aurensa da Aminatu, ba zai iya cewa happy marriage ba ne, and it's not the sad one, sai dai ya samu kasa da farinciki marar misaltuwa, wani irin annashuwa da natsuwa suka saukar masa, fuskarsa sai haiba take kana ganinsa ka ga ango. Ko kadan fuskarsa ko dabi'arsa da mu'amalarsa bata nuna cewar baya son auren ba, domin shi kansa yana jin matsayinsa da kwarjininsa su karu.

BATURIYA POV.

Kamar yadda tai masa alkawari, a ranar ta same shi a gidansa na hutawa, suka aikata masha'arsu kamar wacan lokacin. Sai dai wannan karon bata yarda ta kai dare ba saboda tana son zuwa asibiti ganin likita kamar yadda ta fada a gida da karyar zuwa asibiti ta samu fitowa.
Wannan karon a account ya saka mata 450k a maimakon ya bata a hannu, saboda ta fada masa bata son kudin a hannu. Yadda yake santi yana yabonta har yafi na wacan karon, sai wani narke mata yake a jiki kamar zai shige ciki, daker ta kwanci kanta domin a ra'ayinsa ya so ta kwana a gidan ne, sai ta nuna masa tana a karkashin iyayenta ne za su iya zarginta idan ta kwana, sai dai bata yarda ta nuna masa cewar tana da aure ba, sai ma karyar da tai masa cewar mijinta ya rasu ya barta da yaro daya.

Misalin hudu da kwata ta fito daga gidansa, sai da ta shiga Napep sannan ta kira Ramlee ta sanar mata cewar yanzu ta fito daga gida, domin bada sanin Ramlee ta hadu da shi ba, kuma ta san idan har taji sun hadu ta bayan fage zata iya zargin Baturiya.

“To ki tsaya ta sokoto Road, zan zo a dauke ki”

“Okay toh amman karki dade dan Allah”

“Okay”

Baturiya ta sauke wayar tare da shafa cikinta tana jin irin abun da take ji a duk lokacin da tai yunkurin zubar da cikin, sai dai bata da mafitar data wuce wannan, domin idan bata zubar da cikin ba zai iya bata matsala tsakaninta da Fahat, wanda bata fatan haka.
A kusa da wani shagon mai Napep din ya sauke ta sannan ta fita ta ciro kudinsa ta ba shi taja gefe ta tsaya sai taunar cingan take tana wani kis kis kis, kamar

wata tsohuwar karuwa, dan mayafin dake jikinta ma ba wani abun kwarai ba ne yadda kasan wata yar iskar budurwa haka ta fito, arzikinta daya abaya ce a jikinta ba Atamfa ko lace ba. Ta kusan minti talatin a gurin har ta fara gajiya ta fara takawa gafen titin tana tafiya sannan Ramlee ta kirata sai ta kwatanta mata inda take, tana sauke wayar wata Benz ta wuce gabanta sai kuma ya dawo baya ta faka daidai inda take tsaye. A hankali mai tukin motar ya sauke gilashin motar yana kallonta, suna hada ido sai ta sakar masa murmushi shi kam ya dade da yi ma fuskarsa ado da murmushin.

“Hajiya ke ce haka dai?”

Ta dauke kai tana fari da ido sannan ta sake kallonsa da kyau, shi din ne dai abokin Faruq da ta taba roka kudi ta WhatsApp a lokacin data saci numbersa a wayar Faruq.

“Ni ce dai ranka ya dade, ya akai ka gane ni?”

“Kyakkyawar mace irinki ai kowa ya gani zai tsaya, sai dai daga baya mutum zai tantance idan ya sanki ko akasin haka”

Ta yi murmushi.

“Ka dawo nan ne ko zuwa kai?”

“To gani nan dai, Ina zuwa haka? Ina abokin nawa ya barki a rana tana gasa ki”

“Abokin ka ai ya dade da yin tazara, duk kyau surar nan da kake gani ya zubar wata zai dauko”

“Subhanallahi, lallai da labari a bakin naki mai kyau, da zaki taimaka min da kin shigo motar nan”

“Wallahi kawata nake jira, zata zo nan ta dauke ni”

“Okay”

Ya dauko katinsa ya mika mata.

“Gashi a taimaka a kirani, duk dai na san ba a rasa number”

Ta yi murmushi bayan ta karba, sannan ta daga kai tana kallon Ramlee data faka a dayan gefen.

“Okay zan kira ka Inshallahu”

“Na gode kyakkyawa”

Ya fada yana kare mata kallon irin kallon nan na yan iska. Sannan ya rufe gilashin motar ya hau titi, ita kuma ta nufi gurin da Ramlee ta faka motar ta bude ta shiga.

“Waye wacan?”

“Wani abokin Faruq ne”

“Okay”

Sai da suka hau titi sannan Ramlee ta kalleta ta ce.

“Hope dai kin shirya?”

“A shirye nake, kawai dai ina gudun a samu matsala ne”

“Ba wata matsala, Dr KB kwararen likita ne, ba yau na saba aiki da shi ba, ki kwantar da hankalinki”

Ajiyar zuciya ta sauke tana jin kamar kar ta aikata.

Inshallahu a nan zamu dakata sai kuma bayan sallah idan mai kowa mai komai ya amince mana ganin lokacin cikin koshin lafiya. Fatar Allah ya karba mana ibadar da zamu shiga ya yafe mana kurakuranmu.

Ina neman afuwarku. Sai mun hade a Book 2 bayan Sallah inshallahu. Happy Ramadam

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

AMINATU POV.

Tana jin muryar Talba sai ta bude ido da sauri, domin tabbatarwa idan kunnuwanta daidai suka jiyo mata, tsaye ta ganshi a kanta yana ta kallon kyakkyawar fuskarta cikin damuwa. A take ta zabura ta tashi zaune.

“Ina wuni”

Sai ya zauna kusa da ita yana kallonta cike da kulawa.

“Ya jikin?”

“Alhamdulillah”

Ta fada tana jin kamar an yaye mata ciwon an aje gefe daya. Hannunsa ya kai ya taba wuyanta sai ya ji shi da dan sauran zafi. A nan ya kalli Kaka.

“Wane irin magani aka bata?”

“Wanda ka kawo mata”

Kaka ta fada masa tana wani tsuke baki, ta dauke kai kamar wata yar yarinya wai ita ala dole fushi take da shi.

“Haba Kaka”

Sai kuma ya kalli Aminatu.

“Shalele wani irin magani aka baki?”

“Mai dacin nan na malaria da na ciwon kai, sai kuma ya saka min ruwa, kuma ta min allura”

Ta fada a shagwabe idonta na cika da kwalla ji take kamar ta fashe masa da kuka tunawa da zafin allurar da akai mata gashi kullum yake mata safe da yamma.

“Kin gani ko? Ba ma wani kwararen ba ne, taya zaka baka maganin malaria da allura a lokaci daya, kuma ba a tsaya an auna mutum ba? Maybe ma hawan jini ne tun...”

Kamin ya karasa Kaka ta daka matsa tsawa.

“Can can ga kanka, sai dai idan kai ka shafa mata hawan jinin, dan dai ina da shi ne shine kake son murdowa ta nan kace ni na saka mata? Daman tun da ka tafi take ciwo tana kuka na kira dan Asabe ya dubata yace malaria ce”

“Ba a auna mutun ba za a gano ciwonsa? Ni ban ce kin laka mata ba, daman ya za'ai wani ya saka ma wani hawan jini?”

“Wai idan ma manufar ka kenan ai na san ba so na kake ba”

Da gaske take maganar, a kokarin juya maganar zuwa wasa yai dariya ya amsa mata da.

“Me zan yi da tsohuwa ga sabon jini na samu”

Ya fada yana kallon Aminatu. Kaka ma kallonsa take.

“Ko Shalele?”

Aminatu ta yi kasa da kanta gabanta n bugawa da karfi. Sai yai murmushi

“Kin ci abinci?”

“Bata ci abincin ba ai gidan yan yunwa ka kawo ta ko?”

Kaka ta amsa masa a fusace. Be kula ta ba ya cigaba da kallon Aminatu.

“Bari na fita na bincika idan akwai inda ake siyar da abinci mai kyau sai na siyo miki, hankalina ya dauku shiyasa ban tsaya a hanya na siyo miki komai ba”

Magana yake mata a hankali kamar mai kokarin fahimtar da ita. Sai ta daga masa kai a hankali tana kai hannu ta share kwalla da suka tarar mata.

“Good Girl”

Ya mike tsaye sai ta bishi da kallo har ya fice, Kaka kuma ta bita da kallo mamaki zuciyarta na raya mata wani abun.

“Ke Auta…”

Aminatu ta kalli Kaka da sauri, sai Kaka ta matsa kusa da gadon da take zaune.

“Fada min lokacin da kuna can, yana miki wani abu?”

Aminatu ta yi shiru domin bata fahimci inda Kaka ta dosa ba.

“Yana tabaki ko ya rike hannunki ko ya dan shafa ki”

Aminatu ta yi shiru tana tunanin irin amsar da zata bawa Kaka.

“Karki ji tsoro ko kunya, kin ganshi nan jikana ne, duk yafi soyuwa a raina amman wacan kanen uban nasa da tsinanniyar matarsa da bata nuna masa son yan'uwan uwarsa ba, sun canja shi sun maida shi wani kala, ba san manufarsa a yanzu, na lura sai son shige miki yake kuma bayan ya nuna min shi ba zai aureki ba, har yana wani kiranki Shalele, wannan sunan yan iska ne, karki yarda ya sake ce miki haka kinji ko?”

Aminatu ta daga mata kai, alamar eh sannan tai kasa da kanta tana tauna maganar Kaka ba cewar yace ba zai aureta ba, wa yai masa tayin auren tun farko? Amman miyasa zai aurenta bayan ita da shi akwai banbanci da tazara mai girma?

‘A'uzubillahi’

Ta fada a ranta tare da lumshe ido tana jin kamar ta yi banban sabo saboda zuciyarta na kusanto mata da aurenta da mutumen da ko a mafarki yafi karfinta. Taya mutum mai daraja da tarin dukiya da kyau da iyali kamar Talba zai yarda ya hada jini da irinta? Amman miye manufarsa ta yi mata furucin da yai mata a lokacin da zai tafi? Ta daga idonta ta kalli Kaka.

“Tsohuwa ke kika ce masa ya aure?”

“Eh, saboda ki samu rayuwa mai kyau, kuma kin ga dan'uwanki ne zai rike ki da amana, sannan ni bana son yarinyar can da zai aura, uwarta sau biyu kawai ta taba zuwa garin nan, ita yarinyar ma ban santa ba, amman suka zaba masa ita saboda sun ga yana da dukiya, sai juya shi suke kamar waina, ni bana son ya aureta ma, kara ya auri yar'uwarsa idan ma a nan zai aje ki ai kin ga dole ya rika zuwa yana duba ki mu ma muna ganinsa, kuma sai na nunawa wannan bakar matar ni ma na isa da shi, amman sai ya juya min baya harbda turo wannan uban nasa a waya yana fada min kabli da ba-adi da shika shikan kin aurenki”

“Yana da wanda zai aura Kaka, kuma ba ki ga zubinsa ba? Akwai banbanci rayuwata da dasa, ni fa a kauye na tashi, sannan na rasa abubuwa da yawa da be zama lallai ma wani namijin ya so ni ba, balle kuma shi”

“Ai ba wannan za a duba ba, hadin gida da zumunci ba ruwansa da wannan dan haka ki daina ma duba wannan”

Kaka ta karasa tana mikewa tsaye ta gyara daurin zanenta.

“Bari na yi fitsari”

Aminatu ta yi kasa da kanta idonta na cika da hawaye. Kaka na shiga bandakin Talba yai sallama ya shigo, Aminatu ta kasa amsawa kuma ta kasa dago kai ta kalleshi, har ya zauna kusa da ita ya kai hannunsa ya dago kansa sai yai arba da hawayenta.

“Kaka ta miki wani abu?”

Ta girgiza masa kai alamar no.

“Toh miya faru ko kina jin ciwon ne?”

Wannan karon ta samu damar amsawa.

“Aa”

Sai ya saka hannunss biyu ya share mata hawayenta.

“Idan ina kusa da ke, hawaye basa da muhallin a fuskarki, ki daina kuka kin ji Shalele?”

“Ka daina ce min haka dan Allah”

Ya daga kansa sama yayi murmushi ya sauke.

“Idan Kaka ta zo ki fada mata ba zan daina ba”

Ya fada domin ya san ita ta kitsa mata wannan maganar, domin bata taba masa korafin kiran da yake da Shalele ba sai a yau.

“Na bawa wani ya siyo miki abinci mai kyau, yanzu fada min Kaka ta miki gulma ta?”

Ta yi shiru kanta a kasa.

“Kaka tana fushi da ni, saboda na ce ta aura min ke taki”

“Aa ba sai ka boye min ba, ni bana son aure a yanzu kuma na san akwai banbanci a tsakanina da kai...”

Bata karasa ba ya kai hannunsa ya rufe mata baki.

“Wallahi ban taba ganin wannan banbanci ba, kawai abun da nake tunani yadda zamu fuskanci juna ni da ke, kuma yanzu wannan zuwan da na yi ba zan tafi ba sai da igiyar aurenki”

Ta sakar masa ido sai kuma ta matsa baya kamar mai tsoronsa.

“Kana da wanda zaka aura, Yallabai ka rufa min asiri bana son na sake shiga wata matsalar idan ma Kaka tana fushi da kai ne saboda ka ce ba zaka aure ni ba, na fahimta”

Yayi Murmushi ya kalli wani gefen sannan ya sake kallonta.

“Yan mata, idan ma kin yi karya zuciya bata iya karya ba, na riga na karance ki kina kokarin hana zuciyarki abun da take so ne, a miyasa kika rika tambayar yaushe zan dawo a lokacin da zan tafi?”

“Saboda na sabu da kai ne kawai na kwana biyu”

“Miyasa a lokacin dana tafi kika kwanta ciwo sai a yanzu dana dawo kika samu lafiya?”

Ta yi shiru.

“Kin san saboda me?”

Ta girgiza kai.

“Saboda na tafi da zuciyarki, a yanzu kuma da na dawo na dawo miki da ita, karki yarda zuciyarki ta raya miki banbanci tsakaninki da wata ko wani, karki yarda ki sake nisa da mutanen da suke da muhimmanci a rayuwarki, domin zuciyarki ba zata iya daukar wani ciwon ba”

Har lokacin kanta a kasa yake tana hawaye, shi kuma yana kallonta yana jin kamar ace yana da permission din rumgumarta ya rarrasheta. Kamar daga sama suka ji muryar kaka tana jan tsaki.

“Maye ne kai da ka tafi da zuciyata, ka ji wata maganar banza idan son ta kake da gaske ai aurenta zaka yi”

Runtse ido Talba yai ya bude ya kalli Kaka da be san tana cikin bandakin ba har sai da ta fito.

“Kaka labe kike mana ne?”

“Ina ce dai Dakina ne? Kuma ina jinka dazun kana min karya wai na hana ka Auta, ai ban mutu ba da rai na”

“Dakinki ne, amman ni ma ina da hakki da shi ko? Kuma ai ban fadi karya ba na fada miki a waya zan zo kika ce ba zaki ba ni ba, kin dauka wasa nake? Wallahi Kaka ba zan bar garin nan ba sai na auri Aminatu”

A take Kaka ta washe hakora, gaban Aminatu kuma yai dukan uku uku.

“Aa dan Allah dan Annabi Aa”

Aminatu ta fada cikin kuka, sai Kaka ta watsa mata harara.

“Ke Wallahi baki isa ba ke ma, idan ba haka ba ni da ke ne, wannan abun farinciki da jindadi haka zaki ce wani aa, Mu'azu da gaske kake yi?”

“Wallahi da gaske nake yi kaka, amman dan Allah karki cilasta mata ki barni zan yi magana da ita”

“Mu can da aka mana aure, zabi aka bamu ne? Ko mazan ma ba mu sani ba sai da aka daura auren, karka biye shashancinta yarinya ce karama bata da wayo”

Talba yayi murmushi yana kallon Aminatu dake hawaye. Kamin ya kalli kofar shigowa dakin Kaka na amsa sallamar Aminu baki har kunnen.

“Aminu”

“Na'am Tsohuwa ya jikin?”

“Aa ni ai na warke, abun farinciki ya samu kuma ai”

Har Aminu yayi kamar ya tambaya minene domin ya lura Kaka tana son labarta masa sai kuma wata zuciyar ta hana shi, sai ya karasa gaban Talba ya aje masa kular abinci da ledar lemu ya mika masa canji.

“No ka rike carjin”

“To na gode Allah ya kara sutura”

Aminu na fita Kaka ta bi bayansa domin labarta masa, abun da ya kasa boyuwa a ruhinta. Sai da suka fice sannan Talba ya kai hannu ya bude cooler kamshin ferfesun kayan ciki ya daki hancin Aminatu.

“Sauko ki ci”

“Aa”

Ta fada da muryar kuka, domin kukan ne ya zo mata da gasken gaske. Kallonta yai.

“Shalele? Kar dai ki ce min baki son auren nan?”

Ta daga masa kai.

“No please, kar mu yi haka da ke, ba wai zan aureki saboda Kaka ne kawai ba, zan aureki ne saboda na faranta miki rai, ina tunanin zaki so abun da zai faranta min rai kuma ya shirya tsakanina da yan'uwana, idan har ban aureki ba ina cikin matsala ba yar karama ba...”

From a to z ya zayyana mata komai ciki har da kudirinsa na boye auren na su na wani lokaci. A nan ne hankalinta ya kara tashi.

“Ina jin tsoron abun da rayuwa zata samar min a gaba, komai nawa ya banbanta dana kowa, rayuwata ta zama ba tawa ba, duhu ne ya fara bayyana a ciki, sai iska ya mamaye komai, kamin na ankara taurarin ciki sun tarwatse! Hakan ne silar rushewar duniyata... Talba ba ni da gata, ni fa yar gudun hijira ce kawai...! Ina jin tsoro abun da zai faru”

Ta share hawayenta. Yayi saurin kama hannayenta, a cikin yanayin da ke nuna tsantsan tausayinta, fararen idanuwansa masu kamar madara suka rine da ja tsabar bacin rai da bakinciki.

“Ashe ba ina kusa da ke ba? Ki daina tunani wannan tunanin Shalele da yarda Allah sai na mai da ke yar lele”

“Taya? Kana da wanda zaka aura, kana da rayuwarka da mafarkinka, miyasa zaka rusa komai? Baka tsoron halin da zan shiga? Abun da iyaye basa so akwai hadari a yinsa”

“Ki daina damuwa da iyayena ko Leila, ni mijin mace hudu ne, ba san ba zaki yarda alakar dake tsakanina da Kaka ta lalace ba akan abun da zaka iya yi min, zan sama miki wata rayuwar mai kyau mai inganci, zamu gina wata duniyar mai ciki da daula da jindadi mai cike da zuri'a”

Ta fisge hannayenta hawaye na ta zirya a fuskarta, mikewa tai tsaye tana masa kallon tsoro.

“Ta ya kake tunanin rayuwa zata zama mai sauki a gareni? Ya kake tunanin Leila zata ji idan ta san ka aure ni? Miyasa kake tunanin samun wasu Family a gareni mai sauki ne? Bayan na rasa kowa? Taya mace irina wanda ta rasa komai na kima da mutuncin mace farinciki zai rabeta, ta ya Yallabai...!”

Mikewa yai tsaye yana kallon cikin idonta.

“Kar bakinki ya sake furta irin kalamin nan, ina gargade ki a kan furucin... Ina son na roki ki wannan alfarmar Aminatu, dan Allah ki yarda ki aureni ba dan saboda kanki ba ko Kaka, saboda ni”

Ta runtse ido hawaye na sauko mata, a take ta ji zazzabin ya dawo mata sabo.

“Na san akwai wahala amman ki daure dan Allah”

Ta bude idon ta kalleshi sai kuma ta sake rufewa sakamakon jirin data ji yana dibanta.

“Ina son zan kwanta”

Ta fara lalaben gadon tana kokarin kwantawa idonta a rufe.

“Wannan maganar zata zama a tsakaninmu, bana son Kaka ta san cewa a boye zamu yi wannan aure”

Nan ma bata ce masa komai ba har ta zauna.

“Ki ci abinci sannan ki kwanta”

“Bana jin yunwa”

“Ba zan cilastaki ba, bana son na saka ki a cikin abun da zai haifar miki da damuwa, zan yi magana da Kaka”

Bata ce masa komai ba har ya fice daga dakin. Ta inda yake jiyo muryar Kaka ya nufi sai ya tsaya daga bakin kofar dakin yana sallama.

“Shigo Mana Mu'azu”

Kaka ta fada da far'arta, sai ya cire talkamin kafarsa ya shiga dakin ya zauna kusa da Kaka yana kallon matar kawon nasa dake da far'ar da alama ita ma abun ya mata dadi.

“Mu'azu yanzu nake jin abun alheri Allah ya tabbatar ya sanya alheri”

“Amin na gode”

Kaka ta kalleshi tana fadin.

“Salamatu ce ta zo da wata magana wai idan Alhaji ya ji zai iya hanawa, ko kuma ya cilasta sai ka sake ta”

“Kaka kar wannan na dame ki, da saninsa na zo nan, kawai dai yace babu ruwansa saboda na dage sai na yi auren, shiyasa nake son kamin ya canja shawara a daura mana aure da ita inya so idan tarewa ne sai a barshi har sai komai ya kamalla”

“Amman Mu'azu hakan ba zai haifar muku da matsala ba? Baka ganin hakan zai iya sakawa su can su tsane ta?”

Cewar Salamatu tana kallonsa.

“Idan ma sun tsane ta, ni dai ina son ta kuma ba zan tana yarda a cutar da ita ba ko kuma ni da kaina na cutar da ita, a kokarin sama mata wasu iyalin na kawo ta nan, a can ma abubuwa da yawa marasa dadi sun faru saboda ni da ita, ina tunanin ko da a mafarki aka ce muku zan cutar da ita ko kuma na yarda a cutar da ita ba zaku yarda”

“Wallahi ko kadan, ban kawowa raina Cewar zaka cutar da ita ba, ai babu wanda ya dace ta aura sama da kai, kai da kasan komai nata kuma kake tausayinta, kawai dai ina ji maka tsoron abun da zai faru ne a gaba, kasan za su iya fushi da kai”

Salamatu ta sake fada tana kallon Kaka dake jinjina kai.

“Wannan kuma ai mai sauki ne, komai zai wuce Inshallahu, ni dai yanzu ina son ku amince min ayi komai tsakanin yau zuwa gobe amman da idan har ta amince domin bana son na cilastata”

Kaka ta dafa shi.

“Karka damu ita fa bata san so ba, kuma ta sabawa kanta da kuka tun da ka tafi kullum kuka take sai ciwo, bata da wayo amman an mata auren zata yi hankali”

Yayi shiru ya sauke kansa kasa can kuma yaja numfashi a hankali ya sauke.

“Na yi magana da Kawo Hasan kuma ya nuna min cewar ba wata matsala, amman duk da haka ina son yi sake yin magana da shi, sai a yanka min sadaki kuma idan son samu ne a daura auren nan yau ko gobe kamin Daddy ya canja shawara”.

“Ka yi gaskiya saboda bakar matar nan ma zata iya kitsa masa wani yace ya canja shawara ba zaka aureta ba, kuma dan be saka hannunsa ba, sai me ai mu masu yi maka komai ne, ba mu hana ka auri yarsa ba karawa kawai aka ce kai amman sai taya yarsa kishi yake, wannan abun da kai ni ka yi wa Allah ya maka albarka”

“Ameen”

Ya amsa sannan ya mike tsaye ya saka hannayensa aljihu.

“Idan kun yi magana da su, sai ki sanar min domin ina son komawa yau, idan kuma hakan be samu ba, zan jira har sai zuwa gobe idan an daura auren”

“To bari na nemo shi yanzu”

Kaka ta fada sai ya sa kai ya fice ya bar Kaka da Salamatu kadai a dakin. Salamtu ta kalli sarakuwarta cikin yanayi na damuwa ta ce.

“Inna baki ganin hakan zai iya haifa da matsala? Allah ya ma ba aurenta zai yi ya tafi ya barta ba sai an gansa”

“Aiko da sun ci ubansu, daga shi har uban nasa, be ma isa ba, idan zai tafi kafarta kafarsa haka zai tafi da ita, idan ma wayonsa kenan ba zan yarda ya barta ba”

“Toh sai dai haka nan, kam idan ba haka ba zai iya mana wani wayon kin san halin yaran nn na zamani, amman kam da ta yi miji yaro barakalla da shi gwanin kyau”

Kaka ta tashi zuwa neman danta Hassan. A lokacin da Talba ya fita daga dakin Salamatu sai ya koma dakin Kaka, daga bakin kofa ya tsaya yana kallon Aminatu dake kwance rairai idonta a rufe, sai dai jin kamshin turarensa yasa ta shakar kamshi bada ta san yan tsaye bakin kofar ba, idan yaja numfashin da karfi sai ta sauke a hankali.

“Kina son turarena amman baki son kusanci da ni”

Ta bude idon ta sauri ta juyo ta kalli gurin kofar sai ta ganshi a tsaye, wani irin kwarjini da haifa ya kara a idonta. Idan har tace bata son Talba to ta yaudari kanta kuma ta yi karya, amman tana sonsa? Anya akwai son sa a zuciyar dake cike da damuwa da bakinciki? Anya ma ta gama karantar minene son? Ko kuwa dai sabo ne irin wanda ta ji a wacan lokacin da tafi ya barta, a yanzu ma idan bata amince ba zata sake ganinsa ko kuwa zai tafi ne har a bada ba zai dawo ba?

“Tashi ki ci abinci idan ba haka ba zan kira wannan mutun ya zo yai miki allura”

Daga inda yake tsaye ya fada, sai ta tashi zaune tana turo baki tana masa wani kallo dake nuna alamar kiris ya rage ta fashe masa da kuka. Sai yai murmushi ya saka kafarsa cikin dakin ba tare da ya cire talkaminsa ba.

“Idan kika aminta kika zauna da ni, zamu rika ganin juna kullum, amman idan kika ki ni wata kila ba zaki sake ganina ba Aminatu, amman na san ba zaki bawa Kaka kunya ba ko?”

Ta yi shiru sai kuma ta fashe masa da kukan da bata san na minene ba. Cooler ya dauka ya sake budewa ya saka hannunsa ya rika dauko farfesun ya kai mata a baki.

“Bude baki”

Ta bude bakin daker tana ta kukan shagwaba. Sai ya kai mata a bakin yana kallon kyakkyawan lips dinta.

“Pretty girl”

Ya furta yana hade yawu, even though be taba kissing lips din wata mace ba, he like her pink lips, dan karamin bakinta nan ya dauki hankalinsa sosai da yadda take tauna abinci a hankali kamar ya mata dole. Da hannunsa yake bata har sai da wayarsa tai ringing sannan ya saka hannunsa na hagu ya karba kiran kawo Hassan sannan ya mike tsaye yana fadin.

“Okay gani zuwa”

Be ce mata komai ba ya fice daga dakin, a harabar gidan ya kunna bohore ya wanke hannunsa sannan ya nufi dakin wajen, ba Kawo Hassan Kawai ya samu a gurin ba har da wane kanen Hassan din wanda shi na kawo ne a gareshi da kuma Kaka, kusan abun da suka tattauna a dakin Salamatu shine suka sake tattauna da Uncles din nasa, sai da ya tabbatar musu da babu wata matsala sannan suka amince akan gobe idan an sauke Sallah azahar za a daura masa aure da Aminatu a Masallacin kofar gidan. Kawu Hassan sai nuna bacin ransa yake akan abun da Daddy yai yana ganin kamar ya wulakanta kuma ya nuna shi kadai yake da iko da Talba, be jidadin da za a yi komai ba tare da shi ba, amman be tsammaci haka daga gareshi ba, sai dai dukansu sun raja'ah ne aka ce maganar Kaka cewar saboda ya maida su talakawa ne shi kuma yan ganin shi mai arziki ne.
A garin Talba ya wuni har dare, sai guraren tara da rabi Daddy ya kirashi Saboda Momy ta fada masa Talba baya gidan, sai da ya fita waje can nesa da gidan sannan ya amsa kiran Daddy, ya fada masa cewar yana gurin Kaka.

“Amman kasan yanayin kasar nan ki? Musamman kauye idan sun ga bakuwar fuska har hada kai ake azo a dauke mutum, sannan taya zaka yi tafiya baka fada min ba?”

“Saboda zaka iya hanani da wannan hujojin naka daka zayyano a yanzu, ni kuma ina bukatar zuwa saboda na yi magana da Kaka ka san tana cikin fushin a yanzu”

“Na ji ka dawo da wuri, Allah ya tsare, kuma ka yi addu'a sosai Wallahi ina tsoron garin nan”

“Inshallahu Daddy babu abun da zai faru”

“Toh Allah dai ya tsare, amman ka daina wasa da rayuwarka irin haka”

“Inshallahu”

Daga haka sukai sallama sannan ya kira Momy ita ma ya sanar mata inda yake ya kuma fada mata ba zai samu dawowa ba sai gobe.

“Allah yasa dai ba gurin yarinyar nan ka tafi ba”

Momy ta fada cike da gadara.

“Momy kina manta cewar akwai zumunci a tsakanina da ita a yanzu, ko bayan ita kuma Kaka ta tana nan kuma tana raye dole ne na rika zuwa”

“Hmmm Talba kenan, a hannuna ka tashi karka ce zaka min wayo, ni dai n gargadeka, kuma na ja maka kunne ka fita sabgar yarinyar nan tun wuri indai har ka dauke ni uwa, ina tunanin zaka ji magana ta”

Ya sauke ajiyar zuciya ba tare da yace komai ba, Momy ma bata sake cewa komai ba ta kashe wayar, sai ya koma cikin gidan ya ari wayar Kaka da sunan zai duba wata number yai blocking din number Daddy a wayar Kaka sannan ya goge number gaba daya, gudun kar Kaka tai karabanin cewa zata kira shi.
Bayan ya gama abun da zai yi ya mika mata wayarta ya fita, Kawu Hassan ya shigo dakin Kaka ya saka Aminatu a gaba yana tambayar idan tana son Talba, sai dai Kaka bata bata damar amsawa da eh ko aa ba, duk inda Kawu Hassan yai sai a tare, tana cewa wai Aminatu bata da wayo bata san ciwon kanta ba, kuma ba san minene so ba. Ita kanta Aminatu da za a bata dama da bata san wace kalar amsa zata bawa Kawu Hassan ba, domin kanta a yanzu a duhu yake.
Daga ita har Talba bachinsu kadan ne, misalin biyu da rabi ta tashi ta shiga bandakin Kaka tai alwala ta fara raya daren na Laraba tana kaiwa Allah kukanta da neman zaba mata abun da zai zame mata alheri da kuma rokin daukinsa a dukan al'amurranta, ta bangaren Talba ma sallah nafila ya kwana yi, a da can sai dai yai raka'a biyu yai karatu da addua ta kwanta sai dai wannan karon har asuba yana zaune a saman carpet din da yai sallah yana karatun qur'ane, bayan ya kamalla ya fadawa Allah bukatarsa da neman daukinsa a abun da yake kokarin aikatawa.
Washe gari abun kari na musamman Kaka ta saka aka shirya masa, aka kawo masa har dakinsa, ruwan tea kawai ya sha ya kasa cin komai, sai abubuwan da suka faru a jiya suka rika dawo masa, ya sani akwai kalubale mai yawa a gabansa, sai dai yayi ma kansa alkawarin duk rintsi duk tsanana ba zai taba yarda ya cutar da Aminatu da saninsa ba.
Misalin Tara da yan mintuna Kawu Hassan ya same shi da maganar Sadakin da kuma wanda zai masa walicci domin shi zai dauki bangaren Aminatu ne.

“Na saka dubu ashiri Hajiya tace yayi kadan zai dai a saka arba'in”

“Ba matsala Kawu zan bada 100k, Inshallahu”

Kawu yayi murmushi yana mamaki.

“100k fa kace Mu'azu, aa yayi yawa”

“No be yi yawa ba, ita kanta Aminatun ina son ta ji cewar na dauke ta da kima”

“Duk da haka dai dubu dari yayi yawa”

“Be yi yawa ba Kawu, Allah dai ya tabbatar mana da alheri”

“To amin”

Talba ba mutum ne mai yawo da kudi mai yawa ba, haka ya saka dole sai da ya je POS ya cire wasu kudin sadakin ya bawa Kawu da kuma kudin da za a siye komai na al'ada na daurin auren. Bayan ya dawo ne ya kira Ali ya fada masa komai, at first Ali dariya ya fara masa kamin ya biyo da addu'a sannan ya tabbatar masa cewar da shi za a daura auren nan.
Haka kuwa akai, kamin lokacin daurin auren ya iso garin tare da sabuwar shaddda mai masifar kyau da tsada sai kyalli take kana ganinta kasan ta ci kudi,

fara ce sol zagenta ya fito kwar gwanin sha'awa, not just shadda hula da Talkamin da Ali ya siyo masa ma abun kallo ne.

Misalin karfe biyu da yan mintuna aka daura aurensa da Aminatu, ba zai iya cewa happy marriage ba ne, and it's not the sad one, sai dai ya samu kasa da farinciki marar misaltuwa, wani irin annashuwa da natsuwa suka saukar masa, fuskarsa sai haiba take kana ganinsa ka ga ango. Ko kadan fuskarsa ko dabi'arsa da mu'amalarsa bata nuna cewar baya son auren ba, domin shi kansa yana jin matsayinsa da kwarjininsa su karu.

BATURIYA POV.

Kamar yadda tai masa alkawari, a ranar ta same shi a gidansa na hutawa, suka aikata masha'arsu kamar wacan lokacin. Sai dai wannan karon bata yarda ta kai dare ba saboda tana son zuwa asibiti ganin likita kamar yadda ta fada a gida da karyar zuwa asibiti ta samu fitowa.
Wannan karon a account ya saka mata 450k a maimakon ya bata a hannu, saboda ta fada masa bata son kudin a hannu. Yadda yake santi yana yabonta har yafi na wacan karon, sai wani narke mata yake a jiki kamar zai shige ciki, daker ta kwanci kanta domin a ra'ayinsa ya so ta kwana a gidan ne, sai ta nuna masa tana a karkashin iyayenta ne za su iya zarginta idan ta kwana, sai dai bata yarda ta nuna masa cewar tana da aure ba, sai ma karyar da tai masa cewar mijinta ya rasu ya barta da yaro daya.

Misalin hudu da kwata ta fito daga gidansa, sai da ta shiga Napep sannan ta kira Ramlee ta sanar mata cewar yanzu ta fito daga gida, domin bada sanin Ramlee ta hadu da shi ba, kuma ta san idan har taji sun hadu ta bayan fage zata iya zargin Baturiya.

“To ki tsaya ta sokoto Road, zan zo a dauke ki”

“Okay toh amman karki dade dan Allah”

“Okay”

Baturiya ta sauke wayar tare da shafa cikinta tana jin irin abun da take ji a duk lokacin da tai yunkurin zubar da cikin, sai dai bata da mafitar data wuce wannan, domin idan bata zubar da cikin ba zai iya bata matsala tsakaninta da Fahat, wanda bata fatan haka.
A kusa da wani shagon mai Napep din ya sauke ta sannan ta fita ta ciro kudinsa ta ba shi taja gefe ta tsaya sai taunar cingan take tana wani kis kis kis, kamar wata tsohuwar karuwa, dan mayafin dake jikinta ma ba wani abun kwarai ba ne yadda kasan wata yar iskar budurwa haka ta fito, arzikinta daya abaya ce a jikinta ba Atamfa ko lace ba. Ta kusan minti talatin a gurin har ta fara gajiya ta fara takawa gafen titin tana tafiya sannan Ramlee ta kirata sai ta kwatanta mata inda take, tana sauke wayar wata Benz ta wuce gabanta sai kuma ya dawo baya ta faka daidai inda take tsaye. A hankali mai tukin motar ya sauke gilashin motar yana kallonta, suna hada ido sai ta sakar masa murmushi shi kam ya dade da yi ma fuskarsa ado da murmushin.

“Hajiya ke ce haka dai?”

Ta dauke kai tana fari da ido sannan ta sake kallonsa da kyau, shi din ne dai abokin Faruq da ta taba roka kudi ta WhatsApp a lokacin data saci numbersa a wayar Faruq.

“Ni ce dai ranka ya dade, ya akai ka gane ni?”

“Kyakkyawar mace irinki ai kowa ya gani zai tsaya, sai dai daga baya mutum zai tantance idan ya sanki ko akasin haka”

Ta yi murmushi.

“Ka dawo nan ne ko zuwa kai?”

“To gani nan dai, Ina zuwa haka? Ina abokin nawa ya barki a rana tana gasa ki”

“Abokin ka ai ya dade da yin tazara, duk kyau surar nan da kake gani ya zubar wata zai dauko”

“Subhanallahi, lallai da labari a bakin naki mai kyau, da zaki taimaka min da kin shigo motar nan”

“Wallahi kawata nake jira, zata zo nan ta dauke ni”

“Okay”

Ya dauko katinsa ya mika mata.

“Gashi a taimaka a kirani, duk dai na san ba a rasa number”

Ta yi murmushi bayan ta karba, sannan ta daga kai tana kallon Ramlee data faka a dayan gefen.

“Okay zan kira ka Inshallahu”

“Na gode kyakkyawa”

Ya fada yana kare mata kallon irin kallon nan na yan iska. Sannan ya rufe gilashin motar ya hau titi, ita kuma ta nufi gurin da Ramlee ta faka motar ta bude ta shiga.

“Waye wacan?”

“Wani abokin Faruq ne”

“Okay”

Sai da suka hau titi sannan Ramlee ta kalleta ta ce.

“Hope dai kin shirya?”

“A shirye nake, kawai dai ina gudun a samu matsala ne”

“Ba wata matsala, Dr KB kwararen likita ne, ba yau na saba aiki da shi ba, ki kwantar da hankalinki”

Ajiyar zuciya ta sauke tana jin kamar kar ta aikata.

_____

Inshallahu a nan zamu dakata sai kuma bayan sallah idan mai kowa mai komai ya amince mana ganin lokacin cikin koshin lafiya. Fatar Allah ya karba mana ibadar da zamu shiga ya yafe mana kurakuranmu.

Ina neman afuwarku. Sai mun hade a Book 2 bayan Sallah inshallahu. Happy Ramadam

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Fatar mun yi sallah lafiya. Allah ya maimaita mana.

AMINATU POV.

Tun da kalmar an daura aure ta daki kunnenta sai ta nemi natsuwarta ta rasa, a take wani kalar yanayi mai wahalar misaltuwa ya rufeta, zuciyarta ta shiga bugawa da karfi fiye da fitar numfashinta.
Banbancin wacan bugun zuciyar a wacan daren da yau kadan ne, wacan ya kasance na fargaba da tsoro ne, tsabanin wannan da ba zata kira shi na farinciki ba kuma ba na bakincikin ba ne, wata kila bata cancanci auren a yanzu ba ne, wata kila kuma wani tarin bakincikin ne yake kokarin yi mata sabuwar shimfida. Haka tai ta sake sake tana jin kamar tai kuka gashi kuma hawayen ba su shirya ziyartar idanuwanta ba. Duk shigowar da ake ana saka mata albarka a dakin Kaka bata yarda ta daga kai ta kalli kowa ba balle ta san su waye ke kai da kawo a dakin. Ana kusan sallah La'asar Kaka ta shigo dakin da far'arta ta duka gaban Aminatu ta bude kwanon abincin da aka aje mata.

“Har yanzu ba ki ci ba? Ki wuni da yunwa tun safe ace har yanzu ba ki ci komai ba, to ko dai a kawo miki fura?”

Yunkurin bude baki tai ta amsawa Kaka sai ta ji bakin na ta yayi nauyi kamar wanda kalamanta suka kare, hakan yasa ta girgiza kai, Alamar aa.

“Ai dole ki ci wani abu kam ace mutum ya zauna da ciki haka tun safe”

Kaka ta fada tana Juyowa ta fita, a nan ma Aminatu ta yi ta kokarin ganin ta bude baki ta fada mata cewar ba zata iya shan komai ba amman ta kasa. Hannunta ta kai ta taba bakinta sai ta ji shi a bushe ba bakin ba har makoshinta a bushe yake, iyakar kokarin da tai na hade yawu ne saboda ta jika makoshinta. Idanunta na kan kofar har Kaka ta dawo dakin rike da kankara a cup ta nufi inda kwayar furarta take ta bude ta debi furar ta zuba a cikin kankarar sannan ta rufe ta aje furar ta nufo inda Aminatu take zaune.

“Ta so Mai gida yana son magana da ke”

Kamin Aminatu tai wani yunkuri har Kaka ta rika hannunta tana kokarin mikar da ita tsaye, Aminatu ta saka dayan hannunta ta rike sabon zanen atamfa da Kaka ta tsaga gida uku ta bata daya ta daura dayan kuma ta yafa sai ta saka shirt a jikinta. Kamar wata igiya haka ta bi Kaka dake janye da hannunta suna tafi, zuciyarta sai zillo take kamar zata fasa kirjinta ta fito, ba zata iya musu zuwa ba kamar yadda ba zata iya fisge hannunta daga rikon da Kaka tai mata ba. Kamar wanda akai wa auren dole haka ta samu kanta tana jin kamar ba ta shirya haduwa da Talba ba. Sai dai bata iya komai har Kaka ta fice da ita harabar gidan ta nufi waje da ita. Kaka da kanta ta isa dakin dake zaure ta kwankwasa kofar sai aka bude daga can ciki.

“To ga Amaryar”

Kaka ta fada tana kaucewa ta yadda zai iya hango Aminatu dake tsaye bayanta kanta a kasa. Murmushi yai yana kallon matarsa.

“Ba ki kishi kenan?”

“Aa ni yau cikin farinciki na ke Alhamdulillah ka yi min abun da nake so”

Kaka ta fada cikin murna da farinciki marar misaltuwa, sannan ta juya ta nufi inda ta fito ta bar Aminatu tsaye a gurin kanta a kasa. Talba ya maida dubansa gurin Kaka har sai da ya tabbatar ta koma cikin gidan sannan ya fito daga cikin dakin ya kalli Aminatu, kamshin turaren da ta ji ne ya tabbatar mata cewar angonta ya matso kusa da ita, sai dai bata iya daga ido ta kalleshi ba har ya kai hannunsa ya riko hannunta, wani kalar yanayi ta samu kanta a cikin, yayinda hannunta yake tsarkafe cikin nasa hannun, janta yai a hankali zuwa cikin dakin yana kallon kafafuwanta kamar mai kirga tafiyarta, takawa take tana jin kamar ba tafiya take ba har suka shiga cikin dakin. Sannan ya saki hannunta ya nufi kofar ya rufe sai ya tako a hankali ya tsaya daga bayanta ya kai hannayensa ya kama zanen da take rike da shi da dayan hannunta.

“Saki”

Ya furta jin yadda ta kara rike zanen da karfi gam, jikinta ya fara rawa.

“Daura miki zan yi, ba wani abun zan miki ba, kin min kankanta sai dai nan gaba idan kin kara girma”

Ya fada a kokarinsa na kawar mata da tsoron dake tare da ita. Sai dai hakan be saka ta yarda ta sakar masa zanen ba, be damu ba ya kama zanen a haka ya saka dayan hannunsa ya cire nata hannun dake jikin zanen a hankali, sannan ya daura ba mata, not like yadda take daurawa but he try domin ya saba daura tawul.

“Yauwa”

Ya furta sannan ya juyo gabanta ya tsaya yana murmushi.

“Amarya”

Da sauri ta dago kai ta kalleshi, sai ta ji kamar ta furta mata kalmar ne saboda ya firgitata, sai dai murmushi da haifar da tai arba da ita a fuskarsa ya hana ta

ganin komai. A yau ya fi yi mata kyau fiye da ko yaushe, kimarsa da kwarjininsa sun karu a idonta. Bayan hannunsa ya kai gefen fuskarka yana shafawa a hankali idanuwansan kwancen a cikin nata, yana yi mata haka ne just to make her feel comfortable and saboda yana tausayinta, not because of love, domin ko kadan baya kawo soyayyah a kusa. Ba zai iya cewa ya tsane ba, and haka ma ba zai iya cewa yana kaunarta ba.

A hankali ta sauke kanta kasa hawaye suka kwankwaso mata kofa, kuma ta rasa dalilin zuwan su a yanzu, domin ba farinciki take ba alhalin ma tsoro ne ya cika mata zuciya.

“Waye kai”

Ya furta ba tare da ta kalleshi ba, hannunsa ya kai ya taba fuskarsa wai ko wani abu ya canja ne daga fuskarsa daya saka bata iya gane shi ba.

“Akwai abun da ya banbanta daga ni ne, da ya saka yau ba ki gane ni ba?”

Ta dago ta kalleshi hawaye na sauko mata.

“Asalin kai nake nufi, har yanzu ban gama sanin waye kai ba”

“Me hakan zai amfanar miki?”

“Ban taba gani ba, ban taba ji ba ko a tarihi cewar wani mutum mai daraja da kima irin ka ya auri mace irina ba, kana da komai na duniyana ki kuma na rasa komai na rasa kowa, ban iya karantawa ba balle na rubuta, ban san wani abu rayuwar birni ba balle na waye, rayuwata ta canja daga daren da Barayin Shanu suka shigo mana a gari, kuma na shiga hannunsu sun wulakanta ni saboda ba su san darajar mace ba, ba su san iya abun bakincikin da mace take ji ba ba idan ta rasa martabarta, kuma likitan daya karbe ni ya bani taimako yai min aikin, abokin ka ne, duk baka duba wannan ba ka amince da aurena saboda ka faranta ran Kaka? Baka tunanin a kokarinka na faranta ranta zaka iya ruguza sauran natsuwar da ta rage min? Zuciyarka bata taba ayyana maka kyamata ba?”

Kallonta kawai yake, yana mamakin irin yadda Allah ya zuba mata baiwa da kaifi basira a kwakwalwa fiye da shekarunta. Sai da kalli kasa sannan ya sake kallonta sai kuma ya kai hannu ya kama hannunta ya kai saitin zuciyarsa.

“Wannan ya kamata ki tambaya miyasa ta amince da kudurin Kaka? Wata kila ba saboda faranta ran Kaka ne kawai ba, har da kokarin faranta na ki ranki, zuciyata tana son farinciki”

Ya aje numfashi a hankali sannan ya cigaba.

“Ba zan boye miki ba, bana jin komai a yanzu, kyamarki ko hange wani abu daya same ki a matsayin abun da zai hana ni aurenki ko kuma yin farinciki da ke, ban sani ba wata kila a gaba zuciyata zata iya sauya sai dai bana fatar hakan, kuma a duk halin da na tsinci kaina na miki alkawarin adalci da farinciki”

Ya karasa yana matse hannunta sosai a cikin nasa.

“Sai dai kamin nan ina rikon alfarmarki, ina son...”

Sai kuma ya ji kamar ba zai iya fada ba, kansa ya daga sama kadan ya sauke yaja hannunta a hankali zuwa inda katifa take ya zaunar da ita. Ya saka duka hannayensa ya rika kafardarta.

“Ina son ki min wani alkawari”

Kallonsa tai ba tare da tace komai ba, hakan ya bashi damar gabatar mata da uzurin nasa.

“Ina son auren nan na mu ya zama na sirri, bana son kowa ya san cewa mun yi aure, musamman Momy, Daddy, da kuma Leila da duk wani da yake gidan, daga lokacin da zan dauke ki mu bar gidan nan bana son ki kalleni a matsayin mijinki, har sai idan lokacin bayyana hakan yayi!”

Wani irin kallon rashin fahimta tai masa, a take zuciyarta ta fara raya nata abubuwa mabanbanta, kunyar nunata yake a gurin yan'uwansa ko kuma ya aureta na dan lokaci ne ya rabu da ita shiyasa har baya son kowa ya san alakar dake tsakaninsu? Kamar ya san abun da ke ranta sai fayyace mata komai ta siffar da zata fahimta.

“Na san zaki yi ta Sake Sake a ranki, ba wai na yi hakan da wata manufada nufin cutar dake ba. Tun farko na sanar da Daddy da Momy cewar ina son aurenki, sai dai ban samu goyon baya daga gurinsu ba, and ba zan iya cewa Kaka aa ba, and ba zan iya barin ki fadawa wata rayuwar ba, so i decided na yi auren a boye ba tare da saninsu ba, ba wai ina nufin auren zai yi ta zama a boye ba har abada, no na dan lokaci ne, kuma wannan maganar ina son ta tsaya a tsakaninmu bana son Kaka ta san da komai”

Kallonsa take hawayen dake cika mata ido ya hana ta ganinsa da clear, ta wani bangaren tana jin kamar zata iya, sai dai bata san abun da iyawarta zata haifar ba a gaba, za su yarda su karbe ta ko kuma wani sabon babi na cin mutunci da kyama za su nuna mata, bata gama yanke dayan biyun ba ta ji ya saki kafadarta ya kama hannunta

“Zan tafi yau, ba tare da ke zan tafi ba, kuma zan rika zuwa ina dubaki kamin lokacin da zan dauke ki mu tafi can gaba daya, karki ji komai idan akwai abun da kike bukata sai ki fada min ko ki fadawa Kaka”

A nan mata ce komai ba, sai sauraren yadda yake murza yatsunta a cikin nasa take. Cikin natsuwa ya dago ya kai bakinsa goshinta ya sumbanceta sai ya lumshe ido hawaye suka sauko mata.

“Ba zaki ce Allah ya tsare ba?”

Ya rada mata saitin kunnenta, sai ta aje numfashi a hankali ta hade yawu, tana jin lokacin daya mike tsaye sannan ya mikar da ita sai ya rumgume ta a kirjinsa. Lamooo tai kamar kyanwa tana sauraren yadda zuciyarta da tasa suke bugawa da karfi kuma a lokaci daya.

“Tsarabar me zan miki idan zan dawo?”

Nan ma bata ce komai ba, sai ya dagota a hankali ya kalli kyakkyawar fuskarta yana murmushi.

“Sarkin kuka har da yau kukan kike so ne? Yau fa ranar farinciki ce”

Ya fada yana kai rage tsawonsa ya kai hancinsa saitin nata ya goga mata a hankali, har lokacin idanuwanta a rufe suke.

“Zan je na yi sallama da Kaka..”

Shiru tai tana sauraren sautin tafiyarsa har ya fice daga dakin sannan ta bude idonta sai ta durkushe zaune wasu hawayen masu zafin gaske suka sauko mata. Makomarta take hangowa, ta yi aure auren da Baba da Inna suke da addu'a da burin gani yau ta yi, a lokacin da mutuwa tai mata yankan kauna, kuma auren ya zo mata a baibai ta fuskar data kasa fahimtar ina suka dosa, wani irin zama za su yi kamin komai ya zama daidai? Anya ma komai zai zame mata daidai? Bayan rashin iyaye da rayuwa mai kyau, yanzu kuma kaddarar aure ta bude mata sabon shafi.

“Allah ka taimake ni, ba ni da kowa sai kai Allah, ba ni da gata sai naka Allah, rayuwata tana tafiya a yadda alkalamin kaddarata ya tsara komai, Allah ka yaye min bakincikina ka kuranyen min damuwata, Allah karka jarrabe ni da abun da ba zan iya dauka ba, karka jarrabe ni da abun da zai saka na butulce maka”

Ta roka tana daga hannayenta sama sannan ta shafa addu'ar a fuskarta tare da hawayenta. Tana dukushe a gurin har ya gama abun da zai yi a cikin gidan ya fito, daman tun kamin ya saka Kaka ta kira masa Aminatu ya fada mata cewar ba da ita zai tafi ba, sai ya fara zuwa ya dawo tukuna. Tana jin lokacin da suka iso bakin kofar dakin Kaka na masa addu'ar Allah ya tsare yana amsawa da Ameen, sai wani sabon hawaye ya fara sauko mata wannan karon ba na tunanin makomarta ba ne, na nisantarta da Talba zai yi ne, haka take ji a can lokacin da zai tafi a yau ma haka take ji, saboda tana jin sa kamar wani bangare na rayuwarta, ko kadan bata son yayi nesa da ita. Da kansa ya shigo dakin ya tsaya gabanta yana kallon fuskarta.

“Kuka dai? Ni ko kin ga ban shiri da mai kuka”

Ta yi saurin saka hannayenta ta share hawayen, sai dai hakan be hana su zuba ba, murmushi yai saka nasa hannayen ya rike fuskarta yana share mata sauran hawayen, ganin sun ki tsayawa yai yunkurin rumgumeta, sai dai shigowar Kaka dakin ta dakatar da komai cikin har da saurin dauke hannunsa a fuskarta. Kafafuwanta kawai kake take kallo so take ta gano idan Talba ya taba ba, domin bayan ta kawo ta ta tafi hankalinta be kwanta ba, tana jin kamar zai iya aikata wani abun ya tafi ya bar mata ita daga karshe ma yace ya sake ta.

“Me take yi ma kuka?”

Kallon Kaka yai kamin ya sake kallon Aminatu.

“Bata son na tafi”

“Allah yasa dai ba wani aika aikar kai ba, ka tafi ka barta”

Kaka ta fada tana daga zanenta ta duba kafafuwanta.

“Ku yan birnin nan lamarinku da wahala yake, ni ma ai na yi wauta da na bar maka ita”

“Lokacin da zan aikata ba ki isa ki hana ba, domin matata ce ko a gabanin zan iya komai”

“Allah dai ya tsare yasa babu abun da ya shiga tsakaninku, ke ya miki wani abun?”

Kaka ta tambayi Aminatu, sai ta girgiza mata kai alamar aa. Kaka ta kyale ne kawai ba dan ta gamsu ba, taja hannunta suka nufi kofar fita sai Aminatu ta juyo tana kallon Talba daya biyo bayansu, suna fita daga cikin dakin Kaka ta nufi bangarenta da ita sauran mutanen gidan kuma suka rako Talba har gurin Motarsa suna masa Allah ya tsare, sai a lokacin ma ya tuna da Ali dake zaune cikin tasa motar yana jiransa gaba daya ya manta da shi. Ali na ganin abokinsa ya fito daga tasa motar ya nufo inda Talba yake tsaye.

“Kana can gurin Amarya ka manta da ni”

Talba yayi murmushi.

“To ai dole kai hakuri da ni, ni ma yanzu mai iyali ne”

“Na fika sani, ni da nake da yara ma na rigaka jindadin aure ai, domin ko a yanzu baka da maraba da gwaro, kai da zaka tsere ka bar amarya, kuma wanda ya auri kwaila ai be more aure ba”

“Malam baka san sun fi dadi ba? Kai zaka koya musu komai, amman manyan mata nan idonsu a bude yake sun san komai jikinsu har rawa yake su taba ka”

Ali ya mika masa hannu suka taba suna dariya.

“Talba ashe kai ma A ne”

“To in ba iskanci ba ni zaka fadawa Mace, ni da nake da Leila”

Ali ya bata fuska.

“Matsalarka ke nan, baka da makiyiya Irin Leila, bayan duk cin amanarta da kake a yanzu, gashi har ka yi aure bata sani ba”

“Kai kasan da Leila na aura na fada mata cewa ba zan nuna ta a gurin dangina ba har na wani lokaci da na shiga uku, amman wannan ko magana kasan min ta yi, but i know one thing for sure yarinyar nan tana so na, domin da Kaka taja hannunta za su fita waigena kawai take kamar tace min kar na tafi”

“Daman wace mace ce zata ce bata sonka? Look at you my friend komai ya ji, ai zaka yi tsada sosai shiyasa kake yi ma Leila yadda kake so”

“Take min yadda take so dai, and now komai is over ba zan sake daukar rainon wayonta ba”

Ali ya masa wani kallo.

“What do you mean? Dan ka auri yarinyar ka yi ha'inci Leila kuma yanzu kace zaka bullo da wani abun nooo ba zan bari ba Talba, be kamata ba, ba zan iya saka maka ido ka cutar da Leila ba”

Talba kallonsa yake da wani tunanin na dabam.

“Kai abokin Leila ne kenan not me”

“Ni abokin ka ne? But i won't let anything or anyone hurt her ko da kai ne so karka ce zaka yi mata wani abun just because of ka auri yarinyar nan, bayan kuma kasan idan ta sani zai iya jefata a damuwa, Allah ya tsare hanya”

Ali ya fada da iyakar gaskiyarsa sannan ya juya a fusace ya nufi motarsa, Talba binsa yai da kallo yana mamakin yadda abokin nasa yake zakewa da yawa akan Leila. Yana tsaye a gurin har Ali ya shiga motarsa yai mata key ya kama hanya, Talba yayi murmushin da dan mamaki sannan ya bude tasa motar ya shiga.

MADINA POV.

A firgice ta farka har haki take kamar wanda ta kwato numfashinta da karfi, ta hada wani uban gumi kamar babu ac a falon. Hajiya dake rike da wayarta ta kalleta

“Lafiya?”

“Hajiya Mafarki na yi, mafarki na yi Talba yayi aure ya auri yarinyar nan da na kawo gidan nan”

Ta fada kai tsaye idonta na cika da kwalla kamar ta manta a gabanan mahaifiyarta take.

“To sai me? Ko mata hudu ya aura ma ina ruwanki?”

Ta kalli Hajiya a hankali hawaye na cika idonta.

“Ba saboda ni ba saboda Leila”

“Ba saboda Leila ba ne, daman na lura da take takenki, kuma ina kara jan kunnenki akan lamarin nan ki fita daga hanyar Talba! Ba zaki iya gasa da Leila ba, ba kuma zan bari ki lalata alakata da Mahaifiyarta ba”

Ta yi kasa da kanta hawaye ya sauko mata.

“Hajiya saboda Leila ne”

“Ai na sani, shiyasa daga gama sallah kika kwanta sai mafarkinsa”

Bata sake cewa komai ba, ta mike tsaye ta dauki Hijab din da tai sallah da shi ta nufi hanyar dakinta zuciyarta na wani irin zafi marar masaltuwa, ji take kamar ba mafarki tai ba, kamar gaske ne saboda yadda yanayin ya zo mata. Tana shiga dakinta ta maida kofar dakin ta rufe ta jingina da kofar ta fashe da kuka, mafarkin sai dawo mata yake tana ganin yadda Talba ya angwance cikin farar

shadda mai kyau gaske sai far'a yake ana ta shagalin biki, a dayan bangaren kuma Leila tana ta masifa amman ya dage sai yayi auren. Gaba daya sai ta ji tsana bachin rana ma saboda ta yi mugun kafarkin kuka tai sosai ta saka hijab dinta ta share hawayen sannan ta tashi ta isa gurin gadonta inda wayarta take ta dauka ta shiga Instagram ta nemi account dinsa ta makalle a ciki tana kallon hotunansa.
Sai a lokacin ta ji ta dan samu natsuwa, domin ta san yadda yake da kyau nan kuma yake ji da kansa abu ne mai wahala ya auri mace kamar Aminatu.

“Sherin mafarki ne kawai”

Ta fada tana jin zafin zuciyarta na karuwa, kamar wanda za'ayi ma kishiya. Ta fito daga instagram din ta dannawa number Leila kira, ring daya a dauka.

“Hello Madina”

“Na'am Leila ya kike?”

“Lafiya kalau”

“Leila kin yi magana da Momy akan dawowar yarinyar nan gidan nan? Ina ji miki tsiron abun da zai iya zuwa ya dawo domin zata iya dauke masa hankali ya fara zuwa can yana barinki ki daina ganin kamar bata da wani aji wani lokacin maza ba su da tabbas”

“Na yi magana da Momy na san kuma zata masa magana, dole zai dawo da ita gidan ko ba komai zan jidadin wulakantata a gabansa, kuma zan shiga tsakaninsu”

“Yayi kyau, yana gida ne?”

“No ya fita, wai ke baki san me?”

Leila ta kwashe komai ta fada mata. Madina ta mike tsaye da sauri ta nufi gurin windows din dakinta da mugun mamaki.

“Shiyasa ta wani bangaren ina jin tsoron kar a dawo da ita gidan nan ta goge yace zai aureta, na san be isa ya fasa aurena ba, amman zai iya cewa zai hada mu, ni kuwa ba zan taba tarayya da wata ba akan Talba, ko na shi ba ba zan yi sharing miji da wata ba”

“Idan ke zaki iya bari yarinyar ta waye ta goge irin gogewar da har zai iya furta cewar yana sonta balle har ta kai shi ga aurenta, ni ba zan yi wannan saken ba, ko kwalliya ba zan bari tai ba, kuma ba zamu dasa mata komai ba sai bakinciki, Leila ke wawuya ce Wallahi da ace ni nake da damar da kike da ita da yanzu komai ya zama labari”

Leila ta yi murmushi tana jin dadin yadda kawarta take daukar komai nata da zafi, musamman ta bangaren Leila.

“Ke ma kin san ai ba zan bari ba, kuma ina da ke hankalina a kwance yake, ban matsawa Momy har sai ya dawo da ita gidan nan In Shaa Allah”

“Haka yayi, kuma karki manta da maganar aikina, ko dai na cire rai wai?”

“Haba kawata, ki kwantar da hankalinki na miki alkawari cikin satin nan za a gama komai”

“Na gode, and lastly ya kamata ki saka ido akan mijinki fa, ki rika dauka kamar kin aure shi ne, ki rika sanin ina yake zuwa me yake zuwa yi”

“Madina kina yin abu kamar ba kisan wacece ni ba, ni ma fa na san kaina, ba rokonsa na yi nace ya aure ni ba, god forbid ba zan ma taba yin haka wa namiji ba, ina ma da ina da aji ba zan yi abun da zai zubar min da kima ba, idan ya fita can zai yi rayuwarsa dabam a cikin gidan nan ma zai yi yadda yake so, abun da kawai ba zan dauka ba shi ne, ya auri wata bayan ni ko kuma kamin ni, dan haka ki daina wannan maganar”

“Leila ke nan, wata rana zan baki mamaki Wallahi, ke wai baki san soyayyah ba ruwanta da wani aji ba? Shi miyasa be duba nasa ajin ba yake ta kula yarinyar nan?”

“Wannan kuma ai dabam, ni dai ba zan iya zubar da kaina a gurin namiji ba, ni fa macece karki manta da wannan”

“Ni kuwa kin ga zan iya komai dan na samu abun da nake so, durkusawa wada ai ba gajiyawa ba ne”

“Ni dai ba zan iya ba”

Ta fada tare da kashe wayarta. Madina ta yi murmushi tana taba idonta daya kumbura saboda kukan da tai.

LEILA POV.

Tana aje wayar ta mike ta nufi gurin kofar dakinta da Amal take ta knocking. A fusace ta bude kofar domin Amal ta dade tana dukan kofar tana kwala mata kira.

“Kamar kina bina bashi zaki zo kina dukan kofar dakin nan mi ya faru?”

“Miye idan zaki yi waya sai kin wani rufe kofa, ki fito Ya Kabir yana kiranki”

Amal ta karasa tana murda mata baki, a take Leila ta kai hannu ta tura Amal baya, abun ka da tiles sai Amal ta zame a gurin ta fadi kasa hannunta ya bugu da tile din. Kamar wata karamar yarinya haka ta bude baki ta fashe da kuka ita ala dole auta ce, ta tashi ta nufi hanyar dakin Momy, sai Leila ta rufa mata baya, Yaa Kb dake kasa yana jin kukan Amal ya taso ya nufo upstairs.
Da kuka Amal ta tura kofar dakin Momy ta shiga.

“Momy kin ga Leila ta ture ni na fadi saboda Ya KB yace na kirata”

Momy ta kalli Leila wanda ta shigo dakin da saurinta.

“Momy zuwa tai ta rika dukar min kofar daki kamar na ci bashinta kuma ta karasa min magana tana murguda min baki”

“Leila mi yake damunki ne? Miyasa idan ranki ya bace ba zaki iya controlling kanki ba? Har da yar'uwarki ba ki bari ba? So kike ki tureta ta fadi ta mutu kamar yadda kikai wa Baaba ko kuma kareta kike son yi? Ki duba halin sa kika jefamu saboda bakar zuciyarki, yanzu kuma yar'uwarki ba zaki shafa mata lafiya ba?”

“Amman Momy ai kin san halin Amal”

“Saboda na san halinta sai na bari ki ji mata ciwo?”

“Ita ma Baaba ba da gangan na aikata ba”

“Da sunan ba da gangan ba, Allah kadai ya san abun da kika aikata a gidan nan da wanda kike shirin aikatawa, ya kamata ace kina iya controlling kanki dai”

Leila bata sake cewa komai ba ta juya ta bude kofar dakin zata fita sai tai arba da Kabir a tsaye, kamar an zuba mata ruwan zafi a jiki haka take fatar jikin ma saukowa kasa saboda tashin hankali arba da tai da Kabir.

“Shiga ciki”

Ya fada yana mata wani shegen kallo, sai tai baya baya wanda hakan ya bashi damar shigowa, sai ya maida kofar dakin ya rufe ya kalli Momy dake rike da hannu Amal.

“Ashe ke nan Baaba ba bata tai ba, Leila ta kashe ta, kuka kaita wani gurin kuka jefar ko kuma kuka binneta”

Momy ta saki hannun Amal ta mike tsaye tana kallonsa.

“Wace irin magana ce wannan kuma?”

“Momy na ji komai, kuma abun da kuka aikata be kamata ba, saboda gudun a hukuntata zaki biye mata ku aikata son zuciya? Kuma ku bar bayin Allah iyalanta da zullumin nemanta da tunanin inda take? Rai fa ta kashe Momy rai”

Ya furta a fusace yana jin kamar ya hade zuciya saboda bacin rai.

“Ni ban kashe ta ba, ban ai...”

Bata karasa ba wanke mata fuska da mari.

“Wawuya, sai yanzu na fahimci dalilin daya saka Talba ya tsane ki, baki da zuciya mai kyau Leila, dan'uwana be cancanci aurenki ba Wallahi”

Momy ta daka masa tsawa.

“Kabir.. Karka manta alakarka sa Leila tafi alakar dake tsakaninka da Talba, wannan jininka ce, uwa daya uba daya, kuma karka kuskura ka bar maganar nan ta fita, idan wani ya ji maganar nan ban yafe maka ba!”

Ta mugun mamaki ya kalli Momy ya nuna Leila kana ya nuna kansa.

“Momy saboda Leila ta aikata kisan kai zaki ce ba ki yafe min ba? Wani irin so kike yi ma Leila ne? Kin goyi bayan abun da ta aikata kenan fa!”

“Irin son da nake maka, shi nake mata, fita ka bar min daki”

Momy ta fada tana nuna masa kofa, juyawa yai da sauri ya fice a fusace, fusata iri ta mamakin da bakinciki yadda Momy ta goyi bayan Leila. Sai da Kabir ya fice sannan Momy ta kalli Leila.

“Ki cigaba da abun da kike, har ta kai Talba ya ji maganar nan yanzu dai kin yi nasara Kabir ya ji, sai ki zuba ruwa kasa ki sha”

Leila ta share hawayenta tana hararar Amal.

“Yanzu ma ai Amal ce taja komai, da babu wanda zai ji”

Amal dai bata ce komai ba ta mike tsaye ta nufi kofar fita ta fice daga dakin. Downstairs ta nufo tana saukowa rike da hannunta domin har lokacin tana jin zafin buguwar da tai, bata karasa saukowar ba door bell din falon tai kara, yanayin yadda aka danna door bell din ta gane cewar Ya Talba ne, sai ta karasa kofar da saurinta ta bude masa.

“Wow Ya ka yi kyau kamar ango”

Ta fada tana kallonsa sama da kasa, bata fadi karya ba domin yayi kyau sosai fuskarsa sai haiba take, yana rike da babbar rigarsa a hannu dayan hannunsa kuma rike da hula.

“Da gaske?”

“Eh Wallahi ka yi kyau, Ya ina kaje?”

Tsayawa yai cak yana kallonta sai kuma ya juya ya fice ba tare da yace mata komai ba, kai tsaye ya nufi bangarensa, yana shiga ya canja tufafin jikinsa sannan ya fito nufi bangaren Momy.

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Momy ta tsayar da cin abincin da take ta kalleshi.

“So...?”

“Ina son na dawo da ita nan, saboda ta samu ilmi da kula, kin ga can kauye ne, rayuwarta zata fi kyau a nan”

Wani kalar dadi ne ya lullube Leila jin an tabo mata inda ke mata kaikaiyi, sai dai bata yarda ta nuna ba gudun kar Talba ya zargi wani abun.

“Miyasa kake tunanin zan iya zama da mace da tai sanadin mutuwar aurena? Just because of kana son taimakonta sai ka kawo ta nan? A can kauye babu makaranta?”

“How tai sandiyar mutuwar aurenki?”

Leila ta tambaya da kanka.

“Idan har zaki hukunta wani akan hakan it should be Talba not her, domin bata cikin gidan ma lokacin da abun ya faru”

“Kar so ya rafe miki ido Leila”

“Idan har so zai rufe min ido, ai laifinta zan gani bana Talba ba, kawai ina fadar gaskiya ne, idan baki son ta zauna a gidan nan ba laifi, amman dora mata laifin da be shafeta ba shiga hakkinta ne”

Ba Momy kadai ba har Talba kallon mamaki yake mata, domin bata taba gwada yi ma wani haka ba. Bata taba yabawa wani da yake kasa da ita ba ko da kuwa shi ne da gaskiya. Kabir M kallonta yake yana tunanin kalamanta.

“Shi ke nan, sai ka yi magana da Daddynku idan ya amince ba ni da matsala”

Momy ta fada tana mikewa tsaye taja kujera baya ta sauka ta nufi hanyar upstairs. Leila ma tashi tai ba tare da ta kalli kowa a cikinsu ba ta bi bayan Momy.

“And do you really think Leila da zuciya daya tai maganar nan?”

Kabir ya fada yana kallon Talba, Talba ya dan tabe baki.

“Bana ji, amman mi zai saka ta yi haka?”

“I don't know, amman bana son ka yi abun da zai cutar da kai da kuma ita yarinyar, if possible ka barta a can kauyen ta zauna, besides ta samu iyali a yanzu then miye na takura kanka sai ka kawo ta nan? Ko aurenta kai?”

Talba ya masa wani kallo, na mamaki. Sai yai murmushi.

“Na ga ranar daka dawo ka saka fararen kaya, har da babban riga a hannunka kuma a tarihin rayuwarka baka taba saka babbar riga ba”

Talba yayi murmushi.

“Ka gan ni ko kuma dai Amal ta fada maka”

“Trust me na ganka, domin ina harabar gidan lokacin daka shigo”

“Saboda na saka babbar riga sai ka fara zargin na yi aure? Taya zan yi aure Momy da Daddy ba su sani ba”

“I don't know”

Kabir ya fada yana mikewa tsaye. Talba ya bishi da kallo har ya fice sannan shi ma ya tashi ya nufi sofa din falon ya yana kokarin ciro wayarsa ya kira Daddy.

“Hello Daddy”

“Mu'azz ya kake?”

“Lafiya kalau, Daddy kana office”

“Yeah akwai matsala ne?”

“No gani dai zuwa”

“Okay”

Yana sauke wayar ya mike tsaye ya fice daga falon cikin natsuwa yana wani irin tafiya kamar wanda baya son taka kasa. Ya kusan minti biyar zaune a cikin motarsa sannan ya yi mata key, kamin ya isa gate din har masu gadin sun bude masa. Be faka ko'ina ba sai gaban katon kamfanin ya bude kofar ya fito ya doshi hanyar da zata sada shi da office din Daddy. Sai da akai masa iso sannan ya shiga bayan yayi knocking sau daya.

“Daddy ina da bukata daya a gurinka”

Ya fada tun kamin ya zauna.

Daddy ya mika masa hannu suka gaisa

“Ina ma ina da abubuwa biyu da zan fada maka, the first one is request the second one kuma abun da kake nema ne ya samu”

Fuskar mamaki Talba yayi.

“You go first...”

Daddy yayi murmushi.

“Na farkon Leila ce ta kawo min kararka, wai tana son ka dauki kawarta Madina aiki kaki, ni kuma na ce zan maka magana, a kawancensu da Madina be kamata a kasa sama mata gurbi a gurinka ba”

“Wannan ba matsala ba ce Daddy, zan yi magana da Pa na In Shaa Allah cikin satin ma zata fara aiki, fada min daya”

“Sai ka bani goro, domin ka dade kana jiran zuwan wannan ranar”

Talba yayi murmushi mamaki, ya fara canke canke, har wata zuciyar na raya masa ko dai Kaka ta kira shi ta masa wata maganar ne!

“Momy ka ta yi min magana akan cewar be kamata a zuba muku ido, ita kanta Leila ta fadawa Momy cewar a yanzu ta shirya, and daman nasan abun da kake nema ne, dukanku kun mallaki hankalin kanku kana da aiki zaka iya komai ita ma kuma ta gama karatu ban san zaman jiran me kuke ga a yanxu”

“So...”

Ya tambaya gabansa na dan faduwa.

“Mun yanke shawarar saka muku rana, amman nace sai na fara magana da kai na ji lokacin da kake so”

A take Talba ya nemi annashuwa ya rasa, yana jin kamar be shirya auren Leila a yanxu ba, bayan kuma da can abun da yake ta nema ne.

“Amman Daddy ita Leila da kanta tace ta aminta? Bana son ayi forced dinta ne!”

“Karka damu, idan bata aminta ba Mahaifiyarta ba zata fadi haka ba, kasan yadda take son Leila ai, i don't think tana son ku yadda take son Leila”

Talba ya dauke kansa yana kallon wani gurin daban, not happy and sad, ya samu kansa a cikin wani yanayi mai wuyar fassara.

“Mu'az”

Daddy ya kira sunansa yana kallon yanayinsa. Sai ya juyo ya kalli Daddy yana murmushin yake.

“Allah ya tabbatar mana da alheri Daddy, duk date din da kuka saka yayi daidai”

“Mu saka kusa ko nesa?”

Still Daddy na reading reaction nasa.

“Kusa”

A kokarinsa na kawar da zargi ya amsawa Daddy yana murmushi. Daddy ma yayi.

“Good domin be kamata kai azumi ba mata ba, ga azumi ya kusa”

Ya yi ma Daddy murmushi as respond sannan ya mike tsaye ba tare da ya fada masa abun da ya kawo shi ba, gaba daya maganar da Daddy yai masa ta saka ya manta.

“Baka fada min maganar ba?”

Sai ya dawo ya zauna.

“Daddy Kaka ta kira ka ne?”

“Aa akwai wani abun ne?”

“No daman saboda yarinyar nan ne... ”

Ya gabatarwa Daddy da bukatar, sai dai wani bangare na zuciyarsa na raya masa ko dai Daddy ya san da maganar auren ne shiyasa ya bullo masa ta wannan sigar ya ga iya gudun ruwansa! Be gama bawa kansa amsawa Daddy ya amsa masa.

“Ba matsala, daman can ko ba yar'uwa ba ce ai tana da yancin zama a gidan balle kuma tana jininka, ba wata matsala, zan yi magana da Momynka”

“Sai da na yi magana da ita sannan na zo nan, tace min ba matsala”

“For the first time yau ka fara sirri da ita kamin ni, I'm jealous”

Talba yayi murmushi domin ya san halin Daddy da zolaya. Sannan ya sake mikewa tsaye ya nufi gurin da fridge din Daddy yake ya bude ya dauko gorar ruwa.

“Sai ka shigo Daddy”

Daddy ya daga masa kai yana murmushi, shi kuma ya fice rike da ruwan. Be sha ba sai da ya shiga motarsa sannan ya balle murfin ya daga gorar ya kai bakinsa be sauke ba sai da yai rabin gorar sannan ya sauke gorar yana haki.

“Abubuwa biyu lokaci daya!”

Ya furta yana yi ma motar key, at first gida ya nufa sai kuma ya canja hanya ya dauki hanyar da zata kai shi gidansa. A gaban gidan ya faka motarasa ya fita ya nufi gate din ya bude sannan ya shiga motar ciki ya dawo ya rufe gate din.

LEILA POV.

Tana shiga dakin Momy ta zauna kusa da ita tana fadin.

“Momy i thought mun yi maganar nan da ke, sai kuma gashi ya bukata da kansa miya ba zaki yarda?”

Momy ta kalle.

“Baki da wata magana sai ta Madina, duk abun da Madina ta dora ki akai shi kike, ko da abun nan ba mai kyau ba ne”

“Madina ma ba zata dora ni a wani abu marar kyau ba, kawata ce i trust her, shekara nawa muna tare”

“Fine ranar da zata baki mamaki karki nemi taimakona”

“Haka ma ba zai taba faruwa ba, ya maganar aikinta kin fadawa Daddy?”

“Eh na masa magana, kuma na masa maganar aurenku”

“Aurenmu as how Momy?”

“Nace a saka muku rana, ban san abun da kike jira ba, kina ta bin shawarar zuciyarki, kin gama karatu shi ma kuma yana aiki, to jira na me? Da can ina goyon bayanki amman a yanzu kam bana goyon bayan zaman da saki yi ta yi, domin na lura shawarar Madina kike bi, har yanzu kin kasa fahintar Cewar tana son Talba ne”

Leila ta mike tsaye da sauri tana kallon Momy.

“Momy idan kin tsani Madina ba wani abu ba ne, amman abun da kike jifan Madina da shi yanzu ba zai taba faruwa ba, na san wacece Madina, har abada ba zata taba min abun da kike tunani ba”

Momy kallonta kawai take domin ta lura ba karamin fusata tai ba saboda furucin Momy, ba lallai ne ta fahimta ba balle har ta yarda.

“Ni ban shirya aure yanzu ba?”

“Sai yaushe? Sai ranar da zata yi?”

“Momy please you parents should know your limits, Momy ku ma fa kun yi na ku zamanin haka bata faru, Wallahi a waje ba ayi ma yaya haka, kowa yana da right dinsa”

Momy ta kalleta da kyau.

“Kin manta cewar mu musulmai ne? Kuma idan kin yi karatu a waje that's was before, yanzu kuma kina a nigeria a nigeria ma a zamfara, kuma ke bahaushiya ce karki manta da wannan”

“Na san duk wannan amman ni kuna tauye min hakki, ko da yaushe Talba ne mai gaskiya shi ne mai yanke hukuncin komai, a duk lokacin daya bukaci aure ko wani abu ana bashi kai tsaye, na san shi zan aura, amman ni ma fa ina da right Momy, ku rika min adalci”

“So yanzu dai baki shirya auren ba?”

Momy ta tambaya tana daka mata tsawa, sai ta dauke fuska tana jin bacin ranta yana karuwa.

“I'm not ready gaskiya, or i will think about it”

Tana kawai nan ta juya a fusace ta fice daga dakin kamar walkiya. Dakinta ta shiga ta dauki key din motarta ta yar karamar jaka da wayarta ta fito, daman abu ne mai wahala ka ganta da mayafi idan ma ta saka to ba wai wuce karami ba irin wanda zai tsaya daidai wuya. Yanayin yadda take saukowa daga stairs din ma kadai ya isa ya sanar da bachin ranta, Mairo dake aikin gyara dinning dinbda suka ci abinci sai kallonta take kasa kasa. Da karfi ta bude kofar falon ta fita, kamar an biyota haka ta isa gurin motar ta bude ta shiga, tsakanin hannunta da jikinta ba zaka iya tantance mai fiskar wani ba.
Masu aikin bude gate din gidan sun karanci halinta fiye da kowa a gidan, macece mai matukar wulakanci idan ka shiga konarta, ga ji da kai da daukar kowa ba komai ba, ita dai a idonta kowa kaskastacce ne. Hakan yasa suka bude gate din da sauri tun kamin ta iso, kamar an rubuta cewar Leila kadai akai yi wa wannan titi haka ta rika gudu zuciyarta sai tafasa take. Kamin ta isa gidansu Madina ta cikawa bakinta da iska tana furxarwa ya kai sau goma.
Sau hudu tana danna horn sannan aka bude mata gate din, wani banzan kallon ta watsawa direban cox he got lucky ba a gidansu yake aiki ba da yau sai ta wulakanta shi. A inda ta saba aje motarta ta aje sannan ta dauki wayarta ta kira kawarta Madina, domin sai a lokacin tana doubting tana gida ko tana gurin aikinta.

“Ki shigo cikin gida mana na ga fakin dinki”

Shine abun da Madina ta fada bayan ta amsa kiran, dai Leila ta kashe wayar ta bude motar ta fita ta rufe ta nufi kofar falonsu, tun kamin ta karasa aka bude mata kofar falon, da wata yarinyar kirkice ko a fuska zata yi ma wacce ta bude

mata kofar godiya, amman bata kula ta ba sai ta nufi dakin da Madina take, daman idan ta shigo cikin gidan Hajiya kawai take iya gaisarwa, su kansu kannen Madina har sun saba da yanayinta, ko ba su ba abu ne mai wahala Leila ta ganka a wani gurin tai maka gaisuwa, matukar ba abokin Daddy ko Momy ba ne, su ma kuma ba kowa ba.
Tura kofar dakin tai ta shiga, sai ta samu Madina zaune tsakiyar gado tana duba wasu manyan yan kunne masu matukar kyau.

“Miye haka?”

“Ina zabar wadanda zan siya ne before birthday na”

Ta tabe baki sannan ta zauna gefen gadon.

“Madina yau Momy ta yi min abun da zan dade ina bakinciki”

“Me kuma ya faru?”

“Wai ta fadawa Daddy na ce ina son ayi fixing date din aurenmu da sarkin jin kan nan...”

Wani irin bugawa zuciyar Madina tai, har sai da shiga da fitar numfashinta suka samu tangarda na dan dakiku.

“What...aurenku?”

Ta tambaya tana tuna mafarkin da tai, ashe ba Aminatu tai ma ba Leila tai ma.

“To miye matsalar haka?”

Ta tambaya tana hade yawu da karfi, gaba daya sai jikinta yai weak.

“Haba dai, yanzu zai fara min kallon ni na fara magana fa”

Madina ta kama hannunta hawaye na cika idonta.

“Leila karki ce aa, kawai kin karba ki barwa Allah komai, you got lucky kina da mai son kuma kike so kamar Talba, ji da kai na me Leila? I'm always telling you this kina da dama a yanzu karki yarda ki rasa ta”

Ta karasa na sauko mata, sai ta goge tana murmushi.

“Ji yadda nake farinciki daga jin wannan labarin kawai, ina ga kuma na ga lokacin”

Ta karasa tana fashewa da kuka sai tai saurin rumgume Leila, ta karawa kukanta kuzari da muryar da Leila ba zata iya ji ba.

“Haba dai, Madina kin san fa waye Talba, babu irin zubar da kaina da ban yi ba akan shi, babu kalar Soyayyar da ban nunawa ba bawon Allah ba amman yana min jin kai, ni kuma a yanzu na fishi jin kaina, at least ya kamata ya san na banbanta da sauran mata, amman haka da Momy tai min zai saka ya raina ni kuma yai tunanin na mutu ne akansa”

Madina ta dago daga jikinta sai dai hawayen dake zuba a idonta ba su daina bin fuskarta ba.

“Ki manta da komai, ki kaddara a yanzu wata sabuwar rayuwa za ku fara, Talba zai daina duk abun da yake idan kuka yi aure, kuma duk wani ji da kai zai aje shi gefe, irin wadannan mazanje, suna kula da matansu fiye da tunanunki, kuma basa bawa matan waje fuska, karki watsawa Momy kasa a ido, kin isa aure Leila ba zan boye miki ba kuma kina da wanda kuka dace da juna”

“Miyasa kike kuka?”

Leila ta tambaya ganin hawayen dake zuba a idon Madina yaki tsaya mata. Sai Madina tai saurin share hawayen tana dariya.

“Look at you my girl, kawata zata yi aure ta bar ni, ofourse abun farinciki ne, amman kina tunanin zan jidadi ne?”

“Ke ma dai kamar ba ki san ni ba, idan fa na kafe akan abu daya na dafe kenan, zan tsaya na ga gudun ruwansa, amman ba zan yarda ajina ya zube ba, ke da Momy kun kasa fahimtata”

“Na fahimce ki Leila, kawai bana son na doraki akan turbar da zan zo ina nadama ne ni da ke, but i promise myself zan yi fighting ma abun da nake so har sai na samu cikar burina, ke kawata ce for more than 26 years ba zan iya cutar da ke ba”

Leila ta yi mata kallon rashin fahimta, gaba daya a bayanin da take mata a baibaiye yake babu abun da ta fahimta, gashi sai hawaye take.

“Fight for what?”

Madina ta yi saurin share hawayenta ta hade yawu tana kokarin kawarda maganar.

“For Alakarku da Talba! Mutumen nan yana son ki, ana da kokarin hadaku sai wani botsewa kike, so. Dole sai na yaki wannan zuciyar taki kamin na samu kanki ki amince”

Ta karasa tana kai hannu ta taba kan Leila tana dariyar yake. Leila ta wara ido tana daga hannu sama.

“Wayyo Allah, da na san ke ma goyon bayan Momy zaki yi da ban zo nan ba, i need to go somewhere inda za a fahimce ni ace yes Leila abun da kike shi ya dace”

Tana fadar hakan ta mike tsaye.

“By the way, na yi ma Momy maganar aikinki, ita kuma ta yi ma Daddy ki saurare labari mai dadi soon”

“Awwww Thank you”

Madina ta yi saurin mikewa tsaye ta rumgume tana murmushi, a yayinda fuskarta ta sauka a kafadar Leila sai wasu hawayen suka zubo mata masu kama

da na bakinciki kuma ba bakinciki ba, sai tai saurin saka hannunta ta share hawayen sannan ta dago sai ta kasa hada ido da Leila.
Leila ta mata kallon rashin fahimta, domin bata taba ganin kawarta a irin wannan ba.

“Kamar dai akwai abun da yake damunki kamin na shigo? Can we talk”

“No babu abun da yake damuna, ai kin san bama boyewa juna komai, kawai dai ina jin kamar karki tafi ki bar ni ne”

“Waya ce tafiya zan yi na barki? Mtschee”

Ta dauki jakarta tana kara jan tsaki Madina ta bita da dariya, Leila na ficewa Madina ta fadi zaune saman gadonta not knowing what to do, sai kawai ta fara kuka, if har Leila ta auri Talba ta san ita kuma ta rasa shi, amman miyasa ta fada kaunarsa tun farko bayan tasan haka zai iya kawancenwa?

“Miyasa? Why from first place?”

Ta tambaya da karfi tana fashewa da kuka tare da saukowa saman gadon ta zuba kasa tana jin zuciyarta na mata wani mugun zafi marar misaltuwa. Ta saka duka hannayenta ta dafe fuskarta, tana ta kokarin gano dalili, even if ba Talba ba be kamata ta kamu da son saurayin kawarta ba right? Amiyarta wanda ta bata dukan amanarta!

“Ban yi laifi ba, duk macen da tai arba da Talba dole zata so shi, ba laifina ba ne laifin zuciyata ne”

Ta bawa kanta amsa tana girgiza kai, sai kuma ta tashi ta shiga bandaki sai amai, duk abincin da ta ci a ranar sai da ta amaye shi tana jin kamar har da zuciyarta zata amayar, bayan ta gama ta daura alwala ta fito ta shimfida carpet ta fara sallah nafila, tana kuka idan tai raka biyu sai ta sallame ta sake dorawa ta sallame ta sake yi haka ta jera nafila har aka kira La'asar, zuciyarta na mata zafi tana jin kamar ba zata kai anjima ba.

LEILA POV.

Yadda ta shigo gidan cikin natsuwa ba zaka ce ita ce ta fita a dazun cikin bacin rai ba. Kusa da kofar falo ta faka motarta ta bude ta fito tana kallon Kabir dake zaune kan kujerun dake kusa da kofar falon yana danna wayarsa. Ta ji faduwar gaba da kunya musamman ma da ta lura da ya zuba mata ido yana kallonta kamar wata bakuwar gidan. Har ta kai hannu ta danna door bell din kofar falon sai kuma ta juyo ta dawo ta zauna kusa da shi amman a dayan kujerar without looking at him.

“Na san haushi na kake ji, amman abun da na aikata ba wai na yi da niya ba ne”

“Me hakan zai canja? Kin san abun da ya fi bata min rai? Yadda kuka bar iyalin matar nan a cikin zullumi da tunani a Kullum, and look at you kina rayuwarki normal babu damuwa, and now god has blessed you with good friend Madina mace mai kirki not like you, and still Allah zai baki Talba a matsayin miji, kamilin mutun mai kirki”

Tun da ya fara maganar har ya gama be kalleta ba, harabar gidan kawai yake kallo.

‘Shi ma ai ba wani kyau hali ne da shi ba, sai ji da kai da nunawa mutane isa’

Ta fada a ranta tana hararsa, azahiri kuma sai ta mike tsaye ba tare da tace masa komai ba ta nufi door bell din ta danna aka bude mata ta shiga ciki..

BATURIYA POV.

Tun da akai mata aikin cirar cikin bata sake lafiya ba, yau kusan kwana hudu kenan, jiki ba karfi yawun baki sai tsinke mata suke kamar mai cikin. Sai dai duk da haka ba ta fadawa Umma komai ba, kawai ta fake da ciwon mara ne kawai idan aka ce ta tafi asibiti bata yarda wani ya raka ta sai dai ta fita ita kadai da sunan zuwan asibiti, sai ta zagaya ta tafi gidansu Ramlee, idan ta dawo sai tace likita yace ba wata matsala. Sai duk abun da take Umma na lura da ita da kuma yanayinta, hakan yasa ta titseta kai tsaye da abun da take zargi.

‘Okay Dear Allah ya kaimu ya tsare hanya i will miss you’

Tana ba shi amsa Umma ta jefa mata wata tambayar.

“Wai Rafi'a ko dai zubar da cikin nan kika yi?”

Baturiya ta dago da sauri daga chat din da take da Fahat ta kalli Umma.

“Zubar da ciki kuma? Haba Umma sai kace wanda tai cikin shege?”

Umma ta duba da irin duban nan na uwa da ya wanda babu wasa a cikinsa

“Karki maida ni karamar yarinya mana, ina lura da yanayinki”

Ta yi Shiru kamar mai saka abun da zata ce, can kuma ta dago ta kalleta a raunane kamar zata fasa kuka.

“Ba zubarwa na yi ba Umma, zubewa yai”

“Watan shi nawa?”

“Biyu da kwana shirin da uku”

Umma ta sauke ajiyar zuciya.

“Da sauki tun da ba a busa masa rai ba, amman karki sake, tun da ba cikin shege ba ne”

“Umma gani na yi idan ma na bar cikin wahala kawai zan yi, tun da ba kula zai yi da ni ba, kuma zan yi ta fama da dawainiya da abun da na haifa har sai na yaye sannan na yi wani auren, wani ma idan ya ji cewar kana da yaya biyu ai ba zai aureka ba, amman yanzu kin ga har na cika iddata”

“Ni ma na yi miki wannan tunanin, sai dai tsoron shiga hakki yasa ban miki maganar ba, kin tabbatar dai ba a isa busa masa rai ba ko?”

“Wallahi Umma ba a busa masa ba, ai da an busa ni ma ba zan aikata ba”

“Waya kaiki inda ake zubar da cikin?”

“Wata makociyar mu ce, dake can Maman Noor mijinta na yi shi ne na yi mata magana sai ya bani wasu kwayoyi kuma yayi min allura”

“Kin tabbatar cikin ya zube kuma ba wata matsala?”

“Ba matsalar komai, karfin jiki ne dai har yanzu bana ji, shi ma kuma da na fada masa yace soon zai daina”

Ta fada tana mikewa tsaye saboda kiran Alhaji na shigowa wayarta dake silent domin bata yarda ta amsa kiran wani namijin a gaban Umma, saboda ta san zata mata magana ganin tana cikin idda ne, duk wayar da take sai ta boye kanta a daki ko bandaki take iya amsawa, chat ne kawai take yi a gabanta shi ma dan tana da tabbacin ba zata leka wayarta ba.
Sai da ta maida kofar dakin ta rufe, sannan ta nufi bandakin ta shiga ta rufe kanta kana ta amsa kiran tana murmushi kamar tana ganinsa a fili.

“Haba Sahiba ta, da tsufana da komai ina ta kira ana min yanga?”

“Ba dole ayi maka yanga ba, tun da kai kake nema”

Dariya yai irin ta manyan maza sugar daddy sannan ya amsa mata.

“To na ji, yanzu yaushe zamu hadu, na zaku mu hadu da juna na yi marmarinki Wallahi, har tafiya nake da ita amman na fasa na tura na dana, kuma maganar zuwa na chine yana nan fa sai da ke zan je”

“Karka damu, zan kiraka gobe ina period ne shiyasa nake maka wala wala”

“Ohhhh amman ban jidadi ba, ba akwai dan abun da kuke sha ta dauke ba? Tsakani da Allah ina bukatar Baturiyar mata”

Ta yi dariyar jindadi.

“Zan sha ai, tun da ka matsa, idan ya tsaya min sai na kiraka”

“Yauwa haka nake so, zan aiko da na siyen maganin yanzu nan i love you”

Ya fada daga karshe yana kashe muryar.
Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Ya tabe baki yana kwance saman gadonsa wayarsa makkale a kunnensa yana sauraren dariyar da zolayar da Ali yake masa.

“Wato daman ance mai hakuri mawadaci,kai da kai hakuri sai Allah ya hada maka biyu lokaci daya, ka more abun ka”

Talba yaja tsaki domin shi be ga abun dariya a ciki ba.

“Kana da matsala Ali, kai baka duban irin matsalar da zan shiga? Ina da aure karkashin kasa, kuma yanzu za a kara min da wani a bayyane kuma matar nan fitinanniya”

“Sauki ne a gareka Talba, idan ka auri Leila zaka huta wani abun, kuma ita ma Aminatu zata samu zama a gidan cikin kwanciyar hankali, ka ga Leila tana gidanka kana controlling dinta Aminatu kuma tana gidan iyayenka, kuma bana jin zata samu matsala a gidan idan Leila bata nan”

“Leila tana da fitina ko bata gidan zata iya hana yarinyar zama lafiya”

“To yanzu ya zaka yi?”

“Ya zan yi kuwa, gani dai ga Allah”

Ali yayi dariya.

“An hada maka mata masu kyau da fara da baka, kuma lokaci daya”

Talba ya yanke wayar domin ya san Ali zai yi ta damunsa da zolaya ne kawai, kuma he not in the mood. Dan tsaki yaja ya shiga neman number Kaka, sai da ta kusa yankewa sannan Kaka ta daga.

“Salamu Alaikum”

“Kaka ina Matata?”

“Matarka gata nan tana cin abinci, ita kadai ka sani ban da ni”

“Eh mana, zan zo gobe na dauke ta”

“Ban gane ka dauke ta ba, haka nan kawai ake daukar amarya, ai sai ka fada mana muma mun shirya tukuna, kuma ai ba ita kadai zata je ba dole sai da yan rakiya, sai mun ga gurin zamanta”

Tashi yai tsaye yana kallon dakin nasa.

“Ban gane ba? Sai an rakota kamar ya? Sai kace dai ba ki san waye ta aura ba?”

“Idan na sanka sai na kyaleka ka zo ka dauki amarya ka tafi? Aa dole ne sai na ga inda za a aje ta kuma sai na rakata har dakinta ni da mutane na”

Talba ya daga kansa sama ya sauke yana shafa ya tare da cikawa bakinsa iska ya furzar.

“Na ji, amman kin san auren nan na yi shi saboda ke, ya kamata ki yarda da ni mana Kaka”

“Idan ban yarda da kai ba zan baka auren yarinyar ne? Na yarda da kai amman dai amarya ba zata tare a yanzu ba sai nan da wata uku”

Ya zare ido kamar tana gabansa.

“Wata uku kuma?”

“Eh haka muka yi da Hajiya Laraba”

“Kaka miya kawo Hajiya Hanne Laraba kuma a wannan maganar?”

“Wannan kuma tsakaninmu ne babu ruwanka, idan mun saka ranar da za a dauki amaryar zan fada maka”

“Tana kusa?”

“Ita wa?”

“Shalele”

“Eh amman ba zaka yi magana da ita ba yanzu!”

“Saboda me?”

“Idan an tare sai ka juyata yadda kake so”

“Gaisawa fa kawai zamu yi”

“Ai ko muryarta ba zaka sake ji ba, sai an tare”

“Kaka an daina fa wannan yayin, lafiyarta kawai zan tambaya ba wani abun ba”

“Lafiyarta kalau”

Duk yadda ya so yai magana da Aminatu Kaka bata yarda ta bata wayar ba, a haka sukai sallama be gaisa da Aminatu ba. Kansa ya dafe yana mamakin yadda Kaka take kokarin banbanro masa wani babban aiki.

“Tsohuwar nan ta cika rigima Wallahi, wani irun tarewa Fisabilillahi? Ni da nake zaton daukar mata kawai zan yi, amman yanzu ai tonon asiri ne”

Ya sauke ajiyar zuciya, sannan ya nufi kofar fita yana lalabar keys din motarsa dake aljihunsa. Sai da ya fara bude gate din sannan ya shiga motarsa ya fita da ita ya sake fitowa ya rufe gate din. Slowly yake driving har ya isa gida, haka nan kawai ya ji yana bukatar bata lokacinsa a cikin motar ba tare da aikin komai ba. After like 30 minutes ya bude motar ya fito yana kokarin rufe kofar Leila ta fito ta kofar Kitchen cikin shigar atamfa wanda dikin ya daye jikinta sosai ko'ina na surar jikinta a bayyane yake, hannunta rike da jaka da key da alama dai fita zata yi. Zagoyowa tai ta iso kofar falon tana jiran isowarsa. Tun da ya kalleta sau daya ya dauke kai be sake kallon inda take ba har ya isa gurin kofar sai dai yana ganin irin tsayuwar da tai ya san da magana a bakinta.

“Maganar auren da Daddy yai maka, Momy ta yi magana ne ba tare da sanina ba”

Kallonta yai.

“Really? Bayan kin furta cewar aure kike so yanzu kuma zaki tare ni a nan da wannan maganar? Why don't you talk to daddy about it? Wai kokarin nuna min isa kike a nan ko me?”

Wani banzan kallo ta watsa masa zuciyarta na mugun tafasa.

“Me kake daukar kanka?”

Ya matsa kusa da ita sosai har tana iya juyo saukar numfashinsa, yana kallon cikin idonta, kamar yadda ita ma take kallon nasa.

“Wani mutum wanda idan kika rasa shi zaki haukace ki shiga damuwa, wani namiji da ba zaki iya rayuwa babu shi ba”

Ta yi murmushi zuciyarta na mugun bugawa da karfi, kowanensu yana shakar kamshin turaren dan'uwansa.

“Ka yi kuskure, babu wannan namiji a duniya, wanda Leila zata ce ba zata iya rayuwa babu shi ba, amman akwai mazan da basa iya rayuwa sai da Leila, girman kanka na banza ne tun da har ka amsa cewar kana so na, ji da kanka na banza ne tun da har ka karbi tayin auren da Daddy yai maka da wuri haka, ko da yake samun mace kamar Leila a gurin aure wani abu ne mai matukar wahala”

Ya dan matsa baya.

“Mai matukar arha dai, musamman a gurin namiji irina. Kamin na manta ki sanar da kawarki ta samu aiki zata iya shigowa Monday”

Yana fadar hakan ya karasa gurin kofar ya danna door bell yaja ya tsaya, ita ma a tsaye take a gurin zuciyarta na mugun tafasa, tana kallonsa har aka bude masa kofar ya shige ciki. Kallonsa Momy take har ya karaso kusa da ita ya zauna tare da ciro wayarsa yana kokarin tabawa.

“Akwai wata matsala ne?”

Momy ta tambaya tana kallon yanayinsa dake nuna ransa a bace yake. Kamar mai jira sai ya dago ya kalleta.

“Momy a gaban idonki Leila za tai wannan dress din ta fita?”

“What wrong with it?”

Ya gyara zamansa yana mamakin Momy.

“Kayan fa ya kama jikinta sosai, and even dan Veil din nan da wasu suke sakawa da Leila bata sakawa”

Momy ta sauke ajiyar zuciya tare da cire gilashin idonta.

“Look Talba, karka bari sheidan yai tasiri a zuciyarka, ba yau Leila ta saba irin wannan shigar tana fita ba, miyasa yanzu kake son maida shi wata matsalar ne kawai”

Maida dubansa yai wani bangare na falon, yana jin sabon bachin rai na ta so masa wanda ya fi na Leila.

“Idan kana da matsala da Leila, ko kuma kana ganin ta yi wani abun da baka so, zaka iya samunta ku yi magana ku fahimci juna, amman ba ka kawo min kararta ba, aure fa zaku yi ku yi iyali idan ba ka iya fuskarta ta da magana taya kake tunanin zaku gina rayuwa”

“Momy kin fi kowa sanin cewar Leila bata jin magana ta”

“Ko kuma baka fahimtarta ba, irin rayuwar da kake son ka tafi da ita ba zai yiyu ba Talba, kai da ita dukanku kun yi karatu kun san rayuwa, miyasa ba zaka aje wannan girman kan ba ka bata kulawa yadda ya dace? Ba zai yiyu Leila ta zauna a karkashinka kamar baiwa ba, ta yi kokari na sani, babu irin juyin wainar da baka mata ba, wani gurin ma ita take da gaskiya amman sai na tirsasata yi maka biyayya saboda a samu zaman lafiya, sai dai na fahimci kai din ba canjawa za ka yi ba, na rasa abun da yake damunka, Leila tana iya kokarinta amman baka gani kuma duk abun da kake yi da gangan kake yi, ai lokacin da yarinyar ta zo ina kallon yadda kake kwantar da kai, yanzu kuma har nema mata sauki kai a gidan nan”

Uffan be sake cewa ba, har Momy ta gama zazzaga masa ta mike tsaye ta bar masa falon. Sai ya kai hannunsa saitin bakinsa yana wasa da lips dinsa. Abun da Momy tai masa a yanzu ya fi yi mata zafi fiye da wanda Leila tai masa, ko ba komai idan Leila ta fada masa goma zai iya fada mata ashiri, amman Momy be isa yayi mata wata maganar banza ba, a da can idan wani abu ya faru tsakaninsu Momy tana daukar bangarensa ne ta goya masa baya, duk da ya san bata son ganin Leila.

AMINATU POV.

A hankali take cin abincin tana sauraren wayar da Kaka take da Talba, bata ji ta fadi sunansa ba sai dai a yanayin yadda suke wayar ya tabbatar mata da Talba Kaka take waya, sai dai bata yarda ta dago ba sai da Kaka ta gama wayar tana kokarin zama kusa da ita.

“Ka ji mutum wai yana son magana da ke”

Aminatu ta sauke kanta kasa.

“Ai na fada masa sai nan da wata uku zai sake ganinki ko yayi magana da ke, har da wani maganar tarewa yake, sai kace yar roba aka aura masa, wai zai zo ya dauke ki ku tare, sai kace dai auren karuwai”

Nan ma Aminatu bata ce komai ba.

“Ba zan bari ku tare ba sai na kankaro miki mutunci, na yi waya da Hajiya Laraba tun jiya tace min zata zo ta tafi dake”

Sai a lokacin Aminatu ta bude baki.

“Wacece Hajiya Laraba?”

“Yata ce, ni na haifi abuta da kaina, amman acan Gusau take zaune a unguwar locos a can take aure har da yaranta, mai kudi take aure gidan ma mai kyau ne har da ac, tace wata uku zaki yi a can sai a shirya ki ayi miki komai, kuma ba zan yarda ya dauke ki ba sai ya miki lefe mai kyau tun da ba yar roba bace ke”

Aminatu dai bata ce komai ba, ta dauki ruwa ta sha ta aje kofin.

“Zata koya miki komai, ki sake jikinki karki rike wannan noke noken nan, shi wannan mijin na ki da kike gani dan duniya ne, kunya ma bata isheshe ba, kin san yan boko, ke kuma gani yar daji, dole ne ta koya miki wani abun da yadda ake zaman aure”

“Zan kai kwanon waje”

“Aa aje ni zan kai, ai tace a daina saka ki aiki saboda jikinki ya samu hutu yai kyau, a kai amarya abu haka a bushe kamar wanda ta taso a rame, wannan bakin ma ai yayi yawa ko dai baki murja jikin ne idan kin shiga wanka”

“Ina murzawa, fatar ce a haka”

“Ikon Allah shi kuma gashi fari kamar larabe sai ku haifi yaya fari da baki”

Ta karasa tana daukar kwanon da Aminatu ta ci abinci ta fice. Aminatu kuma ta hau gado ta kwanta tana ta tunanin rayuwarta.

Sai da yamma Kaka ta kira yarta Hajiya Labara tana tambayar ranar da zata zo.

“Dazun ma ai har kirana yai wai zai zo ya dauki amarya, na ce masa sai nan da wata uku”

“Kai kai kai Hajiya wane irin wata uku kuma dan Allah? Waye zai yi aure yai ta jiran Amarya har wata uku?”

“Yo ba ke kika ce idan son samu ne ta samu wata uku ana gyarata ba”

“Eh gaskiya haka ya kamata, saboda a gyara jikinta da dan abubuwan da zai saka kima a idon mijinta”

“Yauwa, kin gani ai dole ya hakura har lokacin, kuma idan yana sonta da gaske zan gane ai, tun da na san ya aureta ne kawai saboda na matsa masa, ga shi kuma wadannan tsinannin sun zubar da yar kimar tata ta mata”

“Karki damu da wannan Hajiya, ai gyaran da za a mata yanzu, Wallahi ko budurwa sai haka, tuwon girma ai miyarsa nama, amman sai an kashe kudi gaskiya, kawata ke yi dana fada mata sai tace na dawo da Aminatu gidana zata rika zuwa tana mata komai ko kuma ita a kaita”

“To ai sai ki taimaka na fada miki marainiya ce ba uwa ba uba”

“Zan yi iya yawa, amman ba zan iya duka ba, dole a samu wani abu daga gurinki”

“Aa ni ba za a samu komai a gurina ba, kara dai angon”

“Wane irin ango kuma Hajiya? Sai a karbo kudin gyaran amarya a gurinsa? Ban taba ji ba”

“Aa na san hikimar da zan masa ai, ai ba zan yi yadda zai gane ba kar ya mata gori wata rana”

“To sai dai haka”

Kaka ta gyara zama.

“Idan kika tafi da ita a wanke fatar nan tai kyau tai dan haske yarinya ga kyau amman fata ta mutu, jiki a bushe kamar kara”

Hajiya Laraba ta yi dariya.

“Kai Hajiya karki damu, Wallahi har jikinta zaki ga yadda zai canja, har jikin za a bata ai kuma a gyara fatar sai kin ga yadda zata yi heki, indai gyara ne ai yar gidan Mai Fata ba daga baya ba”

“To haka nake so, 10k zai isa?”

A dayan bangaren Hajiya Laraba ta zaro ido.

“Haba Hajiya wane irin 10k kuma? Kar fa ki manta Mu'azu babban mutum ne, kuma gyara za a mata wanda shi kansa sai yayi mamaki”

“Ai ni tsoro nake kar ya wulakantata Wallahi, tun da ya ga ita bata da kowa, amman na kula yana dan tausayinta”

“Hmmm ai Wallahi Hajiya, idan muka gyara ta, be isa ya wulakantata ba, idan kika ga ya juya mata baya to ba yin kansa ba ne sai idan asiri akai masa, kuma idan so yana son yarinya domin da baya son ta da ba zai aureta ba”

“Ni ma na yi wannan tunanin, yanzu dai zan karbo dubu ashirin ai zai yi ko?”

“Hajiya karamin gyara kike son ayi mata ne? Domin hawa hawa ne, indai na manyan mutane sai kin karbo 100k na fada miki har dilke za a mata kuma za a bata wanda jikinta zai dan murmure fatarta tai kyau tai sheki, shiyasa ake son a fara da wuri ai ba a kuraren lokaci ba”

“Ashe Laraba baki da hankali? Har dubu dari za'ayi gyaran jiki kudin fili? Da wani gida? Yo ko gwamna zata aura ai ba zan yi almubazzaranci ba, balle wani Mu'azu”

“Hajiya ba laifina ba ne, mai gyara ce tace haka, kuma idan gyara be yi ba ai dole za a biya kudi, idan kana son abun kwarai dole sai an cire kudi mai kima fa, ke ma dan kina a nan ne kike ganin 100k a wani kudi mai yawa, amman ba wani kudi ba ne, idan ma kika ji masu yi na miliyoyi sai kin yi mamaki, kuma kudin nan fa Hajiya ba ke zaki bada ba a jikin wanda za ayi ma gyaran za su fito”

“Kin tabbatar idan gyara be yi ana biyan kudin?”

“Eh dole ne ma wannan”

Hajiya Laraba ta fada tana dariya, ta fadi hakan ne kawai saboda Kaka ta yarda ta bada kudin domin ta san halin kaka.

“To yaushe zaki zo?”

“Idan ya baki kudin kamar a yau ni kuma zan zo gobe na tafi da ita”

“To, zan kira shi da safe, amman ko da ya biki a can karki yarda ya ganta fa ko a waya ban yarda su yi magana ba”

“Hmmm ai ba zai ma fara ba, yaushe rabonsa da gidana? Shi a rayuwarsa ai be san kowa ba sai dangin Mahaifinsa da dangin Amina, mu da muke talakawa ai babu ruwansa da mu, yana taka gidana ma sai na mata tass Wallahi”

“Ki yi masa kam, ai Amina ce bata koya masa son dangin uwarsa ba sai nata, shiyasa ai na dage sai da akai auren nan in ya sonta hadi zuciya ta mutu daga ita har mijin nata, ya auri yar'uwa dai kuma dole ya rika zuwa gurin danginsa”

“Ai Wallahi kin kyau, shiyasa ai nake son ayi mata gyaran kwarai”

“To zan karbo kudin, amman rabi zan bada sai idan bukata ta biya sai a cika saura”

“Haba Hajiya sai kace mai nema magani, na ji zan cika sauran ni sai ki ba ni”

“To haka yayi, zan aje waya ki kashe”

Sai da Hajiya Laraba tai dariya sannan ta kashe wayar. Kaka ta sauke wayar tana fadin.

“Hauka ake yi da zan dauki har dubu dari na bada”

LEILA POV.

Driving take hawaye bakinciki na sauko mata, for the first time yau tana jin tsanar Talba a zuciyarta, ta rasa gane kansa ta rasa yadda za ayi su fahinci juna ita da shi. Taya ma zai fada mata cewar wai ta yi arha samu a gurinsa?

“Me yake daukar kansa ne?”

Ta tambayi kanta tana goge hawayenta, ba wani kwaliya tai sosai ba sai dai haka be hana fuskarka lalacewa ba. A harabar gidansu Maryam ya faka motarta sannan ta kai kanta jikin sitiyarin motar ta kife wasu hawayen na sauko mata, bata dago ba har sai da wayarta tai kara, sannan ta share hawayen ta kai hannu ta dauki jakarta ta bude ta ciro wayarta.

“Hello Madina”

“Baki shigo ba, ana ta jiranki kuma kin san be kamata ace an yi birthday Maryam babu ke ba”

“Na shigo, ina waje ina cikin mota zaune”

“Ya na ji muryarki kamar da damuwa?”

“Ina cikin damuwar ne Madina”

Ta sauke wayar tana kuka marar sauri, cikin yan mintuna Madina ta iso gurin ta bude dayan bangaren ta shiga ta zaune tana kallon Leila cikin tashin hankali duk kuwa da kasancewar tana cikin nata tashin hankalin.

“Lafiya?”

Leila ta dago tana hawaye ta labartawa kawarta abun da ya faru, a take Madina ta ji nata damuwar ya wartsake.

“To be sincere, Talba ya wuce gona da iri, and ina tunanin lokaci yayi da ya kamata ya san cewa kin banbanta da sauran mata kamar yadda kike fada”

“Kin ma mi nake ji yanzu? I hate him”

“Kina da wannan damar, kuma ki yi hakuri da abun da zan fada miki, tsakani da Allah Talba baya son ki, domin mai son ka zai so abun da kake so, zai guji bacin ranka, kuma zai rika rawar jiki da son kusantarka not like yadda yake miki a yanzu, ki duba yadda yake tarairayar yarinyar nan amman ke ko da rana daya bana jin ya taba miki haka, fadi tashi yake ta yi akanta har sai da ya sama mata yan'uwa, idan ke ce kina tunanin zai miki haka? Amman yaje yana kula yarinyar da ko talkami bata isa ta goge masa ba”

“Madina miye abun yi a yanzu?”

“Ban sani ba, amman Tabbas Talba baya son ki, ina tunanin ya amince da ke ne saboda kar ya bawa Daddy kunya”

Ta lumshe ido tana jin wani kalar zafi da zuciyarta ke mata, hawaye kuma na sauko mata har hancinta ya soma ja.

“Yanzu dai ki koma gida ki huta, be kamata ki shiga gurin nan haka ba, zan fadawa Maryam baki jindadi”

“Okay”

Ta amsa sannan ta share hawayen sannan ta sake kallon Madina.

“Yace ma fada miki zaki iya shiga monday a kamfanin”

“Okay, yanzu ba lokacin yi wata magana ba ne, kawai ki shiga gida ki huta zan shigo gobe”

“Okay”

Ta sake amsawa, sannan Madina ta bude motar ta fita tana jin wani irin dadi na lullubeta, Leila kuma taja motarta ta fice daga gidan cikin damuwa da tunanin yadda zata samawa kanta mafita.

“Ba zan maka kuka ba Talba, ba kai na zubar da hawayena akan ba, miye namijin ma da har zan bata lokacina ina kuka akanka?”

Ta furta tana share hawayenta, sai kuma ta shafe da kuka mai karfi tana jin irin kalar bakinciki, maganar Madina na dawo mata. Can kuma tai yi saurin share hawayenta

“No one deserves my tears”

Ta furta cikin muryar tana jin kamar hade zuciya ta mutu.

BATURIYA POV.

Wannan karon sai da ta baro gidan gaba daya sannan ya amsa kiran Fahat ko ba komai zata fi sakewa a wajen gidan fiye da ciki.

“Har yanzu dai kin ki ba ni damar da yanzu mun shiga next level”

Ta yi dariya.

“Me kake ci na baka na zuba? Nan da kankanen lokaci zan ce maka ka aiko”

“Kankanen lokacin har yanzu be zo ba? Da kin san yadda nake jinki a zuciyata ba zaki rika min wannan jan ajin ba”

“Ba jan aji ba ne, kasan komai na rayuwa yana son tsari, na yi ma iyayena magana sai suka ce na dan dakata shiyasa, amman da zarar sun ba ni dama zan sanar da kai”

“Allah yasa dai ba wani suke son aura miki ba”

“Bana jin iyayena za su aura min wanda bana so, kawai dai akwai wani tsare tsare da suke ne, ni kuma ai ba zan yarda na rasa namiji irinka mai qualities da nake so ba”

“To Allah ya tabbatar mana da Alhari”

“Amin Dear, ya maganar tafiya?”

“Tana nan gobe tun da safe zan wuce yanzu haka na shigo Office din Abbah ne zan dauki wasu takardu ne”

“Allah ya tsare min kai ya dawo da kai lafiya”

“Ameen i love you”

“I love you More”

Ta sumbaci wayar har sai da ya ji karar kiss din sannan suka yi sallama. Saman tebur din Abbah ya aje wayar ya janyo wasu takardun yana dubawa. After like 20 minutes aka turo kofar office din wani mutum da ba zai wuce sa'ar babban yayansu ba ya shigo rike da wata leda a hannunsa dayan hannunsa kuma rike da takardu.

“Dr Adamu”

“Ranka ya dade yau kai ne a kujerar Alhaji?”

Fahat yayi murmushi

“Ni ne”

“Allah yasa dai lafiya”

Ya tambaya bayan ya zauna.

“Lafiya kalau, ni ma wasu takardun ne na shigo dauka, saboda zan yi tafiya gobe”

“Okay, ke nan yau gaba daya Alhaji be shigo ba?”

“Ya shigo da safe, amman yanzu ya tashi gaba daya lafiya dai?”

“Daman maganinsa ne na zo masa da shi, tun da bana nan zan koma sai gobe ko jiki sai na shigo”

“Maganinsa kuma? Abbah yana shan wani magani ne?”

“No na ciwon jiki ne kawai”

Fahat ya kalli katuwar ledar da ke dauke da magani ba daya ba.

“Zan iya wuce masa da shi gida ai”

“No gaskiya wannan a tsakaninmu ne, zan dai ba shi da hannuna kamar yadda na saba”
Fahat yayi shiru yana kallon Dr Adamu dake kokarin mikewa tsaye, a iya saninsa Abbah baya shan maganin komai, domin be san shi da wani ciwo ba bayan hawan jini shi ma kuma sai idan abun ya taso masa yake sha.

“Haba mana, Dr zauna dan Allah”

Dr Adamu ya koma ya zauna yana kallon Fahat daya soma masa magana a natse.

“Idan akwai wani abu ka sanar da ni, dan sa ne ni, karka ci tsoro ko fargabar komai, dan Allah ka fada min akwai wata cuta ne da take damun mahaifina?”

Dr Adamu yayi saurin amsawa.

“No, idan ma akwai shi ya kamata ya sanar da ku ba ni ba, saboda abun da ya shafe shi ne, idan har be sanar da ku ba ni kuma be kamata na yi katsalandan ba, domin rayuwarsa ce, mu wuni lafiya”

Ya mike tsaye da sauri ya nufi kofa, Fahat kuma ya bi shi da kallon da mamaki da kuma tunani kala kala a zuciyarsa.

“Ko dai akwai cutar da take damun Abbah ne, be fada mana ba?”

Ya tambayi kansa, sai kuma ya sauke ajiyar zuciya, yana tunanin ko dai diabetes ne, amman idan har shi ai be kamata ya boye ba, saboda yanayin abinci da yake ci da kuma wasu abubuwan. Haka dai yai ta sake sakensa kamin ya hada takardun da zai dauka ya fice tare da rufe office din.

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

OCTOBER 3RD...

Ya jingina jikin motar Ali ransa a bace kansa har wani sarawa yake.

“To wai ina ta kai yarinyar ne?”

“Oho mata, da alama ma yarinyar bata cikin gidan nan fa, domin da tana ciki yadda na yi mata tijara yau da sai ta nuna min ita”

“Oh No Talba don't tell me ka yi rigima da tsohuwar nan?”

Talba ya dago ya kalleshi.

“To mi zan yi? Ban san inda ta kai yarinyar mutane ba, kuma ta ki fada min komai, tun tana cewa wata biyu zata yi gashi har mun shiga wata na hudu”

Ali yayi dariya.

“Yar mutane kuma? To ai tafi kusanci da Kaka fiye da kai, kuma kasan ita ma tana son yarinyar nan ba zata mata komai ba”

“Ban san da haka ba, idan ba wani abun tai mata ba, ko kuma ya faru da ita miyasa bata fada min inda take ba? Ali na damu”

Ya fada da raunanniyar murya kamar mai shirin yin kuka. Ali ya fada shi cike da kulawa.

“I know amman tun da tace ka bata lokaci ka jira mana?”

“Jira nawa zan yi? Har da mun je garin nan ya fi sau uku, amman kaka ta ki ta fada min inda yarinyar nan take, ban san dalilinta na yin haka ba, idan ma wani abun ne ya same ta ya kamata ta sanar min, kasan ma me kake tunani?”

“No”

“Ko dai an dauke ta kaka ta ki ta fada min?”

“Idan har barayi sun shigo, da ai sai kaji”

“Not just Barayi wani ma zai iya, kuma Kaka ta ki fada min”

“Wani wa?”

Ali ya tambaya yana masa kallon fahimtar inda ya dosa. Talba ya saka saka hannayensa duka biyu ya shafa fuskarsa yana sauke idonsa a harabar Company.

“Dan Allah Talba karka saka Leila a maganar nan, na farko dai Leila bata san ka auri yarinyar nan ba, na biyu ban ga dalilin da zai saka tai haka ba, ka rika kyautata mata zato mana, and yanzu idan akai auren nan haka zaka yi ta kallon Leila tana zalintarta? I don't think zaka iya adalci a tsakaninsu ma”

“Ali Aminatu tana da rauni, not like Leila, ina jin rashin yarda da Leila so many times ban san miyasa ba”

“Ya za'ayi ka ji yarda? Bayan ka dauki rashin yarda ka saka a zuciyarka, haka za ku yi zaman auren kowa na ganin laifin dan'uwansa? Kowa yana ji da kansa? Musamman ma kai kara ma Leila ita mace ce kuma kana saukowa na san zata sauko”

Talba ya daga jikin motar yana kallon Ali.

“Baka tana ganin laifin Leila ba, Ali you're always on her side”

“Yeah saboda tana da gaskiya, just like you and Aminatu, ji yadda ka tashi hankalinka saboda kawai baka ganta ba in few months, kaje kauyen nan ya fi a kirga, ka kasa samun natsuwa ka tashi hankalinka just because of her, ashe da ba kai ka aureta ba da ka samu sabon aiki”

Talba ya mike tsaye yana kallon Ali with serious face.

“Wallahi weather you believe it or not I'm not in love with Aminatu, all what i know is i like her and ina matukar tausayin yarinyar fiye da yadda kake tunani, i marry her saboda Kaka, amman da ace yau Aminatu zata ga wani namijin da take so zan iya sakinta ta aureshi kuma zan zame mata uba wajen ganin komai ya tafi daidai ta samu zaman lafiya da kwanciyar hankali, nemanta nan da nake yi i just want to make sure she's safe kuma tana cikin kwanciyar hankali da farinciki ba wai saboda ina son ta ba”

Kallonsa kawai Ali yake not knowing what to say, ya san abokinsa ba zai masa karya ba, and ya san waye abokinsa son wata mace ba abu ne mai sauki ba, sai dai zai iya bada shaidar cewar Talba mutun ne mai matukar tausayi da taimako.

“Idan kuma ita tana son ka fa?”

“Shi kenan sai na zauna sa ita, idan har zan iya nema mata wanda zai bata farinciki me kake tunanin idan tace ni ne farincikinta?”

Ali yayi murmushi tare ta dan tabe baki.

“Zamu gani, bari ma tafi gida, idan an samu wani information sai ka sanar da ni, so that mu shirya inda za a kai Amarya”

“Why not mu yi magana sa matar da muka bawa kwangilar hada mana lefen nan”

“No Khadeeja Candy bata bada hayar gida, iyakarta hada lefe ko koyan kitchen”

“Wai mu mata magana ko ta san wani wanda yake yi”

“Karka damu, ka bar komai a hannuna, ba dai hayar gida ba ne mai komai da komai a ciki? Zamu samu In Shaa Allah”

“Okay”

Ya amsa yana binsa da kallo har ya shige motarsa yai mata key. Sannan Talba ya nufi Babbar kofar shiga Company, tafiya yake cikin natsuwa da isa, kana ganinsa ka ga babban mutum mai matukar kula da lafiyarsa da kuma jikinsa, annashuwa da murmushi su ne abubun da suka nisanta kansu da shi, sai dai hakan be isa ya saka kai masa kallo daya ka kawar da fuska ba, domin tufafin jikinsa sun karbe shi sosai.
Duk inda ya wuce girmansa ake bashi har ya isa cikin office dinsa, a natse ya tura kofar ya shiga cikin katon Ofis mai kamar daki, an kawata ko'ina gwanin sha'awa ga sanyi ta ko'ina da kuma kamshin air freshener da ya gwaraya da turaren jikinsa suka bada wani kalar kamshin na dabam. Phone din shi ce first thing daya fara dauka sannan ya zauna a kujerar dake gefen teburin ta zaman baki. He's just holding his phone not knowing what to do, all these while Aminatu ce a ransa, be san reason din Kaka na hana sa ganinta ba, kuma zuciyarsa ta kasa natsuwa, har yanzu yana kallon rabuwar su ta karshe da ita, is she safe? Ina ma take? Ko dai wani abun ya same ta ne? Ko kuma dai ta gudu ne? Maybe bata son zama da shi Kaka tai forced dinta. Ya mike tsaye yana rike da wayar ya nufi gurin kujerarsa ya dafa kujerar ya jingina da ita.

‘No ba zata gudu ba, idan ma ta gudu ina zata je? Ai bata da gurin zuwa, kuma bata san kowa ba sai Kaka da shi’

Wani bangare na zuciyarsa ya ayyana masa. Sai ya maida dubansa gurin wayarsa ya shiga muhalin kira ya dannan number Kaka ya aika mata kira. Bugu biyu ta daga tana ra gwada masa sallama amai makon ya amsa sai kawai ya gabatar mata da bukatarta.

“Kaka ki dubi girman Allah ki fada min inda yarinyar nan take, Wallahi hankalina ba kwance yake ba, idan ma sace ta akai ki fada min dan Allah”

Kaka ta tabe baki kamar yana ganinta.

“Ka gama fushin da masifa? Ashe dai zaka iya koma kirana”

“Kaka dan Allah ki fada min inda kika kai yarinyar ko kuma ta tafi”

“Yarinya tana nan lafiya kalau fa, kawai dai bata tare da ni ne”

“Haka kike ta fada min kullum, haka ake aure wai? Ko lefen da kika saka na yi na kawo ban ga yarinyar nan ba, ban san manufar ki ko dai so kike na sake ta ne?”

“Aa A'uzubullahi, miya kawo maganar saki kuma ana zaune kalau?”

“To idan ba shi ba miye ma boye yarinyar nan?”

“Wallahi akwai dan abun da ake ne, ba a gama ba, amman da zarar an gama zan fada maka sai ka zo ka dauki amaryar ka a can gusau ma za a dauke ta a kaita

gidanta ba a nan ba, sauran kuma idan an tashi daukar amarya ka zo mana haka nan ba tare da masu biko ba, kamar yadda kai mana a kawo lefe”

Shiru yai yana tunanin dabarar da zai mata ta yarda da shi.

“Shikenan zan yi tafiya next week, kuma ba zan dawo da wuri ba sai na yi wata shida, idan kuna bukatar wani abun sai ki fada min”

“Shikenan ma, ta kwana gidan sauki sai a bari sai ka dawo sai a kawo amaryar”

Ya runtse ido da karfi ya bude yana jin kamar ya shako wuyan Kaka.

“Yes sai na dawo, amman ina son kamin na tafi ki hada ni da ita a waya na yi magana da ita”

“To zan yi magana da Hajiya Laraba tukuna”

“Tana gidan Hajiya Laraba ne?”

“Baka saci kafa ka tafi gidan ba? Miyasa ba ka ganta ba idan har tana cikin gidan? Wai dan baka da kunya har ka iya cira kafa ka tafi gidan Hajiya Laraba, yaushe rabon ka da gidan? Baka san ka taka ka gaishe ta balle ka aika mata da wani abu, sai gashi tana fada min wai kaje har sau biyu neman Auta, Wallahi kai Mu'azu baka san kunya ba”

“To ni dai yanzu zaki fada min inda take ko ba zaki fada ba?”

“Ba zan fada ba, kuma wannan dubun 100k da ka ba ni ta dade da karewa”

“Idan kina son wasu kudin ki hada ni da Aminatu na ganta, Wallahi ba zan ce sai na dauke ta ba, kawai zan tabbatar idan tana lafiya ne”

“Idan bata lafiya zan tsaya ina magana da kai? Na ce tana lafiya”

Ya katse kiran ya daga jikin kujerar yana kofar office dinsa da Sakatarensa ya turo ya shigo tare da Madina. Hannu kawai ya daga masa sai ya juya da sauri ya fice, Madina kuma ta doso gaban teburin cikin wani irin taku na jan hankali tana masa wani irin kallo kamar ta cinye shi, shi ma kallonta yake har ta aje takardun hannunta a teburin sannan ta kalleshi.

“Na kammala aikin”

Ya gyada mata kai alamar gamsuwa.

“Kana bukatar wani abu?”

“Ina da sakatare”

Ta yi murmushi tana sauke idonta kasa kaminta sake kallonsa.

“Na sani, amman hakkina ne, na tabbatar Angon Leila yana lafiya”

Be ce mata komai ba, sai da ta kusa isa kofa sannan ya kirata.

“Madina...”

Ta juyo a hankali ta kalleshi ba tare da ta amsa ba.

“I think mun dauke ki aiki a nan ne, saboda kina so kuma saboda you deserve it, ba a dauke ki aiki a nan dan ki kula da ni ba, wannan ya zama karo na karshe da zaki shigo min office haka nan kawai ba tare da neman izinin satarena ba! Idan wani abun ne ma zaki iya ba shi ba dole sai ni ba, and ki maida hankali akan aikinki ba wai akaina ba, idan ma Leila ta turo ki nan saboda wani plan nata ki aje shi a gefe ki kula da aikinki before you lose it”

Ta yi murmushi tare da kallon yatsun hannunta, kamin ta fara takowa zuwa inda ta tsaya dazun ta kalleshi.

“Talba, ina aiki a kamfanin nan ne, ba da hadin kan Leila ba, ko da wasa Leila bata taba ce min na zo na yi aiki a kamfanin nan ba, ni na ji ina bukatar hakan kuma na gabatar mata da bukatar har ta samu karbuwa, idan ma kana tunanin na shigo nan ne da wata manufa ko ka daina ka kwantar da hankalinka ka samu natsuwa da ni, ban sani ba ko zaka yarda da ni, Wallahi ba zam taba iya yin wani abu da zai cutar da kai ba, ciki kuwa har da abun da zai saka maka bacin rai ko damuwa”

Ta yi shiru sai kuma ta cigaba.

“Ban san miyasa ba, haka nan nake jin kamar na cuta idan na barka ka zauna da yunwa ko kuma bukatar wani wanda na san zan iya yi maka shi, ina jin damuwa da damuwarka sosai, ban taba fada maka ba, ban taba nuna maka ba, kuma ban tana bari Leila ta fahimta ba, har ga Allah ina jin cutuwa idan kuka samu matsala sa Leila, ba dan bana son ku samu matsala ba, sai dai na san hakan zai saka ranka ya bace”

Idonta ya cika da kwalla, sai ta dago ta kalleshi.

“Kai mutum mai matukar daraja da kima a idona Talba, kana kula da mutane da yawa, amman kai babu mai kula da kai, kana da tausayi sosai ka san kimar dan 'adam, amman Leila ta kasa tausayinka kuma ta kasa kula da kai yadda ya dace, gashi har kuna neman zama miji da mata, na san zaka ji bakin kalamai a gareni yau, wata kila ba zaka fahimce ni, ban matsa akan ka fahimce ni ba, domin na lura kana kyarata tun a lokacin dana kama aiki a kamfanin wata uku da suka wuce zuwa yau, baka son ina shiga lamarin, amman ina rokon wata alfarmarki daya”

Ta hade hannayenta guri daya tana kallonsa hawaye na saukowa a idonta suna wanke fuskarta gwanin tausayi.

“Dan Allah karka min shamaki da office sin nan naka, saboda ganinka kadai na daga cikin abun da yake kwantar da min da hankali ya saukar min da natsuwa, a duk lokacin dana samu kaina a damuwa, hotunan ka ne abun da yake debe min kewa, kuma ya saka na dawo cikin natsuwa”

Tana kawai nan ta juya jiki a sanyaye ta nufi kofar fita, bata taba samun kanta a irin yanayin data samu kanta a yau ba, a yau kam ta masa rike hashenta daga furta wadansu kalamai da ta san za su iya ja mata matsala ko kuma su datse alakarta da kawarta. Ta san tana son Talba sai dai ba tabbatar da sonsa ya yi

tasiri sonsa a zuciyarta kamar lokacin data fara aikin a kamfanin zuwa yau, a kullum wutar sonsa kara ruruwa yake a zuciyarta, saboda kusancinsu ya karu a yanzu fiye da da, kusan kullum tana ganinsa, a kullum kyaunsa karuwa yake a idonta, idan ta kalleshi har jin take kamar ta rumgume shi, Talba na da cikar kyau da siffar da ko wace mace zata so ya kasance a mijinta.
Da ido ya bita har ta fice sannan ya girgiza yana daga kafadunsa.

“Ita da Leila duk hankali be ishe su ba, daman ance show me your friend i will tell you who you are”

Ya furta yana mamakin yadda Madina ta rikide masa a yau take masa wasu zantuka marasa kan gado.

AMINATU POV.

Yau ma da kanta ta daura lifayar ta nada kamar yadda Farida ta koya mata, bayan ta gama ta dauki turare ta kara feshe jikinta da shi, domin Farida ta fada mata kamshi na daga cikin abun da yake karawa mace kima da martaba, karta yarda ta zauna babu kamshi a jikinta. Hakan yasa ta saba mata idan zata yi wanka sai an zuba mata turare a ruwan, idan ta fito tawul din da zata tsane jikinta ma an saka mata turare, kamin ta shafa komai sai an fara lullubeta da da zane an mata turaren jiki ya tsara ko'ina a jikinta kamin a gabatar mata da na tsuguna, idan kuma ta gama shafa mai sai ta bi jikinta da turaren jiki ta shafe ko'ina a jikinta. Hakan yasa kamshin ya kama jikinta sosai ko wucewa tai sai ka ji kamshi na tashi kamar mai yawo da ruwan turare. Sai da ta dauki red lipstick ta shafa a bakinta sannan ta isa gaban katon madubin tana kallon kanta. Dan murmushi tai domin ita ma kanta ta san ta canja, jikinta yayi kyau kamar ba nata ba, bakar fatar nan sai sheki take tana shining kana ganinta ka san an kashe mata kudi gurin gyara, kumatunta ma sun dan ciko jikinta ma ya bayyana cif saboda gumbar kiba da take sha a kullum wanda Yar gidan mai fata ta hada mata. Hakoranta ma tasss Hajiya Laraba ta saka aka wanke mata su, hakan yasa ta kara kyau da haifa, fararen idanuwanta suka haska fuskarta. Gashin kanta ma every week ake kaita gidan Farida ko kuma ita ta zo ta gyara mata shi tana saka mata mayuka masu kyau da tsada idan ta bude kan har wani kamshin dadi zaka ji yana yi. Ba gyara ne kadai abun da Farida take zuwa yi mata ba har da koya mata tafiya da saka wasu tufafin da ba bata saba sakawa ba, kamar saka kananan kaya da daura lafaya. Ita kanta tana jin jikinta na canja sosai idan ta taba fatarta tana jinta so soft saboda gyaran da ta sha har wani tsantsi take.
Kasa tai da idonta tana kallon tsadaden agogon hannunta, tun da take a rayuwarta bata taba saka agogo ba, sai da Talba ya hada mata lefe kuma Kaka ta aiko mata da abun ta a gidan Hajiya Laraba, hannu ta kai tana tana agogon hankali tana murmushi tuna zuwansa na karshe a gidan nemanta, sai dai Hajiya bata damar fitowa ba sai ta boyeta a dakin dakin yaranta tace masa ba a kawo ta nan ba, har rufe da tai da fada domin be saba zuwa gidan da sunan ya gaisheta ba ko duba lafiyarta, rabonsa da gidan ma har ta manta. Jin motsin turo kofar dakin yasa ta juyo da sauri ta kalli kofar.

“Maa Shaa Allah, Auta an sha kyau ke ma kin iya gyara kanki yanzu haka nake so, kalle ki kamar ba ke ba Wallahi”

Hajiya Laraba ta fada fuskarta dauke da murmushi tana karasowa kusa da Aminatu. Sai Aminatu ta sauke kanta masa tana murmushi.

“Karbi maganinki ki sha, idan kin sha yau kika sha gobe shikenan ya kare”

Ta mika mata kofin dake dauke da garin maganin mata da aka kada da madara, ita kuma ta saka hannu biyu ta karba ta kafa kai ta shanye. Kusan kullum sai ta sha maganin tun tana jin dacinsa tana kyama har ta saba, ya zame mata jiki na safe dabam na rana dabam na dare dabam, bayan na tsuguna dana shafawa set din back to virgin kusan kala uku yar gidan mai fata ta hada mata. Hajiya Laraba ta karbi kofin tana fadin.

“Haka nake so, saboda Talba ya san ba banza muka aura masa ba, ai ko dan yar'uwata zan dage na yi masa abun kwarai, kuma ya san idan shi ya mantawa mu mu ba zai yiyu mu manta shi ba, domin jininmu ne shi, shiyasa ban ji zafin cire kudin nan na bada a miki gyaran jiki ba, kalli yadda kike ta sheki, gaba daya kin canja yan kumatun ma sun taso gwanin sha'awa, ke nan idan kika shekara ai ba za a gane ki ba”

Wannan karon murmushi mai sauti Aminatu tai, sannan ta zauna bakin gadon tana kai hannunta ta dauki tissue ta gyara bakinta, Hajiya Laraba ta fice tana ta yabawa da yadda Farida ta gyara mata jiki. A hankali ta dago ta kalli kanta a madubi, sai tai yi arba da wata Aminatu ta dabam wacan ba, wannan Aminatun kyakkyawa ce mai kwarjini da haiba, mai kwaliya da kamshi mai cikar sura, ba kamar wacan ba wanda wahala da tashin hankali suka hana ta kumari, zaman kauye kuma yana kyauta bayyana, a yanzu kuma tana cikin ac ta kwanta a gado mai kyau ta ci abinci mai kyau ga supplements da magungunan gargajiya da ake bata na gyara jiki tana sha a kullum. Abu daya wannan Aminatun ta rasa irin wanda wacan Aminatun ma ta rasa shine farinciki, ta kasa mantawa da iyayenta, ta kasa mantawa da gidansu, ta masa manta yadda aka rusa rayuwarta, ta kasa goge hoton yadda aka ruguza danginta.

“Inna...”

Ta furta tana jin kamar ace Inna na tsaye a bayanta a yau, ta ga irin kyau da tai. Ji take kamar ta waiga tai arba da Yayanta Saminu mai yawan zolayarta, a yau ta ji tana marmarin fadan da Ya Amadu da Iro suke mata.

“Allah ya miki albarka ya nuna min aurenki Auta”

Maganar Baba ta dawo mata, daman hawayen ba bakin idanuwanta ba ne, a take ta ji tsayuwar wani mashi a kahon zuciyarta wanda ya saba zuwa ya tsaya mata a duk lokacin da irin wannan tunanin ya zo mata. Hannu ta kai ta dafe kirjinta ta runtse ido sosai tana sauraren yadda zuciyarta take raba jinin dake jikinta da sauri. Kwantawa tai a hankali saman gadon tana maida numfashi cikin natsuwa still idonta a rufe.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa

taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

MADINA POV.

Tun da ta dawo daga gurin aiki take zaune harabar gidan ta inda ba kowa zai ganta ba tana sharbar kuka, tun tana yi tana danne sautin muryarta har ta kai bata iya controlling kanta, faduwa tai daga kan kujerar zuwa kasa sai ta kai hannayenta ta kama kitson kanta ta matse sosai tana jin kamar ta kashe kanta ta huta, zuciyarta na mata mugun zafi kamar zata fasa kirjinta ta fito. Bata taba jin nadamar aikata wani abu ba kamar yadda take jin nadamar furucin da tai ma Talba a yau, ta san be dace ta furta haka ba, ga mijin da kawarta zata aura, idan Leila ta ji ya zata yi? Anya ma zata iya sake hada ido da Talba a yanzu? Anya zata iya komawa gurin aikin nan? Wane irin kallo zai mata?Zai fadawa Leila kalman da tai masa? Ta kasa raba dayan biyu tsakanin rashin dacewa da furucinta a gareshi da kuma irin son da take masa, domin ta wani bangaren bata ganin laifin kanta, kusan awa hudu tai a gurin bata aikin komai sai na kuka, tun tana tana yi hawaye na sauko mata har ta kai tana kukan babu hawaye, idonta ya kumbura kamar an hura shi, yawun bakinta suka kafe, kanta sai sarawa yake ya mata wani uban nauyi. Daker ta iya mikewa tsaye ta fara takawa tana jin kafafuwanta da jikinta kamar ba nata ba, takawa take a hankali tana jin kamar kafafuwanta basa iya daukarta. Tana kaifa cikin shiga falon wani irin jiri ya debeta da karfi ta fadi kasa dafe da kanta a take duk wani abu dake motsi a jikinta ya tsaya cak cikin har da bugun zuciyarta da fita da shigar numfashinta. Da sauri Tima ta yo kanta tana girgiza ta.

“Yaya Madina yaya Madina yaya Madina...”

Ganin babu alamar numfashi a tare da ita yasa ta kwalawa Hajiya kira tana ihu da kuka a take.

“Hajiya ki fito Yaya Madina ta suma”

Sau uku tana kiran Hajiya, kamin tai hudu Hajiya ta fito da gudunta daure da tawul jikinta kuma a jike da sanyin ruwa da alama wanka da fito.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, Madina. Miya same ta?.”

“Ban sani ba kawai tana shigowa ta fadi a nan”

Hajiya ta kai hannu tana tabata..

“Madina, dauko ruwa Tima”

Hajiya ta fada tana fashewa da kuka, sai faman girgiza Madina take tana kiran sunanta. Tima ta tashi ta shiga kitchen da sauri ta dauki katuwar roba ta kunna tap ta cikar robar ta fito a guje ta nufo Hajiya ta mika mata, Hajiya ta karbi ruwan da sauri ta zubawa Madina gaba daya, kamar wanda aka kwato haka Madina ta farko da karfi tana haki.

“Alhamdulillah”

Hajiya ta furta da sautin kuka tana dafe zuciyarta dake bugawa da karfi Tima ta dafa ta.

“Sannu Ya Madina”

Madina ta kalleta.

“Miya same ni?”

“Suma kika yi baki da Lafiya ne?”

Madina ta kalli Hajiya.

“Ba ni da lafiya, kuma ciwo ne da ba zan tana warke shi ba”

“Wane irin ciwo ne haka? Idonki ma duk ya kumbura dubi fuskarki Madina me yake damunki”

Amaimakon ta amsawa Hajiya sai ta lumshe ido ta fashe da wani sabon kuka, can kuma ta bude idon ta soma yunkurin tashi sai ta kasa saboda jikinta babu kuzari.

“Tima rika ni na shiga daki”

Tima ta kamata da sauri Hajiya kuma ta rika dayan bagaren suka mikar da ita tsaye, a hankali take takawa har suka isa cikin dakinta, saman gadonta suka zaunar da ita.

“Na hada miki tea?”

Sai da ta kalli Tima da idanuwanta da suka kumbura sannan ta amsa mata.

“Aa kawo min ruwa na sha”

“To”

Ta juya ta fita da sauri, sai Hajiya ta zauna kusa da Madina tana kallonta cike da tausayi.

“Saboda Talba ne?”

Madina ta yi jimmm na dan lokaci kamin ta daga mata kai alamar eh.

“Hajiya dan Allah ina son ki nema min izini gurin Abbah ina son na koma Kaduna da zama gurin Baba Shehu”

Hajiya ta mata kallon mamaki da kuma rashin fahimta a lokaci daya, sai dai shigowar Tima rike da kofin ruwa ya hana ta cewa komai har ta mikawa Madina ruwan, Madina na karbar ruwan sai ya zube a jikinta saboda bata da kuzarin rike kofin ruwan ma. A take Tima ta saka kuka, domin bata taba ganin yar'uwarta a irin wannan yanayin ba, kuma bata wasa da su balle tace wasa take musu.

“Na shiga uku Ya Madina miya same ki wai?”

“Ba ni da lafiya gobe zan tafi asibiti”

“To Allah ya baki lafiya”

Ta fada tana share hawayenta tare da kai hannu ta dauki kofin ta fice. Hajiya ta kai hannu ta rika fuskar Madina ta juyo da ita.

“Madina... Miyasa kika bari zuciyarki ta kamu da son wanda soyayyarsa zata azabtar da ke har haka?”

“Hajiya shi nake ta kokarin ganowa, akwai maza da yawa miyasa ban kamu da son kowa ba sai mijin da aminiyata zata aura, ga maza da yawa miyasa sai Talba? Hajiya ina jin kamar na sha wani abu na mutu wani lokacin ina jin kamar na yi hauka”

Ta yi saurin kama hannayen Mahaifiyarta ta rike gam.

“Ina son na yi nisa da nan, ina son na tafi nesa saboda na daina ganinsa ko jin duriyarsa, bana son ayi aurensa da Leila ina raye, bana son na zauna a gari daya da su, zan iya cutuwa kuma zan iya cutar da su”

Ta saki hannu Hajiya tana ta share hawayenta.

“Na san be kamata ba, be dace na yi haka ba, amman miyasa na yi? Kaddarata ce a haka right Hajiya? Right?”

Ta fashe da kuka mai karfi, Hajiya ta runtse ido tana hawaye, ma dake tsaye rike da wasu ruwan da ta debo mata hawayen take.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Hajiya ta furta sannan ta bude idon ta share hawayenta.

“Tima kawo mata ruwan ta sha”

Tima ta karaso ta dauki tissue ta share mata fuska sannan ta bata ruwan a baki ta sha mai yawa sosai.

“Kwanta ki yi bachi idan kin tashi zamu yi magana”

Hajiya ta fada, sai Madina ta daga mata kai ta kwanta rairan saman gadon ta lumshe ido. Ganin haka yasa Hajiya da Tima suka fita tare da ja mata kofar dakin a hankali, bude idon tai ta janyo filon dake saman gadon ta rumgume shi a kirjinta tana hade yawu.

BATURIYA POV.

cikin natsuwa ta maida tufafin jikinta sannan ta juyo ta kalli Alhaji dake wani shegen murmushi.

“I hope idan mun je ba dadewa zamu yi ba”

“Aa idan mun je ba zai wuce mu yi sati biyu ba, sai idan kina son Kasar sai mu kara”

“Aa satin biyu dai ya isa, saboda akwai planning din da nake, badan ma ka matsa ba da ba zan je ba gaskiya”

Ya gyara bed sheet din yadda zai rufe masa jikinsa da kyau tana kallonta

“Baki son fita wata kasar ne? Irin Dubai London da sauran kashashen duniya?”

“Ina so kam sosai, sai dai kasan irin mu da mike zaune da iyaye dole sai da dabara muke fita, saboda idan mutane suka gane zai iya taba kimarmu, balle ni da nake da niyar aure”

“Aure kuma? Yaushe ska fara abun da har zaki gaji? Duka duka yaushe kika shigo wannan kasuwancin”

“Na samu iya abun da zan samu, kuma na samu wanda nake so, me kuma zan jira”

Yayi dariya.

“Yaro man kaza, ke yanzu har kina ganin kin tara abun da zai isheki? Ni kaina da nake tsoho ai ban ki na kara ba balle kuma ke da yanzu kurciyarki take cinki, yanzu kike cikin lokacinki”

“Ba ni da dogon buri kuma mijin da zan aura shi ma yana da rufin asiri, beside son sa ba zai bari na dade a haka ba domin shi ma kansa ya matsa min sosai”

“Eyee wani mai sa'ar ne haka? Zai dauke min sweet Baturiyar mata”

Ta yi dariya sannan ta dauki mayafinta ta yafa.

“Wani ne kyakkyawa sosai, mai kudi dan gidan mutunci”

“Gaskiya yayi sa'a samun mace irin ki ai sa'a ne, ina fatar dai alakarmu ba zata yanke ba, duk dai bana son mu'alama da matan aure, amman ina jin kamar ba abu ne mai sauki rabuwa da ke ba”

“Aa gaskiya, ba zan yarda mijina ya gane ba, bana son mu samu matsala da shi duk wani abu da zamu yi zan zubar da shi ne a nan waje”

“Ni dai roko nake, kin san dai dole ne na aje sirrinki ko dan kaina”

“Kadai mu bar shi a nan kawai”

Ta fada bayan ta dauki jakarta ta rataya, sai da ta karaso kusa da shi ta sumbanci goshinsa ta shafa kirjinsa dake sake sannan ta daga ta nufi kofa.

“Na tafi sai mun yi waya”

“Okay Baby”

Juyowa tai ta kalleshi tana murmushi sannan ta bude kofar ta fita. A falon ta tsaya ta saka face mask da katon bakin gilashi sannan ta fito harabar gidan ta fara takawa, kamin ta karasa gate din mai gadin gate din ya bude gate din sai ga wata farar mota ta kunno kai da sauri Baturiya tai kasa da kanta domin bata son tai ido biyu da wanda ke cikin motar duk kuwa da kasancewar tana sanye da mask ba lallai ne a gane ta ba, kamar yadda be zama lallai ace ta san shi ba ko ya san ta, wata kila ma direbansa ne. Ta karamar kofar gate din ta bi ta fice da sauri ta fara tafiya kamar da gudu gudu sauri sauri ko kadan bata yarda ta waiwayo ba sai nitsawa take babban titi unguwar tana nufar inda zata samu Napep..

Fahat na yi parking ya fito da sauri ta tako kasa zuwa gurin gate din yana kallon matar data fita daga cikin gidan. Mamaki yake yi wacece kuma mi ta zo yi a gida? A yanayin rashin jiki da farin fata ta masa yanayi da Baturiya, sai dai ko kadan be kawo cewar ita din ce ba, saboda ya san Fee'at bata daga cikin irin matan da za su aikata wani abu makamancin wannan, from first place be ma kamata ya munanawa mahaifinsa zato ba, what if wani abun ya kawo ta? Sai da ya daina hangota sannan ya juyowa ya dawo cikin gidan jikinsa a sanyeye, ko kadan baya son ya zargi mahaifinsa da abun da zuciyarsa take ayyana masa, amman idan har haka ne ba mi yarinyar mace kamar wannan zata zo yi a guest house dinsa? Har ya iso bakin kofar shiga falon be samu natsuwar da yake son ya samu a gurin mahaifinsa ba. Kasancewar kofar falon tana unlock ne sai kawai ya tura ya shiga, a falon ya samu mahaifinsa zaune yana latsa waya, fuskarsa a hade kamar an masa mutuwa.

“Abbah...”

Ya dago ya kalleshi yana kara hade girar sama da kasa.

“Ya akai? Ban fada muku kar wanda ya shigo min a nan ba tare da ni na kira shi ba?”

“Kai yi hakuri Abbah, daman kudin nr da na ciro na je gida sai Momy tace ta fita, kuma na san ka baro office shiyasa na yi tunanin naka nan ne”

“Amman ai ya kamata ka kira ni kamin ka zo, ba wai ka zo min haka nan kawai ba, kudin tashi zan yi da su da ba za a iya jirana da su a gida ba?”

“Na yi ta kiran number ka a kashe, ka yi hakuri ba za a kara ba, kudin yana cikin mota”

“Ka koma da su can gida”

Ya fada yana mikewa tsaye ya nufi bedroom dinsa sai kabe rigar shaddarsa yake, kana ganinsa ka san ransa a bace yake, ba komai kuma ya bata masa rai ba kamar zuwan Fahat ba tare da saninsa ba, da ace be ji motsin tsayawar motarsa ba yai hanzari saka tufafinsa da Allah kadai ya san a wane hali zai same shi, kuma da Baturiya ba tai hanzarin tafiya ba da yanzu wani labarin ake ba

wannan ba, duk da dai yasan ba zai fada masa daki ba tare da ya bude masa ba, domin a lokacin da suka shiga dakin rufe shi yai da key fitar da Baturiya tai ne ta bude kofar bata rufe ba. Fahat ya mike tsaye jiki a sanyeye ya fito daga falon ya nufi motarsa, ya bude ya shiga yai reverse ya aka bude masa gate ya fice yana driving kamar wanda baya son tukin. Ko kadan be ji dadin abun da ya gani ba, domin yanayin yadda Abbah yake masa masifa ya tabbatarsa da zargin da yake, be taba tunanin dattijin mutum kamar mahaifinsa zai iya maida zuciyarsa ta yara ba, yaran ma marasa tsoron Allah da basa jin kunyarsa. Da tunani kala kala ya isa gida, nesa da kofar falon ya faka motarsa ya fito ya nufi kofar yana jin tausayinsa mahaifiyarsa da kuma su kansu da suke yayansa, ya dade a tsaye jikin kofar kamin yai knocking a bude masa, kamar wanda yai wani aikin wahala ya gaji haka ya shiga cikin falon, be tsaya komai ba ya nufi upstairs da zimmar shiga dakin mahaifiyarsa, sai ya ji tana kiransa.

“Muhammad Fahat”

Juyowa yai sai a lokacin ya lura da inda take zaune tana gyaran fruits, takawa yai ya karasa inda take ya zauna kasan carpet din ya aje makullin motar a gabanta.

“Idan Abbah ya dawo ki basa kudin suna cikin motarsa, yace a dawo da kudin gida”

“Miya faru ya fasa siyen filin ne? Ai daman na fada maka zai iya cewa ya fasa, domin filin miliyan arba'in ya masa kadan, tun da ba zama zai yi ba ajiya ce kawai”

“Ba fasawa yai ba, kawai dai yace a dawo da kudin gida”

Ta mike tsaye cikin yanayin damuwa, har ya juya Momy ta kira shi.

“Muhammad Fahat?”

Ya juyo ya kalleta.

“Kamar kana cikin damuwa miya faru?”

Yayi shiru yana tunanin yadda zai fada mata cewar wata matashiyar yarinya ya gani a gidan mahaifinsa, ya zata ji? Ya zata kalle abun zuciyarta zata iya dauka?

“Ba komai”

Ya amsa sannan ya juya ya fara tafiya.

“Ko dai mahaifinka ya maka fada ne akan yarinyar nan?”

Ya sake juyowa ya kalleta.

“Abbah ba shi da matsala da ita, ke ce kike hana ni aurenta saboda kina ganin kin zaba min wata, amman ba Abbah ba, dan haka babu wani dalili da zai saka Abbah yai min fada akanta, kaina ne yake dan ciwo zan jr na kwanta”

“Allah ya sauwake, ka sha magani please”

Ya gyada mata kai sannan ya dauke kai ya nufi kofar fita. Bangarensu ya nufa domin an ware bangaren yan mazan gidan dabam matan ma bangarensu dabam, kanensa da kuma wadanda ake riko a gidan. Yana shiga Dakinsa ya zauna saman kujera ya ciro wayarsa ya shiga muhallin kira, number Baruriya ya aikawa kira, sai aka sanar masa har lokacin wayarta na a kashe. Dauke wayar yai daga kunnensa ya shiga gallery ya kamo hotunanta yana kallo. Samun kansa yai da murmushi yana kallon kyakkyawar fuskarta sai ya ji son ta ya karu a zuciyarsa. Baturiya na da kyau tana da siffar da kowane kalar namiji zai so ta, amman tana da kyaun zuciya? Tana da tarbiya? Ta fito a gidan kima? Ya tambaye kansa yana kara kallon hotunanta, a yanayin yadda take nuna masa da yadda ya fahimci mu'amalar ta tana da tarbiya, kuma ta fito a gidan mutuncin domin ta dade tana boye masa gidansu da ikirarin ba a barinta zance, sai dai daga baya nan ta kan tsaya da shi a kofar gidan da take ikirarin na su ne. Mikewa yai tsaye ya nufi gurin plasma ya kunna sannan ya dawo ya zauna tare da aje wayar gefe, can kuma ya dauki wayar ma'adanar lambobi ya shiga ya zakulo number Isma'el ya danna kira.

“Hello Isma'el”

“Oga Fahat ya gida?”

“Lafiya Kalau ba zaka daina ce min oga ba ko?”

“Ya za'ayi na daina, ai ka yarda kawai kai oga ne”

Fahat ya dan yi murmushi.

“Ya aikin ya kwana biyu?”

“Alhamdulillah ya na ku?”

“Mun gode Allah, wani aiki ne zan baka kuma sirrina ya zama tsakanina da kai please”

“Okay ina saurarenka”

“Zan turo maka hoton wata yarinya da number wayarta da kuma sunanta da unguwarsu, dan Allah ina son a bincika min komai a kanta, bana son ka boye min komai”

“Yayi Alhaji ka ce lokaci yayi”

Fahat yayi murmushi.

“Amman bana mutuwa ba, ina son yarinyar sosai gaskiya, sai dai kasan halin Momy, to ina son na fara bincike da kaina ne ne kamin su yi na su, dan nasan zasu yi, ina son idan akwai wata matsala na fara sani kamin su, domin ina ta kokarim shawo kansu ne a yanzu”

“Karka damu Insha Allah zan bincika yadda ya dace, Allah ya tabbatar da alheri”

“Aamin ya Rabbi, na san dai ka fini sanin garin nan sosai a yi min bincike da kyau please”

“Okay, ba matsala, sai na jika”

Ya kashe kiran tare da sauke ajiyar zuciya, har yanzu ya kasa daina ganin yarinyar daya ganin dazun a idonsa, hankalinsa ya kasa kwanciya.

AMINATU POV.

“Kuka kike yi?”

Ta bude ido da sauri tare da tashi zaune ta share hawayen, sai kuma ta kasa cewa komai.

“Ko kin gaji da zama a nan ne?”

Da sauri ta girgiza kai ta kara sadda kanta kasa.

“Aa ina tunanin su Inna ne”

“Allah ya musu Rahama, ki daina kewa ke kadai ta so ki fito falo”

Ba musu ta mike tsaye tana gyara mayafin lifayarta. Hajiya Laraba na gaba Aminatu na binta a baya har suks fita daga dakin, a inda tafi jindadin zama ta nufa ta zauna ta maida hankalinta gurin tv da suke kallo. Bata juyo ba har sai da ta ji sallamar Hajiya Hadiza Mai Fata, sai da kowa ya gama gaishe ta sannan Aminatu ta mika mata gaisuwa.

“Ina wuni?”

Cikin far'a Hadiza ta amsa tana kallon yadda komai nata ya canja kamar ba ita ba.

“Maa Shaa Allah, Amina an yi kyau sosai, kamar Aminata”

Cewar Hadiza kasancewar ita ma tana da babbar ya sa'ar Aminatu.
Aminatu ta sauke kai kasa tana murmushi, domin ita ma kanta ta san ta canja duk wani furuci da za ayi mata a yanzu ba zata yi mamaki ba. Har suka gama gaisawa da kawarta Hajiya Laraba bata dago kai ba har sai da Hajiya Laraba ta kirata.

“Aminatu ta so”

Ta amsa tare ta mikewa tsaye ta bi bayan Hajiya Laraba suka koma dakin da ta fito. Ko da ta shiga har sun zauna kan gado sai dariya suke yi suna zancen su na matan aure. A kasa Aminatu ta zauna ta sanda kanta kasa. Sai Hajiya Hadiza tai murmushi ta ce

“Aminatu sarkin kunya, haka ake son mace da kamun kai da natsuwa”

Sai kuma ta kalli kawarta.

“Hajiya ya kamata a kai masa matarsa tun da mun gama gyarata, yanzu ma na wanka ne kawai na kawo mata mata, domin ta gama shan komai daya kamata ta sha, bana haufin komai”

Hajiya Laraba ta saka dariya tare da bata hannu suka tabe.

“Kawata ai na san ki ba daga nan ba, bana shakkar kayanki ko kadan, nan da kwana biyu ai zan a kaita dazun ma Hajiya ta kira tana fada min irin haukar da yai mata akan matarsa nace ta fada masa ya assabar mai zuwa zamu kawo masa ita”

“A gaskiya ya kamata, kam in ma ba dan yana auren kauye ba yaushe za ayi aure har wata uku da wani abu ba a kawo maka mata ba”

“Hana dai, ai ke ma kin san idan aka kai masa ita haka nan ba tare da wani gyara ba, wulakanci zai iya biyowa baya, amman kalleta ki gani yarinya ta kara kyau ga jiki ta yi sai shining take kamar yar waje, bakin ma duk ya ragu kamar ba ita ba, jiya na Ogana zolayata yake wai mun ci amanar ango mun rike masa mata, wai yana da hakuri da shi ne kotu zai maka mu”

Kusan duk a tare sukai dariya, sannan Hajiya Hadiza ta ciro wata kwalba a jakarta ta mikawa Aminatu.

“Wannan idan zaki yi wanka ki rika zubawa, idan ya kare sai ki kara ruraren ki barshi ya dan jika sai ki cigaba da amfani da shi”

Aminatu ta saka hannu biyu ta karba, sannan ta mike tsaye ta fice daga dakin.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazo maku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

“Ke Uwani karbi kira min Mu'azu, na fada masa ya shirya sati na gaba zamu kai masa matarsa”

Wanda Kaka ta kira da Uwa ta ta so da saurinta tana dariya.

“Kuma dai Hajiya, ba kin ce sai kin ga dama ba, har kin sauko?”

“To ya na iya, ita ma Wannan Yar Haj Laraba dana fada mata cewa tai an gama komai sati mai zuwa za a kai masa amaryarsa”

Uwani ta nemo number Talba da Kska ta saka aka rubuta mata Mu'azu a ta kira shi, sai da ta fara ringing sannan ta mika mata.

“Gashi ta shiga”

Kaka ta karba da sauri ta kara wayar a kunnenta ta nufi dakinta. Talba dake zaune a katon falon Momy ya dago kansa kadan yana kallon wayar dake hannun kujera tana ringing, ganin number Kaka yasa ya dauke kai kamar ba zai dauka ba, domin a tunaninsa zata sake masa maganar kudin dazun ne, ko kuma wata maganar ta dabam ba maganar Aminatu ba. Can kuma ya kai hannu ya dauka ya amsa kiran yana kara kishingidawa jikin kujerar.

“Assalamu Alaikum Mu'azu”

“Na'am Kaka”

“Daman na kira na fada maka cewar Innakar Hajiya Laraba tace sati mai zuwa za a kawo maka matarka, sai ka shirya ka aiko da mota”

Ya dan saci kallon Leila dake zaune ita da Amal a kujera daya sannan ya ce.

“A ina za a dauke ta?”

“Gidan yayar mahaifiyarka mana, Hajiya Laraba, amman fa ban siya mata komai ba, babu kayan dafa abinci babu komai”

“Na ji zan ji da komai, amman yanzu Fisabilillahi an san yarinyar nan tana gidan nan aka ki nuna min ita? Kin san zuwa na nawa a gidan nan?”

“Ai ni na fada maka kar ta bari ka ganta, to mi zaka tsinana mata? Ai kara dai sai an gama yi mata gyaran jikin”

“Ku dai kuka sani, dacan ba a san da zacen ba sai yanxu, dan kawai a wahalar da ni”

“To yanzu ba fada maka nake ba”

“Wace rana?”

“Assabar”

“Na ji”

Ya kashe wayar ya aje, ya kalli Amal dake kallonsa, sai kuma ta sakar masa murmushi. Shi ma dan murmushin yai mata kadan ya mike tsaye ya nufi upstairs, kamin ya karasa shiga dakin Momy har Amal ta cin masa ta bude masa kofar, murmushi kawai yai ya dauke kai ya shiga dakin, domin ya san gulma ta kawo ta. A saman kujera ya zauna Amal kuma ta karasa inda Momy take zaune ta zauna.

“Momy ga Yaya nan”

Momy ta dago ta kalleta sannan ta kalli Talba.

“Akwai wata matsalar ne?”

“Aa, akan maganar yarinyar nan ne”

Sai kuma yayi shiru.

“Ehm miya faru?”

“Akan maganar da na taba yi ne, na dawowar ta gidan nan”

“Ba kace Kakarta da ita yarinyar sun fi son zamanta a can ba?”

“Eh, amman ina ganin zamanta a nan kamar zai fi, saboda a can bata karatu, bata komai, a nan kuma ina son na saka ta a makaranta”

“Talba, kana tafiya kauyen nan ne ba tare da mun sani ba?”

Momy ta tambaya da mamakin yadda a yanzu ya dawo da zancen dawowar yarinyar bayan a can baya ya fada mata cewar bata son zama a nan ita da kakarsa, shi kuma ya fadi haka ne saboda Kaka ta dauke masa Aminatu idan be musu wannan karyar ba be san me zai fada musu ba.

“Idan ma na je Momy ai ban yi laifi ba, garin mahaifiyata ne, tana da dangi da iyaye a can, be kuma kamata na watsar da su ba”

Momy ta cire gilashin idonta tana murmushi.

“Gaskiya ne, amman ai ba su san da zamanka sai da ka girma. Any way ba zan hana ka kawo ta ba, saboda Daddynka ya dade da baka wannan damar ni kuma ba mahaifiyarka bace balle na maka magana ka ji, amman ina son na yi maka magana a matsayina na mahaifiyar matar da zaka aura”

Talba ya kalleta, sometimes yana mamakin yadda Momy take sakar masa magana kamar ba ita ba.

“Ka san dai mahaifinku ya saka lokacin aurenku, 24 march nan da wata biyu za ayi aurenku, so ya kamata komai zaka yi ka rika shawararta matarka, kuma ka kuje duk wani abu da zai bata ranta, ba wai ka dauko wannan ballagazar yarinyar yar kauye ka kawo ba, kuma ka fara nuna irin halin daka nuna wacan karon akan Leila, so ka yi taka tsantsan, kuma ban yarda ta zauna a nan tare da mu ba, sai dai ka aje ta BQ”

A take bugun zuciyar Talba ya kara gudu, wanda hakan yai sanadiyar tunzura jininsa fushinsa da bacin rai suka hau a take.

“Ko ba komai Momy, na cancanci idan na kawo wani a gidan nan ki karramashi musamman ace mutumen daga bangaren mahaifiyata yake, babu abun da yake so a yanzu kuma nake kaunar kusanci da su kamar dangin mahaifiyata, na san da tana raye ba zata wulakanta yan'uwanta ba, dan haka a yanzu ma da bata

raye ba zan wulakanta jininta ba, na tashi ban san dangin mahaifiyata ba sai kadan daga ciki, a yanzu ne nake neman saninsu su kuma suke sani na”

Ya mike tsaye yana gyara rigarsa.

“Zata zauna a BQ, ba dan tana ballagaza ba, sai dan tana jinina”

Yana kawai nan ya fice daga dakin fuuu cikin bacin rai. Momy ta bishi da ido Amal kuma ta zaro ido tana kallon Momy.

“Na rantse da Allah bana son yarinyar nan i hate her so much”

“Wata kila akwai abun da dangin mahaifiyarsa suka karanta masa, kallin yadda yake min rashin kunya, akan wata lalatacciyar yarinyar, yar kauye”

“Kuma nan zai dawo da ita, zata zo ta takura mana”

“Sai idan kun so zata takura muku, akwai wanda ya isa ya takura da a gidan ubansa? Ku dai ya kamata ku takura mata har sai ta ji zaman gidan ya isheta”

Momy ta fada tana kallo Amal dake turo baki gaba tana jin haushin dawowar da zata yi a gidan.

“Je ki kira Leila”

Ta mike tsaye ta fice daga dakin tana sanye da gown din shadda kanta ba dankwali, ko da ta sauko kasa Leila ta saka air piece a kunnenta ta kure Volume tana kallon wata waka a YouTube.

“Leila Momy na kiranki”

Bata ji balle ta dago kai ma, sai da Amal ta maimaita haka sau hudu Leila bata dago kanta ba, hakan yasa Amal ta karasa kusa da ita ta kai hannu ta cire air piece din, Leila na dagowa bata tsaya komai ba ta mike tsaye ta dauke ta da mari mai kyau. Wani irin ihu Amal ta saka ta zuba da gudu upstairs, Leila ta saka hannunta ta cire baren daya sannan ta bi bayan Amal. Tana shiga bedroom din Momy ta jingina da kofar sai wani yauki take kamar kubewa, bayan ta shiga ciki tana sauraren yadda Amal ta fada ma Momy mari da tai mata, Momy ta kalleta a fusace.

“Ban ja miki kunne akan sakawa Amal hannu ba? Mike damunki ne Leila?”

“Momy abu ne nake a wayarta fa shine kawai ta cire min air piece, idan ma zata fada min kina kirana why not ta taba ni, amman abun da tai min wannan ai wulakanci ne”

“Hannu ya saba da daukewa a kan Amal, ba zan lamunta ba, next time kika sake yi mata wani abun zan baki mugun mamaki, ke shikenan ba ki iya controlling zuciyarki? Kawai da an bata miki rai sai ki ce zaki yi ma mutun abun da duk ya zo ranki”

“Amman Momy ya kamata ita na tana kiyayewa saboda ta san halina, sometimes ai ba da niya nake ba, kawai dai rai na ne yake baci”

Momy ta bude drawer gadonta ta dauko ATM dinta ta mikawa Amal.

“Shi kenan ki daina kukan, ka atm ki samu direba a cikin direbobin gidan nan ko brothers dinki wani ya kai ki yi shopping gobe da safe tun da yanzu dare yayi”

Ta karba da sauri tana mikewa tsaye a take kukam ya koma dariya har tana yi ma Leila gwalo.

“To Momy na gode, amman ni yanzu zan je gaskiya”

“Allah ya tsare”

“Amin”

Ta amsa sannan ta fice da sauri, haka take idan aka ce za a mata shopping ko taje tai jikinta har rawa yake, ba dan bata da kudi a nata account din ba, sai dan kudin wani sun fi dadin kashewa a gurinta. Sai da ta fice daga dakin sannan Momy ta kalli Leila.

“Talba ya fada miki zai dawo da yarinyar nan gidan nan?”

Leila ta ya mutsa fuska.

“Wace yarinya? Ba dai wannan ba?”

“Ita fa, yanzu yake fada min”

Leila ta karasa kusa da Momy ta zauna.

“Bayan kuma yace ta fi son zama can? What make him change his mind?”

“Oho, yace dai wai a nan zata samu karatu a can bata karatu”

“Wai miyasa yake son dawowa da ita nan ne?”

“Oho ai kina cikin mutanen da suka yi supporting dinsa ya dawo da ita”

“Eh amman saboda Madina ta bani wannan shawarar ne, kuma ina ganin kamar mafita ce a gare ni”

“Ai komai Madina ce take kitsa miki, idan Madina tace ni ban ma isa na ce ki dauka ba, komai dai Madina ce ta iya”

“Amman ai na share maganar da ya fadi cewar bata son nan din, kuma naga kamar ya fita sabgar yarinyar”

Leila ta fada sai Momy ta amsa ta cikin bacin rai.

“Beta fita ba, tun da yanzu gashi ya dawo mana da maganar, hakan yana nufin kenan yana zagayawa bayan idanuwanmu yana tafiya gurin dangin mahaifiyarsa, shiyasa ni na lura tun da aka saka date din auren nan baya wani farinciki, babu ma wani shirye shirye da yake yi, kuma babu wani abu daya canja daga halinsa ko irin ya nuna yana son auren sosai ko yana sonki, na san yana da girman kai, amman da can ai har maganar auren ya taba miki, yanzu kuma an

saka amman baya wani murna, daman ba sona suke ba, kuma ba son ki za su yi ba, wata kila hure masa kunne suke suna zugashi, shi ne yanzu za su dauko wannan yarinyar su bashi ya dawo da ita gidan nan saboda ta shiga tsakaninku”

Leila ta yi shiru tana nazari.

“To idan haka ne, Momy ki hana shi kawo ta a gidan nan mana kawai”

“Ni na isa? Yanzu yaje ya fadawa Daddynku ya kara min wani sakin? Yace ban isa na hana dansa abun da yake so ba a gidansa? Hmmmm ke dai Allah ya sauwake kawai”

Leila ta lula wata duniyar tana wani tunanin na dabam, sai kuma ta mike tsaye da sauri ta fice. Dakinta ta shiga ta fara safa da marwa wayarta a kunnenta tana ala ala Madina ta amsa kiranta, domin tun da rana take kiranta ba tai picking ba.

TALBA POV.

A mota ya labartawa Ali abun da ya faru, da kuma yadda sukai da Kaka.

“Amman Talba ina ganin kamar zamanta a gidan nan zai iya haifar muku da matsala, tsakanin kai da Momy da kuma Leila, da zaka dauki shawarata da ka sakata a wani gidan dabam ta zauna”

“Taya zan aje ta dabam? Bayan a gidan zan rika kwana ba? Kana ganin ita zata iya zama a gidan ita kadai?”

“Aa zaka iya sama mata wata wanda za su zauna tare”

“No ba zan yi haka ba, ni fa ba dan Daddy ba, da babu abun da zai hana ni bayyana aurena da ita, saboda abun da Momy take min”

“No karka ce zaka ga laifin Momy a nan ma, matar nan ita ta rene ka tun kana karami har ka girma, dole a yanzu da ka girma suke controlling dinka ta rika ganin kamar suna mata fin karfi ne”

“Suna controlling dina kamar ya? Please stop saying that, ni dai yanzu i just call to telling you yadda muka yi da Kaka so that ka fara nema mana gida da wuri”

“Okay ba matsala, amman please kar wannan ya zama wata matsala a tsakaninmu, na san yadda ka damu da yarinyar”

“Yes yanzu haka ma ina hanyar zuwa gidan Hajiya Laraba, ganinta kawai nake son yi, just to make sure tana lafiya”

“Oh boy ko kaje ba barinka zata yi ka ganta ba, ka hakura kawai har a kawo maka matarka”

“Ba zanje mata kamar yadda na saba ba, a yau kam da na san inda yarinyar nan take ba, ba zan iya kwana ba sai na saka ta a idona”

Ali yayi dariya

“Idan aka yi magana kace ba son ta kake ba....”

Be karasa ba, Talba ya tsinke kiran ya aje wayar, ya maida hankali gurin tukinsa, sai da ya shiga unguwar sannan ya rage gudun motarsa ya shiga slowly har ya isa bakin gate din gidan Hajiya Laraba har zai danna horn sai kuma fasa yaja motar ya faka ta gefe ya fito ya taka da kafa, at first daya kai hannunsa a karamar kofar gate din knocked zai yi sai ya ji kofar a bude, da alama a bude suke barin kofar ba kamar su ba da sai mutum ya kwankwasa za a bude masa. Turawa yai a hankali ya shiga, kai ya dagawa mai gadin yana sama gaisuwar da yake masa. Sannan ya nufi main door din, ita ma a bude ya same ta domin yana turawa ta bude kamar wacan karon da ya zo same ta a bude. Shiga yai ciki ba tare da sallama ba, not because of be iya sallama ba, but because of baya son sallama in a place like this da akwai mutane da yawa, saboda baya son daga muryarsa. Yaran Hajiya Laraba na ganinsa suka gane shi sai gaisuwa ta biyo, a nan kam dole ya bude baki ya amsa musu sannan ya bisu da kallo ko zai yi arba da Aminatu.

“Je ki kira Mamanki”

Ya ce da yar karamar yarta, sannan ya maida kansa kan wayarsa sai dai gaba daya hankalinsa baya kan wayar. Be dago ba har sai da Hajiya Laraba ta fito ta zauna a kujerar dake fuskarta tasa.

“Ikon Allah wai ashe dai Talba ka san gidan nan, Yanzu zuwanka na hudu kenan, dacan kam baka san ka takonka gaishe ni ba, sai mun manta da kai ma a cikin dangi”

Ya dan yi murmushi.

“Hajiya ai, kuma kuma da laifi, ba ku zuwa gidanmu ku maida ni bare cikin dangi”

“Aa kai ne dai baka rika mu da mutunci ba, da ace ka rike mu da kima kuma ita wacan uwar taka ta koya maka ai da yanzu an wuce gurin, amman mutum zai tashi ya tafi can ai sai ace kwadayi da neman wani abu ya kai shi”

“Yanzu dai komai ya wuce Insha Allah za a gyara, ya gida”

“Lafiya kalau ya aiki?”

“Alhamdulillah, daman Kaka ce tace na zo mu gaisa da Aminatu”

Hajiya Laraba ta yi dariya, tana jinjina halin Kaka bayan ta gama fada mata cewar kar a barshi ya ganta yanzu kuma sai ta fada masa yan zo nan ya ganta.

“To bari ta zo”

Hajiya Laraba na mikewa tsaye sai shi ma yai saurin mikewa.

“Bari na jirata a mota”

Kamin ta amsa ya nufi kofar fita, yana murmushin zuci, saboda ya samu cin ma abun da yake so. Fitowa yai ya ya jingina jikin wata mota dake fake a gurin, yana kallon kofar falon. After like 15min ya hango wata kyakkyawar bakar fata mai matukar haiba da cikar zati ta fito daga kofar falon hannayenta duka biyu rike da farantin ruwa dake dauke da gorar ruwan ita kanta sai kuma cup. A hankali take takowa cikin natsuwa da taka tsantsan, gaban gashinta a bude saboda lifayar data nada ta sauka a bayanta. He can't believe Aminatu ce har sai da ta karaso kusa da motar tana zuba wani irin kamshi, zagayawa tai ta inda take hango shi tsaye, Kamin ta karaso ya raba jikinsa daga motar yana mata wani irin kallo na mamaki.

“Assalamu Alaikum”

Ta masa sallama, and yes muryarta ya ji balle yace ba Aminatunsa ba ce, amman ta canja gaba daya kamar ba ita ba. Be amsa mata ba ya kai hannu ya karbi ruwan hannunta ta dora saman motar sannan juya ya duba dama da hadu ya ga babu mai ganinsa, sai ya janyota ya rumgume a kirjinsa, cos he was shocked and surprised wai Aminatu ce a haka, be ma san mi zai fada mata ba. Lumshe ido ta yi, sai tai lamooo a kirjinsa tana jin yadda tai marmarin kashin turarensa, not just his perfume even his voice da ganinsa ta yi kewar komai nasa kuma bata taba jin haka ba sai a yanzu da kanta yake shimfide a kirjinsa, hannunta ya lalabo ya saka yatsunsa cikin nata, because now he believe yayi missing dinta sosai, gashi ya ganta ba a yadda yai tsammani ba. Baya baya yai ya jingina da motar sannan ya saka dayan hannunsa ya shafa kanta ya dago fuskarta ya sumbanci goshinta ya sake sumbatar hancinta da kuma saman idanuwanta biyu da suke rufe, sai kuma ya fara shinshinar wuyanta kamshin turarenta na kai masa har cikin kwakwalwa, be san da ya zurfafa ba har sai da ta daga daga kirjinsa tai taku daya baya biyu kamin tai na uku ya kai hannayensa kan kafadarta sai kuma ya zagaye fuskarta da hannayen nasa, yana shafa lallausar fatar fuskarta da babban yatsansa.

“Shalele... Waya gyara ki haka.... Look at you... Your face....your skin... Wow..”

Ya fada cikin wani irin rada, a wata kasalalliyar murya kamar ba shi ba, idonsa na kan lips dinta da suka sha man lebe.

“Oh God”

Ya sake matsawa kusa da ita ya rumgumeta.

“I miss you so so so much”

Ya furta yana jin kamar be taba marmarin wani abu so much a rayuwarshi ba irin Aminatu. Ya dago da ita daga jikinsa.

“Zo muje ki raka ni gate”

Sai da ta kalli kofar falon sannan ta fara takawa, gaba daya idonsa na kan tafiyarta har suka isa gate din, da kasa ya bude mata ta fita sannan ya fito suka nufi gurin motar a tare. Key din hannunsa ya danna sannan ya bude mata front seat.

“Shiga”

Ta kalleshi da kyawawan idanuwanta.

“Aa ban fada mata zamu fita ba, ce min tai zamu gaisa kawai”

Tana maganar yana kallon yadda bakinta ke motsawa a shagwabe.

“Shalele kin yi kyau, kin canja you're so beautiful”

Ya furta yana kallon ilahirin fuskarta, hannu ya kai ya kama hannunta zai yi magana, sai aka haskesu da fitilar mota mai matukar haske, daga ita har shi kallon inda hasken yake fitowa suka yi. Sai a lokacin ya lura da mota ce ta haske su direct, gashi unguwar ba irin mai haske ce a ko'ina ba balle yace ya gane ko waye, sai dai da alama wanda yan shi ne domin an haske su ne da gangan kuma anki kashe fitilar. Aminatu ta kai dayan hannu ta rike rigarsa gabanta na faduwa nan da nan hawaye ya taru mata a ido.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

“Tsoro nake ji”

Ta fada jikinta na rawa a take idonta ya cika da hawaye. Dauke idonsa yai daga kallon motar ya kalle tare da kai hannunsa ya shafa kumatunta.

“Babu abun da zai same ki, ki kwantar da hankalinki”

Sakinta yai sai ta saka hannayenta duka biyu ta rikoshi tana mai tsananin tsoro, domin tun a wacan lokacin da barayin daji suka sace ta take a firgice abun ya kasa fita kanta, dan abu kadan idan ta gani ko ta ji sai hankalinta ya tashi.

“Karka bar ni nan”

Sake juyowa yai ya kalleta a karo na biyu.

“Babu abun da zai same ki, zan je na duba wanene”

Ta kara kankame shi da karfi.

“Idan suka maka wani abun fa? Karka je dan Allah”

Murmushi yai hakan nan kawai sai ya ji ta burgeshi, ko ba komai ta damu da lafiyarsa, and she hug him a rayuwarsa be san wata mace da ta taba rumgumarsa ba, Aminatu ce ta farko, ko Leila da take wayayyiya bata gigin taba shi saboda bata ga fuska ba.

“Okay”

Ya furta sannan ya kai hannu ya kwantar da ita kirjinsa, yana shafa bayanta a hankali ita kuma tai lamo kamar kyanwa tana kallon motae data kasa daina haskensu. Can kuma ya dago ta

“Zauna cikin mota, ko kuma ki shiga gida ki jirani na zo, ina son naga ko waye, babu abun da zai same ni”

“To kai addu'a amman kar ayi maka wani abu”

Ya fada hawaye na sauko mata, sakinta yai ya fara tafiya sai kuma tai saurin sake rikoshi.

“Zan rakaka”

Hannunta ya rike suka nufi gurin da motar take fake, sai motar ta fara ja da baya, hakan yasa Talba ya tsaya cak, sai motar ma ta tsaya yana kara step daya sai motar taja baya, idan ya kara sai motar ta sake ja baya, idan ya tsaya sai ta tsaya.

“Minno tsaya nan ina zuwa”

“Aa”

Ta fashe da kuka mai karfi tana rike da shi, duk yadda ya so ta sake shi ya karasa gurin motar kiyawa tai sai kuka take masa domin har ga Allah a tsarace take.

“Ya isa ba tafiya zan yi ba”

“To mu shiga gida tsoro nake ji sosai”

Ta furta tana kuka hawaye shar wasu na bin bayan wasu. Ya gyada nata kai, sannan ya saka hannunsa aljihu ya ciro wayarsa yai dialing number Ali, yana kara wayar a kunne sai motar tai baya da karfi da mugun gudu ta still tana haskensu har sai da ta kai karshen kwanar sannan ta juya dama ta hau titi da gudu. Ba mamaki ne kadai abun da Talba yake ba, har da tsoro domin be san waye ba kuma be san manufarsa ta yin haka ba, ya san shi ko kuma yayi hakan ne kawai dan ya daga musu hankali? Aminatu kam dukewa tai a gurin ta dafe kai tana kuka.

“Hello”

Ali ya amsa kiran bayan wayar ta dade tana ringing.

“Zan kira ka”

Talba ya amsa masa sannan ya kashe wayar ya duka ya kama hannayen Aminatu yana murmushi mai sauti.

“Sarkin tsoro, ko waye ma ya gudu ai”

Ya mikar da ita tsaye ya rumgumeta, for no reason yake jin dadin jinta a kirjinsa.

“Kukan ya isa Auta, daman kun iya kuka ko?”

Ta dan tsagaisa sai dai bata iya hana hawayenta zuba ba.

“Yanzu zaki kara ni ko kuma gida zaki koma?”

“Gida”

Ta amsa cikin kuka, sai yai murmushi ya shafa kanta yana kara matsar da hancinsa saitin inda gashin kanta ya bayyana yana shakar kamshin da kanta yake yi.

“Waya gyara min ke haka? Kin yi kyau sai kamshi kike ta ko'ina, kin kalli kanki a madubi kin ga yadda kika canja kuwa?”

Ta daga masa kai still crying.

“Oo na shiga biyu, wannan kuka haka?”

Ya dagato ya saka hannayenta yana share mata hawaye, sannan ya sumbanci goshinta, sai kuma ya hade goshinsu yana goga mata hancinsa a hankali, saurin dagawa tai ta dan ja baya saboda numfashinsa dake gwaraya da nata. Murmushi yai ya daga kansa sama ya sauke, shi kansa ya zurfafa da yawa, irin zurfafa da be san lokacin da yai haka ba, kuma be sa ran zai yi haka ba. Gyaran murya yai yana kokarin dawowa ainahin shi amman ya kasa, baya iya daure mata fuska ba ya iya nisanta kansa da taba jikinta he don't know why yake behaving wani kalar Talba dabam a gaban Aminatu.

“Muja na raka ki gida”

Ta juya, kamin tai taku na biyu ya kai hannu ya riko hannun, ko da suka isa gate yana murza yatsunta a hankali.

“Sake ni kar wani ya gani”

“Ba haram mu kayi ba you're my wife, ke matata ce”

Sai kawai ta bata fuska tana shirin fara yi masa kuka, sai ya sake hannun nata.

“Okay na saki, Autar kuka ba sai kin min ba”

Ta juya zata kai dayan hannunta ta tura gate din sai yai saurin rikonta ya juyo da ita, ya kai hannayensa duka biyu ya rike kunkurunta sannan ya dora goshinsa a saman nata yana kallon cikin idanuwanta.

“You're so special Aminatu, i mean so so so special, very special ban taba yi ma wata mace abun da nake miki ba, ban taba ganin mace na ji na rasa natsuwata ba irinki, ban taba tunanin zan zama haka ba, ban tana gwada aikata haka ga wata ba but look at me”

Ta kai hannayenta tana kokarin raba hannanyensa da kunkurunta da yake rike da shi yana murzawa a hankali, kwantar da fuskarsa yai ya raba lips dinaa biyu ya saka lip dinta na sama a tsakiyar nasa, ya tsotsa a hankali, sai kuma ya kama na kasan shi ma ya tsotsa, sannan ya cire bakinsa ya sake ta yai baya baya yana kallonta yana murmushi, for the first time in his life yawun wata mace ya gwaraya da nasa, and her lip is so soft and sweet.

Ita kam tsaye tai kamar hoto tana kallonsa ido kamar za su fito wajr su yi magana, tsabar mamaki da kuma tsoro daya same ta a lokaci daya, sai kuma ta kai hannunta ta taba lips din nata still tana kallonsa. Hannayensa ya daga mata yana mata bye bye.

“Shiga gida na ga tafiyarki”

Ta juya kamar marar kafafuwa ta fara tafiya, sai da ta tura gate din ta shiga sannan ta juyo ta kalleshi yana tsaye gurin motarsa yana kallonta har sai da ta saki kofar ta shige ciki, sannan ya sauke sanyayayiyar ajiyar zuciya bude motarsa ya shiga, yai mata key. Dayan hannunsa ya kai ya shafa kansa yana murmushi, zuciyarsa cike da nishadi da farinciki from nowhere, and now he realized he miss alot, ya dan cika bakinsa da iska sannan ya busar a hankali still smiling. Reaction dinta na dazun yake tunawa yadda ta tsaya tana kallonsa da mugun shock. Driving yake a hankali sai da ya iso gate din gidansu sannan mood dinsa ya canja sam ba zaka ganshi kace shi mutumen dazun a gaban Aminatu. Sau biyu ya danna horn aka bude masa gate sai ya shigo cikin gidan kamin a rufe gate din ya tsayar da motarsa ya sauke gilashin motar ya leko waje.

“Garba”

“Na'am”

Mai kokarin rufe gate din ya amsa da sauri tare nufo inda yake, sai police din dake zaune ya tashi ya nufi gate din ya karasa rufewa.

“Gani ranka ya dade”

“Dazun bayan na fita waya fita?”

“Amal ce kawai ta fita tare da Direba”

“Bayan ita fa?”

“Babu wanda ya sake fita, Sai Kabir daya dawo, ita har yanzu bata dawo ba”

“Da wace kalar mota Kabir da Amal suka fita?”

“Amal baka ce ta Hajiya, Kabir ma Baka ce gata can”

Ya nuna inda motar take, Talba ya dan yi shiru yana nazari, hasken motar ba zai bar shi ya ga kalar motar ba, sai dai da ace fara ce da zai iya gane fararce duk da kasancewar akwai duhu sosai a unguwar kuma inda motar ta tsaya yafi duhu.

“Okay tafi”

Yaja motar ya karasa inda ya saba farking ya aje motar, sannan ya bude ya fito ya nufi main door din shiga falon, wani bangaren na zuciyarsa na raya masa Amal ta wani bangaren kuma yana ganin kamar Amal ba zata iya masa haka ba, idan ma ita ce fitowa za ta yi ta nuna masa ta ganshi, duk wanda ya ganshi yai masa abun da yai masa babba ne ba karami ba, and he's very smart.
Door bell ya danna aka sai Mairo ta bude masa kofar tana masa sannu da zuwa, kai kawai ya daga mata ya shiga cikin falon yana sauke idonta akan Kabir dake hakimce saman kujera yana kallonsa fuskarsa da murmushi, Talba ya nufi dinning.

“Ango...”

Kabir ya fada, jutowa yai sai dai be ce nasa komai ba har sai da Sai da Mairo ta koma kitchen sannan Talba ya sake kallon Kabir.

“Kana tunanin abun da kai abun burgewa ne”

Kabir ya masa kallon rashin fahimta.

“Ban gane ba”

Talba ya bar dinning din ya nufo inda Kabir yake yana masa wani mugun kallo.

“Ba zaka gane ba, you're just fooling yourself, idan ma kana ganin kai mai wayo ne, to baka iya komai ba, stay away from me, babu ruwanka da rayuwata, kuma idan wani abu ya samu yarinyar nan kai ne sila”

“Wace yarinya?”

Daga shi har Kabir din stairs suka kalla, sai suka ga Momy a tsaye tana kallonsu sai dai bata karasa saukowa ba. Talba be ce komai ba ya juya ya nufi kofar fita daga falon, Kabir kuma ya bishi da kallo mamaki, domin gaba daya be fahimci inda ya dosa ba, saboda kawai yace masa ango? Kawai ya fada ne dan ya zolaye shi, domin a ganinsa shi ango ne shi tun da an saka date din aurensa da Leila, ba kalmar ango kawai ba, wace yarinya yake magana akai?

“Wace yarinya miya faru me ka masa?”

A lokaci daya Momy ta aiko masa da wadannan tambayoyin. Sai ya kalleta ya daga mata kafadunsa alamar be sani ba.

“No dole akwai wani abu, kuma ya san ka sani, da ba zai zarge ka ba, dan haka ina bukatar sanin komai”

“Ban san komai ba Momy ban ma san abun da yake magana akai ba”

Momy ta nuna shi da yatsa.

“Dole ne ka fada min ko minene idan ba haka ba, idan Daddynku ya dawo zan fada masa abun da yake faruwa”

Kabir ya mike tsaye

“Haba Momy sai kace wani karamin yaro? Ban san komai akai ba, ban san wace yarinya ba ce me yake magana akai i know nothing, excuse me”

Ya barta a tsaye gurin ya nufi kofar fita ransa a bace.

BATURIYA POV.

A cikin napep ta cire mask dinta sannan ta sauka ta mika masa kudinsa ta shiga gida. Da sallama ta shiga falon sai Umma ta amsa mata ciki ciki tana mata kallon tuhuma. Abun ka da marar gaskiya sai ta zauna saman kujera tana dan satar Kallon Umma.

“Daga Ina kike?”

“Gidan Yaya mana”

“Aisha a daga can ta fito, kuma tace baki je can ba”

Wani irin faduwa gaban Baturiya yai sai dai hakan be hana ta kankaro karyar da zata saka ta kare kanta ba.

“Aa naje sai dai ban dade ba na fito na tafi gidansu wata kawata!”

“Wace kawar? Ai baki fada min zaki je gidansu kawarki ba?”

“Haba Umma ni fa bazawara ce a yanzu ba budurwa ba, idan zan je gidan kawaye har sai na fada”

“Saboda kina bazawara shi ya baki lasisin yin yadda kike so? Ni fa kwana biyun nan ban ganewa kanki ba, kina yawan fita da sunan zuwa gurin Yayanku sai yawan fitarda kudi da ban san inda kike samo su ba, ina iya bawa yayana lasisin yin komai ban da aron hannu”

“Haba Umma kalle ni ki gani, tsakani da Allah ina da kyau fa, Wallahi kusan kullum idan na fita sai wani ya min magana, ina tsayawa a gidan Yaya ne nai zance da su, saboda yanayinsu yawanci yayan manya ne kuma kin san gidan yaya yafi wannan kyau da tsari, babu wanda zai ga ka fito daga gidan ya raina maka wayo, yan kudin nan ma da kike gani ta hannunsu nake samu”

“Idan haka ne, ai sai ki fitar da na aure, tun da kin cika idda”

Ta yi dariya.

“Karki damu Umma, nan ba da jimawa ba zan fitar da daya In shaa Allah”

“Allah ya nuna mana”

“Aamin, yau ma akwai wanda zai zo ammam shi gidan nan ma zai zo”

Ta amsa tana mikewa tsaye ta nufi hanyar dakinta, ita da Aisha. Umma dai bata ce mata komai ba, ta bita da kallo har ta shige. Tana shiga ta yaye gyalenta ta aje ta ciro wayarta a jaka ta kunna, tana kunnawa kiran Fahat na shigowa wayarta, da sauri ta danna picking ta kara a kunne tana murmushi.

“Dear”

Fahat ya jingina jikin kujerar da yake zaune yana dan daga gira.

“Na yi fushi, tun dazun nake jiran wayar nan a kashe”

“Ayyah dear kai hakuri, ni ma sai yanzu na lura tana kashe, dazun na zauna a kanta shine ta kashe kanta ban ma lura ba sai yanzu”

“To na hakura, ya kike?”

“Lafiya Kalau, kai fa”

“To gani dai, na dadi ba bakinciki, kin fita yau”

Ta dan yi jimm sannan ta amsa.

“Aa ban je ko'ina ba yau, ya akai yi?”

“Ba komai, kawai na tambaya ne, ya mama?”

“Lafiya kalau take”

“Bari na barki ki huta sai anjima zan kira”

“Okay i love you”

“I love you too”

Ya sauke wayar bayan ta aika masa da sumbata. Da mamaki take kallon wayar, domin be taba tambayarta ta fita ba, why yau ya tambaye ta? Ko dai ya ganta ne. No idan ya ganta zai mata magana ba zai kyaleta ba. Ta dan tabe baki sannan ta kira Ramlee.

“Ramlee da yaushe zamu je?”

“Idan an gama sallah isha'i kin san yafi sirri”

“To wai babu yadda za ayi mu hadu a wani gurin dole sai hotel? Bana son a gan ni ne”

“Babu wanda zai gan ki, idan zaki shiga ki saka mask kuma ai kin ga ba wani dade zaki yi ba, kuma gamawa zan dawo dake gida ko kuma shi ya kawo ki”

“Sai dai ke din, kai Umma ta fara sa ido fa, yanzu ma ta gama min magana, ko yanzu zuwan da zaki yi ki tsaya nesa da gidanmu yadda ba za a ganki ba, domin na fada mata wani zai zo zancen yau, kin ga idan mun fita sai na ce mata daukata yai muka fita yai min siye siye”

“Lalle kanki na kawo wuta Baturiya”

“Yau da gobe ai dole mu saba, yanzu ma yadda zan bullowa tafiyar nan da Alhaji nake domin ya nace sai ya tafi da ni”

“Wallahi Baturiya kina da farin jini sosai, yanzu kin ga wannan mutumen be san ki ba, labarinki kawai na bashi amman karki so ganin yadda ya haukace ya damu yana son ya ganki, duk ya matsu ku hadu”

“Ai dai yau za ayi ta ta kare, kuma haduwa daya zan yi da shi gaskiya, domin ina son na watsar da komai na maida hankali kan aure”

“Toooo amman kin fada masa kina da da?”

“Aa ba zan fada masa ba, kuma ba ganewa zai yi ba dan kin san masu kudin nan ba wani tsayawa suke bincike ba”

“To na mu dai addu'a ne kawai Allah ya tabbatar da Alheri”

“Amin idan na shirya zan kira ki”

Ta kashe wayar tana tunawa da Sultan saboda maganar da da Ramlee tai mata, sai yau kadai ta ji tana kewarsa, ta san yana can gurin danjin ubansa, kuma Faruk ba barinta zai yi ta ganshi ba.

“Allah sarki Faruk, ina son ka Wallahi amman talaucin nan ne matsala, duk mazan nan da nake mu'alama da su babu wanda ya kaika, ko yana ina ma yanzu Oho”

Ta fada sannan ta mike tsaye tana jin kewar tsohon mijin nata da gasken gaske, domin tana sonsa sai dai ba irin son da zai tana ta guje masa ba. Misalin takwas da rabi ta shirya tai kwalliya cikin wata shadda mai kyau sosai da aka mata kwaliya da stones. Amaimakon gyale sai ta saka hijab ta dauko jakarta ta saka facemask a ciki ta da wayarta ta fito daga dakin tana tafiya a natse.

“Umma zan fita ya zo”

Umma ta kalleta daga sama har kasa sannan ta daga mata kai, abun ka da mai nema sai ta fice da kuzarinta tana jindadi. Nesa da gidan Ramlee ta faka motarta kamar yadda Baturiya ta fada mata, da kafa Baturiya ta taka har ta isa gurin motar ta bude ta shiga.

“Kin yi kyau iya kyau, amman da Hijab”

“To ya na iya iyayen ne sai da haka”

Suka saka dariya har Ramlee zata ja motar Baturiya tai saurin dakatarda ita.
“Haba Hajiya dan jira mana, kar ace zuwa yai ya dauke ni kawai, kara dai mu yi kamar mun yi dan zance haka”

Sai da Ramlee tai jiran minti talati sannan ta tashi motar suka kama hanya, suna tafe suna hira har suka isa hotel din. Baturiya ta ciro face mask dinta ta saka

sannan ta mika hannu ta karbi number dakin da Ramlee ta mika mata a karamar takardar.

“Yana ciki yana jiranki”

“Okay”

Ta bude motar ta fita, rashin sabo da zuwa hotel yasa ta fara jin wani iri tana ganin kamar idon kowa yana kanta ko kuma wanda ta sani zai iya ganinta ko ta ganshi. Haka dai ta samu ta kusa ciki har ta isa bakin kofar dakin ta kwankwasa aka bude mata sai ta shiga gabanta na dan faduwa. Kai tsaye ta nufi gurin gadon zata zauna ta cire mask dinta, wanda ya bude mata dakin ya maida ya rufe sannan ya juyo suka hada ido. Mikewa tai tsaye da sauri tana kallonsa, shi ma da yake sanye da boxer da vest kallonta yake with shock.

“Rafi'a...”

“Yaya...”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ya furta sai tai saurin kawarda kanta A take gumi ya fara tarar mata. Mamaki yake ya akai be gane ba, tun a lokacin da Ramlee take kwatanta masa ita, kuma ta fada masa sunanta Rafi'a sai dai be kawo ita ce ba saboda be yi zaton yar'uwarsa na irin wannan sana'ar ba, ya kai ma ta san Ramlee? Zaune yai a gurin ya kifa kai da guiwa.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

MADINA POV.

Ta faka tsakar gidan tana kuka, tare da kai kanta ta jingina jikin sitiyarin tana kuka, gaba daya ji take kamar ta kashe kanta ta hutu. Jin ana kokarin bude gambun motar yasa ta dago kai ta kalli Mahaifiyarta.

“Madina ina kika je cikin daren nan? Karfe 11pm fa hankalina ya tashi”

“Kawai na fita na samu sukunin zuciya ne, Hajiya zan iya mutuwa Wallahi ni kadai na san abun da nake ji a raina”

“Sauko motar fito”

Hajiya ta rika hannun yarta cike da tausayawa, sai Madina ta sauko Hajiya ta kashe motar ta cire key din ta rufe motar sannan ta jata suka nufi cikin gidan. Amaimakon ta kaita dakinta sai Hajiya wuce da ita dakinta kai tsaye, har saman gadonta ta zaunar da ita sannan ta zauna.

“Bana fada miki idan kin tashi zamu yi magana ba? Sai kuma ki kama ki fita tun yamma har dare? Madina karki jefa kanki a cikin wata matsalar fa”

“Hajiya ina son Talba sosai, duk yadda zan misalta miki ba zaki gane ba, ni kadai na san abun da nake ji”

Idon Hajiya ya cika da kwalla.

“Ki yi hakuri Madina wannan jarabarwarki ce, haka Allah ya kaddara miki kaunar Talba ke kanki kin san ba zai yiyu ya fasa auren Leila ya aureki ba”

“Amman Hajiya baya son Leila”

“Baya son ta zai aureta? Lafiyarki kuwa Madina? Kar abun nan ya taba ki”

“Zai aureta ne kawai saboda Daddy, amman baya son ta, baya son ta Hajiya baya sonta...”

Ta fada tana kallon wani gurin daban sai kuma ta kalli Hajiya.

“Ko kuma yana yaudarar kansa ne...”

“Madina karki kuskura ki bari Leila ta gane, kina son Talba, karki yarda shi ma ya sani”

“Na riga na masa alama da haka, na fada masa wasu kalamai da ba su dace ba, ban san ni ba ko ya fadawa Leila tana ta kirana na kasa dagawa”

Ta lumshe ido hawaye na sauko mata.

“Hajiya ba zan iya jure Talba ya auri wata ba, ba zan iya ganinsa da wata ba, Hajiya ina sonsa sosai”

Ta fashe da kuka, sai Hajiya ta kara matsawa kusa da ita cike da tsananin tausayinta ta rumgumeta tana hawaye.

AMINATU POV.

Ta mamaki da tunanin abun da Talba yai mata ta kwana, hannunta a kan lips dinta.

Washe gari kamin tun da asuba suka tashi kamar yadda suka saba, sai dai bata shiga bandakin ba sai da kowa ya gama alwala, sannan ta shiga ta rufe kofar, kamin tai alwala sai da ta kai hannu ta taba lisp din tana kallon kanta a madubin daki. Sai yanzu take jin kamar ba gaske ba ne, kamar mafarki ne ta yi. Sai dai ta ji abun har cikin jikinta sakon da yake son isar mata ya isa har cikin kwakwalwar kanta, kuma ya samu muhali a zuciyarta ya zauna, ta kuma kasa daina jin soft lips dinsa a jikin nata, har yanzu tana jin motsin halshensa a bakinta, and his perfume is wow ta kasa daina jin kamshinsa. Alwala tai ta fito ta yi sallah, for no reason ta ji kyiyar yin azkar yau, gaba daya tunanin abun da Talba yai mata ya dauke mata Hankali, sai ta nade carpet din ta aje.
Haka ta wuni ciki tunanin abun da Talba yai mata, minti daya biyu sai ta kai hannu ta taba lisp dinta, can kuma sai tai murmushi. Ta soma jin kunyar kanta da mutanen gidan kamar an fada mata sun san abun da akai mata.
Misalin tara daidai na dare mai gadin gidan ya kwankwaso kofar falon, Hajiya Laraba tai masa iznin shigowa sai ya shigo ya risina yana fadin.

“Hajiya wai Talba yana sallama da Aminatu a waje yace ta zo da sauri sako zai bata”

Aminatu da hannunta yake cikin plate din tuwo ta sauke kai kasa gabanta na faduwa, abun da ya faru tsakaninta da Talba a jiya sai ya dawo mata.

“To gata nan zuwa, yau ba zai shigo ba kenan”

Hajiya Laraba ta amsa, sannan ta kalli Aminatu.

“Tashi kije idan kin dawo sai ki karasa cin abinci, amman karki dade kina karbar sakon ki juyo”

Aminatu ta mike tsaye ta nufi dakin da suke kwana, ta shiga bathroom din ta wanke hannunta sannan ta fito ta dauki Hijab dinta ta saka ta fito a natse ta ratsa falon ta fice. Bata ganshi harabar gidan ba kamar yadda ta ganshi a jiya, sai kawai ta doshi gate a tunaninta ya tsaya a can ne kamar jiya da ya aje motarsa. Da tunanin abun da zai mata a yau ta isa gate ta bude ta fito, sai tai arba da wata farar mota daidai inda Talba ya faka farar motarsa a jiya, tsayawa tai kallon motar sannan ta karasa gurin motar ta tsaya, banbancin wacan motar da wannan kadan ne, wacan ta Talba ta dan fi tsayi kuma tana da farin gilashi tsabanin wannan dake da bakin gilashi. Bude mata front seat akai ba tare da ta ga wanda ya bude mata ba sai ta leka ciki wata fuskar ta gani mai dauke da mask daya rufe ilahirin mamalakin fuskar, irin mask din da yan fashi suke sakawa, sai ta dago da sauri kamin tai wani yunkuri ta ji an rike ta gam ta bayanta tare da kai katon hannu a rufe mata baki, sannan aka bude bayan motar da karfi aka saka ta a ciki, a nan tai arba sa wani mai mask din hannunsa rike da zungireriyar wuka yana nunata da ita tare da yi mata alama da tai shiru, slowly suka ja motar sukai baya baya sai da suka yi nisa da gidan sannan suka juya suka hau babban titi, mutumen dake rike da ita ya ciro wani bakin kyale ya daure mata idanuwa. Kamar wanda akai wa iyaka da magana haka ta kasa furta komai ko da kuwa roko ne, sai dai bugun zuciyarta ya fara aiki fiye da kima.

LEILA POV.

10am tana zaune tana karyawa wayarta tai kara alamar kira, dubawa tai tana ganin Number Madina sai tai saurin picking.

“Lafiya na yi ta kiranki jiya baki daga ba? Har ina cewa yanzu idan na gama karyawa zan je na dubaki ko lafiya”

Madina ta yi murmushi.

“Lafiya Kalau maganin mura na sha, sai bachi ya dauke ni tun da rana nake bachi har dare, sallah kawai nake iya tashi na yi”

“No wonder, amman dai yanzu kin samu lafiya ko?”

“Gani ma na shigo office amman ban ga angonki ya shigo ba”

“Yanzu ya gama karyawa ya koma bangarensa, maybe zai sake shiri ne kamin ya fito”

“To yayi kyau, amman Leila da ni ce na kira wayarki baki daga ba, ba zan iya kwana ba sai na ji lafiyarki”

“Ni ma fa yau nake son zuwa na duba, ke akwai ma labari fa, wai Talba zai dawo da yarinyar a nan?”

“Haba dai”

A nan ta tsakura mata yadda sukai da Momy.

“Allah yasa dai kar ta kawo muku matsala”

“Hmm tama isa, sai dai ta kawowa kanta, domin zaman kaya zata yi, and ina da wani babban labari da zan baki, kuma akwai abun da na shirya amman maganar ba zata yi a waya ba, and maganar tafiya na gyaran jiki ina son mu yi shawara kamin Momy ta fara kawo min nata”

“Okay zan shigo idan mun ta so aiki”

Daga hala suka yanke wayar. Talba be shiga office ba ai kusan goma, ba Madina kadai ba kowa dake kamfanin idan ya kalleshi zai lura da yana cikin nishadi ba kamar kullum da yake shigowa fuska babu annuri ba. Ita kanta Madina ta yi mamakin yadda ya sake mata fuska yana ta yawan murmushi tana shigowa ya ambaci sunanta kuma ya karbi files din data kawo masa da kansa, tsabanin baya da sai dai ta aje kan tebur. Kamar an mata kyauta wata rayuwa haka ta ji, saboda ganin masoyinta cikin farinciki sai ya saka ita ma ta samu kanta cikin farincikin, a take ta ji duk damuwarta ta wanke, domin bata yi zaton haka ba, ta yi tunanin ko zai koreta ne ko kuma ya tsawalla mata saboda kalaman da tai masa, sai dai ta lura kamar hakan be dame shi ba.

Ana sallame sallah Magariba, Leila ta sauko falon ta zauna tana taunar chewing gum, hankalinta kuma yana kan Zulai da Mairo dake aikin jera abincin dare, dan tabe baki tai ta dauke kai a rayuwarta ta tsani ganinsu a gidan ba tare da sun tare mata komai ba. Sau biyu ana taba door bell din kofar sannan Zulai aje aikin da take ta nufi kofar, wani uban tsaki Leila ta ja.

“Oh na dauka ai jiran kuke sai na je na bude kofar, kamar ba aikin da aka dauke ku kui ba kenan”

Mairo ta kalleta kawai ta dauke kai, Zulai kam ko Juyowa ba tai ba har ta isa gurin kofar ta bude ta sai mai gadin ya miko mata envelop.

“Ga sako in ji wani wai a bawa Hajiya Leila”

Zulai ta karba sannan ta maida kofar ta rufe ta nufo inda Leila take zaune ta mika mata.

“Ga sako ance a baki”

Leila ta kalli envelop din ta yatsina fuska.

“In ji waye?”

“Yusufa ne ya kawo ban san ko waye ya bada ba”

“Dora ta a nan”

Ta fada tana dauke kai, Zulai ta aje a inda ta nuna mata sannan ta nufi dinning dan karasa abun da suke yi. Leila ta cigaba da lasa wayarta na kusan minti ashirin sannan ta aje wayar ta dauki envelop din ta cire salatip din tana duba abun da ke ciki, can kuma ta saka hannu ta ciro dankwali da aka linke yayi datti sosai ga kasa a jiki. Jefar da shi tai da sauri ta mike tsaye with shock har haki take, wani irin ihu ta saka wanda ya saka Mairo da Zulai kallonta, sai kuma tai sauri ta rufe bakinta ta nufi upstairs da gudu tana kiran Momy.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

LEILA POV.

Kamin ta karasa hawa sama har da zamewa tai ta fadi, ta tashi da gudu ta banki kofar dakin Momy ta shiga da gudu. Momy dake tsaye jikin wardrobe ta juyo da sauri tana kallonta, Leila ta karasa kusa da ita ta kama hannayenta ta rike jikinta na mugun rawa.

“Ke Lafiya?”

Sai ta nunawa Momy kofa ta kasa cewar komai, kafafuwanta kuma suka kasa daukarta sai ta zube a gurin rike da hannayen Momy.

“Talk to me miya faru?”

“Momy.... Momy... Envelop aka.... Aka... Kawo... Da na.... Bude... Sai... Na... Ga dankwali.... Da....kasa a jiki..... Kamar kamar kamar na Baaba...”

A rarrabe take maganar saboda tsoro, daga karshe kuma sai ta fashe da kuka. Wani irin faduwa gaban Momy yai sai ta zare hannayenta daga rikon da Leila tai mata, tai baya baya ta zauna kan gado with so much shock tana kallon wani bangare na daki, can kuma ta kalli Leila.

“Waya kawo sakon?”

“I don't know, i don't know, Zulai ce ta karbo”

Momy ta mike tsaye da sauri ta fice daga dakin kamin ta karasa saukowa ta ji motsin Amal a bayanta ita ma tana saukowa.

“Momy na ina sallah na ji Leila ta yi ihu ta kiraki kuma ta daki kofar dakinki da karfi miya faru?”

Momy ta tsaya cak sannan ta juyo ta kalli Amal tana kokarin boye tashin hankalinta.

“Shiga dakinki ki kulle”

“Yan fashi ne suka zo”

Ta tambaya tana zaro ido, sai Momy ta daka mata tsawa.

“Yan ubanki ne suka zo, go back to your room i said”

A yadda Momy tai mata maganar ta san she's serious domin babu alamar far'a a tare da ita, and bata ji ma Momy ta taba zaginta sai a yau. Juyawa tai ta haye saman tana yi tana waigen Momy har ta isa bakin kofar dakinta, sannan ta tura ta shiga. Sai da Momy ta tabbatar ta shiga sannan ta juya ta karasa sauko tana rabon ido a falo. Can ta hango Envelop din a tsakiyar falon da kuma dankwalin, da tsoro Momy ta fara takawa zuwa inda dankwalin yake tana kallonsa, kaminnta duka cikin karfin hali ta dauki dankwalin, daddabe yake da kasa ta kana gani kasan kasar ta dade a jikinsa. Sai kuma ya juya ta dauki envelop din ta bude ciki ko zata samu wani abu, har kasa ta zazzage bata ga komai ba. Kofar kitchen ta kalla duk ta tasan masu aikinta basa a nan irin wannan lokaci domin da zarar sun

gama jera mata abincin dare suke ficewa zuwa BQ, bata basu damar tsayawa a falon ma balle kuma zama.
Mamaki take waya aikata haka? Miye manufarsa na aikata hakan? Dankwalin Baaba da gaske ko kuma wani ne yake son yi musu wasa da hankalinsu, idonta ta kai kan dankwalin tana kara tantancewa, and yes dankwalin Baaba ne. Da sauri ta saka dankwalin a cikin envelop din ta nufi kofar fita daga falon, bata ko tsaya saka talkami ba haka ta fita ta bar kofar a bude, BQ ta nufa, tun kam ta karasa ta kwalawa Mairo da Zulai kira, sai ga su sun fito da sauri cikin tsoro a tunaninsu ma wani laifin suka yi.

“Waya karbi sakon dazun?”

“Ni ce Hajiya”

Zulai ta amsa Mairo kuma ta nuna ta.

“Waya bada sakon?”

“Mai gadi ne”

“Yusufa”

“Be ce miki komai ba da ya mika miki sakon”

“Cewa kawai yai gashi a bawa Hajiya Leila”

Momy ta daga musu kai sannan ta juya ta nufi gate din, gurin da masu gadin gidan suke zama ta nufa suna ganinta sai duke suka mike tsaye wadanda suke cikin daki ma suka fito waje, domin police uku da masu gadi biyu ke kula da gidan.

“Wa aka bawa sakon nan?”

“Ni ne ranki ya dade”

Yusufa ya amsa.

“Waya baka sakon nan?”

“Wallahi ban san shi ba, ya dai kwankwasa gate na leka na ga mutun a tsaye ya faka motarsa gefe, sai ya miko min yace gashi dan Allah na bawa Leila, ba zai samu shigowa ba sauri yake!”

“Zaka iya gane fuskarsa?”

“Aa Wallahi Hajiya, saboda yana sanye da da abun nan da ake yayi na rufe fuska, Mask kuma ya saka facing cap da bakin gilashi, amman ya da dan jiki haka kuma dogo ne sosai motarsa kuma ja ce 406”

“Amman kai wani irin wawa ne Wallahi jahili, ko da yake ba kai kadai ba har da sauran ma, taya wani zai kawo sako ba ku tsaya kun bincike shi ba? Idan kuma Bomb ya kawo fa? Ko kuma yana dauke da bindiga fa? Wani irin tsaro kuke ba mu ne? Miye amfaninku?”

Cikin daga murya sosai Momy take musu fada, suka hau bata hakuri da fadin za su gyara a gaba.

“Hajiya akwai abun da be dace ba ne a cikin envelop din? So that's mu dauki mataki tun yanzu”

Daya daga cikin police din ya tambaya. Sai ta amsa masa da karfi.

“No stay out of this babu komai, ku kula da aikinku kawai”

Tana kaiwa nan ta juya ta nufo kofar falon da tunanin wanda ya aiko da sakon da kuma nufarsa ta yin haka, tana shiga cikin falon ta maida kofar ta rufe sannan ta kalli Leila dake tsaye ta rumgume hannayenta tana kuka.

“Momy kashe ni za ayi”

Momy ta girgiza mata kai da sauri ta karasa kusa da ita tare da aje envelop din kan kujera.

“Ki daina fadar haka, wannan wace irin magana ce? Ba zan iya bari a kashe ki ba, ba zan haka ta faru ba, ko da kuwa komai dana tara zai kare”

Ta karasa tare da rumgume ta tana hawaye.

“Put this in your mind ba da gangan kika aikata ba, ba kina nufin ki kashe ta ba”

“Momy tsoro nake ji, idan Daddy ya sani ko Talba...”

Ta fada cikin kuka tana kankame Momy, bata karasa ba Momy ta dakatar da ita.

“No one is gonna know, no one...”

Sannan ta saketa ta dauki envelop din ta rika hannunta suka hau sama. Momy na shigewa Amal dake labe jikin kofar dakinta ta bude a hankali ta fito taje jikin kofar Momy ta kara kunnenta. Momy har ta zauna sai kuma ta tashi ta isa gurin kofar ta bude a hankali sai kuwa tai arba da Amal a tsaye tsamo tsamo tana kallon Momy.

“Momy daman cewa na yi yanzu zaki ci abinci ko sai zuwa anjima...?”

Momy ta watsa mata wata uwar harara wanda ta saka ta juyawa da sauri ta koma dakinta. Bin bayanta Momy tai har cikin dakin ta cire key din dakin sannan ta fito ta rufe ta daga waje ta cire key din ta nufo dakinta. Shigowar da Momy tai a dakin ma sai da Leila ta zabura saboda tsoro domin a firgice take gaba daya. Momy ta rufe kofar sannan ta karasa kusa da ita ta zauna.

“Waya san da maganar Baaba bayan ni da ke da Kabir da Amal?”

Ta girgiza kai da sauri.

“Babu”

“Think... Dole akwai wanda ya san da maganar nan!”

Har ta fara girgiza kai sai kuma ta ce.

“Ma.. Madina....”

Momy ta daga hannayenta.

“Leila ke wace irin yarinya ce? Ban gargade akan kar kowa ya ji maganar nan ba? Ke baki da sirrin kanki dole sai kin bude cikinki a gurin kawa”

“Momy Wallahi Madina ba zata iya yi min haka ba, i trust her kuma Madina mace ce ba zata yarda tai risking rayuwarta ba for this? Mi zata samu idan ta yi?”

“Okay Kabir ne zai yi ko Amal? Ko kuma ni kaina?”

“Aa amman me Madina zata samu idan tai min haka?”

“Waya sani, amman duk wanda ya fara shirya wannan abun yanada manufa ta yin haka”

“What if lokacin da muke rufe gawar wani ya gam mu? Ko kuma mai gadin gurin ne?”

Momy ta yi shiru tana nazari if could be possible wani ya gansu ko kuma mai gadin gurin yai haka saboda ya samu kudi. Da sauri ta tashi ta nufi inda wayarta take ta dauka ta shiga contact dinta, thinking of da wane suna tai saving din number mai gadin gurin, haka tai ta yawo a muhallin bata samu sunan ba.

“Zan je yanzu na duba shi ki zauna a nan”

Leila ta yi saurin dakatarta da ita.

“Momy karki je cikin daren nan, baki san abun da suka taka ba, kar su kara yin wani abun”

Momy ta koma ta zauna jiki a sanyeye, can kuma ta kalli Leila dake hawaye sosai ta ce.

“Ki tashi ki wanke fuskarki ki kwanta, karki bari kowa ya gane kina cikin damuwa, kuma ki kwantar da hankalinki, indai ina raye babu abun da abun da zai faru”

Ta gyada kai a hankali sannan ta yunkura ta tashi har lokacin jikinta rawa yake kuma tsoron be bar jikinta ba. Bathroom din Momy ta shiga ta kunna fanfo da niyar wanke fuskarta sai kawai ta fashe da kuka tana nadamar abun da ta aikata, event though ba da niya tai ba. Kawai dai ta ture Baaba ne saboda ta fusata, a jikin madubin ta rika kallon kanta idanuwanta har sun kumbura, ga hawayen sun ki su tsaya mata, kallon tap din tai kamin ta kai hannunta ta debi ruwan ta watsa a fuskarka, sai kuma ta sake fashewa da kuka, ta duke a gurin tana rike da tap din.

“Leila wannan abun da kike kina tonawa kanki asiri ne kawai, ki wanke fuskarki ki fito kamin na bude Amal”

Momy ta fada daga can cikin dakin, sannan ta fice. Cikin karfin hali Leila ta mike tsaye ta wanke fuskarta sannan ta fito ta nufo gadon Momy ta zauna tana ta jin

tsoro, sai kallon kofar dakin take. After like 20 min Momy ta shigo rike da tray dake dauke da fruit da madara sai kuma ruwan mai sanyi.

“Ki ci sai ki sha magani ki kwanta”

“Bana iya cin komai Momy”

“Sha madarar ko kadan ne”

Ta dauki cup din madarar ta kai baki ta kurba kadan, sai ta ji ta kamar babu komai a ciki, kamar ba madara ba. Da sauri ta aje ta dauki ruwa ta sha da yawa, Momy ta miko mata maganin ciwon kai.

“Sha”

Ta karba ta sha, sannan ta haye gadon gaba daya ta kwanta jikinta da zafi wani zazzabi ya taso mata ga sanyi da take ji. Momy da kanta ta janyo blanket ta lullubeta.

HAJIYA LARABA POV.

Har ta gama cin nata abincin Aminatu bata dawo ba, sai dai bata ce komai ba saboda tana tunanin ko ya tsayar da ita ne, kamar yadda yai jiya da ya zo, daman ta san za a rina tun da ya ga an gyara masa mata.
Misalin tara ta tashi ta shirya gurin kwanciyar yaranta da suke kanana daman ta saba musu idan zaku kwanta sai ta musu wanka ko kuma ta saka yayarsu tai musu. Bayan sun kwanta ta fito falon tana hamma.

“Rilwan je waje ka ce Aminatu ta shigo gida haka nan”

Rilwan din ya amsa tare da aje remote din hannunsa ya tashi ya fita, tafiya yake a hankali har ya isa gate din ya bude ya leka. Wayam babu kowa babu mota balle kuma Aminatu. Juyowa yai ya dawo cikin gidan.

“Mama ban ganta ba, kuma ban ga ma mota a gurin ba”

Tun daga bakin kofar falon ya fada mata sannan ya karaso ya zauna.

“Kila daukarta yai suka fita, shiyasa ya ki shigowa cikin gidan, ko kunya baya ji, ita kuma wata salula sai ta bishi su tafi”

Ta karasa tana dan jan tsaki, sannan ta dauki dankwalinta dake kan kujera ta daura, ta cigaba da kintsa falon. Wasa wasa har goma ta wuce sha daya saura Aminatu bata dawo ba, a nan ta fara damuwa tana tunanin wata kila wani abu yake mata shiyasa be dawo da ita ba. Misalin Sha daya daidai Mai gadin ya kwankwaso kofar falon, a lokacin tana zaune tare da mijinta ta saka shi a gaba yana cin abinci tana masa hira. Yunkurawa tai ta tashi ta bude kofar falon.

“Garba”

“Na'am Hajiya, na ce a rufe gidan ko kuma mu tsaya jiran bakuwar ta dawo?”

“Aa dan jira bari na kira shi, sai mu san idan can zata kwana”

“To”

Ya amsa sannan ta saki kofar ta dawo tana fadin.

“Mazan yanzu dai kam ba su da kunya Wallahi, tun fa da isha i ya fita da yarinyar har da wani cewa ta zo ta karbi sako ashe so yake.ya dauketa su bar gidan gaba daya”

“Tsakani da Allah ma yama yi hakuri fa, idan ba shi ba yaushe za a aura maka mata a hana ka tarewa da ita har na tsawon wata uku ko hudu ma ko? Ai yayi kokari ki barshi ya huta sa amaryarsa”

Mijinta ya fada yana dariya.

“Ai kiransa kawai zan yi na ji idan can za su kwana kar sai mun rufe gate din kuma ya dawo”

“Tun da ya kai yanxu kam ai kin san ba zai kawo ta yau ba, musamman idan ya san yayi aika aika, ki kyale shi kawai sai da safe”

“Shi ma ai rashin hakuri ne, tun da an kusa kai masa matar ba sai ya jira ba”

Ta fada tana jin haushin abun da yai, sannan ta kira Garba a waya tace ya rufe gate din.

Washe gari ta yi tunanin ko zai dawo da ita da safe amman be dawo da ita ba har kusan azahar hakan yasa ta yanke shwarar kiransa.

TALBA POV.

Sai a waje ya tsaya yai sallah Isha'i sannan ya shigo gidan. A inda ya saba fakin yai farkin sannan ya bude motar ya fito. Bangarensa ya nufa sai da ya fara yin wanka ya saka boxer ya dora jallabiya sama sannan ya fito yana ta kamshin turare ya nufo bangaren Momy. Sau daya ya danna door bell din ya jaya ya tsaya sai Momy ta bude masa.

“Barka da dare”

“Barka dai”

Ta amsa masa cikin yanayin damuwa, kallonta kawai yai ya dauke kai ya nufi sofa ya zauna. Da farko ta yi niyar zama a falon sai dai sanin Talba zai iya damunta da kallon tuhuma ko tambayar abun da yake damunta yasa ta nufi upstairs. Da ido ya bita har ta haye sannan ya mike tsaye ya nufi dinning yana tunanin yanayinta a yau, ganin Momy cikin damuwa abu ne dake daga masa hankali domin ya san halin Momy ba komai take bari ya zama mata damuwa ba, tana son rayuwarta da jikinta hakan yasa take ba su kulawa na musamman, idan har damuwa ta bayyana a fuskarsa to ya san ba karamin abu ba ne. Kujera ya ja ya zauna ya dauki karamin tea cup ya soma hadawa kansa tea. Cube din sugar daya ya saka ya dauki tea spoon ya motsa sannan ya kai tea bakinsa, cup din na taba lips dinsa ya tuna da Aminatu daman wunin yau a cikin zuciyarsa ta wuni, abu daya da biyu sai ya tuna abun da yai mata da reaction dinta.

“Ya Talba”

Ya juyo cikin izzar da be san yana da ita ba ya kalli mai Amal dake saukewa upstairs sanye da riga da wando na material.

“Little Sis”

Ya sakar mata murmushi, ita ma murmushin ta mayar masa, ta karasa taja kujera ta zauna.

“Wai sai yanzu zan ci abincin dare yunwa nake ji, tun dazun Momy ta rufe ni daki”

Ta fada ne kawai saboda tana son ta yi masa gulmar, domin ko kadan abincin dare be dame ta ba wani lokacin sai dai ta sha ruwa kawai ta kwanta ko tea, amman yau ita ce da fadin bata ci abincin dare sai kace wanda ta kai karfe daya kulle a daki. Ta yi hakan ne kawai domin ta ji idan Talba da Leila sun yi fada ne ko kuma Momy da Talba ko Daddy, bata san dalilin Momy na rufeta ba, gashi kuma ta ji Leila nata kuka kamin Momy ta rufeta a dakin.

Jin Talba be ce mata komai ba yasa ta kalleshi ta ce

“Ya ko dai kun yi fada ne? Na ga ran Momy ya bace sosai har tana zagi kuma ka san Momy bata zagi”

Talba yayi shiru yana nazari abun da Amal take fada masa, compare to yanayin da ya ga Momy a yau.

“Aa ba mu yi fada ba”

Ya fada yana tunanin motar data haske su jiya.

“Little Sis jiya ina kika je?”

“Shopping direba ya kai ni?”

“Kun biya wani gurin?”

“Aa”

Ta kai lomar tuwon a bakinta. A iya saninsa Direba ba zai fara masa haka ba ko da kuwa Amal ta bashi umarni, idan ma Amal ce ta ganshi ba zata gudu ba, zata fito tai magana da shi ne saboda gulma, and he don't think Momy zata iya rike maganar bata ce masa komai ba har yanzu, amman idan ba haka ba miya saka Leila kuka? Aje cup din yai ya mike tsaye ya nufi upstairs Amal ta bishi da kallo tana ji kamar ta tashi ta bi bayansa, sai dai gudun kar Momy tace ita tai masa gulmar yasa ta zauna ta cigaba da cin abincinta. Sai da ya fara kwankwasa kofar dakin sannan ya tura ya shiga, a mugun firgice Leila ta tashi zaune tana kallonsa, Momy ma dake zaune kan carpet tana waya kallonsa tai. Karasawa yai kusa da Momy ya zauna sai ta yanke wayar da take tana kallonsa da dan faduwar gaba, ba mamaki Amal ta fesa masa.

“Momy akwai wata matsala ne?”

“Kamar ta me?”

Ya kalli Leila wacce ta koma ta kwanta sannan ya sake kallon Momy.

“Na ga kamar kina cikin bacin rai”

“Na komai, Leila ce bata jindadi”

Sai a yanzu ya daina mamakin ganinta a kan gadon Momy a kwance, Amal ce ta mai mai wannan dabi'ar ba ita ba.

“Allah ya sauwake, kin sha magani?”

Ya tambaya yana kallonta, he did what he did saboda a gaban Momy ne kar tace be nuna mata kulawa ba, because ya san ba amsa masa Leila zata yi ba, and he's right bata amsa masa din ba sai ma juya baya da tai. Mikewa yai tsaye ya fice daga dakin tare da ja musu kofar dakin. Downstairs ya nufo kamin ya karasa saukowa wayarsa tai ringing, sai ya saka hannunsa aljihu ya ciro wayar ya amsa kiran da Ali yake masa.

“Talba na yi magana da wani yace zai zama mana gida mai kyau, amman za a bashi 200 per two days kuma wai duk abun da ya bata ko ya fashe za a biya”

“Okay akwai komai a ciki?”

“Komai akwai, na ma bashi kudin kuma na fada masa on Saturday zamu kawo Amarya a gidan yace kamin lokacin zai hannata mana keys din gidan, akwai ma mai gadi a gidan”

“Okay Allah ya kai mu”

“Aamin”

Har Talba yayi kamar ya fada masa abun da ya faru jiya akan motar nan sai kuma wata zuciyar ta hana shi, sai kawai ya katse kiran ya saka wayar aljihu.

“Little Sis zan je na kwanta, it past 10, ke ma ki kwanta da wuri saboda gobe a akwai school”

Ya fada yana kallon katon agogon dake falon makkale kamar zai yi magana.

“To ai mun kusa gamawa mu huta, Ya me take yi ma kuka?”

Ya dan daga fadunsa.

“Wai bata da lafiya, tana dakin Momy ki shiga ki mata sannu”

“Toh”

Ya daga mata hannu sannan ya nufi kofar falon. Bangaren Daddy ya nufa tana taba kofar ya ji ta a bude sai ya tura ya shiga, ya nutsa kai har karamin falon Daddy inda ya same shi tsaye yana kokarin cire babbar rigarsa.

“Daddy yanzu ma ka shigo kenan?”

“Yes Momynka ma bata san na shigo ba, ba kai bachi ba”

Talba ya saka dariya daman ya san sai Daddy ya zolayeshi, abu ne mai wahala a wuni Daddy be zolayeshi ba sai idan basa tare.

“Haba Daddy sai kace yaro karami, karfe goma zan kwanta gashi nan ma kai sai yanzu ka shigo”

Daddy ya zauna yana kallonsa da fuskar zolaya.

“Kai yaro ne mana, har gobe kamar jariri nake ganinka, kuma ka san ba ka aje yara ba balle ka ce ka girma a wannan sai yaya”

“Ai dai na kusa Daddy a daina min gori”

Daddy yayi murmushi mai sauti yana kallon Talba cike da kauna, kana ganin fuskarsa ka san ba karamin farinciki yake ji ba idan yai arba da dansa Talba.

“To ya aikin? Ango”.

Talba yayi dariya.

“Alhamdulillah, Daddy ka san maganar yarinyar da na taba maka? ata dawo gidan nan da zama?”

“Yes yes miya faru?”

“Zata dawo din ne yanzu, ina son na sakata a makaranta, domin a can ba karatu take ba”

Daddy yayi murmushi da shi kadai ya san ma'anarsa zuciyarsa na raya masa wani abun.

“Mu'az, ba matsala kana da ikon kai duk abun da kake so a gidan nan”

“Na gode Daddy, bari na barka ka huta, sai da safe”

“Allah tashe mu lafiya”

“Aamee”

Ya amsa sannan ya fice, tafiya yake kamar wanda baya son taka kasa har ya isa bangarensa, yana shiga ya cire dogwar rigar jikinsa, ya kashe wutar dakin sannan ya gabatar da azkar din kwanciya bachi ya kwanta. Bachi yai mai kyau kuma mai dadi kusan rabin mafarkina na Aminatu ne, abun da be taba ba, domin ko a lokacin da take asibiti be taba mafarkinta ba. Amman a yau yayi mafarki event though ba zai iya fadar yadda mafarkin ya zo masa ba, he saw her kuma ya ganta cikin farinciki kusan abun da yake mata fata kenan.

Washe gari da wuri ya shirya saboda yana da meeting, hakan yasa be tsaya gida ya karya ba, sai dai saurin da yake ba hana shi ya gaisa da Momy dake aikin hadawa Daddy breakfast sannan ya fito ya shiga bangaren Daddy ya gaisa da shi. Daman komai saurin da yake baya fita sai ya gaisa da Momy, Daddy ne wani

lokacin baya tsayawa gaisawa da shi saboda baya son shiga bangaren idan ba tashi ba.
Misali takwas da rabi shigo kamafanin suka shiga meeting da tara da goma saura suka fito. sai sha biyu ya hada ma kansa abun karyawa daman can ba mutum ne mai cin abincin tun da safe ba, kuma ba lallai ne idan ya tashi ci ya ci mai nauyi ba, and each and every morning sai an kawo sabon bread. Misalin karfe biyu da sun fito daga sallah Azahar yana zaune office dinsa yana wani aikin wayarsa tai ringing. Yana kallon sunan da yai appearing a screen din wayarsa na Hajiya Laraba yai murmushi daman he wanted to call ya ji muryar Aminatu amman yana jin nauyi da ma ace kakace ita baya kunyarta zai iya kira kai tsaye yace ta bawa Aminatu.

“Salamu alaikum”

“Wa'alaikumussalam Talba ya gida?”

“Lafiya Kalau Alhamdulillah”

“Na ce, baka kawo Aminatu ba har yanzu”

Ya dan yi shiru for few seconds, yana tunanin abun da take fada.

“Na'am?”

“Aminatu nace har yanzu ba ta dawo ba?”

“Fita tai?”

Ya bukata yana aje biron hannunsa.

“Ban gane ba, ba jiya ka aiko ka ce ta zo ta karbi sako ba?”

“Ni...!”

Ya nuna kansa kamar tana gabansa.

“E....”

Ta fada masa yadda akai da kuma hanata da mai gidanta yai ta kira shi. Talba ya mike tsaye da sauri.

“No wait wait.... Har cikin gidan aka shigo ko kuma waje?”

“Aa waje ka tsaya”

“I'm not the one Hajiya, ba ni ne na zo ba, rabona da gidanku tun shekaran jiya da na zo muka gaisa da ita, idan ni ne ai dole zan shigo na gaisa da ke, ya zako bari ta fita ta gana da wani da baki da tabbacin ni din ne ko aa kuma har akai yanzu baki kira ni ba? Why?”

Ta tambaya a mugun fusace da wata kalar murya da be taba sanin yana da ita ba, gaba daya ma ya manta da ita din yayar mahaifiyarsa ce.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, Wallahi na yi tunanin kai ne sabo... ”

Bata karasa ba yai wurgi da wayar da mugun karfi.

“Damn it....! Why would someone do such things to innocent girl? Why?”

Ya dafa kansa ya shafa fuskarsa da mugun karfi, wani abu be taba faruwa da shi ya ji ransa yayi mugun bachi kamar haka ba. Watsi yai da tarkadun da suke saman teburin, ya daga kafarsa sama ya buga kasa da mugun karfi, da saurin dauki makullin motarsa ya fice daga office da gudunsa, abun da be taba yi ba a tahirin kafuwar kamfanin, duk inda ya bi kauce masa ake wasu kuma suka tsaya kallon ikon Allah, wanda ke shigowa office tana tafiyar kasaita kamar mai tausayin kasa yau shi ne ke fita daga kamfanin da gudunsa. Yana shiga motarsa yai reverse a hanzarce, ya fisgeta da mugun karfi kamar an biyo shi.

_____

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Kamar wani aljani haka ya isa gidan Hajiya Laraba, shi kansa ba zai iya fadar yadda akai har ya kawo kansa gidan ba, ya san dai ya shiga mota ya fisgeta da karfi, adadin gudun da yai kam be sani ba, kawai ya samu kansa a kofar gidan ne and he can't wait har a bude masa gate ya shiga da motarsa a waje ya faka ya fito da sauri ya shiga cikin gidan, key din ma a jikin motar ya barsa all what he know is ya rufe motar. A kofar shiga falon ma be tsaya an masa izini ba ya tura ya shiga ko sallama babu. A tsaye ya samu Hajiya Laraba waya makalle a kunnenta tana kuka.

“Da wa kike waya?”

“Abban su Baby ne”

Ta fada bayan ta sauke wayar, sannan ta zauna.

“Allah yasa yarinyar nan tana cikin koshin lafiya, Wallahi duk daukata tana gurinka ashe ba kai ba ne, ban san waye ba, Allah yasa ba kidnapping dinta za a yi ba”

“Tun farko Hajiya ya kamata ki bincika, ko da nine ya kamata ki tabbatar kamin ki barta ta fita, kuma da kika ga ta dade bata dawo ba sai ki kira waya ki tambaya, tsakani da Allah idan yarki ce zaki mata haka? Waya san su waye? Me suke bukata? Meye manufarsu? Wane hali take ciki? Gashi har an kwana an wuni”

Ya fada cikin wani irin bacin rai har kalar idanuwansa na canjawa, farin ciki ya rine zuwa ja, da karfi ya yarfar da hannunsa ya cige bakinsa. Can kuma ya juya ya fice daga dakin ya bar Hajiya Laraba tana kuka hankalinta a tashe. Gurin mai gadin ya nufa fuska babu annuri.

“Kai malam kasan wanda ya dauke ta?”

“Wallahi Wallahi ba zan iya gane shi ba, saboda ya saka facing cap kuma da mask a fuskarsa, amman fari ne sosai kamar kai”

Ya fada yana karawa da rantsuwa, a take Talba ya dauke shi da mari.

“Wane irin mai gadi ne kai? Baka san ka yi bincike kamin ka kirata ba? And na taba zuwa na ce ka kira min ita ba tare da na shigo ba? Miyasa ba kai tunanin haka ba?”

“Dare ne ranka ya dade ba zan iya gane cewar kai ne ba ko ba kai ba, dab Allah a gafarce ni, ya kwankwasa kofar kawai yace na kira masa Aminatu na ce mata in ji Talba tai sauri zai bata sako, ni kuma ban yi tunanin wani mugu ba ne, sai na shiga na kirata”

“Okay yayi kyau, idan wani abu ya samu yarinyar nan na rantse maka sai ka yabawa aya zakinta, waya sani ko da kai aka hada baki...”

Yana fadar hakan ya juya ya koma cikin gidan Mai Gadin ya bishi yana kuka yana bashi hakuri amman ko saurarensa be yi ba, falon ya sake shiga sai ya same Hajiya a inda ya barta.

“Akwai hotonta?”

Ta mike tsaye da sauri tana gyada kai ta shiga gallery wayarta ta kamo hoton.

“Amman a waya ne sai dai na tura maka”

“Na fasa wayata just give me your phone”

Be jira ta mika masa ba ya kai hannu ya karba.

“Abban Baby ne Password din”

Be ce mata komai ba, ya juya ya fice da sauri, yana fita mai gadin ya shigo yana kuka yana fadawa Hajiya abun da Talba yai masa. Cikin motar Talba ya koma yana kokarin yi ma ma motar key ya kai idonsa kam wayar, sanye take da atamfa sai farin mayafi ta dan sunkuyar da kai tana murmushi, wani kuma ta

dago kan with the same atamfa, wata boyayyar ajiyar zuciya ya sauke ya kai hannunsa ya shafa hoton.

“Oh God, Allah ka kare yarinyar a duk inda take, Allah ka kare min ita”

Ya jinkina da motar ya lumshe ido yana jin kamar ba shi da kuzari a jikinsa. Can kuma ya bude idon yai ma motar key yai reverse ya hau titi, police station din dake yankin ya nufa, yana shiga ya gabatar masa da abun da ya kawo shi sannan ya tura musu hoton, a take suka dauki case din suka mikawa masu kula da bangaren bincike na musamman akan satar mutane da kisa. Juyowa yai ya fito bayan yai musu duk bayanin da suke bukata, zaune yai a motar yana jin kansa na mugun sarawa.

“Aminatu where are you? Why would someone do this to me?”

Ya tambayi kansa tambayar da be san amsar ta ba, sai kuma ya kai hannunsa ya shafa kansa, thinking of that night da yake tare da ita, abun d ya fara fado masa a rai is waye ne wannan mutumen da ya haske su? Kuma yai baya baya daga karshe ya gudu? Miyasa ya haske su? Key yai ma motarsa ya fice daga harabar zuwa asibiti. Ko farkin din kirki be yi ba ya kashe motar ya fito ya nufi hanyar da zata sada shi da office din Ali. And he got lucky fitowar Ali daga theater kenan yana shirin zama Talba ya shigo. Ali na kallonsa ya san ba lafiya ba, domin kana ganinsa ka san ya fita daga hayyacinsa, kallonsa Ali yake har ya karaso ya zauna.

“Tell a bad news...”

“Someone kidnapped Aminatu...”

At first dariya Ali yai with shock. Sai Talba yai masa wani mugun kallo.

“What is funny? Labarin ban dariya na baka? Ko kuma you're happy da hakan ya faru da ita?”

Ali yayi saurin girgiza kai.

“No No No.... Haba dai i was shock kamar ya an yi kidnapping dinta? Why would someone do this to her?”

“Not to her, but to me duk wanda yai haka yayi ne saboda ni... Because Aminatu is innocent, bata da matsala da kowa....”

Ya fada yana saka hannayensa duka biyu ya dafa kansa. Ali ya nufi fridge dinsa ya bude ya dauko ruwa a gora ya mikawa Talba.

“Bana iya cin komai Ali, bana da kwanciyar hankali har sai na san halin da yarinyar take ciki”

“Amman ka kai report din ga police?”

“Daga can nake, ba ni wayarka zan kira PA na”

Ali ya mika hannunsa ya dauko wayarsa ya miko masa.

“Amman kamar ka yi gaggawa? Idan wadanda suka saceta kudi suke so fa? Kasan kuma basa son ana kai case din nan gurin police”

“What if ba kudi suke so ba? What if someone plan all this? Shekaranjiya muna tare da ita, akwai motar data haska mu, idan na taka zan tafi gurin motar sai motar tai baya, idan an tsaya ta tsaya, na kira wayarka amman ba mu samu magana ba, na so nace ka zo ka same ni a gurin so that ko waye mu ritseshi, sai kawai suka ja motar suka bar gurin da gudu”

Ya karasa maganar yana tuna yadda ta rirrike shi tana fadin tsoro take ji. Ali yayi shiru yana nazari.

“Baka ga kalar motar ba? Kuma lokacin da zaka je baka ka wani na bibiyarka ba?”

“Ban ga komai ba, no har na faka motar waje na shiga cikin gidan ban ga alamar ana bibiyata ba, sai a lokacin da muka fito na rika hannunta sannan aka kunna fitilar motar aka haska mu, sai a lokacin ma na lura da motar a gurin”

Ya shiga contact din Ali ya nemo number PA dinsa, daman Ali yana da number PA din da wasu family members na Talba. Talba ya kira line PA nasa, bugu biyu ya dauka cikin ladabi.

“Jamal ka duba office dina zaka ga wayata somewhere in the office a kasa, ka cire sim din ka siyo min sabuwar waya ka kawo min gida yanzu nan”

“To Ranka ya dade”

Talba ya kashe wayar sannan ya dorata saman tebur din.

“Ka fasa wayarka ne?”

“Yeah”

Ya amsa yana hade yawu tare da aje numfashi da karfi. Ali kallonsa yake yana mamakin yadda ya shiga damuwa haka, sam be taba ganin abokinsa a cikin irin wannan fushin ba sai yau, ya san Talba na da saurin fusata amman ba kamar wannan karon ba.

“Ka fadawa Leila inda Aminatu take?”

Ali ya daga hannayensa.

“That's it, kullum Leila ce first wanda kake fara zargi akan komai”

“No she's my second suspect, Kabir is the first one”

Sai a lokacin Ali ya zauna da mamaki yake kallon Talba.

“Kabir fa kace?”

“Yes ya dawo gida before na dawo, and Amal tooo ta fita a wannan daren, leila ma zata iya fita kuma ta hana mai hadi ya fada min komai, and Kabir was the first person da ya fara kirana da ango a daren nan”

“No look karka zama mahaukaci mana Talba? Me zai saka Kabir yai maka haka? Think about it mana”

“I don't know kamar yadda ban san manufar wanda ya dauke ta ba, and you too because you're the only one dana fadawa inda Aminatu take, maybe cikin labari ka fadawa Leila ba tare da tunanin zata yi wani abun ba”

“Nooo har abada, ba zan taba sirri da kai na kwashe na fadawa Leila ba, god forbid, I'm always on Leila side amman ba zan fada mata wannan ba”

Talba ya kai hannu yana taba hancinsa tare da lumshe ido.

“Leila can do this, maybe Kabir ya fada mata”

“Please Talba, wacan karon ma ka zargi Leila, karka ce zaka zarge ta ma a wannan karon wannan rashin adalci ne...”

Talba ya mike tsaye cike da fusata.

“Don't tell me what to think, kai zan zarga? Ina da bashin gaba da wani ne da zai sace Aminatu? Duk wanda ya aikata wannan abun nan yana kusa da ni ne, kuma ba zan kyale ko waye ba”

Yana kaiwa nan ya mari kujerar daya tashi a kai sannan ya fice fuuu kamar walkiya. Ali na kiransa ko saurarensa be yi ba, Ali yayi saurin daukar wayarsa ya shiga neman number Kabir, bata wani dade tana ringing ba Kabir ya dauka.

“Hello”

“Kabir kana ina?”

Kabir dake zaune yana duba laptop dinsa ya dan yi fuskar mamaki.

“Gida...ya akai?”

“Dan Allah ka bar gidan for now”

“Saboda me?”

“Kawai ka fita dai”

“Okay”

Ya amsa sannan ya sauke wayar, ya tashi da sauri ya dauki keys dinsa ya fice. After Ali ya kira Kabir ya kira Leila sai dai har wayar ta gama ringing Leila bata daga ba, da sauri shi ma ya nufi inda keys dinsa suke ya dauka ya fice.

MADINA POV.

Bata san da fitar Talba daga kamfanin ba har sai da ta kammala aikinta ta doshi gurin sai ta same shi a kulli, tsaye tai tana mamakin yadda akai ya tashi daga aiki da wuri haka kuma ace har sekatarinsa ya rufe office din. Wani irin faduwar

gaba ta ji sai ta juyo ta dawo offices dinsu kasancewar ba ita kadai ba ce a office din kusan su bakwai ne sai dai kowa da bangarensa kuma an sakawa kowa shamaki.
Nata teburin ta nufa ta dauki jakarta da sauran takardun tai musu sallama sannan ta fito, tana tafe tana sake sake a ranta, har ta shiga mota tunani take yi. Tafiya tai mai nisa har sai da ta kusa isa gida sai kuma ta juya motarta ta dauki hanyar gidansu Leila, daman tana son magana da ita tun a jiya saboda tace akwai abun da take son ta fada mata. Horn biyu tai aka bude mata kofar ta shiga tai farkin a harabar sannan ta kashe motar ta bude ta fito ba tare da jakar ba. Tana gyara mayafinta ta nufi entrance din hannu ta kai ta knocking a yayin da ta isa bakin kofar daki. Mairo ce ta bude mata sai Madina ta sakar mata murmushi ita ta mayar mata da murmushin tana mika mata gaisuwa, daman suna yabawa da halinta domin bata da jin da kai kamar Leila, gashi tana sakar musu fuska, Leila kam ko gaisuwa suka mata ba zata amsa ba balle har su ga murmushinta.

“Leila na ciki?”

“Eh tana ciki sannu da zuwa”

“Yauwa sannu da aiki”

A inda aka tanada domin aje talkami ta aje takalmin data shigo da su, sannan ta shigo cikin falon tare da daga kanta sama tana kallon Amal dake saukowa sanye da uniform din makaranta, da alama bata dade da dawowa daga makarantar ba.

“Ya Madina”

“Na'am Amal ya kike?”

“Lafiya kalau, bari na kira miki Leila”

Cewar da Amal tai zata kira mata Leila yasa ta fasa zuwa dakin Leila kai tsaye, sai ta zauna a falon tana jiran fitowarta, Amal kuma ta juya da ta koma sama, sai da ta sanarwa Leila sannan ta sake fitowa kamin ta karasa saukowa ta ji ana danna door bell din da karfi abu ba a taba ba, domin Momy bata son karar door bell yai yawa, da sauri ta nufi kofar kamin ta karasa hawa har da dukan kofar ake.

TALBA POV.

Yana isa cikin gidan yai fakin kusa da entrance din kofar falon ya fito ya doshi kofar, hannunsa ya saka ya danne door bell din ya rika kara kamar zai tashi gidan sai kuma ya saka kafarsa ya halbi kofar. Cikin tsoro Amal ta bude masa kofar tai baya baya tana kallonsa, kusan a rayuwarta bata taba ganinsa cikin irin wannan bacin rai ba, fuskarsa babu annuri idanuwansa sun rine I kamar ba nasa ba.

“Ya...”

Ya watsa mata harara sai tai shiru, Madina dake zaune ta mike tsaye tana kallonsa, shi ma kallonta yai kamin ya dauke kai ya kalli Leila dake saukowa downstairs.

“Between you and Kabir waya haska ni shekaranjiya da mota? And waya dauke Aminatu yau?”

Tsayawa tai cak tana kallonsa, domin gaba daya bata fahimcin inda kalamansa suka dosa ba.

“I'm talking to you”

A nan ma kallonsa kawai take ba ita kadai ba har da Amal da Madina da gabanta ke mugun faduwa. Door bell din aka sake dannawa sai Amal ta nufi kofar ta bude, Ali ya shigo da saurinsa barin kofar tai a bude ta nufi stairs da gudu, domin fadawa Momy abun da yake faruwa.

“Leila na kira wayarki na fada miki ki fita daga gidan nan for a while, ba ki dauka ba please go back to your room...”

Ali ya fada, sai Talba ya kalleshi.

“Really? How could you do such things Ali? Wait wai me kake so na yi ne? Sitting here watching and not doing anything? What do you expect? Na kyale yarinyar nan ta sha wahala?”

“Wace yarinya?”

Momy ta tambaya, sai ya kalleta.

“Aminatu, someone kidnapped her”

“Kuma ka rasa wanda zaka zarga sai Leila? Tana cikin damuwa zaka kara mata wata?”

Cewar Momy cikin daga murya da fusata.

“Not just Leila ina zargin kowa da kowa, idan wani abu ya samu yarinyar na rantse da Allah ba zan kyale ba, no matter how close I'm to you, alkawarin farko dana fara yi ma yarinyar nan is zan kula da ita, and i won't let anything happen to her. Surely i will fulfill that promise!”

Zaunawa yai a kujerar dake kusa da Madina ya dafe kansa da hannu biyu. Madina kallonsa take da mugun faduwar gaba. Can kuma ya dago cike da damuwa.

“Yarinyar nan bata san location din kowa ba, bata san inda zata ce a kai ta ba, and bata da number kowa a kanta poor girl...”

Yana rufe baki Kabir ya shigo mai gadin gidan na biye da shi.

“Ranka ya dade Jamal ya iso yana waje”

Mai gadin ya fada yana kallon Talba.

“Karbo sakon Hannunsa”

Ali ya fada sai Talba ya ce.

“Je ka ce ya shigo”

“To”

Ya juya da sauri ya fita, sai falon yai tsit kamar babu kowa a ciki. Kamar yadda Talba ya umarta haka Jamal ya shigo yana ganin yadda kowa yai tsaye cirko cirko ya san ba lafiya ba, har inda Talba yake zaune ya karasa ya mika masa wayar da already ya saka sim din a ciki ya kunnata.

“Gata ranka ya dade”

Talba ya karba. Sannan ya mika masa wayar Hajiya Laraba bayan ya cire password din.

“Tura hoton nan a wayarka”

Ya karba da sauri ya shiga ya danna share to Xander, sannan ya ciro wayarsa ya shiga tasa Xander yana connecting.

“Done”

“Aje a buga hoton nan a raba shi ko'ina Wanted, ka bada sanarwarta a gidajen radio, kuma a sanar da cewar duk wanda ya gano inda yarinyar nan take zan ba shi naira miliyan uku”

“An gama ranka ya dade”

Jamal ya fada sannan ya fice da sauri, daga Momy har Ali Madina, Leila da Kabir daya shigo yanzu mamakinsa suke. Gmail din wayar ya shiga ya saka gmail dinsa sannan ya dawo gurin contact ya nemo number Dpo ya kira shi.

“Hello Qasim kana office?”

“No ai na bar garin Gusau yanzu, lafiya dai”

“Zan kira ka”

Talba ya kashe wayar.

“Can someone explain to me abun da yake faruwa?”

Kabir ya tambaya, sai Talba ya kalleshi.

“Har sai an maka bayani? Duk wanda ya dauki yarinyar nan yana a nan tare da mu, and if na gano wanda yai wannan aiki... Wow.... ”

Ya furta yana wani murmushin takaici. Leila ta karasa saukowa tana takawa zuwa inda Talba yake zaune hawaye na sauko mata.

“Why is she so important to you? Miyasa idan wani abu ya sami yarinyar nan kake haukace ka fita daga hayyacinka, and why I'm always the first suspect?”

“Because he love her”

Kabir ya amsa mata. Sai Ali yai saurin shiga tsakani.

“No... Ba..”

Be karasa ba Talba ya tari numfashinsa yana mikewa tsaye.

“Yes you're right, i loved her ni ma a yanzu na san da haka, domin idan bana sonta i won't hold her hands and kiss her i wouldn't hug her har ka gan mu a daren daka haske mu a mota”

Ali ya daki kirjinsa cike da bakincikin furucin da yake da kuma zargin Leila, and the way da Leila take hawaye ya saka shi cikin bakinciki.

“Enough.... Talba ka zura da yawa you lost it.... And ka daina zargin Leila ko Kabir ba su suka dauke ta ba”

“Kai ka dauke ta kenan?”

Talba ya fada yana kallonsa with angry face. Ali ya dauke kai yana murmushi sannan ya sake kallonsa.

“Leila was right, kai ne da matsala Talba, and ka bi ka haukace akan yarinyar nan, the girl you meet on the street of the hospital, the girl that was kidnapped and rape? Why is she so special to you? I'm your best friend, Leila is your fiance, Kabir is your blood, Amal and Momy are also there amman idonka ya rufe saboda yarinyar da she can't read and write?”

Talba ya sake tsayuwa a gabansa da kyau yana masa wani mugun kallo.

“Now i know who my friend is, i will soon know my enemies, and kar bakinka ya sake furta wata mummunar Kalma akan Aminatu! You know it ba zan iya daukar hakan ba, a matsayina na mijinta...!”

Kabir yayi gwalo ido waje.

“Oooooo woooooo wait what do you mean?”

Talba ya watsawa Kabir wata uwar harara, Momy, Leila Amal da Madina mamaki ya kusa kashesu a tsaye, Madina ta dafe zuciyarta.

“Aurenta kai?”

Ta tambaya a zuciyarta ba tare da ta san tambayar zata fasa bakinta ta fito ba har kowa ya ji.

“Yes i marry her, i can't hide this anymore, Aminatu is my wife....”

Talba ya amsa mata da kansa yana kallonta, saurin dafa kujera tai saboda kafafuwanta da suka kasa daukarta, a take hawaye suka kwankwaso mata kofa, bakinciki yai mata sallama. Momy ta kalli Talba da wani irin duba na wulakanci da kaskanci.

“Ka tsaya a gabana, kana zargin Yaya da sace yarinyar da bata kai ta wanke tufafin gidan nan ba, you stand in front of me and my daughter, telling us ka auri wata banza sharar bola, Mu'az ko kadai ka rage namiji Leila ba zata aureka ba! And daga yau na ja jan layi tsakanina da kai babu ni... Babu kai.... A yau ina son ka sani ka rasa tun kana karami kuma rashi na har abada I'm not your mother and i will never be...”

Momy na kaiwa nan ta taka zuwa inda Leila take tsaye tana kallon Talba ta riko hannunta ta fisgota da karfi da zimmar ta jata su nufi upstairs, sai Leila tai baya ta sulale kasa sumammiya, Ali da Amal suka yo kanta da sauri suna kiran sunanta. Momy ta yi baya da sauri tana rufe bakinta tare da fashewa da kuka, Madina ta dauki wayarta ta fice da gudu tana wani irin kuka da bata san ta inda yake zo mata. And now it's between Talba and Kabir kowa na kallon dan'uwansa, kallon kallo akuya kallon kura...

Juyawa Talba yai ya dauki wayarsa da wayar Hajiya Laraba ya fice daga falon. Motarsa ya shiga yai mata key masu gadin na ganin haka suka sake bude gate din daman suna komarin rufewa ne bayan da suka budewa Madina ta fita. Tuki kawai yake not knowing what to do or go, gaba daya duniyar ta rikice masa.

“Where are you Shalelena.... Who do this to you....?”

Ya furta yana lumshe ido, be ankaro da driving yake ba har sai da motar dake gefensa ta danna masa horn da karfi saboda hawa tsakiyar titi da yai, da sauri ya sauko saman titin ya faka gefe ya dafe kansa yana jin zuciyarsa na bugawa da karfi. Can kuma ya sake hawan titin ya dauki hanyar da zata kai shi office din Daddy, be taba samun kansa a cikin tsoro marar misaltuwa ba irin yanzu, be san irin kallon da Daddy zai masa ba, but he most face this, ya kamata ya fadawa Daddy da kansa kamin ya ji a gurinsu Momy. Farkin yai harabar ma'aikatar sannan ya fito ya shiga ciki yana tafiya cike da nauyin kafafuwa. For the first a yau ya ji ba zai iya tunkarar office din Daddy ya shiga kai tsaye ba, har sai da ya bukaci Sakataren Daddy yai masa iso, shi kansa Sakataren sai da yai mamaki ganin Talba yayi abun da be taba ba, ko Daddy baya nan shiga yake ciki sai dai ya zauna zaman jiransa hakan yasa idan Talba ya zo sai dai ya gaishe shi, be taba hana shi shiga.

“Ya ce ka shigo”

Sakataren ya fada bayan ya shiga ya sanarwa Daddy. Talba dake zaune ya shafa fuskarsa sannan ya mike tsaye ya nufi office din cikin damuwa da faduwar gaba.

“Yau kai ne da neman izinin shiga office dina da kanka?”

Daddy ya tambaya yana kallon Talba with serious look. Talba ya kasa cewa komai kuma ya kasa daga kai ya kalli Daddy har ya isa gaban teburin ya zauna.

“Akwai abun da yake damunka?”

Daddy ya sake tambaya cike da kulawa, domin ya ga dansa ba a yanayin da ya saba ganinsa ba.

“Daddy magana nake son yi da kai, ina son na fada maka wani abu, amman ban san yadda zaka kalleshi ba, ban san yadda zaka ji ba, amman ina son kasan cewar na aikata abun da na aikata ne saboda gyara ba barna ba...”

“Ina saurarenka...”

Jimmm Talba yai ya dade kansa a kasa kamin ya soma bawa Daddy labarin auren Aminatu da yai a boye da kuma yadda komai ya wakana. Murmushi Daddy yai.

“Come on my friend... Control your tongue young Man”

Sai a lokacin Talba ya dago ya kalle Daddy idonsa cike da kwalla.

“Da gaske nake Daddy, na san zaka kalle a wani mutum dabam kuma zaka ji ba dadi dan Allah kai hakuri ka yafe min”

“Miyasa ka zabi ka fada min a yanzu then?”

“Saboda an sace ta”

Daddy ya sauke ajiyar zuciya ya kai hannunsa kan bakinsa.

“Garin ya?”

“Ban sani ba, ban san manufar wanda ya dauke ta ba, and now i exposed every thing, Momy ta yi fushi da ni”

Ya karasa cikin wata murya mai ban tausayi tare da yin kasa da kansa.

“Hakan yasa kake tunanin ni ma zan iya fushi da kai? Kuskurenka kawai na yi min karya ne ka ce baka sonta, ni kuma ka san ba zan taba shiri da abun da baka so ba”

“A lokacin ban san ina sonta ba Daddy”

“Yanzu kuma ka sani?”

Yayi shiru kansa a kasa.

“Ban san wane hali take ciki ba, ko ta ci abinci ko bata ci ba, ko dukanta suke Allah kadai ya sani... Daddy karka yi fushi da ni dan Allah abun zai min yawa”

“In shaa Allahu tana ciki koshin lafiya, babu abun da zai same ta, a can lokacin da kana karami, idan kai ma Momy ka laifi ko wani bayana kake guduwa ka boya, sai a yanzu da ka girma kake ganin ba zaka iya gudowa bayana ka boya ba? Young Man you're wrong very very wrong, Ba ni da farincikin daya wuce naka, damuwarka damuwata ce, Daddy is always on your side, zan yi magana da CP, za a gano ta In Shaa Allah, ina tunanin wanda ya sace ta yayi ne kawai dan ya gwadaka, so be a Man”

Talba ya mike tsaye da sauri ya zagaya ya nufi Daddy, Daddy na ganin haka ya mike tsaye Talba ya rumgume shi.

“Ba uba kawai ka zame min ba Daddy, ka zamar min har da uwa, ranar da baka nan Daddy zan shiga wani hali”

Ya fada cikin kuka kamar ba shi ba, har cikin zuciyarsa yake jin kaunar mahaifinsa fiye da kima. Daddy yayi murmushi.

“I'm proud of you Talba, and now i know how my son is, ashe kana da raunin zuciya haka?”

Talba ya dago ya share hawayensa ya kalli Daddy.

“Daddy your Son is in Love i don't know what is wrong and right for now, gaba daya bana da kwanciyar hankali”

Daddy yayi murmushi irin na su na manya, sannan ya kai hannu ya dafa kafardarta.

“Karka damu, i was in your shoes before, it's hard right?”

Ya gyadawa Daddy kai.

“Yeah it's”

Daddy yayi murmushi ya kai hannunsa ya danna telephone.

“A fadawa Direba ya shirya zamu je gurin CP yanzu”

Shine kawai abun da ya fada, sannan ya kalli Talba.

“Go home and rest zan kula da komai”

Talba baya son musawa Daddy hakan yasa ya gyada masa kai, ya nufi kofar fita ba dan yana jin zai ma iya zuwa gidan ba, balle kuma wani zancen hutawa ya biyo baya, ba taba samun kansa a cikin tashin hankali irin wannan ba.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

MADINA POV.

daker ta iya kai kanta gida saboda kukan da take, tana jin zuciyarta da mugun nauyi kamar zata fashe. A galabaice tai farkin ta bude motar ta fito ba tare data kashe ba, jikinta har rawa yake kamin ta isa gurin kofar falon ta kai hannu ta kwankwasa, sai kuma ta jingina jikin ginin saboda bata iya tsayuwa da kafafuwanta. Ana bude mata kofar ta shiga da sauri ta tana kuka kamar ranta zai fita. A tsakar falon ta fadi tana kuka kamar wanda akai wa mutuwa har da dora hannu a kai. Hajiya ta fito dakinta da sauri ta doso inda take.

“Ke lafiya?”

“Hajiya Talba yayi aure...”

Ta fada da karfi tana kuka.

“To shi ne me? Daman ai kin san auren za'ayi tun da aka saka musu rana”

“Ba da Leila ba Hajiya, ai na fada miki baya son Leila, da wata da yake so ne wata dabam, yarinyar da ya kawo gidan nan...”

Hajiya ta cika da tsananin mamaki domin bata taba zaton haka ba.

“To ke miye na ki a ciki? Wai Madina ba zaki raba kanki da wahala ba? Da ace kina gabansa ai da yanzu ya fara kula dake, amman ya tsallakeki ya auri wata, kuma Leila da Mahaifiyarta suna gani ba su iya yin komai ba? Har kike tunanin za ki iya yin wani abu da za ki burge shi yace yana sonki? Kina cutar da kanki ne kawai, kuma kina mafarkin da ba zaki taba farkawa ba har a bada”

Dagowa tai ta kalli Hajiya, tsakanin abun da Talba yai a yau da kuma kalaman da Hajiya take fada mata sai ta rasa wanne ya fi yi mata ciwo.

“Ko wace uwa, tana kokari ta ba yarta abun da take so, a yau Momy ta ci mutunci Talba, saboda ya auri wata wanda ba yarta ba, bayan kuma ya san yarta tana sonsa. Amman ni kalleni na rasa wanda nake so, kuma mahaifiyata tana kara min da wani bakincikin”

“Gaskiya nake fada miki Madina, kuma ba ki rasa masoya ba, kawai kin bawa kowa dama ne, saboda tunaninki da hankalinki ya karkarta ya koma gurin Talba, tausayinki nake karki jefa rayuwarki cikin matsala”

Ta daga kai, sannan ta saka hannayenta ta share hawayenta ta mike tsaye, ba tare da tace komai ba. Ta nufi kofar fita ta fita daga falon, Hajiya ta bita da kallo har ta fice sannan ta nufi kujera ta zauna cikin damuwa, domin har ga Allah tana tausayin yarta. Gurin motar Madina ta koma ta kashe motar ta kwashe takardunta da jakarta ta dauki wayarta sannan ta rufe motar, sannan ta dawo ciki daman a bude ta bar kofar. Kallo daya tai ma Hajiya ta dauke kai ta nufi hanyar dakinta.

“Ki yi ta addu'a, sonsa ya fita zuciyarki”

Tsayawa tai cak sannan ta juyo ta kalli Hajiya.

“Lokacin da sonsa zai shiga zuciyata ban ma sani ba, ba addu'a na yi ya shiga ba, kawai na samu kaina ne cikin kaunarsa, irin kaunar da bana jin Daddy ma yana masa irinta, wata kila akwai abun da Allah yake nufi da hakan, mu barwa Allah komai Hajiya”

Tana gama fadar haka ta juya ta shige dakinta. Saman gadonta ta sauke komai sannan ta zauna kanta na mugun ciwo, ta kasa daina jin muryar Talba a lokacin daya amsa mata cewar ya auri Aminatu.

“Talba ka kasa gane cewar ina sonka, ka kasa ganin hakan a cikin idona da mu'amala ta, miyasa idonka ya rufe haka? Baka jin tausayina? Baka ganin ya dace na samu farinciki a tare da kai?”

Ta mike tsaye ta nufi madubinta tana kallon kanta.

“Miyasa jarabawa ta zata zo min ayanyin da ba zan iya dauka ba? Dole ne ka fahimta Talba? Dole ne ka karancin kaunarka a idanuwana kuma ka san da ita a zuciyata”

Ta lumshe ido tana sauraren yadda zuciyarta take mata zafi sosai.

If na gano wanda yai wannan aikin... Wow...

Kalamar ta tsaya mata a rai, iyakar kokarin da take na ganin ta kwantar da hankalinta ne ta manta da komai cikin har da furucin Talba na cewa ya auri Aminatu. Ta dade a haka sannan ta bar gaban madubin ta nufi bandaki sai da ta shiga sannan ta cire tufafinta ta kunna shower ta tara jikinta, sai da ya jike shak sannan ta dauki shower gel ta fara murzawa a jikinta, ta murza ko'ina na jikin da kyau sannan ta daura tawul ta fito rike da wani karamin tawul din tana goge jikinta. A gaggauce ta shirya cikin wata farar abaya ta lullube jikinta da mayafin abaya sannan ta dauki jakarta da key motar da wayarta ta fice daga dakin. Har lokacin mahaifiyarta na zaune a falo inda ta barta kana ganin fuskarta kasan akwai damuwa a tare da ita.

“Ina zaki je?”

“Gidansu Leila?”

“Gidansu Leila”

“Ba yanzu kika fito daga can ba?”

“Suma tai ya kamata naje na dubata”

“Idan har son gaskiya kike wa kawarki ba zaki taba tarayya da abun da kika san rasashi a gareta babbar matsala ba ce”

Madina bata ce komai ba, ta sauke kai kasa ta nufi kofar fita sai kuma ta daga kai ta kalli Tima, sannan ta fice. Tima ta nufo Hajiya rike da serving spoon tana fadin.

“Wallahi Yaya Madina mugun tausayi take ba ni, tana cikin tsaka mai wuya, ki duba halin da take ciki amman duk da haka tana kokarin ganin ta bawa Leila kulawa”

“Nima tana ba ni tausayi, amman idan na ce zan saki zuciyata na nuna mata haka, zata bi son zuciyarta ne wanda zai iya kaita ga halaka mu kuma ya saka mu a dana sani”

“Haka ne”

Ta amsa sannan ta juya ta koma cikin Kitchen din.

Madina na fita daga gidan ta nufi gidansu Leila, sai dai bata tararda kowa a gidan ba, masu gadin suka fada mata an tafi da Leila asibiti. Hakan yasa batai wahalar shiga ba tai reverse tare da daukar wayarta ta kira Ali.

“Hello Ali kana tare da Leila ne?”

“Eh muna asibiti”

“Okay”

Ta katse kiran sannan ta karawa motarta gudu, cikin yan mintuna ta isa asibitin da Ali yake aiki. Ta faka a inda aka tanada dan aje ababen hawa, sannan ta bude motar ta fito ta sake kiran number Ali, sai ya fada mata cewar shi yana office, Momy da Kabir kuma suna ICU room 21. Asibitin ba bakuwarta bace hakan yasa bata tsaya tambayar kowa ba ta doshi ward din tana tafe kalaman Talba na mata yawo a kai har ta isa bakin kofar dakin. A hankali ta tura kofar dakin ta shiga da sallama muryar kasa kasa, Kabir ta samu a jingine ya rumgume hannayensa yana kallon kofar shigowa, Amal kuma na zaune a kujerar dake facing din gadon Leila, Momy na zaune kan gadon kusa da Leila ta zuba mata ido, bata dago ba har sai da Madina ta karasa kusa da gadon.

“Momy ina wuni?”

Momy ta kalleta kamar ba zata amsa mata ba, sai kuma ta amsa mata din ta dauke kai.

“Lafiya Kalau”

“Ya jikin Leila?”

A nan kam Kabir ne ya amsa mata, domin Momy bata sake kallonta ba ma balle ta amsa mata din. Ita kanta sai ta sha jinin jikinta saboda yanayin yadda Momy tai mata, daman can bata saba sake mata ba, sai dai wannan karon tafi daure mata fiye da ko yaushe, wata kila saboda tana cikin damuwa ne, wata kila kuma saboda ta yi kuka ne a dazun ta fita ta bar gidan bata tsaya duba halin da Leila take ciki ba. To ko dai ta yi wani abun da be dace ba ne? Haka dai tai ta yi ma kanta tambayoyin da bata da amsarsu. Kasa zama a dakin sai kawai ta juyo ta fito ba tare da ta yi musu sallama ba. Tafiya take cikin rashin jindadi tana kallon mutane dake kai kawo, amman sam bata lura da Ali ba saboda hankalinta yana wani gurin dabam.

“Madina...”

Ta kalleshi da sauri, sai kuma tai murmushi.

“Ban lura da kai ba”

“Na ga alamar hakan ai, kin dubata”

“Naga alamar hakan ai hankalinki yana wani gurin, kin dubata”

“Eh, tana bachi kuma na ga Momy da Amal suna kanta shiyasa na fito”

“Okay, gida zaki je?”

“Eh.. Talba fa?”

Ta tambaya tana takawa, sai Ali ya bita suka fara takawa tare yana mata rakiya.

“Ban san a inda yake ba a yanzu, na kira shi be daga ba”

“Amman ya kamata ka sance tare da shi saboda yana bukatar abokin magana a yanzu, na san abun da yai be kyauta ba, amman shi ma zai iya shiga damuwa”

“Haka ne, dukanmu ido ya rufe mun aikata kuskure, ko da yake ba laifin mu ba ne duk kidnapping din yarinyar da akai ne ya janyo haka”

Madina ta dauke numfashi a hankali ta sauke a asirce.

“Amman kai wa kake zargi?”

“Na rasa wa zan zarga, wata kila wadanda suka dauke ta sun dauke ta ne saboda neman kudin fansa, wata kila sun ganshi a tare da ita, ko kuma suna bibiyarta ba tare da shi ya sani ba, ko kuma suna bibiyarsa ba tare da ya sani ba, da ba su samu sa'ar sace shi ba sai suka dauke ta, ko kuma suna son sace wani wanda ya fito daga gidan da take ne. Ko kadam bana zargin Kabir bana jin Kabir zai iya yi mata haka, kuma Kabir ma be san inda yarinyar take ba i think, kuma ba zai rika bibiyarsa ba akan abun da ba zai amfane shi ba, Leila ma bana zaginta, saboda tana son Talba, na san tana da zafin kishi amman ba zata aikata irin wannan abun ba, saboda zai ja mata tsana ne kawai da kiyayya a gurin Talba, ba Talba kasai ba ni kaina da duk Familyn gidan nan za su tsaneta saboda abubuwan da suka faru a yau na bacin rai, kuma Daddy zai iya fushi da ita, idan ma har Leila ta ga wani abu makamancin wannan nine mutum na farko da zata fara kawa ma karar Talba, kuma idan ma ta tsara wannan abun ai zaki sani tun da kawarki ce...”

Ya karasa tare da kallonta. Wani irin dauke wuta Madina tai ta hade abu da karfi sannan ta gyada masa kai.

“Ba.. Ba.. Ba Leila ba ce, amman duk wanda yai wannan abun be kyauta ba ko...?”

“Be kyauta ba gaskiya, domin Talba ba zai taba yafe masa ba, na san yadda Talba ya bada cigiyarta In'Shaa Allahu za a ganta, ko ma suwaye za a kama su, kuma dole su fuskanci hukunci”

“Allah ya bayyana ta cikin aminci.”

Madina ta fada, sai Ali ya amsa da amin. Har gurin motarta ya rakata sai da ta shiga sannan ya juyo ya dawo cikin asibitin. Key tai ma motar sai da a bar asibitin sannan ta faka gefen titi ta kai hannu ta dafe zuciyarta ta lumshe ido.

TALBA POV.

daga office din Daddy gidansu Hajiya Laraba ya wuce, ya dade a wajen gate din tsaye yana kallon daidai inda suka tsaya ranar, da irin nishadin da suka yi sannan ya danna horn aka bude masa ya shiga ciki. Ya faka a harabar gidan ya bude ya fito ya doshi kofar falon dake bude ya shiga da sallama ba kamar wacan karon ba daya shiga babu sallama kuma hankali a tashe, a yanzu ma hankalinsa ba a kwance yake ba, sai dai a yanzu yana cikin natsuwarsa.

“Allah yasa an dace”

Kallonta kawai yai ya kawar da ido ya mika mata wayarta daman tun cikin mota ya tura hotunan Aminatu a sabuwar wayarsa.

“Ga wayarki, na saka report ta ko'ina, kuma police dinsun ce idan bukatar bincikenku ya ta so zasu neme ku”

“To Allah yasa a dace, amman dan Allah karka fadawa Kaka saboda hankalinta zai iya tashi kuma ka san tana da hawan jini”

Ta fada cike da damuwa, fatar idonta har ta yi taushi saboda kuka. A gidan yai sallah La'asar gaba daya addu'arsa a sujadar karshe akan Aminatu ne. Bayan ya gama ya fito ya shiga motarsa yai mata key ko kamin ya danna horn an bude masa gate, sai da ya hau titi sannan ya fara tunanin inda zai je, gida? No ba gida ba, office no ba can ba, gaba daya sai ya rasa inda zai je. Fakawa yai gefen titi ya kunna data wayar ya shiga Instagram app ya saka details dinsa yai loging sannan yai rubutun cigiya a page dinsa ya saka hoton Aminatu da goron da zai bawa duk wanda ya gano inda take. Yana posting kiran Daddy na shigowa wayarsa, da sauri ya dauka cike da son jin labari mai dadi.

“Hello Daddy”

“Mu'az ka same ni a office din CP yanzu nan”

“Daddy an ganta ne?”

“Aa yace za a fara wani bincike ne na musamman”

“Okay”

Ya katse kiran ya juya motarsa ya hau titi, cikin kankanen lokaci ya isa gurin, ya kira Daddy ya sanar masa a inda yake Daddy ya aiko da police aka shiga da shi ciki. Few tambayoyin Cp yai masa bayan sun gaisa har yake tambayar ko akwai wanda yake zargi? Talba ya kasa amsawa taya zai ce yana zargin Kabir ko Leila a

gaban Daddy anya Daddy zai jidadi ko da be nuna masa ba ya san hakan zai taba shi.

“Ka fada mana, so that mu saka ido akansu”

“Aa babu wanda nake zargi”

“Amman bayan kai waye ya san inda yarinyar take?”

“Ni ne kawai”

Ya fada saboda baya son saka Ali a cikin matsalar kar su fara bibiyarsa shi ma.

“Okay, zan hada ka da sashen bincike na musamman za su yi aikin mai kyau, kuma za su je su kwaso duka mutanen da suke cikin gidan saboda amsa wasu tambayoyin, idan ta kama ma har cikin gidan za su shiga su yi bincike, ina fatar za su samu hadin kai”

“Ba matsala”

Talba ya amsa. Kamar yadda ya fada haka akai ya hada Talba da masu bincike kan kisan kai da kidnapping suka hau yi ma Talba tambayoyi kamar ance musu shi ya sace ta, sannan suka aika da mota aka gayyato Hajiya Laraba da mijimta da duka yaran gidan har da Mai gadi suka hau yi musu tambayoyi jikin mai gadi sai bari yake yana amsa musu a tsorace. Sai kusan magariba Talba ya baro gurin Daddyn ka daman tun da CP ya hada Talba da masu binciken ya bar gurin zuwa asibiti.
A waje yai sallar isha'i sannan ya shigo gidan cike da damuwa, gaba daya sai ya rika jin kamar daman can ya saba da Aminatu kamar a gidan suka rayu yau kuma bata nan, kewarta ta kama shi. Yana shiga dakinsa ya jingina da kofar yana kallon dakin kamar a yau ya fara ganinsa, sai dai gaba daya hankalinsa ba a gurin yake ba. Closet ya nufa ya raba jikinsa da sutura ya sannan ya daura tawul ya nufi bathroom, yana shiga ya cire tawul din ya aje ya kunna shower ya sakarwa kansa ruwa. Da ya gaji da tsayuwar sai ya zauna a cikin bathtub din ya lumshe ido yana ta sauraren yadda ruwan ke sauka a kansa.

AMINATU POV.

Ba zata iya fadar hanyar da aka bi ba domin idanuwanta a rufe suke, iyakar abun da ta sani sun yi tafiya mai nisa da ita kuma sun yi ta karwade karwade kamin su isa inda zasu aje ta. Bayan sun faka suka fito da ita suna haska fitila zuwa cikin katon gidan mai kama da sabon gida, sai dai ota baya iya ganin komai saboda idanuwanta a daure suke, mutumen daya daukota kuma ya sabata ne a kafada, saurare take ta yi har ta suka isa da ita cikin wani daki suka sauke ta, sannan dayan ya kai hannunsa ya bude mata idon, dayan kuma ya haske mata idanuwan da fitila sai ta kara runtse idon daman bata budesu ba.

“Ka tada mana injin mana”

Ta natsu sosai tana sauraren muryarsa, wai ko zata ji muryar wanda ta sani. Bata bude idon ba har sai da aka kunna engine din haske ya maye ko'ina na

dakin, sannan ta bude idonta a hankali ya kallesu, zaratan mazaje ne gudu hudu saba uku da ta gani lokacin da suka je dauko, daya bayan daya ta bisu da kallo dukansu fuskarsa a rufe take ban da mutum daya dake tsaye s gabanta, fari ne fes farin har ya so yai masa yawa, gashi faffada da jiki sai dai ba sosai ba, ta fi kura masa ido saboda shi ne fuskarsa take a bude kuma shi ne yai mata yanayi da Talba a lokacin da ya saka face mask, sai dai a yanzu ta gane a farin ne kawai sukai kamanceceniya, a fuska ba su da kama ko kadan.

“Kin san ni ne?”

Ta sauke kai kasa. Sam ba zaka ganta ka ce tana jin tsoro ba, domin bata nuna tashin hankali ba, kuma bata yi wani kwakwaran motsi ba, sai dai behind her face duniyar tsoro ce da zullumi, gaba daya sai wacan abun daya faru a wacan daren ya dawo mata sabo, su ma wadannan fyaden zasu mata? Miyasa suka dauko ta? Tana jin lokacin da suka fita suka rufe kofar dakin da karfi har da saka makulli, sai ta rumgume hannayenta ta kwanta akan tiles din hawaye da suka duniyar idanuwanta suka sauko mata sai har lokacin bata bude idon ba. A gurin suka barta ta kwana har safe sai takwas da wani abu suka bude dakin suka shigo sai suka same ta a zaune tana kallon kofar kamar dama tana jiran shigowarsu, wannan karon ma kowa ya rufe fuskarsa ban da mutum daya din nan na jiya. Abinci suka aje mata tare da ruwa.

“Kina bukatar wani abu?”

Dayan mai sanye da mask ya tambaya, sosai bakinta yai mata nauyi sai dai hakan be hanata yakar nauyin bakin ba har ta samu fitar da kalamanta tana kuka.

“Ba ni da uwa, ba ni da uba, ba ni da kowa, idan ma kun dauke ni ne saboda a ba ku kudi babu wanda zai ba ku, an kashe min kowa, kuma ban yi ma kowa komai ba, dan Allah karku cutar da ni, idan ma wani abun na yi muku ba tare da na sani ba, dan Allah ku yi hakuri”

Ta hade hannayenta tana rokonsu. Juyawa suka yi suna fita daga dakin daya bayan daya.

“Ni musulma ce, ina son zan yi sallah”

Ta fada kamin dayan ya karasa ficewa, sai ya juyo ya nuna mata kofar bathroom.

“Ga bandaki can kusa da ke”

Yana fadar hakan ya fice, sai ta juya a hankali ta kalli bathroom din, sai a lokacin ta lura da shi, kwantawa tai a gurin tana wani irin kuka mai taba zuciya, kalaman Inna suka dawo mata na cewar ta adana hawayenta kuka na gaba, a yanzu ta yarda da wannan.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ta fara maimaitawa tana bugun tile din gurin kamar zata ballashi.

_____
Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

BATURIYA POV.

Ji tai kamar kasa ta bude ta shige ciki, duk sanyi ac dakin sai ta ji gumi na kefo mata. Shi ma kansa kunyarta yake ji kuma yana jin kunyar kansa, ya kasa kallon inda take sai girgiza kai yake, be taba tunanin neman matansa zai kawo sa gurin kanwarsa, sam be ma taba tunanin kanwarsa na aikata irin wannan bakar sana'ar ba, kamar marar lafiya haka ya tashi ya nufi gefen gadon can nesa sa ita ya zauna ya dafe kai yana jin kamar yai kuka kuma ba kukan zai yi ba. Tana ganin haka ta sabi jakarta ta sulale ta nufi kofa, garin sauri ta fice daga hotel din ta manta face mask dinta har wani hade kafafuwa take. Tana isa gate din ta fara kalle kalle ko zata ga Napep, tafiya tai mai nisa sannan ta samu isa gurin da Napep din take sai da ta shiga ciki sannan ta fada masa inda zai kaita, nesa da gidan ya ajeta ta fita ta ciro 500 ta mika masa bata ko tsaya karbar canji ba ta fara waige waige ko zata ga wanda ya ganta. Sai da ta ga babu mai binta sannan hankalinta ya kwanta, ta daidaita natsuwarta sannan ta karasa gidan tana ta sake saken abun da zata fadawa Umma. Da sallama ta shiga falon ido wiki wiki kamar an kama barawo.

“Umma ba ki kwanta ba?”

“Karfe nawa yanzu? Yaushe aka gama sallah Isha'i ma”

“Ok ke haka ne”

Ta fada sannan ta zauna tana Allah Allah kar Umma ta tambeye ta inda ta tafi, a zatonta Umma zata yi tunanin ko suna waje ne suna zance.

“Ina kika je?”

Ta hade yawu.

“Wai yayarsa ce da bata da lafiya, shi ne yace na je na dubata, shi ne muka je tare”

“Yayarsa kuma? Yaushe kuka hadu da shi da har zai fara gabatar da ke a gurin danginsa?”

“Gaskiya mun kwana biyu da haduwa, kuma yana zuwa akai akai kawai dai ban bashi dama ba ne”

“To ya kamata ki tsayar da mutum daya, tun da kina da maneman nan, na fara gajiya da yawan fitar nan da kika”

“Ai yanzu kam indai ba wani uzuri ba da wahala na fita”

Umma ta yi shiru bata ce mata komai ba, ganin haka yasa Baturiya ta tashi sususu ta shige dakinsu. Cire hijabinta tai ta zsuna ta rafka tagumi tana tunanin daman duk gani ganin da take yi ma yayanta yana wannan dabi'ar? Tana boyewa gashi yanxu tun ba ta yi nisa ba asirinta ya fara tonuwa duk da ta san ba lallai ne ya fada ba saboda shi ma nasa mutuncin zai zuba a idon mahaifiyarsu. Hannu ta saka a jaka ta dauko wayarta ta kira Ramlee tana dagawa ta fara bata tambayarta inda ta san wannan mutumen.

“Kai ba dai har kin fito ba?”

“Yace wai mu bari sai gobe”

“Lafiya dai?”

“Lafiya kalau wai an kira daga gidansa matarsa ba lafiya”

“Okay bari na zo na maida ke”

“Ni ina gida yanzu, ina kika san shi ni fa ya min”

“Hahaha, kuma Wallahi zaki kwashi naira idan ya sake jiki da ke, mutume na ne sosai, ina kawo masa masu kyau sai dai ya fi son farare kuma sirara kin ga ai yana da jiki sosai”

“Eh, ashe kun saba”

“Sosai ma, ke ma ai labarinki kawai na bashi amman ya takura min na kawo masa ke, kamar zai cinye ni”

“Allah sarki yana da kirki”

“Sosai ma Wallahi”

Sama sama Baturiya ta bugu cikin Ramlee ta ji labarin yayanta sannan sukai sallama. Tun daga lokacin sai Baturiya ta kasa sakewa tana ganin kamar yayanta zai fadawa mahaifiyarta abun da tai ne. Bayan kwana hudu da farar hakan Yayanta ya shigo gidan, abun ka da namiji sai ya murje ido kamar ba shi ba, ita ce ma mai jin kunya, shi kuma sai hararta yake yana jin haushinta, domin a ganinsa bata rasa komai ba a gidan mahaifiyarta balle ace saboda rashi ne take wannan bakar sana'ar. Tana gaishe shi ta shige ciki dakin tana ta chatting dinta Fahat bata fito sai da ya tafi. Tun daga yanayin yadda Umma take watsa mata harara ta san akwai wani abu a kasa, hakan yasa ta fasa zaman a falon ta nufi kofar fita kamar daman can fitar zata yi.

“Rafi'a”

Gabanta ya fadi sosai ta juyo cikin tsoro ta kalli Umma.

“Zo ina da magana dake”

Ta juyo ta dawo kusa da Umma ta zauan kan kujera, zuciyar dake raba jini a jikinta na bugawa da karfi.

“Ga ni Umma”

“Yayanki ya bada sako ya ce a fada miki, ki fitar da mijin aure cikin satin nan ko kuma ya samu miki wani ko ya maidake gidan tsohon mijinki”

“Aa ni ina da wanda nake so”

“Na fada masa kina da manema, sai ce min yai wai Allah yasa ba mutnen banza ba ne, domin shi ya fara tunanin da laifinki a rabuwarku da Faruk shiyasa be fada ba, so yanzu ina son ki fada min, yayanki ya ganki a wani guri ne da be dace ba ko kuma kin fara tsayuwa da mutanen banza ne?”

“Ba ko daya, idan ma mutanen banza ne ni dai ba su zo min da maganar banza ba, dan haka ba zan iya shaidarsu da wannan ba”

“Sannan abu na biyu yace akwai wata kawa taki da kike mu'amala da ita ba yarinyar kirki ba ce”

“Kawata...”

Ta fada da siffar tunani tana kokarin kawar da tunani Umma, ita ala dole bata gane ko wace kawa ba ce.

“Ya fada miki sunanta?”

“Be fada min ba, ke ai kin san a cikin kawayenki wadanda ba mutanen kwarai ba, sai ki rabu da su tun wuri, kin fi kowa sanin yayanku, ko mahaifinku ba kai shi zafi ba”

“To Umma zan gyara”

“Cikin samarin wanda kika ji ya fi kwanta miki sai ki gabatar masa da shi”

Umma na kaiwa nan ta tashi tsaye ta nufi kicin. Baturiya ta sauke ajiyar zuciya cike da jindadin yayanta be fadawa Umma komai ba.

AMINATU POV.

Kullum sai sun bata abinci mai kyau da ruwa mai sanyi, ko bakar magana basa mata balle kuma duka, ko razanar da ita, sai idan tana musu magiyar su barta ta tafi gida, ko kuma ta dame su da kuka wasu daga cikinsu kan daka mata tsawa.

Sai farin mutumen nan ya taka musu burki. Yau kan su biyu suka shigo kawo mata abincin rana, sai suka same ta tana sallah. Tsaye suka yi har ta gama.

“Ki fara shan lemun kamin ki ci abinci”

Kallon lemun tai dake cikin roba da takeaway, sannan ta kallesu.

“Har zuwa yaushe zan yi ta zama a nan? Miyasa kuka kawo nan? Mi na yi muku?”

Ta tambaya hawaye na sauko mata. Sai dayan ya amsa mata.

“Sakamu akai”

“Waya saka ku?”

“Mu wawaye ne da zamu fada miki? Kin ce mana baki da kowa gashi nan an baza hotonki a ko'ina sai nemanki ake, a media an saka kuma saka a jarida da gidajen radio, har da tukuicin naira miliyan uku ga duk wanda ya san inda kike ko kuma ya kawo ki”

Shiru tai tana tunanin wanda zai aikata mata.

“Da gaske nake, bani da kowa, ban san wanda ya saka ayi wannan abun ba”

Ba su sake ce mata komai ba suka fice. Hannunta ta kai a kirjinta ta dafa zuciyarta duk duniya mutum daya ta san zai iya mata wannan shi ne Talba, ashe be manta da ita ba? Yana cikin mawuyacin hali amman haka be hana ta murmushi ba hawaye na sauko mata a lokaci daya. Sai dai abun da ya fi tsaya mata a rai waya saka ayi mata wannan abun? Miyasa suka dauke ta? Kudi suke so ko kuma suna da wata manufa ne na yin haka? Da alama ba mutuncinta suke son tabawa ba, somin ta sha jin suna fadar cewar ance kar su mata komai. Bata taba abincin ba balle kuma har ta sha lemun da suka bata umarnin ta fara shansa kamin ta ci abinci, har suka dawo suka tararda komai a yadda suka barshi.

“Baki ci ba?”

Ta yi shiru tana kallonsu, wannan karon dukansu fuskarsu a rufe take, har da farin mutumen daya saba bari fuskarsa a bude.

“Ki ci abinci yanzu”

Ta girgaiza musu kai a hankali.

“Dure zamu miki idan baki ci ba”

Fadar hakan da dayan yai sai ya saka ta makara jin tsoron, domin ba su taba cilasta mata cin wani abu ba a dole, sai wannan karon hakan kuma na nufin akwai wani abu cikin abincin ko lemu da suke son ta sha.

“Karka mata dore, ance kar mu cutar da ita”

Dayan ya fada, sai na kusa da shi ya kalleshi ya soma magana cikin daga murya.

“Idan ba mu mata duren ba ya zamu mata? Ai ba taba ta muka yi ba ba fyade zamu mata ba”

“Dan Allah Karku min”

Ta fada cikin kuka hankalinta na mugun tashi.

“Dauki ki sha ai ba maganin mutuwa ba ne”

Ta girgiza kai tana fashewa da kuka, sai biyun suka nufeta tana ganin haka ta mike tsaye da sauri ta fara ihu tana musu magiya, dayan ya rike ta ya kwantar da ita a gurin ya danneta da dukan karfinsa, daman abu ga marar karfi sai ta kaea wani yunkurin kirki sai kuka kawai take, dayan kuma ya dauki gorar ya bude ya saka dayan hannunsa ya matse bakinta ba shiri a dole ta bude bakin saboda azabar matsa da ta ji. Ya zuba mata lemun ta hade dan dolenta sannan ya sake zuba mata wani ta sake hadawa da karfi ya sake zuba mata har sau uku sannan ya sake ta ya mike tsaye da lemun. Wanda ya danneta ya sake ta sai ta fashe da kuka tana kallonsu. Yawu ta fara tofarwa duk da kasancewar bata ji wani canji a cikin lemun ba, lemun mangoro ne bata ji ya canja ba a dandanonsa da kuma kalarsa. Sake nufo ta sukai dayan yana rike da wani bakin kyalle, tana ganin su sake dosota sai ta fashe da wani sabon kuka.

“Aa... Aa... Aa.. Dan Allah.... Aa... ”

Ba su saurareta ba suka riketa dayan ya daura mata bakin kyallen a ido ya tsuke idon ta yadda ba zata iya gani ba. Sannan dayan ya dauketa suka fice da ita daga dakin zuwa motarsu, tana jin lokacin sa suka saka ta motar suka yi mata key har suka fita daga gidan tana jin komai, sai dai ta yi shiru tana sausaren motar dake tafiya, sai da suka fara nesa sannan ta soma jin jikinta babu karfi wani abu na sauko mata mai kamar bachi kuma ba bashi ba, gaba daya sai ta ji jikinta kamar ba nata ba, babu kuzari ko kadan, a lokacin ne hankalinta ya fada nisan zango, sai ta fara kalaman da bata ma san tana yi ba.
Nisa sukai da ita sosai kamar za su bar garin gusau da ita sai da suka duba inda babu kowa sannan suka faka suka fito da ita suka shigar da ita cikin gonar dake cike da ciyawa suka kwantar da ita, suka cire mata kyalle. Farin mutumen nan ya tsaya daga waje yana tura rubutawa number Kabir sako.

Idan ka ga dama ka zo ka dauki matar dan'uwanka a lalan area, akwai wata gona a gurin ta gafen gonar akwai ciyayi ka duba da kyau zaka ganta, amman ina gargadinka karka kuskura ka fadawa kowa, kuma karka zo da police a nan gurin idan ba haka ba zmgawarta zaka tarar, kuma zaka jeka kanka a matsala

Bayan ya gama rubuta sakon ya tura masa, sannan ya cire line ya saka a bakinsa ya karya shi ya jefar.

“Let's go guys”

Yana fadar haka sai duk suka nufo motar mai kama da siyana suka shiga daman shi ne mai jan motar sai yai mata key suka kama hanya.

TALBA POV.

Yadda ya ga rana haka ya ga dare, banbancin daren da rana a gurinsa dare akwai duhu rana kuma haske ce, kwana yai sallah da karatun kur'ane yana rokon Allah ya bayyana masa Aminatunsa. Sai da asuba ya fita zuwa masallacin dake cikin gidan yai sallah tare da ma'aikatan gidansu da Daddy da kuma Kabir, bayan sun gama suka fito tare da Daddy suna tafiya a hankali Daddy na yi masa kalamai na kwantar da hankali.

“In shaa Allah za a ganta, an baza security ko'ina ana bincike yadda ya kamata, kuma kaga ga hotunan nan kace ka saka ga kuma kudin daka saka, a media ma an watsa abun a jarida, za a ganta In Shaa Allah, ko dan gudun tonon asirin ko waye”

“Tsoro nake Daddy karsu cutar da ita, ga shi bata dade daga warkewa daga wata damuwar ba ta yan kidnapping yanzu kuma ace ta hadu da wannan Allah kadai ya san wani hali take ciki”

Daddy yayi murmushi irin na su na manya ya dafa kafar Talba.

“Ka kyautata zato kuma ka yi addu'a, babu abun da zai same ta, yarinya marainiya Allah zai tsirarta ita da yarda Allah”

Talba ya daga ma masa kai. Sai da suka isa inda za su rabu sannan Daddy ya ce.

“Ya kamata kaje anjima ka duba Leila, ko kuma ka wuce musu da abun karyawa ma idan an gama, na je jiya da rana kuma na koma da dare Momynka ta fada min baka zo ba, nace mata kana tsoro ne kar ta maka fada”

“Zan je anjima In shaa Allah”

“Good”

Daddy ya fada sannan ya shige part dinsa. Talba kuma ya sauke ajiyar zuciya ya nufi dakinsa yana shiga phone dinsa ce first thing daya fara dauka, sai ya tararda kiran Ali kusan 5, data ya kunna ya shiga social media hoping to see a good news, sai dai har ya gama shawaginsa ya kashe datan be ci karo da inda aka ce masa an ga Aminatu ba, sai dai masu masa repost wasu kuma suna masa addu'a da sharing. Mikewa yai tsaye ya nufi closet dinsa ya cire doguwar jallabiyarsa ya daura tawul ya fito ya nufi bathroom, wanka yai ya fito jiki ba kuzari rabonsa da abinci tun wanda ya ci jiya da safe ban da ruwa babu abun da yake iya ci, ko tea da yake dan sha sai ya ji gaba daya ya fice masa a rai, ga wani zafi zafi da jikinsa yai alamar fever na son kama shi. Karamin tawul ne a hannunsa yana goge jikinsa har ya isa gaban katon madubin dake dakin ya tsaya yana kallon kansa, babu canji a jikinsa shi din nan dai ne, sai dai fuskarsa ta dan fada kamar wanda ya kwana biyu yana ciwo, ga idanuwansa da suka yi ja har yanzu ba su sauya ba farin ya bata. Hakan ya ji baya bukatar shafa komai bayan turaren da ya zame masa rayuwa. Shi kawai ya shafa ya nufi closet din ya saka suit farar riga da bakin wando ya rike jacket din a hannu ya dauki agogonsa ya saka sannan ya saka black cover shoes ya fito ya dauki turaren tufafi ya fesa ma jikinsa sannan ya dauki wayarsa da wallet dinsa da key mota ya fice domin cika umarnin Daddy.

LEILA POV.

A asibitin suka kwana saboda Ali yace a barta ta dan huta in ya so da safe sai ya sallamesu. A dole Momy ta hakura suka kwana a asibitin ta tura Amal gida. Sau biyu Daddy an zuwa dubata, na farkon bayan ya fito daga gurin CP ne ya karaso nan ya dubata a lokacin ma bachi take, bata samu ganinsa. Sai dai Momy ta fada masa komai da Talba yai ban da ita abun da tai ma Talba. A tunaninta Daddy zai nuna bacin ransa ne kan abun da Talba yai sai ta ga tsabanin haka a fuskarsa da kalamansa, sai kokarin wankesa yake a idonta wai kar taga laifinsa, yana cikin rudani a yanzu. Hakan yasa bata sake cewa komai ba ko fitar da yai bata yi masa rakiya ba. Da dare ma ya sake dawowa duba Leila a nan kam ya same ta a farke har yai mata ya jiki ta amsa masa da cewar ta ji sauki. Be yi mata maganar ba gudun kar ya daga mata hankali ita ma Leila bata masa ba, sai dai kana ganinta ka san tana cikin damuwa. Be bar asibitin ba sai da ya tambayi Momy Talba ya zo duba Leila daker ta amsa masa da aa, domin a yanzu ko sunan Talba bata son ji, har Ali da yake abokinsa ya fiye masa shi domin ya nunawa Leila kulawa sosai kamar yar'uwarsa, minti kadan sai ya shigo ya duba lafiyarta. Sai kusan sha daya na dare sannan Momy ta kira Family how dinsu gurin Hajiyarta ta fada musu cewar suna asibiti amman da sauki ba sai sun zo yanzu ba. Hajiya kasa hakura tai sai da aka kawo ta ta duba jikin Leila sannan hankalinta ya kwanta, Momy ta fade mata daga biri har wutsiya na abun da Talba yai, ba laifi ita kan ta ga laifin Talba sosai sai dai tayi ta nanatawa yarta cewar abun da Talba yai ba haramun ba ne. Har guri mota Momy ta rako mahaifiyarta tana kara nuna mata bacin ranta ita kuma tana tausarta.

A asibitin Momy ta kwana tare da Leila, Washe gari guraren karfe bakwai Hajiya Saratu kanwar Momy ta doro asibitin cikin wani irin bacin rai da mamakin abun da Talba yai, Momy ta jidadin zuwanta sosai domin ta samu mai kama mata ta yaga. A nan Momy ta baje mata hajar a faifai, wato ta kara fada mata komai bayan wanda mahaifiyarsu ta fada mata. Hajiya Saratu ta daki kirji ta ce.

“Dan adam butulu, to Wallahi karki yarda, idan ma kika ce ba zai aureta ba ai ita kika jefa a matsala shi kuma kin ba shi damar yayi rayuwarsa yadda yake so, to ba zata sabu ba bindiga a ruwa, Wallahi Talba be isa ba”

Momy ta tabe baki.

“Ai ne ya fice min gaba daya”

Hajiya Saratu ta ja wani dogon tsaki, tana jin kamar ace Talba yana gabanta ta wanke masa fuska da mari.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran

amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

TALBA POV.

Tsaye yai bakin kofar yana jin kamar kar ya shiga. Sai da yaja dogon numfashi ya sauke sannan ya kai hannunsa ya tura kofar dakin ya shiga. Da Momy ya fara hada ido tana ganin shi ne ta dauke kai ta maida wani gafen irin bata ma kaunar ganinsa din nan. Be damu ba ya maida dubansa gurin Leila wanda ta kura masa ido tana ta kallonsa kamar yau ta fara ganinsa. Murya kasa kasa yai sallama daga Hajiya Saratu har Momy aka rasa mai amsa masa, daman ita Leila ba magana take ba sai idan ta kama dole. Karasawa yai kusa da ita ya duka ya aje kwandon dake dauke da ayan abinci.

“Ya jikinki?”

Da sauri ta Leila ta dauke kai ta juyar zuwa wani gafen tana zuciyarta na mugun kuna kamar ana soyata, wani irin son Talba da kaunarsa ke dibanta, duk yadda take yaki da zuciyarta akansa sai ta kasa samun hadin kanta, a yanzu kam ta gane tana matukar son Talba, domin abun da yai mata ya kai ace ta tsani jin sunansa ma balle ganinsa, amman sai jin take kaunarsa na karuwa a zuciyarta, da ace wani namijin ne yai mata abun da Talba yai mata da tuni ta goge shafinsa a zuciyarta, amman ta kasa komai akan Talba, ko zaginsa da Momy take.bata jindadi a yanzu, balle kuma tai yunkurin cireshi a ranta sai take jin kamar zata rabu da rayuwarta ne. Be damu da kin amsa masa da tai ba ya sake tambayarta.

“Zazzabin ya sauka?”

Nan ma bata amsa masa ba, daman can idan yan yangarta suka tashi bata amsa masa balle kuma a yanzu da yai mata babban laifi. Hajiya Saratu ta tabe baki.

“Kai dan Allah yanzu baka ji kunya ba? Kana tare da yarinya shekara da shekaru sai ka tsallake kaje can wani guri ka auri wata, wai kuma har ka iya zuwa kana zargin Leila da sace yarinyar, yanzu duk abun da Yaya Amina tai maka ka manta kenan har na iya zagayawa ka munafunceta ka ci amanarta”

Ko da wasa be kalli inda Hajiya Saratu take ba, sai kawai ya cigaba da magana da Leila.

“Kina bukatar wani abu?”

Nan ma banza ta bawa ajiyarsa. Sai ya juya ya kalli Momy.

“Momy zan wuce, Allah ya sauwake, idan likita ya sallame ku ki fada zan zo na maida ku gida”

Uffan Momy bata ce masa ba, har ya nufi kofar fita ya fice sannan ta bishi da harara tare da jan tsaki. Leila kuma ta kara juyar da fuska tana hawaye, abun da

Talba yai mata abu ne mai matukar ciwo da azabtarwa, ta ya zai auri wata? Bayan ita bata shirya yin sharing dinsa da kowa ba? Not him ko da wani ma ta aura bata da niyar zama da kishiya, kuma kishiyarma sai irin Aminatu?

“Ban san abun da ya gani a jikin yarinyar nan ba”

Ta furta tana Juyowa ta kalli Momy har lokacin hawaye na sauko mota.

“Talba ya cutar da ni”

Ta lumshe ido. Momy ta kyabe baki.

“Uhm yayi duk wannan abun ne saboda yana ganin kamar zaki iya mutuwa idan kika rabu da shi, ni Wallahi sai yanzu nake nadamar rainon yaron nan da na yi, ko dan ganin idona ya kamata ace wani abun be aikata shi ba amman sam baya gudun bachin raina”

“Haka nake ji Momy, ina jin kamar idan na rabu da Talba zan iya mutuwa, a yanzu na yarda Talba yana so na, domin mai son ka yana gudun bachin ranka, kuma yana son farincikinka, amman Talba baya son farincikina, kuma ba shi da buri sai na saka ni a bakinciki, daman Kabir yana ta fada min ban yarda ba...”

Ta fashe da kuka sosai, daga Momy har Hajiya Saratu tausayinta ne ya kamasu.

“Allah zai kawo miki wani, zaki samu mai sonki kamar zai mutu”

Momy ta fada cike da tausayinta sannan ta tashi ta fara cire kayan dake cikin gwandon.

“Wai kina nufin yanzu duk wahalar da kika yi da yaron nan ta tashi a banza kenan? Haka zaki zuba ido yana yadda yake so, ya bar miki ta ki yar a bakinciki bayan kuma ya gama bata mata lokaci, idan ya san baya sonta tun farko miyasa ya amsa cewar yana son ta din?”

“To Saratu ya zan masa? Ai idan na bari Leila ta auri ma na zama wata marar zuciya, kuma ita kanta Leila ta zama wata dabam ba ita ba”

Momy ta zuba soyayen dankali da kwai ta mikawa Leila.

“Ci ko kadan”

“To ai ita kam tana sonsa, kamar ki ce zaki rabasu domin yarki ce zata sha wahala shi kuma yaje ya cigaba da rayuwarsa daman haka yake so, kuma bayan kowa ya san an saka musu rana sai ace an fasa aure? Ai kin bawa dangin mahaifiyarsa abun da suke. So kenan”

Hajiya Saratu ta fada, ajiyar zuciya Leila ta sauke sannan ta girgiza ma Momy kai.

“Ba zan iya ci ba”

Ta sauke kafafuwanta kasa ta sauko saman gadon ta share hawayenta ta nufi kofar fita.

“Ina zaki?”

“Iska zan sha”

Ta amsawa Momy ba tare da ta juyo ba, Momy ta bita da kallo cikin tausayawa.

“Allah sai isar miki ga Talba, yaron nan ya ci amanarmu kuma ba kowa ya daure masa ba irin Engr shi ya daure masa gindi yana yadda yake so, da an taba shi yace dan dan'uwansa kamar shi yafi kowa dan'uwa a duniya, wannan abun ma ai ba mu kadai yai ma ba har da shi amman baya gani, sai kokarin karesa ma yake”

Hajiya Saratu ta bude baki.

“Ahhh to laifin waye? Ai laifin duk naki ne, tun farkon da kika fara ganin take takensa sai ki daukar masa mataki, yanzu haka zaki zuba masa ido yaje ya rayu da wacan yarinyar karama dazun nan ma fa kika gama bani labarin abun da ya faru da yarinyar”

Momy ta zauna a kan gadon majiyanta tana kallon yar'uwarta.

“To ya zanyi? Na isa na yi wani abun Engr ya fara min masifa yace zan kashe masa da? Hmmm ke ma dai kamar baki san yadda yake ji da Talba ba”

“Ai ba kirkiri zaki masa ba, ta hanyar da mutanen nan suka bi ta nan zaki bi, ke yanzu ko ance muki Talba a hayyacinsa yake wannan abun zaki yarda? Daman can yan'uwan uwarasa ba kishi suke da ke ba? Allah kadai ya san hanyoyin da suka bi suka ka laka masa son yarinyar nan, amman Talba dake ji da kansa ko ance min ha kula wata wanda bata kao yarinyar nan ba zan yi mamaki balle kuma wannan!”

Momy ta kalli kofar dakin dake rufe tana nazarin kalaman Hajiya Sadiya. Ganin haka ya bawa Hajiya Sadiya damar cigaba.

“Ke yanzu kina tunanin Talba a karon kasa zai yarda ya auri yarinyar? Har ya fara wannan haukar akanta?”

“Ban fa gane me kike nufi ba?”

“Tsaye za a tashi mana, a gyara shi ya dawo hayyacinsa, kuma a mallake shi ta yadda zai yadda kika juya shi ke da Leila, ai daman gidan Babban mutum kamar Engr haka ake yi, ba ma shi kadai ba kowa ayi ma ake sai ki ga kowa tsoron matar gida yake sai abun da ta fada ake bi, kuma ba a isa a tsabawa umarninta ba kowa tsoronta yake, amman yanzu duba ki ga halin da Leila ta shiga, har kike ikirarin za a fasa aure, idan ma kin ce haka ai ba lallai ne mahaifinta ya yarda ba, kuma yadda kika ga yana wannan rawar kadan idan ma an yi auren ba dadi Leila zata ji ta matar zai yi ta yi, domin bana jin a banza suka bar shi har ya amince da aurenta ma”

Ta kara tana wani kada kai kamar kadangarawa. Momy ta jinjina kai tana kara cika da tsananin mamaki sai a yanzu ita ma tunaninta ya bata haka.

“Lallai da maganarki, daman ba so na suke ba, gani suke na tare musu komai, tun ba kai haka ba suke fadar wai bana bari yana shiga gurin dangin

mahaifiyarsa kaza kaza, sai dangina nake nuna masa magana dai ba kai, ni kuma gani na yi tun da ba wani abun azo a gani suke masa ba, miye na wani bibiyar dangi talakawan banza da basa tsinana masa komai, a nan tare da mu kuma ba rasa komai ba”

Hajiya Saratu ta tabe baki.

“Hmmm ni Wallahi ko a mafarki ban dauka Talba zai iya miki haka ba, ko da ma zai iya yi ma Leila ai ke be kamata yai miki ba, ko da yake ba a cikin hayyacinsa yake ba, idan ba haka ba ace har da dan'uwanka ka zarga? Ko shi mahaifin waya sani ko wani abun suka masa yake masa wannan haukar son kamar zai cinye shi, balle mutanen kauye nan da kika gani suna da sirrika kala kala kuma sun fi mu shiga malamai”

“Ai ni yanzu na yarda da maganarki, ko da ace Talba yayi haka be dace ace akan wannan karamar yarinyar yake wannan abun ba, saboda yarinyar bata dace da shi ba sam, a matsayinsa na babban mutum dan babban mutum, kuma yarinyar da ta gama tambade da lalacewa a cikin daji tare da barayin nan waya sani ma ko tana da wani ciwon?”

“Aifa sai ki yi, shi yanzu ba ganin duk ganin wannan yake ba, an riga an rufe masa idon, magani kawai a warware abun sannan a kalle tsakaninsu, ya ji babu wanda yake so a duniya sai Leila sai ki ga ya koma kamar ba shi ba, amman yanzu kika ce ki raba tsakaninsu ai ita zaki cutar”

“Haka zaayi bari dai mu koma gida, kuma na warware wasu matsalolin da suke gabana, da wata fitina data kunno min kai”

“Ta me ba?”

Hajiya Saratu ta tambaya, sai Momy tai sarin kawar da zance, domin ko kadan bata son kowa ya ji hali da suke ciki ita da yarda a game da Baaba.

“Aa tsanina da masu aiki ne, zan yi solving din komai In Shaa Allahu”

Momy ta fada tana kashe ido, domin ta matsu su koma gida ta tafi gidan gonarta ta binciki mai gadinta. Leila ta kusan awa a waje sannan ta dawo dakin tana kallonta kasan akwai damuwa tare da ita domin fuskarta da yanayinta ya nuna haka.

“Leila ki samu ki ci wani abu, ki kwantar da hankalinki komai zai wuce”

Hajiya Saratu ta fada tana daukar jakarta ta rataya, Leila ta kalleta sannan ta nufi gadon ta zauna, sai Hajiya ta matsa kusa da ita tana murmushi.

“Ke kwantar da hankalinki indai Talba ne zaki same shi yadda kike so, komai zai wuce”

A take idon Leila ya cika da hawaye.

“Mama Saratu babu abun da zai sauya, Talba ya riga ya bata komai”

“Aa lokaci be kure ba, za a gyara komai, duk wannan abun da yake ba a hayyacinsa yake yinsa ba, za a kare ko minene da yardar Allah”

Leila ta yi shiru tana nazari.

“Asiri akai masa kenan?”

“Kema kina gani ai kin san haka, idan ba asiri ba mi Talba zai yi da yarinya kamar wannan, na yi magana da Yaya Amina idan komai ya laba hankali ya kwanta sai a dukufa da addu'a”

“Amman Mama Saratu idan aka kare abun zai rabu da ita?”

“Idan ya dawo hayyacinsa kan ai kin san komai zai koma kamar ba yi ba ne, kuma zai dawo miki kamar bawanki”

“Da gaske Mama Saratu?”

“Ke dai kwantar da hankalinki kawai, na miki wannan alkawari, taya zamu zuba ido ya bata miki lokaci kuma yanzu ya bulo da wannan, ai ba zai yiyu ba”

Leila ta kama hannu Hajiya Saratu ta cike da jindadi.

“Na gode Mama, na gode”

Ta fada hawaye na cika idonta, domin hae ga Allah tana son Talba so mai tsanani, musamman ma a yanzu da take ganin haibarsa da kyausa na kara kwarjini a idonta, fitar da tai a waje ma tunanin yadda zata rayu babu shi a rayuwarta sai ta ji ba zata iya ba, kamar yadda ba zata iya bar ma wata shi ba, haka ma ba zata iya tarayya da shi da wata ba.

*** **** ****

Daga asibitin gidansu Hajiya Laraba ya wuce, yana fatar samun wani labari daga gurinta. A waje ya faka sannan ya fito ya nufi gate din yana tabawa ya ji shi a rufe, be yi mamaki ba wata kila saboda abun da ya faru ne yasa mai gadin yake rufe gate din a yanzu. Kwankwasawa yai mai gadin ya fara lekowa ganin Talba ne sai ya bude karamar kofar yana masa sannu da zuwa. Talba be kula shi ba domin s
haushinsa yake ji sosai saboda abun da ya faru, gani yake kamar ma shi yai causing din komai. Kai tsaye ya nufi main door din yana tuna yadda ta fito ranar ganinsa da ita na karshe. Ajiyar zuciya ya sauke a hankali sannan ya kwankwasa kofar falon, yau ma Hajiya Laraba ce ta bude masa kofar.

“Talba...”

“Ina kwana?”

“Lafiya Kalau, ya hakuri akwai wani labari ne?”

Ta tambaya tana kallonsa cike da tausayawa domin ta ga sauyi sosai a fuskarsa, ya yi rama kadan ga damuwa karar da idanuwansa da suka nuna be samu yin bachi ba a daren jiya.

“Babu, na zo na ji ko an samu wani abu ne”

“Shigo ciki mana”

Ta kara wangale masa kofar, har yayi kamar yace aa ba zai shigo ba, sai kuma ya kasa musa mata ya nasa kafarsa daya a cikin falon ya shiga. Falon tsif kasancewar yaranta duka sun tafi makaranta, da kanta ta nufi fridge ta dauko masa ruwa da cup ta kawo masa, sai ya saka hannu ya dauki ledar pure water din ya fasa ya kai bakinsa, be aje ba sai da ya shanye, ya sake daukar wasu ya shanye sannan ya aje ledar yana kallon wani bangaren na falon.

“Kaka ta kira ka?”

“Aa”

“Ta kirani akan maganar tarewawarta tana tambayar abun da ya dace mu yi, na fada mata ta bar komai a hannuna har kawo amaryar ba sai ta zo ba zan kaita, bana son na fada mata abun da ya faru ne hankalinta ya tashi”

Talba ya hade yawu ba tare da yace komai ba. Can kuma ya mike tsaye.

“Akwai wanda kike zargi da aikata wannan abun ne?”

“Babu Wallahi, tun da Aminatu bata da abokin fada, ni kuma ban san wani wanda zai iya yin haka ba, da akwai ai da na fada tun a lokacin da police din suke min tambaya”

Ya sake hade yawun bakinsa a karo na biyu.

“idan an samu wani labari dan Allah ki kirani”

“Inshallah, amman mutanen da suka dauke ta bana tunanin yan satar mutane ne, domin da su ne da yanzu sun kira”

“Aminatu bara gama sanin unguwanni ba, kuma bana jin tana da nunber kowa a kanta, balle ta ba su su kira ko kuma ita ta kira”

Ya fada yana kara jin ba dadi.

“Kai Allah dai ya bayyanata cikin aminci, kuma ya tsareta”

“Ameen”

Ya amsa sannan ya nufi kofar fita Hajiya Laraba ta rako shi har kofar falon, zuciyarta cike da tausayinnsa, tsaye tai yana kallonsa har ya fice sannan ta koma cikin falon. Da kansa ya bude kofar gate din ya fito ya nufi motarsa, zama yai a cikin motar ya rasa abun da ke masa dadi.

“Duk wanda ya aikata wannan abun idan ma saboda ya nisanta ni da ke ne, ko ya saka na gujeki yayi kuskure, idan kuma saboda ya saka ki a damuwa a ba zan taba yafe mishi ba, kowaye ne”

Ya fada yana hade duka lisp dinsa ya ciza da karfi yana mai jin ina ma ace zai ga wanda ya aikata wannan abun. Slowly yake driving har ya isa office, kamar wani

marar lafiya haka ya fito daga motarsa yana tafiya kamar mai tausayin kasa ya shiga cikin kamfanin. Bata kallon masu gaisheshi balle ya amsa, daman can ba al'adarsa ba ce amsa gaisuwar ma'aikatansa balle kuma yanzu da ba gaisuwar ce a gabansa ba. Zaune a kujerarsa ta office ya saka hannunsa daya yana murza goshinsa dake masa mugun zafi kamar zai cire. Tsakanin shigowarsa office da kwankwansa kofar da Madina tai be fi minti biyar ba zuwa bakwai.

“Yes...”

Ta fada ba tare da ya dago kai ba, ai ta tura kofar ta shiga rike da karamar kula, sai da ta kusa isa inda yake sannan tai masa sallama. Dagowa yai ya kalleta with surprise.

“Na san baka samu ka ci komai ba, saboda damuwa shiyasa na hada maa wannan cake din, kuma zan hada maka tea idan kana so”

Shirun da yai yana kallonta ne ya bata damar cigaba.

“And we can talk if you want...”

“Madina abokin wasarki ne ni?”

“Aa nima ba wasa na zo na maka ba, amman ina ganin kamar babu laifi ka nunawa mutum kulawa, ko ba komai Talba kai ne wanda Leila zata aura”

“This should be the last time da zaki sake shigo min office ba tare da ni na baki umarni ba, idan hakan ya sake faruwa a bakin aikinki, and ni ba irin mutanen da zaki rika tsayin game da su ba ne, get out”

A yadda ta ga temper dinsa ta hau ta san taba cewa tak zai iya marinta ko ma ya sallame ta gaba daya daga kamfanin. Da sauri ta juya rike da kular daman bata aje ba ta fice tana jin kamar ta fashe da kuka. Office dinsu ta dawo ta zauna bangarenta ta aje cake din a kasa tana boye fuskarta saboda idanuwanta dake cika da hawaye. Ta rasa taya zata samu kusanci da Talba, bata san abun da zata masa ba ya sake mata, a yanzu take gasgata zancen Leila da take fada mata cewar Talba mutum ne mai wuyar sha'ani.

‘Ko yaya yarinyar nan tai ta shiga ransa? Gashi nan duk ya be ya haukace akanta, yarinyar da bata kai ma ta wanke min talkami ba balle kuma shi’

Ta fada a ranta tana jin ina ma ace ita ce yake so haka ba Aminatu ba. Bayan fitar Madina ya kira Sakatarensa ya fada masa cewar baya son kowa ya dame shi, be ma'ana kar ya bari kowa ya shigo masa office, yana gama bada umarnin wayarsa tai ringing alamar kira da sauri ya ciro wayar daga aljihu ya duba, ganin Ali ne mai kiran yasa ya aje wayar kan tebur ya kwanta jikin kujerarsa yana lilo. Kiran na yankewa Ali ya sake yi masa wani, sai ya dauki wayar ya kasheta gaba daya ya aje.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Ali ya girgiza kai tare da maida wayar aljihu.

“Bana jin mun taba samun matsala da Talba da ta kai na jera masa kira fiye da hudu ya ki dagawa, ko da be daga kirana ba daga baya zai iya kirana sai dai yace min ina damunsa, ko kuma idan na sake kiran ya amsa, amman tun jiya da abun nan ya faru nake ta kiransa ya ki ya daga kuma be kira ni ba, Talba ya dauki zafi da yawa wannan karon”

Leila ta daga kai ta kalleshi.

“Saboda yana sonta ne right?”

Ali ya kalleta sai ya ji tausayinta ya kara kama shi, shekara nawa tana rainon soyayyar Talba a zuciyarta, ta shanye duk wulakancin da yake mata girman kansa da ji da kai duk ta dauka, amman ace a yanzu ya saka mata da wannan, shi kam yana ji Leila bata cancanci ma yai mata kishiya ba ko da tana gidansa balle kuma a yanzu da be aureta ba ya auri wanda bata kai tai tarayya da ita akan Talba ba, kuma ba tare da saninta ba. Ajiyar zuciya ya sauke ya zauna gefen gadon da take zaune.

“Leila Talba yana da fushi sosai, abu kadan ma zai iya saka shi fushi ko bacin rai, ke kanki kin sani. Wani abun ma zaka yi ne domin ka burge shi amman daga karshe ya dawo yana jin haushinka ko ganin laifinka, saboda ya nuna wannan kulawar ba shi yake nuna cewar yana son Aminatu ba, ina tunanin ya damu ne saboda a yanzu kamar tana karkashin ikonsa ne ta bata, kuma kin san halin gogan naki da tausayi, yana tausayinta sosai”

Leila ta yi irin murmushin nan da hausawa ke cewa ya fi kuka ciwo.

“Tausayi wani mataki ne ya so ne Ali, duk wanda ke tausayinka yana gudun wani abu ya same, yana gudun abun da zai saka ka kuka ko bakinciki, kuma tausayi kan hana mai yi maka shi cutar da kai, tun daga lokacin da ka hada shi da ita ya ji yana tausayinta sai komai ya canja, idan kana tausayin mutum zaka ji baka son komai ya taba shi, tausayi ya fi so ya fi kauna Ali. Mahaifina yana matukar tausayin Talba, saboda yana ganin ya tashi ba uwa ba uba, Daddy yana ganin Talba ba shi da wani gata a duniyar nan sai nasa, ba shi da kowa sai shi, wannan dalilin ya saka mahaifina baya iya musa a kan komai, kuma yana gudun abun da

zai bata masa rai ko kuma ya ji cewar yana kewar iyayensa saboda rashin wani ba... To irin wannan tausayin ne Talba yake yi ma Aminatu, yana gudun bacin ranta, ba shi da budi sai na son faranta mata, ranar daya kawo ta a gidan nan har muka samu tsabani da ita baka ga halin daya shiga ba, bana jin yana tausayin kansa kamar yadda yake tausayin Aminatu, sai dai ka san abun bakincikin? Ni baya tausayina, baya damuwa da damuwata, kin ci abinci miyasa ba ki ci ba? Me yake damunki? Me kike son ki ci? Shirya mu tafi wani gurin, Leila ina matukar kaunarki, me ya same ki? Zamu iya zuwa likita ya dubaki? Zamu tafi gurin shakawata, meet my new friends duk be taba min ba. Shim mu ba masoya ba ne?"

Ta karasa tana kallon Ali hawaye na zirya a fuskarta, sai kuma ta sauke kanta kasa tana watsa da yatsunta.

"Idan wani abu ya faru ni ce ta farko da yake fara zargi kamin kowa, ashe masoyi ya taba zama makiyi? Wani abun dariya kuma na kasa rabuwa da shi, a duk lokacin da na yi yunkurin yin haka sai na zuciyata ta hana ni, Talba yayi min duk wani abu daya kamata na goge shafinsa a tahirin rayuwata amman na kasa, yayi min komai daya kama ace na juya na bashi baya amman na kasa... Wata kila saboda..."

"Saboda baki taba bawa zuciyarki damar gwada son wani abun ba sai Talba"

Ya marasa mata sai ta kalleshi, numfashi ya aje sannan ya cigaba.

"Leila let me tell you something, ba a mutuwa akanmu mu maza, kuma ba a rayuwa saboda maza. Ke mace ce, mace tana da daraja a ko wane irin hali da yanayi na rayuwa. Ba a zabar mutuwa saboda namiji kamar yadda ba a zabar rayuwa saboda shi. Ki mutu a karan kanki idan kin tashi, mazan da suka ji za su iya mutuwa a tare da ke, za su zo ku mutu tare. Ki zabi rayuwa a lokacin da kike jin kin dace ki yi rayuwar, wadanda suke son ki za su zo ku rayu tare! Ki so kanki irin soyayyar da za ki iya kashe kanki saboda ki raya kanki, karki yaudari kanki ki bar zuciyarki ta raya miki wani namijin zai iya mutuwa saboda ke, kuma karki wulakanta kanki ki ji cewar zaki iya kashe kanki saboda Soyayyar Namiji, karki zurfafa karki tsananta kar kuma hakan ya saka ki yi ma soyayyar Namiji rikon sakaina kashi...!"

Ta share hawayenta tana nazarin kalamansa, sai kuma ta dago ta kalleshi shi ma kallonta yake kamin ya sauke idanuwansa ya mike tsaye. For the 100 time ta kara jin Ali ya burge ta, rayuwarsa so simple ba kamar Talba ba, ina ma ace Talba ne yake nuna mata wannan kulawar!

"Idan kin kimtsa zan iya saukeki gida, na fadawa Momy zan kawo ki gida da kaina"

Ya fada ba tare da ya kalleta ba, feeling some how. Dan murmushi ta samu kanta da yi sai a lokacin ta dauke idonta daga barin kallonsa.

"Matarka ta yi dace Ali, kana da saukin rayuwa, kuma kana da zuciya mai kyau, ka san yadda zaka kwantarwa da mace hankali"

"Abokina ma ya sani, Leila Talba yana da hali mai kyau, idan kika samu soyayyarsa zai maida ki sarauniya, domin idan yana son abu yana so ne da duka gaskiyarsa, Talba baya neman mata, ba neman mata kawai ba, Talba ya irin

mazan nan ba ne da kowace mace ke burgeshi ba, samu miji irin Talba da ce, ina fadi miki wannan ne from the bottom of my heart”

Ya fada yana jin kamar be dace ya dorata a wacan line na farko ba, miyasa ma zai fada mata wasu kalaman da zasu iya sauketa daga line da Talba yake.

“Amman...”

“Ina jiranki a waje”

Ya tari numfashinta tun kamin ta fadi abun da zata fada, be tsaya jiranta ba ya fice daga dakin. Murmushi tai ba wannan karon ba domin kalamansa ba sai dan tunawa da maganar da Hajiya Saratu tai mata. Mikewa tai tsaye ta juya ta kalli ko'ina na dakin sannan ta nufi kofar fita. Tafiya take tana kallon mutanen dake kai da kawo kamar ba ita ba, ba zaka ce tana cikin damuwa ba, kamar yadda ba zaka karancin nishadi a fuskarta ba.

*** *** ***

Lokacin da Ali ya ba su takardar sallama ya fadawa Momy ta tafi gida shi zai sauke Leila da kansa saboda akwai maganar da yake son yi da ita. Momy bata musa masa ba, ta Hajiya Saratu da Kawarta kuma aminiyarta Hajiya Murja da kuma mahaifiyar Madina wato Hajiya Aisha.

“To Hajiyoyi mun gode fa sosai Allah ya saka da alheri, na gode sosai”

“Ba komai Wallahi Allah dai ya kara lafiya, Madina ma ta so ta zo, sai dai kin san halin gogan naki baya son ana masa wasa da aiki, kuma tace wata kila ma Leila bata farka ba lokacin”

Momy ta yi murmushin yake.

“Allah sarki babu komai ai, idan ta dawo aikin sai ta zo ta dubata”

“Eh haka na ce mata nima, na san ai tana tasowa aikin zata fara zuwa”

“Uhm”

Momy ta fada sannan ta kalli Mairo dake hada kayansu tace.

“Ki yi ki hada kar a bar Direba yana ta jira”

“To Hajiya”

Ganin hakan ya yasa Hajiya Murja mikewa tsaye rike da key dinta na mota.

“Hajiya sai idan mun shigo gida, Allah kara sauki”

Ta fada tana kallon Ali da dan mamaki. Bayan fitarta mahaifiyar Madina ta fice ita ma, sannan Momy ta kalli Hajiya Saratu ta ce.

“Saratu zaku wuce gida tare da Mairo, ni zan shiga tawa motar akwai inda nake son biyawa”

“Okay”

Ta dauki jakarta ta bi bayan Mairo, sai da suka fita sannan Momy ta kalli Ali da Leila tana murmushi.

“To ni zan wuce sai kun shigo”

Leila ta daga mata kai, alamar to Ali kuma ya amsa mata.

“Okay Momy”

Sai da ta gyara mayafinta sannan ta fito daga dakin, kadan kadan take tafiya domin bata son ta hadu da su Mairo. Tsaye tai a bakin ward din tana kallon mutane, da gangan ta bata lokaci sai da ta tabbatar sun isa sannan ta karasa gurin da ta aje motarta ta saka key ta bude ta shiga. Reverse tai sannan ta dauki hanyar fita daga fita asibitin. Kai tsaye ta dauki hanyar da zata kaita tsohon gidan gonarta. Daman tun lokacin da aka aiko musu da sakon nan take son zuwa amman bata samu dama ba saboda abubuwa da suke faruwa, ga shi ta nemi number mai gadi ta rasa a wayarta. Tana driving tana kallon motocin dake bayanta, kamar an fada mata wani zai bibiyeta. Hankalinta be kwanta ba sai da ta shiga area babu wata mota dake binta a baya. Farkin tai gaban gate din ta danna horn, tana jiran mai gadin ya fito ya bude mata, sai ta ji shiru, hakan yasa ta sake danna horn din har sau hudu amman ba a bude mata ba, bude motar tai ta fito cike da mamaki, domin ta saba zuwa ta tararda shi kuma horn daya take ko biyu zai fito ya bude mata idan ma yana waje yana ganinta zai tashi ya bude gate din. Rufe motar tai ta fara takawa ta karasa daf da gate din sai a lokacin ta lura da an sakawa kofar gate din padlock har biyu, wani irin faduwa gabanta yai.

“Padlock yau kuma a gidan nan?”

Ta furta cike da tsananin mamaki, domin ba a taba saka padlock a rufe gidan ba, idan ma za a rufe gidan ta waje sai dai a saka key ba padlock ba. Har hannu ta kai ta taba domin tabbatarwa.

“To ina yaje? Ina iyalansa?”

Ta tambaya cike da confused, a take zarginta ya zama biyu bayan Madina a yanzu ma tana zargin mai gadinta, maybe shi ma yana da sa hannu a ciki. Tsaye tai tana ta kallon kofar da mamaki da kuma tunanin kala kala a ranta. Can kuma ya juya tana kallon unguwar, mai dauke da manya da kuma kananan gidaje. Gurin wani mai shago ta nufa tana isa tai masa sallama.

“Wa'alaikumussalam”

Mai shagon da mutanen da suke zaune tare da shi suka amsa mata.

“Dan Allah tambaya nake, Sani Mai gadin gidan can nake tambaya baban Rukayyah yana da mata Nafisa”

“Oh na gane shi ai mutume na ne, kullum yana nan muna hira, amman kwana biyu na daina ganinsa gaskiya, yaransa ma da suke dan fitowa suna wasa na daina ganinsu”

“Ya tashi ne dan Allah?”

“To Wallahi bana tunanin haka, domin a yadda muke da shi da ace tashi yai zai mana sallama, kuma zamu ga yana kwasar kaya, amman ko daya ba mu gani ba, kawai dai mun wayi gari mun ga gidan a rufe da kwado, kuma mun kira wayarsa kullum cewa ake a rufe take”

“Amman wani abu ya faru ne kamin ku daina ganinsa?”

“Aa Wallahi, babu abunda ya faru sai dai ba mu sani ba ko wani abun ya faru ya boye mana”

“Kuma ba ku ji labarin inda ya koma ba?”

“Aa Wallahi har yanzu ba su san komai akai ba, amman lafiya ke kike nemansa”

“Ni ce wanda yake yi ma gadi, kwana biyu ina zuwa bana tararda shi, ina ganin ya kamata na bincika, domin wayarsa bata shiga idan na kira”

“Ah gaskiya dole ne ki bincika kam, amman ke Hajiya ba ki san garin da yake ba?”

“Wallahi ban sani ba, wani mai gadin gidan mijina ne ya same min shi, saboda na fada masa ina son na samu mai min gadi saboda ba zai yiyu a bar guri haka ba kowa ba, nace masa ya sama min mai iyali”

“To shi ya kamata ki koma ki bincika gaskiya, wata kila shi ya san inda yake”

“Haka za ayi”

Ta fada sannan ta juya ta nufi gurin motarta. Bata ji tana iya musu godiya ba dan haka bata musu ba ta koma cikin motarta tai mata key, zuciyarta cike da tunani.

“To ko dai shi ne wai? Amman yadda yake dab kauyen nan zai iya wannan abun ma? Ina zai samu kudin hayar mutune da za su kawo sakon babu ko tsoro a tare da su? Ko kuma dai wani ne dabam? Amman taya akai shi kansa ma ya sani?”

Haka ta isa gida da sake sake, ta kulla wacan ta kwance wannan. Ba ta labartawa Leila komai ba sai da akai Sallah la'asar sannan ta kira Leila a waya tace mata tana son ganinta dakinta. Azaton Leila Momy zata yi maganar da Hajiya Saratu tai mata ne hakan yasa ta taso da saurinta ta shigo da dakin.

“Momy gani”

Ta fada bayan ta zauna kusa da Momy sai dai ita ta zauna kan gado ne, yayinda Momy kuma take zaune kan carpet da plate din fruit a gabanta.

“Kin ci abinci?”

“Momy bana son cin komai yanzu, bana ma sha'awar komai, amman Madina ta zo min da ice cream na sha”

Momy ta tabe baki.

“Naje tsohon gidan gonata dazun, kuma na tararda gidan a rufe da kwado har biyu, me gadin baya nan.... ”

Momy ta fada mata komai ciki har da amsar da mai shago ya bata.

“To Momy ko dai shi ne?”

“Na yi wannan tunanin, to amman kuma ai be san abun da muka saka a gurin ba, kuma na saka tanki ruwa a gurin an cika shi da ruwa saboda kar ma wani yai tunanin ko akwai wani abu a gurin kin manta”

“Amman Momy ke fa kika sa shi ya gina ramin”

“Ai na fada masa kudi zan rufe a ciki, ta wani bangaren bana zargin mai gadin nan, domin ko samun wanda zai shirya wannan abun da shi aiki a gurinsa a yadda yake da kauyancin nan, dole dai akwai wani na kusa da mu daya san da wannan abun, kuma Madina nake zargi”

Leila ta daga kai sama.

“Haba Momy wani irin Madina kuma? Madina ba zata min haka ba, sai dai idan wani ne dabam”

“Wai har yanzu ba ki gane cewar Leila tana son abun da kike so ba? Ke yanzu baki gane saboda Talba ta nemi aiki a kamfanin nan ba? Ba ki gane saboda shi take kara kusanci da ke ba? Ko jiya da Talba yake magana baki lura da yadda ta fara kuka ba, ita fa da kanta take tambayarsa ka yi aure? Sannan ta fice tana kuka, na lura neman gindi zama a gurin Talba yasa ta dauki yarinyar nan ta kaita gidansu, amman ke da yake baki da tunani duk hankalinki be kawo miki haka ba”

Leila ta yi shiru tana nazarin kalaman Momy da suka soma shigar mata a kwakwalwa.

“Kin fada mata inda muka binne Baaba?”

“Eh saboda ta tambaye ni lokacin da nake bada labarin kuma na fada mata”

“Hmmm Leila baki jin magana, sai da na gargade akan karki fadawa kowa wannan maganar amman baki ji ba, saboda kin dauki Madina kin maida ta uwarki, ba ki da shawara sai nata”

“Amman wace riba Madina zata ci idan tai min haka Momy, ko da ace tana son Talba ta yi kokari tun da har ta iya boyewa”

“Saboda ta lalata aurenku mana, idan muna cikin wannan tashin hankalin kina ganin zamu iya sakin jiki har mu yi komai cikin kwanciyar hankali? Kuma zata iya tona miki asiri har Talba ya san komai, shiyasa har yanzu ta ki ta kulawa kowa kuma taki ta tsayar da wani”

Leila ta kada kai.

“Ina jin kamar haka ne, amman Wallahi na kasa yarda Madina zata min haka”

“Kin fada mata cewar an kawo miki Envelop da dankwalin Baaba a ciki?”

“Eh na fada mata, sai tace min wai akwai mai bibiyata wata kila lokacin da muka rufe akwai wanda ya gani, shi ne zai yi amfanin da wannan damar ya samu kudi, har take ce min wata kila ma shi ne yai garkuwa da Aminatu”

Momy ta nisa duniyar tunani tana nazari.

“Wani lokacin Momy ina ganin kamar Madina ba zata iya min haka ba, domin ko a yanzu magana take min akan abun da Talba yai har take cemin kar hakan da yai ya saka na gujeshi ko na ce na fasa aurensa kamar yadda kika yi ikirarin aikatawa, tace min idan akai haka ai an bawa ita Aminatun damar da take so”

“Makirin mutum babu abun da baya iyawa Leila, munafukin mutum yana da wuyar ganowa, ki yi taka tsantsan da ita, kuma ki daina fada mata sirrinki, Allah yasa ma baki fada mata maganar da muka yi dake da Saratu ba”

“Na fada mata, kuma tace kar na yi domin magani dan kwana arba'in ne, kuma zai iya yiyuwa ba asiri suka masa ba, akaran kansa ne yake yin komai, tace min wai duk ranar da maganin ya kare Talba zai ji ba zai iya zama da ni ba”

Momy ta yi murmushin takaici.

“Ina jin wani sirrinki ma da Madina ta sani ni kaina ban san shi ba, yadda kika zaunawa ki bude mata cikinki ai ita bata bude miki nata haka, ko ta taba yin zancen wani sauyinta da ke? Kin tambayarsa miyasa bata tsayuwa da samari? Amman kin zama sakarya kullum sirrinki na cikin kunnuwanta, ta san komai na ki”

“Zan canja mata ai yanzu, idan tana da wata manufar zan gano”

Momy ta tabe baki.

“Allah yasa zaki iya, je da kanki ki kira min Mustapha ki bude masa kofar karamin falo ta baya ya shigo, kuma ban ce ki bari kowa ya sani ba”

“Mustapha kuma Momy?”

“Eh mi ya kawo min Sani ai, zan tambaya na ji ko yasan inda sanin yake da kuma garinsu”

“Amman Momy kar garin bincike mu tonawa kanmu asiri fa”

“Babu abun da zai faru”

“Okay”

Ta mike tsaye ta nufi kofa kana ganin tafiyarta kasan bata da wani kuzari a jikinta. Tana daf da ficewa sai kuma ta juyo ta kalli Momy.

“Momy yaushe zaki yi magana da Mama Saratu?”

“Sai mun natsu tukuna, kuma ki kama bakinki idan Amal ko Kabir ya ji maganar nan kin san har Daddynku sai ya ji ta”

Ta gyada kai sannan ta kai hannu ta bude kofar ta fice.

_____

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

KABIR POV.

Murmushi yai ya kalli Doc Hassan.

“Ai yawanci haka ake ta fama, musamman masu haihuwar fari din nan, shiyasa bana son ana kirana na karbi haihuwa sai dole Wallahi”

“Ai idan ta kama kam dole ake kira, kuma idan kai ne a duty dole kaje”

“To ya muka iya, ai dole mu yi”

Cewar Doc Hassan, Kabir yayi murmushi tare da saka hannunsa aljihu ya ciro wayarsa tai kara alamar shigowar sako. Ganin private number ya bashi mamaki tun a saman screen din ya fara karanta sakon kamin ya bude shi gaba daya.

Idan ka ga dama ka zo ka dauki matar dan'uwanka a lalan area, akwai wata gona a gurin ta gefen gonar akwai ciyawa ka duba da kyau zaka ganta, amman ina gargadinka karka kuskura ka fadawa kowa, kuma kar ka zo da police a nan gurin, idan ba haka ba gawarta zaka tarar, kuma zaka jefa kanka a matsala

Da farko ji yai kamar be fahimci sakon ba, hakan ya saka shi sake karantawa, a karo na biyu kuma sai yake ganin kamar be karanta daidai ba. Haka ya bi ya karanta sakom yafi a kirga sannan ya yarda da shi aka turawa shi, amman waya turo? Number a boye take. Da sauri ya saki karfin da yake rike da shi ya juya har Doc Hassan na tambayar lafiya amman be tsaya ya amsa masa ba. Number Talba yai dialing sai ya ji ta a rufe, da sauri ya kira number Leila sai da wayar ta kusa yankewa sannan tai picking.

“Hello”

“Leila Talba na gida?”

“Aa”

Ya kashe, sannan ya shiga contact dinsa neman number Ali, ya kira shi bugu daya Ali ya dauka.

“Hello Kabir”

“Talba na tare da kai?”

“Aa lafiya?”

Kabir be tsaya ce masa komai ba ya katse kiran, kamin ya karasa office dinsa har da hadawa da dan gudu, yana shiga ya dauki keys dinsa ya fito da sauri kamar gudu gudu. Ya nufi gurin da aka tanadarwa likitocin domin aje motocinsu ya , rumfar da aka rubutawa Doc Kabir Mu'az Shimkafi ya nufa yana isa gaban motar ya bude ya shiga, yadda yai reverse ma sai da ya firgita mutanen dake zaune kusa da parking spot din. Kamar an biyoshi haka ya fara gudu yana tukin da dayan hannunsa dayan hannun kuma sai kiran number Talba yake ana fada masa a kashe take. Sai da ya kusa isa Lalan sannan wani tunanin ya zo masa.

‘Idan kuma wani ne yake shirya masa wani abun fa? Ko kuma an fada gurin ne saboda ya zo ayi garkuwa da shi? Ya kamata ya samar da Police’

Ya rage gudun da yake ya sauka daga titi da zimmar komawa ya je police station, sai kuma wata zuciyar ta kawo masa wani tunani.

‘Idan kuma kamin police din su zo wani abun ya same ta fa? Ko kuma police din su kara bata masa lokaci, idan kuma ya fadawa Momy hana shi zuwa zata yi, Daddy ma zai iya hana shi zuwa saboda tsoro, kuma idan ya kyaleta a can be yi ma Talba adalci ba saboda halin da yake ciki’

Ya cika bakinsa ya iska ya busar. Sai kuma ya hau titi ya cigaba da tafiyar, sai da ya isa unguwar sannan ya tsagaita gudun da yake ya faka motar a kusa da inda suka kwatantan, a cikin motar ya zauna yana kallon ko'ina yaga idan akwai wani mai ganinsa ko kuma mai bibiyarsa, cikin tsoro ya fito daga cikin motar ya nufi gonar har ya isa cikin ciyayin ya fara leke leke yana lekawa yana waiga bayansa, babu mai ganinsa domin gurina da babu mutane sosai manya da kananan motoci dake kai kawo. Kara matsawa yai gaba cikin tsoro da fargabar abun da zai same shi yana dubawa, har zuciyarsa ta fara raya masa cewar karya ne kawai an shirya masa hakan ne wata kila saboda a sace shi, kamar ance masa yi hakuri ka kara gaba kadan yana yin haka sai ya hango mace a kwance tana ta juyo bakinta na motsi, sai dai baya iya jin abun da take fada saboda ta yi nisa da shi sosai, da sauri ya saka wayarsa aljihu ya karasa kusa da ita tana kwance cikin ciyayin idonta a rufe da bakin kyalle bakinta kuma a bude tana fadin.

“An kashe Baba...Babana.... Kuma sun kashe Inna... Sun yankan... Ya Saminu... Sun yanka Yaya Ibrahim.. Sun fasa kan Ya Rilwanu, ba ni da kowa a yanzu sun kashe min kowa sun kone mana abinci....”

Dukawa yai ya saka hannunsa biyu ya dagata sannan ya kwance kyalen dake idonta. Sai ta ji ta rike shi da mugun karfi.

“Tsoro nake ji, kashe ni za su yi....”

Idonta a bude suke amman sun juye kamar wanda tai shaye shaye gashi sun mata ja sosai. Daukarta yai ya fito da ita daga cikin gurin da sauri har yana hadawa da gudu gudu. Yana fitowa gurin ya nufi inda ya aje motarsa kasa ya fara ajeta da zimmar ya bude motar sai ta rike masa riga gam.

“Tsoro nake ji, gasu nan da fuskoki za su dauke ni”

Duk yadda ya so ya daga ya bude motar sai ta ki sakinsa, sai da yai da gaske sannan ya samu ya banbare hannunta ya bude back seat ya dauke ta ya saka ta cikin ya rufe, har lokacin bata daina kalaman da take ba, duk abun da ya zo bakinta fada take tun daga kan abun da ya faru da ita a kauye, sai kuma ta tsakuro wani bangare na sace da mutanenan suka yi. Kabir fuki yake gabansa na faduwa sai kuma ya juya ya kalleta.
Dayan hannunsa ya saka ya ciro wayarsa ya kira asibiti ya sanar musu zai zo da Emergency su shirya masa komai. Yana yi yana juyawa ya kalleta. Cikin kankanen lokaci ya isa asibitin kai tsaye emergency ya nufa yana faka motarsa aka kawo dago da sauri, sai ya fita ya zagaya ya bude motar ya fito da ita daga cikin motar sai ta rike shi da karfi tana kuka.

“Dan Allah ka ce karta min komai, dan Allah ka basu hakuri, ban musu komai ba, ban yi ma kowa komai ba, marainiyace ni ba uwa ba uba ba ni da kowa”

Fada kawai take domin har yanzun mutanen take gani, kuma abun ya zame mata biyu tana ganin wadannan tana wadancan barayin dajin, shi kansa Kabir din data rike bata sam ko waye ba domin bata iya ganin komai sai fuskokinsu. Wani irin tausayinta ne ya kama Kabir daker ya samu ya kwantar da ita saman gadon sai ta rike masa hannu.

“Yankani za su yi, dan Allah ka ba su hakuri...”

Dauketa yai daga kan gadon ya nufi main door din emergency da ita. Da kansa ya shigar da ita daya daga cikin dakunan da aka tanada domin bata taimakon gaggawa, a nan ma da yai yunkurin sauke ta akan gadon sai ta ki bashi hadin kai hawaye sai sauko mata suke gwanin tausayi.

“Bani allura”

Nurse din ta shiga hada allurar ta mika masa, sai ya karba da dayan hannunsa ya ware cinyar hannunta Nurse din ta saka kaďa ta goge mata inda za a ayi mata allurar shi kuma ya soka mata a hankali, sai da ruwan allurar suka fara shiga a cikinta sannan ta soma jin zafin allurar a take ta kara bata fuska ta fashe da kuka.

“Wayyo Babana....”

Sai ta sake shi domin jikin nata ya kara zama weak. A nan ya samu damar kwantar da ita saman gadon ya soma bata taimakon gaggawa. Sai da ya tabbatar komai ya tafi daidai sannan hankalinsa ya kwanta ya fito ya baro mata dakin. Waje ya fito zuciyarsa da tunani kala kala, waya turo masa sakon miye dalilinsu na yin haka? Ina suka kaita da suka dauke ta yanzu kuma miyasa suka dawo da ita?

“Dole ne na sa a bincika min boyayar number idan akwai yadda za ayi ta fito, saboda na gano ko waye”

Wannan karon a fili yai zancen, sannan ya sake dialing number Talba, har lokacin a kashe take, hakan yasa ya yanke shawarar tura masa sakon karta kwana.

Na kira wayarka switch off, wani ya turo min sakon inda Aminatu take kuma na je na dauko ta tana nan asibiti

Bayan ya tura ya jingina da karfen gurin, yana kira number wani abokinsa.

“Doc Kabir”

“Dahiru ya kake ya gida?”

“Wallahi Alhamdulillah, kwana da yawa”

“Mun gode Allah, tambayarka nake son yi nasan ku ne masana harkar computer kuma kana aiki da kamfanin line”

“Okay ina saurarenka”

“Wani case ne muke ciki, kuma yau sai aka turo min sako da wata boyayyar number, to shi ne nake son na ji idan akwai yadda za'ayi a gano number da kuma mamalakin line”

“Shi ya fi komai sauki, ka shigo gobe domin yau na tashi aiki, and make sure ka zo da police order”

“Okay, ba matsala, zan shigo goben In Shaa Allah Thank You”

Ya katse kiran tare da sauke ajiyar zuciya, sannan ya dago daga jinginen da yake ya nufi ward din da Aminatu take, a hankali ya mai hannu ya tura kofar dakin ya leka. Sai ya hangota tana ta sharar bachinta drip din da aka saka mata yana tafiya kamar yadda ya saka shi. Sakin kofar yai a hankali ta rufe kanta sannan ta koma office dinsa ya zauna. Sai da yai kamar ya kira Momy ya fada mata sai kuma wata zuciyar ta hana shi, saboda zata iya fadawa Leila kuma ba zama lallai ganinta ya yi musu dadi ba. Jinginawa yai da kujerarsa yana kallon kofar office din kamar mai jiran shigowar wani. Ta wani bangaren kuma yana tuna wasu kalamai da take ta fada wadanda suka shafi tarihin rayuwarta.
Gaskiya ya tausaya mata, a yadda take da matashiya da ita ace ta fuskanci irin wannan kalubalen na rayuwa abar tausayi ce sosai. Be koma dakin ba sai da ya sauke nauyin sallah La'asar, daman ya kwatantan zata farka kamin lokacin ko kuma ta gota 4pm kadan. Da wayarsa ya sake kiran number Talba sai ya jita a kashe a lokacin ne gabansa ya soma faduwa, domin be san Talba da kashe waya ba, ko Meeting zai shiga sai dai ya saka wayarsa Silent, amman ace tun safe har la'asar wayarsa na kashe.

“Allah yasa lafiya dai”

Ya furta cikin tsoro da faduwar gaba.

“Doc Kabir baka wuce ba? Ko kana da da duty dare ne?”

Ya juyo yana kallom kashiya dake masa maganar.

“Aa ina da patient ne shiyasa ban koma gida ba”

“Okay Allah ya sauwake”

“Amin”

A tare suka jero suna magana sai da suka kawo cikin asibitin sannan suka rabu shi ya nufi gurin harkokinsa, Kabir kuma ya nufo Ward din da zata sada shi da dakin da Aminatu take ciki, wannan karon ma kamar barawo haka ya tura kofar dakin ya shiga, ya karasa har gaban gadonta ya kama hannunta ya cire mata drip din a hankali sannan ya aje hannun yana kyakkyawar bakar fuskarta, ta yi kyau sosai kamar ba ita ba, ba kyau na kwaliya ba, yana mata kallon wacan lokacin ne da Talba ya kawo ta gidansu, a lokaci akwai rama da duhun fata, a yanzu kuma ta yi jiki kuma bakin fatarta ya ragu sai sheki yake. Agogon hannunsa ya kalla sannan ya juya ya fice daga dakin, be wuce two to three steps ba wayarsa dake hannunsa tai kara yana dubawa sai ya ga number Talba.

“Tana wane daki?”

“Emergency room 7”

Yana amsa masa ya tsinke wayar, Kabir ya dan tabe baki sannan ya nufi pharmacy dake asibitin domin karbo mata wani magani, da yake ganin ya dace ta sha shi idan ta farka.

Fitarsa da kamar minti hudu ta fara motsa kafafuwanta, tana jin jikin kamar ba mata ba, kanta yayi nauyi sosai har bata iya bude idanuwanta, duk yadda ta so tai unkurin bude ido sai ta kasa, ta dan bude baki tana fitar da iska, can kuma ta fara motsa yatsunta. Ta fi karfin minti goma a haka tana son bude idon ta kasa, haka ma ta yunkura ta tashi zaune shi ma ta masa, daker ta samu ta fara motsa hannunta, da kafafuwanta tana jin masalar na dan rage mata. Tana cikin wannan halin ta ji an turo kofar dakin da karfi, da gudun Talba ya karasa kusa da ita yana kallonta da mugun shock numfashinsa har wani rawa yake, a take idonsa suka cika da kwalla, hannu ta kai ta inda iskar dake zirya a hancinta yana shiga da fitar da numfashi ya sanar mata zuwan Talba. Dukawa yai a gurin kamar mai rokon gafara ya kama hannunta ya rike da hannayensa biyu yana sumbata kamar wanda baya hayyacinta, kamin ya dago ya daga ta daga kan gadon ya rumgume ta a kirjinsa tsantsan kamar ance masa wani zai sake sace ta. Lumshe ido yai yana kara matseta a kirjinsa gaba daya sai ma rasa abun da zai yi kuka ko farinciki.

“I miss you so much Shalele na i miss you”

Ya furta yana dagowata daga kirjinsa ya sumbanci goshinta, ya kai hannunsa ya shafa gashin kanta, ya sake shafa fuskarta sannan ya maida ita a kirjinsa.

“I can not do without you, the only one girl i miss”

Ya fada yana lumshe ido, ya kara matseta kirjinsa. Wani irin bugawa zuciyarsa take da karfi irin bugun da ya wuce misali. A hankali ta bude idon sai ta soma

ganin dishe dishe kamar wanda ta shekara tana bachi, dagowa tai a hankali ta kalleshi sai ya sauko da fuskarsa saman tata yana shakar numshinta kamar yadda take shakar nasa, kallonta yake ido cikin ido hancinsa da nata suna gogar juna, sai hawaye mai zafi ya sauko ta gefen idonta, da sauri ya rumgumeta.

“You are safe in this hands of mine, ba zan sake nisa da ke ba, babu abun da zai sake samunki i promise you this”

Ya fada try to calm himself.

“I love you so much Aminatu, you drive me crazy, dana rasa ki na ji kamar na yi hauka, i miss you more than i did before”

I kara matseta a kirjinsa kamar zai fasa kirjin nasa ya saka ta ciki.

“I feel you... You're heart in my heart”

Ya fada idonsa a rufe hawaye na sauko masa, ba tabbatar haka haka tai marmarinta har sai a yanzu da take gabansa, ya rasa inda zai saka ta a kirjinsa kamar ya hadeta ta zauna a cikinsa haka yake ji.

“Ya...lla...bai.. ”

Ta gwada yin magana, sai ya dagota da sauri ya saka hannayensa yana shafa fuskarta cikin wani irin shauki na farinciki.

“Talba...”

Ya fada nata sannan ya sunbancin goshinsa ya sumbanci saman idonta na dama ya sumbanci na hagu ya sumbanci hancinta, sannan yai masa da bakinsa ya shigar da lips dinsa cikin nata. Kabir na gani haka sai ya saki kofar a hankali ta yadda ba zata yi mara ba, kamar yadda ya bude ba tare da ta yi kara ba, juyawa yai rike da takardar maganin ya nufi office dinsa.

FARUQ POV.

Mama ta fashe da kuka, domin tun da ya tafi be taba kiranta ba ko sau daya, tun tana jiran kiransa har ta fara tsarata tana tunanin ko wani abu ya same shi ne.

“Haba Mama sai ka ce mutuwa na yi”

Faruk ya fada daya dayan bangaren a wayar abokinsa daya ara ya kira da line kasar wato line nijar mai +227.

“Miyasa baka kirana? Kasan irin tashin hankalin da nake ciki? Tun da ka tafi baka sake kira mun ji halin da kake ciki ba, kullum hankalina a tashe yake”

“Mama Wallahi inda muka je ba a kira, domin daji ne da ba a samun service sai an fito cikin gari, kuma a lokacin da muka isa muna isa aka ce mana ga motar da

zata tafi aiki nan, ba mu tsaya komai ba muka bita, kuma tun da muka shiga ban fito daga dajin na Libiya ba sai yanzu”

Mama ta share hawayenta.

“Kana dai lafiya ko?”

“Lafiya kalau Mama, addu'arki ta karbu na samu zinari mai yawa wanda ban taba saka ran samu ba, kuma In shaa Allah cikin satin nan zan dawo”

“Alhamdulillah Alhamdulillah Alhamdulillah, haka nake so, Allah ya tsare ya dawo da kai lafiya”

“Aamin Mama, Mama ina Sultan?”

A take murmushin dake fuskar Mama ya bace, sai dai tana ganin a irin wannan halin da yake ciki na farinciki be kamata ta fada masa abun da zai bata masa rai ba.

“Ya fita waje gurin wasa, idan ya dawo zan fada masa kana gaishe shi”

“To Mama, ya jikin na ki?”

Ta kalli hannunta na hagu da bata iya komai da shi saboda paralyze din dake son kamata na hawan jini.

“Alhamdulillah Lafiyata kalau, Allah ya maka albarka ya dawo da kai lafiya”

“Aamin Mama ina dawowa zan siya miki gida mai kyau mai tales da gate ki zauna ke kadai”

“Allah ya amince, kuma ya sa muna da rabon ganawa”

“Aamin Mama, ban mika masa wayar, idan zan taso zan sake kiranki”

“Toh Allah ya tsare ya dawo da kai lafiya”

“Aamin”

Shiru tai tana saurare sai da ya katse kiran sannan ta sauke ajiyar zuciya tana murmushi.

“Mai hakuri madawaci, Allah ya kawo ka lafiya dana, dan albarka”

Kanwarsa dake kusa da Mama ta karbi wayar tana murmushin jindadi.

“Na san yana zuwa zai daukeki ya kai ki asibiti, a baki magani mai kyau”

Murmushi Mama tai.

“Allah ya kawo shi lafiya”

“Amin”

Ta amsa cike da jindadi, Mama ma jindadin ne karara a fuskarta.

“Je ki kai wayar kar masu ita su aiko”

“To”

Ta amsa tana mikewa tsaye ta dauki Hijab dinta ta saka sannan ta fice. Da wayar komata ya kira saboda ya kira line Mama ya ji shi a rufe na kanwarsa ma haka ya san ba zai wuce ace sun siyar da wayar ba abu a gurin talaka.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

“Na ji tsoro sosai”

Ta fada hawaye na sauko mata fuskarta na tsakiyar hannayensa, yawo kawai yake da idonsa a fuskarta.

“I know, dole zaki ji tsoro, amman na miki alkawari daga yau ba zaki sake jin tsoro ba, i will always hold your hand and walk right beside you, you will never be alone”

Ya maida ta a kirjinsa.

“Me kike so ki ci?”

Ya sake dago da ita daga kirjinta yana jiran amsarta, sai ta kura masa ido bakinsa a bushe.

“Talk to me Baby”

Ya fada yana kallon lips dinta, sai ta marairaice masa tana shirin yin kuka, ganin haka yasa ya maida ita kirjinsa ya rumgume.

“Okay, zan kawo miki tea ko wani abu mai nauyi ki sha okay?”

Ta gyada masa kai a jikinsa tana kara lafewa kamar kyanwa. Saman kanta ya sumbanta sannan ya dago da ita.

“Zaki iya zaunawa na zo?”

Ta lake bafada tana turo baki gaba kamar zata yi kuka.

“Tsoro nake ji”

Ya kai hannunsa ya shafa gefen fuskarta.

“Babu abun da zai same ki, okay”

Ta mike tsaye a hankali yana dauke hannunsa daga fuskarta Kabir ya turo kofar dakin ya shigo. Sai Talba ya juyo yana kallonsa Kabir ma kallonsa yake daman saka a ransa Talba zai zarge shi.

“Look, ni ban dauki yarinyar nan ba, kuma ban san wanda ya dauke ta, kawai sako ya shigo a waya ne cewar naje na dauketa a inda na daukowa da boyayyar number, and a daren da kake magana ban bibiye ka ba, ban san ka aureta ba ma, ko da na sani babu abun da zai... ”

Kabir be karasa ba Talba ya isa inda yake tsaye ya rumgume shi da sauri. Tsaye Kabir yai a gurin kamar hoto domin be tsammaci haka daga gurin Talba ba, kallon Aminatu dake zaune tana kallonsu.

“Thank you so much”

Ya furta sannan ya sake shi ya nufi kofa.

“Zanje na samo mata wani abu ta ci”

Kabir ya juya ya bishi da kallo da mugun mamaki har ya fice sannan ya juyo ya kalli Aminatu.

“Did he...”

Sai kuma yai shiru ya daga kafadunsa ya karaso inda take zaune.

“Idan kin ci wani abu ki sha wannan maganin ko wane biyu”

Ta daga masa sai ya juya ya nufi kofar fita, yana daf da ficewa ta ce

“Na gode”

Sai ya juyo ya kalleta.

“Aikinmu ne ceton rayukan mutane”

Ya furta sannan ya fice tare da ja mata kofar. Talba ya shiga motarsa ya dauki wayarsa daya bari a cikin motar ya kira Daddy ya sanar masa, har yayi dialing number Momy sai kuma yai shiru yana nazari, ya san ba dadin labarin zata ji ba, hakan yasa ya fasa kiranta sai ya kira Hajiya Laraba ya fada mata, sannan ta kira Ali. Ring daya ya dauka.

“Ka gama fushin ne ko kuma ka kira ka yi min wani fadan ne?”

Talba yayi shiru kamar ba zai ce komai ba, sai kuma yai murmushi.

“An ga Aminatu”

“Wow What? I mean how”

“Labarine mai tsayi, yanzu zan je na siyo mata abun da zata ci ne, we will talk later”

“Okay kuna ina ne?”

“Asibiti Kabir ne ya daukota”

“Kabir kuma? How?”

“Later”

Talba ya kashe wayar, domin a yanzu bata mamaki ko tunanin abun da yadda akai komai ya faru yake ba, ta lafiyar Aminatu yake daga baya komai zai zo. Wani restaurant dake kusa da asibitin ya nufa ya siyo farfesu da snacks da drinks, sai kuma wani tea da yaga suna hadawa mai kamshi, ya hado da bread din na kwakwa, sannan ya fito waje ya siye fruits aka hada masa komai da komai dake gurin. Kamin ya dawo asibitin har ya tsawalla tafiyar tai masa nisa sosai. Da taimakon masu mopping din asibitin ya samu ya shigo da duka abun da ya siyo. Sai da suka jera komai sannan ya ciro wani abu daga aljihunsa ya mika musu. Dagowa Aminatu tai tana kallonshi.

“Oh na manta ban siyo brush ba, amman ai zan iya wanke miki baki da wannan”

Ya nuna yatsansa, sannan ya karasa kusa da ita ya kama hannunta yana wasa da siraran yatsunta.

“My cute girl”

Ya sumbacin yatsun hannunta, ta kalleshi ido narai narai kwalla kwance a ciki.

“Yunwa nake ji”

“Okay”

Ya sauka saman gadon da saurinsa ya sauko da kafafuwanta da zimmar daukarta sai ra marairaice masa fuska.

“Zan iya tafiya fa”

Baya musa mata hakan yasa ya kama hannunta ta mike tsaye, sai dai tafiyarce da rawar jiki, yana ganin haka ya saka gefenta a gefen jikinsa ya rumgume yana kallon yadda take takawa kamar mai kirga steps dinta. Sai da ya fara shiga bathroom din sannan ya shigo da ita har lokacin tana makkale a barensa, tap din ya kunna ya tara hannunsa ruwa suka taru sai ya kai mata a baki ya zuka ya kurkure bakin ta zubar.

“Good, to yanzu bude baki”

Ta bude kamar yadda ya bukata, manununsa na yatsa ya saka ya a cikin bakinta yana gogawa, sannan ya cire yatsan ya sake cika hannunsa da ruwa ya kai mata ta zuka ta sake kurkire bakin ta zubar. Sannan ya sake saka mata yatsan wannan karon da dan karfi ya goga mata saboda ya samu ya wanke mata bakin yadda ya kamata, sai ta bata fuska tana son yi masa kuka.

“Da zafi”

“Okay”

Ya rage gogar da karfi, har ya gama wanke mata ya wanke mata fuska sannan ya rumgumota suka fito daga bandakin. Da zata zauna saman gadon ma be yarda ya kyaleta ta yi da kanta ba sai ya cirata ya dora saman gadon sannan ya fara bude ledodin.

“Me kike son ki ci, snacks akwai fruits kuma ga tea shiya kamata ki fara sha”

“Ruwa”

Ta fada domin ruwan ne abun da tafi bukata a yanzu.

“Ki fara shan tea saboda ruwa zai takure miki hanji ne a yanzu”

Sai ta lake kafada, kallonta yai cike da burgewa.

“Da alama zamu yi ta drama da ke”

Ya dauki gorar ruwan ya bude ya mike tsaye ya kai mata a baki, tana shan kadan yai hanzarin cirewa, ya dauko tea dake cikin wani kofin roba ya bude ya kai mata a baki.

“Tun da kin sha ruwan yanzu ki sha tea”

Ba musu ta bude bakin a hankali tana shan tea har sai da ta sha rabin cup sannan ya rufe ya aje, ya bare ayaba ya kai mata a baki. Sai da ya tabbatar ta koshi sannan hankalinsa ya kwanta ya samu natsuwa, ya bata ruwan ta kara sha.

“Wannan likitan yace idan na ci abinci na sha magana”

Magana take masa kamar zata yi kuka, domin ko kadan bata son magani balle kuma allura. Ya nufi inda ledar maganin take ya bude duba sannan ya juyo ya kalleta.

“Nawa ake sha?”

“Wai biyu biyu”

Ya ballo ko wane biyu ya dawo kusa da ita ya zauna rike da magani.

“Shalele na, magani ne kawai zaki sha saboda ki kara samun lafiya da kuzari”

Ta kara bata fuska kamar ta fasa masa kuka, sai ya kai dayan hannunsa ya kwanto da ita jikinsa sayan hannun kuma dake rike da magani ya mika ya dauko gorar ruwan ya kai mata maganin a baki.

“Bude baki sai ki sha ruwa kadan”

Fashewa tai da kuka, daman ko a gidan idan tao ciwo. inna da Baba suka ce ta sha magani kuka take.

“Sorry”

Ta bude bakin ba dan ranta na so ba, daker ya samu ya tura mata maganin, sannan ya dora mata da ruwa, tana hade maganin take ta shan ruwa. Ya kai hannunsa ya shafa kanta.

“Ko dankwali babu akanki haka kika fita ko kuma su suka miki haka?”

“Da hajab ns fita ko lokacin da zasu min dure abun nan ina da hajab a nan dai ne na farko na ga babu hijab a jikina”

Ya gyada mata kai, baya son ya cika ta da tambaya ne abun ya tsaya mata a rai. Mikewa yai tsaye ua fara gyara gurin yana dauke abubuwan da ta ci ya maida su gefe daya, suna haka akai knocking kofar kamin ya bada damar shiga police din suka shigo cikin shigar gida.

“Pls ku dan jira a waje ta kintse mana”

Da okay suka amsa masa suka juya suka fice, dai ya cire shirt dinsa ya mika mata.

“Daure kanki”

Ta kalli kirjinsa dake rufe da vest.

“Kai fa?”

“Ina da veat ai kuma ina da jacket a mota”

Ta nada rigar ta daura yadda zata iya sai ta ki tsayawa akanta saboda riga ce ba dankali data saba daurawa ba. Da kansa ya dauki rigar ya nadata kamar naden dankwali ya daura mata kai, ya gyara mata rigar jikinta, sannan ya maida ta gurin kan gadon.

“Zauna a nan”

Ya nufi kofar fita ya bude ya leka ya kirasu, sannan ya dawo da sauri ya zauna kusa da ita ya kareta ta yadda ba zasu iya ganin jikinta ba, sai fuskarta shi ma idan ya leko. Tambayoyi suka yi mata akan mutanen da kuma inda suka kaita da

abun da sukai mata, bata boye komai ba, tun daga daukarta da akai har zuwa yanzu da take kwance a asibitin sannnan suka saka aka kira musu Kabir sukai masa tambayoyi daga karshe suka karbi wayarsa suka tafi da ita saboda bincika wanda ya aiko masa da sakon. Sai da suka fice sannan Talba ya juyo ya kalli Aminatu sai tausayinta ya kara zurfafa a zuciyarsa.

“Kin shiga taskun rayuwa kala kala, amman yanzu komai ya wuce, babu abun da zai sake faruwa na miki alkawari, wani ba zai sake taba ki ba, ko a bachi ne”

Zancensa na karshe ne ya bata dariya har sai da ta bayyana hakoranta.

“Ya zaka san wani ya taba ni a bachi?”

Kallonta yake da murmushi a fuskarsa.

“That's cute smile i miss it...”

Ya kai hannu ya laba lips dinsa, aka turo kofar dakin, wannan karon Momy ce tare da Kabir sai kuma Leila dake tare da ita. Aminatu na ganin Momy da Leila wani irin tsoro ya kamata sai tai saurin kwance rigarsa dake kanta ta mike masa ta matsa baya. Kallonta yai sai ga gaba daya ta rasa natuwarta, ta sauke kai kasa. Juyowa yai ya kalli Leila dake sanye da wata farar rigar yadi saidai ta matse ta sosai tana rataye da jakarta sai bakar hula dake kanta, dauke ido yai ya kalli Momy wacce ta tabe baki tana kallonsu.

“Abun farinciki haka ba za a fada mana ba saboda an dauke mu makiya, sai Daddynka ne yake kirana ya sanar min”

“Ban san yadda zaki ji ba idan an sanar miki hakan ya saka ban sanar miki ba”

“Murna zan yi mana, ko ma komai surukata ta dawo, kuma zargin da kake akan yayana zai wanke, any way mun zo ne dai mu dubata ya jikin nata”

“Ta ji sauki”

“Bata iya gaisuwa ba ne”

Momy ta fada tana kallon yadda tai kyau kamar ba ita ba, duk da kasancewar a yanzu bata cikin kwanciyar hankali. Aminatu ta dago a hankali ta kalli Talba, sai ya gyada mata kai, sannan ta kalli Momy.

“Ina wuni?”

“Lafiya kalau ya jikin”

Momy ya amsa bayan ta bata kusan minti biyar tana kallon yadda bakar fatarta ke shining. A nan ma Aminatu kallon Talba tai yi sai da ya daga mata kai sannan ta amsa.

“Alhamdulillah”

“Sosai ko sai an fitar da ita waje?”

Kamin Talba yai magana Kabir ya tari numfashinsa.

“No daman sun bugar da ita ne,wata kila saboda kar ta ji ko ta gane inda take, amman ba wata matsala da na gani gaskiya, zama a iya sallamarta yau”

Momy ta juya ta kalleshi.

“No, ka bincika jininta in and out, kuma ayi mata hoto, ina son na tabbatar tana lafiya kalau so that mu samu salamar zuciya kamin mu zauna da ita”

“Tace ba a mata komai ba.”

Talba ya fada, sai Leila ta kalleshi tana dan daga gira zuciyarta na mugun soyuwa na ganinsu zaune a muhalli daya, daman dazun da ta tararda rigarsa a kan Aminatu shi yana sanye da Vest mutuwa ne kawai ba tai ba, I domin zuciyarta ta buga matuka.

“Really...? And you believe her?”

Talba ta juya ya kalli Aminatu dake cike da tsoro idonta har ya cika da kwalla, sai kuma ya juyo yana murmushi ya kalli Leila.

“Me zai hana? I trust her”

Ta yi murmushin takaici.

“That's good”

Ya sakar mata murmushi as respond, sannan ya kalli Momy dake fadin.

“Idan an gama bincikar komai aka tabbata tana lafiya, sai ya dawo da ita gida”

Kabir ya kalleta da mamaki.

“Gida...?”

“Yes.. Tana da gurin daya fi inda mijinta yake zaune ne?”

Talba ma kallon Momy yake kamin ya kalli Kabir su hada ido.

“Anjima Mairo zata kawo muku abinci da abubuwan bukata, idan kuma akwai abun da kuke so zaka iya kirana, and zan iya turo Zulai ta kwana da ita ko Hajiya Saratu”

Momy ta fada sai Talba ya girgiza mata kai.

“Za ta iya kwana ita kadai”

Leila ya kalleshi kamin ta sake Kallon Aminatu da har lokacin kanta yake kasa, ji take kamar tai kukan kura tai cikinta ta makureta.

“Allah ya bata lafiya, ya tsare gaba”

Momy ta fada sannan ta juya, Leila ce ta fara fita sannan Momy Kabir ya zama daga karshe. Suna ficewa Talba ya kai hannu ta dago fuskar Aminatu dake

hawaye, sai kawai ta fashe masa da kuka sosai har wani shessheka take alamar kukan ya tarar mata.

“Ohhhh”

Ya rumgume kirjinsa da sauri.

“Miye na kuka yanzu?”

“Baka fada min cewar Momy ta san ka aureni ba? Kuma ka san zata iya yi min komai, gashi Leila ta gan mu tare... ”

Yayi murmushi ya sumbanci saman kanta.

“Na yi laifi, amman ai kin ga yanzu kika dawo ko? Yaushe ma muka zauna Hira balle na baki labarin? Amman zan fada miki komai idan hankali ya kwanta”

Kamar yace mata na fada din haka ta ji, sai ta karawa kukanta mai har tana dan daga murya. Kara rumgumeta yai ya hura mata iska a saman idon sannan ya fara shafa kanta.

“Yi hakuri, ba zan sake ba ki daina yawan kuka yana damuna kuma kina takurawa kanki”

Ta dade tana ta kukan sannan ta tsagaita ba dan ta gama ba, sai dan ta gaji da kukan for now. Dagota yai daga kirjinsa

“Hey Black beauty.... So kike ni ma nai kuka?”

Ta kai hannu ta share hawayen daya makalle a idonta, sai ya yi murmushi ya kai hannu ya ja lips dinta ta turo gaba. Wayarsa ce tai ring sai ya mike tsaye ya dauki wayar ganin number Ali yai picking

“Hello?”

“Kuna Room nawa ne? Gani tare da Madam zamu dubata”

Talba ya fada masa sannan ya aje wayar ya kalleta.

“Ya kamata na sama miki tufafi mai kyau da zaki saka, bana son na ga jikin mace a awaje ko kuka mutane suna kallonta anyhow, bana son na ga mace tana barin jikinta a waje even though most of ladies sun dauki hakan a matsayin wayewa, amman ni bana so, kwaliyar mace da sakin jikinta is only for her husband, not for society”

Hausar kawai take oya ganewa idan yai, duk kalarmar daya hadata da turanci bata fahimtar komai idan ba Okay ba, shi ma saboda ya zama ruwan dare ne. Ta daga masa kai alamar to, sannan ta dauki rigarsa ta dora akanta ta kalleshi sai yai dariya har fararen hakoransa suka bayyana domin yadda ta dora rigar ne abun dariya. After like five minutes Ali ya turo kofar ya shigo, irin zaman da Talba yai a dazun da polisawan nan suka zo shi ya sake yi ya tare matarsa, fuskarsa ba yabo ba fallasa Ali na ganinsa ya san be gama saukowa daga fushin da yai ba. Haulat ta matsa kusa da Aminatu ta aje kular abinci tana kallon Talba.

“Maa Shaa Allah, wannan ce Amaryar ta mu?”

Amimatu ta kalleta da idanuwanta da sukai ja, sannan ta kalli Talba ya gyada mata kai sannan ta gaishe da Haulat matar Ali. Haulat ta amsa tana murmushi sannan tai ma. Talba barka da arziki.

“Can we talk”

Ali ya fada sai Talba ya mike tsaye daman yana jin kumyar ganinsa da vest da Haulat tai yi, a ganinsa hakan be dace ba, ko ba komai ita ai matar wani ce kamar yadda yake jin ba zai iya kyale matarsa ta kalli wani a haka ba. Ali ne ya fara fita sannan Talba ya bi bayansa, Haulat na ganin haka ta dawo kusa da Aminatu ta zauna.

“Ashe Amaryar ta mu kyakkyawa ce shiyasa Talba ya haukace mana”

Aminatu ta yi masa da kanta, sai Haulat tai murmushi.

“Da ma kin sake jikinki domin ni ba bakunta nake ba, na dade ina jiran na fa matar da Talba zai aura, muna ta saka ran Leila ce ashe kina nan daga gefe kina fadin ni ce”

Ta fada da fuskar zolaya tana lekan fuskar Aminatu, domin har ga Allah Aminatu ta burge ta, ga ta yarinyar kuma da alama bata da hayani da ji da kai ba kamar Leila ba da sau daya suka taba gaisawa da ita duk kuwa da irin shirin da Talba yake da Ali. Har Haulat ta bude baki ta sake zolayarta sai kuma ta fasa.

“Bari dai na kyale ki da ganin wannan ruwa ruwan kuka ce, kar Talba ya zo yace na saka masa mata kuka, amman dai ai zamu yi hira ko?”

Nan ma Amimatu bata ce komai ba, sai watsa take da yatsunta.

“Doc yace min galadi kike ina da yan'uwa a can wane gefen kuka a galadi? Ni ina ta kan wurin sarki ne”

Ko da jin an ambaci garinsu sai ta dago kai ta kalleta.

“A marnawa muke mu”

“Okay na san marnawa, akwai ma wani makocin mu dan can ne yana yawan zuwa, sai dai yanzu hare haren nan da ake kaiwa yasa ya daina zuwa dan yace an kashe masa yan'uwa gaba daya, yace yanzu ba shi da kowa sai dangi na nesa, matarsa ma ta dade rabon da taje garin balle kuma ni da yan'uwan nesa ne a garin rabona da garin yanzu kusan shekara goma kenan”

“Kai kin dade”

“Eh gaskiya na dade, tun Kakata na da rai, Yanzu rashin tsaron nan ma ai ya hana zumunci sai dole”

“Muma barayin suka koremu sun kashe min kowa”

“Haka Doc ya fada min, ai Wallahi na tausaya miki, Allah ya musu rahama amman yanzu komai zai wuce ai, kuma yadda Allah ya hada ki da Talba ai kin

warke domin zai kula da ke, ki rike abun ki hannu biyu da kyau, ko ba komai ai dan'uwanki ne”

Aminatu ta yi kasa da idonta, Haulat ta yi murmushi tana kallonta.

“Su Momy sun zo dubaki?”

“Eh ta zo, har da Leila”

Haulat ta dan tabe baki, sai dai bata ce komai ba, ta bar gulmar a zuciyarta, because this is not the right time da zata yi maganar da wasu da Aminatu no matter how little it's.

*** *** ***

“Ya akai Matarka ta san na auri Aminatu”

Talba ya tambaya fuska a hade sam ba zaka ganshi kace shi ne a dazun yake ta washewa Aminatu hakoraba yana rumgumarta.

“I told her saboda ta tambaye taga ka saka kudi da duk wanda ya gano inda take, amman ban fada mata abunbuwan da suka faru da Aminatun ba, kawai dai na fada maga gar gudun hijira ce kuma an kashe mata kowa nata, at the end kuma yar'uwarka ce Kaka ta saka ka aureta to abun da ya faru”

Talba ya bude motarsa ya dauko jacket din dake ciki ya saka, baya bukatar abokinsa ya rantse masa domin ya yarda da shi 100% akan sirrinsa.

“Don't tell me ka zo dubata ne, you're always on Leila side”

Cewar Talba yana jan zip din rigar data kara masa kyau. Ali ya sauke ajiyar zuciya.

“Look Man I'm sorry, na san na yi abun da be dace ba a ranar, ni ma raina ya bace ne sosai shiya saka abun da kai wa Leila baka kyau ta, taya zaka zargeta da batan Aminatu?”

“Idona ne ya rufe ta yadda bana iya ganin komai kuma bana saurarawa kowa a akan Aminatu, kamar yadda naka idon ya rufe ka ci zarafin matata a gabana, kuma kamar yadda idonka yake rufewa a duk lokacin da muka samu matsala da Leila”

Mutuwar tsaye Ali yai a gurin sam be tsammaci haka daga bakin Talba ba. Talba ya bude motarsa.

“Zan tafi wani gurin, you can take your wife mun gode da ziyara”

Yayi shigewarsa motar yai mata key ya bar Ali tsaye a gurin da mugun mamaki, sai da ya daina hango Motar Talba sannan ya ciro wayarsa dake aljihu ya kira matarsa ya ce ta same shi a mota.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Sai da dare Hajiya Laraba ta zo dubata, domin ta kira mijinta ya ce ta jira har sai ya dawo su taho tare. Haka kuwa akai sai da ya dawo sannan suka zo tare shi ya riko mata kulolin abincin da tai mata, ita kuma ta riko jakar kala biyu data riko mata. Ko da suka shiga dakin Amimatu na zaune kan sallaya tana sallah, Talba kuma na zaune kan kujera rike da wayarsa. Tashi yai ya koma zaman gadon ya bawa mijin kanwar mahaifiyarsa gurin zama.

“Maa Shaa Allah, Allah mun gode maka tun dazun na zo na zo ban samu na zo ba, ina fatar dai babu abun da ya same ta?”

Ta tambaya tana kallon Talba. Sai ya girgiza mata kai.

“Babu abun da ya same ta, kuma dazun da maraice ma an gwada jininta, hoto ma na can da safe za a karbo”

Aminatu na sallamewa ta juyo da sauri ta kalli Hajiya Laraba.

“Mama sannu da zuwa”

Sai Hajiya Laraba ta tashi da sauri taje ta rumgume Aminatu idonta na cika da kwalla.

“Alhamdulillah Auta, kin dawo mana”

Talba yayi murmushi domin ya lura da yadda ita ma Aminatun ta kankame Hajiya da alama ta shaku da ita.

“Ga abinci ma kawo miki, kuma abun da kika fi so na dafa miki shimkafa da wake”

‘Her favorite food’

Talba ya fada a ransa.

“Ga kuma lemun kwakwa na san shi ma kina son shi sosai”

Hajiya Laraba ta fada tana dire katon kofin dake dauke da lemun kwakwa.

‘Her Favorite drink’

Ya sake fada a ransa yana kara haddacewa.

“Na gode Mama, Ina Yusura da Khadija na yi marmarinsu”

“Duk za su zo, yau ni zan kwana a nan ne gobe zasu zo su wuni dake”

Ta yi murmushi, Talba ma murmushin yake domin yana son farincikin Aminatu.

“To ni zan tafi”

Hajiya Laraba tana dago tana kallon mijinta daya mike tsaye.

“To Allah ya kiyaye, sai da safe”

Ya mikawa Talba hannu suka gaisa sannan ya fice. Da kanta ta dauki plate ta subawa Aminatu shimkafa da wanken daya ji vegetables ga egg a gafe sai tiriri yake.

“Ya isa”

Talba ya fada domin a dan zaman nan na yau da tai asibitin ya lura matarsa ba mai ci bace sosai, gashi daman bata dade da gama cin wani abincin ba. Hajiya ta mika mata, Aminatu ta saka hannu biyu ta karba tana tambayar kaka.

“Kaka tana nan lafiya, ban fada mata komai ba, amman nace mata ni da yan'uwa da suke nan da kuma kawaye zamu kai ki gidanki ba sai ta yi wahalar zuwa ba, nace mata idan ta tashi sai ya shirya zan aiko a dauke ta taje ta ga daki”

“Kuma ta yarda?”

Talba ya tambaya.

“Eh ta yarda, amman ta yi da fada daker na shawo kanta, yanzu haka abun da take dauka an kai a jiya”

Aminatu ta fara cin abinci a hankali, Talba na ganin haka ya zuba mata ruwa a cup din da Momy ta aiko Mairo ta kawo musu dazun ya mika mata. Sai ta karba ya sha kadan ta rike tana ta cin abinci.

Hajiya ta juya ta kalli Talba.

“Momynka ta ji abun da ya faru?”

“Eh ta sani, dazun ma ta zo ta dubata tare da Leila”

“Leila ita ce wanda zaka aura ko?”

A nan kam Aminatu dagowa tai tana kallonsa, shi ma kallonta yai kamin ya amsawa Hajiya.

“Eh.. Ita ce”

Sai Aminatu ta sauke kanta kasa tana tauna abincin a hankali ta kasa hadewa.

“Ta ce idan ta ji sauki za mu koma gida a tare, wata kila ma gobe a sallame mu”

“Gidan ka ko can family house dinku?”

“Family House”

“To miyasa ba zaka tare da matarka ba? Kasan dai ba dadin zaman gidan zata ji ba, wata kila ma zata yi ta kallon kamar mun aura maka ita ne saboda mu musguna mata ko yarda daman can ba jituwa tsakaninmu, kuma ga yarta a gidan taya Aminatu zata sake? Ka na ganin dai yarinyar nan marainiya ce kuma amana aka baka”

“Bana son na musa mata ne kawai, shiyasa zan zauna da ita a can kamin mu tare din, ke ma ai kin ina da mata ba zai yiyu nai ta zama a gidan ba, kuma for now na san Aminatu tana jin tsoro so zamanmu a can zai taimaka ta manta wani abu kamin mj koma zama mu kadai”

Hajiya ta yi shiru tana nazari, kamin ta gamsu.

“Toh Allah ya tabbatar da alheri”

“Amin”

Ya amsa sannan ya duba agogon hannunsa.

“Goma ta kusa, bari na tafi gida tun zaki kwana a nan ko?”

“Eah Allah ya tsare”

“Amin”

Ya kalli Aminatu yana jin kamar ya sumbance ta sannan ya tafi amman babu hali saboda Hajiya Laraba na gurin.

“Zan tafi akwai abun da kike bukata na zo miki da shi da safe?”

Taki daga ido ta kalleshi kuma ta ki amsawa for no reason, har sai da Hajiya Laraba ta maimaita abun da ya fada sannan ta ce.

“Aa”

Ya juya ya nufi kofa, sai da ya juyo ya kalleta sannan ya fice.

LEILA POV.

tana tsaye jikin windows din dakin Momy tana kallon Talba daya faka motarsa ya fita ya nufi part dinsa, sannan ta saki curtains din ta juyo ta kalli Momy zuciyarta na mugun zafi.

“Momy anya zan iya jure wannan abun? Kalli fa sai yanzu ya dawo gida yana can gurin wacan yar iskar”

“Haka nan zaki daure har ki saba, idan ba haka ba muna nuna mata tsantsar kiyayya, wani abu na faruwa za a fara tuhumarmu, amman idan kika daurewa zuciyarki abun da kike ji babu wanda zai zargi komai, duk kuma kika kuskura kika ce zaki nunawa yarinyar kiyayya karara matsala za ku samu da Talba, wata kila ma yace ba zata zauna a gidan ba ya dauketa su tare can dabam, kin ga tun nan mun fara samun matsala, ni kuwa ba bari zan yi ba ko daki daya ba zan bari su kasance ba balle kuma gida daya”

“Amman Momy kina ganin zai yarda ta zauna bangarenmu shi kuma yana can?”

“Ai ba a yi kirikiri, na yan siyasa za ayi siye zuciyarsa za'ayi kamin tafiya tai nisa aure ya bare, be da zancen wata mace sai ke”

Leila ta sauke ajiyar zuciya.

“Amman Momy za a dade kamin abun yayi? Baki ji yadda nake ji ba”

“Bana jin zai dade, ke dai bari Hajiya Saratu ta dawo sai mu ji komai, je dakinki ki kwanta da safe kuma ki gaishe shi ko ki tura masa sakon gaisuwa, kuma ki fada masa kina gaishe da yarinyar”

“Toh”

Ta mike tsaye ta fice daga dakin tana share hawayenta. Sai da Momy ta tabbatar sha daya ta yi sannan ta sauko kasa ta fita daga falon ta nufi harabar gidan. Gurin Mustapha mai gadinta ta nufa yana ganinta ya taso da sauri sai ya koma gefe ya bi bayanta suka tsaya.

“Ka bincika?”

“Eh Wallahi, su ma garin sun ce be zo ba, rabon Sani da garin nan yanzu wai wata uku”

“Subhanallahi, to Allah yasa lafiya yake dai ace a rasa inda mutum ya shiga”

“Amin Yanzu haka dana fada musu hankalinsu duk ya tashi”

“Magidancin mutum ace ya bata lokaci daya, ko da yake bana jin bata yai tun da har ya iya sakawa gidan padlock wata kila guduwa yai, dalilinsa na guduwa ne ba mu sani ba”

“Allah dai yasa yana cikin aminci”

“Amin”

Ta amsa sannan ta juyo ya dawo cikin falon da tunani kala kala, sai kusan sha biyu ta shirya cikin kayan bachi ta sauko ta nufi bangaren mijinta.

MADINA POV.

ta saka hannunta ta dafa goshinta ya sauke ajiyar zuciya sannan ya juyo ta dawo karshen dakin tana sanye da tufafinta na bachi.

“Yanzu Abokiyar fadana daya ce, Leila ba Aminatu ba”

Ta fada tana cikawa bakinta iska ta busar, tun lokacin da Leila ta fada mata cewar Mama Saratu tace za a tashi tsaye ta kasa samu kwanciyar hankali, tana ji a ranta idan har ta bar Leila ta aikata abun da take kudi ba Aminatu kadai ba har ita kanta ta rasa Talba kenan har abada. Zauna tai bakin gadonta ta dauki wayarta ta kira Leila bugu daya Leila ta dauka.

“Yanzu fa nake son kiranki”

“Gashi ni na kira ai, ya kike?”

“Lafiya kalau, labari zan baki”

Madina ta nade kafafuwan kan gadon tana gyara zama.

“Wane irin labari ne?”

“An ga Aminatu oh Mai sunan Momy ya kama na ce, ko ma nace kazamar yarinyar nan yar kauye”

“An ganta a ina?”

Leila ta bata labari, sai Madina ta tabe baki not surprised.

“Daman ai na san za a ganta”

“Kamar ya kin san za a ganta?”

Ta dan yi shiru tana nazarin abun da ta furta.

“Yeah saboda an baza hotunan a ko'ina, kuma gashi har da tukicin kudi Talba ya saka, kin ga ba zata yi wahalar gani ba, wata kila ma a cikin mutanen da suka dauketa wani zai iya blackmailing din wanda ya sace ta yaje ya kaita saboda kudin, hakan zai saka mai wanda ya dauke ta jin tsoro ya jefar da ita”

“Ai ba jefar da ita sukai aka tsinceta ba, sms aka turawa Kabir yaje ya dauke ta”

“Ya kai aka samu number Kabir din?”

“Oho muma shi ne abun da yake ta bamu mamaki, Momy tace na kusa da mu yake playing wannan game din”

“Gaskiya kam, yanzu tana can asibitin kenan?”

“Eh amman Kabir yace za a sallame ta gobe, kuma Momy tace a dawo da ita a nan gidan ta zauna”

“Kuma kin yarda?”

“To miye a ciki ta zo ta zauna din, indai Talba ne ai kwana biyu zasu bare na san halin mutumena ai”

Madina ta sauka daga kan gadon.

“Allah yasa dai ba kina nan kam bakarki ba, ta yin asiri”

“Kai hana ina! Ai tun da kika bani shawarar nan na watsar da maganar, kawai dai ina son na nuna masa ban damu bane ni zan ma iya bar mata shi gaba daya”

Sai a lokacin Madina ta samu salama har ta sauke ajiyar zuciya.

“Gaskiya kam, kara dai karki yi ki saka musu ido kawai”

“Haka zan yi ai, zan kwanta kawata sai da safe”

“Sai da safe mu kwana lafiya”

Leila ta sauke wayar tana murmushi, for the first time ta fara yi ma Madina karya tana boye mata sirrinta kamar yadda Momy ta koya mata. Aje wayar tai ta fice daga dakin tana saukowa kasa ta nufi kitchen tana son hadawa kanta tea, domin tun ganin da tai ma Aminatu da Talba a dazun bata sake saka komai a cikinta ba. Tana shiga ta samu Kabir a tsaye yana wanke apple a tap. Gurin da aka jera cup ta nufa ta bude ta dauko cup din.

“Ina fatar ba wani abu kuke shiryawa yarinyar nan ba, ba zan sake bari ki aikata wani kisan kai ba bayan wanda kika yi ma Baaba”

Juyowa tai ta kalleshi.

“Da Momy ya kamata kai wannan maganar ba da ni ba”

“Saboda Momy ce ta kashe Baaba?”

Ta yi shiru tana kallonsa maganarsa na mugun sukarta.

“I warn you, karki cutar da yarinyar nan she's innocent bata ita tace Talba ya aureta ba, idan zaki yi fadanki ki yi da Talba not her”

Yana kaiwa nan ya dauki plate din dake dauke da apple hudu ya fice daga kitchen din ya barta tsaye tana kallonsa da mugun bacin rai.

BATURIYA POV.

Fahat ya wara ido yana kallonta da mugun mamaki, domin ya dade yana jiran zuwan wannan ranar, a duk lokacin da yai mata magana sai ta kawo wani uzuri yau kuma da kanta take gabatar masa da bukatar.

“Da gaske ko dai mafarki nake yi?”

Ta yi murmushi.

“Da gaske mana, a gida sun min magana sun ce na fito da miji ni kuma na fada musu babu wanda nake so kai sai suka ce na fada maka ka turo”

“Alhamdulillah, na dade ina jiran zuwan wannan ranar, Wallahi gani nake kamar ma mafarki ne”

“Gaske, daman na ce yau zan maka albishir da abun da kake so”

“Aiko goronki mai girma ne a yau, na jidadi sosai kuma na miki alkawari kyauta ta musamman”

Ta yi murmushi, wani irin kallonta yake cike da shauki yana jin sonta na karuwa a zuciyarsa.

“I can't wait to talk my mom”

“Ba ka ce akwai wanda take son ka aura ba?”

“Yes amman ai dole zata so wanda danta yake so ko?”

“Haka ne, Allah yasa tai maraba da ni”

“Zata ma yi i promise you ina zuwa gidan yau zan bata ku gaisa”

“Aiko da na jidadi sosai”

Rumgume hannayensa yai yana kallonta cike da shauki, domin har cikin zuciyarsa yake jin son Baturiya, domin tana da siffar da yake so a jikin mace gashi kuma naturally Allah ya saka masa sonta sosai. Sun dade suna hira sannan ta bude motar ta fito rike da ledar da yai mata siyayya ta shiga cikin gidan ita ma cike da shauki. A falo ta baje hajar turarukan saya siyo mata tana murmushi.

“Lallai mutumen nan na ji dake, duk ya zo sai yayi miki siyayya mai yawa”

Cewar Aisha tana sauko daga kan cushion din da take zaune ta duba kayan.

“Dan masu kudi ne sosai, idan na aure shi ba ke ba ko kawayenki sun huta balle kuma ke, fatana dai Umma ta bani hadin kai”

“Ba ruwan Umma ita daman abun da take so kenan ai, Ya ma da kansa yai magana ya ce ki fito da mijin aure fa”

“Na sani, ai yanzu haka na masa maganar, yace min zai je ya samu iyeyensa yai maganar da su, duk yadda sukai zai kirani ya fada min, kuma yace kamin su zo zai so ya gaishe da Umma kuma su gaisa da Yaya”

“To miye abun tsoron?”

“Aisha be san na taba aure ba, kuma ban taba fada masa ba, a zatonsa ni budurwa ce, shi ne nake son na lalaba Umma ta goya min baya ta yi magana da Yaya”

Aisha ta rufe baki.

“Amman kin yi kuskure gaskiya, ai gwara dai ki fada masa gaskiyar idan ma ya ji ba zai iya aurenki a haka ba ai kin ga dai kin fada masa gaskiyar, domin idan ya sani zai ji haushi”

“Abu ne mai wahala ya sani, domin su masu kudin nan ba wani bincike suke akan aure ba, ko ba su ba ma yanzu an daina wani dogon bincike akan aure ai”

“Amman idan ya aureki zai gane ai, sannan ya zaki yi da Sultan idan zai zo ganinki musamman idan yai wayon ya san yaje gurin mahaifiyarsa?”

“Sultan saba masa zan yi da zama a gurin mahaifinsa shiyasa ai ban damu naje na duba shi ko sau daya ba, duk da yana rai na amman bana son ya saba da ni ne. Wannan kuma kamin na yi auren zan tafi gurin yar gidan mai fata ta gyara ni zan siye set din back to virgin shikenan an wuce gurin”

“Tab amman dai gaskiya kin yi sakaci, da dai kin fada masa gaskiya idan ya ji zai aureki a haka sai ya aureki, idan kuma ya ji ba zai iya ba kin ga baki yaudare shi ba”

“Ni dai yanzu abun da nake so dake ki taimaka min, ki lallaba min Umma ta amince kuma ni ma zan yi magana da ita kuma zan saka Anty ma ta yi”

“To Allah yasa ta aminta”

“Aamin yawwa yar kanwata haka nake son ji”

Ta fada tana dauka kusan turare uku ta mika mata kyauta.

FAHAT POV.

yana shigowa falon ya zarce dinning inda Mahaifiyarsa take zaune tana cin abinci, kallo daya tai ma fuskarsa ta fahimci yana cikin farinciki.

“Mommy yau ina da labari mai dadi da zan baki”

“Ai naga haka a fuskarka ai, minene fada min”

“Sai kin ba ni goro babba”

Ta yi murmushi.

“To fada na ji idan ya kai na baka goron ai zan baka”

“Yarinyar da nake fada miki, yau dai ita da kanta tace na turo iyeyena”

Mommy ta tsayar da cin abincin da take ta kalleshi.

“Shi ne wani abun farinciki?”

Ya dan bata fuska.

“Haba mana Mom kin san fa ina son yarinyar nan”

“Toh Allah yasa alheri, zan sanar da daddynka idan ya dawo, but kamin nan ya kamata ka same ta kai magana da ita”

“Magana kuma?”

Ta tambaya with confused.

“Yes ka yi magana da ita ko kuma ka saka a bincika mana ita kamin a tura manya, domin na yi nawa bincike ina ganin kamar akwai abun da yarinyar nan take boye maka”

Yayi shiru yana nazari.

“Mommy akwai wata matsala ne a tare da ita?”

“Aa ba zaka ji a bakina ba, idan na fada ai laifina zaka gani, wata kila ma ka karyata, amman idan ka bincika da kanka ko kuma kai magana da ita zaka fi gamsuwa”

“Mommy dan Allah kin fada min”

“Babu abun da zan fada maka, lokacin da zaka ganta ka ce kana so ni na fada maka inda take ne? To haka zaka yi naka bincike ka gano komai da kanka”

Tana fadar hakan ta mike tsaye ta zari tissue tana goge bakinta. Jan kujera yai ya zauna da tunani, sannan ya saka hannunsa aljihu ya dauko wayarsa sai yanzu yake ganin ya dace ua bincika friend dinsa daya saka yai masa bincike akan Baturiya, wata kila by now ya samu wani labari da zai fada masa, domin kwana biyu da suka wuce ya kira shi ya tambaye yace har yanzu be binciken yadda ya kamata ba.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

FARUK POV.

Tafiyar Kwana uku sukai a hanya sannan suka iso Ilela. A sokoto ya kwana washe gari motar data tashi faga sokoto karfe 7am zuwa Zamfara ya shiga, kamin su isa mahaifarsa har ya zaku yana ta marmarin ganin Mama da kanensa da kuma dansa, ga kuma tafiyar da yai ya samu rabo mai yawa wadanda yake jin cewar ya wadatar da shi ya fara sana'a mai karfi da zai rike kansa ko da be samu aiki ba. Ana shiga garin Gusau sai ya ji yanayi da kamshin garin daya baro da inda yake a yanzu ya banbanta. Tasha suka sauke duk fasinjojinsu. Faruk ya fito motar kamar wani buzo saboda sumar daya tara, domin a dajin da suke ko magani babu balle shagon aski wani sai yayi wata daya ma be yi wanka ba, saboda tsoron kar ya tube kaya yaje wanka a sace masa sinari domin sata ake a gurin sosai kana yin wasa da zinarinka za a sace maka shi. Tsaye yai yana kallon cikin tashar kamar wani bako, bangerensa an hagu na rataye da jaka irin ta goyo wanda matafiya suke saka tufafi ko littafai a ciki. Gurin wani mai shago ya nufa ya zaro naira goma dake aljihunsa ya siye pure water ya sha sannan ya nufi kofar fita gate din, kamin ya karasa titi ya tare wani mai achaba ya hau yana fada masa unguwar da zai kai shi.
Yana shigowa cikin unguwar mutanen da suka sanshi suka fara daga masa hannu wasu kuma na kai masa gaisuwa. Sai ya amsa yana daga musu hannu har ya isa kofar gidan ya sallami mai achaba ya shiga da sallama. Kanwarsa na jin muryarsa ta fito waje da gudu ta rumgume shi.

“Yaya Faruk oyoyoyoyoyo”

Dariya ya saka sannan ya sake ta nufi dakin data fito wato dakin mahaifiyarsa, domin yana cike da zumudin ganinta yana shiga dakin sai yai tsaye bakin kofa ganinta kwance ta rame sosai kamar ba ita, gaba daya kassanta sun fito idonta yayi wani zurfi tsufan wahala ya taso mata.

“Maa Shaa Allah sannu da zuwa Umaru”

Ya karasa kusa da ita jiki a sanyeye domin be jidadin ganin mahaifiyarsa a haka ba, ya san ya barta a yunwa da rashin lafiya irin ta yau da gobe, amman be dauka abun yayi tsanani haka na.

“Mama baki da lafiya ne?”

Ta yi murmushi.

“Bari ka hutu labari ai zai zo daga baya ko? Kai da ka kwaso hanya, kasa wa kasa bama gari wa gari ba!”

Ya zauna kusa da ita cikin rashin walwala.

“Gashi babu waya, inda nake ba a waya Wallahi sai an fito gari kuma fitowar ne aiki, kullum ina son na kira ko na yi muku aike amman ba dama”

“Babu komai ai yanzu gashi ka dawo, ya hanya”

“Alhamdulillah Mama, tun yaushe ne baki da lafiya”

“Tun tafiyar, daman kasan lafiyar ba wai ta wadace ni ba ne, sannu sannu abun ya fara har ya kai ni kwance”

“Hawan jinin ne ko Mama?”

“Shine kam domin ba ni da wani ciwo sai shi”

“Tunani kika saka a ranki Mama”

“Tunani ai ya zama dole abu ga talaka, kullum kana tunanin abun da zaka ci, abu ga talaka, kuma tafiyar nan da kai babu kira babu sako, dole ai hankalina ya tashi”

“Zaki iya shiryawa mu tafi asibiti ko sai Rukaiya ta rikaki”

“Haba dai Ka bari ka natsu mana, ka ci abinci ka yi wanka kalli gashin kanka ma, kuma ba ni kadai ce mai ciwon ba ai har da danka”

“Miya samu Sultan”

“Kyanda, tun da yai shi be sake lafiya ba, kullum ciwo yake”

“Ina yake?”

“Gashi can gindin icce”

Mama ta fada tana masa zunde da baki tana nuna masa inda Sultan yake. Juyawa yai ya kalli Sultan dake tsakar gidan kwance gindin ice yana sharar bachi, mikewa yai tsaye ya nufi inda yake tun kamin ya karasa kusa da shi ya lura da yadda ya rame sosai yai baki, domin har yanzu akwai dambunan kyandar Jikinsa. Risinaws yai yana kallon dansa cikin rashin jindadi.

“An kai shi asibiti?”

Ya tambaya yana kallon Rukaiya dake bayansa tsaye.

“Aa Yaya ka san yadda muke fama, ta abinci muke yi bata magani ba, Mama da ace da kudi ai ba nan zaka tarar da ita ba sai asibiti”

Hannu ya kai ya taba sai ya ji jikinsa da dan zafi ba sosai ba. Sake dawowa yai dakin ya aje jakarsa gefen daya sannan ya ciro 2k ya mikawa Rukaiya.

“Je ki siyo wani abun ku ci, zan je na yi wanka na shirya sai mu tafi asibitin”

“Toh Yaya”

“Da dai ka hakura sai gobe idan ka huta sai mu tafi”

Mama ta fada murya kasa kasa, baya son musa mata ne, hakan yasa ya amsa mata da toh sannan ya fita daga dakin zuwa asalin dakin da yake bachi. Tufafin

jikinsa ya tube ya saka short ya fito ya cika farin bokitin fenti ya shiga bandaki yai wanka ya fito fes da shi, ya saka wasu tufafin sannan ya fita waje. Tun da ya fito yake gaisawa da mutane suna masa sannu da zuwa har ya isa titi, shagon wani mai askin zamani ya shiga shi ma sai da suka gaisa sannan ya zauna mai askin ya kunna injin ya soma gyara masa kansa. Duk tulin gashin dake kansa sai da aka zubar da shi aka gyara masa fuska, sannan ya sallame shi ya dawo gidan.

Tabarma ya dauko ya shimfida a waje ya koma dakin ya dauko Mama ya dawo ta ita a wajen ya zaunar da ita, sannan shi ma ya zauna ya tisata a gaba yana ta kallo.

“Na yi kewarki sosai Mama kullum sai na yi mafarkinki”

Mama ra yu murmushi.

“Ai shiyasa na ce ko sa ka kira kar a fada maka bani da lafiya ko danka, saboda za a tada maka hankali ne kawai”

“Amman Mama da na kira din aka fada min ai sai na aiko da na magani”

“Mama bata son tashin hankalinka ne shiyasa”

Cewar Rukaiya dake aikin jajagen kayan miyar da zata yi miya. Faruk yayi murmushi. Yana kallon dansa daya fara motsawa kana ya bude ido. Tsayawa yai kallon Faruk da mamaki yana ganin kamar mafarki ne.

“Daddy”

Ya kirashi sannan ya tashi zaune yana kallonsa.

“Na'am”

Faruk ya amsa ya mika hannu ya dauko shi ya zaunar saman jikinsa har lokacin jikinsa da dan zafi.

“Sultan ya jikin”

Ya taba jikinsa.

“Akwai zafi kuma cikina na ciwo”

“Sannu zaka sha bobo ko madara”

“Aa”

Ya fada yana jin cewar baya son komai domin bakinsa babu dadi. Faruk ya taba jikin nasa yana kara tabbatarda dansa ba shi da lafiya, saboda ya san dansa da kwadayi ko da ya koshi da abu idan akai masa maganar bobo ko madara ko nama jiki na rawa yake cewa eh.

“Dady karka sake tafiya ka bar ni kaga ina ciwo idan baka nan”

“Ba zan sake ba, babu inda zan sake zuwa”

“Dady tare da Momy kuka dawo”

Faruk ya kalli Mama, Mama ta kalleshi.

“Haka yake kullum maganarsa Dady Momy”

“Rafi'a ta zo dubashi?”

Mama ta girgiza kai.

“Wallahi har yau bata zo ba, kuma kullum sai yayi maganarta”

Faruk ya shafa dansa cike da tausayin rashin samun uwa ta gari. A saninsa da ace yayi dacen mahaifiya ba za a dauki sati ba zata zo ta duba shi amman ace har yanzu bata waiwayi inda danta yake ba.

“Shiyasa ma da bashi da lafiyar nan ban fada mata ba”

Mama ta fada. Sai Rukaiya ta kyabe baki.

“Ita fa gani take ta rabu da talauci ta huta, bata da wata damuwa”

“Allah ya sauwake”

Faruk ya fada cike da tausayin dansa, sai duk suka amsa da Ameen har shi Sultan din.

TALBA POV.

A hankali Leila ta sauko downstairs din tana kallon Talba dake zaune dinning area rike da wayarsa yana chat. Sai dai har ta sauko ta karaso inda yake taja kujera ta zauna be dago ya kalleta ba.

“Good morning Babe...”

At first saurare ya tsaya yi da shi take? Sannan ya dago ya kalleta with surprise, murmushi ya gani s fuskarta tana kallonsa.

“Ya mai jiki?”

“Ta ji sauki”

Ya amsa a takaice sannan ya mike tsaye ya nufi kitchen.

“Mairo ba a gama ba”

“An gama ranka ya dade ina hada kayan guri daya ne”

“Zan jiraki a mota”

Ya juyo ya nufi kofar falon.

“A gaisheta da jiki zan shigo anjima da dare”

Be kulata ba balle har ya amsa abun da take fada ya sa kai ya fice. Cikin motarsa ya zauna ya kunna motar yana jiran fitowar Mairo, sai ya hango Leila ta fito rike da kwandon abincin ta nufo motarsa. Da kanta ta bude back seat ta saka masa sannan ta rufe.

“Safe drive”

Kallonta yai sannan yai reverse ya nufi gate din gidan, har ya isa asibitin tunanin abun da Leila tai masa a yau yake, da zuciya daya tai ko kuwa dai tana da wata manufa? Ganin Aminatu ne yasa ta zubar da duk wani hali nata da girmankan da take ji da shi ko kuma me? Yana yin parking kiran Ali ya shigo wayarsa, picking yai ya kara a kunne ba tare daya ce komai ba.

“I just call to ask...”

“Uhmm...”

“Ya jikinki Aminatu?”

“Ta ji sauki, za a sallame ta yau”

“Allah kara sauki, ina son magana da kai serious talk”

“Okay zan kira ka idan na fito”

“Okay”

Ya sauke wayar ya saka aljihun jean dinsa sannan ya bude motar ya fito ya bude back seat din ya dauki abincin ya nufi ward dinsu Aminatu.

AMINATU POV.

“Mama ina kwana”

Hajiya Laraba ta yi murmushi tana kallon Aminatu.

“Lafiya Kalau Auta ya jikin?”

“Na ji sauki”

“Me kike son ki ci?”

“Ba komai”

Ta fada tana yin kasa da kai. Hajiya Laraba ta daka mata tsawa har sai da ta zabura.

“Ke... Sake jikinki idan kina son wani abu ki rika fada, birni ba irin kauye ba ne, musamman ma inda zaki zauna yanzu, ban san irin tarbar da zasu miki ba, amman ba sonki suke ba, duk abun da akai miki ki bude baki ki fadawa mijinki,

idan kuma ya kasa komai ki fada min ko kuma idan shi din ma ya taba ki ki fada min, idan akai miki abun da baki gamsu ba ko baki so ki rika magana, idan ba haka ba rainaki zasu yi, kuma ban da kazanta kin ga irin turbar da muka doraki to ki bita ta zame miki jiki, karki kuskura ki bari su raina ki wannan sukukun da kike ba zai amfana miki komai ba a can, kina ganin da gogangin yan duniya ne kuma wayayyi, amman saboda son da mijinki yake miki ya saka dole su zauna dake, kuma karki sake masa yai ta zama dake a gidan, kara ku tare a naku gidan kinji ko?"

"Toh Mama"

Ta amsa sannan ta dago ita da Hajiya Laraba suka kalli kofa, Talba ne ya shigo rike da abinci fuskarsa da murmushi sai da ya gaisa da Hajiya Laraba sannan ya karaso ya aje abinci sannan ya kalli Aminatu.

"Ina kwana..."

Ita da shi suka hada baki gurin mikawa juna gaisuwa, sai Hajiya Laraba tai murmushi.

"Ai ita ya kamata ta gaishe ka"

Shi ma murmushin yai ya kalli Aminatu.

"Ya jikin?"

"Na ji sauki"

"Ashe manya na tashi da wuri, 6:30 fa"

Cewar Hajiya Laraba, sai ya kalli agogon hannunsa.

"Tun 4am na tashi Mairo na ce ta shirya mata breakfast"

"Baka son matar taka ta ji yunwa kenan"

Yayi murmushi ya sauke kai kasa, sai ta mike tsaye.

"Bari na kira oga mu gaisa"

Ta dauki wayarta sannan ta fice, tana fita Talba ya janye daga jinginen da yake jikim gadon ya koma kusa da Aminatu ya zauna.

"Pretty na"

Ta ki dago kai ta kalleshi, sai ya kai bakinsa gefen bakinta ya sumbance ta.

"Good Morning Babe i miss you so much"

"Minene i miss you din?"

Ta tambaya tana kallonsa domin ta san good morning. Murmushi yai ya rumgumeta yana kara kissing dinta

“Ina nufin na yi kewarki”

“Sake ni kar ta dawo taga ka rika ni”

Ta fada tana kokarin kwace kanta daga rikon da yai mata.

“Okay ki sumbance ni sai na sake ki”

Ta zaro ido da mugun mamaki da tsoro domin bata tsammaci jin haka daga bakinsa ba.

“Kai....”

“Yes”

“Dan Allah sake ni”

“Wallahi ba zan sake ki ba, kin sumbance ni kin ji kuma na rantse, sai dai ta tararda mu a haka”

“Dan Allah dai...”

Ta marairaice masa tana shirin yin kuka har ta turo baki gaba. Hannu ya kai ya taba bakinta cike da burgewa.

“Na fa rantse ba zan saki ba, sai kin sumbance ni”

Ya kalli kofar gabanta sai faduwa yake, sannan ta kai hannunta ta daba bakinta ta shafa masa a gefen fuska.

“Nop ba haka ba, bakinki zaki saka ki sumbance ni”

Ya fada har da lumshe ido yana jiran ta sumbance shi, hawaye ne ya sauko mata shi kuma sai kara janta yake jikinsa. a dole ta mike beautiful lips dinta ta sumbance shi ta dauke bakinta da sauri.

“To na yi”

Ta fada tana kallon kofar kirjinta sai bugawa yake gani take kamar Hajiya zata shigo ta tararda su a haka. Murmushi yai ya bude idon ya sumbanci saman hancinta sannan ya saketa ya mike tsaye ya koma inda yake tsaye ya rumgume hannayensa yana sotsar lips dinsa kamar ya samu sweet sai kallonta yake, suna hada ido ya kanne mata ido daya, sai tai saurin kawar da fuskarta tana turo baki ta sa hannu ta share hawayenta.

Hajiya Laraba na dawowa dakin ta zuba ma Aminatu abinci, soyayyar doya da kwai sai tea da aka hada yana ta kamshi, da farfesun naman rago. Bayan ta zuba mata ta zuba ma kanta.

“Talba a zuba maka?”

Kamar zai ce eh sai kuma ya kalli abincin Aminatu.

“Aa zan ci anjima”

“Okay”

Kadan kadan take cin abinci Hajiya kam tuni ta gama ta sha ruwa mai sanyi. Da ido yake ta gadinta har ta gama cin abincin Hajiya ta mika mata ruwa ta karba ta sha sannan ta aje.

“Kin koshi?”

Talba ya tambaya, sai ta girgiza masa kai alamar aa tana turo baki, saboda ganin Hajiya kanta na wani gafen bata ganinta, wai so take ta rama kissing din da ya saka ta tai bata so ba.

“Hajiya a kara mata”

Hajiya ta juyo ta kalleta.

“A kara miki?”

“Na ce na koshi”

Ta furta tana kallon Talba, sai ya dan fiddo ido, can kuma yai murmushi, ita ma murmushin tai ta sauke kanta kasa tana kallon siraran yatsunta.

“Jiya da dare likita ya shigo bayan tafiyarka, amman ba wacan likitan ba ne, ya dai ce jikinta ba shi da matsalar komai wai idan likitan safe ya shigo zai sallame ta”

“Eh idan Kabir ya shigo anjima zai sallame ta”

“Can din zata zauna kenan?”

“Eh amman ba wai zama ta dade ba, kawai dai zata zauna ne kamin komai ya koma daidai”

Hajiya ta sauke numfashi.

“Ke dai Auta na fada miki ko?”

“Tau”

Hajiya ta mike tsaye.

“Ni zan tafi na yi wanka na shirya, idan likitan ya sallame ta sai ka fada min da wuri saboda yarana suna son zuwa a nan, idan kuma ta kuma can kuma duk daya zasu je su dubata”

“Okay In shaa Allah”

Ta hada kayan data kawo abincin da su jiya ta dauka.

“Bari na sauke ki”

“Aa ita kadai za a bari a nan? Kasan dai abun da ya faru ba mu gama fita daga zullumi ba, zau hau Napep”

“Okay Allah ya tsare”

“Aamin”

Ta nufi kofa, Aminatu ta bita da ido ido narai narai kamar zata yi kuka, ji take kamar ta bita. Sai da ta fice sannan Talba ya tashi ya koma can kan carpet din da Aminatu take zaune ya zauna ya dauki plate din data ci abinci ya zuba farfesun ya saka spoon ya fara ci.

“Babe na”

“Ni ka daina ce min Babe”

“Saboda me?”

“Yarinya ce ni da zaka ce min Babe”

Dariya ya saka irin wanda ya dade be yi ba ita kanta sai da ta kalleshi domin be taba ganin yayi irin wannan dariyar ba. Aje plate din yai ya kalleta yana tauna naman.

“I love you girl”

Ita dai sai kallonsa take da mamaki.

“Ba sai karami ko jariri ake cewa Babe ba, za ki iya kirana da Babe idan kina so nima zan iya kiranki”

“Kuma ka amsa?”

Ya kai hannu ya fika fuskarta.

“Why not? Dadi ma zan ji”

Ta kawarda fuskarta daga rikon da yai mata ta mike tsaye sai ya rikota ua janyota da karfi.

“I can't believe wai ni mai mata ne a yanzu, ina da aure, matata ce wannan, ban san haka ake ji ba da na yi aure since”

Ya kama hijab dinta zai cire sai ta fara kokuwa da tana son hana shi.

“Ki sake jikin ki idan kina tare da ni, mijinki ne ni, aikina na kula da lafiyarki da komai na ki i feel proud Wallahi”

Ya cire mata hijab din da karfi sannan ya rumgume ta, sai ta saka hannayenta ta rufe fuskarta. Murmushi yai ya kama hannayen nata ya sumbanta sannan ya sake ta ta mike tsaye da sauri ta dauki Hijab din ta saka ta haye saman gadon ta zauna. Kamar hadin baki tana zaunawa Kabir ya shigo dakin rike da wasu files.

“Good morning”

Talba ya mike tsaye ba tare daya amsa ba.

“Ya mai jiki?”

“Ta ji sauki, i think yau zaka sallame ta ai ko?”

“Definitely Yes”

Ya fada yana mika masa takardar sallamar.

“And hoton da akai mata ya nuna bata da wata matsala”

Talba ya dafa shi.

“Thank You Kabir”

“Ur welcome, amman a can zaka zauna da ita?”

“Yes, bana son na musa ma Momy ne”

“Yeah but zan iya magana da ita, no Daddy ma zai iya tsaya maka ai, kana nuna masa baka so zai hana”

“Zata ga kamar ban yi mata biyayya ba, kuma zata jidadi ba, na yi aure a boye yanzu kuma tana bani umarni ina kin yi ba zata jidadi ba”

“Amman baka ganin zai zame mata takura ita?”

Talba ya juya ya kalleta sannan ya kalli Kabir.

“For now ban sani ba, amman idan na ga alamar zata takura ba zan barta ta cigaba da zama haka ba”

Kabir ya gyada masa kai sannan ya karasa kusa da Aminatu.

“Madam, an sallame ki zaki dawo gidanmu da zama yanzu, ina fatar dai kina so ko?”

Ta kalli Talba daya hade mata fuska kamar ba shi ba, ba dan komai ba sai dan baya son ta bawa Kabir din fuska. Da sauri ta sauke kanta kasa. Sai yai murmushi ya juya ya fice.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar

dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Littafin nan na kudi ne biya ki karanta cikin aminci. Pay 500 to 2451879008 Hadiza Abubakar Zenith bank, then send the evidence via 08036126660

Ba su bar asibitin ba sai da ya kira Momy ya sanar mata ta aiko musu da Zulai saboda ta kwashe kayan da suka yi amfani da su, Zulai ce ta kwashe komai ta saka a motar Talba, bayan ta fita ya kalli Aminatu.

“Ta so muje”

Ta kalleshi kamar zata yi kuka.

“Tsoro nake ji”

“Nooo babu abun da zai same ki gidanmu ne fa, kuma nima ina cikin gidan, ki kwantar da hankalinki kinji”

“Toh”

Ta amsa hawaye na sauko mata sai ya saka hannunsa ya shafe mata sannan ya rika hannun nata suka fito tare, yana rike da hannunta har gurin motarsa, front seat ya bude mata ta shiga ta zauna, ya rufe sannan yai ma Zulai alama data bude back seat din ta zauna. Sai ta mika masa envelop din hannunta.

“Gashi wani mutum yace na baka wai ka bawa Leila”

Tsayawa kallon Envelop din Talba yai kamin ya juya yana kallon harabar.

“Waye ya baki?”

“Wallahi ban san shi ba, yana dai sanye da mask da bakin gilashi kuka kansa da hula”

Ya sake kallon Envelop din sannan ya kai hannu ya karba.

“Me yace miki?”

“Sallama yai min na amsa ya mika min wannan yace na bawa mai motar nan ya bawa Leila”

“Ta ina ya bi?”

“Mota ya shiga ya wuce”

Ya karba ba tare da yace mata komai ba ya zagaya bangarensa ya bude ya shiga, sannan ita ma ta shiga. Gaban motar ya aje envelop din wondering miye a

ciki, sai da yai ma motar key yai reverse ya fita daga gurin sannan ya kai hannunsa ya kama hannun Aminatu ya rike sai da tai kamar zata fisge hannu saboda ganin Zulai na bayan motar, sai ya girgiza mata kai a dole ta kyale. Zulai kam dadi ta ji ko ba komai ta san za a takurawa Leila ita da Mairo har tsegumin suka yi.
Da hannu daya yake driving hannunsa daya na rike da hannun Aminatu har suka isa gida ya faka dai dai kofar falon.

“Zulai fitar mana da kayan nan”

“To ranka ya dade”

Ta bude motar ta fita sannan ta fara fita da kayan sai da ta aje komai a wajen motar sannan ta rufe motar. A lokacin ne ya kalli Aminatu.

“Ki sake jikinki, ki dauka nan din ma kamar gidanku ne, and idan wani yai miki wani abu ki fada min kinji?”

Ta yi shiru, sai ya daga dayan hannunsa ya nuna mata part dinsa.

“Kin ga bangarena can, kina turawa zaki shiga ciki”

Ta kalli gurin kamin ta juya ta kalli Momy da Leila da Madina da suka fito daga kofar falon suna kallonta, sai kuma ya juyo ta Talba, ya sakar mata murmushi. Ya saki hannunta ya dauki envelop din ya fita, da gangan Aminatu taki fita daga motar ta zauna a ciki tana kallonsu har sai da ya zagayo ya bude mata.

“Fito”

Sannan ta nasa kafarta a waje ta fito ya rufe motar, kana yai mata iso da hannunsa.

“Bismillah...”

Ta fara takawa a hankali Talba yana kallon steps dinta har ta hau saman entrance din. Leila ta hade yawu tana kallon Aminatu zuciyarta na bugawa da karfi, Madina kam ji take kamar data bude baki hayaki ne zai fito saboda yadda wutar bakinciki da kishi dake cin zuciyarta, musamman yadda ta ga Aminatu ta canja ta yi kyau sosai kamar ba ita ba.

“Sannu da zuwa”

Leila ta fada tana kallon Talba, sai ya amsa mata da kai, Madina ta kalleta da mugun mamaki, Momy ma murmushi ne fuskarta.

“Sannu da zuwa sukarmu”

“Ina wuni”

Aminatu ta gaisheta sai ta amsa tana murmushi.

“Lafiya Kalau Takwarata, amman a nan sai su maida ke Ummi ko Meena ko?”

Ta yi kasa da kanta bata ce komai ba. Talba ya mikawa Leila envelop din hannunsa.

“Wani yace a baki”

Tana kallon Envelop din sai tai baya baya kamar wanda tai arba da wani abun tsoro. Madina ta kalleta ta gefen ido kamar zata yi murmushi sai kuma tai saurin batsarwa.

“Wani wa?”

Momy ta tambaya tana kai hannu ta karbi envelop din.

“Ban san shi ba, Zulai ya bawa yace a bani na bawa Leila, ban san miye a ciki ba”

“Oo. Okay... Shi..ga da ita ciki, dakin data taba zama na sakan Mairo ta gyara mata shi”

Har Madina ta kai hannu ta kama hannun Aminatu sai Talba ya rigata rika hannun matarsa ba tare da tunanin komai ba, a ganinsa Leila ma tai haka wa kawayenta maza da ba muharramanta ba balle shi da take matarsa. Yana rika hannun nata yaja ta zuwa ciki juyawa tai tana kallon yadda ya rika hannun nata tana jin kamar tai haniniya tai cikinsu ta fisge hannun Aminatu daga rikon da Talba yai mata. Leila kam bata kula ba sai hawaye take domin gaba daya hankalinta a tashe yake, Momy ce kawai ta tsare Madina da ido tana karanta karantun da ita kadai take gane shi.

“Unko shiga cikin da Envelop din”

Leila ta kasa karbar Envelop din da Momy ke mika mata ta juya da sauri ta shige falon. Ganin haka yasa Madina ta fara takawa zata bi bayan Leila ba tare data juyo ba, sai Momy ta kirata.

“Madina...”

Sai ta juyo sannan ta amsa.

“Na'am”

Momy ta matsa kusa da ita tana mata wani shegen kallo.

“Stop playing this game...”

Madina ta yi ma Momy kallon rashin fahimta.

“Yes kin san abun da nake nufi, ki daina wasa da hankalinmu kina tsorata min ya...”

“Ban fahimta ba Momy”

“Kin san me nake nufi, kina wasa da hankalin saboda zuciyarki na raya miki zaki iya lalata alakar Talba da Leila ki kulla taki, kina son Talba Madina na sani”

“You are not make any sense right now”

Madina ta fada with shock. Momy ta yi murmushi.

“Na harbo jirginki, kuma ina gargadinki domin zaki jefa kanka a matsala ne kawai, domin ba zan zuba ido a kai yata a gidan yari ba”

“Momy kina magana da ni kamar kin manta cewar ni kawar Leila ce kuma aniyarta”

“Ban manta ba, shiyasa nake gargadinki, kin hada baki da mai gadina kina kara jefa kanki a halaka, make sure kin dawo da gawar Baaba a inda take if not...”

“Ban san wani mai gadin kika magana akai ba, ban san gawar da kika magana ba, I'm not heartless like you and your daughter da zaku binne gawa na bita na tone ya kamata ki san da wannan, kuma ni ba zan taba blackmailing din Leila ba har abada”

Tana kaiwa nan ta sauka daga entrance din ta nufi motar cikin bacin rai, miyasa Momy zata zarge? Tana kama sa makiyiyar Leila ne? Why her? Bata zargi kowa ba sai ita. Momy ta bita da kallo har ta shiga motar ta fice sannan ta juya ta koma ciki. Har tayi kamar ta shiga dakin da Aminatu take sai kuma ta nufi dakin Leila kai tsaye domin ta san yarta tana cikin tashin hankali a yanzu. Tun kamin ta tura kofar dakin ta shiga ta ji sautin kukan Leila. Da sauri Momy ta karasa kusa da ita ta kai hannu ta dago ta daga kwance da take tana rera kuka idonta har yayi ja.

“Hana Leila so kike ki tonawa kanki asiri? Tun kamin a karaso gurin kofar dakin nan fa ana jin kukanki?”

“Momy na fara gajiya, waye yake min wannan abun? Momy ko waye tona min asiri zai yi, bana son na tafi gidan yari Momy bana son na mutu, Momy ba da gangan na kasheta ba”

Momy ta yi saurin rufe mata baki.

“Ki daina fadar haka, ba zan taba barin haka ta faru ba”

“Momy duba abun da yake cikin takardar nan”

Ta fada tana nuna Momy envelop din, Momy ta juya ta kalli Envelop din, rigar Baaba ce dake kalar dankwalin nan da aka aiko mata wannan karon ma rigar da datti kuma da kasa a jiki. Momy ta karasa ta dauki rigar tana dubawa.

“Shiyasa nake kyautata zatona akan yarinyar Madina ita kadai zata iya haka”

“Momy to ina zata samu kayan Baaba”

“Wata kila ta hada kai da mai gadin ne ta fasa ramen ta dauke gawarta shi ne take amfani da tufafinta take tsorata ki, amman dai ko minene zan je yau zan samu wanda zai yanke mana kwadon bincika gidan”

Ta share hawayenta.

“Kar garin yanke kwadon kuma sirrinmu ya kara bayyana, Momy tsoro nake ji sosai”

“Ki saka a ranki, ko asiri ya tonu ko be tonu ba babu abun da zai faru da ke, kin fi kowa sani ni da mahaifinki ba zamu saka ido a kaika gidan yari ba alhalin muna da kudin da za su iya siye komai, dan haka ki kwantar da hankalinki kamar baki aikata komai ba okay”

Ta gyada ma Momy kai sannan ta kara share hawayenta.

“Ko ma waye zamu gano shi, dan haka ki watsar da wannan damuwar ki maida hankali kan aurenku da Talba okay”

Nan ma kan ta daga ma Momy sannan ta mike tsaye ta nufi bathroom ta wanke fuskarta, ta fito ta je gaban madubi ta shafa hoda saboda ta batar da fuskar kukanta. Momy na kallonta har tai ta gama sannan ta mike tsaye ta dauki envelop din da rigar ta nufi dakinta da ita, a inda ta aje dankwalin ta saka rigar sannan ta fito ta sauko kasa tana kwalawa Talba kira.

*** *** ***

A hankali ya cire bakinsa daga nata ya kurawa fuskarta da idanuwanta dake rufe ido, kamin ya kalli bakinta da take motsawa a hankali. Dagawa yai daga jikinta ya saki hannayensa daga rikon da yai musu. A a lokacin ta samu ta bude idonta ta sauke kasa, hannunta ya riko suka fito daga bandakin ya zaunar da ita gefen gado, shi ma ya zauna ya ciro wayarsa yana kiran Hajiya Laraba yana shafa kansa idonsa na gurin Aminatu dake hawayen, gaba daya abun da yai mata a yau ya tsorata fiye da ko yaushe daga sunan nuna mata bandaki sai ya rike kunkurunta ya hana fita tana mika hannu fa kwaci kanta sai ya mannata jikin tile din dake bandakin ya rike hannayenta gam ya hade goshinsu guri daya ta yadda ba zata iya motsa kanta ba, sannan yai kasa da bakinsa ya kama lips dinta ya fara kissing in a romantic way, ita kanta a yau ta ji ta a wani yanayi da bata taba jin kanta ba. Yana jin muryar Momy ya mike tsaye da sauri yana murza idonsa da dayan hannunsa wai ko idon nasa da suka canja launi za su dawo daidai, ya nufi window ya tsaya rike da wayar a kunne sai wani jan numfashin yake yana ajewa kamar mai yaki da wata dabba.

“Hajiya mun dawo gida, an sallame mu”

“Okay to yara za su shigo anjima za su zo da tufafinta da sauran kayanta, amman dan Allah ka kula da ita Talba kana ganin yarinyar nan marainiya ce kuma bata san kowa ba a gidan nan sai kai”

“In shaa Allah”

Ya sauke wayar sannan ya juyo ya kalli Momy dake tsaye bakin kofar dakin, daman ya ji lokaci data bude kofar dakin.

“Ka fada mata kar tace zata takura kanta da zaman daki ta rika fitowa falo tana zama tare da mu”

Momy ta fada fuska ya yabo ba fallasa, Talba ya kalli Aminatu.

“Kin ji maganar Momy ko? Idan kina so ki rika fitowa falo ko harabar gidan akwai kujeru a ko'ina zaki iya zaunawa ki huta”

Ita dai bata ce komai ba, har ya fice dakin Momy ta bi bayansa. Bangarensa ya koma yai sabon wanka ya shirya cikin wasu tufafin sannan ya fito ya shiga motarsa zuwa office.

Tun da Aminatu ta shiga dakin bata fito ba sai karfe uku na rana, shi ma saboda Momy ta aika Zulai tace ta kirata ta fito falo ta ci abinci rana. Kamar wanda aka cilasta haka ta fito falon tana sanye da short Hijab, sai doguwar rigar abaya brown color kanta a kasa har ta karaso inda suke zaune a dinning din. Amal ta tabe baki tana kallonta, Kabir ma kallonta yake shi da Leila Momy ce kawai bata gurin duk da kasancewar ita ta saka a kirata.

“Sai kin ja kujerar tukuna ki zauna, na san baki taba zaunawa a kujerar cin abincin ba”

Leila ta fada tana watsa mata harara Amal ta fara dariya da karfi sai Kabir ya daka mata tsawa.

“Ke...”

Ta rufe bakinta da sauri, Aminatu ta yi tsaye a gurin tana jin kamar ta juya ta koma dakin. Kabir na ganin haka ya mike tsaye yaja mata kujerar.

“Zauna”

Sai ta zauna amman ta masa daga ido ta kalli kowa. Kabir da kansa ya zuba mata abincin ya zuba mata drinks.

“Ya Kabir ka zuba mata a glass cup ai bata taba sha a ciki ba, zai iya faduwa a hannunta”

Amal ta fada, Kabir ya watsa mata harara.

“Idan na sake jin wata magana marar kyau daga bakinki sai na baki mugun mamaki, kun dauka abun da kuke yi mai kyau ne? Talba kuka muzantawa ba ita ba”

Amal ta mike tsaye sanye da uniform din islamiya.

“Ni dai na tafi Islamiya kar ace na yi wani abun”

Leila ta saka dariya tana cin abincin.

“Ke kike tsoron ace kin yi, mu kam komai ba ma gudu”

Ta karasa tana murmushi, Aminatu ta mike tsaye idonta tab da hawaye, Leila da Kabir suka kalleta.

“Zauna ki ci abincin ki mana”

Kabir ya fada, sai ta girgiza masa kai.

“Saboda ban saba a taburin cin abinci ba, kuma ba mu da kofin gilashi a gidanmu ba shi yake nufin idan na zo gidan wasu a wulakanta ni ba”

Tana fadar haka ta juya ta fito daga dinning area din ta koma dakinta, tana shiga ta maida kofar dakin ta rufe ta jingina jikim kofar ta fashe da kuka marar sauti. Kuka tai sosai har sai da ta gaji dan kanta ta shiga bandakin ta wanke idonta sannan ta hau saman gado ta kwanta.
Sai 4pm Talba ya shigo gidan, sosai ya so ya dawo da wuri gidan sai dai aiki ya rike shi, yana shigowa gidan bangaren Momy ya fara shigo saboda hankalinsa yana gurin Aminatu.

“Sannu da zuwa Babe”

Leila ta fada tana zaune kan sofa rike da remote. Be amsa ta ba ya kalli Mairo dake aikin fesa air freshener ya ce.

“Mairo mai sunan Momy ta ci abinci?”

Kamin Mairo ta amsa masa Leila tai murmushi ta ce.

“Yau kuma kunyar kiranta kake da Shalele? Bata ci ba, Momy ta ci a kira har ta fito sai kuma ta koma”

Dakin ya nufa, sai da ya fara knocked sannan ya tura ya shiga ya maida kofar ya rufe, wani irin abu marar dadi ne ya ziyarci zuciyar Leila, tashi tai taje kofar dakin ta labe ta dora kunnenta saboda ta ji abun da ake fada. Aminatu na ganin Talba ta juya kai daga kwance da take ruf da ciki ta bashi baya. Zagaya yai gefen da fuskarta take yana karantar idonta.

“Kuka kika yi?”

Sake juyar da fuska tai sai ya hau saman gadon gaba daya ya dagota ya kwanto da ita jikinsa.

“Waya taba min Shalele?”

Ta yi shiru sai kawai ta fara hawaye, sakata yai a kirjinsa ya rumgume a tunaninsa kewa ce da rashin sabo, ita kuma bata son fada masa ace fa fara kai kara tun yanzu, wata kila zai iya fada da Leila.

“Sorry ina gurin aiki amman hankalina yana gurinki, na zo na dawo amman ban samu dama ba, kin ci abincin rana”

Ta girgiza masa kai tana kuka.

“Okay bari na kawo miki a nan ki ci ko zaki iya fitowa?”

Ta girgiza kai masa kai.

“Bari na saka a kawo miki a nan, daina kukan ya isa haka”

Ya saka hannunsa yana share mata hawayenta, sannan ya sake ta ya mike tsaye ya fice daga dakin, sake komawa tai ta kwanta a saman gadon tana jin kamar bed sheet din na warin jaɓa.

FAHAT POV.

“Okay na gode”

Ya fada sannan ya sauke wayar cikin rashin jindadi, kansa har sarawa yake saboda maganar da mutumen ya fada masa.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ya furta sannan ya mike tsaye ya fara zagaya dakin. Mamakin yadda akai Baturiya ta boye masa wannan abu mai muhimmanci yake, sam batai masa kama da wanda tai aure ba har ta haihu, sai dai ya san mutumen da ya saka yai masa abinciken ba zai masa karya ba. Ya tabbatar masa da bata da wata matsala amman ta taba yin aure ta auri wani dan'uwanta har ta haihu daya kuma ta fito da ciki. Zaunawa yai bakin gadonsa gaba daya sai ya rasa abun da ke masa dadi a rayuwa.

“Iya wannan ne abun da Momy ta sani ko da wani?”

Ya tambayi kansa, kamin ya kai hannu ya matse fuskarsa, sai kuma ya ake mikewa tsaye ya dauki wayarsa ya kira Baturiya few seconds ta dauka kana jin muryarta ka san tana cikin farinciki.

“Hello Dear”

Sai da yai controlling kansa sannan ya iya yi mata magana.

“Kina ina?”

“Lafiya?”

Ta tambaya domin muryarsa ta karanta da ita ba lafiya ba.

“Ba komai, kawai ina son ganinki ne”

“Bana gida yanzu, amman idan na dawo zan kira ka”

“Okay”

Ya amsa, sannan ta sauke wayar da dan mamaki, ta dauke hannun Alhaji dake kirjinta ta mike tsaye.

“Ya akai?”

“Wanda zai aure ni ne ya kirani, wai ina nake kuma na ji muryarsa kamar akwai matsala”

“Babu matsalar komai ki kwantar da hankalinki mu yi komai cikin natsuwa sai ki je ki same shi, wata kila shi ma yana son ya huta da ke ne”

“Aa irin wannan mu'amalar bata taba hadamu ba, akwai dai abun da yake faruwa gaskiya”

“Oh kina ji da saurayin nan naki, har na fara kishi”

“Dan ma baka ganshi ba kyakkyawa ne sosai ga naira”

Ta fada tana murmushi

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Tana jin Talba zai fito sai tai saurin barin jikin kofar ta koma ta zauna a inda take zaune dazun. Ko da ya fito ya same ta a inda ya barta wannan karon ko inda yake bata kalla ba, har yayi kamar zai je dinning din sai kuma ya nufi kofar fita domin ya fara zuwa ya canja tufafin jikinsa, domin suit ne jikinsa kuma baya sakewa idan yana sanye da shi a gida. Yana fita falon ta tashi da sauri ta nufi upstairs, dakin Momy ta shiga sai ta samu Momy na waya, kusa da ita ta zauna jikinta na rawa.

“Momy ki kashe wayar ki ji”

Momy ta yi holding call din ta kalleta.

“Lafiyarki?”

“Momy yanzu tace masa zata ci abinci”

Da sauri Momy ta katse kiran gaba daya.

“Bude jakata ki dauki maganin, but make sure babu kowa a falon nan kamin ki saka, ki tabbatar babu mai ganinki”

“Ko dai na dauko miyar na kawo nan?”

“Zai fi je ki dauko”

Ta tashi da sauri ta fice daga dakin, Momy ma tashi tai ta nufi inda ta aje jakarta ta bude ta dauko kullin maganin dake cikin kyalle ta zauna bakin gadonta tana jiran shigowar Leila. Leila kamar wanda tai sata haka ta shigo dakin dauke da miyar ta aje gaban Momy sannan taje ta rufe kofar dakin. Momy ta kwance kyalle ta zuba kadan sannan ta saka yatsanta ta motsa miyar.

“Dauki ki kai, kar kuma ki sha, yana zuba mata sai ki dauka ki zubar”

Da kai ta amsa mata sannan ta dauka ta nufi kofar ta bude ta fice, Momy ta tashi ta shiga bandaki ta wanke hannunta sannan ta fito ta dauki wayarta ta kira kanwarta Hajiya Sadiya, sai da ta kusa yankewa sannan Hajiya Sadiya ta dauka tana sallama. Momy ta amsa sallamar tana dariya.

“Hajaju Sadiya ya gidan ya yara”

“Wallahi lafiya kalau, ya su Leila kuma ya aikin ana nan ana ta yi ko?”

“To me za a fasa me nema a duhu kuma balle an haska masa? Amman fa na tsallakawan nan har da mu mun tsallaka, Allah yasa dai babu wata matsala”

“Aa babu yace ai ko da kun tsalla ba matsala ba ne domin shi da sunanta da sunansa aka hada akai so su kadai abun zai kama, wanda yake da matsala na a abincin nan dai kar ki bari Leila ta ci”

“Ai ba zan bari ba, yanzu haka am an zuba mata”

“Yauwa haka ake so, so ake ta ci, sauran wanda za ayi kuma yace sai an zo da Leila”

Momy ta dan yi shiru.

“Zuwan ne aiki ai, kin ga irin mu ba yawan fita muke ba, musamman ma irin kauyen nan ba son shiga nake ba, kar wani ya ganka yace ga wace can ina dadi?”

“Haba dai, ai ba shiga zaki yi yadda za a gano ki ba, cikin sirrin zaki shiga kuma ba dole sai kin je ba, Leila kawai ta wadatar”

“Ba zai yiyu shi ya zo ba? Ko kuma ya aiko mata da sakon?”

“Ai kin san da zai yiyu da haka zan yi, wannan ma dana karbo ai ba zuwa tai ba, amman wanda za a mata na tsakaninta da Talba yace sai ta zo fa”

“To a lallaba mana shi idan zai yiyu a dauko mana shi mana”

“To bari zan masa magana naji, sai dai kauyen ne na su ba samun network ake sosai ba wani lokacin sai kai ta kira bata shiga sai sa'a amman dai zan yi magana da shi”

“Okay duk yadda kuka yi sai ki sanar min”

“Toh shi kenan”

Daga haka suka yi sallama, Momy ta sauke wayar tana murmushi.

*** *** ***

Da farko ya shiga dakin ne kawai saboda ya canja tufafinsa, sai dai abu ne mai wahala ya cire wasu tufafin ya saka wasu ba tare da yayi sabon wanka ba, hakan yasa ya daura tawul ya shiga yai wanka a gaggauce ya fito ya saka short jean da jallabiya ya fesa turare ya nufo bangaren Momy, garin sauri har ya manta wayarsa. Danna door bell din Leila ta bude masa tana murmushi, kallonta kawai yai ya shiga cikin falon domin a yanzu mamaki take ba shi, gaba da ta soma canjawa. Dinning ya nufa kai tsaye ya dauki plate ya zuba abincin ya dauki cup ya saka spoon ya nufi dakin da Aminatu take, dadi kamar ya kashe Leila daga inda take zaune ta bishi da kallo har ya shige dakin. A kasa ya aje plate din sai ya dan kwanto da kanta tana kallon abincin, shimkafa da miya ne da coslow daya ji hadi, bata ce masa komai ba har ya fita ya dauko mata lemun kwali da ruwa ya aje mata.

“Sauko ki ci”

Ta dago a hankali ta kalleshi shi, sai kuma ya koma ta yi kwanciyarta kamar ba da ita yake magana ba.

“Babyna sauko ki ci abinci mana”

Nan ma bata juyo ba.

“Ko dan na dade? Na dan tsaya wanka ne, ni ma ban ci abincin ba, yanzu nake shirin ci”

Ya juyo ta kalleshi.

“Ni bana son wannan abun da aka zuba sama”

Ya kalli Coslow din.

“Akwai dadi fa?”

“Ni dai bana so ba zan ci abincin ba, bana son kamshin wacan abun”

Ta nuna cucumber.

“Okay na zuba miki wani?”

Ta yi shiru kamar ba zata ce komai ba, daman can ita ba wani son shimkafa da miya take ba. Ya zauna bakin gadon yana kallon yadda ta turo baki gaba tana kallon abincin.

“Baby waya bata min ke? Da can ba ki wannan abun?”

“Ni dai bana so, kuma dazun ma...”

Har zata fada masa Leila ta kira yar kauye sai kuma wata zuciyar ta hana ta.

“Okay bari na zubo miki da miyar ba da wannan abun ba, zaki ci?”

“Aa ni dai bana son abincin”

“To mi zaki ci?”

“Bana son komai”

“Kin ci wani abu ne da rana?”

Ta girgiza masa kai tana kallonsa kamar za ta yi kuka.

“Okay zan saka Mairo ta dafa miki indomie zaki ci?”

“Taliyar yara?”

“Eh”

Ta danne kafada.

“Bana so”

“Me zaki ci?”

“Ni ma ban sani ba”

“Okay”

Ya mike tsaye ya dauki abincin ya fice daga dakin, yana aje abincin a dinning Momy na saukowa sanye da wata tsadaddiyar atamfa.

“Yayi ango, kai da kanka kake bata abinci baka bari yan aiki da kanenka su yi aikinsu”

Ya juyo ya kalleta da dan kunya domin sai yanzu yake jin kunyar abun da yai.

“Leila ta fada min bata ci abinci ba, sai na shiga na tambaye ta ko tana son wani abu ne”

Momy ya karasa dinning din tana kallon abincin da ba a taba ba.

“Bata ci ba?”

“Eh wai bata son warin cucumber ne”

Momy taja wani numfashi na bakinciki ta aje.

“To yanzu yaya kenan?”

“Zan fita waje na samo mata shimkafa da wake, na lura tana son shi, ko kuma na bata biscuits da tea ta gwada sha kamin a gama na dare”

Bakincikin kin cin abincin da Aminatu tai yasa Momy ta rufe da fada.

“Wannan abun da kake rashin kunya ne Talba, kamar kanka farau mata? Yaushe ta zo gidan? Amman har ta fara maka zaben abun da zata ci, ko kunya baka ci ka dauki abu kaje kana kai mata, idan tana bukatar wani abun ka fadawa yan aiki mana ko kuma kanenka ko kuma duk ba su wadatar ba?”

Be ce komai ba, kuma daman ba zai ce din ba, sai dai abun da ya tabbatar Leila ce yai ma haka ba zata yi fada ba sai dai ta yaba masa. Shi kuma yana yin haka ne saboda ganin Aminatu bakuwa ce a gidan kuma bata sake da kowa ba kamar yadda ta sake da shi. Hannayensa ya saka aljihu ya nufi kujerar da ta Leila ta tashi ya zauna, domin Leila bata falon a lokacin. Momy ta kara masawa tana kallon shinkafar gashi bada ta yawa sosai da zata ci zata iya cinyeta tass amman ta ki ta ci kamr wanda ta san an saka wani abu a ciki. Daukar abincin Momy tai ta nufi kitchen ta zuba abincin a dustbin, sannan ta kalli su Mairo dake ta hada hadar hada abincin dare.

“Ina miyar da aka ci abincin rana da ita?”

“Leila ta zuba a shara, sai kular ta aje mana tace mu wanke”

“Good”

Ta fada sannan ta juyo ta fito daga kitchen din, ta nufi upstairs har ta fara takawa sai kuma ta sauko ta nufi bangaren da dakin Aminatu yake ta tura ra bude kofar sai ta hangonta kwace rairaim tana watsa da yatsunta tana ta silawarta a hankali. Momy ta saki kofar ta haye sama cikin bacin rai domin kin cin abincin sa Leila tai be yi mata dadi ba sam. Ta maida kofar dakin ta rufe tana jan tsaki, Leila dake zaune rike sa waya tana chat ta kalleta.

“Miya faru?”

“Bata ci abincin nan ba, wai wani bata son warin cucumber kiji min iskanci da samun guri”’

Leila ta zaro ido.

“Bata ci ba kuma? How ya shiga daki da abincin fa”

“Hmmm wannan yarinyar idan ta kara gogewa nan gaba sai ta yi ma mutane iskanci”

“A yanzu ma baki ga ruwanta ba, dazun fa saboda mu da Amal mun tsargeta sai cewa tai wai saboda ta fito kauye ba shi yake nufin a musguna mata ba, ko tsorona dana Kabir bata ji kuma ta ki cin abincin Wallahi wai ita uwar zuciya”

“Ai dole tai ba yayi ta hauka yana abubuwan ba akanta, ko wacan fadan da yai da ke a kanta ai kin san ba mantawa zata yi ba, tun daga lokacin zata fara ganin damarki ai, ”

“Kuma ina jin Momy wani gurin ya kaita ta waye sosai sai kamshi take, ta yi kiba ta yi kyau abun har mamaki yake ba ni”

“Gurin wannan kanwar mahaifiyarsa ya kaita fa,a garin nan ba shi da wata shakikiya ta bangaren mahaifiyarsa da ta kai Laraba, acan aka koya mata

wannan makircin shi kuma sai wani rawar kai yake kamar wata amaryar azo a gani”

“Ni Wallahi na matsu komai ya faru, ya sauwake mata ta koma can daji cikin yan'uwanta”

“Sai an yi hakuri Leila, ba wai farat daya komai yake faruwa ba da sannu sannu yake fara kamawa har ya wuce inda ake so, dazun ma na yi waya da ita ta ce yace sai kin zo akwai aikin da zai yi, amman gaskiya ina jin tsoron tafiya irin gurin nan saboda yanayin tsoro kuma zaka iya haduwa da wanka ka sani ko ya sanka”

“Aa Momy sai na rufe fuskata, indai za a samu biyan bukata ina ruwana da duk wanda zai gan ni!”

“Amman dai na yi magana da ita, idan zai yiyu shi ya zo nan din ko nawa ne zamu kashe”

“Idan ma be zo ba ni zan iya zuwa, biyan bukata ya fi dogon buri”

“Ki daina garaje Leila ki bi komai a hankali, abu na biyu kuma kar na sake ganin Madina a gidan nan, kar wata alaka ta sake hada ku, riga na ja mata kunne idan bata ji to zata janya kanta matsala”

Leila ta kalli Momy da sauri.

“Momy Allah yasa ba maganar envelop kika mata ba? Momy na fara canja mata fa duk dai saboda na gano idan ita din ce, amman yanzu haka da kika yi idan ba ita ba ce kin lalata alakarmu kenan fa haba Momy”

“Karki dame ni da wata magana, tashi ki fita”

Momy ta fada tana nuna mata kofa fuska babu alamar wasa. Leila ta mike tsaye kamar zata yi kuka ta fice daga dakin, downstairs ta sauko ta nufi inda ta bar wayarta ta dauka ta kira Madina. Sai ta samu Talba zaune a gurin yana kallon stairs din da alama jiran saukowarta yake. Bata ce masa komai ba ta kai hannu ta dauki wayarta.

“Miye a cikin Envelop din dazun?”

Ta mike tsaye a hankali gabanta na faduwa tana tunanin irin amsar da zata ba shi.

“Invitation card ne na birth wani friend dina he wanted to surprise me, that's why ya baka yace ka bani”

Ya dauke kai ba tare daya ce mata komai ba kuma ba dan ya yarsa ba. Juyawa tai da sauri ta fice daga falon zuwa harabar gida. Mikewa Talba yai tsaye ya nufi kitchen, Mairo da Zulai na ganinsa suka gaishe shi ya amsa musu da kai, sannan ya dauki karamin cup ya nufi flask din ruwan zafi ya bude ya zuba ya saka lipton da cube sugar uku sannan ya bude inda ake aje musu biscuit ya dauko leda biyu ya dora a plate ya fito daga kitchen din ya nufi dakin da Aminatu take. A hankali ya bude da dayan hannunsa yayinda dayan yake rike plate mai dauke da cup din

tea da biscuits manya biyu. Murmushi yai yana sauraren yadda muryarta take da dadin sautin a yayinda take karanta Suratul Yasin.

“Maa Shaa Allah, to sauko ki ci wannan kamin akai ga na dare”

Tsoroce ta juyo domin bata ji motsin Shigowar ba, sai ta tashi zaune da sauri tana kallonsa har ya aje plate din a saman gadon.

“Tea ne da biscuits zaki ci?”

Ta daga masa mai, domin tana jin yunwa. Sauke plate din yai kasa ya sai ta sauko ta nade kafafuwanta ta zauna. Kallonta yake for no reason bakar fatar jikinta tana burgeshi, gashi kyauta sai karuwa yake a fuskarsa, shi ma saukowa yai kasa ya zauna ya rika hannunta na dama da take cin biscuit din da shi yai kissing sannan ya matsa kusa da ita yai hugging dinta.

“I love you”

Ya saka hannunsa ya dago fuskarta tare da kwanto da tashi.

“Mu ji biscuit din yana da zaki”

Ta kai hannu zata dauki daya ta mika masa sai ya kai bakinsa daman ba rikon wasa yai na ma fuskarta ba, tana kokarin kwacewa amman ta kasa, a light kiss yai mata but very romantic one. Sannan ya cire bakinsa ya mike tsaye sai kuma ya kai hannunsa ya shafa kanta zuwa fuskarta yana murmushi ya fice. A hankali yaja kofar dakin ya rufe ta yadda ba zata yi kara ba, sannan ya nufi kitchen din ya hada na kansa tea da biscuits ya fito falo ya zauna yana sha.
Misalin 6pm Amal ta dawo daga islamiya, tana ganin Talba a falon gabanta ya fadi, ta yi zaton ko zai mata maganar abun da tai ma Aminatu ne a yanzu, da tsoro tsoro ta gaishe shi, sai ya kalleta yana murmushi.

“Little Sis kin dawo?”

“Eh kai kadai kake zauna a nan?”

Ya daga mata kai, cikin tsoro ta nufi stairs tana ta jiran ta ji ya kirata ya mata wata maganar amman shiru ba ce mata komai ba har ta haye sama. Ba shi ya tashi gurin ba sai da akai Magariba, sannan shiga bangarensa yai alwala sai a lokacin ya tuna da ya bar wayarsa a gurin, hannu ya kai ya dauka sai ya tararda eight miss calls from Ali, dan tabe baki yai ya saka wayar aljihu yana tuna kiran da Ali yai masa cewar yana son su hadu. Bayan sallah magarin ya dawo falon ya zauna, plasma ma kawai yake kallo Amman hankalinsa yana can gurin Aminatunsa, samun kansa yai da murmushi tunawa da yai da wasu abubuwan da suka wakana a tsakanisna da ita. Yana zaune a falon har Mairo da Zulai suka Gam jera abincin dare sannan suka fice zuwa bangarensu. Sai da akai sallah Isha'i sannan Kabir ya shigo falon, a lokacin Talba na zaune yana taba wayarsa.

“Kai kadai kake zaune? Ina amarya?”

Talba ya dan yi murmushi ba tare daya kalleshi ba.

“Ka karbo wayarka?”

“Yeah, amman ba wani update, wai Mutumen da suka gani a line wani igbo ne”

Ya fada yana kokarin zaunawa. Talba ya dago ya kalleshi.

“An ganoshi ne?”

“No mutumen da tai register line dai”

“Maybe sun siye line ne suka yi amfani da shi”

“Su ma haka suke tunani, amman dai zasu cigaba da bibiyar line ko za su samu wani abu”

Talba yayi shiru be ce komai ba. Kabir ya nufi dinning ya bude warmers din sai kamshi ya fara tashi na tuwon siyo da miyar danyen kubewa data ni ganda da kifi da nama.

“Wow...”

Ya fada sannan yaja kujera ya zauna. ya dauki plate ya zubawa kansa abincin ya fara ainawa cikinsa. Har ya ci ya koshi ya tashi ya bar falon Talba ne motsa daga inda yake ba. Contact dinsa ya shiga ya kira line Amal ringing daya ta dauka.

“Ya Talba?”

“Ba zaki ci abincin dare ba ne?”

“Zan ci”

Tana amsa masa sai ya kashe wayar, sai gata ta sauko sanye da tufafinta na bachi kanta babu dankwali, gabanta sai faduwa yake domin har yanzu ganin take Talba zai iya mata magana akan abun da tai.

“Ya kai ma zaka ci?”

“Me aka dafa”

Ta karasa dinning din ta bude tana dubawa.

“Tuwo ne”

“Na san tuwo ne ai, tuwon me?”

“Semo”

Ya girgiza mata kai alamar aa. Sai taja kujera zata zauna.

“Je ki kira mai sunan Momy ku ci abincin tare”

Fasa zaman tai ta juyo ta nufo dakin da Aminatu take, daga bakin kofa ta tsaya tana mata magana.

“Ya Talba ya ce ki ta so mu ci abinci”

“A nan zan ci”

Amal ta juyo ta kalli Talba.

“Wai a nan zata ci”

Talba ya fyada mata kai, sannan ya mike tsaye ya isa dinning ya zuba mata abincin da kansa ya saka man shanu sannan ya dauka ya nufi dakinta, ba tare da wahala ba ya shige dakin sakamakon barinsa bude da Amal tai a dazun. Amal dai sai kallonsa take gulma na cinta rai kuma bata san da waye zata yi ba. Zaune ya same ta saman dankwalinta tana kallon kofar dakin.

“Ki daina kadaice kanki, idan kina so ki rika fitowa kina zaunawa a falo ko harabar gidan”

Ya fada bayan ya aje mata abincin, ita dai bata ce komai ba, ta sauke ido kasa tana kallon tuwon da yai mata kama da na masara.

“Tuwon masara?”

“Aa na Semo ne, shi ma yana da dadi ki ci ko koshi kin ji?”

Ta daga masa kai, sai ya juya ya fita be dade ba ya dawo dakin da ruwan sanyi na roba da cup ya aje mata a gabanta.

“Karki yi saurin bachi, maybe Daddy zai kai goma na dare kamin ya dawo, ina son ku gaisa da shi”

“Toh”

Ta fada tana auna yadda zata ci tuwon da cibi domin da hannu ta saba cin abinci. Matsawa yai kusa da ita ya sumabanci goshinta ya shafa fuskarta sannan ya fice daga dakin. Tana ganin ya fita ta tashi ta shiga bandakin ta wanke hannunta ta dawo ta zauna ta fara cin tuwon.
Sosai ta ci shi saboda yunwar da take ji gashi kuma ta ji shi kamar tuwon masara da suka saba ci a garinsu.
Bayan ta gama ta wanke hannunta ta dauki plates din ta fice da su daga dakin zuwa falo, bata ga kowa a falon ba sai Amal sai ta doshi inda Amal din take tana cin abinci.

“Ina ake aje kwanuka idan an ci abinci?”

Amal ta nuna mata da hannu, Aminatu ta nufi kitchen din farkon shigarta sai ta rasa inda ma zata aje kayan, sai da ta kare kallon yadda tsarin kitchen din yake da yadda aka kawata ko'ina sannan ta matsa kusa da inda ta ga an aje wasu kwanukan ta aje, fito.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Yana fita daga falon ya koma part dinsa ya dauki key din motarsa ya fito ya shiga motar, yana mata key ya danna horn alamar fita zai yi, da sauri masu gadin suka bude masa gate. Reverse yai ya fice daga gidan, sai da ya isa bakin gate din gidan Ali sannan ya kira shi ya sanar masa yana wajen gidan. Kashe motar yai ya fito ya zagaya bayan motar ya tsaya yana kallon gidajen dake makota da Ali.

“Yau kuma a wajen kake son tsayawa? Ko kuma fushin har yanzu baka gama ba?”

Ali ya fada yana dariya, sai Talba ya juyo ya kalleshi da dan murmushi kadan a fuskarsa.

“Sai ka ce wani karamin yaro dai?”

“To ai naga ka dauka da zafi ne sosai, ka ki ka sauko”

“Wanda ka taba ce mai zafin shiyasa ban saurara maka ba, you know sometimes zaka iya yi ma mutum abu ya share weather ya ji zafin ko akasin haka, amman idan ka taba wanda yake da muhimmanci a rayuwarsa sai ya ji yafi tsanarka fiye da kowa a duniyar nan”

“Yeah”

Ya fada yana tuna yadda yake ji idan ya musgunawa Leila ko ranta ya bace. Shi ma yana jin ba dadi saboda ya damu da ita, ba wai dan yana sonta ba.

“So you have to be very careful next time, idan ma akwai wani da kake ji a zuciyarka game da Aminatu, ka aje shi a cikin ranka, she's my wife and i love her, ko da ace bana sonta ba zan lamunci wani ya ci mutuncin ko fada mata wata magana marar dadi ba saboda tana karkashin ikona kulawarta tana karkashina, balle kuma ina sonta”

Yayi murmushi mai sauti.

“Yanzu ka yarda kana sonta kenan? Da can baya ai baka yarda ba”

Shi ma murmushin yai ya kalli bangarensa na dama.

“Na yarda, domin na ji abun da ban taba ji ba, a lokacin data bata, kamar na yi hauka haka na ji, kuma data dawo sai na gane na fi batanta haukacewa, i believe ba tausayi ne kawai ba har da kauna”

“Tana ina yanzu? Asibiti?”

“No tana gida, Momy ta bukaci na aje ta gidan i have no other choice, sai idan na ga da matsala sannan na canja mata guri, kuma na san zaman da zata yi na dan lokaci ne”

Ali yayi murmushi.

“Leila zata yi kishi wata zata rigata tarewa, Talba baka da kirki”

“Na yi kokari fa Ali, na yi bibiyar yarinyar nan mu yi aure amman taki, kuma ka san at my age ya kamata ace na aje yaya ma, kuma ni kaina ina bukatar auren Ali”

“To ai kai ne baka fiton ta sigar da zata gane ba, kai ka rika yin abu cikin izza da nuna isa”

“Amman duk da haka na nuna, kuma yi magana ai ya kamata ta saurareni ta amince ko?”

“Ai ko yanzu da kai da wanda be yi auren ba duk daya, tun da baka tare da matar ba”

Cewar Ali yana masa dariya.

“Da babu ai gwara ba dadi, kuma idan Momy bata duba ta ji tausayina ta barmu mun tare ba, matsala zata biyo baya, domin ba zan ga samu na ga rashi ba, wai ance ga koshi ga kwanan yunwa”

“Ina mamakin yadda kake sakewa da yarinyar Aminatu, baka yin haka da Leila”

“Nima ina mamakin kaina wani lokacin, sai dai ka san komai shi yake samawa kansa muhalli, Amina bata da girmankai da jin kai kamar Leila, ita dai barta ga shagwabar kuka, idan na ce ta daina abu kaza zata daina, kuma na fahimcin tana da jin magana tun a yanzu, what do you expect idan mun zauna a gida daya a matsayin miji da mata? But look at Leila the way da take dress ta fita bana so, kuma ban isa na yi magana ba, ba canjawa zata yi ba, wani abun kuma Momy zata fara shigar mata tana cewa wayewa ce ko kuma ina takura mata, Ali abun da baka sani ba, Leila tana takama da kudi, tana jin Daddy yana raye, and even between her and Amal Momy ko da yaushe tana side din Leila, so Leila tana jin babu abun da zata rasa, not like Aminatu, data rasa Mamanta Babanta da duka familynta, and now na aureta idan ban tausaya mata ta ji sanyi a gurina ba a ina zata ji shi? Bana ma fatar juya mata baya”

“Haka ne, kana da gaskiya, Allah ya baka ikon rike su duka da amana da kuma adalci”

“Aamin, shi ne fata na gari”

Ali ya jingina jikin motar ya rumgume hannayensa yana kallon Talba.

“Na Kira ne na kara baka hakuri ne akan abun da na yi, na ji ba dadi gaskiya”

Har Talba ya bude baki zai yi masa wata magana sai kuma wata zuciyar ta hana shi.

“Saboda kana... Ba komai komai ya wuce ai”

“Secondly kuma Madina ta kirani tana kuka wai Momy ta zarge ta da shirya abun da ake yi ma Leila”

“Me ake yi ma Leila?”

“I don't know, na tambaye ta, sai tace min be kamata ma ta yi min maganar ba, saboda sirrinsu ne”

“Wane irin sirrin kuma bayan ta fada maka?”

Ali ya daga kafardarsa.

“Ni ma dai shi na gani, amman kuka take sosai gaskiya”

“Amman ni miya kawo ni cikin maganar ta ne?”

“I don't know ko kai zata fada maka abun da yake faruwa, kuma a yadda suke da Leila be kamata ace Momy ta mata haka ba, ya kamata a shiga lamarin aji me ke faruwa, ko ba komai ta maks hallaci na aje maka Aminatu”

Talba yayi murmushi.

“Abun bashi ne?”

“No amman dai ya kamata ka shiga tsakani gaskiya”

Talba ya kalli agogon, ya sake kallon Ali.

“Zan yi magana da ita, on Monday idan ta shigo office”

“Okay duk yadda kuka yi da ita, please let me know”

Talba ya gyada masa kai.

“Zan tafi kar dare yayi”

“Yayi kyau ango”

Ali ya fada da siffar zolaya yana murmushi. Talba ma murmushin yai ya bude motarsa ya shiga.

“Lokacin da kai naka ai babu wanda ya rikama, ka jira ma wani abun sai na tare”

Ali ya saka dariya sosai, yana kallon Talba cike da mamaki, sai da yai reverse sannan ya fisge motar da karfi. A hanya ya tsaya gurin wani mai gasa kasa ya siya mata daya ya kara gaba ya sai yogurt. Karfe goma da yan mintuna ya faka

harabar gidan kusa da motar Daddy. Kashe motar yai ya bude ya fito ya bar kazar a ciki, ya nufo bangaren Momy. Sau daya ya danna door bell din Amal ta bude masa.

“Sannu da zuwa Ya”

“Yauwa, baki kwanta ba?”

“Eh yanzu zan kwanta dai”

“Good je ki kwanta”

“To sai da safe”

Ta nufi upstairs dana yi tana waigensa daman gulma ce ta tsayar da ita har yanzu bata kwanta ba. Tsaye yai dai da ya tabbatar ta haye sama sannan ya juya ya bude kofar ya barta bude ya koma gurin motarsa da sauri ya bude ya dauko ledar kazar da Yogurt ya dawo falon, kamar wanda yai sata haka ya tura kofar dakin Aminatu ya shiga. Kwance ya hangota saman gadon sanye da hijab tana ta sharar bachi. Karasa yai kusa da gadon ya aje mata ledar sannan ya dan risina ya kai hannunsa ya taba ta.

“Shalele”

Ko matsawa ba ta yi ba balle ta amsa, da alama bachin ya mata dadi kuma ya nina. Mikewa yai tsaye gaba daya ya matsa gurin kanta ya cire mata hijab din jikinta ya dauki dayan zanen gadon dake gefen gadon ya lulluba mata, sannan ya zauna kusa da ita yana kallon fuskarta, can kuma ya kai hannu ya shafa fuskar.

“Na ce miki karki yi bachi, saboda ki gaisa da Daddy amman kin yi”

Ya fada yana murmushi still yana shafa fuskarta, yaja hancinta ya kai bakinsa ya hura mata iska a ido.

“Cute girl”

Ya fada sannan ya sumbance ta ya mike tsaye ya fice daga dakin. A hankali yaja kofar dakin ya rufe sannan ya nufi upstairs, tura kofar dakin Momy yai ya shiga da sallama, sai ta amsa masa fuska ba yabo ba fallasa.

“Barka da dare”

Ya fada bayan ya zauna saman kujera, sai ta amsa masa ba tare da ta kalleshi ba.

“Barka dai”

Sai ta cigaba da duba akwatin sarkokin da take, ta yi banza da shi kamar bata san da zamansa dakin ba. A zatonsa zata ce ya kai Aminatu gurin Daddynsa su gaisa amman bata ce masa ba. Yana kokarin tashi wayarsa tai ringing.
Da murmushi yai picking call din Daddy.

“Daddy”

“Ranka ya dade kana ina?”

“Gani dakin Momy”

“Yayi dan gidan Momy, to a sanar da ita na dawo kuma ina son ganinka idan da hali”

“Gani zuwa”

Ya fada yana mikewa tsaye, sai da ya saka wayar aljuhu sannan ya kalli Momy.

“Daddy yace a fada miki ya dawo”

“Toh”

Har yayi kamar yai mata maganar Madina, sai kuma ya fasa ya sa kai ya fice daga dakin, a tunaninsa zai fi kyau ya ji daga bangaren Madina kamin yai magana da Momy, maybe zai san yadda zai bullowa lamarin. Ta cikin falon ya bude kofar da zata sadashi part din Daddy. A falon farko ya samu Daddy zauna yana kallon labarai, sallamar da Talba yai ne yasa ya juyo ya kalleshi with smile.

“Ranka ya dade sai na bukata ake zuwa ganina”

“Daddy da safe baka fita da wuri fa, kuma kasan ka'ida ne idan baka tashi ba, ba zan tayar da kai ba, secondly kuma na yi shiru”

“I know that's why na kiraka ai na bka hakuri, yau na ke da niyar zuwa na dubata sai gashi da dare Momynka na fada min za'a sallame ta yau kuma a nan zata zauna, shiyasa na ce bari na bari sai kun dawo ta gida”

“Amman Daddy...”

Sai kuma yai shiru sakamakon daga masa hannu da Daddy yai yana murmushi.

“Ba sai ka fadi komai ba, na san ina da laifi ai, amman duk da haka ai ya kamata ku zo tare a gabatar min da ita ko? Dan dai kasan gidana na iyalina ne ni kadai, na baku aro ne”

Ba Talba ba har Daddy da yai maganar sai da yai dariya, balle kuma Talba.

“Na ce kar ta yi bachi zata zo ta gaisheka, but kamin na dawo sai na tarar ta yi bachi”

“Ba kai ya kamata ka kawo ta ba ai, Momynka, zan yi magana da ita, je ka kwanta”

“Okay Daddy mu kwana lafiya”

Ya fada yana mikewa tsaye, Daddy ya bishi da murmushi, wannan karon da zai fita ta kofar gaba ya fita ba kamar dazun ba, da ya shigo ta kofar part din Momy.

  Aminatu bata farka ba sai asuba, rabon da tai yi bachi mai dadi irin wannan har ta manta, sauka tai saman gadon ta nufi bathroom din dake cikin dakin tana

murza ido, alamar bachi be gama fita idonta ba. Fitsari ta fara yi sannan tai alwala ta fito ta nufi inda carpet take shimfide, sai a lokacin ta tuna hijabinta data kwanta da shi.

“Waya cire min Hijab to”

Ta tambayi kanta tana juyowa ta karewa dakin kallo, sai tai arba da zanen gadon daya lulluba mata.

‘Talba ne’

Ta fada a ranta, domin ta san shi kadai zai iya shigowa dakin ya cire nata hijab ya lullube ta, Leila dai ba zata mata haka ba, balle kuma Momy Kabir kuma be isa ya shigo dakin ba har ya lullube ta. Murmushi tai ta nufi inda Hijab din yake ta dauka ta saka sannan ta dawo ta fara sallah.
Raka'a biyu tai ta sallame, a sallamarta ta biyu ne ta lura da bakar ledar dake gafen gadon data kwanta, bata taba ledar ba sai da tai addu'a ta gama, sannan ta kai hannu ta janyo ledar mai cike da maiko. Budewa tai sai tai arba da katuwar kaza, dayar ledar kuma yogurt ce a ciki. Murmushi tai ta shiga bandakin ta wanke bakinta da brush sannan ta dawo ta zauna ta tisa kazar a gaba tana ci. Tun tana ci a hankali har takai bata da gurin numfashi a cikinta, har wani uban nishi take kamar wanda aka ce dole sai ta cinye duka. Ragowar kazar ta hade da kassa ta maida inda ta ganta, yogurt din kam ko taba shi ba tayi ba. Daker ta tashi tana gyatsa ta shiga bandakin ta wanke hannunta ta fito tana ta raunar naman data gagara hadewa. Zaunawa tai bakin gado sai kuma ta haye gaba daya ta kwanta rairai tana kallon fankar dake kashe, ac ne kawai ke aiki. Ba shiri ta zabura ta tashi zaune tana kallon kofar shigowa da ake murdawa, a zatonta Talba ne sai tai arba da Leila dake sanye da tufafin bachi.

“Gimbiya sai ki ta so mu shirya breakfast ko?”

Ta fada tana dan hararta a kaikaice. Uffan Aminatu bata ce ba, duk kuwa da kasancewar ta fahimci abun da take nufi, domin a makarantar da take zuwa talla da kuma mu'amala da dalibai da take tana tsintar wasu kalamai na turanci.

“Ke fa nake jira”

Leila ta maimaita ganin ko motsawa Aminatu ba ta yi ba. Sai a lokacin ta sauko daga kan gadon tana kallon Leila

“Ni ba komai na iya dafawa ba”

“Tare zamu yi ai, ki same ni kitchen”

Leila na fadar haka ta saki kofar dakin ta juya. Aminatu ta turo baki gaba, domin ta san wahalar da ita ne kawai Leila take son yi, tun sa akwai yan aiki a gidan. Kamar zata fasa kuka haka ta fita dakin ta nufi inda take kyautata zaton madane, ta tura ta shiga sai ta tsaya daga bakin kofa tana kallon Leila da ita ma tsayen take kamar mai tunanin abun yi. Me zata fara? Fasa kwai? Ko feraye dankali? Ko kuma mai zata fara soyawa? Ko ruwan zafi zata fara dorawa ta tafasa? Dan juyowa tai ta kalli Aminatu dake tsaye jikin kofar tana kallonta, sai tai saurin dauke ido, ta nufi kofar waje ta kitchen din ta bude sannan ta dawo ta dauki roba ta fita zuwa inda ake zube buhun dankalin turawa, ciko robar tai ta dawo kitchen din ta mikawa Aminatu.

“Ki fara da wannan, ni zan fasa kwai”

Aminatu ta karba ta matsa kusa da fridge ta risina.

“Ki bani wuka da wani roba mai ruwa”

Leila ta dauki wata robar ta cika ta da ruwa, sannan ta zaro wuka ta mikawa Aminatu. Karfi hali kawai take domin ba sanin tai yadda ake shirya breakfast din gidan ba, ta fi gane yadda ake ci kawai, idan ta gama a kwashe kwanunkan.

“Ki dawo daga nan sai na taya ki mu karasa da wuri kamin Momy ta farka”

Aminatu bata yi mata musu ba ta dauki komai ta maida inda ta nuna mata kusa da tab. Door bell din falon ce tai kara, sai ta kalli Aminatu fuska a yatsine.

“Bari na fadawa Mairo da Zulai yau mu zamu shirya breakfast”

Ta fada sannan ta juya tana murmushin keta ta fice daga kitchen din. Kai tsaye kofar falon ta nufa ta bude, Mairo ta fara gaisheta sannan Zulai amman bata amsa musu ba.

“Aminatu zata shirya abun karyawa, idan an gama za a sanar muku”

Bata tsaya jin abun da zasu ce ba ta rufe kofar tana jan tsaki.

“Kullum ku rika damun mutane da farar safiya kamar dole”

Daman can tana jin haushin yadda suke zuwa da sassafe a falon, idan kuma ba su shigo da wuri ba Momy zata yi fada. Ko da ta dawo har Aminatu ta feraye dankali uku ta saka a roba. Tsaye tai bakin kofar kitchen din tana watsa mata harara wani hayakin bakinciki na taso mata. Jin motsin shigowar mutum a kitchen din yasa Aminatu ta juyo ta kalleta, sai Leila ta tsuke baki ta karasa kusa da ita ta zari wuka, ta dauki dankwalin ta fara gyarawa. Tsit kitchen din yai kamar ba kowa a ciki, Aminatu na ta aikin gyara dankali Leila kuma ta kasa feraye ko daya sai wasa take da shi tana watsa mata harara kasa kasa, can kuma ta dago tana murmushi ta ce.

“Kin ba ni tausayi sosai, Talba ya fada min abubuwan da suka faru, Allah ya jikan iyayenki”

Aminatu ta yi shiru for few seconds sannan ta amsa.

“Ameen”

“Azzaluman mutane ne, gashi suna wulakanta mata ba kadan ba”

Aminatu ta tsayar da gyaran dankalin da take ta. Hakan kuma ba karamin dadi yai ma Leila ba, daman burinta ta bakantawa Aminatu.

“Akwai zafi ko? Wai ya kika ji lokacin da suka miki fyade?”

Aminatu ta dago ta kalleta da idanuwanta da suka cika da hawaye zuciyarta kuma ta hau bugawa da karfi.

“ Na ji kwatankwacin abun da kika ji a lokacin da kika ji Talba ya aure ni, shi ai ya fiki sanin abun da ya same ni ko? Kuma a haka ya aureni ya bar ki, ni da ke muna jin bakinciki daya ne, har kara ni na auri wanda ya san abun da ya faru da ni, ke fa babu abun da ya same ki amman ya barki ya aure ni”

Mutuwar tsaye Leila tai tana kallon Aminatu with shock, bata san lokacin data rika kan Aminatu da mugun karfi ta buga a tab din sannan ta jefar da ita kasa da mugun karfi. Wata mahaukaciyar kara Aminatu tai ta dafe goshin tana faduwa kwance.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Ihu sosai Aminatu take, daman ita da kuka are 5&6 mai neman kuka an fada masa masa mutuwa, daman can ko ba a taba ta idan kuka ya motsa yi take balle yanzu kuma da akai mai dalili, gashi kalamin da Leila tai mata ya mata zafi fiye da goshinta dake zafi, wannan yasa kukan nata ya karu tana ta ihu kamar wanda aka cirewa ido. Kukanta ne ya saka Amal cire hijab din da tai sallah ta nufi kofa daman ita ake bari baya a kullum gurin sallah asuba, abu ne mai wahala ta farka a lokacin da kowa yake farkawa. Da sauri ta sauko downstairs ta nufi kitchen din da take jin ihun na fitowa tana daf da shiga kitchen din Leila ta fito a fusace har suna shirin yin karo da Amal. Amal ta bita da kallo kamin ta kalli kofar kitchen ta leka a firgice, hango Aminatu tai a kwance tana ta rusar ihu, bata tsaya ta ji dalilin kukanta ba balle har ta san abun da take yi ma ihun ta juyo da gudu ta nufi kofar dage can dayan bangaren falon, kofar dake sadasu da part din Daddy, domin Momy tana bangaren Daddy. Da gudu Amal ta shiga part din ta tura kofar falon Daddy ya shiga kamin ta karasa karamin falonsa har haki take, sai da ta isa kusa da kofar bedroom dinsa sannan tai burki, shi ma ba dan Momy ta hana ta shiga dakin Daddy kai tsaye ba da shiga zata yi, ta tsaya tana kwalawa Momy kira.

“Momy, Momy ki fito Laila da mai sunanki sun yi fada”

Da iyakar karfinta take fada ganin babu alamar fitowar Momy yasa ta karasa bakin kofar tai knocking.

“Momy Leila ta yi fada da Aminatu, mai sunanki tana can a kitchen tana kuka”

Tana fada tana kwankwasawa, tana jin an taba kofar ta dan matsa bawa, a zatonta Momy ce sai tai arba da Daddy sanye da jallabiya.

“Daddy ina kwana? Mo... ”

Sai kuma tai shiru ta kara karasawa daman gulmarta ce ta saka take son fada, yanzu kuma tana tsoron kar Momy tai mata fada.

“Me na ji kina fada?”

“Daman Momy na ke nema”

“Munafuka, bayan kin gama fadi? Yanzu zaki wani canja magana kina nemana, waya sani ko ke kika haddasa komai”

Momy ta fada tana fitowa daga dakin.

“Miya faru?”

Daddy ya sake tambaya.

“Daman Aminatu ce na ji ihunta sai na sauko sai na ga Leila ta fito kitchen ita kuma Aminatun tana kuka”

Ta fada tana satar kallon Momy dake hararta. Daddy ya nufi kofar fita daga falon kai tsaye, Momy ta watsa mata harara.

“Aku, ke kan kin ji haushin rayuwa, yanzu sauranki Talba da Kabir”

Ta karasa tana jan tsaki, sannan ta bi bayan Daddy. Tsaye Amal tai sai da ga sun fice daga karamin falon ta kofar ciki, sannan ta nufi kofar gaba ta bude ta nufi part din Talba da Kabir, madaidaicin falo ne, mai dauke dakuna guda uku, daya daga dama na Kabir sai na Talba daga hagu sai kuma na tsakiya wanda ake sauke bako, idan na musamman ne, an kawata falon da kananan cushion daya bangare kuma an saka karamin teburin cin abincin, sai katon plasma da ba kallo suke da shi ba, domin kowa yana da na shi a dakinsa.
Dakin Talba ta nufa ta kwankwasa masa, ta san baya son ana masa knocked fiye da uku, amman da yake wannan gulma ce sai ba tai kasa a guiwa ba wajen dagewa tana buga masa kofar da karfi.

“Yaya Talba”

Be ta ji motsin zai bude ba sai da ta ambaci Aminatu.

“Yaya Leila ta yi fada da Aminatu tana can tana kuka sosai”

Tana gama rufe baki da dakiku ya iso gurin ya bude kofar yana kallonta jikinsa sanye da pajamas.

“Ina take?”

“Tana kitchen”

A bude ya bar dakin ya fice da sauri, sai ta bi bayansa, kamin ya karasa gurin kofar falon har da saurinsa, sau daya ya murda kofar ya ji a rufe sai ya juyo da sauri zuwa part din Daddy daya hango kofar a bude. Ta cikin falon Daddy ya bi ya shiga part din Momy, da gudunsa ya karasa kitchen din sai ya samu Momy da Daddy tsaye Aminatu kuma na kwance tana rusar kuka Leila na daga gafe.

“Daddy zagina fa tai”

Leila ta fada tana kokarin kare kanta daga fadan da Daddy yake mata. Da sauri Aminatu ta tashi zaune tana rike da goshin da yayi kololo.

“Karya take ban zage ta, ita ta tambaye ni na amsa mata shi ne ta ji haushi ta buga min kai a fanfo kuma ta wulgar da ni kasa”

“Ke Aminatu yaushe kika koyi munafurci? Sannan Leila bata girme ki ba da zaki ce karya take, fitina kike son hada mana a gida”

Daddy ya jefawa Leila wata bakar harara, kamin ya kalli Momy dake kokarin tare mata.

“Kina nan lokacin da komai ya faru? Ko kuma laifin yarki kike kokari karewa? Shiyasa kika ce ya dawo da ita gidan nan saboda ku musguna mata? Idan ma zaginta tai me kai hannunta a jikinta? Yarta da zata daketa? Ke kanki baki dukan yayanki balle wani ya dukar miki yaya, akan mi Leila zata daga hannu ta daki yar wasu? Kuma matar Talba? Ni kuka wulakanta da ni Talba, domin ko yar tsana ɗana yake aure be kamata ku wulakanta ta ba, balle mutum”

Sai a lokacin Talba ya nufi inda Aminatu take zaune, domin tun da ya shigo kitchen din tsaye yake bakin kofa saboda bacin rai da kaduwa, kasa cewa komai yai ya karasa kusa da ita tana kuka ya rika hannunta yana kokarin duba goshin sai ta fisge hannunta ta sake dafe gurin tana kuka.

“Ki bata hakuri yanzu nan?”

Leila ta kalli Daddy da sauri, Momy ma kallonsa tai.

“Haba Engr, ayi mata hakuri dai, kasan Talba bata iya controlling kanta idan rai ya bace, amman kamata yayi ka bincika abun da ya faru, yaushe yarinyar ta zo? Ba mu gama sanin halinta ba, wata kila ita ta ziga Leila ne da yawa har ya saka ta mareta, kasan kuma Leila da saurin fushi”

Daddy ya nuna Momy da yatsansa cikin bacin rai.

“Wannan ya zama na karshe da zan sake saka yayana wani abu ki shiga a ciki kina son tsaya musu, kin ga wacan yarinyar da Leila daga lokacin da Talba ya aureta matsayinsu daya a gurina, muna nan da ke wata rana sai na yi mata abun da ban yi ma yaya ba, ko kuma na hana yayana abu na yi mata”

Ya juya ya kalli Leila yana daka mata tsawa.

“Duka ki bata hakuri”

Leila ta resina da sauri idonta na cika da hawaye, muryarta na rawa.

“Ki yi.... Hakuri....”

Ta mike tsaye da sauri sai, sai Daddy ya sake daka mata tsawa.

“Duka ki bata hakuri na ce”

Leila ta kalli Momy da sauri, sai Momy ta gyada mata kai alamar ta yi, domin ita kanta tana shakkar Daddy idan ransa ya bace. Leila ta duka kasa tana kuka.

“Ki yi hakuri ki gafarce ni...”

Ta mike tsaye tana jin wani irin wulakancin da kaskanci da bata tana ji ba. Da gudu ta fice daga kitchen din tana kuka. Daddy ya juyo ya kalli Talba.

“Ba ka sati daya, ka dauke matarka daga gidan nan ka kaita gidanka ku tare can, ka fadi duk abun da kake bukata zan saka a zuba muku kamin lokacin”

Momy ta bude baki da sauri.

“Haba Engr, na ga ai Leila ta bata hakuri, kuskure ne ana samun tsabani ma tsakanin halshe da hakori balle kuma dan adam”

Uffan Daddy be ce mata ba ya fice daga kitchen din sai ta bi bayansa, Amal dake labe ta fito ta leka kitchen din.

“Kai ashe har da kololo bari na kira Ya Kabir ya saka mata magani”

Sai da ta juya ta fita daga kitchen din sannan ta tuna ita ma ai ba kaunarta take ba, sai kawai ta fasa zuwan ta nufi upstairs. Amal na ficewa Talba yai saurin rumgume Aminatu ta runtse ido yana jin wani irin tausaynta.

“Baby na miyasa kika shigo kitchen din? Ji yadda ta taba min jiki har yayi kololo”

“Ita ce ta ce na zo mu yi girki”

Aminatu ta fada cikin kuka, sai ya kara rumgumeta yana jin kukanta har cikin ransa.

“Bana son gidan nan... Bana son gidan nan....”

“Shiiiiiii”

Ya fada yana kokarin kai bakinsa kunnenta sannan ya mike tare da ita tsaye, ya dan saketa daga rikon da yai mata yana duba goshin.

“Bari na duba kadan”

Ta ki bari sai kuka take, hannayensa ya saka ya dauketa cak ya fice da ita daga kitchen din, Kofar fita falon ya nufa ya bude da hannunsa na hagu yana rike da ita ya fita daga falon, be direta ko'ina ba sai gaban motarsa. Be damu da duba waye a gurin ba ya kai bakinsa ya sumbanci hannayenta.

“Bari na dauko keys dina na kai ki asbiti, amman ki daina kukan dan Allah”

“Ni dain na tsani gidan nan”

Ta fada domin har ga Allah ji take ta tsani gidan. Da sauri ya nufi bangarensa ya shiga da sauri, be taba saka tufafi ba tare da yayi wanka ba sai yau a gaggauce ya shirya. Ya dauki keys dinsa da walle da wayarsa ya fice da sauri. Leila na tsaye jikin windows din dakinta tana kallon fitowar da Talba yai har ya karasa gurin motarsa ya bude wa Aminatu front seat ta shiga ta zauna, ya rufe sannan ya zagaya side dinsa ya shiga da sauri ya tashi motar. Juyowa tai ta share hawayenta sai da ta kai karshen dakin ta juyo ya dawo gurin window ta leka kasa, sai sake juyowa ta dawo tana rumgume da hannayenta hawaye na sauko mata. Zaunawa tai bakin gadonta tana jin zuciyarta kamar zata fasa kirjinta ta fito, kamar ance dago tana dagowa Momy na turo kofar dakin ta shigo.

“Leila miya kaiki aikata wannan abun?”

“Momy kin san abun da ta fada min? Ce min tai wai Talba ya aureta ya bar ni”

Momy ta zauna kusa da ita da mugun mamaki.

“Ita da bakinta ta fada miki haka? Wato har ta samu bakin fada miki bakar magana?”

Leila ta rumtse ido hawaye na fito mata.

“Daddy ya saka na bata hakuri, Momy kishiyata? Na bata hakuri bayan kuma na fita komai, kuma ita ta tararda da ni a gidanmu? Ta auren min miji a yau har tana min alfahari da cewar ya aureta ya bar ni”

Ta nuna kanta wasu zafafan hawaye na sauko mata. Tausayinta ya kama Momy.

“Duk ba laifinsu ne, laifin Talba ne, da kuma Ali duk shi ya m haddasa komai, da Talba be sake mata ta samu fuska da wuri haka ba, da bata isa ta fada miki magana ba, amman komai zai wuce, na rantse miki da Allah Leila sai Talba ya aureki kuma sai ya rabu da yarinyar, saboda haka ki kwantar da hankalinki ki daina kuka ki bar komai a hannu, ki rika karfafa min guiwa mana, ina fama da mahaifinku ke kuma kina nan kina min kuka? Na samu ya yarda ta zauna a nan ta yadda zamu samu abun da muke so, sai kuma ki rika janta har tana fada miki magana da zaki kasa rike kanki? Leila ki rage wannan zafin zuciyar, saboda wannan zafin kika aikata abun da kika aikata gashi naj ya zame mana fitina, ke kenan idan rai ya bace baki san ki rike kanki ba? Miya kai ki janta har kitchen?”

“Ba janta na yi ba, kofi ta shiga dauka, shi ne fa daga na mata maganar Talba sai ta yabo min bakar magana”

“Ki daina yi mata maganar mana, babu ruwanki da safgarta, ke dai ki saka ido ki yi kallo”

Momy ta karasa tana dafata, kamar wanda aka yayewa bakinciki haka Leila ta ji, a take kukan da take ya yanke ta share hawayenta farinciki ya baibaiye ta, domin Momy ta yi rantsuwa kuma ta san Momy idan tace zata yi zata yi balle kuma yanzu da ta hada da rantsuwa.

“Momy karshen kaunar da zaki muna min ita ce ki kori yarinyar, ni Wallahi ko ban auri Talba ba zan fi kowa farinciki idan ta rabu da shi”

“Zan yi haka, amman ki yi taka tsantsan da ita, ki kawar da ido ga duk wani abu da zaki gani, kuma ki rika controlling wannan zuciyar taki Leila”

“Inshallah”

“Bari naje na ji da Mahaifinki shi kuma, kin san idan ya hau be iya saukowa cikin sauki ba, musamman akan Talba nan”

“Momy kina jinsa har da cewa wai bata da banbanci da ni”

Cewar Leila tana jin haushi.

“Ba sai idan ta zauna a gidan ba tuluna, anjima idan Talba ki samu Talba ki ba shi hakuri, kuma ki saka shi gaba ku je gurin mahaifinku ki ba shi hakuri”

Ta gyada kai, sannan Momy ta tashi ta fice daga dakin.

TALBA POV.

Faka motarsa yai ya juyo ya kalli Aminatu da har lokacin kuka take kanta yayi wani gummmm kamar ba nata ba. Kujera yaja mata ta kwanta baya. Sannan ya ciro wayarsa, ya kira Ali, sai da wayar tai ring har ta katse Ali be yi picking ba, daman kuma ya san haka zai faru saboda safiya ce wata kila wayarsa ta kwana a silent ne.

“Ba lallai ne ace asibiti sun fito ba yanzu, zai kaiki gurin abokina unguwar Yarima ya dubaki okay”

Ya fada yana kallon yadda idonta sukai ja.

“Ni dai bana son gidan can, ka kai ni gurin Mama”

Ko kadan baya son kaita gurin Hajiya Laraba domin ya san wani fadan ne zai ta so.

“Shikenan, amman ki daina kukan nan ji idonki”

Ya fada cike da damuwa, sannan ya ja motar suka hau titi. In few minutes suka iso kofar gidan, sai ya danna horn aka bude masa, ya shiga har gaban entrance din ya faka motar ya bude da sauri ya fita ya shiga knocking din kofar da karfinsa. Babban dan Ali ne ya bude kofar mai shekara bakwai, yana ganin Talba yai saurin gaishe shi.

“Daddy ina kwana”

“Lafiya Kalau Sadiq, shiga ka ce ma babanka yana da bako”

“Toh”

Ya juya da sauri ya koma ciki, Talba ya dawo cikin motar ya kashe ac, ya juyo yana kallon Aminatu dake ta faman sauke ajiyar zuciyar kamar zata tashi sama

saboda kukan data sha. Hannunsa ya kai ya kama hannunta ya rike yana kallonta kamar zai cinye ta.

“Karki sake yarda ki kebe daga ke sai Leila, bana son wani abu yana faruwa”

“Bana son wannan matar bana kaunarta”

“Shiiiiii”

Ya fada yana kai hannunsa ya bakinta.

“Ki daina fadar haka, ki da ita dole me ku ko yi zama da juna, domin a karkashina zaku zauna, dole ne ku hada kai ku kaunaci junanku, bakinki ya daina furta irin wannan irin wannan maganar, ita ma zan yi magana da ita”

“Gori fa ta min tace min, wai ya na ji lokacin da aka min fyade... ”

Ta kara fashewa da sabon kuka. Gana daya sai Talba ya ji jikinsa ga mutu, he never thought Leila zata iya yi mata irin wannan maganar.

‘Why Leila miyasa baki jin magana ne?’

Ya fada a ransa yana jin haushin abun da tai, kamin ya fita daga motar ya ganin Ali daya fito da sauri ya daso inda ya aje motar.

“Allah yasa dai lafiya”

“Ina lafiya Leila ta taba min Shalele, N san ba kowa ne likita ya fito ba a yanzu 7 ba bata yi ba, dan Allah ka duba min ita”

Ali ya karasa gefen da Aminatu take ya bude motar, sai Aminatu ta dago ta kalleshi tana hawaye.

“Subhanallahi miya faru?”

“Zamu yi magana daga baya, yanzu dai so nake a dubata, ayi mata hoto a duba kanta idan bata samu matsala ba”

Har Ali yayi kamar zai yi magana, sai kuma na hadewa, tunawa da yadda Talba yake daukar zafi akan Aminatu.

“Okay, but yanzu zan rubuta mata magani, hoton anjima idan masu yi sun fito sai a kaita sh dauki hoton”

“Rubuta min”

“To ka shigo da ita ciki mana”

Talba ya leka fuskar Aminatu.

“Zaki fito?”

Ta lake kafada, alamar aa.

“Bana son ko'ina ni ka kai ni gurin Mama”

“Bata so, Rubuta min maganin kawai, kai yi hanzari please ”

“Amman Talba...”

Sai kuma ya fasa ta hanyar yanke maganar ya nufi cikin gidansa. Ba jimawa ya fito rike da takarda ya mikawa Talba.

“Gashi Allah ya sauwake”

Talba ya karbi takardar da sauri ya shiga motar, tun kamin ya gama juya motar mai gadin gidan ya bude masa gate ya fice da gudu kamar an koroshi. Ali ya bishi da kallo kamin ya girgiza kai.

“Talba zai haukace akan yarinyar nan”

Juyawa yai ya koma ciki yana mamakin abun da ya hada su da har Leila ta ji mata wannan ciwon.

A gaban wata katuwar Pharmacy Talba ya faka, ya fita rike ta takardar ya shiga, be dade ba ya fito ya dawo cikin motar dauke da ledar maganin. Bude maganin yai ya balla kowanen, ruwan dake motar ya bude ya mika ya kai mata a baki.

“Bude bakin”

Ta bude ladan sai ya zuba mata ruwan sannan ya saka mata maganin, daker ta hade maganin saboda bata kaunar magani balle kuma allura.

“Yi hakuri Shalele daure ki hade”

Ya kara kai mata wani maganin, ta bude baki tana ya mutsa fuska.

“Ba zan iya shanyewa duka ba”

Ta fada ganin maganin yana da yawa.

“Idan kin shaye zan kai ki gidana ki huta tukuna sai na kaiki gidan Mama”

“Aa ka kai ni gidan Mama yanzu”

“fo shanye maganin duka”

Ta bude baki ya zuba mata ruwa sannan ya saka mata maganin kana ya kora mata da ruwa. Sannan ya rufe gorar ya mika hannunsa gurin sitiyarin motar yaja motarsa ya dauki hanyar da zata sada shi da gidansa.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa

taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Tana ganin yayi parking a bakin gate din gidan ta gane inda suka zo, juyawa tai ta kalleshi tana son fashewa da sabon kuka.

“Ba nan nace ba, gidan Mama”

“Okay zaki huta anan kamin mu je can gidan Mama din, kin san idan ta ga idonki haka hankalinta zai tashi”

Ya fada sannan ya bude motar ya fita, ya saka key ya bude gate din ya dawo ya shiga da motar ciki, sake fita yai yaje ya rufe gate din ya dawo bangaren da Aminatu take ya bude side dinta.

“Fito muje ciki ki kwanta ki huta”

“Gidan Mama zaka kai ni”

Ya fada hawaye na sauko mata, sai ya resina gabanta ya mika mata hannunsa.

“Bani hannunki”

Ta mika masa hannunta, sai ya rike ya sakar mata murmushi.

“Kin yarda da ni?”

Ta daga masa kai.

“Good ai ba zan kaiki inda zaki cutu ba, ba nace zan aje ki a nan ba har na tsawon lokaci, no zan ki zauna ki huta idan kin farka zan kaiki gidan Mama ki zauna a can har na gama gyara inda zamu zauna”

Ta sauko da kafarta sai ya mike tsaye yana rike da hannunta ta fito motar ya rufe. Rumgumota yai ya kwanto sa ita kirjinsa yana tafiya a hankali har suka isa bakin kofar ya saka keys din hannunsa ya bude kofar falon suka shiga. Dukawa yai ya dauke ta cak ya nufi upstairs, be sauketa ko'ina ba sai akan gadon dake dakin, ya saka hannunsa ya cire mata hijab ya kwantar da ita.

“Kwanta ki huta bari na nemo miki abun da zaki ci”

“Amai nake ji”

Ta fada tana jin zuciyarta na tashi.

“Eh saboda kin sha magani ne baki ci abincin ba”

Ta sauke ajiyar zuciya da karfi, sai ya gyara mata kwanciyarta ya sumbaci kumatunta sannan ya sauka daga kan gadon. Sai da ya sake bude gate din ya fita da motar sannan ya rufeta ta ciki ya dawo ya cikin motar. Be yi wata tafiya mai nisa ba ya faka gaban wata restaurent ya shiga ciki waina ya siyo mata da miya da nama, sannan ya dawo cikin gidan. Ko da ya shigo ya samu ta yi bachi sai ya shiga kitchen ya dauki cooler ya saka wainar ya rufe ya dawo cikin dakin. Inda ya saba aje tawul dinsa ya nufa ya dauki daya, sai da ya juyo ya kalleta ya ga idonta a rufe sai ya juya ya cire tufafinsa ya daura tawul din, ya nufi bathroom, shower ya kunna yai jika jikinsa sannan ya dauki sabulun Showel gel a murza a jikinsa. Bayan ya gama wanka ya fito ya daure da tawul dayan hannunsa kuma rike da karamin tawul yana goge jikinsa. Turare ya dauka ya shafa a jikinsa sannan ya fesa body spray, sannan ya juyo ya hau saman gadon, zuwa yai bayanta ya kwanta a hankali ta kai hannunta ya rumgume ta sannan ya sumbancin bayan kanta. Ya saka hancinsa cikin gashin kanta yana shinshina har shi ma bachin ya dauke shi.

Bata farka ba sai kusan goma na safe tana bude ido sai ta jita a jikinsa, idanuwanta suka sauka kan kirjinsa da sauri ta tashi zaune ta matsa baya, sai ya bude idon ya kalleta.

“Ya akai?”

Ta juya baya da sauri ta sauke kafafuwanta daga kan gadon, sai ya kalli jikinsa da idon bachi yai murmushi ya mika hannu ya riko hannunta.

“Ni bana bachi da riga a jikina, kuma ai ba wani abu ba ne, ni mijinki ne muharraminki”

Ya tashi zaune ya matsa kusa da ita ya rumgumeta ta baya.

“Za...za...za..za...”

Ta kasa fadi maganar sai rabe mata take ta kasa hada kalmomin ta fada. Sai yai murmushi ya sake ta ya sauko saman gadon, wani dan karamin daki ya nufa ya saka tufafi sannan ya fito yana kallonta.

“Yanzu fa?”

Ta ki ta yi magana, kuma ta ki ta kalleshi gaba daya kwarjininsa ya kamata, ta kasa daina ganin kirjinsa da idanuwanta sukai arba da su a dazun. Ya rika hannunta yana murmushi.

“Ta so muje ki wanke baki, sai ki ci abinci na siyo miki waina kina sonta?”

Ta mike tsaye a zatonta hannunta zai ja su shiga ciki, sai ta ji ya dawo bayanta ya rumgumeta tana turata gaba kadan kadan suna tafiya, har suka shiga cikin bathroom din, har gaban madubin ya tsaya da ita ya ware hannayensa ya matsa toothpaste a brush daya ya kai mata a baki.

“Bude”

Ta bude bakin kamar yadda ya umarceta, sai ya saka brush din yan soma murza mata a hakora, sai ya wanke mata bakin tas sannan ya tara hannunsa yana zuba mata ruwa tana kurkurewa ya zubar ya wanke mata fuskarta. Kana ya sake

zuba toothpaste din a jikin brush din ya wanke bakinsa sannan suka fito tare. Saman gadon ya zaunar da ita ya fita ya dauko wainar da plate da ruwa ya kawo dakin ya aje. Yana saka mata biyu ta ce.

“Ya isa”

Ya kalleta.

“Waina biyu? Fushi kike da abincin ne?”

Ta yi shiru can kuma ta ce.

“Ya ishe ni ne ai”

“Waina biyu ba ta da yawa, ki dauri ki ci ko uku”

Ya fada yana saka wainar guda biyar a plate.

“Sun min yawa”

“Tare zamu ci”

Ya zuba miya, sannan ya sauko da ita kasa kamar wata yarinya ya saka hannunsa yana deban wainar yana kai mata a baki, kadan kadan take taunawa tana hadewa, idan ta hade sai ya kai mata wata, haka haka dai har ta cinye biyu ganin shi be ci yasa ta kalleshi.

“Baka ci ba”

“Zan ci amman sai kin koshi”

Ta bude baki ya saka mata wainar, sai da ya tabbatar ta koshi sannan ya cire hannunsa, yana kokarin mikewa tsaye ta ce.

“Baka ci ba”

“Ni bana son waina daman, bana son cin abu mai nauyi da safe, zan soya kwai na ci”

Sai da ya kwashe komai sannan ya dawo ya rika hannunta.

“Ta so muje ki soya min kwai kin iya ai ko?”

Ta gyada masa kai, ta mike tsaye suka fice daga dakin. Kitchen suka nufa yana rike da hannunta, babu wasu kayan aiki sosai saboda shi kadai yake zaune a gidan kuma ba yawan zuwa yake ba sai idan ta kama. Gas ya fara kunnawa sannan ya kalleta.

“Sai ayi me ma?”

“Sai an fara fasa kwai an kada an saka magi da komai sannan ake hura wuta fa, sai a soya mai a saka albasa idan ta yi sai a zuba kwan”

Ya wara ido yana kallonta.

“She kin iya, okay kin ga inda kwai yake can bari na dauko miki magi da sauran kayan sai ki soya min”

Ya fada yana nuna mata, sannan ya dauko, mata komai ya aje ya fice daga kitchen din. Bedroom dinsa ya koma ko da ya shiga wayarsa na vibration karasa yai ya dauki wayar, yana dubawa kamin ya kaita a kunnesa.

“Hello Momy”

“Na'am Talba kana ina? Baka karya ba ka fita ita ma kuma bata karya ba”

Ya dan yi shiru kamar mai nazarin abun da zai ce. Sai ta sake aiko masa wata tambayar.

“Na yi zaton a gida zaka barta Kabir ya dubata, ka kaita asibiti ne?”

“Eh”

“Yaushe zaku dawo?”

“Ta ce tana son na kaita gidansu Hajiya Laraba ta kwana biyu”

“Aa aa dan Allah karka kaita, kasan tana gani ranta zai bace ka dawo da ita gida, na maka alkawari babu abun da zai sake faruwa”

“I will talk to her idan ta aminta tana so zan dawo da ita, idan kuma tace sai can zan bar a can ta kwana biyu kamin na gama gyara inda zamu zauna”

“Ka biye mahaifinka kenan, haba dai saboda wannan abun daya faru har ya kai ace zaka yi fushi ka dauki mata ku tare a can? Ina da plan din abubuwan da na yi maka, ko na ce na yi musu, ina son idan Leila zata je gyara jikin sai a tafi Aminatun ayi musu komai tare, tarewar ma sai a saka lokaci daya ayi musu walima da komai a tare”

“Aa Momy, bana son Leila ta sake kebewa da yarinyar nan, saboda idan Leila ta sake kai hannunta a jikin Matata ni kaina ban san iya abun da zan mata ba, yanzu ma na kyale ta ne saboda Daddy ya gama magana kuma yayi abun da ya kamata, ban yi zaton saboda a wulakanta ta kika bukaci na kawo ta gidan ba, kuma ni ma ban kawo ta saboda a wulakantata ba”

Momy ta yi murmushi.

“Talba kenan, yau ni kake fadawa haka? Saboda soyayyar yarinyar nan? Allah ya kyauta”

Ta kashe wayar yana saukewa kiran Hajiya Laraba na shigowa. Sai ya sake picking.

“Hajiya ina kwana?”

“Lafiya Kalau Talba ya Auta da jiki?”

“Alhamdulillah”

“Tana kusa?”

“Aa ina wani guri yanzu, ita kuma ta fita tare da Momy”

“Da Momy kuma?”

“Eh”

Hajiya Laraba ta yi jimmm kamin ta tabe baki ta ce.

“Idan ta dawo ina son magana da ita, kuma yaran nan suna son zuwa gurinta”

“Eh idan ta dawo zan fada miki sai su zo”

“To, a dai ji tsoron Allah a rike amana”

Yayi murmushi.

“Inshaallah”

Ya sauke wayar sannan ya aje ya fito daga dakin zuwa kitchen, ko da ya shiga ya same ta tsaye a gurin gas din ta soya kwan na farko ta sauke zubi na biyu kuma yana kan wuta, tana ganinsa tai saurin tare wanda ta soya saboda ya dan kone.

“Ga wani nan ina soyawa”

“Wanda kika soyan fa?”

Ya fada yana leken bayanta, sai ta kara karewa.

“Ya dan yi kauri shi ne nake soya ragowar”

“To ni ba a min barna a gida”

Ya karasa kusa da ita ya janyeta ya duba kwan, sai ya saka hannunsa ya dakon.

“Zaki ci wannan ni zan ci na kan wuta, saboda ke kika kona shi”

“To ai kai ka cika wutar har ya kone, yanzu ne na rage shiyasa zai so yu da kyau”

Ya saka dayan hannunsa ya rikota with serious face.

“Ni ba ruwana, ke zaki cinye shi”

Ya ware zaro ido.

“Mai kauri?”

“Eh waya saka yayi kaurin?”

“To waya ce ka tafi ta bar ni a kitchen din?”

“Waya na amsa, kuma ke kika ce kin iya”

Ya fara kokarin saka mata kwan da karfi, ita kuma tana ta son kwatar kanta amman ta kasa, tun tana yi da gaske tana son masa kuka ganin da gaske kwan yake son saka mata a baki har ta gaji ta fashe da dariya, sakamakon cizon data gantsara masa yayi ihu.

“Wayyo ta cije ni”

Dariya take sosai tana kallonsa kamar ba ita ba. Shi ma dariyar yai yana kallon yadda nata dariyar ya kara mata kyau. Ya rikota ya kai hancinsa a a nata yana goga mata a hankali yai kasa da bakinsa ya kama lips dinta yana sotsawa a hankali, sai ta lumshe ido yana sauraren yadda halshensa yana yawo a bakinta yana sotsar soft lips dinta kamar ya samu sweet. Sai da ta soma jin kauri sannan ta bude idon, ta dago hannunta tai masa magana sai ya saka hannunsa na hagu ya rike mata hannu. Ya cire bakinsa daga bakinta zuwa gurin wuyanta yana lasa yana mata tafiyar tsutsa.

“Kwan ya kone”

Ta fada tana jin jikinta na wani irin tsammm sigar jikinta na tashi, ganin ba shi da niyar daina abun da yake yi yasa ta matsa baya, hakan ya bashi damar manna jikinta da ginin gurin ya kai bakinsa ya kama kunnenta yana kissing.

“Wayyo Yallabai dan Allah ka daina”

Ta fada da muryar dake nuna tana daf da fashewa da kuka. Sai ya dago ya kalli kwayar idonta ya sake kai hannunsa ya rika kunkurunta.

“Shalele ki daina jin tsoro kinji? Ni mijinki ne”

Ya fada murya kasa kasa idonsa kamar ba nasa ba. Sannan ya sake ta, sai kuma ya juyo da sauri ya rike ta ganin tana kokarin barin kitchen din, ya janyota ya motsa da ita kusa da gas din ya kashe wutar ya sauke kwan sannan ya zube na hannunsa ciki ya ya matsa jikin tap ya sakata tsakiyarsa ya raba hannayensa ya wanke hannunsa jikin tap diin sannan ya kashe tap din ya juyo da ita ya dagata sama da dora a gurin ya matsa daf da ita yana kallon fuskarta.

“Ba zaka ci kwan ba?”

Ta tambaya jikinta na dan rawa tana jin tsoron irin kallon da yake mata, domin ta hangi tashin hankali da fitina a idonsa.

“Ya kone”

“Bari na soya maka wani”

“No”

Ya amsa yana kai hannunsa ya dage doguwar rigar jikinta ta fara shafa cinyarta still yana kallon cikin idonta.

“Zan yi fitsari”

Ta fara kokarin tureshi. Sai ya dauketa ya lakar da ita jikinsa ya sumbancin kirjinta, kokarin saukowa take ya hanata, ta fara tafiya da ita a haka ya suka shiga bedroom din ya sauke ta saman bed shi ma ya hauro saman gadon yana kokarin kwantar da ita.

“Ka ce zaka kai ni amin hoto anjima asibiti”

“Eh zan kai ki”

Ya sake ta ya sauka saman gadon ya rike kansa ya rumtse ido sosai.

“Ta so muje ki yi wanka”

Ya fada sannan ya bude idon ya miko mata hannunsa.

“Na iya wanka ai”

“Muje ki yi na gani idan kin iya din”

Ta girgiza masa kai.

“Ni dai na iya”

Be sake ce mata komai ba ya hauro saman gadon ya fara kokarin cire mata rigar jikinta.

“To tsaya tsaya zan cire a bandaki”

“To muje”

Ta rigashi sauka saman gadon ta nufi bandakin, tana shigewa ta maida kofar ta rufe ta saka key. Dariya yai ya kwanta saman gadon yai ruf da ciki ya rumtse ido yana kije baki.

FAHAT POV.

Baturiya ta kalleshi ganin tun da ta shigo motar yayi shiru be ce mata komai ba, tana kallon fuskarsa ta san akwai damuwa a tare da shi.

“Kamar akwai abun da yake damunka”

“Yes”

“Miya faru dear”

Ya sauke ajiyar zuciya.

“Mommy na ce, ta ki amincewa dake”

Ta kalleshi da sauri.

“Kamar ya?”

Ya sake sauke ajiyar zuciya.

“Cewa take ba ki dace da ni ba, daman ta dade tana min wannan maganar, sai dai bata taba min fada sosai kamar dana fada mata cewar iyayenki sun ce na turo ba”

Baturiya ta ji gabanta ya fadi.

“Akwai wani abu ne daya saka ta tsane ni ko kuma bata son aurena da kai?”

“Bana tunaninka, akwai dai saboda tana kawo min yan'uwa da yayan abokanta ni kuma ban yi na'am da ko daya ba, yanzu kuma na gabatar mata da wanda ba zabinta na ce ita nake son aure”

“Amman kana jin zata amince?”

“Zata amince, saboda tana son abun da nake so, kuma idan har ta yi bincike bata ga wata matsala a tare da ke ba ba zai hana ta amince ba, Abbah zai tsaya min”

Ta sake jin faduwar gaba.

“Shiyasa a daren nan kace min idan ka koma zaka bata mu gaisa, ina ta jira baka kira ba, tun lokacin zuciyata ta raya min akwai matsala”

Idonta ya cika da hawaye.

“Ki daina kuka komai zai wuce, ki yi ta addu'a kuma ki sani cewar ina kaunarki, no matter Fee'at”

Har cikin zuciyarsa yake wannan maganar da ita, domin yana sonta sosai kuma yana jin cewar abun da aka fada masa ba zai saka ya ki aurenta ba sai idan Mahaifansa ba su amince ba. Dagowa tai ta kalleshi.

“Kamin wani alkawari Fahat”

Yayi shiru yana kallonta. Sai ta kama hannunsa ta rike hana hawaye.

“So nake ka min alkawari ba zaka taba rabuwa da ni ba, ina son ka yi min wannan alkawarin Fahat”

Ya kurawa hannunta ido yana kallo, ya kasa cewa uffan har na tsawon lokaci, hawaye sai sauko mata suke tana kallonsa tana son ya amsa mata.

“Fahat...”

Sai ya janye hannunsa daga rikon da tai masa, ya kawar da fuskarsa.

“Fahat...”

Ta kira sunansa da mugun mamaki.

“Idan har mahaifiyata ta dage akan cewa ba zan aureki ba, to bani da wani zabi daya wuce na barki, amman bayan haka bana ji akwai wani dalili da zai saka na guje miki, kuma ina son ki san cewa ina kaunarki sosai”

Ta share hawayenta ta bude motar ta fita, da kallo ya bita har ta shige ciki gidan sannan ya dora kansa saman sitiyarin motar. Fata kawai yake abun da abokinsa ya fada masa ya zama ba gaske ba, duk kuwa da ya san abokinsa ba zai masa karya ba, amman miyasa zata boye masa abu mai muhimmanci irin wannan? Why? Ko tana ganin kamar idan ya sani ba zai aureta ba ne? Wata kila tana jin tsoron rasa shi ne, kamar yadda shi ma yake jin tsoron rasata a yanzu domin abu ne mai wahala iyeyensa da yan'uwansa su amince masa ya auri bazawara a halin yanzu. Ya dade a kofar gidan sannan ya buga motarsa yai reverse ya fita daga unguwar, rasa abun da ke masa dadi, domin tun da yake a rayuwarsa be taba jin son mace ba kamar yadda yake son Baturiya, duk macen da aka kawo masa bata masa sai Baturiya, yanzu kuma wannan matsalar ta bullo bayan ita da shi duk sun kamu da son junansu, da ace ta tun farkon haduwasu ta fada masa komai da zai gina soyayarsu ne akan haka, kuma zai gabatarwa iyayensa da ita a matsayinta na bazawara, amman a yanzu iyayenta da shi kansa duk suna mata kallon budurwa ne, har sai da binciken da binciken daya saka abokinsa ya tabbatar masa da haka, a yanzu ya gane da wannan Mommy take masa shagube, wata kila ita ma tayi nata binciken ta gano haka. Sai dai shi ya kasa nunawa Baturiya cewar ya sani, ita kuma ta ki ta fada masa komai.
Misalin tara da rabi ya faka motarsa harabar gidan, sannan ya bude ya fito kamar marar lafiya haka yake tafiya, har ya iso kofar falon dake bude ya shiga ciki, saman sofa ya fara zama sannan ya tashi ya nufi dakin mahaifiyarsa. Da sallama ya shiga ta amsa masa ta kalleshi tana aje plate din hannunsa, sai ya zauna kusa da ita cikin yanayin damuwa.

“Kin yi magana da Abbah?”

“Muhammad Fahat, daga shigowarka babu gaisuwa babu komai sai tambayar na yi magana da mahaifinka?”

“Na ga yau kwana kusan uku da yi miki maganar nan”

“Amman na ce maka kaje na kara bincikar yarinyar nan ko? Kamin ka gabatar da ita gurin mahaifinka ya kamata ka san wacece ita”

“Na san wacece ita Mommy, kawai dai baki son ta ne saboda bata daya daga cikin yan matan da kike zaba min”

“Ba ko daya, kawai dai yarinyar bata dace da kai ba ne, saboda ta taba aure idan ma baka sani ba bari na fada naka, ni na saka ayi min bincike akanta”

Yayi murmushin karfin hali.

“Daman abun da kike nufi kenan da ta taba aure? Ai na san bazawara ce”

“A can kam baka sani ba, ai baka taba nuna min cewar bazawara ba ce, sai yanzu da kai naka bincike aka tabbatar maka da haka ko? Ko kuma ta gaji ta fada maka, kuma duk da haka ka dage kana son aurenta, to bari na ji na fada maka, in dai ni na haifeka ba zaka auri yarinyar nan ba, sai kace wanda akai wa baki, kana saurayinka matashi ka auri bazawara mata har da danta, ance ma da ciki ta fito gidan wacan mijin”

“Mommy duk be dame ni ba, ina son ta tana so na, ba ni da matsala da wannan”

“To na fada maka ba zaka aureta ba, kara ma ka rabu da ita tun wuri”

Mahaifiyarsa ta fada cikin tsawa, sai ya mike tsaye yana kallonta cikin damuwa.

“Idan kin dage na rabu da ita zan rabu da ita Mommy, amman Wallahi ba zan taba son wata ba”

Ta juya ya fice daga dakin cikin bacin rai.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

FARUK POV.

Washe garin ranar aka kai Sultan asibiti tare da Mama. Sai dai kowa bangarensa dabam, kanwarsa da wata yar'uwar Mama suka rakata, shi kuma ya kai dansa bangaren yare a Yariman Bakura. Sultan magani kawai aka rubuta masa da allurar ya dawo da shi. Mama kuma suka bata gado saboda yanayin jikinta. A wajen asibitin ya siye magani suka rubuta masa yadda ake amfani da shi, sannan ya wuce tare da Sultan asibiti da akai Mama domin ita private hospital aka kaita. A wajen asibitin ya tsaya sai da ya kira Maman Safiyya ta fada masa inda suke sannan ya karaso yana dauke da Sultan. A harabar asibitin ya sami Maman Safiyya zaune tana hira da wasu mutane dake kusa da ita. Karasa yai da sallama ya gaishe da mutanen sannan ya zauna a gurin.

“Ya jikin Mama”

“Da sauki amman sun bata gado tana can ciki”

“Okay bari na duba ta”

Ta mike tsaye sai ta mika hannu ta karbi Sultan din dake kafarsa, a take Sultan ya juya baya.

“Zo nan Sultan, ya jikin naka”

“Na ji sauki, ba zan sauko ba”

Daga mahaifinsa har mutanen dake gurin sai da suka yi dariya, Sultan akan a bakin gaskiyarsa ba zai sauko ba, domin ganin yake idan ya sauko Faruk zai sake yin tafiya ne ya bar shi, a dole Faruk ya shiga ciki tare da shi. Katon daki ne da aka jera gadajen marasa lafiya a ciki, sai dai ko wane tsab kuma an saka curtains an zagaye kowane gado sai idan kana ra'ayi zaka bude, sai dai kasan cewar rana da dan daga kowane gado an bude shi ga likitoci sun shigo suna duba mutane, yana tafe yana duba dama da hagu har ya ha hango mahaifiyarsa ya kwance ana saka mata ruwa. Rukaiya na zaune daga gefe tana rumtse ido, sallama yai murya kasa kasa ya karasa Nurse din da amsa masa da murmushi a fuskarta, sannan ta aje hannun Mama a hankali bayan ta gama.

“To bude idon sarkin tsoro, ashe ba zaki iya aikin asibiti ba”

Nurse ta fada, sai Rukaiya ta bude idon tana murmushi.

“Gaskiya ba zan iya ba, ina da tsoro sosai”

“Aiko aikin lafiya yana da kyau mace tai shi, domin ana karuwa da ita, kuma ko ba komai yana mata kyau”

Ta fada da yar siririyar muryarta, sai Faruk ya karasa mata yana murmushi.

“Musamman irinki”

Kallonsa tai tana murmushin daya bayyana dimples dinta.

“Na gode, bari na kira Doctor”

Ta sadda kai kasa ta nufi hanyar fita daga gurin.

“Doc na gama”

“Okay”

Doc ya fada, ya cigaba da duba file din da yake na wata patient din sai da ya gama sannan ya dawo inda Mama take, Doc ya mika masa suka gaisa.

“Ya akai kuka yi sake har hawan jininta ya kai haka? Na tambayi wannan ta ce kun san tana da shi, amman ba ku yi komai ba har ya kai haka?”

“Gaskiya mun san tana da shi, amman ni ban san abun ya kai haka ba saboda bana kusa, kuma babu kuwa a kusa da ita sai wannan ita kuma ba wani hali da ita ba, shiyasa abun yai tsamari haka, amman dai ina fatar zata samu lafiya?”

“Inshallah, zamu dorata a kan magani, kuma ba ma son ku yi wasa da shi, sannan za a rika yi mata gaji, akwai takardar magani, a je a nemo maganin”

Rukaiya ta mike tsaye tana kallon Kabir da dan tsoro da kuma faduwar gaba.

“Amman dai likita zata samu lafiya ko?”

Doc yayi murmushi.

“Zata samu lafiya Inshallah”

“Za a nemo maganin yanzu, amman likita akwai dakin da ake kai mutane na zaman mutum daya?”

“Eh akwai”

“Ina bukatar a kaita a can dan Allah”

“Okay”

Doc ya fada sannan ya fice daga gurin, Rukaiya ta matsa jikin kujerar Faruk ya zauna Sultan na jikinsa.

“Sannu Mama”

Ya fada cikin damuwa, sai ta sakar masa murmushi.

“Ka dawo? Ya jikin Sultan din”

“Da sauki sosai, magani suka rubuta masa, zan bar shi sai na siyo maganin tukuna”

“Aa Dady aa”

Sultan din ya amsa sa kansa yana kara rike Faruk.

“Ba wani garin zanje ba, dawowa zan yi, magani kawai zan yi ma Mama”

“To kaje da ni”

“Aa zaka zauna gurin Maman Safiya ko Mama Rukaiya sai su baka magani”

“Dady karka tafi ka barni Momy ta tafi bata dawo ba, kai ma sai ka dade kake dawowa”

Ya fada yana fashewa da kuka, sai Faruk ya rumgume shi yana kallon Nurse din data dawo.

“Likita yace za a canja muku daki”

“Eh”

“Okay, amman fa akwai tsada”

Ta fada tana murmushi saboda ganin yanayinsu kamar ba za su iya biyan kudin dakin ba, sai Faruk yai mata murmushi.

“Karki damu ko nawa ne a kai, tun da kika ga mun zo asibiti mai zaman kanta ai kin san mun shirya”

“Haka ne”

Ta fara kokarin cire mata drip din, wata Dattijuwa ce sanye da uniform din masu aikin asibitin ta shiga da Wheelchair, sai Nurse din ta rika Mama ita da Rukaiya suka zaunar da ita saman kujerar, Dattijuwar ta soma turata, sai Faruk ya sauke Sultan kasa ya karbi matar ya soma tura Mama, ita kuma Nurse din ta mikawa Dattijuwar files din Mama da drip din, Rukaiya na kokarin daukar Sultan da ya fara kuka sai ta rigata ta saka hannu biyu ta dauke shi.

“To yi shiru kyale Daddy, ya sauke ka?”

Sultan ya daga mata kai.

“Tafiya zai yi ya bar ni, ba zai dawo ba sai an dade”

“Saboda me?”

“Ni ma ban sani ba, Momy bata dawo ba, kullum Mama tana cewa zata zo bata zo ba”

“Miyasa bata dawo ba”

Ta tambaya tana dariya, ta kalli Rukaiyah.

“Ina mamansa? Ko ta...”

Sai kuma ta kasa karasawa, a tunaninta ta rasu ne kuma ba a son a fada masa ne.

“Tana nan”

Da mamaki Nurse din ta ce.

“Miyasa ba a kai shi gurinta? Ba a gari daya suke ba?”

“A gari daya suke”

Ta dan rage tafiyar da take saboda Faruk yai nisa da su sosai.

“Bata da lafiya ne?”

“Kina da son tambaya”

Rukaiya ta fada tana murmushi, ita ma murmushin tai ta gyara Sultan.

“Rabuwa suka yi ba irin wanda ake so ba, domin ta guje shi saboda ba shi da kudi wai ba zata iya zaman talauci ba, abun bakincikin kuma yar'uwarsa ce ta jini”

Nurse din ta tsaya cak tana kallon Rukaiya da mamaki.

“Da gaske?”

“Wallahi, kuma tun da suka rabu bata sake zuwa ta duba danta ba, shiyasa muma ba mu damu mu kai mata shi ba”

Ta kalli Sultan cike da tausayi kamin ta maida duban gurin mahaifinsa dake kokarin shiga corner.

“Amman ya kike da shi yaron nan?”

“Dan dan yayana ne, ni ce auta a gidan mu, shi ne Babba sai yayata da akai wa aure kwanakin baya”

“Allah sarki, ni kuma ni ce ta farko a gidanmu Babana yana so na sosai”

Sai duk suka saka dariya, sannan suka cigaba da tafiya. Sai da matar da duba dakin da babu kowa sannan ta shiga ciki Faruk ya bi bayanta, da kansa ya dauki mahaifiyarsa ya dorata a saman gadon, sannan nurse din da shigo tare da Rukaiya, sai a sannan ta sauke Sultan kasa Faruk ya kalleta.

“Wai daman daukarshi kika?”

“Eh mana so kike yayi ta kuka? Ka aje shi kana dutyn wata, ni ma ai dole na yi naka”

Faruk yayi murmushi.

“Mahaifiyata ce”

“To sannu mai uwa, Mama kina jin shi ko?”

Mama ta yi murmushi, Nurse din ta karbi Files din dake hannun Dattijuwar ta aje su a muhallinsu sannan ta shiga dorawa Mama drip.

“Ashe kana da karfi, dan dai na san kai ka dora Momy a nan”

Ta fada ba tare data kalleshi ba, sai yai murmushi ya kama hannun Sultan.

“Ke yanzu kya kalli majiyi karfi irina ki ce ina da karfi”

“Ji yadda kake magana kamar wani Jarumi, Ke yanzu kya kalli majiyi karfi irina ki ce ina da karfi”

Ta karasa tana kwaikwayar muryarsa har da wani yatsina fuska take. Murmushi yai, Mama ma murmushin take tana kallonsu.

“Rukaiya bani takardar maganin”

Rukaiya ta mika masa da sauri sai ya karba.

“Akwai abun da kuke bukata?”

“Eh zan je na fadawa Maman Safiyya an canja mana daki, kuma ta zo ta zauna da Mama zan je gida na dauko kayan shimfada”

“Okay zan taho da abinci idan zan dawo”

Kamin Rukaiya tace komai, Nurse din data gama daurawa Mama drip ta kalleshi.

“To sannu acici mala'ikun tauna, ita dai maganar kayan shimfida tai ba na abinci ba”

Da kamar mamaki Faruk yake kallonta, wata kila fuskar yara ta gani a nasa fuskarsa shiyasa take masa zolaya any how. Girgiza kai yai ya fice ba tare da ya sace cewa komai ba, sai ta bishi da kallo tana murmushi, bayan ya fice ta saka hannunta aljihu ta ciro karamar wayarta kalli Rukaiyah.

“Saka min number mu rika gaisawa ko?”

“Ai ba ni da waya”

“Kamar ke za a ce baki da waya?”

“Allah da gaske nake”

“To ki saka min number Mama ko wani wanda zan iya kiranki mu gaisa mana”

“Mama bata da waya yanzu, sai dai Ya Faruk”

“To saka min, idan na kira sai nace masa ya bani ke mu gaisa, Rukaiyah ko?”

“Eh”

“Ni kuma Sunana Ramla Isma'el”

“Allah sarki”

Ta karbi wayar ta saka mata number, sannan ta mika mata.

“Ni zan tafi gida na gama aikina na yau, sai kuma gobe”

“Okay to Allah ya kai mu”

Ramla ta kalli Mama

“Mama zan tafi Allah ya sauwake”

“Amin Ramlatu mun gode”

Ta juyo ta kalli Mama tana wara ido.

“Laa haka Mamana take kirana Ramlatu”

Mama ta yi murmushi, ta bita da kallo cike da burgewa har ta fice.

“Tana da far'a da son mutane”

Rukaiya ta fada, sai Mama tai murmushi.

“Ni ma na lura da haka, tana da saukin kai”

“Mama bari na tafi gida na dauko kayan kar rana da kara yi, gashi ko abun sallah ba mu da shi”

“To sai kin dawo”

Ta fice daga dakin, Mama ta gyara kwanciyar ta lumshe tana murmushi.

BATURIYA POV.

tun da ta shigo dakin take ta kuka taki ta fadawa kowa abun da yake faruwa, kamin safe idonta ya kumbura har bata gani sosai da shi. Tana yin sallah asuba ta koma ta kwanta wai ko zata samu tai bachin da bata yi ba jiya, amman ina damuwar abun da ya faru jiya ya hana ta rumtsawa ta rufe idon kawai amman babu alamar bachi ma a kusa da idon nata. Sai da ta gaji da kwanciyar sannan ta tashi zaune wasu sabbin hawayen na sauko mata, har kusan sha daya na safe bata fito daga dakin ba, kanwarta har ta shirya ta tafi makaranta. Ganin haka yasan Umma ta leka dakin tana kiran sunanta.

“Rafi'a Lafiya kike yau kuwa? Har rana baki fito ba?”

Baturiya ta daga ido daker ta kalli Umma, a lokacin ne hankalin Umma ya tashi domin fuskarta ta kumbura sosai idanuwanta ma sun ciko kamar an busa su. Zuwa tai ta zauna kusa da ita tana kallonta.

“Subhanallahi me ya same ki?”

Kamar tace bude baki ki fara kuka sai kawai ta fashe da kuka ta kwanto jikin Umma.

“Ba kuka zaki yi ba, bude baki ki fada min abun da yake damunki mana”

Sai da tai kuka ta gaji sannan ta share hawayenta ta soma magana cikin kuka.

“Umma Fahat din da nake fada miki na tsayar har na fada masa ya turo iyayensa ba zai aure ni ba?”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, saboda me?”

“Mahaifiyarsa bata so na...”

“Ko dai ta gano kin tana haihuwa ko? Abun da kike ganin kamar ba za su gane ba yanzu sun gano ko?”

“Ba su gano ba ai da ya min maganar, kawai dai daman can ya taba fada min tana kawo masa yan mata yace baya so sai da ya hadu da ni”

“To Allah ya sauwake, auren da uwar miji bata so ko anyi shi ba dadi yake ba, kuma duk yadda kike gani da tunanin zaki iya boye cewar baki tana haihuwa ba, ba zai boyu ba, saboda a garin nan kike kuma agarin nan kika haihu, mutane da tsegumi, ni sam bana ganin haka a matsayin wata dabara, ba mafita ba ce a gareki, daman kin ki fada gaskiya tun farko kamin tafiya ta yi nisa idan yaji zai iya ya auri a haka yau ala saba saurayi ya auri bazawara balle ki da idan ba an sani ba ba ma za ace kim haihu ba, kuma idan ma yace ba zai aureki ba miye na kuka kina haka da ke tsaye da kyau zaune da kyau”

“Umma ina son shi sosai, kuma kin ga yana da kudi ga shi saurayi kuma yaro, kuma yana so na, kara na auri wanda makiya da magulmata za su ji haushi, kin san halin dana fito fa, idan na auri wanda zan sha wahala ai ko Faruk sai ya min dariya”

“Masu kudin ai da yawa Rafi'a, nima bana miki fatan auren talaka a yanzu, ka fito gidan wahala kuma ka koma kana shan wata wahalar? Idan kika auri talaka ai Faruk da mahaifiyarsa ma dadi za su ji, aa Wallahi kara dai inda zaki huta”

“Ni ma haka nake so Umma shiyasa nake son na auri Fahat”

“Idan ma be auri ba, ai ba zaki rasa mai so ba, amman kya zauna ki yi ta kuka ki saka kanki a wahala saboda namiji? Kika haihu da Faruk ma kika rabu da shi balle wannan”

“Momy Wallahi ina masifar sonshi, idan ya rabu da ni zan shiga damuwa ”

“Ya fada miki ba zai aure ki ba ne?”

“Aa amman alamu ya nuna haka saboda mahaifiyarsa bata son auren, kuma yace idan ta dage ya rabu da ni zai rabu a ni”

“To tun wuri ki ki fada masa gaskiya, ba sai ya gano da kansa ba, ni daman tun da kika saka Aisha tai min maganar nan hankali be kwanta ba, domin ni ban ga abun boye boye ba, kara komai za ayi a fadi gaskiya a huta, amman na kyale ki ne saboda kin nuna kin fi son ki boye masa din, amman ni na san ko gurin Yayanki suka je ai dole zai fada musu gaskiya, ko da nace kar ya fada ba zai yarda ba”

“Amman Umma idan na fada masa yanzu zai iya kara zama silar rabuwa ta da shi saboda ban fada masa ba tun farko na boye masa gaskiya”

“Amman fa dole zasu yi bincika, musamman da kika ce mahaifiyarsa bata sonki, idan kika ba ayi binciken auren ba to auren yar Alhaji wane ne da Alhaji wane, isu isu masu kudi, amman idan mai kudi da talaka ne sai an yi bincike kuma kin ga ita neman aibinki take saboda bata son danta ya aureki”

Ta share hawayenta.

“Idan na fada masa ya ce ba zai aure ni ba fa?”

“Shikenan kin huta babu wani abun boye boye tsakaninku, kuma kina zaune wani zai ce yana so, gari da yawa ai maye baya cin kansa”

Ta sauke ajiyar zuciya da karfi.

“Ki daina wahalar da kanki a kan namiji, haka kika yi ta zaman nan a gidan Faruk kina cutar kanki, yanzu kuma kim fito zaki karawa kanki wani ciwon namiji? Ina dalili”

Umma ta fada tana jin haushin yadda Baturiya take ta hawaye. Share hawayenta tai.

“Zan fada masa, amman idan ta tabbata ba zai aureni ba zan shiga damuwa sosai Umma, saboda ina son Fahat”

Ta karasa cikin kuka.

“Yanzu dai tashi ki wanke fuskarki ki fito ki karya”

“Toh”

Ta amsa cikin kuka, sannan ta tashi ta nufi bandakin tana tafiya kamar zata fadi, Umma ta girgiza kai.

“Allaha ya dauke miki wannan jarabawa da kike sha akan maza, kin samu kin rabu da kaya yanzu kuma zaki daukowa kan ki wani sabon kuka, sai kace shi kadai ne autan mazan duniya”

Cewar Umma sannan ta tashi ta fice daga dakin.

AMINATU POV.

Tana gama wankan ta dauki tufafin data cire zata maida sai ta ji yana mata magana kamar ya san abun da take.

“Karki maida wannan tufafin”

Ta kallin tufafin dake hannunta.

“To akwai wani? Ai babu wani”

“Akwai mana”

“To ba ni”

“Kin rufe bandakin ya za'ayi na baki?”

Ta aje kayan hannunta ta matsa kusa da kofar ta kara gyara daurin zanenta ta bude kofar a hankali ta mika masa hannunta.

“To ba ni”

Tana jiran ta ji ya miko mata tufafin sai taji ya rike hannunta yayi sama da shi yana shafawa a fuskarsa, a dayan bangaren kuma yana kokarin tura kofar ya bude, tana dannowa da karfi sai ta danne hannunta a dole ta saki kofar ya bude yana murmushi.

“Wai ke sarkin wayo ko?”

Ta bata fuska ta ki kallonsa.

“Na rantse kin ma fi kyau da kika yi fushin nan”

Ya fada yana janyota ya fito da ita daga cikin dandakin, sai ta saka dayan hannunta ta rike tawul din kirjinta.

“Sake min hannu”

Ta fada a shagwabe, a maimakon ya sake ta sai ya mika dayan hannunsa ya kama dayan hannun ya rike yana kallon black skin dinki data jika da ruwa tana ta shining.

“Idan anki fa”

“Ba zaka kai ni asibitin ba?”

Ta fada idonta na cika da kwalla, a take ya saki hannayen nata ya rika kanta cike da kulawa.

“Zan kai ki mana, kan yana miki ciwo har yanzu”

Ta daga masa kai.

“Okay saka tufafin sai muje yanzu”

“Ba kace akwai sabo ba?”

“Babu wasa nake miki”

Ya juya ta koma bandaki sai ya sauke idonsa a kasa yana kallon bayanta.

“Fine girl...”

Ya fada da muryar da shi kadai zai iya ji yana murmushi, sannan ya koma sannan gadon ya zauna yana kallon kofar bandakin a idonsa yana auna yadda take saka tufafin, yana gama observation dinsa tana bude kofar ta fito, sai ya dauke kai yana murmushi ya mike tsaye, ya mika mata hannunsa.

“Zo ki saka Hijab dinki”

Ta matso kusa da shi, amman bata rika hannun nasa ba, sai ta hau saman gadon zata dauki hijab din, sai jin tai an kwanto ta baya ta, ya dora kansa saman bayanta ya rumtse ido, yana shafata da duka hannayensa.

“I Love So much”

Ya fada cikin wata kalar murya yana kokarin jan rigarta yai sama da ita, sai wayarsa tai ringing.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata

ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

A dole ya sauka saman jikinta ya mulmula gefe ya kai hannu ya dauki wayar.

“Leila”

Ya furta kamin yai picking. Ya kara a kunne ba tare da yace mata komai ba.

“Hello Baby”

“Ya akai?”

“Haba sai ka ce mai waya da makiyinsa? Ko da yake na san na maka laifi amman kai hakuri dan Allah, daman na kira ne na baka hakuri, kuma na ji idan mai sunan Momy na kusa na bata hakuri ita ma”

Talba ta kalli Aminatu dake kokarin saka Hijab dinta ya ce.

“Bata kusa”

“Okay idan ka dawo gida ina son ganinka, ko kuma ka fada min inda kake zan kawo muku abinci dan Allah”

“Bana tare da ita, na kai ta gidan Hajiya Laraba”

Ta yi wannan karyar ne saboda ya samu sallama, domin ya san anjima kadan Momy zata iya kiransa ta ce ya dawo da Aminatu gidan, ya kuma san Amintun zata iya cewa ba zata koma ba.

“Idan ma kana tare da ita, ni ba wani abun zan yi ba, domin na rumtse ido ban ga kyau a makanta ba, kana wani abu kamar kai ne mutum na farko da zaka fara saninta a ya mace, miye abun burgewa a auren macen da maza fiye da biyar suka kwanta da ita a lokaci daya? Har kake ganin kamar ka yi wani abun arziki?”

Ya tashi zaune ransa a bace.

“Leila ke baki san kaddara ba ne? Ba ki san kowa be isa ya wuce kaddararsa ba? Idan za a bata zabi kina tunanin zata zabi abun da ya same ta ne? Ko kuma ke zaben rayuwa kika yi aka baki?”

“Na san kaddara mana Talba, ai na san kaddara ce ta saka ka auren bazawara a matsayin budurwa, kuma kaddara ce ta saka ka auren da wasu mazan wulakantatu kaskantattu suka gama amfani da ita, mazan da ba su kai ma su wanke maka mota ba, kana ji da kanka kana dan Babban mutum amman ka auri mai kamar akuya wanda bunsura suka gama bibiya, shiyasa ai ka boye auren saboda ka san ba abun kwarai ka aura ba, kuma ka kasa yin bikin tarewa sai

boyun amarya kake, ko garkuwar da akai da ita waya san iya abun da suka mata...?”

“Look at you da farko kina magana kamar mai hankali kamar da gaske kin yi nadama, amman sai kishi da hassada yasa kika kasa rike kanki, hakan yana nufi ba zaki taba iya controlling kan ki da zuciyarki ba Leila, duka abubuwan da kika zano na riga ki saninsu, kuma a haka na ji zan iya zama da ita, kuma kin san minene, ko da rana daya ban tana jin ma tsane ta saboda wannan ba, and this should be the last time da zaki sake bude baki ki fadi wata mummunar kalma akan matata, kuma ya zama na karshe da zaki sake saka hannunki ki daki Aminatu, na rantse miki da Allah Leila kika sake yin daya daga ciki, sai mun samu matsala da ke matsala ta har abada, idon wanda baki taba mafarkin samu zamu ba”

Yana kaiwa nan ya yanke kiran yana jin wani irin tsanar Leila da be taba ji ba a rayuwarsa, domin duk tsabanin da suke samu ya kan ji ransa ya bace amman baya jin tsanar, sai dai a yau tsanarta yake ji a ransa fiye da kima. Ya saka wayar aljihu ya dauki keys dinsa sannan ya kalli Aminatu dake kallonsa hawaye na sauko mata tana murmushin da ya fi kuka ciwo. Takawa yai ya karasa kusa da ita ya rika fuskarta ransa a bace, ko be fada mata ba ta san abun da suka tattauna akai, domin ta fahimcin wani bangare na hirarsu.

“Tana nanata maka abun da ta fada min ne a dazun? Ba a taba jefata da wata kalma da nake jin kamar na kashe kaina na sake sabunta rayuwata ba irin kalmar da Leila take jefata da ita, ka fada mata ba da son raina komai ya faru ba, shim ita ba mace ba ce? Bata san zafin da mace take ji ba idan wani namijin ya keta haddinta ba tare da son ranta ba? Na sha wahalar rayuwa na samu yanzu na yantu amaimakon a tausaya sai kuma ya zama abun gori a gareni? Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ta fashe da kuka mai karfi, sai ya kurawa fuskarta ido yana jin wani sabon tausayinta na kara kama shi.

“Rayuwa tana cike da kalubale Aminatu, ba zaka taba zama 100% babu damuwa babu jarabawa ba, kamar yadda ba zaka taba zama 100% cikin farinciki da jin dadi ba, no dole ne sai an surka maka, kowa ye kai kuwa a rayuwa, sai da kaddararce kowa tasa daban. Ina son ki saka a ranki a duk lokacin da wani ko wata zai fada miki wata magana saboda ya muzantaki ko ya muzanta rayuwarki, ki saka a ranki, Talba yana nan kusa da ke, kuma ba zai taba gudunki ba, ba zai taba kyamarki ba”

Ya rumgumeta a kirjinsa, sai ta ji wata rahama da natsuwa da bata taba ji ba sun lullubeta, sai ta samu sa'ida a zuciyarta tana jin kamar damuwarta ta warke.

“Ko babu komai Allah ya hada ni da wanda ke damuwa da kukana”

Ta fada cikin kuka tana rumgume shi abun da bata saba ba. Sai yai murmushi ya sumbancin saman kanta.

“Kuma yake son ganin murmushinki”

Ya sake ta, ya rika hannunta suka fice daga dakin, sai da suka isa gaban motar ya bude mata ta shiga sannan cikinsa ya soma kuka.

“Kin ga kin hanani cin abinci ko? Kuma dan abun da na ke ta kwadayi ban samu ba”

Ya fada yayinda ya shiga cikin motar yai mata key, sai ta kalleshi ta soma masa magana cike da kulawa da muryar kuka.

“Me kake kwadayi kwai? Zan iya sake soya maka yanzu”

Yayi murmushi domin ya san bata fahimcin inda zancen nasa ya nufa ba.

“No zan siye abinci a hanya”

Ya mika mata bakinsa.

“Kiss me zan je na bude gate”

Ya sakarwa bakin nasa ido kamin ta sauke kai kasa.

“Ke fa nake jira”

“Ban iya ba”

“To kawo ni na miki”

Ta mika masa hannunsa.

“Baki na ce”

Ya fada cikin yanayin dake nuna har yanzu be gama hucewa daga kalaman da Leila ta fada masa ba. Ta kalleshi sai ta sauke kanta kasa, ganin zata bata masa lokaci yasa ya fita motar ya zagaya side dinta ya bude motar ya sumbanci bakinta sannan ya nufi gate din ya bude ya dawo cikin motar yaja ta suka fita waje, ya sake dawowa ya rufe gate din, sai kuma ya sake komawa cikin motar. Wannan karon be jira cewar ba ya kai hannunsa ya riko fuskarta ta sumbanci kumatunta sannan ya fara driving da hannu daya, dayan hannun kuma ya mika mata sai ta saka hannunsa cikin nasa, yatsunsa da nata sukai taraiya a gurin daya.

“Saka hannunki ki ciro min waya a aljihuna”

Ta mika hannunta inda aljihun yake ta saka ta ciro wayar, sai ya janyo hannunta ta dora sitiyarin motar.

“Rike haka nan karki saki kuka karki murda”

“Ban fa iya ba”

Ta fada a tsorace domin ganin take kamar hadari za su yi. Sai ya sumbanci gefen fuskarta dake kusa da shi.

“Na sani”

Ya saka dayan hannunsa ya cire password din wayar ya kira Ali ya saka wayar a speaker ya dora a cinyar sannan ya rike sitiyarin, ita kuma ta dauke hannunta da sauri tana jin tsoro.

“Ali kana gida har yanzu?”

“Haba sai ka ce dai kai? Ina asibiti ka. Shigo ne?”

“Gani a hanya dai”

“Okay sai kun iso”

Ya kashe wayar sannan ya kalli Aminatu dake kallonsa.

“Sarkin tsoro”

“To idan muka yi hatsari fa?”

“Shikenan sai na mutu sai ki auri wani”

Ya fada yana dariya, sai ta bata fuska ta sauke kai kasa tana jin kamar tai kuka. Murmushi yai ya cigaba da tukin ba tare da sake ce mata komai ba, lokaci lokaci take dagowa ta kalleshi sai ta kara matse hannunta a cikin nasa, murmushi yai ba tare da ya kalleta ba ya cigaba da tukin. Sai ya ya fara harabar asibitin sannan ya saki hannunta ya kalleta.

“Bude ki fita”

Sai ta leke fada, alamar ba zata rufe ba tana kallonsa da fararen idanuwanta da suka kara haska bakar fatar fuskarta. Murmushi yai ya bude side dinsa ya fita ya zagaya ya bude mata, sannan ta fito sai kallonsa take kamar yai ta fara ganinsa, matsawa yai da ita daga jikin motar sannan ya samu ya rufe kofar ya danna key din hannunsa sai ya kama hannunta suka shiga ciki. Kai tsaye office din Ali suka nufa, shi kuma ya rubuta musu takardar ya turasu gurin hoto tare da wata mata. A nan Talba yake labarta masa abun da ya faru tsakanin Aminatu da Leila. Ba laifi akan kan ya dan bawa Leila laifi amman kadan ta dayan bangaren yana ganin zafin kishi ne ya saka ta yin abun da tai, a office din Ali Talba ya hada tea ya sha da biscuits domin baya iya cin bread idan rana tai, shayin ma iyakarsa ta sha na safe wani lokacin ya kan da dare sai dai ba sosai ba. Bayan an dawo da hoton Ali ya duba komai sannan ya kalli Talba yana murmushi.

“Kanta ya samu matsala gaskiya, zata iya mantawa da kai”

Talba ya kalli Aminatu dake zaune a kujerar dake facing dinsa yana murmushi.

“Idan ta mutu ko? Domin ko mutuwa na yi bana jin Shalele zata manta da ni, sai dai idan ita ta mutu shi ma saboda ance ana manta komai”

Ali yayi murmushi.

“Toh yayi sarkin soyayyah, babu abun da ya samu kanta buguwa ce kawai kuma zata samu sauki soon”

Aminatu ta yi masa da kanta, sai Talba ya mike tsaye ya rika hannunta.

“Ta so muje”

“Gida zaka mai da ita?”

“Tace bata son can, kuma ka san Daddy ma ya kore ni yace ba mu sati daya mu tare a gidanmu”

Ali yayi murmushi.

“Ka ce Daddy ya maka abun da kake so kawai”

“Wallahi kuwa, amman duk da haka ba zan koma ba sai da amincewar Momy, domin ita ma uwata ce”

“Hakan na da kyau Allah ya bada sa'a”

“Ameen”

Aminatu ta zare hannunta daga rikon da Talba yai mata a hankali saboda ganin Ali ya taso zai rakosu.

“Ka ga ta ma fika kunya”

“To ni kunyarka zanji? Haba Malam”

Ali yayi dariya, ya rakosu har inda Talba ya aje motarsa, suna tafe suna hira har suka iso. Talba ya bude motar Aminatu ta shiga ta zauna ya rufe ta ya juyo yana magana da Ali.

“Ka yi magana da Madina?”

“No sai ranar Monday, zan kirata office dina na yi magana da ita”

“Okay, for Leila karka dauki abun nan da zafi sosai Talba kai ma kowane bangaren adalci, ita ma tana sonka kuma ta jin kishi dole tai abun da tai”

“Na sani, ba dan adalcin ba Wallahi ba zan aureta ba, a rayuwata ba ni da burin auren mace fiye da daya, kuma bana son fitinar mata kasan kuma Leila zata yi da kirkiro abubuwa kala kala”

“Haka ne, amman hakuri ake, mata sai hakuri”

Talba ya sauke ajiyar zuciya, sannan ya dauko masa zancen abun da Leila tai masa dazun data kira shi. Kalle kalle Aminatu ta fara yi sai ta hango farin mutumen nan da ya taba sace ta, shi ma ita yake kallo kasancewar farin gilashi ne, sai dai shi zare mata ido yake yana tsortata har ya shiga motar dake kusa da ita yai mata alama da tai shiru ta hanyar dora dan yatsansa saman bakinsa, sai gum kamar yadda ya umarce ta tana masa kallon tsoro har ya tashi motarsa yai reverse ya kama hanya, sai yai nisa ya kusa fita gate sannan ta bude motar ta fito da sauri.

“Wacan mutumen shi ne wanda ya sace ni”

Daga Talba har Ali kallon inda take nunawa sukai da sauri.

“What... ”

Talba ya amsa da karfi sannan ya zagaya da gudu ya shiga motarsa, sai Aminatu da fita daga cikin motar da sauri sai ya miko hannu ya rufe gambun yai reverse a haukace ya fisgi motar ya yana hawa titin da zai sada shi da gate din motar wacan mutumen na ficewa daga gate din. Ali kuma yai hanzarin koma ciki ya fadawa securities din ciki su fadawa na gate su rufe gate din su tare mutumen, amman ina kamin ya isa gurin ma har mutanen ya fice daga gurin. Aminatu kam komawa tai gafe ta tsaya ta rumgume hannayenta tana jin tsoro sai hawaye suka fara mata zirya, sai da ta soma tsawalla da yadda mutane ke kallonta sannan ta juya ta koma inda Talba ya shiga da ita dazun, da zimmar ta koma office din Ali sai ta kasa gane gurin, ta bace hanya. Hakan yasa ta nufi wani ward din da babu mutane sosai ta tsaya daga jikin kofar farko ta jingina tana hawaye sai tsoro take ji. Bude kofar akai Faruk ya fito rike da hannun Sultan, dan tsayawa yai kallonta.

“Lafiya?”

Ta ki ce masa komai ta kalli Sultan kawai ta juya ya koma gaban wata kofar ta tsaya.

‘Ko wani take nema? Ko kuma mutuwa akai mata’

Ya raya a zuciyarsa, be sake ce mata komai ba ya rika ja hannun Sultan zai wuce. Sai jikinta ka fara rawa wani irin tsoro da faduwar gaba suka taso mata sai jiri ya fara dibanta, fashewa tai da kuka ta sulale kasa idanuwanta suna son rufewa. Da sauri Faruk ya saki Sultan ya karasa kusa da ita sauri.

“Subhanallahi....”

Ta kalleshi da idanuwanta da suke daf da rufewa, sai ga wani duhu ya baibaye idon nata, daga lokacin me ta masa jin komai ganinta ya bace bat.

*** *** ***

Yanayin yadda Talba ya fito da motar saya securities din gate din hanzarin rufe gate din. Talba ya faka motar ya fito da sauri yana fadin.

“Bude min gate din nan wanda ya fita yanzu kidnapper ne nemansa muke”

Zuwa sukai suka rike Talba, saboda an kira daga ciki an ce su rufe gate din, a zatonsu Talba ne Wanda ake nufi domin shi ya zo a guje. Duk yadda ya so su sake shi sai suka ki har sai da Ali ya iso gurin.

“Ku sake shi ba shi ba, wanda ya fita yanzu mai 406 ash color”

Talba ya koma motar da sauri cike da fatar ganinsa, sai suka bude masa gate din ya hau baban titi kamar an koroshi sai kalle kalle yake wai ko zai ganshi, ba ankaro ba wata babbar mota ta bugi motarsa domin ya taho a guje babban motar kuma ta fito kan kwana, sai aka hankada motar Talba can gafe ta sake

bugun wata motar, shi kuma ya buge wasu masu babur suka fadi sai sitiyarin motarsa ya fito da karfi ya daki kirjinsa.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ya furta yana jin wata kalar azaba a kirjinsa, kamar an hura mata wuta a ciki, daga nan be sake sanin inda hankalinsa yake ba.

LEILA POV.

Ta sauke wayar cikin da bakinciki, har ita Talba zai sakawa sharadi saboda ta fadi abun da yake gaskiya akan Aminatu? Amman ba laifinsa ba ne laifin Momy ne da ta saka ta kira shi ta bashi hakuri, bayan kuma Daddy ya gama wulakantata ya saka ta bata hakuri. Ta cika bakinta da iska ya busar.

“Ko da yake Momy ta min rantsuwa ai, Allah kasa na iya rike kaina, kamin komai ya kallama”

Ya fada tana wurga wayarta kan gado.

“A yanzu ba ni da burin daya wuce ganin yarinyar nan ta wulakanta Wallahi, ji wai har wani kareta yake yana fada min magana, wai ni Leila”

Ta nuna kanta, can kuma ta fara shinshinar jikinta tana jin wani wari da bata san na miye ba.

“Me na taba haka”

Ta fada tana yamutsa fuka, domin bata san wani abu mai wari haka ba, kuma bata san ta taba wani abu ba balle tace shi ne. Da sauri ta cire tufafin jikinta ta daura tawul ta shiga bathroom tai wanka. Sai da ta gama wanka ta fito sannan ta daina jin warin jaban, sai dai ita bata san warin jaba ne domin bata ma san jaba ba balle ta san warinta. Sai da ta fara zuwa gaban madubi ta gyara jikinta sannan ta nufi wardrobe dinta ta dauko wasu tufafin ta saka, bata damu data daura dankwalin tufafin ba ta dauko wayarta ta fito dakinta zuwa dakin Momy. Wani kalar farinciki ne ya lullube ta ganin Hajiya Sadiya kusa da Momy suna hira.

“Mama Sadiya kin zo?”

Hajiya Sadiya ta kalli Leila tana murmushi.

“Ba dole na zo ba, Mamanki ta kirani tana fada min abu ba dadi? Ai tana gama fada min na shirya na tafi kauyen nan yanzu haka na ba ni wani maganin amman ya ce na tsakanin yarinyar ne da Talba, na tsakanin ke da Talba kuma sai kin zo da kanki”

Kamin Momy tace komai, Leila ta ce.

“Wallahi zan je, yaushe zaki koma Mama Sadiya? Saboda yarinyar nan ta ishe ni Wallahi, yanzu ma baki ji abun da yake fada min ba saboda ita har da rantsuwarsa”

Hajiya ta tabe baki.

“Ai ba a banza yake komai ba, shi kansa malamin ya fada min asiri aka masa yake ta faman hauka akanta”

Momy ta daga kai.

“Abun da nake ta fada mata kenan, amman ta ki ta gane, sai wani wuta wuta take, shi fa yanzu baya hayyacinsa, amman idan kika bi komai a sannu sai ya tafi yadda ake so, ba rantsuwa na miki sai na raba shi da yarinyar nan ba? Ai ki zuba ido ki gani”

“Na fada masa haka, yace zai yi farraqu tsakaninsa da ita, zai raba su rabuwa ta har abada, ko dazun da na tafi gurinsa sai da na jaddada masa haka, kuma ya ce min na saka ido kawai na yi kallo”

Cewar Hajiya Sadiya. Tsabar jindadi da murya yasa Leila ta rumgume Hajiya Sadiya cike da farinciki.

“Na gode Mama na gode”

Ta fada cikin farinciki marar misaltuwa.

TEAM Leila
TEAM Aminatu
TEAM Madina
TEAM Faruk
TEAM Baturiya

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Khadeeja Candy

Kamar wanda aka jefowa rai haka ta farko da karfi tana haki, but still dishe dishe take gani ga wani uban nauyi da kanta yai. Faruk da ya kusa kawai karshem ward din ya dawo da sauri yana kallonta.

“Sannu...”

Ta dago a hankali ta kalleshi amman bata iya gane fuskar waye, muryar kawai take ji, wani irin faduwa ta ji gabanta na yi.

“Sannu”

Ya sake furtawa yana kallonta, sai ta yunkura zata tashi ta kasa.

“Bari na dubo likita zauna nan?”

“Aa zzza... Zan iya tafiya”

Ta fada bakinta na rawa kamar yadda jikinta ma yake rawa, har Faruk ya mika hannu ya rikata sai tai saurin matsawa duk da kasancewar bata iya ganinsa da kyau.

“Ina da aure ni matar aure ce”

Saurin janye hannunsa yai daga rikon da yake da miyar yi mata.

“Zaki iya tafiya?”

“Eh zan iya”

Ta amsa tana dafa ginin gurin.

“Dan Allah kasan inda Office din Doc Ali yake?”

“Ban ma san waye Doc Ali a nan ba, amman bari na tambaya miki”

Ya juya ya koma dakin da Mama take, Maman Safiyya ta kalleshi.

“Faruk har ka dawo?”

“Daman ban yi nisa ba, wata yarinya ce ta fadi a nan, dan Allah dan zo ki rikata”

Maman Safiyya ta mike tsaye da sauri tana fadin.

“Subhanallahi ina take”

Mama dake kwance dagowa tai tana kallon kofar. Faruk ya fara fita Maman Safiyya ta bi bayansa da sauri, sai suka samu Aminatu a tsaye tana kallon ward din kamar mai tunanin yadda zata isa gurin. Maman Safiyya ta rikata da hannu biyu tana mata sannu Faruk kuma ya wuce gaba, a nan Aminatu ta samu kuzarin takawa Maman Safiyya na rike da ita, har suka fita daga ward din. Gurin da ta fito Faruk ya nufa ganin ya fi mutane wai ko a can za a samu wanda ya san office din Doc Ali, kusan duk mutanen dake kai da kawo idan ya tambaya cewa suke ba su sani ba, hakan ya saka ya nufi reception din inda nurses suke.

“Dan Allah Doc Ali muke nema”

Faruk ya tambaya, sai wata nurse ta nuna masa shi daga inda take zaune.

“Ga shi can”

Faruk ya juya ya yana kallon Doc Ali dake kokarin bude back seat nurse din dake gaban motarsa suka matso da gado da taimakon ma'aikatan jinyar aka fito da Talba suka dorashi saman gadon sannan suka shiga kofar emergency da shi.

“Ina ganin yana busy ne, ina ne office dinsa”

“Eh abokinsa ya samu hatsari”

Wata nurse din dabam da ba wacan ta farkon ba ta amsa masa. Wani irin amsawa gaban Aminatu yai sai ta juya tana kallon gurin duk kuwa da kasancewar bata iya gani sosai.

“Ina office din nasa yake da wanda ke nemansa nan sai a kaita ta jira shi?”

“Kabi ta can, kwana ta biyu zaka ga wani ward na yan haihuwa kusa da gurin akwai offices ko wane da suna a jiki zaka ga an rubuta sunansa”

“Okay mun gode”

Faruk ya fada sannan ya nufi gurin, Maman Safiya na rike da Aminatu dake ta kallon wajen Emergency, komai dishe-dishe take ganinsa sai dai jinta sarai yake, kalmar abokinsa ya samu hatsari ya shiga kunnenta kuma ya nemi guri a kwakwalwarta ya tsaya, takawa take amman hankalinta da tunaninta sun tsaya cak akan abun da Nurse din ta fada, zuciyarta sai bugawa take da karfi kirjinta na mata zafi marar misaltuwa. Kwatancen da akai ma Faruk shi ya bi ya isa kofar office din ya kai hannunsa ya bude sai yai arba da wani mutum zaune a office din yana operating system, sai da Faruk ya gaisa da shi sannan ya gabatar masa da Aminatu.

“Okay ta zauna a nan, Doc baya nan”

“Eh mun ganshi a waje ance abokin ya samu hatsari”

“Abokinsa?”

Mutumen ya tambaya yana kallon Faruk kamim ya kara da fadin.

“Subhanallahi”

Maman Safiyya ta mufi kujerar ta zaunar da Aminatu.

“Allah ya sauwake”

Aminatu tana son ta bude baki tace mata Amin kuma ta mata godiya amman ta kasa yin ko daya, saboda rikewar da zuciyarta sai bakinta ma yai nauyi sosai. Kusan a tare Faruk da Maman Safiyya suka fita, Aminatu ta zauna a gurin kamar hoto, numfashi kawai take fitar amman ko motsi kasa yi tai, mutumen dake zaune ya kalleta bayan ya gama abun da yake ya ce.

“Zan rufe office din”

Ta mike tsaye cikin rashin kuzari ta nufi inda take kyautata zaton kofa ce, da taimakon hannayenta ta fito daga office din ta dafa kujerar dake gefen kofar ta zauna, sannan mutumen ya fito ya rufe office din. Sai da ya kusa awa daya da tafiya sannan Doc Ali ya shigo ward din kana ganinsa kasan yana cikin damuwa da tashin hankali marar misaltuwa, rage tafiya yai hango Aminatu zaune ya san shi take jira ko Talba, for the first time ya ji ta bashi tausayi. Taya zai fada mata Talba ya samu hatsari? Ta ma zata ji. Sai da ya kawo kusa da ita sannan ya sauke ajiyar daya gagara saukewa tun lokacin da abun ya faru.

“Aminatu”

Ta kasa amsawa, sai kallonsa take ta kai hannu ta fara murza idon ko zata ganshi daidai. Hannu ya kai ya murda kofar office din sai ya ji a rufe, juyawa yai ya koma inda ya fito be dade ba suka dawo tare da mutumen dazun wanda ya rufe kofar.

“Yauwa yarinyar nan tun dazun take jiranka, har na gama abun da zan yi na ce ta fito na rufe office din”

“Karka sake yin haka, ka barta a ciki office din Matar Talba”

“Ai ban santa ba ne shiyasa ko shi... ”

Mutumen be karasa ba, Ali yai saurin dafashi ya girgiza masa kai ta sigar da Aminatu ba zata gani ba. Sai da aka bude office din sannan Ali ya kalli Aminatu.

“Ta so ki shiga ciki”

Ta mike tsaye ta nufi kofar ta shiga a hankali tana dafawa har ya isa gurin kujerar data zauna dazun ta sake zaunawa, sai ta bishi da kallo, so kawai take ta ji ya mata magana, shi kuma ya gagara hada kalmomin da zai fada mata komai.

“Bari na kira Mama ta zo ta tafi dake, amman kina jin wani ciwon ne?”

Ta lumshe ido.

“Ko baki da kuzari ne?”

Nan ma bata ce masa komai ba.

“Aminatu”

Ta bude idon ta kalleshi.

“Kina jin wani abu ne?”

“Talba...”

Ta furta daker tana jin wani abu na sokar kirjinta.

“Ya tafi ya kai report gurin police ne, shi ya ce na kai ki gidana, zai je can ya daukeki”

Ta sauke kai kasa ta kasa cewa komai, kuma ta masa yin kuka ta kasa yin wani kwakkwaran motsi, ta rasa wani tunani zata yi. Yana kallonta yana dialing number matarsa har kiran ya shiga, sai ya mike tsaye ya nufi windows hawaye na cika idonsa.

“Ki zo yanzu yanzu office dina ki tafi da Aminatu, Talba ya ce akai ta can kamin ya zo”

“Lafiya?”

“Lafiya Kalau, ta ga wanda yai kidnapping dinta ne kuma ta fada masa to ya bi sawun mutumen ne”

“Okay, gani nan, zuwa”

Sai da ya share hawayensa sannan ya juyo ya zauna saman kujerar ya fara ya kulle bakinsa gam, can kuma ya mike tsaye yana dialing Number Kabir ya fice daga office din. Sai da yai nisa da office din sannan ya amsawa Kabir.

“Kana ina?”

“Gida”

“Zaka iya zuwa Asibitin nan yanzu?”

“Miya faru?”

Ali ya kai hannunsa ya shafa kansa hawaye na sauko masa.

“Bana son na fada maka abun da zai tada maka hankali, saboda bana son hankalin yan gidanku ya tashi musamman Leila”

“You can tell me”

“Talba ya sami accident, and mun yi duk iya kokarin da zamu yi mu har yanzu be farka ba?”

Kabir dake zaune Garden ya mike tsaye da sauri Laptop din dake jikinsa ta fadi kasa.

“How Ali how?”

“Aminatu ce ta ga wani mutum tace shi ne wanda yai kidnapped dinta, sai ya shiga motar yabi bayansa bayan mutumen ma yayi nisa, shi kuma ya fita da gudu mutanen da suka san abun da ya faru sun ce babbar mota ce ta buge shi, shi kuma ya bugi wasu masu babur, ni kuma na bi bayansa ko da na isa hatsarin har ya afku daker muka samu ciroshi cikin motar saboda tarin motar ya danne masa kirji, jini sai fito masa yake ta baki da hanci, mun kasa dawo da numfashinsa Kabir yana raye amman ba numfashi”

Kabir ya kashe wayar ya fito da gudu ya nufi part dinsa ya dauki keys dinsa ya fito ya shiga motarsa yana mata key ya yai reverse kamar mahaukaci ya har wani hayaki ke fita, horn din saya danna yayi goma lokaci daya, da gudu suka bude masa gate din ya dauki hanyar asibitin.
Ali na jin Kabir ya kashe wayar ya daga kansa sama yana kokarin ganin be yi hawayen da suka cika idonsa ba su zubo ba, sannan ya sauke kan ya juya ya koma office din. A tsaye ya samu Aminatu tana kallon kofar office din kamar tana jiran shigowarsa.

“Kin gaji da zaman ne?”

Ta kasa cewa komai, sai dai ta koma ta zauna tana murzar idonta.

“Ko wani abu ya samu idonki ne?”

Ta daga masa kai kawai ta kasa cewa komai, kujerarsa ya nufa ya zauna yana kallonta, sai tausayinta ya kara kama shi. After like five minutes Kabir ya turo kofar office din ya shigo da saurinsa hankalinsa a tashe.

“Ina yake”

Ali yayi saurin kallon Aminatu sannan ya mike tsaye ya nufe shi.

“Could we talk outside?”

“No Ali wannan ba magana ce da za a rufe ba, just ka fada min ina dan'uwana yake? Transfer za a masa zuwa wata asibiti”

“Muna da dukan nin abun da asibiti, idan har muka kasa yin wani abu wace asibiti kake tunanin zaka kai shi duk fadin garin Gusau?”

Kabir ya shafa kansa ya lumshe ido ya bude, zai yi magana sai suka ji Aminatu ta fashe da kuka jikinta ya shiga rawa sosai.

“Ka gani ko? Shiyasa nake shakkar fada maka, kai kanka ka kasa rike kanka yanzu ka zo nan ka tashi hankalinta”

Kabir ya juya ya fita yana lasa wayarsa sai Ali ya bi bayansa.

“Wa zaka kira?”

Ali ya tambaya bayan ya rufe kofar office din.

“Daddy mana”

“No you can't do this Kabir, kasan yadda Daddy yake son Talba zaka tayar masa da hankali ne kawai, miyasa kake abu kamar mace?”

Sai da wayar ta fara ringing sannan tunanin yadda Daddy zai ji ya zo masa, a dole ya yanke kiran ya juya da sauri ya nufi hanyar daga ward din, Ali ya bi bayansa. Ali ya rigashi isa ICU din, likitoci biyu dake tsaye kan Talba suka kalli Ali.

“Ya motsa?”

Ali ya tambaya, sai dayan ya amsa masa da sauri.

“No, but he is still alive”

Ali ya girgiza kai yana jin kamar ya dora hannu akai yai ihu, daya daga cikin nurses din da suke tare da Docs din ta kalli Ali da ke cikin tashin hankali ta ce.

“Doc be kamata ka shigo a cikin wannan yanayin ba”

“I know”

Ya fada jikinsa na kara mutuwa, juyawa yai ya fice daga ICU din, Kabir dake tsaye bakin kofar ya juya ya fara safa da marwa. Kamin ya juyo ya kalli Ali

“Hoto ya kamata masa yanzu, maybe jini ya taba wani guri ne a jikinsa ko zuciyarsa, maybe sai an kwashe jinin zai samu farfadowa, transfer za a masa zuwa asibitina”

Kabir na rufe baki Talba yai tari da karfi sai jini ya cika Oxygen din dake bakinsa, da saudi suka cire suka zubar da jinin.

“Alhamdulillah”

Daya daga cikin likitocin ya fada da karfi, da sauri Ali ya juya ya koma ciki, ya karasa gurin Talba cikin farin ciki. Sun kusa awa daya a dakin sannan suka samu komai ya daidaita, likitoci biyu suka fito daga dakin tare da Ali. Sai da suka fito sannan Kabir ya kira Momy ya fada mata a kokarinsa na kwantar mara da hankali yake fada mata cewar komai ya zo da sauki. Sai dai hakan be saka ta iya rike kanta ba saboda tashin hankali sai ta fara kuka. Kabir na jin haka ya kashe wayar ya Kalli Ali dake tsaye yana kallonsa with shock.

“Ka kira kawai ka tada musu hankali?”

“Dole ne ai za su sani, kuma tun da har hana raye, komai mai sauki ne”

Ali ya dauke kai cike da jin haushin abun da Kabir yai ya fice daga gurin, tura kofar Kabir yai ya shiga ya zauna gurin dan'uwansa.
Ali ya nufo Office dinsa, yana shigowa sai ya samu Aminatu tare da matarsa Haulat tana bawa Aminatu hakuri akan kukan da ita.

“Doc ban san abun da ya faru ba, sai kuka take, kuma na yi na yi da ita ta taso mu tafi ta ki saurarata ma”

Ali ya kalli Aminatu.

“Ki kwantar da hankali yana can kwance ya samu farfadowa daga suman da yai yanzu haka bachi yake ma”

Bata ji ce komai ba kuma bata fasa kukan da take ba, jikinta da muryarta sai rawa suke sosai.

“Miya samu Talba?”

“Accident yai amman dai da sauki sosai gaskiya, domin ya farfado”

“Subhanallahi Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un garin ya?”

Ali ya labarta mata a abun da ya faru sannan ya kara da nasa labarin saboda ya kwantar da hankalin Amina.

“An yi arziki sosai, kuma yana farkowa sunan Aminatu kawai yake kira sai da muka, masa allurar bachi sannan muka samu salama”

Fadar hakan be saka Aminatu ta daina kuka ba, a tunaninta yana fada ne kawai saboda ya kwantar mata da hankali ba wai dan haka din ta faru ba. Tissue ya dauka ya mikawa matarsa ta zara ta mikawa Aminatu.

“Share idonki sai ku tafi gida, Maybe anjima da dare ya farka sai a dawo dake ki ganshi, Haulat ki ja ku tafi Momy tana nan Zuwa saboda Kabir ya fada mata, kuma idan ta zo zata iya blaming din Aminatu, Talba kuma ba zai ji dadi ba idan wani abu ya faru”

“Haka ne gaskiya, tashi mu je Aminatu”

Ta mike tsaye rike da tissue ta kasa share hawayenta sai dai ta rage sautin kukan da take, har yanzu tsoro take ji ji take kamar Ali yana boye mata ne kawai, waya sani ma ko harbeshi akai saboda ya bi bayan wacan mutumen. Haulat ce ta zari wani tissue ta goge mata fuskarta sannan ta rika hannunta suka fice daga dakin zuwa inda ta faka motarta, suna tafe tana yi ma Aminatu kalaman da za su kwantar mata da hankali har suka isa gurin motar ta bude mata ta shiga sannan ita ma ta shiga mazaunin direba tai ma motar key.

Sai da Ali ya tabbatar sun yi nisa sosai sannan ya dauki wayarsa dake kan tebur ya kira Leila, haka wayar tai ringing har ta tsinke ba ayi piciking ba, daman kuma he expect that indai har Momy ta fada mata abun da ya faru, ita kanta Momy ya san tana bukatar kalaman da za su kwantar mata da hankali a yanzu balle kuma Leila. Mikewa yai tsaye yana sake kiran number nan ma ba a daga, sai yai deciding ya kira Madina.
He got lucky ringing biyu Madina tai picking ta amsa sallamar da yai mata murya kasa kasa.

“Wa'alaikassalam, Doc Ali”

“Na'am ya gida”

“Alhamdulillah”

“Madina wata alfarma nake son ki min please, na san ke da Leila kun samu misunderstanding, ko kuma na ce ke da Momy, but Leila need you the most tana bukatar wanda zai kasance tare da ita a yanzu ya kwantar mata da hankali”

Madina ta aje kofin ruwan dake hannunta da sauri tana tambayar Ali.

“Miya faru?”

In brief ya labarta mata abun da ya faru, sai ta dafe zuciyarta ta fashe da kuka mai tsanani.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, Dan Allah yana raye?”

“Yana da rai, amman yana cikin mummunan yanayi gaskiya, but Alhamdulillah tun da yana da rayuwa”

Ta rumtse ido ta kai hannu ta rufe bakinta sannan ta yanke kiran ta mike tsaye ta fara kai da kawo a kitchen din idonta tap da hawaye.

“Duk ni na ja komai”

Ta sadda kai kasa hawayen suka sauko mata.

“Na jefa rayuwar mutane cikin hadari, kuma na jefa rayuwata”

Ta durkushe kasa ta fashe da kuka marar sauti.

“Dubi abun da ya same shi, all because of me”

Ta zauna a gurin tana wani irin kuka mai taba zuciya. Sai kuma tai saurin mikewa tsaye ta share hawayenta ta fito daga kitchen din da sauri ta nufi dakinta, mayafinta kawai ta dauko sai key motar ta fito rike da wayarta ta fice daga falon ba tare data sanar da kowa ba. Motarta ta shiga ta tai mata key tai reverse ta fice daga gidan tana driving tana kuka har ta isa asibitin. Tsakanin asibitin da gidansu tafiya ce da ba zata wuce minti biyar ba, tsakanin unguwar su Momy da asibitin tafiyar 40 minutes hakan ya saka ta riga su kawowa. Number Ali ta kira yana picking ta ce

“Talba yana ina?”

“ICU kin shigo ne”

Bata bashi amsa ba, ta kashe wayar ta nufi gurin daya fada mata, sai da ta isa bakin kofar sannan ta fara tafiya a hankali kamar mai jin tsoro gabanta sai faduwa yake hawaye na sauko mata, hannu ta kai a hankali ta tura kofar dakin tana hade yawu sannan ta juyo ta kalli bayanta ko zata ga wani. Juyawa tai ta shiga cikin dakin dankwalinta na sauko daga saman kanta zuwa kafadarta. Da farko ta yi zaton zata samu Leila a dakin, sai tai arba da Kabir zaune kusa da Talba, wani irin tausayinsa ne ya kara kama kamata, domin kana ganinsa kasan yana cikin mawuyacin hali. Hawaye da suke sauko mata ne suka cigaba da aikinsu, sai ta juya a hankali zata fice without making any sound.

“Madina...”

Kabir ya kirata sai ta tsaya cak, ta kai hannu ta share hawayenta sannan ta juyo tana kokarin hana wasu hawayen saukowa amman bata samu wannan hadin kan ba. Kallonta yake cike da mamakin dalilin kuka da hawayen da take at first ma ya dauka ko tare take da Leila. Har ta bude baki tai magana sai ta kasa saboda kukan daya ci karfinta, kalma daya idan ta fito bakinta kuka ne zai maye gurbinta. Juyawa tai tana kallon kofar da Momy ta shigo tare da Leila da Amal kowanensu fuska kaca kaca da hawaye, Leila ta nufi gurin Talba da sauri ba tare da ta kula da Madina ba, Momy ce ta tsaya kallon Madina da mamaki.

“You? Again ban gargade ki akan shiga lamarin Leila ba? Ban miki iyaka da ita ba?”

“Shiiiiiiiii Momy asibiti kike fa, kuma a gaban marar lafiya and you see his condition”

Kabir ya fada yana mikewa tsaye. Momy ta riko Madina da karfi kamar wanda ya kama barawo ta fito da ita daga cikin ta jefar da ita waje.

“Na gargade ki sau daya, wannan ya zama na biyu karki kuskura yin na uku, makira munafuka”

Kabir yayi saurin tare Momy daga marin Madina da take son yi.

“Get out of here”

“Momy Madina ce fa”

Kabir ya fada da mamaki.

“Na san ita ce ai”

Madina da kuka ya ci karfinta ta juya ta nufi kofar fita tana kuka kamar ranta zai bar jikinta, tana tafe tana hawayen mutane sai kallonta suke, wani bangare na asibitin ta nufa, inda daidaikun mutane suke zama, ta samu wani dakali ta zauna tana ta kuka marar sauti, dan tsagaita kukan tai jin motsin tsayuwar mutum a gefenta dankalin da take zaune.

AMINATU POV.

Tana shiga motar Haulat sai kuka ya yanke mata, sai dai bata ce komai ba har suka isa gidan, duk kuwa da irin kalaman da Haulat take mata na kwantar da hankali.
Da kanta ta bude motar ta fita ta tsaya jiran Haulat ta zagayo ta bude kofar falon. Kana kallonta ka san tana cikin damuwa, domin fuskarta ta fada ga idonta ya kumbura, yanayin yadda take kalle kalle ma kadai ya isa ya sanar maka akwai tunani a cikin kanta kala kala, har lokacin bata iya gani da kyau ga wani uban ciwon kai da take ji da nauyin jiki. Haulat ta isa bakin kofar ta saka key ta bude sannan ta juyo ta kalli Aminatu.

“Shigo ciki Aminatu”

Aminatu ta kalli kofar dakin a azahiri, sai dai a badini tunani take idan Talba ya tafi ya barta ya zata yi? Tana da mai mata gata a yanzu sama da shi? Haka zata yi ta rasa mutane masu muhimmanci a rayuwarta, bayan Inna da Baba da yan'uwanta yanzu kuma Talba?

“Aminatu?”

Haulat ta taba ta ganin kamar hankalinta yana wani gurin dabam, sai ta zabura ta kalleta.

“Na'am”

“Muje ciki mana”

“Amman Talba zai ji sauki dan Allah?”

“Inshallah, zai samu lafiya sosai ma, kawai abun da yake bukata addu'a”

Tafiyar ta fara sai ta ji ina ma bata fada masa mutumen ba! Da yanzu be fita da gudun nan ba, da duk hatsarin nan be afku ba, da yanzu ya kaita gidan Hajiya Laraba ko kuma gidansa. Sai da ta shiga cikin falon sannan wani sanyi da lullubeta sakamakon zazzabin da take ji da ya hadu da sanyin ac dake falon. A maimakon ta zauna saman kujera sai ta zauna masa ta rakube ta rungume hannayenta.

“Haba dan Allah ya zaki zauna kasa kamar wata marar gata? Tashi ki zauna akan kujera mana”

“Nan ma ya isa”

Ta fada tana yin kasa da kanta. Haulat bata sake ce mata komai ba gudun kar ta takura mata. Sai kawai ta nufi hanyar bedroom dinta, sai da tai kusan minti talatin da shiga sannan Aminatu ta tashi ta nufi kofar falon ta bude a hankali ta fito harabar gidan tana kalle kalle sai dai ba kallo irin na duba tsari da kyau gida ba, kallo na tunanin makomarta da rayuwarta ta baya. A dare daya rayuwa ta canja mata, a wacan daren komai na rayuwarta ya zama tahiri, a wacan dare ta rasa kowa da kowa nata. Kamar a yanzu komai yake faruwa haka take ji a cikin kanta abubuwan da suka faru a baya suka dawo mata sabbi suka tsaya mata a rai. Kuka kuma yai mata nisa, tana ta nemansa ya ki ziyartar idanuwanta, a maimakon kukan sai ta samu kanta da murmushin bakinciki.

Wai shakikanta a yanzu duk sun tafi sun barta, mutumen dake neman farincikinta kuma a yanzu ba shi cikin hankalinsa, zai dawo gareta ko kuma shi ma rasa shi zata yi? Bakincikin rashin uwa da uba dabam yake, wani kalar babi ne da ke budewa kansa sashe a zuciyar baya, karyar duk wani mai jini da jijiya ne ya fassara maka yadda ake ji matukar be tana rasawa ba. Wanda ya rasa uwa ya rasa abokiyar shawara, ya rasa mai tarbarsa da hannu biyu a ko wane irin hali, ya rasa wanda bata kyamarsa kuma bata yarda wani abun ya same shi. Wanda kuma ya rasa uba ya rasa babban jigo, bango majingina, gata mai share hawayen yayansa. Wanda kuma ya rasa duka biyun fa? Anya alkalami da takardu za su isa a bayyana irin bakinciki da damuwa dake tattaren da wannan rashin? Aminatu ta rasa duka kuma ta rasa majinginar da zata raba a tsakanin yan'uwanta maza ta ji sanyin rashin da tai, domin a jarabawar da aka hada mata har rasa su a ciki...

Ta sake yin murmushin bakinciki a karo na biyu tana ganin rayuwarta ta baya kamar a video, yan'uwanta da suke tsokanarta da mahaifiyarta da Mahaifinta da yake raye. Sautin muryarsu da hoton fuskokinsu sai suka dawo mata tana komai a zahiri, wannan karon murmushin da take ba na bakin ciki ba ne, domin wacan lokacin take gani a wacan rayuwar a cikin wacan kauyen da Yaya Sanusi ke tsokanarta shi da Yaya Rilwanu. Till Haulat touch her.

“Ke Lafiyarki?”

Sai ta yi firgigit ta juyo da sauri ta kalli Haulat kamar wanda ta farko daga dogon bachi, har hadiyar yawu take tana maida numfashi da karfi.

*Done with my test, In Shaa Allah, zamu cigaba kamar yadda muka saba. Fatar za a min afuwa Na san dai Masoyana basa fushi da ni *

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa Madina ta mike tsaye da sauri ta juya tana kallon Leila. Sai Leila tai murmushi.

“Da gaske? Kukan akan me?”

Madina ta dauke kai tana kara goge fuskarta. Leila ta rumgume hannayenta tana kallonta.

“Kin san me? Lokacin da Momy tace min kina son Talba ban yarda ba, karyatata na yi, ashe gaskiya take ta fada min amman hauka da kuma yardar da na yi da ke ta hana ni ganin haka, it's very unfortunate a yadda muka ta so tare da kuma irin yardar da na yi miki ace kin butulce min”

Madina ta yi murmushi idonta na sake cika da hawaye.

“Ke kanki idan aka tambaye ki ya akai kika kamu da son Talba yaushe kika fara sonsa, ba zaki iya fada ba, saboda kamuwa da so abu ne mai sauki kuma mai saurin shiga a rayuwa, Leila Talba yana da kyau da siffar da kowace mace zata so shi, yana kyau, yana da ilmin, yana da kudi, yana da tarbiya da family ma su asali, kuma ya iya kwalliya, so kamuwa da son Talba abu ne mai matukar sauki, kin san mai wahalar?”

Leila ta ki ta amsa tana mata ma Madina wani shegen kallo na tsana, Madina da hawaye suka gama wanke mata fuska ta cigaba.

“Fitar da so a zuciya, musamman ace ya zauna a inda ba muhallinsa ba, Leila na yi ta jihadin yakar Soyayyar Talba a zuciyata amman na kasa, a duk lokacin da na yi unkurin haka maimakon na samu nasara da kwarin guiwa, sai sonsa ya kara a zuciyata, ina yawan fadawa kaina cewar be kamata ba, amman zuciyata sai ta nuna min ita abun da take so kenan”

Ta karasa tana kai hannu ta taba zuciyarta, sai kuma tai kasa da kanta hawaye na sauko mata.

“Shi ne kawai hujjarki? Na raina wayonki Madina, taya zaki tsaya a gaban idona kina fada min yadda kike son mijin da kika san an saka min ranar aure da shi? Ashe ki ji kunya ba? Miya kawo ki nan? Waya fada miki Talba ya samu hatsari?”

Leila na maganar tana kai hannu tana tura Madina. Madina ta kalleta.

“Ali ne ya fada min, saboda yana tunanin kina bukatar wanda zai kwantar miki da hankali a halin yanzu”

“Amman a maimakon ni, sai kika nufo Talba saboda shi ne a ranki. Let me warning you today Madina... Karki sake shiga rayuwata, bana son ma zuciyarki ta ayyana miki a rayuwarki, ki manta da wata alaka da ta taba shiga tsakaninmu ta abota, kuma aikin a kamfaninmu daga yau babu shi, daman ai Momy tace saboda ki samu kusanci da Talba ne kika aikata yanzu kuma na yarda”

Madina ta yi saurin rikota.

“Kar idonki ya rufe Leila, karki zuciyarki ta raya miki abun da ba shikenan ba, kar daga karshe ni da ke mu sauka a jirgin nadama”

Leila ta fisge hannunta.

“Nadama kam yanzu haka ina kan yi ta, na yarda da na yi da ke 100% na dauki sirrina na fada miki, har ya baki damar amfani da wannan abun da na yi kika kokarin tsorata ni, a yanzu na gano manufarki ta aikata wannan abun saboda ki lalata aurena da Talba, kuma haka ba zai taba faruwa, kuma ina gargadinki tun a yanzu Madina, ki daina abun da kike yi domin kina wasa da halshen wuta ne kawai”

“Kar dai ke ma kin yarda da zancen Momy? Kina jin zan iya aikata abun da Momy take zargina da shi?”

“Kwarai kuwa, ai ke ce mai wannan wasan boyan, kuma sake gargadinki ki daina domin akuya bata gasa da kura, Talba ya miki nisa kamar yadda kasa tai ma sama nisa. Babu wanda ya san wannan sirrin nawa sai ke Madina, dan haka karki kuskura ki ce zaki maida ni karamar yarinya”

“Amman idan lokacin da kuka aikata abun wani ya ganku fa? Idan akwai wani wanda ya samu labarin fa? Leila taya idonki zai rufe a dare daya ki rika min kallon makiyiyarki?”

“Saboda ke din makiyiyata ce, ba wannan kawai ba, har sace Aminatu da akai ke kika aikata Madina, kuma kika shirya komai ta yadda ba za a gane ba?”

“Me Aminatu tai min da zai saka na yi mata haka?”

“Saboda Talba ya aureta...! And if you're thinking the same akaina, kin yi kuskure karki kuskura ki jefa kanki a matsala, domin zan rusa rayuwarki na saka ki yi nadamar haihuwarki da uwarki ta yi, na shafe tarihinki a duniyar nan, Madina kina wasa da halshen wuta ba tare da kin sani ba”

Madina ta share hawayenta tana yi ma Leila kallon takaici.

“Ke ce kike wasa da wuta Leila, macen da kika san ta san sirrinki in and out ita kike tsaya a gabanta kina fada mata magana son ranki har kina zagin iyayenta?”

“To me zaki yi? Fadawa duniya abun da na yi? Won't change anything, kin san dai iyayena ba zasu taba yarda suna raye ba na tafi gidan yari, dan haka ki daina wannan wasan tun yanzu, ki sallame yan wasanki ki watsar da makamin, idan ba haka ba zaki gina ramen binne kanki da kanki”

Madina ta yi murmushi.

“Kina magana kamar kin sha wani abun maye, kisan kai fa kika aikata Leila, kika kashe tsohuwar da zata ji ba, ba ta gani ba, saboda muguwar zuciya irin taki, kuma kin bar yayanta da wahalar nemanta da tunanin dawowarta, me kike zato idan iyalinta suka san abun da kika aikata? A tunaninki Talba zai aureki idan ya san kin kashe Baaba saboda bakar zuciya? Idan ma Momy da Daddy sun goyi bayanki, duniya zata goyi bayanki ne? Kina ji a ranki kina da sukunin da zai barki ki yi yawo a cikin mutane kamar wanda bata aikata komai ba? Sai Human Rights da yan uwan matar su saka miki ido saboda kawai kina da uwa da uba a raye? Ko ba komai kin bata sunan mahaifinku kuma kin lalata rayuwar aurenki! Kin yi kuskure Leila, kuma ina gargadinki karki sake aikata wani kuskuren, domin shi kike kokarin yi a yanzu, gyara barna da barna, bana bukatar dukiyarki ko wani abu na ki, ya kamata ki san wannan, ashe ko idan har son Talba ne kawai abun da yake damuna ashe abu ne mai sauki daya kamata ki bi ta lala saboda samawa kanki mafita, idan ba haka ba sai na ruguza rayuwarki na lalata zancen aurenki”

Leila ta yi dariyar da ta fi kama da ta yake.

“Kuma a tunaninki hakan zai saka Talba ya fasa aurena? Noooooooo”

Madina ta taka daya zuwa biyu ta matso kusa da ita.

“Yes, na san Talba fiye da naki sanin, matukar ya ji wannan ba zai tana aurenki ba, and Yes Momynki da ke kanki kun yi gaskiya, ni na aika sakon da ake kawo miki, ni nake shirya komai, kuma tabbas saboda na tashi hankalinki ne na lalata zancen aurenki da Talba ba”

Wani kalar kallo Leila take yi ma Madina da mugun mamaki. Madina har ta juya sai kuma ta juyo ta nuna Leila da yatsa.

“A yanzu ma, ba fasawa zan yi ba, wasan ne zai sauya salo, domin umarni zan baki wanda ya zame miki dole ki bi, ina son ki fadawa Momy da Daddy cewar kin fasa auren Talba”

At first Leila ta ji abun kamar a mafarki, not just abun da Madina ta fada mata a yanzu even the whole conversation din ta ji kamar a mafarki ne ba gaske ba, taya Madina zata tsaya a gaban idonta tana fada mata irin wannan maganar?

“Madina ni kike fadawa wannan maganar?”

Leila ta tambaya tana nuna kanta with shock.

“An Fada miki, ni ba a yanzu kika gama fada min magana ba? Kenan idan wani ne ya shirya wannan abun ba ni ba yarda za ki yi, why not ki fara karyata kunnuwanki ki kyamaci abun a ranki? Idan har zan gwada yakar zuciyata na hanata son abun da kike so, ya kamata ke ma ki gwada yi min kawaici ko da sau daya ne, amman a maimakon haka sai kika manta da komai, babu amana a kawancen mu Leila. Kuma idan har zan rasa Talba ke kika fi cancanta da ki rasa shi, domin be dace da ke ba”

“How dare you look in to my eyes and tell me Talba be dace da ni ba? Da ke ya dace kenan? A yanzu na gane ke macece mai mugun son kanta Madina, shiyasa kika sace Aminatu, me kike idan Talba ya samu wannan labarin?”

“Ni ban sace Aminatu ba, kuma a lokacin da aka sace ta, daga ni har ke ba mu san cewar Talba ya aureta ba, and even if i did kina da wata ahauda da zata tabbatarwa duniya cewar na aikata? You better watch your mouth Leila? I'm not as nice as I used to be”

Tana kaiwa nan ta nufi hanyar da zata fitar da ita daga harabar gurin cikin bacin rai, har hade kafafuwa take kamar zata fadi. Leila ta hade yawu tana binta da kallo.

“A snake in the grass, a hidden enemy, we can not believe every one”

Ta juyo ta fara takowa zuwa cikin asitin har lokacin mamakin abun da ya faru be sake ta ba. Ko da ta dawo ward din ta samu Daddy a tsaye yana kallon Ali ransa a bace, Momy da Kabir na tsaye, Amal ta kwantar da kanta kafadar Leila Kabir har lokacin hawaye take.
Ajiyar zuciya Daddy ya sauke bayan Ali ya gama fada masa yadda komai ya faru.

“Allah ya sauwake, ina ita matar tasa take?”

“Na saka Haulat ta zo ta dauke ta ta tafi da ita gida”

“Saboda me? Ga kowa a nan, can ai hankalinta ba zai kwanta ba”

“Idan ma ta tsaya me zata yi masa ranka ya dade? Ni Wallahi bana kaunar ganin yarinyar nan, kalli halin da yake ciki saboda ita ne fa”

Momy ta fada cikin bacin rai, sai Daddy ya daga mata hannu.

“Aa karki zama marar tauhidi mana, duk wani abu da zai samu bawa an rubuta masa shi tun ba yau ba, ko da ita ko ba da ita ba, daman can an rubuto haka zai faru kuma dole sai ya faru, dan haka ki daina ma dora nata laifi kina kokarin kwace hanya, kuma dole ne a bata hakkinki domin matarsa, ta riga ta zama daya daga cikin iyalan gidan nan a yanzu”

“Shi kansa idan ya farka be ganta ba, ai ba zai jidadi ba, tun da tana nan lokacin da abun ya faru”

Kabir ya kara da na shi.

“Amman dai mu nan ai mun wadatar ba sai mun ta zo ba, tun da ba cire masa ciwon zata yi ba”

Momy ta fada tana jin wani tsanar Aminatu na kara taso mata. Sai Daddy ya kalli Kabir cike da jindadin kalaminsa domin Daddy yana son mutum mai tunani da fadar gaskiya ko aiwatarda ita, yana daya daga cikin dalilin daya saka yake kaunar Talba.

“Yes kuma ya riga ya aureta, ko ganin kika yi zai wulakantata be kamata ki kyale ba, domin a yanzu kamar Amana take a gurinkinsa da kuma mu iyayensa”

Momy ta dauke kai tana tabe baki ba tare da tace komai ba, ta kalli Leila da hankalinta yake wani gurin dabam kana ganinta ka san tunanin wani abun take.

“Ka dawo da ita a nan tare da mutane, zai fi can da zata zauna da tunani”

Daddy ya fada yana kallon Ali, sai Ali ya dan risina alamar girmamawa.

“Okay Daddy”

Ya amsa sannan ya ciro wayarsa ya fice daga gurin. Daddy ya juyo ya kalli Leila.

“Ki kwantar da hankalinki, babu abun da zai faru da yardar Allah”

Leila ta sauke kanta kasa, a cikin kalaman da Daddy yai mata last sentence dinsa kawai ta ji, domin har lokacin hankalinta yana can duniyar tunani. Momy ta fara takawa a hankali cike da kasaitar data zame mata jiki, tana tafe fana lasa waya tana fadawa yan'uwanta, sai da Daddy ya kara shiga ya duba Talba sannan ya fice.

AMINATU POV.

Rikota Haulat tai suka shigo falon, saman Cushion din falon ta zaunar da ita, tai mata kalamai masu kwantar da hankali sannan ta shiga kitchen ta dora girkin dare, sama sama take jefowa Aminatu hira saboda ta dauke mata hankali, amman Aminatu bata cewa komai har Haulat ta ci ta shude.
Kiran wayarta da ake ne yasa ta fito kitchen din da saurin ta nufi inda wayar take ta dauka ganin number mijinta yasa rai saurin picking, ta juya ta koma kitchen din tana amsa masa.

“Hello Doc”

“Na'am ya gidan?”

“Lafiya kalau ya mai jiki?”

“Alhamdulillah, Aminatu na tare dake?”

“Eh lafiya?”

“Lafiya Kalau, Daddy ya ce a dawo da ita, wai hankalinta zai fi kwanciya idan tana nan”

“Gaskiya kam, domin hankalinta a tashe yake a nan, bata cewa komai sai tunani take, har bata sani idan an mata magana sai an taba ba, abun ya shiga ranta sosai”

“Ai dole, ki kawo ta yanzu”

“Okay”

Ta fada sannan ta sauke wayar, tana kallon girkinta dake kan gas, sannan ta juyo ta fito kitchen din ta nufo inda Aminatu take zaune, ganinta ya saka Aminatu ta mike tsaye da sauri tana kallonta gabanta na faduwa daman tun da tai picking call din ta ji ta ambaci sunan Doc hankalinta ya tattara ya koma can.

“Kin yi sa'ar siriki Aminatu, Daddy ya ce a dawo dake asibiti wai idan kina ganinsa hankalinki zai fi kwanciya”

Aminatu ta daga kai da sauri daman abun da take nema kenan, sam anan bata jin zata iya samu natsuwa, kara a can tana kusa da shi ko da kuwa ba zata iya hana komai faruwa ba, zata fi samu sukuni ace tana ganinsa kuma ta san halin da yake ciki, tsabanin nan da tana zaune ne kawai amman hankalinta yana can. Haulat ta yi murmushi.

“Ni ma ai na fada masa haka, amman na san da Momy ce ba zata ce a kawo ki ba, kuma dan Allah komai Momy tai miki ko ta ce miki kar ranki ya bace, kar ma ki biye nata ki maida hankali gurin mijinki”

Ta daga kai.

“Wa zai kai ni?”

“Ni yanzu girki nake, kuma yara suna nan dawowa daga islamiya, amman ai zaki gane gurin ko?”

“Eh”

“Okay bari na kira Maman Walida na ji idan mijinta na kusa sai ya kaiki, domin Napep yake ja”

“Toh”

Ta amsa ta koma ta zauna tana jin kamar tai tsuntsuwa ganta a gurin. Haulat ta shiga contact dinta neman number Maman Walida, ta aika mata kira. Wayar bata wani dade tana ringing ba ta dauka da sallama.

“Wa'alaikissalam, Maman Walida ya gida ya su Walida”

“Lafiya Kalau Hajiya ya yau”

“Lafiya Kalau, dan Allah tambaya bake ko Abban su Walida na kusa, wata yarinya zai kai asibitin da Doc yake aiki”

“Eh gashi nan yanzu ma ya gama cin abinci, bari na masa magana”

“Okay”

Ta kalli Aminatu bayan ta sauke wayar.

“An yi sa'a yana gida, daman da maraice yake dawowa cin abinci idan ya tashi shago mun yi sa'a yana gida. Amman idan kin je karki fada cewar ba ni na kawo ki ba, zai iya yin fada ki ce ina kawo ki na aje ki na wuce saboda ina girki kuma yara za su dawo makaranta yanzu”

“Toh”

Aminatu ta amsa da sauri, sannan ta mike tsaye daga zaunen da take. Haulat ta koma Kitchen din ta duba girkinta, sai ga wayarta ta sake ringing.

“Hello Maman Walida”

“Na'am ya ce wai ta fito kofar gida yanzu zai fitar Napep din Titi”

“Okay”

Haulat ta fito kitchen din ta nufi dakinta ta dauko Hijab dinta ta nufi kofar fita daga falon.

“Zo muje”

Aminatu ta bi bayanta da sauri suka fice, har gurin gate din Haulat ta kaita sannan ta tsaya jiransa domin ba su tarar da kowa a gurin ba, after like five minutes ya fito kwararon dake gefen gidansu, domin gidansa yana cikin kwararon ne kasancewarsa mai karamin karfi ba kamar sauran mutanen unguwar ba. Yana daf da kawowa gate din wani tunanin ya zo ma Haulat tunawa da an taba sace Aminatu kar wani abu ya sake samunta a yanzu dalilinta ya san kuma ba saurara mata kowa zai yi ba.

“Ko dai na kashe girkin na kai ki da kaina, kar wani abun ya faru na shiga uku”

Ta bukata tana kallon Aminatu dake kallon napep din data karaso kusa da inda suke tsaye jikin gate din. Da sauri mai Napep din ya fito daga cikin Napep din yana kallon Aminatu irin kallon nan na mamaki. Aminatu ta gwalo ido tana kallonsa tare da kai hannayenta duka biyu ta rufe bakinta sai yawo take da kanta kamar wata tababbiya.

“Ya ya Bashir.... Ya ya....Bashir... Da gaske Yaya Bashir... Da gaske....”

Shi kam ya kasa cewa komai sai kallonta yake baki sake da mugun mamaki. Haulat na ganin haka ya bude gate din ta fisgo Aminatu ta saka ta ciki, sai Aminatu ta fara kokuwar kwace kanta tana kuka.

“Yayana ne....dan....uwa... Na... Na... Ne... Yayana..ne.... Ya Bashir.... ”

Ta kwala masa wani irin kira da mugun karfi tana tsalle.

“Kai rufe gate din nan”

Haulat ta fadawa mai gadinta, sai ya tashi ta sauri zai rufe gate din sai Bashir ya kwankwaso kofar gate din.

“Auta Auta Auta...”

Haka yake ta kiranta sai ta amsa daga can cikin gidan Mai gadin ya rufe gate din da karfi. Har sai da Bashir yaja baya da sauri ya koma cikin Napep din ya juya ya kwayar daya fito jikinsa na rawa.

“Wallahi yayana ne dan'uwana ne shi kadai ya rage min”

Aminatu tana kuka sai kokarin kwatar kanta take daga rikon da Haulat tai mata amman ta kasa.

“Ban yarda da wannan ba, ki bari idan na hannataki da mijinki ko ma minene sai ayi, amman yanzu kam wani abu na zai same ki ba ace Haulat ce”

Haulat ta fada sannan ta saketa ta nufi cikin gidan, kitchen ta shiga ta kashe girkin sannan ta shiga dakinta ta dauko keys din motarta ta fito ta bude motar tai mata key.

“Ki taso ki shiga motar nan na kai ki gurin mijinki idan ya farfado sai ayi wanda za ayi, amman ba a yanzu ba, idan kuma ba zaki je ba na koma na cigaba da girkina amman ba zan yarda ki ga kowa ba yanzu”

Ta fada da iyakar gaskiya, domin tsoro take kar wani abu ya faru, kai tsaye ba zata ce ta gamsu Mijin makociyarta Maman Walida da Aminatu suna da alaka ba, ba kuma zata karyata ba, domin gari da kamani sun nuna haka. Aminatu ta taso tana kuka ta nufo inda Haulat ta kunna motar ta bude front seat ta shiga ta zauna tana kuka.

“Dan Allah ki bari na yi magana da shi, dan Allah Wallahi dan'uwana ne”

“Aa ki bari idan kin tafi can ki fada musu”

Ta fada tana reverse din motar, wanda yai daidai da shigowar kira a wayarta da number Maman Walida, sai dai bata yi piciking sai ta aje wayar a gefe ta cigaba da tukinta har ta isa gate. Mai gadi na bude gate din sai ta hango Maman Walida da Mijinta tsaye da sauri ta saka motar lock ta yadda Aminatu ba zata iya budewa ba, sannan ta sauke gilashin motar na gefenta ana kallon Maman Walida.

“Laaa Wallahi Auta ce”

Maman Walida ta fada, sai Aminatu ta leko ta gurin tana kallon Yayanta.

“Yaya Bashir”

Ya karaso gurin motar da sauri yana kallonta idonsa na cika da kwalla.

“Aminatu, Auta Auta... Auta... ”

“Baban Walida dan Allah ku kwantar da hankalinku, yanzu zan kai yarinyar asibiti gurin mijinta, idan hankali ya kwanta a can sai ayi ta nan, babu inda zata je kawai dai yanzu bana son wani abu ya faru tana gurina ne ni kadai ba tare da sanin kowa ba”

“Mijinta kuma? Aminatu bata da aure...”

“Kai ne baka sani ba, yanzu dai hakura har na dawo sannan ayi komai dan Allah”

“Toh”

Ya amsa yana jin kamar ya saka hannu ya fisgota, ba dan ya san Haulat da mijinta farin sani ba, da babu yadda za ayi ya yarda ta tafi da Aminatu dake ta kuka tana son bude kofar motar ta fita faki budewa, zagaya yai gefen ta Aminatu take yana kallonta yana murmushin farinciki tare da yi ma Allah hamdala. Hankali Aminatu be kara tashi ba har sai da Haulat taja motar suka hau titi sai ta hau gaiye tana kallon Ya Bashir tana jin kamar ba zata dawo gareshi ba. Sai da suka yi nisa sannan Haulat ta dan kalleta.

“Da gaske yayanki ne?”

Aminatu ta daga mata kai da sauri tana hawaye sai matsar kukanta take kar ya fasa bakinta ya fito. Sai a lokacin Haulat take tuna cewar dan garin su Aminatu ne, da kuma irin hirar da suka sha ita da Maman Walida lokaci aka kai hari a garin, da yadda ta fada mata cewar yan kashe iyayen mijinta da yan'uwansa, ita kanta wasu iyayen nata an kashe su. Sai da suka shiga cikin asibitin sannan Aminatu ta share hawayenta, Haulat na yin farkin ya kira wayar mijinta ta sanar masa inda take. Be a dauki dogon lokaci ba ya iso gurin sai a lokacin ya cire motar daga lock ta bude ta fita ta bar Aminatu a cikin motar, magana tai da Ali ta fada masa abun da ya faru, sai ya bude bangaren da Aminatu take zaune ya lekota.

“Ya akai kika gane yayanki ne? Ba kin ce an kashe yan uwanki ba?”

“Shi kadai zai iya amsa min, dan'uwana ba zai taba bace min ba”

“Amman kin san a nan yake zaune?”

Ta daga masa kai.

“Amman ban san cewa yana raye ba, kuma ban san inda yake zaune a birnin ba”

Ajiyar zuciya Ali ya sauke, sannan ya kara fadada kofar.

“Fito muje ciki”

Ta fito kamar yadda ya bukata, sai ya rufewa matarsa motar yai mata sallama yai gaba Aminatu ta bi bayansa, tana tafiya kamar mai koyon yadda ake takawa gaba daya ranta a jagule yake, ta rasa abun da zata yi murna ko kuma? Abubuwa biyu mabanbanta sun same ta a lokacin daya. Kanta a kasa har suka isa ward din, sanin ba jituwa za su yi da Momy ba, yasa be kaita a inda suke ba tare da mutanenta da wasu yan'uwan Daddy da suka samu labarin abun da ya faru ta hanyarta suka taho asibiti. Sai ya kaita dakin da Talba yake kwance kai tsaye, duk kuwa da kasancewar ya san Leila tana ciki. Shi ya fara isa bakin kofar ya tura ya shiga sannan Aminatu ta shigo. Leila dake tsaye rumgume da hannayenta ga kalli Aminatu ta kalli Ali da mamaki.

“Kawo ta ka yi?”

“Daddy yayi umarni da haka, kuma a gabanki kin san kuma ban isa na ce aa ba”

“Ai sai ka amsa masa, amman ka share maganar a bayan idonsa, ta zo nan ta yi miye, har wanda be san yayi wannan shegen auren ba yanzu zai sani, abun kunya kalleta da Allah”

Leila ta fada tana nuna Aminatu. Aminatu ta kalleta da idanuwanta da suka yi ja ta ce.

“Ni na fi cancanta zauna kusa da shi sama da ke, domin ni matarsa ce ba budurwarsa ba, ko ba komai saboda ni komai ya faru, ashe kuwa na fi kowa cancantar zama kusa da shi”

Leila ta matso kusa da ita kamar zafa daketa.

“Ke ni kike fadawa magana?”

“Ba magana nake fada miki ba, gaskiya nake nuna miki wanda kika kasa gani, a rayuwata ban taba ganin wani mutum mai son wata mace tsakani da Allah ba kamar yadda Talba yake so na, ya san zai iya mutuwa ko wani abu ya same shi amman a haka ya bi bayan wanda ya sace ni, saboda kawai ya gane waye ya hukunta shi, Wallahi da zan iya da sai na cire masa ciwon nan gaba daya, musamman a yanzu da nake da labari mai dadi da zan bashi....”

Ta karasa hawaye na sauko mata. Wani irin bugawa zuciyar Leila take tana son matsowa kusa da Aminatu ta saka mata hannu Ali ya shiga tsakaninsu, shi kansa mamakin bakin Aminatu yake, he never thought zata iya irin wannan furucin.

“Leila karku tada fada a nan, Talba ba a kwance yake kina gani”

“Baka jin abun da take fada min, yar kauye da ita jahila, ko kunya bata ji ta tsaya a gaban mutane”

Yadda Leila take daga murya ya saka wata nurse shigowa dakin.

“Ke da kike da ilmin da wayewa me suka amfana miki? Me suka kareki da shi? Saboda ina yar kauye kina yar birni ba shi yake nufin ki mutum ba ce ni dabba, kuma ke ce ya kamata ki ji kunya kina zuwa jinyar mijin da ba na ki ba, tun da ba a daura miki aure da shi ba”

Leila ta kalli Ali tana girgiza kai.

“Sai na yi kasa kasa da yarinyar”

Nurse din ta rike ta tana kokarin fitar da ita. Ali kuma yana kokarin kwantar mata da hankalin.

“Dan Allah Leila ki yi hakuri aje sai ku yi nan asibiti ne kuma a kusa da marar lafiya, be kamata ba ki yi hakurin har ya samu lafiya tukuna please”

Ta fisge hannunta daga rikon da Nurse din tai mata ta fice daga dakin bayan ya harari Aminatu sai haki take kamar wanda tai fada da zaki. Ali ma kallon Aminatu yake da mugun mamaki, ashe tana da bakin maida magana haka. Be ce mata

komai ba ya fice daga dakin bayan ya fadawa Nurse din ita kadai za a bari ta zauna a dakin. Sai da suka fita sannan ta nufi kujerar dake kusa da gadon ta zauna ta saka hannunta biyu ta rike hannunsa daya ta matsar da kujerar ta kwantar da kanta jikin gadon tana kallon fuskarta.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

FAHAT POV.

Sai da ya gama karyawa sannan ya fito bangarensa, ya nufi bangaren Mahaifinsa. Da sallama ya shiga sai ya samu mahaifiyarsa zaune tare da Abbah tana masa hira, kallonsa take har ya zauna a kasa inda suke zaune su duka biyun.

“Abbah barka da safiya”

“Muhammad an tashi lafiya”

“Lafiya kalau”

Ya kalli Momy sai kuma ya yi unkurin tashi tsaye, sai dai lura da Abbah yayi da akwai magana a bakinsa ya saka ya dakatar da shi.

“Akwai wata magana ne Muhammad?”

“Wata kila karata ya kawo”

Momy ta fada, sai Fahat ya dawo ya zauna yana kallon mahaifinsa da fuskar damuwa.

“Abbah akan maganar aurena ne da yarinyar nan, yanzu haka ta fada min a gidansu ance ta fitar da miji ta fada min na turo”

“To akwai wata matsala ne?”

Abbah ya tambaya ganin yayi shiru be karasa ba.

“Momy ta ki aminta”

Abbah ya kalleta.

“Saboda me?”

“Bazawara ce fa yarinyar, haihuwarta daya”

Abbah was so confused.

“Bazawara kuma? Daman ba budurwa ba ce?”

“Karya tai masa, cewar ita budurwa ce, domin har yanzu be gano cewar bazawara ba ce sai yanzu da nake maganar nan, shiyasa na fada masa yaje ya bincike ta domin ba zamu yarda ya dauko mana yarinya ya kawo a family ba daga baya abu ya zame mana matsala”

“Kina da gaskiya, ba ma shi ba yaran yanzu ba wata doguwar tarbiya ce da su ba, sai ka ga yarinya karama tana shigewa manyan mutane saboda neman abun duniya”

“Shiyasa ai ko wacece zai aura sai na saka amin bincike akanta saboda kar a dauko mana mugun abu akawo mana a gida”

“Gaskiya ne, kuma ina ganin Muhammad kamar be dace ka auri bazawara ba a yadda kake da kurciyarka, kuma ace mace har ta haihu, kana saurayinka kuma auta a cikin mazan gidan nan”

“Amman Abbah ba haramun ba ne, kuma yarinyar bata da wata matsala ta rashin tarbiya, haihuwa ce”

“Kai yanzu kana jin zaka iya zama wanda ta taba aure? Abokanka yan'uwa da mutane duk zaka iya shanye irin kallon sa suke maka”

Cewar Abbah yana kallonsa shi kansa be yi na'am da auren bazawarar ba.

“Abbah ina sonta sosai Wallahi, akwai mata da yawa a gari da kuma cikin familyn nan, amman ban kamu da son kowa ba sai ita. Amman hakan ba zai saka na yi jayayya da ku ba, idan baku ra'ayinta zan hakura da ita”

Abbah yayi gyaran murya.

“Aa ba zamu hana ka abun da kake so ba, amman shi lamarin duniya ana bin komai a sannu, bana son soyayya ta saka ka yi abun da zaka yi nadama, kuma ba zamu so mu hanaka abun da kake so ba, auren bazawara ba haramun ba ne dan haka ba zamu hana ka ba, sai dai ina tabbatar maka da cewar ni ma zan yi nawa bincike idan na same ta da irin halin matan zamanin nan ba zan yarda ka aureta ba”

“Na yarda Abbah na yarda”

Ya amsa da sauri yana murmushi.

“To shikenan, yaushe iyayen nata suka ce a turo”

“Ba su saka rana ba, ta fada min ne cewar ance ta fitar da miji kuma ta fitar da ni, so ni take jiran na fada mata ranar da zan aiko”

“Okay tau zuwa karshen watan nan... Kamin lokacin In Shaa Allah, zan yi abun da ya dace”

Fahat ya kama hannun mahaifinsa da sauri ya rike yana murna.

“Na gode sosai Abbah na gode Allah ya kara girma”

Mommy kam hade rai tai kamar bakin hadari.

“Haba haba Alhaji akan me zaka goya masa baya ya auri bazawara yana yaronsa? Kuma mata har ta haihu daya dan Babban mutum kamar Fahat sai kace dai mata sun kare a duniya”

“Hajiya tun da har yana so, be kamata mu hana abun da addini be hana ba, ba mu sani ba ko Alheri ne, yanzu ba zamani ba ne da ake yin auren dole”

“Amman dai...”

Abbah ya daga mata hannu, sannan yai ma Fahat Umarni daya tashi ya tafi. Fahat ya tashi cikin farinciki ya fice daga falon. Sai da ya fita Abbah ya kalli Mommy ya ce.

“Idan mutum yana farin ciki da abu baka tsake masa wannan farincikin kai tsaye ko da kuwa illa ne a gareshi, kara kai masa nuna sa illar idan zai iya gani, idan kuma ba zai gani ba sai ka bishi da lalama har ya fahimci komai, amman a yanayin yadda yake a yanzu idan muka hana shi aurenta kai tsaye, zai rika kallonmu a wasu kalar iyaye da basa son farincikinsa, amman yanzu idan aka bashi dama idan ma akwai wata illar a tare da ita shi zai fara ganewa a hankali”

“Kana da gaskiya, amman idan ba a nuna masa hanya ba, so zai rufe masa ido ya kasa ganin komai, ko zancen zawarcin nan bana jin ya sani har sai da na yi nawa bincike na gano haka, domin daya sani da tun farko zai fara fada min, amman ka ga sai ta boye masa”

“Da ya gano hakan ai ya kamata yai yayi tunani akai, amman so ya rufe masa ido baya ganin wata illa ce a gareshi, wannan kadai ya isa ya nuna miki idonsa a rufe yake”

“Toh Allah ya sauwake, amman Wallahi sam bana kaunar aurensa da yarinyar nan ko kadan”

“Ki yi addu'a kawai, idan Alheri ne Allah ya tabbatar, idan kuma akasin haka ne Allah ya raba tsakaninsu”

“Amin”

Ta amsa tana mike tsaye ta dauke kwanunkan da suka ci abincin ta fice.

BATURIYA POV.

Ta tabe baki tana maida wayar a dayan kunnenta.

“Ramlee ni yanzu matsalar da nake ciki ma ta ishe ni, ba ta neman kudi nake ba”

“Wace irin matsala?”

Baturiya ta sauke ajiyar zuciya sannan ta labarta mata abun da ya faru tsakaninta da Fahat, amaimakon Ramlee ta tausaya mata sai kawai ta fashe da dariya.

“Fee'at kina bani dariya, kamae ba mace ba, iyayen na mu mata ma yanzu suna samun samari su saura balle ke da kike da kurciyarki? Haihu daya fa, kuma yaron ma ba a hannunki yake ba, to miye damuwarki a ciki? Ko cewa yai ya fasa aurenki ai ba wani abu ba ne, ke dai ki tara kudi kawai ki aje, ko tsufa kika yi kika ce saurayi zaki aura zaki samu Wallahi”

“Ramlee ba zaki gane ba, ni bana son wannan kazamar rayuwa, kuma kin ga gida tun ban je ko'ina ba am fara saka min ido”

“Baturiya ke ce baki iya abun ba, wata yar sana'a zaki samu ki fake da ita, ko kuma ki koma makaranta ki cigaba sa karatu kina fakewa da wannan kina sha'aninki yadda kike so, amman ki ce zaki daina tun yanzu me kika samu a ciki? Ni kaina sa nake da gida da mota naje makka na leka wasu kasashe ai bana jin na gama tarawa balle kuma ke da ko kan akaifa baki tara ba”

“Ni yanzu ba wannan ya dame ni ba, burina na samu miji na yi aure kuma babban mutum mai kudi, yanzu kuma na samu sai na bar wannan damar da wuce ni?”

“Toh sai miye? Ana lamarin duniya ake yin na kiyama fa, aa Wallahi karki ce zaki takura kanki akan soyayyar wani namijin banza, ke idan kika kware a lamarin nan fa har mutanenda kike mu'alama da su zaki iya aurensu”

“Aa ni dai ina son Fahat sai idan ban samu aurensa ba sannan zan hakura”

Ta sauke wayarta daga kunnenta ta duba kiran dake shigowa, sannan ta maida wayar kunnenta.

“Kin ga ma gashi nan yana kirana, yanke kiran zan kiraki anjima”

“Oh wato har ya fini muhimmanci, to ni yanzu ya zan yi da wannan mutumen da na yi ma alkawari”

“Ki sama masa wata mata, domin ni idan aurena da Fahat ya tabbata babu wani abun da zan sake yi, saboda dole ne na fara taka tsantsan da rayuwa”

“Yar wahala ina nan da ke zaki dawo kina rokon na maida ke ruwa”

Ramlee ta fada cike da jin takaici sannan ta kashe wayar. Ramlee na kashe wayar Baturiya ta maidawa Fahat kiran da yai mata bata yi piciking ba, wayar na fara ringing yai picking, sai yai shiru ba tare da yayi magana ba, haka ya saka gabanta faduwa sosai domin be saba yi mata haka ba.

“Hello kana jina”

“Ina jinki”

“An tashi lafiya?”

“Lafiya kalau, ya gida?”

“Lafiya Kalau, na ji muryar kasa kasa akwai wata matsala ne?”

Yayi shiru kamar ba zai ce komai ba, sai kuma yaja dogon numfashi ya sauke.

“Akwai abun da nake son mu tattauna da ke, kuma akwai abun da kika yi wanda ya bani matukar mamaki, domin na yi zaton komai da zai fito daga gurinki gaskiya ce kai tsaye”

Ta dafa kirjinta gabanta na mara faduwa.

“Akwai abun da na fada maka wanda ka bincika ka tarar ba haka yake ba Fahat?”

“Ba magana ce da ya kamata mu yi da a waya ba, zan shigo anjima”

“Ba zan iya jira har anjima ba, ka tayar min da hankali, dan Allah ka fada min ko ma minene, wata kila zan iya maka bayani ta waya ko kuma idan ka zo anjima din, ko kuma ka shigo yanzu”

“Safiya ce, zan shiga office yau idan na fito zan zo gida na same ki”

Yana kaiwa nan ya katse wayar, yana mata duk wannan abun ne saboda ta fahimci cewar ransa ya bace na boye masa zancen ta taba aure da tai. Ba dan yana tsananin sonta ba da wannan karyar kadai ta isa ta saka ya rabu da ita, sai dai soyayyar da yake mata ta hana shi aikata haka, sai dai bata rufe masa ido ta hana shi ganin laifinta ba. Safa da marwa ta fara yi a dakin tana ra tunani kala kala, gabanta sai faduwa yake.

‘Ko dai ya ji na taba yin aure ne? Ko kuma an fada masa an gan ni a gurin da be kamata ba ne? Ko kuma wani ne ya kai masa sukarta?’

Haka dai tai ta sake sake cikin ranta, ta kasa gane dalilin wannan furucin da Fahat yai mata. Gashi kuma ta kasa samun natsuwa, abun ka da marar gaskiya, hankakinta ya tashi sosai domin a yau ta ji shi a wani yanayi da bata saba jinsa ba. Ta san sun rabu cikin damuwa a jiya, sai dai damuwar bata kai kamar ta yau ba.

“To ko dai binciken da nake ganin kamar ba za ayi ba ya saka an yi masa ko kuma iyayensa sun gano cewar na taba aure?”

Wannan karon a fili tai tambayar, gaba daya ta kasa natsuwa. Sake kiran wayarsa, sai dai be yi piciking ba har wayar ta gaji da ringing ta yake, sake kiran tai sai da ta jera masa miss calls hudu tana kokarin sake yin na biyar ta ji. Ko sau daya a tahirin haduwarta da Fahat bata taba kiransa yaki dagawa ba sai wannan

karon. Ji tai kamar ta dora hannu saman kai fara ihu, jikinta har rawa yake nan da nan gumi ya kadyo karyo mata kamar wanda ke gaban alkali.

MADINA POV.

Sai da ta gama kukanta da bakincikin sa'insar da sukai da Leila sannan ta sake yi ma motar key ta hau titi tana kai hannunta ta zaro tissue ta goge fuskarta ta gyara hancinta.

“I promise myself this, ba zan jefa rayuwata a hatsari ba, kuma na kasa samun abun da nake so, daga karshe kuma ace ni ce zan fada a matsala”

Taja numfashi da karfi, ta kai hannunta ta sauke gilashin motar ta jefar da tissue din.

“Ya kamata Leila tai min sadaukarwa ai, ko da a munafurci ne, amman ji sai. Barazana take min, tana zagina ya kamata ta yarda da ni ko sau daya ne, amman idonta ya rufe”

Ta fada tana jin tsantsanar nadamar a abun da ta aikata.

“Na jefa kaina a halaka, miyasa na aikata tun farko? Hajiya ta yi ta gargadina amman ban ji ba, gashi tun ba ayi nisa ba, ban samu biyan bukata ba, kuma zan jefa kaina a halaka, kuma na saka Talba? Miyasa wani lokacin nake da son kai ne why?”

Ta fashe da kuka tana dukan sitiyarin motar. Kai fa girgiza tana jin wata masifaffiyar kaunar Talba na taso mata, ta rasa dalilin daya saka Talba ya kasa ganin kaunar da take masa, wata kila yana duba kusancinsu da tsakaninta da Leila ne, yes ta san abun kunya ne ace tana soyayya da shi, amman ai so be san wannan ba, ita kanta da son ya duba kusanci da kunya da be shiga zuciyarta ya zaauna ba har ya rufe mata ido ta aikata abun da ta aikata a yanzu. Sai da ta kusa isa gidansu sannan ta samu ta kukan da take ya tsaya mata, a inda ta saba aje motarta ta aje faka ta kwantar da kanta jikin sitiyarin ta lumshe ido, wacan daren take ta gani a idonta daren daya hanata samun sukuni saboda arba da tai da abun da bata yi zato ba, daren daya saka tunanin aikata abun da ta aikata a yanzu. Dagowa tai tana kallon harabar gidansu

“So babu ruwansa sa kyau, babu ruwansa sa asali, babu ruwansa da hali, babu ruwansa sa waye kai, babu ruwansa da kusanci, babu ruwansa da matsayi, shiyasa ba duba ni lokacin da zai jefa min son Talba, kuma be duba Talba ba ya jefa masa son Aminatu, yarinyar da ko a mafarki ban yi zaton zata samu kusanci da Talba har haka ba”

Ta girgiza kai tana lumshe ido, tana lasar bakinta daya bushe.

*** *** ***

“To laifin waye? Da baki sake mata fuska ba har ta ga damarki ta fada miki magana mai zafi haka? Kamar wannan yarinyar”

“Momy laifin Talba ne, shi ya nuna mata bana da wata kima a idonsa shiyasa har ta samu dama”

“Yanzu Talban ne a farke da take fada miki haka? Ke dai kin maida kanki wata sakarya, da an yi miki abu sai dai ki ce zaki daki mutum ,amman bakin san ki tsaya me, ki yi abun da ya kamata ba, haka kika dauki yarinyar nan kika maisa ta uwarki, wani sirrinki da Madina ta sani ni da nake mahaifiyarki ban san shi ba, gashin yanzu ta samu damar da zata juya”

Leila ta kalli Momy cikin fusace ta ce

“Momy idan kika ji irin maganar da Madina ta fada min yau sau mamaku ya kusan kasheki, ashe zargin da kika mata gaskiya ne, ita ce take aikata komai”

Da mamaki Momy take kallon Leila, sai dai ganin ba su kadai ba ne a gurin yasa bata zafafa tambayar komai ba, sai kawai ta tabe baki tana kallon Gwaggonsu da ta doso gurin, wato Hajiya Hanne wata kanwar Daddy wanda take zaman cousins a gurinsa.

“Ki bar maganar nan, idan mun koma gida zamu yi magana, ki iya bakinki”

Leila ta daga kai. Tana juyawa dayan side dinta ta kalli wandanda suke gefenta sai dai suna da nisa da ita sosai, yastinar hanci ta fara tana jin irin warin nan data taba ji a gida yana fitowa a jikinta. Mikewa tai tsaye fana fadin.

“Momy zan je gida na yi wanka na dawo”

“Okay, ki cewa Amal ba sai ta dawo ba, tun da likitoci sun ce kar a dame shi, bari sai gobe idan Allah ya kai mu sai ta zo ta duba shi”

Kai ta dagawa Momy tana yastinar fuska, domin ta tsani warin da take jin jikinta na yi duk da bata san na minene ba. Bayan sun da gaisa da Hajiya Hanne, ta karbi key mota a gurin Momy domin nata motar yana gida, sannan ta fice ba tare data koma dakin duba Talba ba, ba dan kuma bata bukatar haka ba sai dan bata son tai arba da bakar macijiyar, Momy ma yafe dakin tai saboda sanin Aminatu na ciki. Kamin ta isa gurin motar har da hadawa da dan sauri take tana jin kamar zata yi amai.

AMINATU POV.

Bachi ne ya dauke ta daga zaunen sa take tana kallon fuskar Talba. Bata farka ba sai da aka kira Magariba, shi ma ta hanyar Ali ne daya shigo dakin ya duba abokin, sai ya dan buga gafen gadon a hankali. Sai ta dago ta kalleshi tana mitsika ido.

“Tashi ki yi sallah ko kin yi?”

Ta girgiza masa kai, sannan ta mike tsaye ta tana kallon kofar fita kamar mai jiran shigowar wani.

“Ga bandaki can”

Ali ya nuna mata sai ta juya tana kallon inda saitin hannunsa yake, sannan ta nufi gurin da kofar take ta tura a hankali ta shiga, fitsari ta fara yi sannan tai alwala ta fito tana gyara Hijabinta. Da kwalinta ta cire ta shimfida ta kabbatar sallah, a sujidarta ta karshe ta rokawa Talba lafiya, Ali na cikin dakin har tai ta gama ta sake daga hannunta tai wata addu'ar ta shafa sannan ta tashi ta nade dankwalin ta rike a hannu, tana kallon Talba, kamar mai jiran wani bayani daga gurin Ali. Shi dai be ce mata komai ba ya juya ya fice daga dakin, ya san zuwanta ne ya hana Momy shigowa ita da Leila da adakin zai tararda da ita, wata kila Leila da Momy sun yi fushi ne shiyasa ko dakin ba su sake shigowa ba.
Hakan kuma ba karamin dadi yai ma Aminatu ba ko ba komai zata samu ta sake, ba kamar idan suna dakin ba. A inda ta zauna dazun wato saman kujera ta sake komawa ta zauna ta kwantar da kanta jikin Talba tana cigaba da kallon fuskarsa, labari ne cike fal a cikinta so take ta fada masa ta ga Ya Bashir amman ba dama, tun da baya cikin hayyacinsa. Lumshe ido ta yi tana maida numfashi a hankali, tunanin fadan da sukai da Leila dazun ya dawo mata, sai ta turo baki tana jin tsanar Leila na karuwa a ranta. Ji tai ana taba kanta dake cikin hijab, da sauri ta bude ido ta juyo ta kalli Talba gabanta na bugawa da sauri. Murmushin karfin hali ne shimfide a fuskarsa yana lumshe ido yana budewa, kamin ya saka dayan hannunsa ya cire Oxygen din dake fuskarsa. Aminatu ta mike tsaye da sauri tana zaro ido tana jarfar da hannu alamar jindadi sannan ta rumgume Talba daga kwance da yake.

“Alhamdulillah...”

Ta furta cike da annashuwa da farinciki marar misaltuwa.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Ya dan yi yar kara, sai tai saurin daga daga jikinta idonta na cika da hawayen farinciki.

“Sannu Sannu Sannu, bari na kira likita”

Ta juya da sauri, sai yai hanzarin bude idonsa ya rika hannunta da hannunsa na hagu. Tana jiyowa ya girgiza mata kai alamar aa, sai ya sake lumshe ido. Tsoro ta ji ganin ya rufe idon duk da, duk da kasancewar yana rike da hannunta. Kura masa ido tai tana ta kallon fuskarsa, ganin be bude idon ba har na tsawon lokaci yasa ta matsa kusa da kunnensa ta kirashi a hankali.

“Yallabai...”

Sannan ta dago ta kalleshi, still idonsa a rufe, sai ta sake maida bakinta sautin kunnenta.

“Talba”

Ta sake dagowa a karo na biyu ta kalli fuskarsa, still be bude idon ba. Sai maida bakinta tai a karo na uku sai dai wannan karon ba saitin kunnensa ba ne, sai tin kumatunsa ta kai bakin ta sumbance da soft pink lips dinta a hankali. A hankali ya fadada fuskarsa da murmushi yai bude idon yana kallon dayya ta saka dayan hannunta tana jiran ya bude nasa idon ta rufe nata.

“I love you Babe”

Ya furta da kamar rada, sai tai saurin rufe idon tana jin wani kalar kunya ta rufeta. Hannunta dake cikin nasa yaja ya kai saitin kirjinsa yana kallon fuskarta data rufe da dayan hannunta.

“Hawo nan mu kwanta”

Ta janye hannunta da sauri.

“Zan kira likita ya dubaka, wannan Abokanka, ko wani”

Ya girgiza mata kai.

“Yana zuwa zai fara damuna da magana babu abun da zai min a yanzu, zo mu kwanta”

Ya fada yana gyara kwanciyarsa daker domin har yanzu kirjinsa ciwo yake, matsa mata yai ta yadda zata samu gurin kwanciya a saman gadon. A kokarin na ki gujewa kwantawa gurin ta ce.

“Ina da wani labari da zan baka”

“To kwanta a nan sai ki fada min”

Tsayawa tai kallon gadon sannan ta cire talkaminta ta hau saman ta kwanta gefensa tai matashin kai da gefen kirjinsa zuwa damtsen hannunsa, tana kwantawa sai tai lamooo kamar bata gurin, sai kamshin turarensa ke kai mata hari a hanci. Ya kai bakinsa ya sumbacin goshinta yana kallon saman idonta kasancewar ta rufe idon ne gabanta sai faduwa yake.

“Fada min kyakkyawata labarin me?”

Ta bude idon ta sauri saboda ya tabo inda yake mata kaikayi.

“Da baka dawo ba, sai wannan abokinka likita ya ce matarsa ta kai ni gida....”

Daki daki ta tsara masa hadda lamarin ya faru har zuwa inda take son direwa, tana yi tana zane a jikin rigarsa, kana gani kasan tana cikin farinciki da jindadi. Murmushi yai yana ta kallon kwayar idonta, ba zai karyatata ba, amman

labarinta be yi making sense ba, after ta fada masa ta rasa duka familynta yanzu kuma tace ta ga yayanta? How? Kallonta tai jin yayi shiru be ce komai ba, yasa ta fara rantsuwa.

“Wallahi da gaske nake, ba karya ba”

Ya kalli bakinta dake matsawa a hankali, sannan ya sake kallon idonta.

“Hug me rumgume ni”

Ta sauke nata idon daga nashi tana dan turo baki ganin ba ce komai ba.

“Baka yarda da labarina ba?”

Yayi murmushi ya lumshe ido, baya son musu da ita a yanzu kuma baya son ya zurfafa a tattaunar, domin jikinsa baya masa dadi.

“Hug Babe”

Ta dan yi sama kadan ta mika hannunta jikin wuyansa ta rumgume shi tana kallon kyakkyawar fuskarsa,sai ta kai hannu ta taba tsinin hancinsa, murmushi yai ba tare daya bude ido ba, ita ma murmushin tai tana kallon fuskarsa. Kara turo kofar dakin da suka ji yasa ta dago ta leka kofar sai tai arba da Kabir, Talba kam ko motsawa be yi ba, cos to him ba wani abu ba ne dan an tararsa shi yana kwance da ita a gado daya, idan ma akwai wanda zai ji ma kunya Daddy ne ko Momy, amman sauran siblings dinsa ba.

“Wanene?”

Ya tambaya still idonsa a rufe.

Sai tai masa rada tana kallon Kabir dake doso inda suke.

“Kabir ne gashi nan yana zuwa gurinmu”

Kabir yayi murmushi yana kallonta cike da burgewa.

“Ashe kin iya rada, yan matan Talba”

Sai tai saurin rufe idonta tana murmushin jin kunya, Talba ya bude idon ya dago cike da karfin hali yana kallon Kabir.

“Dan sa'ido”

Kabir yayi murmushi ya kai hannunsa ya cirewa Talba drip din dake hannunsa sannan ya zauna yana kallonsa.

“Ya jikin?”

“Alhamdulillah, kirjina ciwo yake sosai”

“Dole ne wannan, saboda kirjin ne ya bugu, amman yanzu tun da ka farka ai sai ayi maka hoton gurin a duba matsalar”

He nodded his head

“Ina Daddy?”

“Tare muka zo da shi, yana waje”

“Ya sani?”

“Yeah ya zo dazun ma, yanzu kuma ya sake kirana yace na zo muje, i told him ai fa ba zaman lafiya tun danka na asibiti”

Talba ya fadada fuskarsa da murmushi yana cin kaunar Daddy har ransa. Aminatu ta fara kokarin tsallaka Talba ta sauka.

“Bari na kira Likita”

“Ni kuma Nurse ne?”

Kabir ya tambaya yana kallonta, sai Talba yai hanzarin riko kwankwasonta, yana kokarin dawowa da ita.

“Ai kai ba likita ba ne”

“Saboda ban tana miki allura ba ko?”

“Aa ai likitoci da an gansu ana gane su, wannan abokin nasa ai shi kowa ya san likita ne, ban san ko wasa kake ba dai”

Kabir ya wara ido yana murmushin daya fi kama da dariya.

“Wato ni bana da kama da likitoci?”

“Aa ina nufi...”

“Shiiiiii”

Bata karasa ba Talba ya dakatar da ita ta hanyar yi mata alama da tai shirun, sai tai shiru kamar yadda ya bukata.

“Kai gawa ta ki rame, daga dawowarka zaka fara damun mutane?”

“Talba yayi murmushi, Please je ka shigo min da Daddy”

“Ya kamata ka ci wani abu yanzu ba”

“Kira Momy ta bani”

Kabir ya mike tsaye, sai da ya kalli Aminatu sannan ya juya ya fice daga dakin. Talba ya kalli Aminatu.

“Babe bana son kina sakewa da mutane, baki san muryar mace al'aura ba ce?”

“No muryar mace ba al'aura ba ce”

“To ni a gareni al'aura ce, bana son kina sakewa da maza any how, yanzu kin fada min wani wai kin ga yayanki waya sani ko kama ce kawai? And ya za'ayi ya zama yayanki bayan duka yan'uwanki an kashe su? And now you're sitting next to me kina magana da Kabir kamar wani dan'uwanki i don't like it”

“Ai ba wata maganar nake da shi ba, kuma shi din ai dan'uwanka ne”

“Dan'uwana ne, amman idan na mutu a yanzu he can marry you, bakin san wani namiji yana kishin aji muryarsa matarsa ba, balle har ace wani yana magana da ita? Ko da mummuna ce balle ke da kike kyakkyawa, muryarki kuma tana da dadin saurare, hakan zai iya sakawa mutum ya jaki da dogon hira saboda yai ta saurarenki”

Shiru tai bata ce komai ba, ba dan bata da abun fadar ba, sai dan bata son musu da shi.

“Sauko kar Daddy ya iskoki haka”

Ta rika hannunsa ta sauko saman gadon, ta nufi inda aka aje flask din ruwan zafi.

“Bari na hada maka shayi”

Ya kalleta kawai yayi murmushi ya yunkura ya tashi zaune daidai ya jingina da gadon. Tana daukar cup Momy na shigowa dakin tare da Kabir da Hajiya Sadiya da wata yar'uwar Daddy Hajiya Tuni, sai Daddy dake tare da wani abokinsa Alhaji Tukur. Kowane fuskarsa sake cike da farinciki. Ban da Daddy daya matso daf da Talba ya zauna saman gadon yana kallonsa fuska a hade. Talba na ganin yanayin Daddy ya san da magana a bakinsa, sai ya sauke kasan kasa yana amsa ya jikin da ake masa.

“Daman ka dade baka kwanta gado ba, yanzu ai ka kwanta yadda kake so, tun da baka da hankali baka san ciwon kanka, balle ka damu da halin da wasu zasu shiga idan wani abu ya same ka”

Alhaji Tukur ya tari numfashin Daddy.

“Kaddararo ne, ba a isa a kauce musu ba, kuma tun da har ya samu lafiya ai komai mai sauki ne”

Daddy ya kalli Alhaji Tukur rai a bace ya ce

“An fa fada yadda ya hau titin, duk abun da yai da gangan yai, tun da ya san akwai motoci a fiti ba shi kadai akai wa Titi ba, idan ma wani abun be ba akwai police ba, ce masa akai idan ya kama mutumen tsayawa zai yi? Waya sani ma ko yana da makami yai masa wata illar?”

“Daddy I'm sorry...”

Talba ya fada sai Daddy ya daka masa tsawa.

“Rufe mana baki, daman abun da kuka iya kenan bada hakuri, lokacin da zaku yi abu ba zaku duba kanku ko halin da na kusa da ku zasu shiga sai kawai ku aikata, idan an zo magana ku fara bada hakuri”

“Ai ba laifinsa ba ne, laifin wannan yar iskar yarinyar ne, mahaukaciya daga ganin mutum sai ki fara cewa ga wanda ya kamaki can, waya sani ko ba shi ba ne, shi kuma komai ta fada masa sai ya dauka”

Cewar Momy cikin tsawa tana watsawa Aminatu data kasa juyowa harara.

“Idan ta fada masa, shi ba shi da hankali ne? Ai ba fada masa ne matsalar ba, yadda yake wasa da rayuwarsa ne, taya zaka hau titi kana gudu kamar kai kadai akai wa titin”

Daddy ya kara fada, Kabir yayi murmushi.

“Wato dai idan mutum yana da uwa da uba a raye ya huta, ji yadda kuka masa fada kamar karamin yaro”

Aminatu ta juyo a hankali rike da cup din da bata gama hadawa ba, kanta kasa. Momy ta mata wani mugun kallo.

“La la la.... Uban waye ya ce ki taba kayan tea din nan? Da na aje cewa na yi ki dauka ki hada ki sha...?”

“Aa daman... ”

Bata karasa ba, Hajiya Saratu ta kai mata duka a kafada.

“Makira, munafuka”

Aminatu ta aje kofin da sauri idonta na cika da hawaye. Talba ya kalli Aminatu da sauri yana jin ba dadi.

“Haba Mama Saratu ni nace ta hada min”

“Ko ba kai kace ba, ma ai matarka ce, tana da yancin ta taba duk wani abu daya alakantu da kai, weather we like it or no, ta riga ta zama part of us, wannan abun da kuke yi ma yarinyar nan be dace ba Momy”

Kabir ya fada cikin rashin jindadi, sai Momy ta watsa masa harara, zata yi magana Daddy ya rigata.

“Na dauka na gargadeki akan yarinyar nan? Ita miye laifinta a ciki? Idan zaki huce haushi ki sauke akan Mu'az, ba ita ba. Kuma wannan ya zama na karshe da za ku sake cin mutuncin yarinyar ko ku kai mata hannu”

Momy bata yarda ta sake cewa komai ba, ta fice daga dakin cikin bacin rai Hajiya Saratu ta rufa mata baya, kofar bata rufe ba Ali ya shigo, farincikin dake fuskarsa baya boyuwa na ganin abokinsa a zaune. Sai da ya gaisa da su Daddy sannan ya shiga duba Talba, yana tambayarsa abun da yake ji.

“Kirjin ne dai kawai yake ciwo”

“Za a maka hoto sai a rubuta wasu magungunan, yanzu dai ka saka wani abu a cikinka”

“Okay”

Daddy ya mike tsaye.

“Kai ma Ali kana da kana laifin ai, idan ka ga Talba zai yi wani abu kamata yai ka hana shi, amman ka bar shi yana risking rayuwarsa kamar mai rai biyu”

Alhaji Tukur yayi dariya kamar Yadda Kabir da Hajiya Tuni suke. Ali ya ce.

“Daddy ka san halin ɗanka ba jin magana yake ba”

“Yanzu dai aikin gama ya gama, sai dai a harari gaba, Allah ya kara tsarewa, kuma ya baka lafiya Talba”

Cewar Hajiya Tuni, sai duk suka amsa da Ameen, ban da Aminatu da ta maida fuskarta gefe tana ta hawaye. A tare Daddy ya fita da yar'uwarsa da kuma abokinsa, sannan Kabir ya saci kallon Aminatu.

“Ta hada maka wani tea, ko na hada maka”

“Zata hada”

Talba ya amsa masa, sai yai murmushi ya fice. Talba ya kalli Ali dake kallon Aminatu ya ce

“Ali samo min tissue please”

“Ayi me?”

“Hawayen matata zan share saboda na san zata min kuka”

“Kai ka gwada mata ta rika maka kukan kenan”

Ali ya fada sannan ya nufi kofa, yana ficewa Aminatu ta juyo ta fado jikin Talba ta fashe da kuka mai sauti riri kamar yar shekara biyu. Talba ya rumtse ido domin ya ji ciwon fado masa da tai.

“I knew it”

Kuka take masa sosai har wani maida numfashi take da karfi, Talba ya saka hannunsa a bayan hijabinta yana shafata ba tare da yace tai hakuri ba. Suna haka Ali ya dawo dakin, rike da tissue paper ya mikawa Talba yana kallon Aminatu dake ta kuka shagwaba, sai dai ganin Ali yasa ta rage sautin kukan.

“Me akai mata?”

“Ka san ita da Momy basa shan inuwa daya”

Talba ya amsa masa.

“Make sure ka ci wani abu kamin na dawo, sai ka sha magani akwai allurar da za a maka”

Kai Talba ya daga masa, shi kuma ya juya ya fice. Talba ya dago kanta cikin rashin karfi jiki yana kallon fuskarta.

“Duk wannan kuka na fadan Momy”

“Ba na Momy kadai ba har da na wannan matar da ta dake ni a kafada”

Yayi murmushi yana ayyana yadda kuka baya mata wuya, abu kadan sai hawaye, ko da yake daman masu yawan shiga damuwa kukansu a kusa yake, kana taba su za su fara maka kuka kamar jarirai. Tissue din ya zara ya fara goge mata fuskarta.

“Yi hakuri, ba su sake ba ai kin ji Daddy ya musu magana ko?”

Ta turo baki gaba wasu hawayen na sauko mata.

“Miyasa Momynka bata so na wai?”

“Momy tana sonki mana, kawai dai ranta ne ya bace saboda abun da ya faru”

Ta kai hannu ta murza idonta.

“Ka kira min Mama”

Ta fada tana kara kwantawa jikinsa kamar kyanwa, sai ya rumgumeta ya dora wuyansa gurin kanta. Ko bata ce masa Hajiya Laraba ba ya san ita take nufi domin ita take kira da Mama kamar yadda yayanta suke kiranta. Da karfi Leila ta turo kofar dakin ta shigo cikin da annashuwar kiran da Momy tai mata ta fada mata cewar Talba ya farka, hakan ya sa ta dawo asibitin da sauri. Sai dai a yadda ta tararda Aminatu da Talba ya saka hankalimta ya tashi kuma ranta ya bace sosai, sai ta nemi farincikin farkawarsa ta rasa. dan dagowa yai daga jikin Aminatu saboda ya san zata ji ba dadi, shi kuma be shirya batawa kowa rai ba a yanzu.

“Talba miye haka?”

Ta tambaya muryarta na rawa, sai Aminatu ta juyo ta kalleta.

“Taya zaka maida kanka wani iri kana hada jiki da wannan yarinyar? Kalleta ba Wallahi ba ajinka ba ce, gaba daya an bi an magance ka baka ganin komai sai ita, dubi halin daka jefa kanka all because of this stupid girl, yarinya karama ta canja ka Talba jikinka mai tsada kake bari wannan kazamar yar kauyen tana tabawa, gaba daya an canja ka Talba, yarinyar nan ta mallakeka”

Aminatu ta daga jikinta daga jikin Talba, tana kallon Leila, daman tana bata gama huce haushin abun da Momy da Hajiya Sadiya sukai mata ba, ita kuma ta zo zata kara mata da nata.

“Idan asiri gaskiya ne ai sai ki je yi, baki san ma na mallake shi ba sai na hana shi aurenki, kuma kauye ai kowa salinsa kauye ne”

Boom! Wannan karon Leila ce ke mamakin jin furucin Aminatu ba Talba ne, he was shocked ace kalaman nan daga bakin Aminatu suka fito, how? Yaushe tai baki haka? Bata ma jin tsoron. Ya kalli Leila da tai shiru tana wani irin cika kamar zakanya, sannan ya kalli Aminatu still yana mamaki.

“So you can talk”

Leila ta kalleshi da mugun takaici.

“What do you mean she can talk? Are you supporting her? Taya kana kallon karamar yarinya kamar wannan tana fada min magana without doing anything?”

Hawaye ya sauko a idonta.

“I'm not supporting her, ke kika fara fada mata magana marar dadi and ta rama, na ce na goyi bayanta?”

“Thank You”

Ta furta tana murmushin daya fi kuka ciwo sannan ta juya zata fice, sai ya kirata da sauri.

“Leila...”

Bata amsa ba balle ta juyo ta kalleshi ma, ta fice dakin cikin bakinciki da bacin rai. Talba ya kalli Aminatu cikin rashin jindadin yadda Leila ta fita dakin.

“You shouldn't talk to her this way Babe, be kamata ki fada mata haka ba”

Kamar mai jira nan da nan nata idon ya cika da hawaye.

“Ni me na mata da take fada min magana? Ita da mahaifiyarta me na tare musu? Kana jin tana ce min yar kauye kazama”

Ya daga kansa sama yana sauke numfashi.

‘Oh ya Allah’

Ya furta a ransa sannan ya mika mata hannunsa, sai ta nade hannayenta ta matsa baya tana turo baki, hawayen har ya fara sauko mata, wani zafi ma take jin zuciyarta na mata saboda ya shigarwa Leila.

“Ni ka kira min Mama, ta zo ta tafi da ni”

Sai ya sauko a hankali saman gadon ya mike tsaye, ya karasa inda take cike da karfin hali ya rumgumeta.

“Yi hakuri. Kin ga babu waya tare da ni, bari Ali ya shigo ko Kabir na tambaya waya dauki wayata sai na kira miki ita, amman kamin nan yanzu ina son ki hada min tea na sha, sai ki zuba min abinci gashi nan a cooler. Zan wanke bakina”

“Toh”

Ta amsa cike da shagwaba, murmushi yai ya sake ta, ba karamin burge shi take ba idan tana masa shagwabar, ko ba komai hakan da take tana nuna masa shi ne gatanta, kuma shi ne wanda zai iya share mata hawaye, kuma ya fahimci damuwarta, daman mace da shagwaba aka santa, ba kamar namiji ba. Ya fara takawa cike da karfin yana jin kirjinsa kamar zai rabe gida biyu, sai dai baya son nunawa kar ta gani hankalinta ya tashi. Sai ya shiga bandaki ya rufe sannan ya

ya dafe kansa ya durkushe a kasa ya cige bakinsa, alamar yana jin azaba sosai. Sai da ya lumshe ido ya bude a hankali sannan ya yunkurin ya tashi yana ambaton Allah a zuciyarsa ya karasa gurin da tub din yake.

*** ** *** ** ***

Leila ta nufi inda su Momy suke zaune tana hawaye ta zauna tana jin kuka na son kwace mata, bata taba sanin haka take kishin Talba ba sai yau, ji tai kamar ace tana da wuka a hannunta ta yanka naman Aminatu.

“Ke Lafiya”

Hajiya Saratu ta tambaya.

“Mama ina shiga dakin nan na same ta rumgume da shi, na yi magana har tana cewa wai ta yi asirin sai ma ta hana shi aurena, imagine yar kauye kamar wannan zata fada min magana”

Momy ta saki baki da mamaki.

“Ashe yar iska ce? Ita Aminatun ta fada miki haka? Shi Talba yana nan, ita wannan yarinyar har ta samu baki?”

“He take her side”

Ta amsa tana share hawayenta. Hajiya Saratu ta tabe baki.

“Hmmm ai raba kanki da yan kauyen nan, ai idan suka shiga birni sun fi yan birnin iskanci, da nuna isa, ko kishi kike da yar kauye sai a fi sonta da ke, ai yan kauyen nan kwace miji suke yi,duk wata kirsa da kisisinar shiga zuciyar miji sun sani, kuma basa barin zama banza ai”

“Tab di jam, Leila ba karamin aiki ke gabanmu, tun yanzu kenan? Me kike tsammani a gaba?”

Momy ta fada, sai Hajiya Saratu tai kwafa.

“Ki bar komai a hannuna, Wallahi wannan bokan ya iya aiki, shiyasa ma nake son Leila ta tafi ko miye zai mata yayi mata abubuwa su fara tafiya yadda muke so, ya fada min da bakinsa cewar da Ja6a ma zai yi aikin, kin san ko yadda Ja6a take da wari dole ma zai rabu da ita”

“Yauwa haka muke so”

Cewar Momy, sai Leila ta sake share hawayenta tana kallon Hajiya Saratu.

“Minene Ja6a Mama Sadiya?”

“Wata abu ce mai shegen warin tsiya, zaki ganta kamar 6era amman ita wari ne da ita sosai, ba a son tana ra6ar mutane ne ma saboda warinta”

Leila ta dan shinshina jikinta.

“Amman fa ni ina jin wani wari, marar dadi ni ban ma taba jin irinsa ba, ko dazun sai da na yi wanka sannan na daina jinsa, sunan Aminatu kika bada ko nawa?”

Daga Momy har Hajiya Saratu kallon Leila suke da mamaki.

“Tun kwanan baya na fara jinsa, ina jin yau kwana biyu ko uku kenan warin har hawan kaina yake...”

Leila na kai aya kiran Madina ya shigo wayarta dake hannunta, sunan Madina na appearing gaban Leila yai mugun faduwa.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Ya dan yi yar kara, sai tai saurin daga daga jikinta idonta na cika da hawayen farinciki.

“Sannu Sannu Sannu, bari na kira likita”

Ta juya da sauri, sai yai hanzarin bude idonsa ya rika hannunta da hannunsa na hagu. Tana jiyowa ya girgiza mata kai alamar aa, sai ya sake lumshe ido. Tsoro ta ji ganin ya rufe idon duk da, duk da kasancewar yana rike da hannunta. Kura masa ido tai tana ta kallon fuskarsa, ganin be bude idon ba har na tsawon lokaci yasa ta matsa kusa da kunnensa ta kirashi a hankali.

“Yallabai...”

Sannan ta dago ta kalleshi, still idonsa a rufe, sai ta sake maida bakinta sautin kunnenta.

“Talba”

Ta sake dagowa a karo na biyu ta kalli fuskarsa, still be bude idon ba. Sai maida bakinta tai a karo na uku sai dai wannan karon ba saitin kunnensa ba ne, sai tin kumatunsa ta kai bakin ta sumbance da soft pink lips dinta a hankali. A hankali ya fadada fuskarsa da murmushi yai bude idon yana kallon dayya ta saka dayan hannunta tana jiran ya bude nasa idon ta rufe nata.

“I love you Babe”

Ya furta da kamar rada, sai tai saurin rufe idon tana jin wani kalar kunya ta rufeta. Hannunta dake cikin nasa yaja ya kai saitin kirjinsa yana kallon fuskarta data rufe da dayan hannunta.

“Hawo nan mu kwanta”

Ta janye hannunta da sauri.

“Zan kira likita ya dubaka, wannan Abokanka, ko wani”

Ya girgiza mata kai.

“Yana zuwa zai fara damuna da magana babu abun da zai min a yanzu, zo mu kwanta”

Ya fada yana gyara kwanciyarsa daker domin har yanzu kirjinsa ciwo yake, matsa mata yai ta yadda zata samu gurin kwanciya a saman gadon. A kokarin na ki gujewa kwantawa gurin ta ce.

“Ina da wani labari da zan baka”

“To kwanta a nan sai ki fada min”

Tsayawa tai kallon gadon sannan ta cire talkaminta ta hau saman ta kwanta gefensa tai matashin kai da gefen kirjinsa zuwa damtsen hannunsa, tana kwantawa sai tai lamooo kamar bata gurin, sai kamshin turarensa ke kai mata hari a hanci. Ya kai bakinsa ya sumbacin goshinta yana kallon saman idonta kasancewar ta rufe idon ne gabanta sai faduwa yake.

“Fada min kyakkyawata labarin me?”

Ta bude idon ta sauri saboda ya tabo inda yake mata kaikayi.

“Da baka dawo ba, sai wannan abokinka likita ya ce matarsa ta kai ni gida….”

Daki daki ta tsara masa hadda lamarin ya faru har zuwa inda take son direwa, tana yi tana zane a jikin rigarsa, kana gani kasan tana cikin farinciki da jindadi. Murmushi yai yana ta kallon kwayar idonta, ba zai karyatata ba, amman labarinta be yi making sense ba, after ta fada masa ta rasa duka familynta yanzu kuma tace ta ga yayanta? How? Kallonta tai jin yayi shiru be ce komai ba, yasa ta fara rantsuwa.

“Wallahi da gaske nake, ba karya ba”

Ya kalli bakinta dake matsawa a hankali, sannan ya sake kallon idonta.

“Hug me rumgume ni”

Ta sauke nata idon daga nashi tana dan turo baki ganin ba ce komai ba.

“Baka yarda da labarina ba?”

Yayi murmushi ya lumshe ido, baya son musu da ita a yanzu kuma baya son ya zurfafa a tattaunar, domin jikinsa baya masa dadi.

“Hug Babe”

Ta dan yi sama kadan ta mika hannunta jikin wuyansa ta rumgume shi tana kallon kyakkyawar fuskarsa,sai ta kai hannu ta taba tsinin hancinsa, murmushi yai ba tare daya bude ido ba, ita ma murmushin tai tana kallon fuskarsa. Kara turo kofar dakin da suka ji yasa ta dago ta leka kofar sai tai arba da Kabir, Talba kam ko motsawa be yi ba, cos to him ba wani abu ba ne dan an tararsa shi yana kwance da ita a gado daya, idan ma akwai wanda zai ji ma kunya Daddy ne ko Momy, amman sauran siblings dinsa ba.

“Wanene?”

Ya tambaya still idonsa a rufe.

Sai tai masa rada tana kallon Kabir dake doso inda suke.

“Kabir ne gashi nan yana zuwa gurinmu”

Kabir yayi murmushi yana kallonta cike da burgewa.

“Ashe kin iya rada, yan matan Talba”

Sai tai saurin rufe idonta tana murmushin jin kunya, Talba ya bude idon ya dago cike da karfin hali yana kallon Kabir.

“Dan sa'ido”

Kabir yayi murmushi ya kai hannunsa ya cirewa Talba drip din dake hannunsa sannan ya zauna yana kallonsa.

“Ya jikin?”

“Alhamdulillah, kirjina ciwo yake sosai”

“Dole ne wannan, saboda kirjin ne ya bugu, amman yanzu tun da ka farka ai sai ayi maka hoton gurin a duba matsalar”

He nodded his head

“Ina Daddy?”

“Tare muka zo da shi, yana waje”

“Ya sani?”

“Yeah ya zo dazun ma, yanzu kuma ya sake kirana yace na zo muje, i told him ai fa ba zaman lafiya tun danka na asibiti”

Talba ya fadada fuskarsa da murmushi yana cin kaunar Daddy har ransa. Aminatu ta fara kokarin tsallaka Talba ta sauka.

“Bari na kira Likita”

“Ni kuma Nurse ne?”

Kabir ya tambaya yana kallonta, sai Talba yai hanzarin riko kwankwasonta, yana kokarin dawowa da ita.

“Ai kai ba likita ba ne”

“Saboda ban tana miki allura ba ko?”

“Aa ai likitoci da an gansu ana gane su, wannan abokin nasa ai shi kowa ya san likita ne, ban san ko wasa kake ba dai”

Kabir ya wara ido yana murmushin daya fi kama da dariya.

“Wato ni bana da kama da likitoci?”

“Aa ina nufi...”

“Shiiiiii”

Bata karasa ba Talba ya dakatar da ita ta hanyar yi mata alama da tai shirun, sai tai shiru kamar yadda ya bukata.

“Kai gawa ta ki rame, daga dawowarka zaka fara damun mutane?”

“Talba yayi murmushi, Please je ka shigo min da Daddy”

“Ya kamata ka ci wani abu yanzu ba”

“Kira Momy ta bani”

Kabir ya mike tsaye, sai da ya kalli Aminatu sannan ya juya ya fice daga dakin. Talba ya kalli Aminatu.

“Babe bana son kina sakewa da mutane, baki san muryar mace al'aura ba ce?”

“No muryar mace ba al'aura ba ce”

“To ni a gareni al'aura ce, bana son kina sakewa da maza any how, yanzu kin fada min wani wai kin ga yayanki waya sani ko kama ce kawai? And ya za'ayi ya zama yayanki bayan duka yan'uwanki an kashe su? And now you're sitting next to me kina magana da Kabir kamar wani dan'uwanki i don't like it”

“Ai ba wata maganar nake da shi ba, kuma shi din ai dan'uwanka ne”

“Dan'uwana ne, amman idan na mutu a yanzu he can marry you, bakin san wani namiji yana kishin aji muryarsa matarsa ba, balle har ace wani yana magana da ita? Ko da mummuna ce balle ke da kike kyakkyawa, muryarki kuma tana da dadin saurare, hakan zai iya sakawa mutum ya jaki da dogon hira saboda yai ta saurarenki”

Shiru tai bata ce komai ba, ba dan bata da abun fadar ba, sai dan bata son musu da shi.

“Sauko kar Daddy ya iskoki haka”

Ta rika hannunsa ta sauko saman gadon, ta nufi inda aka aje flask din ruwan zafi.

“Bari na hada maka shayi”

Ya kalleta kawai yayi murmushi ya yunkura ya tashi zaune daidai ya jingina da gadon. Tana daukar cup Momy na shigowa dakin tare da Kabir da Hajiya Sadiya da wata yar'uwar Daddy Hajiya Tuni, sai Daddy dake tare da wani abokinsa Alhaji Tukur. Kowane fuskarsa sake cike da farinciki. Ban da Daddy daya matso daf da Talba ya zauna saman gadon yana kallonsa fuska a hade. Talba na ganin yanayin Daddy ya san da magana a bakinsa, sai ya sauke kasan kasa yana amsa ya jikin da ake masa.

“Daman ka dade baka kwanta gado ba, yanzu ai ka kwanta yadda kake so, tun da baka da hankali baka san ciwon kanka, balle ka damu da halin da wasu zasu shiga idan wani abu ya same ka”

Alhaji Tukur ya tari numfashin Daddy.

“Kaddararo ne, ba a isa a kauce musu ba, kuma tun da har ya samu lafiya ai komai mai sauki ne”

Daddy ya kalli Alhaji Tukur rai a bace ya ce

“An fa fada yadda ya hau titin, duk abun da yai da gangan yai, tun da ya san akwai motoci a fiti ba shi kadai akai wa Titi ba, idan ma wani abun be ba akwai police ba, ce masa akai idan ya kama mutumen tsayawa zai yi? Waya sani ma ko yana da makami yai masa wata illar?”

“Daddy I'm sorry...”

Talba ya fada sai Daddy ya daka masa tsawa.

“Rufe mana baki, daman abun da kuka iya kenan bada hakuri, lokacin da zaku yi abu ba zaku duba kanku ko halin da na kusa da ku zasu shiga sai kawai ku aikata, idan an zo magana ku fara bada hakuri”

“Ai ba laifinsa ba ne, laifin wannan yar iskar yarinyar ne, mahaukaciya daga ganin mutum sai ki fara cewa ga wanda ya kamaki can, waya sani ko ba shi ba ne, shi kuma komai ta fada masa sai ya dauka”

Cewar Momy cikin tsawa tana watsawa Aminatu data kasa juyowa harara.

“Idan ta fada masa, shi ba shi da hankali ne? Ai ba fada masa ne matsalar ba, yadda yake wasa da rayuwarsa ne, taya zaka hau titi kana gudu kamar kai kadai akai wa titin”

Daddy ya kara fada, Kabir yayi murmushi.

“Wato dai idan mutum yana da uwa da uba a raye ya huta, ji yadda kuka masa fada kamar karamin yaro”

Aminatu ta juyo a hankali rike da cup din da bata gama hadawa ba, kanta kasa. Momy ta mata wani mugun kallo.

“La la la.... Uban waye ya ce ki taba kayan tea din nan? Da na aje cewa na yi ki dauka ki hada ki sha...?”

“Aa daman... ”

Bata karasa ba, Hajiya Saratu ta kai mata duka a kafada.

“Makira, munafuka”

Aminatu ta aje kofin da sauri idonta na cika da hawaye. Talba ya kalli Aminatu da sauri yana jin ba dadi.

“Haba Mama Saratu ni nace ta hada min”

“Ko ba kai kace ba, ma ai matarka ce, tana da yancin ta taba duk wani abu daya alakantu da kai, weather we like it or no, ta riga ta zama part of us, wannan abun da kuke yi ma yarinyar nan be dace ba Momy”

Kabir ya fada cikin rashin jindadi, sai Momy ta watsa masa harara, zata yi magana Daddy ya rigata.

“Na dauka na gargadeki akan yarinyar nan? Ita miye laifinta a ciki? Idan zaki huce haushi ki sauke akan Mu'az, ba ita ba. Kuma wannan ya zama na karshe da za ku sake cin mutuncin yarinyar ko ku kai mata hannu”

Momy bata yarda ta sake cewa komai ba, ta fice daga dakin cikin bacin rai Hajiya Saratu ta rufa mata baya, kofar bata rufe ba Ali ya shigo, farincikin dake fuskarsa baya boyuwa na ganin abokinsa a zaune. Sai da ya gaisa da su Daddy sannan ya shiga duba Talba, yana tambayarsa abun da yake ji.

“Kirjin ne dai kawai yake ciwo”

“Za a maka hoto sai a rubuta wasu magungunan, yanzu dai ka saka wani abu a cikinka”

“Okay”

Daddy ya mike tsaye.

“Kai ma Ali kana da kana laifin ai, idan ka ga Talba zai yi wani abu kamata yai ka hana shi, amman ka bar shi yana risking rayuwarsa kamar mai rai biyu”

Alhaji Tukur yayi dariya kamar Yadda Kabir da Hajiya Tuni suke. Ali ya ce.

“Daddy ka san halin ɗanka ba jin magana yake ba”

“Yanzu dai aikin gama ya gama, sai dai a harari gaba, Allah ya kara tsarewa, kuma ya baka lafiya Talba”

Cewar Hajiya Tuni, sai duk suka amsa da Ameen, ban da Aminatu da ta maida fuskarta gefe tana ta hawaye. A tare Daddy ya fita da yar'uwarsa da kuma abokinsa, sannan Kabir ya saci kallon Aminatu.

“Ta hada maka wani tea, ko na hada maka”

“Zata hada”

Talba ya amsa masa, sai yai murmushi ya fice. Talba ya kalli Ali dake kallon Aminatu ya ce

“Ali samo min tissue please”

“Ayi me?”

“Hawayen matata zan share saboda na san zata min kuka”

“Kai ka gwada mata ta rika maka kukan kenan”

Ali ya fada sannan ya nufi kofa, yana ficewa Aminatu ta juyo ta fado jikin Talba ta fashe da kuka mai sauti riri kamar yar shekara biyu. Talba ya rumtse ido domin ya ji ciwon fado masa da tai.

“I knew it”

Kuka take masa sosai har wani maida numfashi take da karfi, Talba ya saka hannunsa a bayan hijabinta yana shafata ba tare da yace tai hakuri ba. Suna haka Ali ya dawo dakin, rike da tissue paper ya mikawa Talba yana kallon Aminatu dake ta kuka shagwaba, sai dai ganin Ali yasa ta rage sautin kukan.

“Me akai mata?”

“Ka san ita da Momy basa shan inuwa daya”

Talba ya amsa masa.

“Make sure ka ci wani abu kamin na dawo, sai ka sha magani akwai allurar da za a maka”

Kai Talba ya daga masa, shi kuma ya juya ya fice. Talba ya dago kanta cikin rashin karfi jiki yana kallon fuskarta.

“Duk wannan kuka na fadan Momy”

“Ba na Momy kadai ba har da na wannan matar da ta dake ni a kafada”

Yayi murmushi yana ayyana yadda kuka baya mata wuya, abu kadan sai hawaye, ko da yake daman masu yawan shiga damuwa kukansu a kusa yake, kana taba su za su fara maka kuka kamar jarirai. Tissue din ya zara ya fara goge mata fuskarta.

“Yi hakuri, ba su sake ba ai kin ji Daddy ya musu magana ko?”

Ta turo baki gaba wasu hawayen na sauko mata.

“Miyasa Momynka bata so na wai?”

“Momy tana sonki mana, kawai dai ranta ne ya bace saboda abun da ya faru”

Ta kai hannu ta murza idonta.

“Ka kira min Mama”

Ta fada tana kara kwantawa jikinsa kamar kyanwa, sai ya rumgumeta ya dora wuyansa gurin kanta. Ko bata ce masa Hajiya Laraba ba ya san ita take nufi domin ita take kira da Mama kamar yadda yayanta suke kiranta. Da karfi Leila ta turo kofar dakin ta shigo cikin da annashuwar kiran da Momy tai mata ta fada mata cewar Talba ya farka, hakan ya sa ta dawo asibitin da sauri. Sai dai a yadda ta tararda Aminatu da Talba ya saka hankalimta ya tashi kuma ranta ya bace sosai, sai ta nemi farincikin farkawarsa ta rasa. dan dagowa yai daga jikin Aminatu saboda ya san zata ji ba dadi, shi kuma be shirya batawa kowa rai ba a yanzu.

“Talba miye haka?”

Ta tambaya muryarta na rawa, sai Aminatu ta juyo ta kalleta.

“Taya zaka maida kanka wani iri kana hada jiki da wannan yarinyar? Kalleta ba Wallahi ba ajinka ba ce, gaba daya an bi an magance ka baka ganin komai sai ita, dubi halin daka jefa kanka all because of this stupid girl, yarinya karama ta canja ka Talba jikinka mai tsada kake bari wannan kazamar yar kauyen tana tabawa, gaba daya an canja ka Talba, yarinyar nan ta mallakeka”

Aminatu ta daga jikinta daga jikin Talba, tana kallon Leila, daman tana bata gama huce haushin abun da Momy da Hajiya Sadiya sukai mata ba, ita kuma ta zo zata kara mata da nata.

“Idan asiri gaskiya ne ai sai ki je yi, baki san ma na mallake shi ba sai na hana shi aurenki, kuma kauye ai kowa salinsa kauye ne”

Boom! Wannan karon Leila ce ke mamakin jin furucin Aminatu ba Talba ne, he was shocked ace kalaman nan daga bakin Aminatu suka fito, how? Yaushe tai baki haka? Bata ma jin tsoron. Ya kalli Leila da tai shiru tana wani irin cika kamar zakanya, sannan ya kalli Aminatu still yana mamaki.

“So you can talk”

Leila ta kalleshi da mugun takaici.

“What do you mean she can talk? Are you supporting her? Taya kana kallon karamar yarinya kamar wannan tana fada min magana without doing anything?”

Hawaye ya sauko a idonta.

“I'm not supporting her, ke kika fara fada mata magana marar dadi and ta rama, na ce na goyi bayanta?”

“Thank You”

Ta furta tana murmushin daya fi kuka ciwo sannan ta juya zata fice, sai ya kirata da sauri.

“Leila...”

Bata amsa ba balle ta juyo ta kalleshi ma, ta fice dakin cikin bakinciki da bacin rai. Talba ya kalli Aminatu cikin rashin jindadin yadda Leila ta fita dakin.

“You shouldn't talk to her this way Babe, be kamata ki fada mata haka ba”

Kamar mai jira nan da nan nata idon ya cika da hawaye.

“Ni me na mata da take fada min magana? Ita da mahaifiyarta me na tare musu? Kana jin tana ce min yar kauye kazama”

Ya daga kansa sama yana sauke numfashi.

‘Oh ya Allah’

Ya furta a ransa sannan ya mika mata hannunsa, sai ta nade hannayenta ta matsa baya tana turo baki, hawayen har ya fara sauko mata, wani zafi ma take jin zuciyarta na mata saboda ya shigarwa Leila.

“Ni ka kira min Mama, ta zo ta tafi da ni”

Sai ya sauko a hankali saman gadon ya mike tsaye, ya karasa inda take cike da karfin hali ya rumgumeta.

“Yi hakuri. Kin ga babu waya tare da ni, bari Ali ya shigo ko Kabir na tambaya waya dauki wayata sai na kira miki ita, amman kamin nan yanzu ina son ki hada min tea na sha, sai ki zuba min abinci gashi nan a cooler. Zan wanke bakina”

“Toh”

Ta amsa cike da shagwaba, murmushi yai ya sake ta, ba karamin burge shi take ba idan tana masa shagwabar, ko ba komai hakan da take tana nuna masa shi ne gatanta, kuma shi ne wanda zai iya share mata hawaye, kuma ya fahimci damuwarta, daman mace da shagwaba aka santa, ba kamar namiji ba. Ya fara takawa cike da karfin yana jin kirjinsa kamar zai rabe gida biyu, sai dai baya son nunawa kar ta gani hankalinta ya tashi. Sai ya shiga bandaki ya rufe sannan ya ya dafe kansa ya durkushe a kasa ya cige bakinsa, alamar yana jin azaba sosai. Sai da ya lumshe ido ya bude a hankali sannan ya yunkurin ya tashi yana ambaton Allah a zuciyarsa ya karasa gurin da tub din yake.

*** ** *** ** ***

Leila ta nufi inda su Momy suke zaune tana hawaye ta zauna tana jin kuka na son kwace mata, bata taba sanin haka take kishin Talba ba sai yau, ji tai kamar ace tana da wuka a hannunta ta yanka naman Aminatu.

“Ke Lafiya”

Hajiya Saratu ta tambaya.

“Mama ina shiga dakin nan na same ta rumgume da shi, na yi magana har tana cewa wai ta yi asirin sai ma ta hana shi aurena, imagine yar kauye kamar wannan zata fada min magana”

Momy ta saki baki da mamaki.

“Ashe yar iska ce? Ita Aminatun ta fada miki haka? Shi Talba yana nan, ita wannan yarinyar har ta samu baki?”

“He take her side”

Ta amsa tana share hawayenta. Hajiya Saratu ta tabe baki.

“Hmmm ai raba kanki da yan kauyen nan, ai idan suka shiga birni sun fi yan birnin iskanci, da nuna isa, ko kishi kike da yar kauye sai a fi sonta da ke, ai yan kauyen nan kwace miji suke yi,duk wata kirsa da kisisinar shiga zuciyar miji sun sani, kuma basa barin zama banza ai”

“Tab di jam, Leila ba karamin aiki ke gabanmu, tun yanzu kenan? Me kike tsammani a gaba?”

Momy ta fada, sai Hajiya Saratu tai kwafa.

“Ki bar komai a hannuna, Wallahi wannan bokan ya iya aiki, shiyasa ma nake son Leila ta tafi ko miye zai mata yayi mata abubuwa su fara tafiya yadda muke so, ya fada min da bakinsa cewar da Ja6a ma zai yi aikin, kin san ko yadda Ja6a take da wari dole ma zai rabu da ita”

“Yauwa haka muke so”

Cewar Momy, sai Leila ta sake share hawayenta tana kallon Hajiya Saratu.

“Minene Ja6a Mama Sadiya?”

“Wata abu ce mai shegen warin tsiya, zaki ganta kamar 6era amman ita wari ne da ita sosai, ba a son tana ra6ar mutane ne ma saboda warinta”

Leila ta dan shinshina jikinta.

“Amman fa ni ina jin wani wari, marar dadi ni ban ma taba jin irinsa ba, ko dazun sai da na yi wanka sannan na daina jinsa, sunan Aminatu kika bada ko nawa?”

Daga Momy har Hajiya Saratu kallon Leila suke da mamaki.

“Tun kwanan baya na fara jinsa, ina jin yau kwana biyu ko uku kenan warin har hawan kaina yake...”

Leila na kai aya kiran Madina ya shigo wayarta dake hannunta, sunan Madina na appearing gaban Leila yai mugun faduwa.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Mikewa tai tsaye ta nufi wani bangare na asibitin dake nesa da su Momy ta yadda ba za su iya jin wayarta da Madina ba..

“Now what?”

Madina ta yi murmushi tana gyara kwanciyarsa saman gado.

“Kawata kenan, kawai na kira ne na gargade ki, karki kuskura kowa ya ji maganar da muka yi”

“Kina magana kamar kin manta wacece ni Madina, kina tunanin zaki iya juya ni yadda kike so ne?”

“Na san wacece ke mana, Leila Mu'azu Shimkafi, kin yi wasa da damarki ne, shiyasa na ke taya ki jefa kwallo a raga, your destiny is in my hand now”

“Abun mamaki, wai Madina ce yau take min maganar, kina wasa da wuta a hannunki ba tare da kin sani ba”

“Ke ce dai kike wasa da wutar, kin san babu yadda za'ayi rayuwata ta lalace na cire rai daga samun abun da nake so, kuma ke da kika haddasa komai na saka miki ido, at least we're friends ai, ya kamata ace idan na fadi ke ma ki fadi”

“Duniya tana bani tsoro wani lokacin ace abokiyar da kuka ta so tare tun kuna yara, rana daya ta koma makiyiyarka”

“Duniya tana cike da abubuwan mamaki kala kala Leila, a cikin akwai aure Talba da Aminatu tai, ga kuma butulce min da kika, a tunanina, a yadda muke da ke, idan kika fahimci ina son Talba zaki iya yafe min shi, ko da a munafurce ne, sai gashi kin bani mamaki, a lokacin ne na kara fahimtar cewar abotar da nake da ke, akwai yaudara a ciki”

“Yaudara ta wuce wanda kika min? Wata kila da auren Talba nake still zski kulla soyayya da shi a waje?”

“Ban kira saboda mu yi irin wannan maganar ba, na kira ne kawai na gargadeki”

“Miyasa kike jin tsoro? Ashe ma ke karamar yar iska ce”

“Ina jin tsoron yadda duniya da yan'uwanki zasu kalleki idan na fallasa wannan sirrin naki”

“Ba ni kadai duniya zata kalla ba, har da ke”

“Iyakar abun da duniya zata ji akaina, shine na ci amanar kawance mun, ke kuma fa? Yar aikin gidanku kin binne gawarta tare da Mahaifiyarki ba tare da sanin kowa ba”

Leila ta yi murmushi.

“Madina kenan, idan kina son asirinki ya rufu ba sai kin tona nawa ba, zaki iya fadawa Mutanenki su nisanta daga inda Aminatu zata gansu, ko kuma ma su kasheta, ke da su hankalinku ya kwanta, kin ga babu wanda ya san kin aikata haka sai ni, ni kuma ba fada zan yi ba”

Madina ta yi shiru tana nazari, kamin ta tashi zaune ta girgiza mata kai kamar tana gabanta.

“Kina ta kokarin kakaba min abun da ban aikata ba, saboda ni da ke mu zama masu laifi daya ko? Ni ban dauke Aminatu ba, ban kuma san wanda ya dauke ta ba, babu wasu mutane da nake aiki da su da zasu dauketa”

“Madina kar mu yi haka mana, a dare da abun ya faru ina gida, Momy kuma bata san da maganar auren ba, balle a zarge ta, haka ni ma. Sannan a daren Talba yace mota ta haska su, shiyasa saka ya zo gida yana zargina da Kabir, ni kuma ban fita ba a ranar, babu kuma dalilin da zai saka Kabir yai masa haka, saboda Kabir ba son Aminatu yake ba, balle ya dauke Aminatu dan kar ta auri Talba, haka kuma, ba kyamar aurenta yake da Talba balle ya dauke ta gudun kar Talba ya aureta. Sannan da kika sace ta kika rasa yadda zaki da ita gudun kar asirinki ya tonu sai kika yi amfani da Mutanenki kika saka suka turawa Kabir sako, saboda Talba ya zarge shi kin ga ke kin fita kenan, saboda kin san yana zargina da Kabir. Kin iya game Leila kuma na jinjina miki, sai dai kuskuren da zaki yi a yanzu shi ne na wasa da damarki ki tonawa kanki asiri”

Madina ta ji gabanta yayi mugun faduwa, sai dai bata yarda ta nuna ba.

“Abun da kika tsara a ranki kenan? What if akwai wani mai son ganin bayan Aminatu ko Talba? Waya sani ma ko ke da kanki mai maganar akwai hannunki a ciki? Na kira ne kawai na gargade ki karki yarda ki fadawa kowa maganar da muka yi, kuma idon yana kanki daga yanzu, and don't forget the rules idan baki son asirinki ya tunu”

“Rules?”

“Yeah, ko har kin manta? Ban fada miki ki janye zancen aurenki da Talba ba?”

Leila ta buga wani uban tsaki ta kashe wayar. Sai Madina ta mike tsaye tana kwafa.

“Okay kashe min waya kika yi”

Tana fadar haka ta dago da sauri ta kalli kofa jin an turo kofar an shigo. Hajiya ta tsaya jikin kofar tana kallon Madina cike da zargi, ita kanta ta san kalar kallon da Hajiya take mata a yau ba irin na kullum ba ne.

“Da wa kike waya?”

Ta sauke numfashi a hankali ta yadda Hajiya ba zata ji ba sannan ta ce.

“Wani abokin aikina ne”

“Abokin aikinki? Madina me kike kokarin aikatawa? Ko kuma na ce me kika aikata?”

“Babu komai Hajiya, kin ji wani abun ne na dabam?”

Hajiya ta maida kofar ta rufe ta nufo inda take ciki tsawa.

“Karki maida ni karamar yarinya mana Madina, ina tsaye jikin kofar nan ina sauraren duk abun da kike fada”

“Wata kila ba ki ji da kyau ba ne Hajiya, amman ni babu wanda na yi ma komai, kawai dai ina waya da abokin aikina ne?”

“Leila ita ce abokin aikin? To yayi kyau”

Hajiya na fadar hakan ta juya ta fice daga dakin, sai Madina ta dora hannu a goshinta tana jin wani gumi na taso mata.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ta fara safa da marwa a dakin tana tunanin abun da zata fadawa Hajiya ta wanke kanta.

“Gaba daya ta ji abun da ta fada ko kuma wani ta ji?”

Ta dora duka hannayen saman kanta, jefar da wayar tai saman gado ta nufi kofar fita da sauri ta bude kofar ta fita, falon ta fara dubawa bata ga Hajiya ta nufi kitchen nan ma bata ciki, sai ta juyo ta nufi dakinta, sai ta isa gurin kofar dakin gabanta ya tsananta faduwa. Juyawa tai zata koma sai kuma ta juyo ta mika hannu ta bude kofar, can kuma ta dauke hannu tunanin yadda zata wanke kanta take, ta san idan bata fada ma Hajiya gaskiya ba, zata kara jefa kanta cikin wani ramen ne. Cike da karfin hali ta tura kofar ta shiga gabanta na faduwa, ko sallama kasa yi tai not just her heart ilahirin jikinta ma rawa yake. Ta karasa kusa da Hajiya ta zauna tana kallonta. Hajiya ta hade rai ko da wasa bata dago ta kalli inda Madina take zaune ba.

“Hajiya...”

“Idan kin san kin zo nan ne saboda ki min karya ki tashi tun yanzu ki bani guri”

Hajiya ta fada ba tare da ta kalleshi ba, sai da Madina ta kalli wayar da Hajiya take tabawa sannan ta ce.

“Gaskiya zan fada miki Hajiya, ba abun da kike zargi ba ne, da gaske da abokin aikina nake waya”

Hajiya ta kalleta

“Idan ma wani abun ne, ki fada tun da wuri, saboda mu yi tifkar hanci. Kurciya na damunki kina neman jefa kanki a halaka, naja miki kunne akan Talba ba ki ba, me kika aikata Madina?”

Madina ta hade yawu da karfi idonta na cika da hawaye.

“Hajiya...”

Sai kuma ta kasa magana, ta mike tsaye zata fice daga dakin.

“Idan wata matsalar ta doso ki, karki yi tunanin kina da wata uwa da zata share miki hawayenki, matukar baki fada min damuwarki a yanzu ba”

Juyowa tai ta kalli Hajiya hawaye na sauko mata.

“Fada miki damuwata a yanzu, kamar kara jefa kaina ne a cikin wata damuwar, saboda zaki tsane ni ki fara min fada”

Kallonta Hajiya take da kyau tana karantar hawayen dake sauko mata.

“Zo ki zauna”

Ta tako a hankali ta zauna a inda ta zauna dazun still hawaye na sauko mata.

“Me kika aikata”

Ta yi shiru sai kuka take.

“Ki fada min damuwarki, wata kila zan iya taimaka miki tun a yanzu, zamu iya samun mafita a yanzu ba sai gaba ba lokacin da komai zai chabe mana”

Nan ma kasa magana tai sai hawaye take.

“Ni mahaifiyarki ce Madina, baki da wata kawa a duniyar nan da ta wuce ni, bayan Allah baki da wanda zai miki maganin damuwarki kamar ni, ki fada min abun da yake faruwa so that mu samu mafita tun yanzu”

“Hajiya.... Na aikata kuskure, a lokacin da zan aikata ido ya rufe ban ga komai ba, har sai bayan na aikata”

Hajiya ta dafata cikin sanyin jiki.

“Me kika aikata?”

“Hajiya kin san yadda na ke son Talba, ina sonsa sosai Hajiya, ina masa irin son da ko Leila da wanda yake aure a yanzu basa masa irinsa”

Sai tai shiru. Sai Hajiya ta ce

“Na sani”

Madina ta yi saurin kama hannanyen Hajiya ta rike.

“Dan Allah Hajiya karki min fada, karki tsane ni, na san kin yi ta ja min kunne akan Talba, amman Hajiya abun da kake so rabuwa da shi ba zai yiyu ba a cikin sauki”

“Har yanzu ba ki fada min abun da kika aikata ba”

“Hajiya, kin san irin kawance dake tsakanina da Leila bata iya boye min komai”

“Na sani”

“Hajiya Leila ta gaba kashe wata mata mai aikinsu, sunanta Baaba”

Hajiya ta dora hannnu a kirji tana zaro ido, iya abun da ta ji ko ta sani shi ne Baaba ta tafi ganin gida garinsu ba a san inda take ba, domin Madina bata taba fada mata komai akan haka ba.

“Ta kashe ta?”

“Eh, amman ba da gangan ta aikata ba, a yadda ta fada min kuma na san ba zata min karya ba, sai suka dauke ta suka saka ta a mota ita da Momy zuwa asibiti, sai dai kamin su isa asibitin suka ji ta yi kalmar shahada ta daina numfashi, sai suka yi zaton ko ta mutu ne, bata min yadda akai suka tabbatar da mutuwar, ta dai fada min cewar hankalinta ya tashi sosai kuma Hajiya tace idan suka kaita asibiti dole za a san sun da maganar, gudun hakan yasa suka binne gawar a tsohon gidan gonar Momy, bata fada min yadda suka binne gawar ba, amman ta fada min cewa a tsohon gidan Momy suka rufe gawar. Tun daga lokacin sai tsoro ya kama Leila har mafarki Baaba take, wani lokacin kirana take ta fada min, and i always told her rai ne dole hakkin rai zai saka ta a haka.. Life goes on... Wallahi ban taba tunanin zan aikata wani abu makamancin wannan ba”

Hajiya da jiri ya fara dibanta ta cire hannayenta daga na Madina tana kallonta a tsorace.

“Kisan kai kika aikata?”

Madina ta yi saurin girgiza kai.

“Aa, ban aikata kisan kai ba, sai dai son Talba ya saka na aikata abun da ban yi tunani ba, lokacin da maganar auren Leila da Talba ta matsa kusa sai na ji kamar mutuwata ce take matsowa a kusa da ni, saboda ina son Talba, kuma na san abu ne mai wahala Leila ta yarda na auri Talba idan har ta aureshi. Hakan yasa na yi amfani da wannan damar na shirya yadda zan tsorata Leila saboda na saka hankalinta ya tashi maganar auren ta watse, na so na saka Leila a cilas ta rabu da Talba ta hanyar da ba zai san dalilin rabuwar da tai da shi ba, so that ya kalli hakan a matsayin cin amana, ni kuma sai ya so ni”

“Ban fahimci me kike nufi da kin tsorata taba?”

“Wasika na shirya aika mata a gidansu, da duk wani gurin inda zata risketa, wasika ta tsoratarwa na abun da ta aikata, bayan na gano inda gawar Baaba take”

Wani irin kallo Hajiya take yi ma Madina mai cike da alamar tambaya kala kala, gaba daya sai take ganinta kamar ba yarta. Ta ya ta aika duk wannan abun?

“Ya akai kika gano inda gawar take? Ke da wa kika yi wannan abun Madina?”

Ganin idon Hajiya ya kawo ruwa ya saka Madina ta fashe da kuka.

“Ni kadai, ni kadai na aikata haka, sai kuma mutanen da na biya”

“Ina kika same su?”

“Na yi magana da, Jamil ne Hajiya ai kin san shi? ”

Hajiya ya gyada kai.

“Na kira a waya na fada masa, akwai wani neighbor din mu da yake min cin mutunci yana zagina, so nake a dauko min shi a bashi kashi a sake shi, sai yace min ba matsala zai sama min wasu yan unguwarsu yaran yan siyasa ne ya san za su iya wannan aikin, mun yi magana da shi da safe da yamma ya kira ni yace min ga inda zamu hadu mu yi magana. The following day after na dawo daga aiki na saka mask na tafin can na hadu fa su suka fada min zan ba su 20k da address din inda mutumen yake, ba su fake addressees kuma na yi musu kwatancen karya na fuskar yadda mutumen yake, na karbi number wayarsu, sai bayan da na bar gurin kuma na tabbatar Jamil ua tafi sannan na kira su na fada musu ba wacan aikin za ayi min ba, wani dabam ne na fada musu ina son na tsorata wata ne, kuma zan ba su 500k amman yanzu zan fara ba su 200k idan aiki yayi zan cika musu 300k, sai suka ce min ba za su iya wannan aiki ba, amman ba su hada ni da wanda yake yin irin wannan aiki, suka kirashi a waya suka hada mu kai magana da shi, sai ya fada min inda zamu hadu, na je na same shi a gurin muka yi magana na fada masa komai, sai ya fada min dokokinsa cewar zan ba shi 500k a yanzu, idan aiki ya gama zan ba shi 500k kuma dole ne na bude fuskata ya gan ni, a dole na bude fuskar, sai yace min weather na yarda ko ban yarda ba, deal ya fara daga yanzu saboda ya ga fuskata, wai idan ban aminta na aikata ba, zai same mi wadanda nake son aikatawa haka ya fada musu, kuma ta aikata hakan a matsayin ni ce, a dole na aminta wasu abubuwan shi ya shirya yadda za su kasance, ban san yadda akai ya samo abubuwan da yake turawa Leila ba, sai dai idan ya aikata ya kan fada, saboda na sani, amman na fada mishi ya dakata daga lokacin da Momy ta fara zargina”

Madina bata karasa ba, Hajiya ya mike tsaye baki sake ta nufi gurin wardrobe dinta tana jin kamar mafarki take. Madina ta daga kai tana kallon mahaifiyarta.

“Na aikata duk wannan abun ne saboda Talba Hajiya, ina matukar son Talba”

Hajiya ta juyo ta kalleta hawaye na sauko mata.

“Ki kaddara baki aikata komai ba, ki rufe wannan sirrin ki aje, bayan shi wannan mutumen waya san da kin aikata haka?”

“Leila, saboda ta yarda da managar Momy da kuma hadarin da aka fada min Talba yayi na tafi gurin duba shi ba tare da ta sani ba, mun fadawa juna magana ni da ita, a ciki na amsa mata cewar tabbas ni na aikata hakan amman ba ni na sace Aminatu ba kamar yadda take zargina”

Da mamaki Hajiya take kallonta kamin ta dawo ta zauna.

“Wa sace ta? Yaushe aka sace ta?”

Madina ta share hawayenta ta hade abu da karfi.

“Hajiya na taba fuskantar Talba a office dinsa na yi masa kalamai na nuna kauna a gareshi, amman be saurareni ba, sai yai kamar be fahimci manufata ba, a lokacin na san ban yi abun da ya dace ba saboda yana a matsayin mijin da Leila zata aura, amman ganinsa da na yi da Aminatu ya saka na ji a ranar cewar baya son Leila kuma zai iya kamuwa da so na indai har zai so yarinya kamar Aminatu”

Ta kai hannu ta share hawayen dake sauko mata.

“Ranar da na fita da dare, ban san inda zan je ba, saboda bacin rai ina ta yawo ba dan na san inda zanje ba, na shiga area Igala sai na ga farar motar Talba fake gaban wani gida, har na wuce sai kuma na dawo na koma nesa da inda ya aje motar na faka tawa motar, ban san gurin wa ya zo ba, amman na yi tsammanin ko abokinsa ne ko kuma wani abun na dabam ya kawo shi. Kuma ni burina a lokacin ya fito na yi arba da fuskarsa na samu natsuwa, ba da wata manufa na yi haka ba, amman a mamakina da ya fito daga gidan sai ya fito tare da Aminatu, kuma ya rumgumeta na Wallahi a lokacin na ji kamar na mutu, domin ban taba tsammanin Talba zai iya sumbantar yarinya kamar Aminatu ba, bata da komai a yanzu kuma ita ba yar kowa ba ce, a lokacin zuciyata bata raya min cewar aurenta Talba yai ba, domin babu wanda ya san da maganar auren, cikin kuka na haskasu da motata, idan ya tako zuwa gaba sai na matsa baya, idan ya tsaya sai na tsaya, ganin ina yin baya ya saka ya ciro wayarsa ban san wa yake kira ba, ni kuma sai na ji tsoron kar wani ya tararda ni a gurin sai na baya da gudu na fice daga area gaba daya”

Ta hade yawu sannan ta kalli Hajiya.

“Idan zaki tuna ranar na fita na dade a waje, har hankalinki ya tashi, na fita ne saboda na samu sanyin zuciya na kalaman da na yi ma Talba a office, amaimakon haka sai bakincikina ya karu, na dawo gida cikin damuwa ina kuka, a ranar na fada miki cewar Talba baya son Leila, domin da yana son ta ba zai kula Aminatu ba”

Hajiya ta daga mata kai tana tuna lokacin.

“An yi haka”

“A cikin dare na yi magana da wannan mutumen da na fada masa ina son ya sace yarinyar, na fada masa yadda zai ce da kuma kalar motar da zai tafi, washe gari kuma muka je na nuna masa gidan da kaina amman na fada masa kar ya mata komai, da farko ita ma na so a tsorarata ne ta yadda zata nisanta kanta da Talba. Amman sai hankali ya tashi a lokacin da Talba ya ji an sace ta ya haukace har yake fadar cewar ya aureta kuma yana zargin Leila da Kabir a hannu a sace ta, a lokacin tabbas na ga irin son da Talba yake yi ma yarinyar a kwayar idonsa,

kuma na tabbatar idan wani abu ya same ba zai saurarawa kowa ba, domin yayi ta fadar irin abun da zai yi ma wanda ya saka aka yi mata haka”

Hajiya ta rufe baki hawayen idonta ya tsaya cak. Madina ta sauke ajiyar zuciya ta ce.

“Shiyasa sai na ce ya aje ta a cikin daji ko gona, kuma ya turawa Kabir sako saboda shi ne namiji kuma zarge shi, na saka yayi masa haka ne saboda zarginsa ya karfafa kansa, ita kuma ita Leila ta ji da wacan plan din, domin rana daya aka aikata komai sace amintun da kuma kai wasikar”

Hajiya ta kasa cewa komai sai kallonta take with shock, da ace wani ne ya fada nata yarta Madina zata aikata haka ko kuma ta aikata ba zata tana yarda ba.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

“Mi ya zo cikin kanki ne Madina? Taya idonki ya rufe kika aikata duk wannan abun? Baki yi tunanin halin da zaki jefa kanki ba? Baki yi tunanin matsalar da zata biyo baya ba?”

Ta girgiza ma Hajiya kai.

“Duk wannan tunanin be zo min ba Hajiya, har sai da na riga na aikata, a tunani asiri ba zai tonu ba, domin zan aikawa da hakan ne kawai da nufin na tsorata Leila a fasa auren, ita ma Aminatu na tsoratata ta nisanta kanta daga Talba, a tunani babu wanda zai gane, yanzu gashi Aminatu ta ga mutumen har ta fada cewar shi ne ya sace ta, garin nemansa ne ma Talba yayi hadari?”

“Be rufe fuska ba a lokacin da zai dauke ta?”

“Ya ce min be rufe ba, ban kuma san dalilinsa na yin haka ba”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Hajiya ta furta tana sake mikewa tsaye jikinta har rawa yake.

“Shi ne maganar da kika ji ina yi da Leila, ina son na tsoratata ne ta fasa auren Talba da kanta so that ni da ita duk mu rasa”

“Ba shi ne matsalar ba Madina, ke kina ganin yadda kika jefa janki a wannan halin Leila da Momy za su zuba miki ido ne kina wasa da rayuwarsu? Kina son cilasta Leila ta fasa auren Talba? Kuma kin riga kin san sirrin da suke boyewa? Momy ba zata yarda Yarta taje gidan yari ba, haka zaki ka saboda ke Leila ba zata fasa auren Talba ba, kuma Aminatu zata yi ta sheidar fuskar mutunen har a gane inda yake ya fadi cewar ke kika saka shi”

“Me kenan zai faru”

Ta tambaya tana mikewa tsaye tare da zaro ido.

“Dole za su shirya miki wata gadar da ba zaki iya tsallakewa ba, ko kuma su kashe kamar yadda sukai ma Baaba, wata kila ita ma akwai wani abu data sani shiyasa suka aikata mata haka. Madina baki san zuciyar mutane ba, kashe rai a gurin wani ba komai ba ne, musamman wannan zamanin da muke ciki, mutane da yawa suna aikata kisan kai saboda cikar burinsu da biyan bukatunsu”

“Na san na jefa kaina a matsala Hajiya, amman ba zai zama ni kadai ce a tashin hankalin ba, dole ne ni da Leila mu rasa”

Hajiya ta fashe da wani kuka ta bata san ta inda ya zo mata ba.

“Miyasa kika aikata Madina? Kin jefa kanki a Matsala, kin san hukuncin da ake yi ma wanda yai kidnapping kuwa? Kuma kin bata budurcinki, kin bata sunan gidan nan, ba ke ba ko yan'uwanki sai ya shafa, kamin ki aikata komai ya kamata ki yi tunani, ba a biyewa son zuciya Madina, zuciya tana kai bawa ga halaka ne, kuma tun ba yau ba na fada miki ki shafa kanki lafiya ki cire son Talba a zuciyarki, amman baki ji ba ana nuna muku abun da ya dace ku yi kuna bin son zuciyarku. Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Madina ta hade abun da ya tsaya mata a wuya, hankalinta be taba tashi akan abun da ta aikata ba irin yanzu da Hajiya ya zayyana mata irin matsala da hukuncin da zata fuskanta. Kasa tai da idonta zuciyarta na bugawa kamar zata fado, tafiya ta fara yi a hankali tana nufi kofar fita ba tare da ta sake cewa Momy komai ba, ta fice daga dakin zuwa dakinta gaba daya jikinta ya mutu, tsaye tai a dakin kamar mai tunanin abun da zata yi, kamin ta juya ta kalli wayar ta sako ya shigo, karasawa tai jikin gadon ta kai hannu ta dauki wayar, 8 miss calls ta tarar daga Leila sai kuma sako daya da ya shigo wayarta a yanzu shi ma daga Leila ne, bude sakon tai tana dubawa.

Kina tunanin kina da wayo? Karki fasa ki cigaba sa aiko min da sakon da kika, sai na nuna miki na fiki iya game din, tsakanin ni da ke sai an ga waye loser

Ta karanta sakon yafi a kirga bata fahimci komai ba, domin bata san ta saka a sake aikawa da Leila komai ba, wata kila kuma Leila tana kara gargadinta ne akan maganarsu ta farko.

“Ba zan ni kadai ce a damuwa da halaka ba, kamin wani abun ya faru ya kamata na dauki mataki”

Ta fada tana jin kamar kuka zai zo mata, sai karfin halin tare shi take ta hana hawayen dake idonta zubowa.

“Why? Kamar wanda akai wa asiri miyasa idona ya rufe?”

Ta zauna gefen gadon tana tambayar kanta, hawaye na sauko mata daga bisani sai ta fashe da kuka.

FARUK POV.

Ya karbi kofin da Mama ta gama shan shayi da shi ya aje.

“Amman ki daure ki cinye wainar kwan”

“Gashi ai ina ci, Allah ya maka albarka”

Mama ta fada tana murmushi, sai ya amsa da Amin ya kama hannun Sultan ya rike.

“Likitan yace ko da an sallame ki zaki rika zuwa ana miki gashi”

“Gashin nan fa ance akwai tsada sosai”

“Haba Mama idan Allah ya kawo abu ai sai ayi maka shi, samun lafiyarki ya fi min komai a yanzu”

“Duk da haka dai, bana son ka kashe kudin nan, ka samu gida ka siye ka siye dan abun hawa, sai kuma business kamin Allah ya kawo aiki”

“Inshallah haka zan yi, yanzu dai so nake ki samu lafiya hankalina ya kwanta, sai na je na kai zinarin na siyar na siye gidan da abun hawa, kuma a saka Sultan makaranta, Rafi'a ma ina son na bincika yawan kudin abincin da ta ci na biya kuma na siye komai na suna”

Mama ta dan yi shiru kamin ta kalleshi ta ce.

“Anya wai akwai cikin nan kuwa? Tun fa da tafi bata taba waiwayarmu ko sau daya tace a siya mata kaza ba ko ayi mata kaza”

“Ba zata yi ba, saboda tana ganin ta bar gidan talauci tana ganin cewar ba ni da komai to me zata tambaya? Amman ni dai zan sauke nauyin hakkina da Allah ya dora min”

Mama ta tabe baki.

“Rafi'a bata da tunani sam”

“Kowa yai na gari dan kansa, komai mai wuce nan yanzu ma ya zama kamar ba ayi ba balle kuma gaba? Shiyasa ni yanzu ba duk mace ke burge ni ba, yawancin matan yanzu kwadayi yayi musu yawa, kuma ba kowa ke tsoron Allah ba”

“Haka ne, amman ai ba taru an zama daya ba, kuma duk yadda mutum yake zai samu mai sonsa”

“Wallahi ni gaba daya aure ya fita raina Mama, ban sani ba dai ko gaba”

“Aiko yanzu ya dace ka yi shi, ka siye gida ka tare kai kadai babu mata?”

“Ga ku? Ai mai Part biyu zan siya Mama, ku daya ni daya”

“Duk da haka dai, aure cikar kamalar mutum ne, kuma idan kai auren a yanzu ai zata ji haushi ta san cewa akwai masu sonka”

“Ya zaka yi ka gane masoyan gaskiya Mama”

“Duk yadda zaka yi ba zaka taba ganewa ba, kawai dai ka auri yar gidan mutuncin kuma ka barwa Allah zabi kai ta addu'a”

Ya sauke ajiyar zuciya ya saki Sultan ya zuba hannayensa duka biyu aljihu.

“Allah ya zaba mana abun da ya fi zama alheri, ya baka mata da gari mai kaunarka tsakani da Allah”

“Ameen”

Mama ta mika masa plate din bayan ta gama cinye wainar kwan.

“Na zaka dauki shawarata, da kaje ka siye gidanka tun yanzu saboda kudi ba a wasa da su, kuma kasan mutane suna da sa ido, wani zai iya maka ture ko ma ya zo da kansa, saboda ana ganin ka dawo ka samu dukiya, kara ma kome zaka siye ka siye shi da wuri, kasan kasar nan kis ake jira kuma mutane na da hassada, wani ma yana ya tsila ido yana son ganin me ka zo da shi, kuma shi irin wannan kudin na zinari mutane suna cewa baya son ajiya fa”

“Duk yadda kika ce Mama haka za'ayi, amman dai sai jibi idan na ga yadda jikin na ki ya kara yi tukuna”

“Jiki ai yanzu Alhamdulillah, lafiya ta samu sai dan abun da ba a rasa ba, daman can damuwa ce da rashin abinci mai kyau, yanzu kuma Alhamdulillah”

Mama ta fada tana dariya, shi ma dariyar yai ya kalli Ramla data shigo rike da kula dayan hannunta kuma rike da jup.

“Salamu Alaikum”

Mama ta amsa mata tana murmushi, Faruk ma murmushin yake amman be amsa mata ba. Dukawa tai gaban Mama ta aje kofin tana murmushi.

“Daman na ce yanzu kin isa karyawa, shiyasa soya miki kayan fulawa, na miki lemun kwakwa”

“Maa Shaa Allah, har da saka kanki a wahala haka”

“Ba komai Wallahi, ya jikin na ki?”

“Alhamdulillah”

Faruk kam kallonta yake da mamaki. Ta juya ta kalleshi.

“Ban san ko kana son snacks, even though ba kai na yi ma ba, i did it for Mama amman zata iya sammaka”

Ya dan yi murmushi ya girgiza mata kai.

“No, thank you”

Ta dauki plate din data gani a gurin ta zubawa Mama snack din sannan ta matsar mata da jup din lemun kwakwa hadin gida da tai mata, sannan ta dauki daya ta mikawa Sultan.

“Gashi ka ci, ya ma sunanka?”

“Sultan”

Ya amsa mata yana mika hannu ya karba. Murmushi ta sakar masa sannan ta juya ta kalli Mama.

“An yi hoton?”

“Eh an yi hoto an gwada jini, likita yace komai zai koma daidai da yardar Allah”

“Allah ya kara lafiya, yau ina Rukaiyah?”

“Ta tafi gida, a nan ta kwana shiyasa sai nace ta je ta yi wanka ta kimtsa mana gidan”

“Okay, bari na koma gurin aikina”

“Okay Allah ya taimaka, ba yanzu zaki wuce da kwanukan ba?”

“Aa sai gobe, Sultan ko zaka zo muje”

“No fita zamu yi da shi yanzu”

Faruk ya amsa da sauri yana kama hannun Sultan, sai ta kalleshi. Ganin yanayinsa ya dan canja ya saka ta jin wani iri.

“Okay”

Ta nufi kofa ta bude ta fice. Mama ta yi murmushi.

“Yarinyar tana da kirki, kuma ina ganin kamar duk saboda kai take wannan abun”

“Ta kuwa yi a banza, ni ma na fahimci haka ai yanzu, in ba shi ba miya kawo snacks”

Mama ta yi murmushi tana karo na biyu.

“Kar dai ka ce zaka watsa mata masa a ido, ba dai wani abu ta gani ko ta ji balle ka ce”

“Mama haka suke fa, kin manta Rafi'a ita ai bayan aure ne ta tsiri wannan halin, balle wannan mai rawar kan tsiya”

“Kurciya, kana ganinta ai kasan Rukaiya ta girme ta, wannan ai ba zata wuce 20 ba Idan ta yi da 21, ban jidadi da kaki karba ba, kuma ka hanata tafiya da Sultan”

“Idan ban mata haka ba, gaba zata iya wuce gona da iri, kara dai a tsaya baki nan”

“Zan je na yi magana da abokina Shamsu na ji yadda zamu yi, maganar gidan ina son na siye na miliyan biyu, ni motar ma bata dame ni ba zan iya bari sai nan gaba”

“To ba zan hana ka ba, amman dai abun hawa yana da dadi ko da babur ne ka siye”

“In Shaa Allah”

Ya rika hannun Sultan.

“Sultan zaka zauna a nan ko tare zamu tafi”

“Tare zamu tafi ba zan zauna a nan ba”

Mama ta yi murmushi.

“Mama akwai abun da kike bukata?”

“Aa Alhamdulillah bana bukatar komai a yanzu”

“To sai mun dawo”

“Allah ya tsare”

“Ameen”

Ya ja hannun dansa Sultan suka fice daga dakin. Yana fita asibitin ya nufi gurin sana'ar abokinsa Shamsu, sai da suka gaisa sannan ya gabatar masa da abun da yake tafe da shi. Da mugun mamaki Shamsu yake kallonsa.

“Ashe dai da gaske ne ana samu kudin nan da ake fada, Allah mai iko kuma mai yadda ya so, kai kam Allah ya yaye maka matsala Faruk”

Faruk yayi dariya.

“Ya dai ba ni, amman yayi matsala gaba daya ai ba ta yiyuwa, dan'adam kullum a cikin jarabawa yake”

“Haka ne, amman kai kam ai kakarka ta yanke saka, yanzu Zinarin yana ina?”

“Yana can gida”

“To amman kasan mai siyen zinarin ne mai tsaye”

“Eh akwai wani can da muka hadu da shi Nijar dan garin nan shi haka yake, idan ya samu sai ya zo nan garin ya saida ma masu siya ya fada min ai nan sun fi tsada sama da can, ya bani number mutumen yace idan na zo nan na kira shi na masa bayani zai siya, domin ya kira shi tun can nijar din ya fada masa sunana kuma ya fada masa cewar zan kawo masa zinarin”

“To ai kamata yai kai hanzarin kai masa, ku yi cikini amman fa ya saka maka kudinka account dinka na banki domin aje kudi a gida yanzu yana da wahala”

“Haka nake so, a account din ma ba dadewa nake son su yi ba, shiyasa na same ka da wannan maganar gida nake so mai kyau kamar na miliyan biyu haka so that ina siyar da zinarin zan siye gidan”

“Siyen gida yanzu ai ba shi da wahala indai ga kudi, zan yi magana da dillalin unguwarmu na fada masa, Allah ya tsare ya saka albarka Faruk muma kuma Allah yai mana wata hanyar, abu kamar wasa ya zama gaske, wai kai ne yau da siyen gidan miliyan biyu, har yanzu fa ina kallon lokacin da ka zo kace min zaka yi sana'ar ginin nan da muke”

Faruk yayi murmushi.

“Ko yanzu ai, sana'ar zan yi saboda aikin ya zama sai godiyar Allah”

“Ko da aikin ma zaka iya sana'a ai tun da aikin nigeria yanzu sai a hankali”

“Wallahi, kasar ce sai kasheta ake kara yi”

Sai kusan azahar ya bar gurin bayan ya bawa Shamsu 5k. Asibitin ya koma bakin gate aka sauke shi ya dauki dansa suka shiga cikin asbitin, kamin su karasa ya ciro wayarsa ya shiga neman number mutumen ya kira shi, wayar na daf da tsinkewa yai picking sai Faruk yai masa sallama yana kara gyara natsuwarsa saboda wanda ya bashi number ya fada masa cewar Babban mutum ne.

“Wa'alaikumussalam”

“Ranka ya dade sunan Faruk, kwanakin baya Ayuba ya kiraka akan maganar siyen zinari har ya bani kai muka gaisa, lokacin ina nijar na fada maka idan na dawo zan kawo maka zinarin ka siya”

Alhajin ya dan yi shiru yana nazari kamin ya ce.

“Oh an yi haka, ka dawo ne yanzu?”

“Eh na dawo, shi ne nake son na ji ranar da kake free sai na kawo maka Zinari na gani”

“Kullum ai ina free indai akan sana'ata ne, zaka iya zuwa gidana yanzu ka same ne zinarin yana tare da kai?”

“Aa yana gida, amman zan iya zuwa na dauko sai na kawo mana”

“Zai kai na nawa?”

Faruk ya juya ya kalli dama da hagu domin ya tabbatar babu mai jinsa sannan ya ce.

“To a yadda aka kiyasta dai zai kai na miliyan shida”

“Okay ba mai yawa ba ne, zaka iya zuwa gida ka kawo min”

“Amman ban san gidan naka ba ranka ya dade”

“Kasan Million quarters?”

“Eh na san gurin”

“Idan ka zo a aje unguwar ka tambaya gidan Alhaji Isma'el Zabarma”

“To ranka ya dade gani nan zuwa yanzu nan”

Ya kashe wayar yana jindadi ya yaba yadda Alhaji yake amsa masa. Cira kafa yai ya karasa cikin asibitin da kuzarin, kai tsaye ya nufi inda Mama take. Zaune ya same ta a dakin tare da Rukaiya da wata kawar Rukaiya suna hira. Sai da ya amsa gaisuwar da Rukaiya take masa da kawarta sannan ya kara kusa da Mama murya kasa kasa ya fada mata yadda sukai da Alhaji.

“Zan je gida na dauko sai na kai masa”

“To Allah ya tsare, ayi addu'a dai”

“Inshallah”

Ya amsa sannan ya saki hannu Sultan.

“Sultan ka zauna gurin Mama zan je na dawo”

“Aa Dady”

“Ba dade zan yi ba zan dawo yanzu nan, na maka alkawari”

“Idan baka dawo ba zan ta yi maka kuka”

“Na yarda”

Sai Sultan din ya nufi gurin Rukaiya yana bata fuska yana son yin kuka, Rukaiya ta dauke shi ta dora saman cinyarta tana rarrashinsa. Faruk har ya juya zai fice Mama ta kira shi ya dawo.

“Kai kadai zaka je? Ba zaka nemi wani ya raka ka ba? Karbar kudi haka mai yawa Faruk?”

“Babu abun da zai faru da yardar Allah, ai ba a hannu zan riko kudin ba a account za a saka min, kuma yanzu kowa ai ba abun yardar ba ne akan kudi, kara ma kasan kai kadai ka tafi”

“To Allah ya tsare”

“Ameen”

Ya amsa sannan ya juya ya bude kofar ya fita, sauri ya fara yi gudun kar ya batawa Alhaji lokaci. Yana kawowa karshen ward din suka kusa cin karo da Ramla dake cikin shirinta na barin asibitin.

“Wannan saurin duk na minene?”

Ya kalleta sai dai be ce mata komai ba, ya wuce ta fuska ba yabo ba fallasa. Juyawa tai fa bishi da kallo har sai da ta daina hangoshi sannan ta juyo ta cigaba da tafiyarta. Dakin da Mama take ta shiga ta dubata, sannan ta kalli Rukaiya ta ce.

“Dazun nake tambayarki aka ce min kin tafi gida wanka, yanzu kuma na hadu da yayanki yana ta sauri kamar zai hade kafa, na dauka ma ko ciwon Mama ne ya tashi”

“Aa jikin Mama yanzu yayi sauki gaskiya, akwai dai inda zai je”

Rukaiya ta fada tana murmushi.

“Aiki? Ko yana duty Rana ne? Mu gashi yanzu zamu tashi”

“Aa wani abun ne dai ya taso, ai Yaya baya aikin yanzu”

Mama ta dan harari Rukaiya kasa kasa tana jin haushin yadda ta saki magana haka. Ramla ta ce

“Saboda me?”

“Aikin ne be fito ba tukuna, amman muna nan muna ta addu'a”

Wannan karon Mama ce ta amsa mata, sai tai murmushi.

“Kuma yayi karatu ko?”

“Yayi karatu aikin dai ne har yanzu, kin san kasar nan aiki ma yanzu sai kana da gata”

“Haka ne gaskiya, Allah ya kawo babban rabo”

Sai duk suka amsa da amin.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar

dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Sai da ya je gida ya dauko zinarin zan dake cikin wata jaka ta ratayawa irin ta maza, sannan ya tari wani mai achaba ya fada masa inda zai kai shi. Suna isa cikin unguwar ya tambaya gidan Alhaji Isma'el Zabarma sai aka nuna masa, mai achaba sauke shi ko'ina ba sai bakin gate din gidan. Hannu ya saka aljihu ya ciro dari biyar ya mikawa mai achaban ya cire kudinsa ya bashi canji. Gaban gidan Faruk ya tsaya yana kallon ikon Allah, wai duk wannan katon gidan da gate dinsa ma abun kallo ne, gidan mutum daya ne.

‘Wasu na tara dukiya kamar ba a mutuwa’

Ya fada a ransa sannan ya karasa gurin gate din ya gaisa da masu gadin dake gurin.

“Dan Allah nan ne gidan Alhaji Isma'el Zabarma?”

“Eh nan ne, waye kai?”

“Mun yi waya da shi yace min na zo na same shi a gidansa”

“To ka kira wayar ka fada masa kana waje, ya aiko a shigo da kai”

“Okay”

Faruk ya ciro wayarsa yai dialing number Alhaji, wannan karon sai da ya jera masa kusan miss calls uku ana hudu ya dauka.

“Salamu Alaikum ranka ya dade gani kofar gidan”

“Kai wa?”

“Faruk wanda muka yi waya da kai yanzu ka ce na zo na same ka gida akan maganar zinari”

“Okay Haka haka, ka tambaya ina Usman ka mika masa wayar”

“Okay. Wai waye Usman?”

Faruk ya tambaya ba tare da ya sauke wayar ba, daya daga cikin mazan da suke zaune a gurin ya mike tsaye ta sauri yana fadin.

“Gani nan”

Faruk ya mika masa wayar. Sai ya karba ya kai kunnesa.

“Ranka ya dade Usman ne”

“Usman a shigo da mutumen nan, a me yake?”

“A kafa ya zo ranka ya dade”

“To a shigo da shi karamin falon baki, ace masa ya jira ni”

“To ranka ya dade”

Ya kashe wayar ya mikawa Faruk.

“Biyo ni muje”

Ya bude karamar kofar gate din, Faruk ya bi bayansa suka shiga cikin gidan, Faruk sai rabon ido yake yana mamaki ace gida mai kyau kamar wannan na mutum daya ne, gida kamar na minister, ko da yake ba abun mamaki ba ne, domin masu sana'ar zinari suna da kudi sosai, su da suke ganowa ma sukai kudi balle manyan dilolin dake siye su siyar. Ko rabin gidan ba su ba aka bude katon gate din wata hadaddiyar mota ta kunno kai a cikin gida, ta doshi filin da aka tana da domin aje motoci ta faka, sau daya Faruk ya kalli motar ya dauke kai yana basarwa kar a ce masa bakauye.

“Abban Sultan mi ka zo yi gidanmu”

Ba a saba kiran da sunan ba, sai dai jin an fadi Sultan din kuma ance me ka zo yi gidan mu ya bayyana masa cewar da shi ake. Hakan yasa ya juyo ya kalli inda detection din motar yake, sai yai arba da Ramla sanye da uniform dinta na ma'aikatan jinya wato Nurse, fuska da annashuwa kamar kullum.

“Gidanku?”

Ya fada yana nuna ta da mamaki, sai ta gyada masa kai tana murmushi daya zame mata al'ada domin abu ne mai wahala kai arba da fuskar Ramla bata sammaka murmushin da take rabo ba.

“Yes”

“Hajiya Ramla sannu da zuwa”

Usman ya fada, sai ta amsa masa tana doso inda suke rike da jakarta.

“Yauwa Usman, ina zaka kai shi?”

“Alhaji ne ya ce a shigo da shi”

“Je ka zan shiga da shi”

“To ranki ya dade”

Usman din ya juya ya koma inda ya fito, ita kuma ta karasa kusa da Faruk tana murmushi dimple dinta har lutsawa suke.

“Daman saurin da kake ta yi nan zaka zo?”

Ya dan yi kamar ba zai amsa mata ba.

“Eh, da gaske nan gidanku ne?”

“Na yi kama wanda zata iya maka karya?”

“Aa kin dai fi kama da wadanda za su iya yin zolaya”

Ta fadada murmushinta, sannan ta nufi hanyar part din Mahaifinta.

“Biyo ni muje”

A tare suka jera suna tafiya, har suka isa bangaren. Hannu ta kai ta tura kofar ta bude masa.

“Bismillah”

Sai da ya fara shiga sannan ta bi bayansa, yana shiga sanyin ac da wani turaren wuta mai matukar dadi yai masa lale marhabun. Ta cire karamin Hijab din da yake kanta ta goge one seater ta sofa.

“Zo nan ka zauna”

Sai da ya kalli gashin kanta da tai parking ya sauko har bayanta, sannan ya nufi kujerar ya zauna.

“Kalli can”

Ta nuna masa katon hotonta tare da mahaifinta dake tsaye a cikin katon parlor dake cike da kayan alatu na kawata falo.

“Yanzu ka yarda ni ba makaryaciya ba ce ko?”

“Daman ban ce karya kike ba ai”

Ta yi murmushi mai sauti.

“Bari na kira maka Babana idan ba haka ba, sai ya manta da kai ya fita ya barka a cikin gidan kana jiransa”

Ta mike tsaye ta nufi wata katuwar kofa dake dayan bangaren, a lokacin data shiga bata rufe kofar ba, hakan ta bawa Faruk damar hango wani falo dake gurin a tunaninsa daki zata shiga ashe nan ma wani falon da ya ci uban wannan da kyau, ta cikin falon ya hango yadda take taka stairs ta haye sama. Sannan ya dauke idonsa yana ta mamakin ace gidansu ne, sake maida dubansa yai gurin hoton yana kallo kamar mai kwankwanto.

LEILA POV.

Haushin abun da Madina ta fada mata na cewar ta fasa auren Talba a karan kanta ne ya bata haushi har ta yanke wayar ta sauke tana jan saki. Juyowar da

zata yi sai tai arba da wata mata ta doso inda take tsaye tana sanye da uniform din masu shara. Kallonta Leila take har ta karaso kusa da ita.

“Dan Allah ke ce Leila?”

“Ni ce”

Leila ta amsa mata bayan ta gama bata mata lokaci.

“Gashi wani mutum yace na baki”

Leila ta leka bayan matar ko wata hango wani amman bata ga wanda take zargi ba.

“Ina yake?”

“Ya wuce, ya dai bani wannan envelop din yace na baki”

“Sanye da me kika ganshi?”

“Facing cap, sai kananan kaya fuskarsa da mask”

“Okay”

Ta fada sannan ta karba, matar ta juya ta koma inda ta fito, Leila ta sake dialing number Madina cikin bacin rai, wayar tai ring har ta katse Madina bata daga ba, ta jera eight miss calls sannan sauke wayar, ta bude envelop din sai ga hakora biyu da hotunan gawar Baaba sun kwado a kasa. Ihu tai taja baya da sauri ta rufe baki, hango Momy da Hajiya Saratu sun kallon inda take yasa tai saurin dukawa ta dauki hakura tana yamutsa fuska ta saka a envelope din ta dauki hoton ta saka, sannan ta doso inda suke gabanta na faduwa.

“Ke lafita?”

Hajiya Saratu ta tambaya, sai da ta kalli Momy sannan ta amsa.

“Ba komai, zan tafi gida yanzu”

“Gida kuma? Anya lafiya dai?”

“Ba komai”

Ta amsa bata jira abun da zata kara cewa ba, ta nufi hanyar ficewa daga gurin da saurinta, jikinta sai rawa yake domin ba a taba aiko mata da wani abu daya data mata da hankali ba irin wannan, inda ta faka motarta ta nufa ta bude motar ta shiga ta jefa envelop din front seat ta fashe da kuka.

“Miyasa abubuwa zasu chakude min haka? Why?”

Ta daki sitiyarin motar da mugun karfi tana jin kamar ta fisge shi ta jefar saboda bacin rai. That's how she is idan ranta ya bace duk abun da ya zo mata aikatawa take. Kwafa tai ta shiga message ta rubutawa Madina sako ta tura mata. Sannan tai ma motar key tai reverse ta fice daga gurin.

*** *** ***

Momy ta kalli kanwarta Hajiya Saratu a kokarinta na kawar da tunanin Hajiya Saratu tace.

“Allah yasa dai ba kuskure kika yi gurin bada suna ba, kin ji tace tana jun warin ja6a nan fa”

“Aa na fada masa sunan Aminatu kuma na fada masa na Leila, har ma sai da ya rubuta a jikin takardar, sai dai idan can shi yai wannan shirmen”

“To gaskiya ki koma masa ki fada masa, har yanzu shiru kuma ita wanda ake son a kulla soyayyar tsakaninsu ita ke warin Ja6a”

“Ai dole gobe zan koma na fada masa, kuma na tambaya dalilin warin da take ji, ko dai shiyasa ya ce sai ta zo?”

“Wannan ai na tsakaninta da Talba ne, yace sai ta zo wannan kuma na Aminatun da Talba ba kin ce shi ne yace zai yi da Ja6a ba”

“Eh shi ne, zan koma gobe na yi masa bayani, wata kila an samu matsala ne”

Momy ta daga mata kai ba dan hankalinta na gurin ba, tunaninta ya tafi gurin abun da Leila take yi ma ihu, domin ta lura da envelop din hannunta lokacin da zata wuce.

“To wai Hajiya na ce ita wannan yarinyar a nan zata kwana tare dashi?”

“Aa yanzu nan zan aikata gida, na bar mata dakin ne saboda bana son na yi wata abun da zai saka Engr magana, amman daga yau ma ba zan sake bari ta zo asibitin ba”

“Yauwa haka ya kamata, ko da magani sai da aikatawa fa sai ana yaki da baki magani ya fi ci, kuma idan ta koma gidan nan Leila ta saka ido ayi mata miyar ta dabam a saka wannan maganin a samu ta ci, ya ce ta taci fa shikenan bukata ta biya”

“Ko ba Leila ba, ni da kaina ma zan saka ta cin abincin ai”

“Ya ma fi, tun da ita ba maida hankali take ba, kuma idan ke ce zata iya ce amman Leila zata iya mata rashin kunya ma ko kafiya saboda Talba ya bata fuska ta riga ta raina ta”

Momy ta daga mata kai, tana wani tunanin na dabam.

‘Wato Madina sake aiko mata tai da sakon nan ko kuma me?’

Ta tambaya kanta tana jin kamar ta daga waya ta kira Leila ta tambaye ta, amman ba dama saboda kanwarta na gurin, ita kuma Momy bata yarda kowa ya ji wannan abun da suka aikata ba, Madina ma saboda rashin jin Leila ne rike sirrinta ya saka ta sani.

AMINATU POV.

Ko da ya fito ya samu Aminatu ta zuba masa komai ta zauna tana jiran ya fito. Ido ta kura masa tana kallon yadda yake cira kafarsa yana takawa a hankali ya karantar da yanayin da yake ciki, duk kuwa da irin kokarin da yake ya boye mata, da ido ta bishi har ya zauna.

“Kirjin yana ciwo har yanzu?”

“Aa ba sosai ba”

“Likita yace ka ci abincin zai zo ya baka magani”

Ta fada tana kallonsa cike da tausayinsa. Ya gyada mata kai yana murmushi, sai ta fara mika masa tea har ya mika hannu ya karba sai ta zarce da shi ta kai masa a baki, kallonta yai sannan ya bude bakin zai sha.

“Bari dai na ji zafinsa kar ya kone ka”

Ta maida kofin bakinta ta fara kurbawa kadan.

“Akwai zafi”

Ta soma hura masa, ta sake kurbawa sannan ta kai masa a baki.

“Bude bakin”

Ya bude ta zuba masa kadan.

“To hade”

Ya hade kamar yadda ta bukata sannan ya sake budewa ta kara masa, ya hade ta sak kara masa.
Wato yau ita ce babba shi ne karami kenan, dariya ce sosai ta zo masa, sai dai ciwon kirjin da yake ji ba zai bashi damar yin dariyar ba, kadan kadan take ba shi har ya sha ya koshi, sannan ta aje ta dauko plate din abincin ta fara bashi a hankali yana taunawa.

“Zauna nan”

Ya fada yana riko kwankwasonta ya zaunar da ita saman jikinsa. Ba musu ta zauna saman jikinsa tana bashi abinci a hankali yana ci.

“Na koshi”

Ya fasa yana kawarda kansa, sannan ya mika hannu ya karbi plate din.

“Kawo na baki”

“Aa bana ci”

“Why? Kin ci abinci”

“Eh”

Ta fada ba dan ta ci din ba. Sannan ta sauka saman jikin ta dauko ruwa ta zuba masa a cup ta kai masa a baki ya sha.

“I love you so much”

Ya fada yana rumgumota, har cikin ransa yake jin kaunarta. Sun dade a haka sannan ya sake ta ta aje cup din tana kokarin hada kayan abincin gefe daya Ali yai knocked dakin, sanin yadda ya tararda su dazun ya saka yanzu ya zabi sanar musu da zuwansa kamin ya shigo.

“Yes”

Talba ya fada, sai ya turo kofar dakin ya shigo hannunsa rike da ledar magani.

“Allah yasa ka ci abinci”

“Yeah na ci”

“Good”

Ya fada yana aje maganin a inda aka tana da domin aje magani, sannan ya bude ledar ya fara hada allura, Aminatu na gani ta rumtse ido. Talba ya saci kallon Ali ya ga hankalinsa ba a gurinsu yake ba, sannan ya saka kafarsa ya goge a kafar Aminatu kadan, sai ta bude ido ta kalleshi ya sakar mata murmushi sai ta maida idon ta rufe.

“Neighbor din mu ya kirani yace shi ne yayan yarinyar nan yana son ganina bla bla bla, zai zo ya same ni, wai yana son ganin yarinyar na ce masa a a, ni ma a karkashin ikona take ba, bari zan yi magana da mijinta tukuna”

Aminatu na jin haka ta bude ido da sauri.

“Wallahi da gaske ne, yayana ne na ganshi, Ya Bashir ne”

Talba ya kalleta sannan ya kalli Ali.

“Yaushe ka san makocin ba”

“An dade gaskiya, kuma abun da yasa na yarda da shi saboda Matata ta taba fada min cewar an kashe masa duka family da suke kauye Galadi, har gaisuwa na yi masa a lokacin, amman abun da yake ba ni mamaki ya akai ya zama yayanta bayan ta fada mana cewar an kashe mata kowa”

Yana kai aya, Aminatu tai karaf jiki na rawa ta ce.

“Wallahi ba karya nake ba, a lokacin...”

Bata karasa Talba ya riko hannunta ya girgiza mata kai.

“Bari na yi magana da shi, idan har da gaske yayanki ne, abin farincikin mu mu duka, kuma babu abun da zai saka na hanaku haduwa da juna, amman sai mun bincike sosai, saboda bana son abun da zai cutar da ke, ki kwantar da hankalinki okay”

Ta daga masa kai idonta na cika da kwalla, tana sauraren yadda yana murza yatsun hannunta a hankali. Ya mikawa Ali dayan hannunsa dake da cannula yai masa allura, sannan ya cire safar hannunsa ya balla magani ya mika masa. Talba ya karba da hannunsa na hagu sai Aminatu ta zare hannunta daga nashi ta zubo masa wasu ruwan ta mika masa ya karba ya sha maganin.

“Ka bincika mana shi sosai Ali, har DNA test sai anyi, saboda bana son wani abun da zai je ya dawo, kasan dai ba mu gama fita daga wani ramen ba”

“I know”

“Ina wayata?”

“Tana office”

Talba yayi shiru be ce komai ba, har Ali ya gama abun da zai yi.

“A kawo maka wayar ne?”

“Yeah”

Ali ya juya ya fice daga dakin. Ba dade ba da fita ba Momy ta turo kofar ta shigo Aminatu na ganinta ta sha jinin jikinta, ta dan matsa can kusa da gadon asibitin ta tsaya, Talba ya kalleta yana jin tausayinsa ganin yadda ta rakube yanayinta ya canja saboda shigowar Momy kawai.

“Ke je waje direba yana jiranki zaku tafi gida”

Aminatu ta kalli Talba da sauri kamar mai shirin yin kuka.

“Ai yayi waya da Mama tace zata zo ta dauke ni yanzu”

Momy ta kalli Talba dake kallonta.

“Wace ce Mama?”

“Hajiya Laraba”

“Okay baka yarda da zamanta a gidanku ba ne, shiyasa zaka kira wata ta tafi da ita ko me?”

“No ta kira ni ne, saboda ta mun yi da ita cewar yaranta za su zo su duba mai sunaki, sai na fada mata cewar na samu hatsari ina asbiti, shi ne tace zata zo ta duba ni daga nan sai ta tafi ta ita saboda tufafinta suna can idan ta dauko sai akaita can gidan gurinku”

“To ka fada mata, ya zo mata da tufafinta, gidanmu zata zauna domin ita a yanzu matarka ce”

“Toh Momy”

Ta kalli plate din abincin.

“Ka ci abinci?”

“Yeah na ci har na sha magani”

“Okay, ki jira ta zo idan kuka gaisa sai direba ya kaiki gida”

Ta karasa tana kallon Aminatu, kamin ta juya ta kalli Talba.

“Ka kirata ka fada mata ta zo mata da tufafinta”

“Okay”

Ta juya ta fice daga dakin, komawa tai gurin Hajiya Saratu ta dauki jakarta.

“Saratu zan je gida na dauko kayan kwana na dawo”

“Oh ke zaki kwana da shi? Na dauka Kabir zai kwana a nan ai”

“To zan yi magana da shi na ji, idan zai kwana nan ne sai mu dawo tare shi ya kwana a dakin mu kuma mu kwana a waje, wai kin jin yaro munafuki hatsarin nan daya faru har ya kira dangin uwarsa ya fada masu”

Hajiya Saratu ta kebe baki.

“Too shi Talba?”

“Eh, wai har yana fadar Hajiya Laraba zata zo ta tafi da Aminatu”

“Karki yarda Wallahi”

“Ai na ce masa aa, ta zo dai su gaisa a nan din. Ni zan tafi sai na dawo”

“To Allah ya tsare”

Momy ta nufi kofar fita tana kiran direbanta a cikin motar data saka shi jiranta tun a lokacin daya kawo ta asbitin, ba dan ta dauko tufafi take son tafiya gida ba, sai dan tai magana da Leila kuma ta bincika halin da yarta take ciki.

*** *** **

Momy na fita Aminatu ta zuba a gurin zata fara kuka, Talba yai saurin mika mata hannunsa.

“No no noooo, karki yi kuka na san baki son zuwa can ai, wayo zamu yi ma Momy idan ta zo sai ta tafi dake a boye”

Ya fada yana riko hannunta ya matso da ita kusa da shi, sannan ya saka dayan hannunsa mai cannula ya share mata hawayen da suka fara mata zuba. Knocked din da Ali yai ne yasa shi sakinta ya kalli kofar.

“Yes”

Ali ya turo kofar ya shigo, ya mika masa wayar, ba tare da yace komai ba ya kalli Aminatu sannan ya juya ya fice

---

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Kunna wayar ya yi ya shiga ma'adanar numbobi ya nemo number Hajiya Laraba ya yi dialing din number ya saka a speaker, sannan ya dago kansa yana kallon Aminatu dake tsaye kusa da shi tana kallon wayar. Dayan hannunsa ya saka ya zagaye madaidaicin kunkurunta, fuskar shagwaba tai, sai dai tana jin muryar Hajiya Laraba sai ta fara murmushi.

“Assalamu Alaikum”

“Amin'Wa'alaikissalam Mama ya gidan?”

“Lafiya kalau, na kira wayarka na ji ta a kashe”

“Eh na samu hatsari ne, amman dai da sauki, ina asibiti yanzu haka”

Daga can cikin wayar Hajiya Laraba ta amsa da

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, Subhanallahi, garin ya?”

In brief ya fada mata abun da ya faru sai hankalinta ya tashi sosai.

“Allah ya tsare gaba, kana waje asibitin yanzu?”

“Huda Special Hospital”

“Toh gani nan zuwa yanzu, wani daki”

Sai da ya kalli Aminatu take da zumundin a bata wayar sannan ya ce.

“Emergency, Mama ga Aminatu tana son magana dake”

“Okay tana kusa da kai?”

“Eh”

Ya mika mata wayar, tana karba sai ta raba jikinsa da nata ta nufi kofar fita, shi dai binta kawai yai da kallo har ta bude kofar dakin ta fice, a zahiri karamace amman tana da basira da wayo irin na manya. Sai da ta janyo kofar dakin ta rufe sannan ta jingina kusa da kofar ta kara wayar a kunnenta.

“Mama”

“Na'am Aminatu kina lafiya”

Hajiya Laraba ta fada cike da tausayin Aminatu.

“Lafiya Kalau, Mama ki zo yanzu ki tafi da ni dan Allah, Momy tace zan kwana a gidanta ni kuma bana son kwana a gidanta, kin san ita da Leila wulakanci suke min, ko yanzu da ta zo sai da ta fada min magana marar dadi, kuma ni dai na fi son gidanki”

“Toh gani nan zuwa yanzu Auta”

“Toh kuma Mama na ga Yaya Bashir yau”

Hajiya Laraba ta dan yi shiru tana nazari.

“Wane Yaya Bashir?”

“Yayana ne uwa daya uba daya, wanda yake zaune a nan garin”

Hajiya Laraba ta saki kirji.

“A ina kika ganshi Aminatu? Yana raye kuma?”

“Eh gidan abokin Ya Talba wannan likita nan Doc Ali makotansu ne, amman matar bata bar ni na yi magana da shi ba, kuma Ya Talba yace sai sun bincike shi”

“Toh Alhamdulillah, gani nan dai zuwa yanzu”

“Toh Mama ki zo da sauri”

Ta fada sannan ta sauke wayar tana kallon kiran screen din da kiran ke reading har lokacin, ba iya kashewa tai hakan yasa ta juya ta tura kofar ta shiga ciki ta mika masa wayar.

“Gashi nan ka kashe”

Ido ya sakar mata yana ta kallonta kamin ya kalli wayar sannan ya saka hannu ya karba, kamin ya kashe wayar Hajiya Laraba ta katse daga dayan bangarenta.

“Come here”

Ya rika hannun Aminatu ya zaunar da ita saman cinyarsa, ya mika mata wayar.

“Hold this”

Ta rike kamar yadda ya nuna mata, sannan ya karanta mata password din wayarsa yana nuna mata kowane harafi, har ya bude wayar da pin number, sannan ya umarce ta data saka so that ya tabbatar ita ma ta iya, ta saka da farko sai tai mistake sai ya sake nuna mata ta saka da kanta, sai wayar ta bude, da sauri ta kalleshi tana murmushin jindadi.

“Idan kina son ki kira wannan wajen zaki shiga”

Yana fada yana nuna mata har da yadda zata katse kira idan ta kira, sannan ya shiga can cikin wayar ya dauki shatin yatsanta as his finger print, ya nuna mata yadda zata yi ta bude wayar da yadda zata rufe.

“Amman ai ba wayana ba ce”

“Zan siya miki ta kii nan gaba, idan kin kara wayo”

Ta wara ido jin abun da ya fito daga bakinsa.

“Kai ina da wayo fa”

“Na sani ai, tun da kika iya rufe ni a cikin daki ki fita waje ki yi waya da Mamanki”

Cikin siririyar muryarta ta kyalkyale da dariyar da be taba jin ta yi irinta ba, ta rufe fuskarta da hannayenta alamar kunya ya shigar da fuskarta kirjinsa ta boye kanta. Samun kansa yai da murmushi yana jin kaunarta na kara neman muhalin a zuciyarsa ta zauna, hannu ya saka yana shafa bayanta.

“I love you”

Ya furta mata murya kasa kasa, sannan ya dagota daga kirjin nasa dake masa zafi har lokacin.

“Fada min me kika ce?”

Ta sauke kai kasa tana watsa da yatsunta.

“Ba komai”

Ta amsa sannan ta dauko carpet ta shimfida zata zauna.

“Me zaki yi?”

“Zama”

“No karki zauna a nan, zo ki zauna a gado mana”

“Gado ai naka ne, idan na zauna Momy ta gani zata iya yi min fada ma”

“Ba zata miki ba, zan fada mata cewar ni na ce ki zauna”

Ta mike tsaye ba dan ta gamsu Momy ba zata mata fadan ba, sai dan bata son yi masa gardama. Sai da ta nade carpet din sannan ta hau saman hadon ta zauna.

Kallonta kawai Talba yake kamar ya cinye ta, the way da yake kallonta sai na ka rantse da Allah his life depend on her.

“Fada min, kuna kama da yayanki?”

He just ask dan ya dauke mata hankali daga tunanin da yake ganin ta fara, sai ta kalleshi ta dan yi murmushi kadan.

“Ba sosai ba, saboda mutane suna cewa ni na fi kama da Baba, shi kuma yana kama da Innata, amman shi yana da dan haske ba kamar ni ba”

“Natural beauty... Bakinki mai kyau ne mai daukar hankali i love it”

Ta dan yi murmushi.

“Haka Inna take cewa, tace duka na fi yan'uwana kyau kuma ba gaskiya ba ne, wasu sun fi ni kyau”

“Bata ganin wasu sun fiki kyau ne, balle har ta ga muninki, kamar yadda a yanzu nake ganin kamar kin fi duka matan duniya kyau”

Dariya tai mai sauti kamar ba ita ba, domin ta san yana yi ne kawai saboda ya wasata.

“Baki karyata?”

Ya tambaya yana kallon yadda dariyarta ta kawata fuskarta ta kara mata kyau da annashuwa.

“Ka fada dai kawai”

“Bana fadar karya ai”

Ta sauke kai kasa tana kallon yatsun hannunta, sannan ta kwanta saman gadon a hankali.

“Ba bachi zan yi ba”

“Ni ma bance bachi zaki yi ba”

Ya amsa mata yana maida hankalinsa gurin wayarsa, ganin haka ya bata damar rufe ido daman barawon jira kawai yake sai yai gaba da ita. Dagowa yai ya kalleta sai yai murmushi ya mike tsaye ya isa gurin gadon ya risina ya sumbanci kumatunta sai ta bude idonta da bachi ya shiga ciki yai kwance kamar ruwa. Hannunsa ya saka yana buga bayanta irin yadda ake yi ma yara idan ana son su koma bachi take ta sake rufe idon ta bawa gadon amanar kanta. Blanket din dake gurin ya dauke ya lullba mata sannan ya dawo ya zauna saman kujerar yana kallon fuskarta, bachi take hankalinta kwance numfashin ma fita yake a hankali yana shiga cikin sukuni. Ta kusan minti ashirin tana bachin sannan aka turo kofar dakin aka shigo, Talba da idonsa ke kan wayarsa ya dago yana kallon Hajiya Laraba wacce ta shigo tare da yayanta mata uku, biyu ba za su wuce sa'ar Aminatu ba sai babbarsu. Dukansu da sallama suka shigo, sai dai shi kanwar mahaifiyarsa kawai ya amsawa. Cike da tausayin da kulawa ta karaso kusa da shi tana kallon jikinsa, a zatonta zata ga an sake gurare da yawa sai dai bata ga

komai ba bayan cannula dake hannunsa, gashi zaune a kan kujera Aminatu kuma na kan gado kwancenta da blanket din daya lulluba mata.

“Kai ne baka da lafiya ko ita?”

Hajiya Laraba ta tambaya tana yi masa kallon mamaki, sai yai murmushi ya kalli Aminatu.

“Ni ne, tana jin bachi ne shi ne ta kwanta kamin ki zo”

Hajiya Laraba ta yi murmushi.

“Ya jikin na ka?”

“Alhamdulillah, daman a kirji ne kawai na bugu kuma nan yake min ciwo, shi ma kuma da sauki”

“Allah ya tsare gaba ya kara lafiya”

Ya amsa da Ameen sai yaranta suka masa ya jiki ya amsa, sannan Hajiya ta dora.

“Gaskiya Talba baka da uwar kwarai, yanzu da baka kira ka fada mana ba, shikenan babu wanda zai san abun da ya faru cikinmu? Muna yan'uwan mahaifiyarka uwa daya uba daya?”

“No ba haka ba ne, ita ma hankalinta ya tashi ne sosai, shiyasa ba tai tunanin kiran kowa ba”

“Ba wani tashin hankali tun kamin wannan ma ai bata taba kira tace da sunan fada mana wani abu naka ba, alheri ko sheri, bana ma jin tana sa number wani a cikin familynmu, kuma ba laifinta ba ne, laifin mahaifinka ne shi da be nuna mata ba, kai ma ba dan Aminatu ta so a kira ba na san ba zaka kira ba”

Yayi murmushi.

“Wani lokacin bana son na tashi hankalinku ne, ko yanzu ina rokon alfarmar kar a fadawa Kaka”

Hajiya ta tabe baki.

“Kai da ka sani, ban taba ganin mai watse da dangin mahaifiyarsa ba irinka, su da kake son ka tashi hankalinsu ai sun sani”

Murmushi yai, daman ya san halin Hajiya Laraba indai gurin fada ne ba a barinta baya. Hannu ya saka tana tashin Aminatu sai ta bude ido ta kalleta ganin Hajiya Laraba yasa tai saurin tashi zauna.

“Laa Mama”

Ta sauko saman gadon ta rumgume ta cike da farinciki. Hajiya Laraba ta yi murmushi.

“Auta yar albarka”

“Mama na gode kika zo”

Ta fada tana kallon sauran yaran Hajiya Laraba tana murmushi su ma murmushin suka mayar mata.

“Mama na ga Ya Bashir”

“We don't know yayanki ne or not sai mun tabbatar, ki daina saka abun a ranki da yawa saboda kar ayi bincike ya zama ba haka ba ki fara damuwa”

Talba ya fada da iyakar gaskiyarsa.

“Ba a bincika ba?”

“Eh nima na ji labarin ne daga bakinta sai kuma Ali, kuma Hajiya kin san inda muka fito, ba lallai ne na yi saurin aminta da wani ba sai na yi bincike mai tsanani”

“Haka ne, kara ayi bincike gaskiya saboda gudun abun da zai je ya dawo”

Talba ya kalleta da mamaki.

“Hajiya idan har da gaske yayanta ne, ya akai baki san shi ba? Kuma kuna gari daya?”

“To ai zumuntar ce ta zama sai a hankali, yan uwan kusa na ba kowa ka sani ba balle na nesa”

“Ashe ku muka gado, Hajiya a daina ganin laifina”

Ya fada yana murmushi, sai Hajiya ta tabe baki.

“Ka ji da shi”

Ta mayar masa sannan ta zauna gefen gadon, kallon kofar dakin yai sannan ya kalli Aminatu.

“Za ku iya tafiya ai, saboda dare yayi idan Momy ta zo zan fada mata kin bi Hajiya”

“Eh Hajiya tashi muje kar ta zo”

Aminatu ta fada, har Hajiya ta bude tace wani abu sai kuma ta hade maganar ta mike tsaye.

“Ba mu riko maka komai ba, na san ko ma mun riko ba lalle ne uwarka ta bari ka ci ba, idan kuma akwai abun da kake so ka fada gobe idan zamu dawo sai a zo maka da shi”

“Aa bana bukatar komai”

“To Allah ya sauwake”

“Amin”

Yaranta suka masa sallama suka fara fita sannan Hajiya Laraba ta bi bayansu.

“Sai da safe Allah ya sauwake”

Aminatu ta fada zata juya yai saurin riko hannunta, ya sumbanceshi.

“Haka nan ake sallama da miji? Kiss me mana”

Ta kalli kofa sannan ta matso kusa da shi tai masa kiss din.

“Allah ya baka lafiya”

“Amin”

Ya sake mata hannun, sai ta fice da saurin jikinta har rawa yake kar Momy ta dawo ta ce ba za a je da ita ba. Bata yi minti biyar da fita ba Kabir ya turo kofar dakin ya shigo, sai da ya kalli ko'ina na dakin kamar mai neman wani abu sannan ya kalli Talba.

“Ina matarka?”

Talba ya masa wani kallo dake nuna he is not ready to say anything.

“Momy tace na saka mota tare da Mama Saratu”

“Hajiya Laraba ta tafi da ita”

Ya amsa a takaice sannan ya tashi nufi gadon ya hau ya kwanta yana kallon ceiling dakin. Kabir ya dan tabe baki kadan ya juya ya fice daga dakin yana ciro wayarsa ya kira Momy ya fada mata, sai ta hau shi da fada kamar shi yace a tafi da ita.

“Taya zaka bari su tafi da ita? Ban fada maka ka saka mota tare da direban da zai kawo ka ba ya kawo ta ita da Hajiya Saratu?”

“Momy Easy mana nima ko da na shigo na tarar bata nan. Already matar ta zo har ta sun tafi tare”

“Mtssss bari na kira shi”

Ya sauke wayar ya nufi wani bangaren na asibitin, iskar dake kadawa tana ratsashi, wani sanyi mai dadi na shiga jikinsa. Fitowa yai harabar asibitin ya zauna a inda mutane suke zaman domin amsa waya ko yin hira, guri ne dake da itace kamar garden kuma ba garden ba, an wadata gurin da muhalin zama na irin na sinti. Zaunawa yai ya ciro wayarsa yana latsawa, can kuma ya dago kansa yana kallon Rukaiya dake zaune gefe daya tana kallon wani gurin na dabam, murmushi yai ya kashe data ya saka wayar aljihu ya mike tsaye ya nufi inda take zaune.

“Salam...”

Ta dago ta kalleshi.

“Sannu”

“Sallamata ya kamata ki amsa”

“Wa'alaikassalam”

“Good, me kike yi a nan around this time?”

Ya tambaya yana karewa gurin kallon.

“Ina jinyar Mama”

“I say a nan not in the hospital, duk wanda ka gani asibiti a irin wannan lokacin dole ce ta saka”

Ta dan kalleshi ta sauke ido kasa.

“Gurin yana da dadin zama ne”

“Yeah, that's why na zo na karbi kudin zaman guri ai, dole ne ki biya”

Ta yi murmushi mai sauti.

“Haba karka zama AA mana”

“Waye AA?”

Ya tambaya look so confused.

“Wani Jarumi ne a cikin wani littafi dana saurara mai suna Fulani, so AA ya fi kowa son kudi a cikin book din, sunansa Sardauna, ya hadu da wata yarinya yar Sarki, tana zuwa Restaurant dinsu ta zauna, to idan ta yi bachi sai yace sai ta biya kudin bachi da ta yi”

Kabir yayi dariya.

“Aiko yayi daidai ai mata sai da haka, kuna kudi da mu muma ya kamata mu fara tunanin mafita akanku, dan haka ba wani wayo da zaki min sai kin biya”

“So yanzu dai ka zama AA kenan?”

“Ko ma AC na ji na zama din”

Ta yi dariya mai sauti.

“Yanzu dai zauna sai na ji nawa zan biya”

Ba musu ya zauna, sai tai hanzarin tashi tana fadin

“Idan ka tashi biyan naka, ka biya har da nawa, kaga ba ni kadai na zauna ba kenan?”

Kyalkyale Kabir yai da dariya, yana kallonta cike da burge.

“Ni zaki yi ma wayo ko?”

Murmushi tai masa ta juya ta fara tafiya zuwa cikin asibitin, sai ya bita da ido yana kallonta har ta bace masa.

“Cute girl”

Ya furta sannan ya sake ciro wayarsa ya dora kafa daya saman daya ya jingina da kujerar kunna date sa.

LEILA POV.

Daga asibitin gida ta nufo cikin damuwa, a harabar gidan ta faka motarta ta bude kofar ta saka kafarta daya a waje ta jingina da motar tana jin kamar tai kuka kuma ba kukan take son yi ba. Ta rasa abun da yake mata dadi, miyasa abubuwa za su zo mata a haka, a irin wannan yanayin? The most painful part is yadda Madina ta juya ya zama makiyiyarta, har tana neman ruguza rayuwarta, after auren da Talba yai a bayan idonta? Wata ta rigata shiga gidan aurenta? Kwantar da kujerar tai baya ta lumshe idonta tana sauraren bugun zuciyarta, da yadda kwakwalwarta take kawo mata abubuwa mabanbanta, tunani kala kala ta kulla wannan ta kwance, ta sake kullawa. Bata bude idon ba har sai da ta ji motsin keys din motar da Kabir yake kokarin sakawa a jikin motarsa dake kusa da inda ta faka motarta, ta bude idon ta sauke su kan Kabir. Ta sani da da ne ya ganta a irin wannan yanayin ba zai iya wucewa ba, sai ya nuna mata kulawa, zai fara tambayarta abub da yake da damunta, idan a tsakaninta da Talba ne zai bata shawara ko da ace ba zata mata dadi ba, amman a yanzu komai ya canja.

“Kabir...”

Ya juyo ya kalleta.

“Kai ma na zama makiyiyarka ko?”

Ya rufe motar daya bude ya karaso kusa da ita.

“Ya akai?”

“You change”

“You change too”

Ta kawardar fuskarta hawaye na cika idonta, sai kuma ta sake kallonsa.

“Miya ba zaka dauki abun da ya faru da ni a matsayin kaddara ba? Miyasa sai kaddara mai kyau kawai ake yarda da ita ba a yardar da marar kyau”

“Saboda ke kanki da abun ya faru dake baki yardar kin dauki kaddarar ba, taya mu zamu yarda da ita mu dauka?”

“Amma ba zan aikata hakan da gangan ba, ba zan taba kashe rayuwar da zata zo tana addabata a bachi ba, ba zan kashe ran da yau kawata zata koma tana

blackmailing dina da shi ba, i didn't do it intentionally, Wallahi ban yi dan na kasheta ba”

Ta karasa cikin muryar kuka.

“Tun ba yau ba, Leila kina da wata rayuwa, hitting people anyhow, idan ranki ya bace sai ki ce komai zaki iya aikatawa. And ba abun da yafi bani mamaki kamar yadda kuka kasa kai matar nan asibiti, babu wanda ya san inda kuka kaita, kuma kuka bar yan'uwanta yayanta jikokinta da tunanin inda take, kuma sun kasa yin komai saboda sun san ba zasu iya da gidan nan ba, har yanzu ba su sake waiwaar gidan nan akanta ba, kin san saboda me? Saboda suna tsoron kar su munana zato ace sun yi sheri za a hukunta su, and do you really think hakkin matar nan da iyalanta zai barki ki zauna lafiya? Hakkin rai? Wallahi karya ne Leila, babu wanda ya zai kashe rai ba a bisa hakki ba kuma Allah ya bar farinciki ya dawwama a zuciyar wannan mutumen, ban san abun da yake damunki ba a yanzu, amman zaki yi ta ganin abubuwa na rashin jindadi da kwanciyar hankali ta bangagori dabam dabam wani abun ma har ta inda ba ki yi tsammani ba”

Yana kai aya aka bude katon gate din gidan, direban Momy ya kunno kai ta, bayan motar Leila Momy ta saka direban ya faka motar sannan ta bude ta fito tana kallon Kabir. Karaso tai kusa da su still tana kallonsa.

“Lafiya?”

“Lafiya kalau”

Ya juya ya nufi motarsa.

“Ka je asibiti ka kwana da Talba, and Hajiya Saratu tana can, make sure ka saka Aminatu a motar nan sai su taho tare da Hajiya Saratu, direba zai koma yanzu ya dauko su”

“Okay”

Ya amsa sannan ya bude motar ya shiga, reverse yai Momy ta bishi da ido har ya fice daga gidan. Momy ya karaso saitin inda Leila take zauna ta kalleta.

“Ki same ni ciki zamu yi magana yanzu”

Tana fadar hakan ta bi gaban motar ta wuce ta hau stairs din da zai sadata da falonta.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban

daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Sai da ta share hawayenta, sannan ta dauki envelop din ta fita motar ya rufe ta fara takawa kamar mai jin nauyin kafafuwanta, kamin ta kara gaban kofar falon ma wani sabon aiki ne. Tana kai hannu ta kwankwasa kofar sai ta ji a bude, turawa tai a hankali ta shiga sai kuma ta samu kanta ta tsayawa tana kallon stairs din kamar mai tunanin hawa. Ta hade yawu yafi a kirga sannan ta cira kafarta ta fara takawa har ta isa gurin stairs din ta hau ta shiga dakin Momy. A tsaye ta samu Momy tana jiran shigowarta, maida kofar dakin tai ta rufe sai ta tsaya jikin kofar tana kallon Momy cike da damuwa.

“Zauna”

Momy ta fada tana nuna mata gadonta, sai da ta kalli gadon sannan ta karasa ta zauna, Momy ma ta karaso ta zauna kusa da ita.

“Miya faru?”

Ta Mikawa Momy envelop din, tsayawa tai kallon Envelop din kamin ta mika hannu ta dauka, ta bude cike da tsoro tana duba abun da yake ciki, mikewa tai tsaye ta zazzage abun da ke cikin envelop din a kasa sai ta matsa baya da sauri. Hakora ne da ba zata iya shaidar na Baaba ba ne ko akasin haka, sai kuma hotunan gurin da aka rufeta.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, me Madina da zama ne? Taya zuciyarta ta bushe haka? Har zata iya ciro hakoran gawa ta turo mana? Bata yarda mun gane ta ba ne?”

Momy ta nufi inda wayarta take ta dauka cikin bacin rai. Sai Leila ta kalleta tana hawaye.

“Momy that's enough...”

Momy ta kalleta.

“Dole mu yi wani abu, ba zamu zuba mata ido tana yi mana yadda take so ba?”

“Me zamu yi? Mu kasheta? Ko kuma mu fara mata abun da take mana? Momy Madina ta fada min idan har ban fasa auren Talba ba, zata tona min asiri”

“Okay shiyasa kika zauna a mota kina kuka? Me kika fadawa Kabir? Ita har ta isa ta baki umarni ki bi? Kuma kika yarda zaki nade hannayenki akan abun da kika kauna saboda wata banza? Laifinki ne tun farko na gargadeki akan karki fada mata amman baki ji ba, yanzu ai gashi nan abun da kika ja mana”

“Momy, da ban aikata ba da Madina bata yi min barazana da wannan ba, and we.....”

Ta kasa karasawa, sai ta fashe da kuka mai karfin gaske. Wani irin tausayinta ne ya kama Momy, sai ta matsa kusa da ita ta zauna da sauri tana hawaye.

“Ya isa Leila, na san yadda kike ji, ga matsalar Aminatu ga ta Madina right”

Leila ta daga mata kai tana kuka, sai Momy ta kwantar da kanta jikinta.

“Is okay, zan sama miki mafita, ba zan iya barin wasu wawayen mutane su ruguza farincikinki ba, i can't.. Ina kaunarki Leila ina kaunarki fiye da duka yayan da na haifa, zan magance miki komai, komai zai wuce and zan nuna miki kina da uwa a raye kuma jajirtacciya i promise you this”

Cikin kuka Momy take maganar cike da tausayin yarta.

“Kisan kai ba sabon abu ba ne, balle ke da kika aikata akan kuskure, ba zan wannan sirrin ya bayyana ba, mutuncin mu ba zai zuba be, babu abun da zai canja daga yadda muka tsara shi, zaki auri Talba, and dole ne Madina ta barki ki huta dole... Duk abun da yake na ki will be yours forever”

Leila ta kamkame Momy tana kuka.

“Idan Daddy ya ji zai tsane ni, kamar yadda Kabir yake min a yanzu, and Talba ba zai aure ni ba, kuma duniya zata san abun da na aikata, Momy ki sama min mafita”

“I will i will i promise, komai zai zo karshe soon”

Ta fada tana kara rumgume ta tana hawaye. Sannan ta sake ta ta dauki wayarta ta kira Kabir tana tambayar domin ta ji idan ya saka Aminatu a motar, ba karamin bacin ranta yai ba jin cewar ta ji Hajiya Laraba. Katse wayar tai tana tsaki, sannan ta kira wayar Talba, ringing daya ya daga.

“Hello”

“Ban fada maka yarinyar nan gurina zata kwana ba?”

“Eh tana jin bachi ne sosai shi ne Hajiya ta ce.... ”

“Hajiya uwarka ce? Hajiya bata san da kai ba sai da na raine ka ka girma yanzu zata nuna min fin karfi akan matarka? Taya zan fada maka yadda nake so na kira waya yanzu ka ce min wata banza ta sauy...”

“Nooo Momy karki zurfafa, ita da ke duka daya kuka a gurina, ita ma uwata ce kamar yadda kike uwata, baki koya min yadda zan raina danginki ba, dan haka be kamata ki bar ni na raina dangin mahaifiyata ba balle kuma ke da kanki ki aikata, taya kika ganin zan jidadi ki kira kanwar mahaifiyata da banza a cikin kunnuwa, just because of ta tafi da Matata”

“How dare you questioning my orders? How dare you Talba?”

Ta fada da kakkausan halshe sannan ta yanke wayar.

“Daman ance idan ka yi sake, sai ayi maka Sakkiya, abubuwa da yawa da ya kamata na aikata tun tuni ban yi ba, gashi nan ina ganin yadda komai yake juyawa, gidaje da yawa ina ganin yadda matan gidan suke mulki idan suka fada ba musawa amman ban da gidana, da wata macen ce Wallahi mijinta be isa ya

yanke hukunci ba tare da izininta, amman kalle ni Engr har saki na yai saboda na kira dansa da tsintacciyar mage, mayan gidaje da yawa mazan ne suke tsoron matansu amman ni, ni nake tsoron mijina tabbas na yi sake Saratu ta taba fada min haka ban saurareta ba amman yanzu na fahimta, duk wani kuskure da na yi a baya sai na gyara shi, Wallahi da wata mace ce umarni kawai zan bawa Talba na ce ya saki yar kauyen nan kuma dolensa ya saketa, amman dubi yadda yake min magana wai ina kiran kanwar mahaifiyarsa da banza! Hmmm”

Ta kalli Leila.

“Tashi ki wanke fuskarki ki, ki samu wani abu ki saka a cikinki kamin ki kwanta”

Ta share hawayenta sannan ta tashi ta fice daga dakin, Momy ta shiga call list din ta kira line Hajiya Saratu, sai ta Hajiya ta dauka sannan Momy ta kara wayar a kunne.

“Saratu, direba ya dawo zai dauko ki ina son ki zo gidan nan ki kwana, akwai abun da nake son mu warware tare da ke”

“Toh, Aminatun fa?”

“Wai Talba ya bawa kanwar mahaifiyarsa ta tafi da ita”

“What? Baki fada masa gurinki zata kwana ba?”

“Hmmm ke dai zai kin zo, zan je na shiryawa Engr abinci kamin ya dawo”

“Yanzu shi Talba har ya isa ki fadi abu ya tsallake?”

“To ya na iya? Ai ba ni da gata a gidan nan Saratu, sai kin iso”

Momy ta sauke wayar, tana kallon wardrobe dinta kana ganinta ka san ranta a bace yake domin har wani kashe ido take. Can kuma ya dauki wayarta ta shiga wayarta ta nemi number Madina ta rubuta mata sako ta aika mata sannan ta saka wayar a key ta aje ya mike tsaye ta nufi bandakinta ta dauko safa ta saka sannan ta kwashe hakoran da hotunan ta saka a envelope din ta nufi karkashin gadonta ta saka, kana ta sake komawa bandakin domin tsabtace kanta.

MADINA POV.

Madina yanzu aka fara wasan, ba kin zabi cigaba da abun da kika yi ba? Kina tunanin barazanarki zata haifar miki da da mai ido? Kina ganin a kanki zan bar Leila ta fasa auren Talba? Kina kara jefa kanki ne a cikin matsala, kuma kina kara nuna mana cewar baki da imani, tun da har zaki iya fasa kabari ki ciro hakoran gawa ki aiko mana, to ki saurare sakamakonki

Madina na gama karanta sakon, ta yi saurin tashi daga kwancen da take ta zauna tana kara duba number Momy, domin tana da number a wayarta kamar yadda Momy ma take da number ta.

“Kenan Leila bata ji maganar da na yi mata ba? Sai da ta fada Momy? Ko kuma dai ta yi haka ne saboda na dauka Momy ce? Ko kuma Momynce da gaske?”

Magana take da kanta tana kara duba sakon.

“Wane irin hakora kuma? Yaushe na aika da wani sako?”

A nan ma bata samu amsar tambayarta ba, sai ta fita daga message din ta shiga contact list dinta ta nemi number Alfa ta kira shi. Kamin yai picking zuciyarta har bugawa take.

“Alfa...”

“Ranki ya dade...”

“Ka sake aika sakon gidansu Leila ne?”

“Eh, na aika mata da sako”

“Saboda ne? I thought mun yi magana da kai cewar ka dakatar da aika mata komai”

“Ke dakata, ba a min tsawa, yanzu ni nake da iko da ke ba ke kika da iko da ni ba. Kina yin wasa zaki jefa kanki a matsala, kin san case biyu ke kanki ko? Bayan na Leila akwai na yarinyar da kika saka muka dauke, and Ina ta tabbacin cewar kin ji cewar yarinyar nan ta gan ni”

Baki sake Madina take saurarensa.

“Amman na cika maka kudin aikinka a kan yarinyar nan? Miyasa zaka bari yarinyar ta ganka? Wannan ba matsalata ba ce i think na yi nawa yanzu kuma sai ka samawa kanka mafita”

Yayi dariya.

“Sai dai ki sama min mafita, gidan kina son yarinyar nan ta daina ganina dole ne sai ki siye ni, idan ba haka ba duk inda yarinyar nan ta gan ni zata shaida ni kuma asirinki ne zai tonu, shi ne amfanin barin fuska bude da muke ai, saboda irin wannan kasuwancin”

“Ya kake magana kamar ba kasan da wanda kake magana ba”

“Na sani mana, ni zan miki wannan barazanar kuma na kara tunatarda ke cewar kina kara jefa rayuwarki a hatsari ne kawai”

“Ina ka samu hakoran da ka aikawa, Leila, at first na dauka kana amfani da wata atamfar ne saboda ka tsoratata, sai dan yanzu mahaifiyarta ta aiki min sako cewar ka aika musu da hakora da hoto a ina ka samu”

“Ba a tambayar irinmu ina muka samu abu, sai dai ana tambayarmu miyasa muka aikata, ke dai muradin ki a tsoratata ko? Kuma na yi aikina ya rage na ki si siyeni ko kuma ki bar ni na cigaba da abun da zai amfane ni”

“Idan Leila da mahaifiyarta suka mika lamarin a hannun hukuma, ni da kai duk rayuwarmu tana cikin hatsari, domin haka nake shawararta da ka daina abun da keke tun yanzu, kuma ka daina takurawa gawar matar nan”

“Gawar da aka aje a zaune? Aka rufe da kasa kuma aka dorawa dankin ruwa? Wahalar ta nawa kuma? Masu son su wahalar da ita ai sun yi, yanzu kuma kina son ki yi amfani da ita ki samu biyan bukatarki”

Ta lumshe ido ta bude tare da mikewa tsaye ta sauka saman gadon ta nufi windows din dakinta ta tsaya.

“Alfa me kake so?”

“Kudi...”

“Bayan kudin da na baka na aikinka”

“Wacan na abun da za a gabatar miki ne, na yanzu kuma wanda yake tsakanin ni da ke ne”

“Nawa kake bukata?”

“Zaki biya ne gaba daya ko kuma na raba miki”

“Ka fadi ko nawa kake so, zan baka amman zaka min alkawarin cewar ko ganina kai ba zaka tana nuna ka san ni ba, saboda a yanzu kana neman jefa rayuwata ne a cikin matsala”

“Haka nake so, da zarar kin ba ni wannan kudin ba zan sake waiwayarki ba, kuma ba zan sake shaidar fuskarki ba”

“Nawa kake so?”

“Miliyan talatin, idan ya miki nauyi zaki iya ba ni goma yanzu, sai idan na waiwayeki sai ki sake bani goma ko ashiri, ni bana ma matsawa mutane ko biyar kika da hali zan karba na yi sha'anina”

“Are you fucking kidding me? Miliyan talatin? Ina zan samu miliyan talatin? Ai ko rai na kashe diyar bata kai haka ba”

“Ai wannan abun da kika aikata kusan hukuncinsa daya da kisan kai, da zaki kashe rai ki biya diya da zai fi miki abun da kika aikata a yanzu, saboda wannan kina neman rufin asirinki, tsabanin biyan diya da kowa ya san abun da kika aikata”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, daman haka kake? Daman can kai baka a mana da kai? Miyasa zaka juyar da wannan abun a kaina?”

“Baki san iya yadda na yi na kawar da komai ba kamin na samu biyan bukatarki, even mai gadin gidan da aka aje gawar nan kin san yadda na yi da shi? Kin san yadda na yi na gano inda gawar take? No...! Abun da kawai kike so a tsorata Leila kuma an yi”

Ba kai aya ba ta tari numfashinsa cikin kuka.

“Amman ai ba mu samu biyan bukata ba, ban samu abun da nake so ba, Alfa karka jefa rayuwata a hatsari, zaka saka Momy ta fara bibiyar rayuwata, zaka raba min hankali gida biyu”

“Daman can baki shirya ba kika fara, mu haka muke na mu kasuwancin indai har kina son zaman lafiya, dole ne ki bani wannan kudin da zarar kin biya babu ni babu ke”

Ta sauke wayar ta katse kiran tana lumshe ido, bata taba jin tashin hankali ba irin wannan. Baya baya tai har ta isa jikin gadonta ta zauna ta dafe kanta.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, na jefa kaina a cikin hatsari, Momy zata iya kashe ni saboda Leila, kuma wannan mutumen ya sako ni gaba why?”

Ta fashe da kuka mai karfi, kamin tai saurin rufe bakinta, ta mike tsaye ta nufi kofar fita, da sauri ta fito dakinta da zimmar shiga dakin mahaifiyarta sai dai jin motsinta a kitchen yasa ta nufi kitchen din da saurinta tana hawaye. Hajiya dake aikin wanke hannu a tab ta kalleta.

“Madina lafiya”

Madina ta share hawayenta shiga message ta bude sakon da Momy ta turo mata ta mika mata wayar hannunta. Hajiya ta yarfar da hannunta dake da sanyin ruwa sannan ta karbi wayar ta shiga duba sakon.

“Miyasa kika sake aika musu da sakon?”

Ta girgiza kai tana kuka.

“Ban aika komai ba Hajiya, shi ne ya tura mata sakon da sunan ni na aika, kuma na kira shi na yi magana da shi ya ce min sai na bashi miliyan talatin, idan ba haka ba zai tona min asiri har dauke Aminatu da na yi zai tona”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, kin ga ni ko? Kin jefa kanki a matsala saboda son zuciya, kin biyewa zuciya gashi nan ta kai ki ta baro, kin saka kanki a matsala, kuma Momy zata yi komai ta cire yarta daga masifa kuma ta wankenta, ke fa? Kim dorawa kanki dutsen da ba zaki iya dagawa ba balle ki tashi”

“Hajiya ki taimaka min dan Allah, mu bashi kudi, zan yi magana da Leila”

Ta fada tana kama hannayen Hajiya ta rike duka biyun tana kuka domin hankalinta yayi matukar tashi.

“Ba bada kudin ne matsala ba, irin wadannan mutanen da kike gani dama suke nema, ko an bashi wannan kudin zai sake dawowa ya nemi wasu, idan ma mun ji da na shi na Momy ki yi yaya da shi?”

Madina ta mike tsaye hawaye na sauko mata kamar ba gobe.

“To ya zan yi? Talba zan fadawa gaskiya ko kuma yaya?”

“Idan kika fada masa gaskiya kuma, daureki zai yi, a gidan yari zaki kare rayuwarki, babu ke babu auren wani ma dabam balle Talba, kuma duniya zata kalleki a matsayin macuciya, ko wace jarida zata yi ado da ke ace kin ace matar wanda kika kauna saboda son zuciya, kin lalata rayuwarki tun da kurciyarki, ba Talba ba ko wani dabam ba zai aureki ba Madina”

Hajiya ta karasa tana fashewa da kuka mai taba zuciya.

“Kullum ana nuna muku hanya, ba ku gani, kullum kun fi son ku aikata abun da ranku yake so, a kullum ba ku kallon abun da zai biyo baya, burinku kawai, wannan abun da kika aikata zai zubar da kimar gidan nan, kuma ba kedai zai shafa ba har yan'uwanki sai ya shafa”

Hajiya ta dafe kirjin tana jin wani zafi da zuciyarta take.

“Tun ba yau ba, Madina ina ta nuna miki illar abun da zuciyarki take raya miki amman kin kasa ganewa, kin kasa ganin komai, taya zaki ce Talba ya aureki bayan kin san Momy tana raye, kin fi kowa sanin Momy ba kowa take son yana kusantar familynta ba, balle kuma kin san cewa Talba Leila zai aura, yanzu ina fa'idar abun da kika yi? Ina amfaninsa? Da kika aikata hakan ya saka Talba ya so ne? Sai dai ya kara tsanarka, bama Leila kadai ba kin saka wata wanda babu ruwanta a cikin lamarin nan, shine babban abun da zai haifar miki da matsala, da ace Leila ce kawai kika yi ma haka da mafitarki mai sauki ce”

Madina ta kalli Mahaifiyarta.

“Hajiya, da kin san abun da nake ji a zuciyata, da baki lisaffa min duk wannan abun ba, na san na jefa kaina a matsala, amman ban gane hakan ba sai yanzu, yanzu kuma mafita nake nema”

Hajiya ta yi kokarin tsagaita kukan da take ta aje wayar Madina dake hannunta.

“Taya zamu yarda cewar idan aka ba shi wannan kudin zai rabu dake? Zan iya yin magana da Momy zan iya fahimtar da ita, wata kila ta fahimta kuma tai miki uzuri, amman shi wannan fa, taya zai kyale ki?”

“Ba ni da miliyan talatin yanzu Hajiya”

“Ni zan yi mafitar miliyan talatin, kin sani ba zai gagara ba, matsalar kar ya sake waiwarmu ne yace sai mun ba shi wani kudin, kuma na san zai iya”

“Momy ma zata iya kashe ni, zata iya yi min wani abun saboda biyan bukatarta ina jin tsoron Momy fiye da wannan mutumen, domin shi da ni asirinmu daya ne, idan nawa ya tonu nasa zai tonu, amman Hajiya ba zata taba yarda asirin Leila ya tonu ba, kuma ba zata kyale ni ba, tun da har ta san da cewar na san sirrinta”

Hajiya ta kalli yarta cike da tausayin rayuwar data jefa kanta.

“Yaran zamani kenan, ana baku tarbiya kuna daukar taku dabam, ban miki irin wannan tarbiyar ba Madina, kuma ban nuna miki wannan hanyar ba”

Ta karasa tana share hawayenta, sannan ta fice daga kitchen din ta bar Madina a tsaye tana kallon kitchen kamar bakonta.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son

gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

AMINATU POV.

Kwantar da kanta tai jikin Hajiya Laraba tana jin kamar mahaifiyarta.

“Mama ko zamu je gidansu mutumen, ya nuna mana gidan Yaya Bashir ki ganshi, ni ma ina son na sake ganinsa”

“Wace unguwa yake?”

Ta dan yi shiru tana nazari kamin ta amsa.

“Ban san sunan unguwar ba, amman dai gidansu abokin Yaya Talba ne, wannan likitan ki kira shi ki tambaye shi kin ji?”

Hajiya Laraba ta yi murmushi.

“Ba zaki hakura har Talba ya gama nasa binciken ba?”

“Mama na kagu na ganshi, ba ki san yadda nake ji ba a zuciyata, ji nake kamar na runtse ido na je gurinsa”

“To bari na kira Talba ba tambaya, amman ai yanzu dare yayi ba zasu ce mun zo musu a dare ba”

“Ba zasu ce ba Mama dan Allah”

“Toh”

Mama ta kai hannunta cikin jakarta ta dauko karamar wayarta ta kira Talba ta kara a waya.

“Amman karki fada masa cewar tare za mu je, zai iya hanawa”

“Na san yadda zan masa ai”

Hajiya ta fada sannan ta maida hankalinta gurin wayar.

“Hello”

“Salamu Alaikum”

“Wa'alaikissalam Mama har kun isa?”

“Eh, magana ma nake yi da Abban su yake tambayar inda inda abokin naka yake domin su bincika”

Talba yayi murmushi kamar ya san manufar Hajiya Laraba.

“Mama mikawa Aminatu wayar”

“Toh”

Sai Mama ta cire wayar daga kunennta ta mikawa Aminatu, da sauri Aminatu ta daga daga jikinta tana girgiza mata kai.

“Aa Mama ki ce masa bana nan mana”

Sai a lokacin Hajiya Laraba ta fahimcin katobarar da tai, sai tai saurin rufe baki. Talba ya fadada murmushinsa daman yayi hakan ne saboda ya gane idan tana tare da Aminatu, domin ya san ba su isa kaiwa gida ba. Aminatu ta karbi wayar ta kai kunnenta kamar zata yi kuka.

“Hey Baby ban fada miki zan yi bincike akai ba? Why zaki takurawa Mama zai ta kai ki gurinsa?”

“Ya akai ka gane?”

“Ai na san Matata, na san zaki iya haka, ki daina damun kanki gobe zan saka a zo da shi ku yi magana, na san kin kagu ki ganshi ko?”

“Eh sosai”

“Toh zaku yi magana gobe, shikenan?”

“Eh”

“Okay i love you, ki yi addu'a kamin ki kwanta”

“Toh sai da safe”

Ya katse wayar, ta mikawa Hajiya Laraba wayar tana fada mata yadda su kai da shi.

“To kin ga haka ma yafi, gobe idan Allah ya kai mu sai ki taho da wuri”

“Toh Mama”

Ta sake kwantar da kanta jikin Hajiya Laraba. Bata daga ba sai da suka isa gidan, kanen mijinta ne dake tukin motar ya fara budewa ya fita sannan suma suka bude suka fita.

“To ka je ka kai mishi motar na san yana can yana jiranka”

“Toh”

Ya amsa sannan ya koma cikin motar. A dakin da suka saba kwana lokacin da suna gidan ta kwana tare da yayan Hajiya Laraba, sai dai Aminatu ba ta yi wani bachin kirki ba saboda tunanin haduwa da zata yi da Bashir gobe, duk kuwa da kasancewar bata kwanta da wuri ba saboda ta dade suna hira ita da Hajiya Laraba tana fada mata abubuwan da suka faru a gidan Momy lokacin da Talba ta tafi da ita har zuwa ganin da tai ma wanda ya sace ta. Washe gari ana sallah azuba Hajiya ta shigo ta tashe su sukai alwala sukai sallah, sauran suka koma bachi ita kuma ta fito falo ta zauna tana tasbihi da hannunta, daman ta saba zamanta a gidan Hajiya Laraba ta saba mata idan tai sallah azuba bata komawa bachi, tun a wacan lokacin tare da ita suke shirya abun karyawa kamin ta iya ta fara shiryawa da kanta. Tana zaune saman kujerar Hajiya Laraba ta fiton dakin mijinta dake kusa da nata dakin tana sanye da karamin Hijab. Da sauri Aminatu ta duka ta gaisheta.

“Mama ina kwana”

“Lafiya Kalau an tashi lafiya”

“Lafiya kalau”

“Baki koma bachin ba? Ai da kin koma kin kwanta zan shirya muku abun karyawa sai na diba miki wanda zaki kai masa asibiti”

“Aa Mama zan taya ki”

“To, amman kamin nan shiga dakina ki duba kan madubi zaki ga wayoyi ki dauko karamar ita ke da kati sai na kira miki mijinki ki gaishe shi”

Hajiya Laraba ta fada tana murmushi, sai Aminatu ta amsa da to, ta tashi ta nufi dakin Hajiya Laraba kuma ta nufi kitchen dinta. Gas ta fara kunnawa ta tana kokarin dora ruwan zafi Aminatu ta shigo rikr da wayar.

“Mama gashi”

Ta aje pot din ta mika hannu ta karba, ta kira shi sai da wayar ta fara ringing sannan ta mikawa Aminatu tana fadin.

“Wata kila ma be tashi daga bachin ba, tun da baya jindadi”

“Sallamu Alaikum”

Aminatu ta yi masa sallama murya kasa kasa tana jin kunyar Hajiya Laraba data cigaba da aikin da take.

“Daman na ce yau tun asuba zaki kira ni, saboda kin kwana kina tunanina, kuma kin yi ta mafarkina”

Ta dan saci kallon Hajiya Laraba sannan ta girgiza kai.

“Aa Mama ce tace na kira na gaishe ka”

Ya dan tabe baki.

“Kenan dai albarkacin Mama na ci, ba dan kin kwana kina tunani na ba, shikenan na gode”

“Ya jikinka”

“Ban ji sauki ”

“Saboda me? Da gaske?”

“Saboda baki kusa da ni”

“Sai anjima”

Ta fada tana dan murmushi sannan ta sauke wayar tana danna inda ya nuna mata ana kashewa idan ta kira ko an kirata, ma'ana gurin jan maballi.

“Miya ce miki?”

“Wai na yi mafarkinsa shiyasa na kira shi, shi ne na ce masa ke kika saka na kira shi”

Hajiya Laraba ta yi murmushi tana kallon Aminatu.

“Toh ai dan kin ce masa mafarkinsa kika yi kika kira shi ba laifi kika yi ba, ba saki san Namiji yana son ana nuna masa kulawa ba? Namiji yana son a nuna masa an damu da shi, ko da tunawa kika da wani abu da mijinki yake miki na jindadi just picked up your phone ki fada masa na tuna da abu kaza da abu kaza da kake min, zai jidadi kuma zai yi da son yai miki idan na kyautata wa ne zai so ya cigab da kyautata miki, ba laifi ba ne dan kin nunawa mijinki kulawa da jindadin wani abu, Allah yasa dai karatun da muka miki ba ki zubar da shi ba a banza”

Aminatu ta rufe fuskarta da sauri tana murmushi. Hajiya Laraba ta yi dariya.

“Ato, kin ga dai mijinki yana son ki, kika yi sake sai Leila ta kwace miki shi. Ni jiya ma ta tunanin maganar da muka yi na kwana a raina”

“Wace magana”

“Anya ba Leila ce ta saka a saceki ba? Idan ba ita ba waye zai yi haka? Ko ita ko mahaifiyarta kuma Allah kadai ya san abun da suka so su yi miki dan dai kawai Allah be ba su sa'a ba ne”

“Ni ma ina wannan tunanin, saboda tana da zuciya sosai kuma kin ga tana jin haushin na auri mijinta”

“Mijinki dai, ki daina cewa mijinki mijin wata, ko da ta riga ki shiga gidansa balle kin rigata, Allah dai ya tona asirin wanda ya aikata wannan abun”

“Ameen”

Aminatu ta fada sannan ta shiga raya Hajiya Laraba aikin. A tare suka gama komai Hajiya Laraba ta zubawa Talba nasa dabam, ta kawo na yaranta da Aminatu a falo, ta saka Aminatu ta tashe su suka fito wandanda za su karya a

nan suka karya wandanda kuma za su tafi da abincin makaranta aka zuba musu na su.
Bayan sun gama karyawa suka gyara dakunansu suka gyara falon Aminatu ta gyara kitchen ta wanke kayan da suka bata. Sannan ta koma dakin ta zuba ruwa tai wanka ta fito ta shirya cikin wani chocolate material ta saka bakin Hijab ta fesa turare.

“Har zance ki tashi ki shirya Baban su ya wuce da ke idan zai kai yara makaranta ashe kin shirya ma”

Hajiya Laraba ta fada tana rike da curtains din kofar dakin. Sai Aminatu ta juyo ta kalleta.

“Eh na shirya yanzu zai tafi”

“Eh kin san 8 suke zuwa makaranta yanzu zai fito, idan ya aje su sai ya kai ki asbitin daga nan shi ma ya shiga ya duba shi”

“Toh”

Ta mike tsaye ta fito, ta nufi kitchen din ta dauko abincin da aka zuba masa ta fito falon ta zauna. After like 5 minutes ya fito sanye da jallabiya fuskarsa da murmushi hannunsa kuma rike da keys din motarsa dayan hannunsa rike da hula.

“Amarya ce amarya data tada mana hankali”

Aminatu ta yi murmushi ta sauke kai masa tana jin kunya.

“Ina kwana?”

“Lafiya Kalau, ya gajiya”

“Alhamdulillah”

Ya yi gaba ta bi bayansa, Hajiya Laraba ta fito rike da karamar yarta dake shan nono ta rako mijinta har gurin motarsa. Yaran suka shiga baya Aminatu ta shiga gaba rike da abincin.

BATURIYA POV.

Tun shekaranjiya da Fahat ya ce mata zai zo, bata sake samun natsuwa ba, idan ta kira shi baya picking, idan ta tura masa sako baya mata reply hakan yasa ta shiga damuwa sosai, domin tana sonsa fiye da yadda komai yanzu a rayuwarta kuma ta ci burin aurensa. Ta bangaren Fahat ba dan komai yake mata haka ba, sai dan ta gane girman laifin data aikata masa ba boye masa sirrin cewar ta taba aure har tana da yaro, domin har yanzu be yi mata maganar ba, ita kuma bata nuna masa komai akan haka ba.
Rashin kulawar da bata samu a gurin Fahat ya saka ta watsar da duk wata alaka dake tsakaninta da Alhaji Idriss Ali, daman can ta shirya watsar da wannan rayuwar saboda auren Fahat da take son yi. Balle kuma yanzu da take tsoron kar

ayi wani bincike a gano tana tare da wani, ya kara lalata maganar aurenta da Fahat.
Tana zaune tana cin abincin, wani almajiri ya shigo yana sallama.

“Wai an ce ana sallama da Rafi'a”

Ba ita kadai ba har Umma da kanwarta sai da suka kalli Almajirin, domin bakon abu ne a gurinta wani ya aiko yana mata sallama, domin duk masu zuwa gurinta suna da number wayarta kiranta suke idan za su zo.

“Je ka ce waye”

Umma ta fada, sai Almajirin ya juya ya koma, Baturiya bata sake maida hannunta a cikin abincin ba, na bakinta ma kasa hadewa tai saboda tunanin wanda ke kiranta, zuciyarta sai sake sake take mata.
Ba dadewa Almajirin ya dawo ya ce.

“Wai ance Fahat ne”

“Fahat”

Baturiya ta maimaita sannan ta tashi da sauri ta shiga dakinsu ta dauko hijab dinta ta saka ta fesa turare ta fito da saurinta ta fice Umma ta bita da ido tana dan tabe baki, domin ita bata ga wani abun rawar kai da kafa akan namiji ba.
Tsaye tai jikin gate din gidansu ganin bakar motar da bata san Fahat da ita ba, sai Ramlee sai dai ba zata iya shaidar Ramlee ba ce kai tsaye saboda motar ta bata baya, lambar motar ta kalla ta tana kara raya ma zuciyarta cewar Ramlee ce, sai dai sunan Fahat da almajirin ya ambata ya saka gabanta faduwa da tunani, tana tare da Fahat din ne ko kuma ita ce ta ce ace haka saboda ta fito?
Da kamar tsoro ta karasa gurin motar ta bude front seat gabanta na mugun faduwa, sai tai arba da fuskar Ramlee tana murmushi.

“Daman na san zaki fito da wuri saboda na ambaci masoyinki”

“Kina tare da shi ne?”

Baturiya ta tambaya tana shiga cikin motar ta leka baya, sai Ramlee ta bude baki.

“Wa? Na isa? Saurayin da ko gaisawa da shi baki taba bari na yi ba? Ina zan ganshi? Ko ma na ganshi shi ai ba sanina yayi ba balle har ya shigo motata ya biyo har nan”

Bayan Baturiya ta sauke ajiyar zuciya ta kalli Ramlee tace

“Idan kina son magana da ni Ramlee ba akwai waya ba? Zaki iya kirana ta waya ai, kin san inda Umma ta ganki a nan zata min fada sosai”

“Saboda na zama annoba ko?”

“No saboda bata son alaka ta da ke kuma kin sani”

Ranlee ta dan taba baki.

“Ke kin ga nima dalilin zuwana, magana nake son yi da ke akan shiyasa na zo, magana waya bata yi kuma na san idan na ce mu hadu zaki yi da saka min rana kina dagewa saboda Fahat ya dauke miki hankali a yanzu”

“Uhmmm Fahat din da ni kwana biyu ma na rasa gane kansa”

“Ban gane ba”

“Idan na kira shi baya dagawa, idan na aika masa sako baya mayar min, yace min yana nan zuwa yana son mu yi wata magana mai muhimmanci amman har yanzu shiru be zo ba kuma be sake kirana yace min komai ba”

“To Allah ya kyauta, ni na dauka ma magana har ta yi nisa ana ta shirye shirye?”

“Ni yanzu ma ban san mi zan fadawa Yayanmu ba, dan nasan sai ya sake min magana tun da yace na fitar da miji kuma ya ji na masa shiru, iyeyen Fahat din basa son aurena da shi, wata kila shiyasa ma ya daina zuwa”

“To wai ke har yanzu baki fada masa cewar kina da da ba? Ko dai ya gano ne? Shiyasa suka hana shi aurenki?”

“Idan ya gane ai zai min magana amman be ce komai ba”

“Allah ya kyauta, ni idan ma ya fasa aurenki ai ya taimaka min domin ban gama samun kudi da ke ba”

Sanin maganar da zata iya biyo baya bayan wannan yasa Baturiya ta dauko dayar maganar da tai mata da farko a kokarinta na kawar da wannan.

“Maganar me kike son mu yi, wanda ta fi karfin waya?”

“Wallahi akan Alhaji Idris ne, mutumen nan ya bi ya takura min da maganarki, kin san su manyan mutane idan suka ji zuma a abu hankalinsu baya kwanciya sai sun gama yayinsa, kuma Wallahi yana sonki sosai Baturiya, ni da a yadda nake gani ma zai iya aurenki”

Baturiya ta yi mata wani kallo na mamaki.

“Dan Allah daina wannan maganar, taya zan auri tsoho? Ke yanzu na miki kama da wanda zata iya auren tsoho?”

“Eyeeee matsayi, wasu suna nan suna neman tsohon ba su samu ba, ke yanzu ba ki san Sugar daddy ake yayin aure ba? Indai mutum yana da rufin asirinsa yana da kudi ina ruwanki da tsufa”

“Aa ba zan iya auren tsoho ba, koma zan auri tsoho sai na auri Alhaji Idris mutumen da muka gama lalacewa a titi”

“To na nawa akai, idan can da ana samu zunubi yanzu ba sai a samu lada ba, ina ce dai muradinki ki samu kudi, shi ma wannan Fahat din ai ba dan yana da kudin kike sonsa, ba dan kurciya ba, tun da be fi Faruk komai ba”

“Ni dai yanzu ki fada min abun da ya kawo ki”

“Maganar Alhaji ce, ya matsa min yana ta son na lalaba masa ke, har albishir yace na miki zai biya miki maka kuma zai sai miki gida ya siya miki mota idan zaki yarda ki zauna da shi tsawon shekara daya”

“Baki fada masa zan yi aure ba? Na fada masa cewar zan yi aure fa ko be yarda ba ne”

“Wallahi na fada masa, cewa yai shi ina ruwansa, indai zaki ba shi abun da yake so, kin san manyan masu kudin nan suna daukar kwangilar mata fa, kuma Wallahi kika sake jiki zai miki komai saboda yana son ki, ke da ni ake so haka ai da na warke”

“Miyasa ba zaki ba shi kanki ba idan gaskiya ne, sai ni kike turawa kuma na fada miki aure zan yi amman ke da shi kun kasa fahimta, so kike na fasa auren na cigaba da wannan shiriritar ne ko kuma so kike na cigaba da yin abun da nake da aure?”

“Na dai babu bako a cikin abun da kika ambata yanzu, kin yi karuwanci a lokacin da igiyar aure take kanki ai, kuma kike dauke da cikin Faruk ma, kuma kin kashe aure kin yi karuwanci kuma kin samu biyan bukata to miye bako a ciki? Ni kina ganin idan ina da value da za so mu'amala da ni zan tsaya ina rarrashinki ne?”

Baturiya ta yi mata kallon rashin fahimta.

“Ban gane ba”

“Uhm. Baturiya shi wannan kasuwancin da kike gani yana da wani limit idan ka wuce wannan limit din,to zaka daina samun riba ne za a daina yayinka sai dai ka laba da rigar wasu kana samun biyan bukata, kamar yadda nake yi a yanzu, ke yanzu tunaninki ba baki cewar Alhaji Idris ya gama yayi na ba ne shiyasa nake kawo masa wasu?”

“Amman kuma shi ne ni kike neman ki jefa ni a cikin wuta? Abokin mutuwa kike nema? So kike ni ma na yi expire na dawo kamar ke na rasa madafa? So that mu zama Magajiya da kawar magajiya? Haba Ramlee!”

“Ya kika magana kamar kin manta wacece ni Rafi'a, ni fa na tsamoki daga bakin talaucin da kike ciki a wacan kangon gidan na maida ke mutum har kika hadu da Fahat din da kika min wannan haukar saboda shi”

“Aa ni tun kamin aurena ya mutu na hadu da Fahat, baki san inda na hadu da shi ba, ba ki san komai akan alakarmu ba”

“Okay fine amman dai ni na wayar da ke har kike wannan rawar kan ko? Har kina fada min na rasa madafa”

Baturiya ta sauke ajiyar zuciya.

“Amman Ramlee kina ganin ina cikin matsala a maimakon ki sama min mafita sai ki bijiro min da wata maganar ta dabam”

“Idan mafita kike nema ai kin san yadda zaki nemita, kuma kin san inda zaki same ni mu yi magana, ba wai ki fito haka kai tsaye ni tsaye ba?”

“Ki yi hakuri ba zan sake ba”

Baturiya ta fada ba dan ranta ya so ba, sai dan ganin yadda ran Ramlee ya bace, gudun kar ta kullace ta da wani abu, domin ta san Ramlee da mugun abu, daman kuma karuwai su gaji cuta da hassada.

“Ki je ki yi shawara akan abun da na fada miki, domin ba zaki barki da Alhaji yana damuna da maganarki ba, ya riga ya kwallafa rai akanki”

“Shikenan, zan yi tunani akai”

Ta bude motar ta fita sannan ta rufe tai tsaye tana kallon motar dake tafiya har ta daina hangota a layinsu.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

“Ba saki hada ni da wata matsala ba, ina fama da ta Fahat ki kara kin da ta wani banzan tsohon mazinaci da be san mutuncin kansa ba balle na iyalinsa, zan yi magana da shi ai, dole na ja masa kunne kuma na shata masa liyi, ai ke dole ki haukace saboda kina samu kudi da ni a wannan bakar sana'ar taki, gashi nan garin bakin kwashe kwashenki kin hada ni da yayana”

Sai da ta gama fadanta sannan ta juya ta koma cikin gidan, iyakar kokarin da tai na kawar da bacin dan da yake fuskarta ne gudun kar Umma ta gane wani abu. Da sallama ta shiga yana kirkiron murmushin karfin hali.

“Fahat din ne?”

Umma ta tambaya.

“Eh shine”

“Amman fada muka yi ne? Ko kuma me? Na ga idan ya zo ai wayarki yake kira”

“Ni ma haka na ce masa, sai yace min yau wai haka ya ga dama, wai yayi zaton ana aikowa kawai zan fito ba tare da na tambaye waye ba”

“Ashe kara da aka tambaya”

“Wallahi kuwa da na jawa kaina fitina yau”

“Toh ya kuka yi da shi?”

Umma ta tambaya domin a saninta Baturiya ta fada mata cewar iyayensa basa son aurensa da ita.

“Umma bari na dawo mu yi wannan maganar yanzu dai bari na tafi gidansu Maman Ummi ta kira ni a waya wai tana son ganina”

“Okay to ki gaishe ta”

“Okay zata ji”

Ta amsa sannan ta koma cikin dakin ta dauko jakarta ta sakala ciki hijab saboda kar Umma ta gane cewar nesa zata je, sannan ta dauki wayarta ta fice daga dakin ta fito falon tana sakar kallon Umma har ta fice tana fadin.

“Sai na dawo”

“To Allah ya tsare, tun da na ga fuskar a sake na san akwai labari mai dadi ai”

Umma ta karasa tana dan murmushi, domin rabon da ta ga Baturiya a irin wannan yanayin tun daga lokacin data fada mata cewar iyayensa basa son ya aureta. Baturiya na samu ta fito ta ari kafa tana ta zuba sauri, sai ta karya kwana sannan hankalinta ya kwanta ta ciro wayarta ta nemi number Alhaji ta aika masa kira. Few seconds yai picking muryarsa cike da nishadi.

“Hello Hajiya, ina ta kira ana min ganya daukar wayar ma sai an ga dama”

“Alhaji kana ina?”

“Lafiya dai?”

“Lafiya kalau yanzu Ramlee ta zo min da wata magana shiyasa nake son ganinki ina son mu yi magana akai”

Yayi murmushi mai sauti irin na jindadi.

“Kin gan ni nan office yau aiki ya rike mu”

“Fada min inda kake zan so na same ka”

“Gurin aiki ne fa?”

“Eh ai magana kawai zan yi da kai”

“Ki Samina naka, kusa da wani gidan sojoji zaki ga wata matuwar ma'aikata kina isowa gurin ki tsaya bakin gate ki kira zan aiko a shiga dake ciki”

“Toh”

Ta kashe wayar, ta cigaba da tafiya yana yi yana baigawa ko zata samu Napep din data fito daga liyinsu ko kuma wanda zata biyo gaba ba, amman bata samu ba hakan ya sa ta tari mai achaba ta fada masa inda zai kaita ta hau babur din. Sai da su kai nisa sannan ta tuna bata dauko facemask dinta ba, sai dai tunawa da ba wani mugun guri zata je ba yasa hankalinta be tashi sosai ba.
Tafiyar minti talatin da biyu suka isa gurin sai ta sauka achaban ta bude jakarta ta dauko kudinsa ta mika masa, yana kokarin bata canji ta ce.

“Bar shi kawai tafi da shi”

“Okay na gode sosai”

Ta koma gefe tana hango cikin ma'aikatar kasancewar gate din a bude yake kuma irin wanda ke bawa na waje damar ganin na ciki ne, kamar yadda na ciki ke gani na waje. Kiransa rai a waya ta fada masa cewar tana waje gurin gate din.

“Okay koma kusa da security ki tsaya wani zai zo ya shigo dake yanzu nan”

“Toh”

Ta amsa sannan ta kashe wayar, ta koma kusa da su tai musu sallama suka amsa ta fada musu wani ne yace ta jira shi a nan zai aiko a shiga da ita. Bata wani dade tana jira ba wani ya iso gurin da kafa ta gaisa da su sannan ya kalleta ya ce.

“Ke ce Baturiya”

“Eh ni ce”

“Biyo ni muje”

Ta bi bayansa yana gaba tana biye kanta a kasa domin bata son ta ga wanda ta sani ko kuma wanda ya santa ya gane ta, bata daga kanta ba har suka shiga ciki, musamman ganin gurin ma'aikata ce mai cike da jama'a. Kasa kasa take kallon kowa har suka haura sama hawa na biyu suka shiga wani karamin office dake dauke da mutum daya, wato Sakatarensa sannan suka ya tsaya daga nan ya nuna mata office dinsa.

“Ga office din can”

“Okay”

Ta fada sannan ta doshi kofar, ta tura ta shiga tun kamin ta rufe kofar ya mike tsaye yana kallonta fuskarsa dauke da annashuwa.

“Maraba maraba da zuwa”

Maida kofar tai ta rufe, ta karasa inda yake fuska ba yabo ba fallasa.

“Gaskiya Ramlee ta kyauta min yau, rabon da na yi arba da fuskar nan an kwana biyu, an bar ni nan sai hade yawu nake”

“Na zo nan ne saboda na yi magana da kai”

Ya nuna mata kujera.

“Zauna mana, zaki iya fadin maganarki, idan ka san wanda zata daga min hankali ce ki rike abun ki sai mu je guest house mun kebe abun mu, saboda nan kowa zai iya shigowa at any time”

Magana yake yana wani kashe mata ido kamar tsoron shegen. Sai ta tabe baki

“Da yake baka san mutumcin kanka ba, shiyasa zaka lake ka takurawa kanka cewar sai ka yi mu'amala da karamar yarinya sa'ar yarka irina, wai Alhaji ban fada maka cewar zan yi aure ba? Ban fada maka cewar ni a yanzu na daina wannan bakar sana'ar ba? Amman ka nace sai ka yi mu'alama da ni har kana neman haka ni da Ramlee”

A take murmushi da annashuwar dake fuskarsa ya gushe. Sai dai hakan be saka ta fasa fada masa abun da tai niya ba cikin daga murya ta ce.

“Kana tunanin dan ka yi min albishir da gida da mota zai saka na fasa auren wanda zan aura saboda kawai na cigaba da mu'alama da kai? Ko kuma kana tsammanin zan cigaba da mu'amala da kai bayan aurena ne? Wai kai da tsufanka har da hurhura amman idonka ya rufe baka ganin komai sai...”

Bata karasa ba ta tsayar da hannunta ta da take nuna shi da shi, jin an bude kofar dakin ta juyo da zimmar duba ko waye, sai dai kamin ta karasa juyowa Fahat ya karaso inda take tsaye rike da takardu a hannunsa yana kallonta, kamin ya kalli mahaifinsa da fuskarsa take a hade ya karasa gurin tebur din ya aje masa takardun.

“Fee'at mi kike a nan?”

Ta dan yi murmushin karfin haka dake hade da mamaki tana sauke hannunta daga nuna Alhaji da take.

“Am... Ha.... Eh... Na.. Na.. Nazooo.. Gurin... Abokin Babana ne...”

Da mamaki Fahat yake kallonta yana karantar yadda ta rasa matsuwarta da kuma ya tararda ita tare da mahaifinsa.

“Daman ka santa ne Abbah?”

Ya tambaya yana kallon mahaifinsa, Alhaji Idris ya hade yawu da karfi yana kokarin daidaita kansa.

“Eh... Yar abokina ce... Na ce ta zo ta karbi abu ne...”

“Ita ce wanda zan aura ai”

“Wannan...?”

Alhaji Idris ya nuna Baturiya da sauri yana zaro kamar wanda ya ga wani abun tsoro.

“Yes”

Wani uban gumi ne ya karyo ma Baturiya, wata muguwar mutuwar tsaye tai da mamaki.

“Fahat... Alhaji Idris Ali ne mahaifinka?”

“Yes, and it seems like you know each other...”

Ya fada with confused, domin bata taba nuna masa ta san mahaifinsa ba, duk da yake ba taba zaunar da ita ya fada mata waye takamaiman mahaifinsa nasa ba, kuma ba zama lalle ace mahaifinsa ya san ita zai aura ba saboda ya ce a gurinsa kuma da mahaifinta yake alaka ba da ita ba.

“Allah sarki...yarinya mai kirki.... Allah sarki tana da tarbiya sosai.... Ai ban san ita ba ce, mahaifinta yana da kirki sosai abokina ne yanzu ma shi ya aiko ta ta karba masa sako...”

Alhaji Idris ya fada yana dariyar data zame masa dole. Fahat ya kalleshi cike da zargi.

“Mahaifinta ya rasu Abbah”

Sai Alhaji Idris ya kara fada da dariyarsa....

“Aha... Aha... Aha.. Haka ne.. Wallahi... Wallahi... Ya rasu... Ka san sabo... Na ga kamar yana raye.... Haka...ne.. Allah ya masa Rahama... Ke. Baturiya kike ko India sai ki tashi ya kai ki gida ai, ba yanzu zan tashi aiki ba ni da sai na sauke ke ki...”

Ya karasa yana saka babbar rigarsa ya share gumi dake sauko masa duk kuwa da irin sanyin ac dake office din.
Baturiya da hawaye ya gama wanke mata fuska ta share hawayenta ta maida kanta masa.

“Zan hau Napep”

“Muje na sauke ki mana”

Fahat ya fada, yana jin wani irin abu a zuciyarsa narar misaltuwa, domin a yanzu ya soma yardar da wani abu da zuciyarsa ta taba raya masa akan Baturiya a lokacin da ya ga mai kama da ita a gidan hutawar mahaifinsa yaki yarda da zuciyar tasa.
Wucewa yai gaba ta bi bayansa tana tafiya kamar kazar da kwai ya fashewa a ciki, bata taba jin kunyar data hana ta numfashi yadda ya kamata ba irin wannan, a yau ba jin take kamar kasa ta bude ta shige ba, ji take kamar ta mutu gaba daya ta huta. Sai da Fahat ya isa gurin motarsa da kusan minti goma sannan ta iso ta bude motar jikinta na rawa ta shiga ta zauna ta rufe motar ta kasa kallon inda yake. Shi ma be kalleta ba har yayi ma motar key ya suka bar harabar ma'aikatar.
Uffan bata ce masa ba shi ma be ce mata ba har suka isa kofar gidansu, ya faka a inda ya saba fakawa, sai ta kasa bude motar ta fita kuma ta kasa kalle inda yake balle tai attempting din yi masa magana.

“Baki taba fada min ko nuna min kin san mahaifina ba, miyasa kike boye min abubuwa ne? At first na dauka auren da kika taba yi ne kawai abun da zaki boye min”

Ta kalleshi da sauri.

“Fahat waya fada maka na taba yin auren?”

“Bincike, Fee'at ko a cikin masa kai abu ba zai taba boyuwa ba, domin wata rana zai fito kowa ya gani ko ya ji, balle babban abu kamar wannan, a lokacin da na, na yi ta kokarin karyatawa saboda baki fada min ba, amman daga baya na yarda saboda gaskiya ce ko na yarda ki akasin hakan, na ga laifinki sosai a lokacin kuma kin bata min rai, amman na yi ta kokarin danne zuciyata na ganin ban ga laifinki ba, kuma a haka na ayyana a raina cewar zan iya aurenki saboda ina sonki, wannan ya saka na kaurace miki na kwanakin nan saboda na auna son da kike min kuma na nuna miki girman laifin da kika aikata”

Be karasa ba ya tsaya saboda bacin dake zuciyarsa dake saka shi jin kamar zai amayar da zuciyar daga kirjinsa, domin muryarsa har rawa take kamae ba tashi ba. Ta kalleshi tana kuka marar sauti irin wannan dake shiga zuciya ya danne numfashi.

“Ban boye...maka dan komai ba, sai dan ina tsoron an rasa ka Fahat, ina jin tsoron kar ka san cewar na taba aure har ina da yaro ka fasa aurena... Kuma Wallahi ban san cewar Alhaji Idris mahaifinka ba ne... Ban sani.. Ba Fahat”

“A lokacin da na ganki a office din, da farko na yi tunanin ko kin kawo karata ne ko kuma kin zo ki roki mahaifina ya bar ni na aureki ne, sai dai na karanta yanayinki ke da shi sai na fahimci akwai wata alaka mai karfi a tsakaninku, domin na taba ganinki a gidansa amman ban bar zuciyarta ta kulla abun da take son kullawa ba saboda na kyautata miki zato, na rasa gane wace irin macece ke Rafi'ah, taya zaki yi taraiya da mahaifina kuma a haka zuciyarki ta daya miki aurena daidai”

“Billahil Azeem ban san Alhaji Idris mahaifinka ba ne Fahat, ban sani ba”

Ta fada tana Fashewa da wani irin kuka.

“Na ji, fitar min a mota”

Ta bude motar ta fita still tana kuka kamar ranta zai fita, wani mugun kallo Fahat ya watsa mata yana jin wani irin tsanarta a zuciyarsa domin kazantarta ta shahara a gurinsa, bayan boye masa asalin aurenta yanzu kuma ya gama fahimtar mu'alamar ta da mahaifinsa, domin da farko ne yayi ne kawai saboda ya bugi cikinta kuma ta bashi damar fahimtar komai.

LEILA POV.

A gidan Hajiya Saratu ta kwana a dakin Momy. Momy kuma ta kwana a bangaren Abbah, bata dawo bangarenta ba sai da safe shi ma saboda ta zuba

masa nasa abun karyarwa ne da yan aikinta suka gama gadawa. Bayan Momy ta gama shiryawa Daddy komai nasa na karyawa sannan ta juya zata fita.

“Ina ganin gobe a asibiti zamu yi breakfast da lunch da dinner”

Momy ta juyo ta kalli Daddy da mamaki.

“Asbiti kuma?”

“Eh, kin san mun saba yin breakfast da lunch tare every week, so wannan weekend din Mu'az yana asibiti a can ya kamata mu yi tare da shi zai jidadi”

Daddy ya fada bayan ya kai soyayyen dankwali bakin. Sai ta amsa masa domin ta san bata isa ta musa masa ba, kuma bata isa ta nuna masa bata so ba, saboda ta san yadda yake jin Talba, abu kadan zai iya munana mata zato.

“To Allah ya kaimu, a shirya komai kamin lokacin”

Ta fada sannan ta juya ta fice tana tabe baki, bangarenta ta dawo bacin rai da damuwar da take ciki ba zai barta ta tsayawa yin breakfast tare da Daddy ba, shi kuma be damu ba domin ya saba time to time ta kan yi breakfast dinta ita kadai ba tare da shi ba, ko kuma shirya masa abun karyawa ya ci shi kadai kuma tana a zaune kusa da shi ba tare da ta ci ba. Da mamakin maganar da Daddy yai mata ta dawo bangarenta ta shiga dakinta ta samu Hajiya Saratu tana karyawa, kusa da ita ta zauna tana labarta mata abun da Daddy ya fada mata.

“Tun ba yau ba ai ina ta nuna miki hanya amman kika rufe ido gam kika toshe kunnuwa ke ba zaki saureare ni ba, yanzu ai ga irinta nan”

Momy ta daga kai.

“Ai ko jiya sai da na tuna da maganarki, na ce da na bi shawararki da yanzu ba wannan labarin ake ba, shiyasa na ce ki kwana a nan saboda mu san yadda za a bullowa lamarin nan”

“Bullowa lamari ya wuce ki tashi tsaye, ki kama mijinki hannu biyu ya zama kamar waina a tanda, yanzu irin wannan kudirin da yai na cewar aje can a ci abinci idan isassun mata ne ya isa ya yanke wannan hukuncin ba tare da ya shawararce ki ba? Ke kina ganin idan wata Hajiyar ce mai amsa sunanta Talba har ya isa ya taka dokarki balle ya fakaici idonki ya aurowa yarki kishiya wata yar kauye jahila?”

“Abun da na gama tunani kenan jiya, sai a yanzu nake ganin illar tsallake maganarki da nake ta yi Wallahi”

“Yanzu ni abun da nake ganin yafi kawai ayi miki na mallaka tsakaninki da mijinki, a mallake miki kowa har Talban, ai yawancin matan manyan gidaje haka suke yi, sai ki ga ko kallonsu ba a son yi saboda tsoron”

“Gaskiya ina son irin wannan ta yadda idan na fadi magana daya ta zauna kenan ba canji. Bayan shi kuma akwai wata matsalar”

Hajiya Saratu ta dauki kofin tea ta sha ta aje tana kallon Momy.

“Wace matsalar ta Aminatu?”

“No”

Cewar Momy tana kallon Leila wance da shigo sanye da gown din doguwar rigar atamfa kamar kullum kanta babu mayafi. Kusa da Momy ta zauna cikin yanayi na tausayi da ramar fuska irin na tashin hankali.

“Mama Saratu Good morning”

“How are you Leila? Baki jin dadi ne?”

Momy ya janyota jikinta ta kwanto da ita cike da tausayinta.

“Ina lafiya ita kuma kawa ta saka ta gaba”

“Ban gane ba, kawa kamar ya?”

Momy ta sauke ajiyar zuciya tana tunanin ta inda zata fara bawa kanwarta Saratu labarin abun da ya faru, sai dai ya zama dole ta fada mata komai saboda amsawa kanta mafita.

“Kuskure ne ya faru, akwai wata mai aiki da na yi wata tsohuwar da muke kira da Baaba idan zaki tuna”

“Na san Baaba kam, ba ta bata ba?”

“Ba bata tai ba, mutuwa tai”

Cike da mamaki Hajiya Saratu take kallon Momy.

“Amman aka ce mana fa bata”

“Mun yi hakan ne saboda a rufe komai, abun da ya faru muna zaune Falo tare da Amal, sai Leila ta shigo cikin fushi ta nufi dakinta, to a lokacin Baaba na tsaye stairs tana mopping, a maimakon Leila tai mata magana tace mata ta bata waje ta wuce sai ta fisgota ta hannu ta jefar, kin jikin tsufa, sai matar nan ta gangaro ta fado kasa, tun da ta fado bata motsa ba har muka dauke ta zuwa asibiti, kamin mu isa asibitin ta farfado tai kalmar shahada tana fadin kafarta kanta sai kuma yai shiru, na faka mota na taba ba ban ji alamar numfashi ba, sai na yi zaton ta mutu kuma kin san idan muka ce zamu je asibiti dole kowa zai yi, ga Leila sai kuka take min, na rasa yadda zan yi da ita sai na yi tunanin binneta”

Hajiya Saratu ta gwalo ido tana kallon Momy da mugun mamaki da kuma tsoro, Leila kuma ta fashe da kuka tana shigar da kanta jikin Momy tana boye fuskarta.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu

sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

“To kika yi yaya da gawar?”

Hajiya Saratu ta tambaya baki sake tana mamaki yadda Momy ta iya aikata wannan abun. Cike da nadama da damuwa Momy ta ce.

“Mai gadin tsohon gidan gonata na kira, na fada masa ina son ya haka min rame saboda na zuba wasu kudade da gwalgwalai, gudun kar yayi wani tunani ya saka na ce yayi ramen a tsaye kuma na fada masa a cikin dare nan nake son yayi min shi, a take a fasa bangaren da muke aje tankin ruwa ya yi dogon rame, sai na isa gidan ya tsaya a gaba ya marasa ramen, sannan nace ya fita waje ya tsaya daga waje ko da zai ga wani mai zuwa, ni da Leila muka dauko gawar muka saka a zaune cikin ramen saboda ba zai isa mu kwantar da ita ba, haka dai muka saka a takure muka rufe, sannan ya kira shi ya dawo na fada masa cewar na aje dukiya mai yawa a gurin, kuma saboda na yardar da shi ne yasa na yi haka, bam yarda ya fadawa kowa na yi ajiya a gurin ba ko da kuwa matarsa saboda za a iya budewa idan kuma aka bude shi zan zarga, sai na saka ya dauko takin ruwa ya mulmulo shi zuwa gurin kasar na ce ya sika shi da ruwa, ban bar gurin ba sai na tabbatar ya cika tankin da ruwa”

“To yanzu ina mai gadin yake?”

“Wallahi ban sani ba, lokacin da Madina ta fara yi mana abubuwan nan, naje duba shi aka ce wai ya tashi daga gurin tare da matansa da yayansa, kuma babu wanda ya san inda suka koma, har garinsu na saka an bincika min ance baya can, ban san inda yaje ba, gidan ma an rufe shi da padlock da na so a bude amman ina tsoro ban san ko gawarsa ce a cikin gidan ba ko kuma wani abun, kar na shiga ciki na jefa kaina a matsala kuma kar na kira mutane a tararda wani abun asirinmu ya tonu”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, kai Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, Allah ya tsare mu da mummunar kaddara, domin wannan ita ake cewa mummanar kaddara”

“Shi ne sai...”

Momy ta zayyana ma Hajiya Saratu komai from A to Z, na abun da Madina take mata har zuwa jiya da ta aiko mata da wannan wakon. Hajiya Saratu ya jinjina kai tana kallon yar'uwarta.

“To ai ni har na fasa wanne ya fi bani mamakin tsakanin abun da kika aikata da kuma wanda Madina take yi, yanzu Fisabilillahi duk kin san da wannan abun amman kika rufe baki fadawa kowa ba?”

“Gani na yi ba wani abun dadi ba ne da zaka yi ta yadawa duniya, kuma kin san halin mahaifiyarmu tana jin maganar nan zata fitine ni”

“Ai ba dole sai ta jiya ba, a tsakaninmu ma sai mu samawa kanmu mafita, yanzu da kin fada min wannan abun tun wuri ai duk be kai ga haka ba, balle har ita Madina ta samu wata dama ta yi ma Leila zagon kasa”

“Yanzu dai aikin gama ya gama, mafita muke nema shiyasa ma nace ki zo nan ki kwana, domin abun ya daure min kai, duk tunanin da na yi sai ga kamar ba mafita ba ne”

“Yanzu ita Madina ko d ace Leila ta barta sak ta yarda ta auri Talba saboda bata da kunya ko?”

“Ai da ta san kunya da bata aikata abun da take aikatawa a yanzu ba, duk kuwa da ta san da cewar an gano ita ce, shiyasa ai jiya na aika mata da sako”

“Kika ce mata me?”

Hajiya Saratu ta tambaya, Leila kuma ta dago tana kallon Momy domin bata san Momy ta aika mata da sakon ba. Hajiya Saratu ta girgiza kai bayan Momy ta fada mata sakon data tura mata.

“Wani lokacin kina ba ni mamaki yaya, kina babba amman tunaninki kamar na autar mu, ke da kike neman mafita kuma zaki yarda ki tura mata wani sako irin wannan?”

“To ya zan yi Saratu? Ta saka Leila a gaba, ga tashin hankalin da muke fama da shi na Aminatu ita kuma wannan ta kunno kai tana son kara mana wani”

“Ai ba zaki nuna mata komai ba, so that tai ta zaton kuna jin tsoronta, daga nan zamu samu sa'a ku cafke kafarta ku jefa rame”

“Taya, a yadda na fahimta ba zata daina abun da take ba saboda bata samu cikar burinta, kuma kin ga tana tsoron asirinta ya tonu na sace Aminatu da tai ya zama ita kadai ce a kan case din, so take ta jefa Leila ciki ayi mutuwar kasko”

“To ai wannan kadai ya isa ya saka bi bita sannu sau da kafa har ki samu sa'arta”

“Yanzu me kike ganin za'ayi?”

“Me kuwa za'ayi da ya wuce a binneta”

“A binne ta kuma?”

Wannan karon Leila ce tai tambayar cike da mamaki.

“Eh mana, mai neman mutuwa ba kamata yai ka tura shi a rame ya mutu ba, ke yanzu ban da shashanci irin na ki irin wannan sirrin ai ba abari ya fita, mutane da yawa suna aikata irin wannan abun wasu ma dagangan suke amman basa barin kowa ya san abun da suka aikata”

“Ni ma abun da na yi ta nuna mata kenan”

Momy ta fada tana kallon Leila. Hajiya Saratu ta ce.

“Ko da saboda irin wannan abun, ya saka mutane suka daina binne gawa sai dai a jefar, saki ki ance an tsinci gawar wane ko wance a guri kaza ba a san wanda ya akashe ta ba, wannan ko Madina bata yi ba wai mai gadin zai iya yi muku idan ya san me muka aje a gurin kuma akai sa'a dan duniya ne, gaskiya kin yi sake Yaya ai jefarwar ake, sai ku samu wani rame ko bakin ruwa ko rijiya ki jefata”

“To kuma idan aka gano gawarta fa na ce mi? Lokacin da abun ya faru dare ne ba safiya ba ko rana, domin tana mopping din dare ne, a lokacin mopping biyu take mana saboda ta san bana son kazanta tsantsin gurin ne ma da be gama bushewa ba ya kara janta ta fadi”

“Sai ki ce kin aiketa ta siyo miki wani abu, amman irin wannan abun ba dan kuna yan babban gida ba ai da police ma madai za su iya gono karya ne domin za su iya fadada bincike su gano gaskiya, ai ko Amal da Kabir be kamata su sani ba”

“Amal a gaban idonta komai ya faru, amman ban fada mata yadda na yi da gawar ba, sai dai na gargade na ce ko da wasa ta fadawa wani a cikin gidan nan abun da ya faru sai na kasheta, Kabir kuma nace idan ya fadawa wani zan tsine masa”

“Ba dan haka ba kam, da Amal ta tona miki asiri. Allah ya tsare gaba kuma sai yi taka tsantsan domin za a iya bincikar gidan nan naki fa, a yanzu din ma baki san miye a ciki ba tun da mai gadin ya gudu kuma an rufe gidan”

“Shi me tsorona Wallahi, ni da ina tunanin ko na samu wasu na sa a bincika min gidan?”

“No ai karin tonon asiri ne, abun da ya kamata ki yi kawai ki saka a bankawa gidan wuta a kone ko'ina da komai da komai dake cikin gidan, kin ga ko akwai gawa ba zata shafe ki ba, domin kamin ki bude gidan masu kawo agaji sun rigaki kuma komai ya kone”

Momy ta dan yi shiru tana nazari.

“To idan mun yi haka ita kuma Madina fa?”

“Madina na fada miki binne ta za'ayi”

“Ni fa ban gane binnewar nan ba”

“Gurin wannan bokan zan je yayi mana aiki, ko dai a halbeta ta mutu ko kuma a canja mata gari taje can tai ta hauka”

Leila ta girgiza kai.

“Haba dai mu da muka neman mafita sai kuma mu sake aikata wani laifi? Haba dai mu ji da hakkin dai mana, kar a sake aikata wani abun da zai zame mana fitina, ni abun bokanyen nan ma ba wani yarda na yi da shi ba, gashi nan wannnan da akai ma Aminatu har yanzu shiru kamar ba ayi komai ba”

“Karki damu, komai sai kama ki bar gaggawa”

Leila ta juya ta kalli Momy tana girgiza mata kai.

“Momy aa dan Allah, kar a sake kashe wani rai, wacan kan kuskure ne, gashin alhakin yana ta bibiyata balle kuma idan muka kashe da ganganci”

Momy ta daga mata kai.

“Shikenan, ni ma hakan be min ba, zamu canja wata shawarar dabam, yanzu tashi ki tafi ki kaiwa Talba abun karyawarsa”

“Toh, amman Momy dan Allah dan Annabi Karku kashe Madina dan Allah, idan ma ya zama dole ayi to a nisantata da garin nan amman kar mu kasheta, ita ma zuwa zata rika min a mafarki tana fargita ni kamar Baaba, kuma kin riga kin tira mata wannan sakon dole za a zarge mu”

“Ba zamu yi hakan ba, ki kwantar da hankalinki, ke ma kin san ai ba zan yarda na kara wani kuskurenba”

Ta gyada kai ta share hasayenta ta tashi tsaye ta fice daga dakin daga Hajiya Saratu har Momy binta sukai da kallo sai da ta fice sannan Hajiya Saratu ta kalli Momy ta ce.

“Yarinyar nan bata da wayo sam”

“Ina fa, kin ga garin wannan sakarcin nata ne har kawarta ta ji komai, ai ba zan biye nata ba ta kai ni ta baro, yaushe zaki je gurinsa?”

“Aa ni yanzu da na shirya ai ba zan dira ko'ina ba sai gidansa, irin wannan babban lamari har sai an kwana kansa? Daman kuma ina je saboda na Aminatun nan yanzu kuma sawun giwa ya take na rakumi”

“To, gama karyawa ki shirya ki tafi, daga nan ki fada masa har yanzu ba mu samu ta ci na miyar ba, idan akwai yadda zayi a canja mana da wani sai ya fada, kudi ba matsala ba ne ke kin sani. Ni ma bari na shirya na tafi asbitin”

Momy ta karasa tana mikewa tsaye.

“Zan fada masa komai, har na warin da Leila ta ji zan fada masa”

“Toh, idan zaki tafi ki min magana na baki ATM dina, idan kuma transfer za a miki ya ma fi sauki”

“Wannan kuma ki bar har sai ya fadi abun da za a bashi”

“To ba matsala, Allah yasa mu ji alheri”

“Ameen”

Momy ta fice dakin ta bar Hajiya Saratu da mamakin da ya ki fita cikin kanta.

FARUK POV.

Ya kusan minti talatin zaune a falon, sannan Ramla ta fito a kofar data shiga tare da mahaifinta suna tafe suna hira yana dariya, kana ganin su kasan akwai shakuwa mai karfi a tsakaninsu. Sai da mahaifinta ta fara zaunawa saman kujera sannan ta zauna kusa da shi tana murmushi, Faruk kuma ya mike tsaye ya karasa inda yake mika masa hannu suka gaisa. A lokacin ne mahaifinta ya kalleta.

“To Madam a bani guri business zamu yi”

Ta yi dariya mai sauti.

“Dady korata ma kake yi?”

“Eh mana, kin ga ai ni har yanzu ban san nawa kika dauka albashinki ba, dan haka ba zan bari ki san sana'ata ba, kudi be fi kudi ba”

Ta mike tsaye tana dariya.

“Na ji amman idan an gama a bani la'ada ta”

“Na ji”

Mahaifin ya fada sannan ta kalli Faruk ta dauke kai ta fice daga falon, ko kadan bata nunawa mahaifinta ta san Faruk ba, a cikin dakinsa m da ta matsa masa ya fito cewa tai wani ne a falo yake nemansa kuma ya dade a zaune. Bayan ta fice mahaifinta ya karbi Zinarin dake ciki wata karamar doba, yana dubawa, sannan ya ciro wayarsa ya kira wani yaronsa.

“Ka zo nan falo da kayan awo ka auna mana mana nauyi da ingancin zinari nan”

“To ranka ya dade”

Mutumen ya fada sannan ya katse wayar, babu bata lokaci mutumen ya iso da kayan awonsa ya auna ya fada wa Alhajin ingancinsa da komai sannan Alhajin ya fada masa ko nawa suke sayen kila, da kuma wanda ba kilo ba. Ba karamin mamaki ne ya kama Faruk ba ganin Alhaji Isma'el Zabarma ya siye zinari da be wuce wani karamin dutse ba, har mikiyan bakwai da dubu dari biyu.

“A account za a saka maka kudin ko kuma kasa za a baka?”

“Ranka ya dade a account dai, riko kidi a hannu yanzu ai sai manya”

Alhaji Isma'el yayi murmushi ya kalli mutume dake zaune kasa kusa da shi ya ce.

“Ka karbi account dinsa ka fadawa Ibrahim a saka masa kudinsa yanzu nan”

“Toh ranka ya dade”

Mutumen ya karbi account number din Faruk ya turawa wanda aka umarta, sannan ya dauko littafi ya shiga yi musu takardar shaidar ta mai siye da mai siyarwa kamar yadda al'adar cinikayya da Alhajin take. Kamin ya gama rubuta har kudin sun shiga account dinsa. Da mugun mamaki da farinciki Faruk ya rike wayar yana duba yadda aka jera zerukan dake son rikita shi.

“Ko sun shigo ne”

“Sun shigo Alhaji na gode sosai Allah ya saka da alheri”

Alhaji ya daga masa kai yana murmushi, sannan aka mika masa takardar suka rike daya, kamar zai yi tuntube ya fadi haka ya fito falon cikin wani irin farinciki da zumudi marar misaltuwa. Daga gidan Alhajin asibitin ya nufo gurin mahaifiyarsa, tana ganin yadda fuskarsa take kyalli ga bakinsa daya kasa ruwa ta san danta ya samu biyan bukata. Kusa da ita ya zauna yana murmushin farincikin daya manta when yayi irinsa.

“Mama ya siye, kuma ya saka min kudin a account kin gan su nan”

“Alhamdulillah, Allah ya sa albarka Faruku, Allah yasa silar arzikin ka ne”

“Amin Mama. Amin..”

Ya amsa yana jin kamar ya hade kansa saboda tsabar farinciki.

“Mama wai kin san me?”

“Aa sai ka fada”

“Alhaji nan da na kawai zinarin nan ya siye mahafin nurse din nan ne data kawo miki snacks”

Mama ta kalleshi cike da mamaki.

“Da gaske?”

A nanya kwashe labarin komai ya fadawa Mama, sai tai murmshi.

“Ai kana ganinta ka san yar babban gida ce, yarinyar ta burge ni, ko kadan bata da daukar kai, ko bayan fitarka sai da ta shigo nan tana tambayar inda zaka je wai ta ga ka fita da gaggawa”

Faruk ya dan yi murmushi yana kokarin siyen data ta line sa na Mtn. Rabonsa da chat ma har ya manta.

“Ta cika rawar kai ne, ba zaka ganta ka ce wannan mutumen nan mahaifinta ba ne”

“Kai dai kam kamar baka gama karantar mutane da rayuwa ba Faruk, ai yan adama kamar yatsun hannu suke kowa Allah yayi shi dabam dabam”

“Haka ne, bari na kira Shamsu na tambaya yadda akai maganar gidan”

“Ya kamata kam domin tun da zafi zafi ake duka karfe”

Cewar Mama tana murmushi zuciyarta kal da farincikin daya kasa boyuwa a fuskarta. Yana kokarin kiran Shamsu sako ya shigo email dinsa sakamakon data daya kunna, sai dai be tsaya duba sakon ba ya kara wayar a kunnesa.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Yana gama waya da Aminatu Ali ya kira wayarsa, sai da ya gyara zamansa sannan yai picking call din ya saka a speaker domin baya jin kai wayar a kunnensa.

“Hello”

“Ranka ya dade ya jikin naka?”

“Alhamdulillah”

“Kana jin wani ciwo yanzu?”

“Yeah kirjin ne kawai sai kuma cikin kaina ina jin yana dan sara min sai dai ba sosai ba”

“Waya kwana da kai Momy ko Aminatu ko Kabir or...”

“Sabuwar dokar asibiti ce dole ku san wanda ya kwana da wani?”

Ali yayi murmushi mai sauti.

“No, akwai abun da nake son tambaya ne”

“Go straight to the point”

“Ba da kai zan yi ba da wanda ya kwana da kai zan yi”

“Kabir”

Ya amsa masa a takaice.

“Okay good zan yi magana da shi, and karka ci abu mai zafi please”

“And you know me bana son abu mai sanyi”

“Yes a yanayin da kake a yanzu ba a son ka ci abu mai zafi ko mai yaji, idan ya zama dole to kar yayi zafin da kake shan tea, jiya ma mantawa na yi ban fada maka ba”

“Na ji, ina neighbor din ku yake?”

“Yana gidansa”

“I need to talk him, Shalele ta damu tai magana da shi”

“You said sai an yi DNA and so on kamin ka barshi ya ganta”

“Yes, just to make sure yayanta ne na gasken, kuma za a je har gurin police tare da Lawyer na, ayi duk abun da ya dace”

“Arrest din shi zaka yi?”

“Why would i?”

“Then why are you taking him to police station with your lawyer?”

“Ba zaka fahimta ba, mutane yanzu ba abun yarda ba ne were not so sure yayanta ne or not, za a iya rabarta a cutar da ita kamar yadda akai a baya, secondly wani zai iya kawo wannan shawarar”

“Amman idan an kawo ita bata san yayanta ba? Haba Talba Aminatu fa ba jaririya ba, ta san idan dai dai ta san akasin haka”

“She's more than that to me, mace bata da wayo ai no matter how old she's balle wannan da yanzu take sanin rayuwa, na bukata ci kamin haka ne saboda ka san halin da nake ciki, da lafiya nake zan iya yin komai da kaina”

“Shikenan, sai kai ma Lawyer naka magana ai”

“Zan tura masa sako yanzu, and the DNA test...”

“I will handle it”

Talba ya katse wayar, sannan ya maida hankalinsa gurin tasbihin da yake da yatsun hannunta. Misalin 7:30am Daddy ya kira shi amsa kiran yayi daidai da shigo Kabir a dakin, kallon kawai Talba yai ya dauke kai yana mikawa Daddy gaisuwa ta wayar.

“Good morning Daddy”

“An tashi lafiya? Ya jikin naka?”

“Alhamdulillah”

“Kana samun sauki?”

“Sosai ma Daddy”

“Ya kirjin naka?”

“Da ji sauki fa Daddy, komai ya daina min ciwo yanzu”

“Alhamdulillah, Allah ya kara tsarewa, kuma sai ka kula da kanka Mu'az, yanzu fa iyali zaka fara, kai da ya kamata ace idan kaga wani yana yi ka hana shi sai kuma ace kai kake yi? Ita rayuwar daya ce, rai daya ne da zarar ka rasa shi ba zaka sake samun wani ba, idan ma kana ganin kamar kai idan ka mutu baka da wata matsala kai tunanin mutanen da suke tare da kai, su ya zasu rayu idan baka raye kuma ya za su ji idan wani abun ya same ka”

“In Shaa Allah zan kiyaye Daddy haka ba zai sake faruwa ba, sai dai abun da Allah ya kawo”

“Haka nake son ji, Allah ya kara tsewa, akan mutumen kuma i talk to CP akwai wadanda za su zo za su dauki Aminatu su tafi da ita gurinsu ta zayyana musu fuskar yadda mutumen take so that a gano waye shi”

“Yanzu?”

“No not now Maybe tomorrow ko anjima, be dai fada min takamaiman lokacin da za a kaita ba”

“Okay, amman da za su bari na ji sauki zai fi Daddy domin ita ma yanzu hankalinta ba kwance yake ba”

“No ba matsala zan yi magana da shi, shi ma kuma na san ba shi da matsala”

“Na gode sosai Daddy”

“Ur welcome”

Kabir ya kalleshi yana dura allura a syringe.

“Daddy's Boy, bani hannunka allura za a maka”

“Bana son ta bachi please”

“Jiya ba ka yi bachi daya kamata ba, ko da aka kira sallah idonka biyu”

“Amman ba ciwo ne ya hana ni bachi ba”

“Miya hana ka bachi?”

“I don't know kawai dai ina ta tunani sai bachi yaki ya dauke ni”

“To mi kake tunani? Kai da kake da komai a kusa da kai, and you got lucky mata biyu ka samu a lokaci daya”

Talba yayi murmushi.

“You know kana tsara rayuwarka, Allah yana tsara maka yadda zata kasance, i never thought zan iya zama da mata biyu, kai ma kuma ai dan baka so ba ne”

“Na kusa ai, ban samu wanda nake so ba ne, kuma ni har yanzu Daddy da Momy ba su maida hankali akaina ba, balle su min maganar aure ko irin dan hadin nan da ake na zumunci ayi min, wai ko bana da farin jini ne”

This time around Talba dariya yake yi sosai.

“Oh Man wane irin farin jini kuma? I swear a whole handsome like me, ace mata basa crushing a akaina, to ko dai aljana ta aure ni ne?”

“joke apart, kai ne dai baka ba su dama, ka cika daure da yawa, and kai ma kanka baka tana ganin wata ka ce kana so ba”

“So nine na cika daurewa? Talba kai har kana da bakin fadawa wani yana daurewa da yawa? Kai ma zuwan yarinyar nan ne ka waye, ta wayar da kai ka shigo gari har kake sakewa da mutane”

Yayi murmushin gefen fuska.

“I love her”

“I know...”

Kabir ya amsa masa, sannan ya zauna kusa da inda yake zaune, ma'ana saman gadon.

“When you meet someone you love, wani abun baka sanin ka yi shi, so babu ruwanshi da matsayi babu ruwansa da kyau ko muni, babu ruwansa da kudi sarauta ko talauci, so na gaskiya babu ruwansa da wannan, yana canja kowa kuma ya caja kowa”

Talba ya kalleshi yana murmushi da kuma tunanin yadda yake magana.

“Ka samu wanda kake so ne?”

“No ban samu ba, zuciyata dai ta fara son wata yarinya”

“A familynmu?”

“No... A cikin asibitin nan, farkon abun da ya fara burge da ita shi ne natsuwarta, natsuwa da kunya yana daga cikin abun da ke karawa mace kyau da kwarjini, ka ga yayan talakawan nan suna da mugun shiga rai, suna da tarbiya sosai ga kunya”

“Ba dukansu ba, ko'ina akwai na kirki a akwai bata gari”

“Na sani, amman mafi yawansu haka suke, suna da natsuwa da tarbiya”

“Finally Kb is in love”

Talba ya fada yana dukan kafadarsa. Sai ya kara fadada murmushinsa.

“Yes, but the most funniest part is i don't even know how to approach her, should I say hey beauty how are you can i get your number or hey I'm Kabir by

name what is your name? Or no maybe it will better if i say yan mata zan iya kai ki gida? No...”

Ya dafe hancinsa yana jin kalaman sun masa wani irin, sam a rayuwarsa be taba taron mace ya tsayarda ita da sunan so ba, not even in chat be san ya nunawa mace wani abu soyayya ba. Talba yayi murmushi mai sauti.

“Or Maybe it will be better if you help her idan mai neman taimako ce, kasan wasu matan basa son tambaya kai tsaye, wasu ma zasu ga kamar wulakanci cewa ka rage musu hanya or something like that, kar kuma kaje wa mace kai tsate wai ina kaunarki, ka fara da wani abun da take so ko yake burgeta, is she working here?”

“No i think jinya take yi”

“That's mean you can lose her anytime, you have to make some effort to save your love”

“Duniya juyi juyi yau kake ba ni tips akan love”

Kabir ya fada yana kallon Talba da murmushi a fuskarsa, Talba ma murmushin yayi

“Yes, because now you're in my shoes”

“Fine ba ni hannunka, na bar allurar ta sha iska”

Ya fada yana kokarin canja needle din.

“No please na fada maka ina bana son ta bachin nan, zan yi bachi da kaina anjima”

“Okay, but make sure kana cin abinci ka sha maganinka”

Ya aje allurar.

“Okay Doc”

Kabir yayi dariya tare da juya ya kalli kofar da aka turo aka shigo. Aminatu ce dauke da basket din abincin da Hajiya Laraba ta zuba Talba, Mijin Hajiya Laraba yana bayanta. Kabir da Talba suka hada baki gurin amsa masa, sai ya karasa gurin Talba fuska sake yana masa ya jiki, Talba ya amsa yana tambayarsa ya aiki da yara.

“Komai lafiya, mamanka tace a gaishe ka, zata zo anjima”

“Okay Allah ya kaimu”

Kabir ya mika masa hannu suka gaisa, sannan ya fice daga dakin ya wanda hakan ya bawa mijin Hajiya Laraba zaunawa yana fadin.

“Ai abun ya zo da sauki ma sosai, Allah dai ya kara tsarewa”

“Ameen Ameen”

Sai ya mike tsaye.

“Bari na wuce yara zan sauke school kar su yi lati”

“Okay”

Ya ciro kudi mai dan dama ya mikawa Aminatu.

“Karbi wannan kya rage wani abun”

Sai ta girgiza masa kai da sauri.

“Aa akwai komai a nan babu abun da muke siye”

“To kyauta ake ba ku, in da ke da kurciyarki, karbi mana”

Ya fada, sai Talba ya ce.

“Wallahi babu abun da zamu karba, haba ziyarar ai ita ce mai muhimmanci”

Rantsuwar da Talba yai ne ya saka shi maida kudin aljihunsa yai masa addu'a ya fice. Kofar ya rufewa Talba ya kalli Aminatu sai ta sakar masa murmushi ta matsa kusa da shi ta kai hannunta tana taba jikinsa.

“Ya jikin?”

Ya hade fuska in a cool way.

“Ban sani, fushi nake kin ce baki yi mafarkina ba”

Sai tai murmushi ta kai hannayenta ta rika fuskarsa ta matse masa kumatun kamar zata kwance shi.

“To ban yi ba sai na yi karya”

“Da kin kwanta da tunani ai dole ne ki yi mafarki”

Ta yi murmushin daya kara ma fuskarta kyau.

“To zan yi gobe”

Ya mika hannunsa ya shafa hannayenta ya matso da fuskarta a kusa yana kissing din goshinta before ya hancinta sannan ya dire a bakinta, a hankali yana tsotsa soft lips dinta wanda hakan ya saka ta rufe tana shakar numfashinsa, rumgumota yai ya dawo da ita saman jikinsa yana kallon kwayar idonta dake rufe, wani irin zaki yake ji a lips dinta kamar an saka mata honey ga wani taushi da suke masa kamar mada, a hankali ya cire bakinsa sai ya goga mata lips dinsa saman nata ya rike hannunta yana murza yatsunta a hankali.

“Sweet lips”

Ya furta da muryar da ita kadai zata iya jinsa, yana kallon lips din nata looking for more. Bude idon tai ta sauka daga saman jikinta.

“Ga breakfast dinka nan”

Wani irin kallonta yake kamar yau ya fara ganinta, har na Allah ba san adadin kaunar da yake yi ma Aminatu ba, idan tana kusa da shi yana jin kamar ya hadeyeta ta zauna a cikinsa, for him everything about her is perfect.

“Ke kin karya ne?”

Ya fada looking at her pretty face.

“Eh mun karya a can, wannan naka ne”

“Hada min”

Ya shiga zuba masa abincin kamar yadda ya bukata.

“Ka ce yau zaka hada ni da Ya Bashir ko?”

“Eh, amman sai anjima za a zo da shi”

“Toh”

Ta amsa tana murmushin jindadi cike da zakuwa.

LEILA POV.

Sai da ta ja kofar dakin, sai kuma ta dawo ta tsaya jikin kofar ta kara kunenta tana sauraren abun da Momy take fada ita da Mama Saratu. Sai da ta ji alamar Momy zata fito sannan ta daga jikin kofar ta sauko kasa da sauri ta nufi kitchen din dak falon. Mairo ta samu a tsaye tana wanke kayan da suka bata tana ganinta ta gaishe ta da sauri, sai ta daga mata kai alamar amsawa ba tare da ta amsa da bakin ba. Kofi ta sauka ta tara a tap din ta cika kofin ta shanye tana jin kamar numfashin da take baya wadatar da huhunta.

‘Miyasa Momy zata yarda a kashe Madina? Just because of wani ra'ayi na su na dabam? Idan aka kashe ta zai zama musu mafita? Shim asirinta zai rufu har abada? Ko kuma wata matsalar zata kara afkawa? Anya lokaci be yi da ya kamata ta karbi kaddara? Idan wacan kuskure ne yanzu kuma minene? Ganganci right? Ta dade tana mafarkin Baaba da kuma tunanin ita ma da akai akan kuskure kenan? Yanzu kuma idan a tai na ganganci fa? Miye makomarta? ’

Kiran da Momy tai mata ne ya katse mata tunanin da take ta juyo a firgice numfashinta har rawa yake.

“Na'am...”

“Baki tafi ba?”

“Ina?”

Ta tambaya tana jin kamar kamar wata bakuwa ce a kunnenta. Da mamaki Momy take kallonta.

“What are you thinking? Ba cewa na yi ki kaiwa Talba abincin a asibiti ba”

“Eh abincin na shigo dauka, Momy dan Allah kar mu sake aikata wani kuskuren”

Momy ta kalli Mairo ta kalleta da sauri tana dan zare mata ido alamar bata son su yi maganar a nan. Ita kanta Leila ta manta da Mairo na guri har sai da Momy tai mata ishara da ido.

“Je ki kai mishi abinci”

“Okay”

Ta fada sannan ta juya ta fice daga kitchen din ta nufi dinning, sai da ta dora hannunta kan kulolin sannan ta tuna da key din motarsa, hakan yasa ta dauke hannunta ta juya ta hau sama ta shiga dakinta ta dauko key din da wani karamin mayafi da wayarta ta fito, a hankali take saukowa har ta sauka downstairs ta nufi kulolin wannan karon bata tsaya jiran amsu aiki su kai mata mota ba, sai ta dauka da kanta tare da tray ta nufi kofar fita falon, a nan kam sai da ta aje kayan hannunta ta bude kofar sannan ta dauki abincin ta fice. A front seat ta saka sannan ta zagaya bangaren direba ta zauna tai ma motar key. Cikin mintunan da ba su fi ashirin ba ta isa asibitin, a gurin da aka tanada domin faka motoci ta faka motarta sannan ta bude ta fito ta dauki abinci ta shiga da shi ciki. Tana isa kofar dakin ta tura kofar ta shiga ba tare da tunanin komai ba, and she saw what she didn't expect, Aminatu na zauna kusa da shi yatsun hannunta na tsoke cikin na Talba, she lay down her head on his shoulder tana kallo da wayar da ke rike a dayan hannunsa.
She feel the pain so badly, ba zata iya zaya irin bakinciki da kishin da ta ji a lokacin, wani dauke kai tai ta aje numfashi a hankali, hakan kuma be hanata karasawa cikin dakin ba, jikinta rawa yake sosai kamar tray da ke hannunta zai subuce ya fadi, cikin sakewar zuciya ta duka ta aje tray sannan ta Talba da yai saurin zare hannunsa daga Aminatu, not because of yana tsoronta but because of baya son ya batawa dayansu rai, domin ya san zata ji zafi, Aminatu ta daga kanta daga jikinsa ba tare da ta kalleta ba.

“How are you feeling now?”

Ta fada idonta na makkale da hawaye, sai ya ji tausayinta ya kama shi, domin Leila bata taba gwada kishi da wata ba ko wani akan komai ba balle akan Talba, and wanda be saba fuskanta zafin da bakincikin kishi ba, zai ji kamar ya haukace idan ya kasance shi.

“Feeling much better, abinci kika kawo?”

“Yeah, amman na ga ki karya ma already”

Ta fada tana kallon kololin da Aminatu ta kawo. Sannan ta mike tsaye.

“Ina son mu yi magana da kai”

Aminatu na jin haka sai ta tashi rike da wayar ta fice har lokacin bata kalli Leila ba. Sai da ta fice sannan Talba ya kalli Leila ya ce.

“Akwai matsala ne?”

Ta lumshe ido hawaye ya sauko mata.

“Ni kadai nake da matsala ta, na kai wani stage sa babu mai fahimtar yarena a yanzu, ni kadai na san yadda nake ji”

Ta yi saurin rufe bakinsa saboda kuka dake son yaci karfinta. Talba ya nuna mata guri kusa da shi.

“Zauna a nan”

Ta zauna still hawaye an sauko mata kamar ba gobe.

“Me ke damunki?”

“Abubuwa da yawa, amman a yanzu abun da na fi bukata shi ne ka kasance a tare da ni, saboda na san Daddy ba zai fahimce ni ba”

Talba thought Leila tana magana da shi ne saboda Aminatu that's why he say.

“Leila, na san kina jin kishi ne kina jin Danuwa, i just want you to know that, ba kaunarki ne bana yi ba, akwai wadansu dabi'u da halayya da bana so na ki, kuma saboda na auri Aminatu ba shi yake nufin bana son ki ba, ina son ki ina sonta kowa da matsayinsa,and i want you to know that I love you no matter what happen”

Ta share hawayenta tana dan murmushi.

“Zan tafi gida Allah ya sauwake”

“Amin”

Ya amsa yana karantar yanayinta dake nuna akwai damuwa sosai a tare da ita. Da kallo ya bita har ta fice sannan ya sauke ajiyar zuciya ya busar da iskar bakinsa.
Tana fitowa dakin ta samu Aminatu a tsaye bakin kofar rike da wayar Talba, wani irin abu ta ji ya soki zuciyarta, no matter how she try to control herself ta kawar da komai a ranta sai ta kasa, ji tai kamar ace akwai wuka a kusa da ita ta dabawa Aminatu gurin, sai dai bata iya ce nata komai ba ta nufi hanyar fita ward din tana haki kamar wanda tai gudu. Komawa tai cikin motarta ta dauki wayarta ta kira Ali, sai da wayar tai daf da katsewa sannan ya amsa kiran.

“Yau kuma an tuna da ni?”

Runtse ido tai wani sabon kuka na zo kwankwaso mata kofa.

“Ali... Ali... Ina son magana da kai”

Yanayin yadda ta ji muryarta ya san ba lafiya ba.

“Okay....kina ina yanzu...”

“Ina Asibiti”

“Zaki iya zuwa coffee center mu hadu ko kuma na same ki asbitin?”

“Zan same ka a can yanzun nan”

“Okay”

Ta katse kiran sannan ta jingina kanta da sitiyarin motar ta fashe da kuka sosai. Ta bata minti ashirin a haka kamin tai ma motar key ta fice daga asibitin, kai tsaye a inda suka yi za su hadu ta isa, ko da ta fito motarta tana tsaye jikin tasa motar yana jiranta, ganin yanayinta yasa ta karaso kusa da ita.

“Leila are you okay?”

“I just need someone to talk to, Ba ni da kowa yanzu, my best friend betrayed me, and my mom won't understand, Daddy da Talba na san za za su tsane ne... ”

Tana magana hawaye na wanke mata fuska.

“Koma cikin motarki zamu yi magana a ciki”

Ya fada yana zagaya dayan side din.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Sai da ta bude motar ta shiga sannan ta fara tunani, anya ya kamata ta fada masa? Idan ma ta fada masa zai sama mata mafita ne ko kuma zata kara tura kanta a hadari ne?

“Miya faru Leila”

Ya fada yana kallonta cikr da damuwa, sai ta kara sharw hawayenta ta ja mayafinta ta na kara gyara fuskarta, tissue dake gaban motar nata ya mika mata, sai ta karba ta gyara hancinta.

“Ba komai daman i need someone to talk to”

“Yes I'm here you can talk me”

Ta kirkiron murmushin da bata san ta ina ta samo shi ba.

“Maganar bata da wani muhimmanci, domin yin ta ba zai canja komai ba”

“Wata kila kuma zai canja fiye da yadda kike zato”

“Ba zai canja komai ba, ya riga ya aureta kuma ba sakinta zai yi ba, babu abun da zai canja”

Ta juyarda maganar zuwa da Aminatu a kokarinta na kwatar kanta daga wacan maganar ta farko da tai. Kallonta yai ba dan ya gamsu da abun da take fada ba, domin matsalar Aminatu ba sabuwar matsala bace da zata saka Leila a cikin halin da take a yanzu, kuma idan har matsalar Aminatu ce miya kawo Madina a ciki har take fadar Daddy zai yi fushi da ita? Talba zai tsane ta? A take zuciyarsa ta raya masa akwai abun da take boyewa, sai dai be nuna mata ba.

“Ki yi hakuri Leila, lokuta da dama abubuwan da muke tsarawa ba su suke faruwa ba, karki dubi auren dake tsakanin Talba da Aminatu ki dubi soyayyar dake tsakaninku, zaki zauna a matsayinki na matarsa ita ma haka kowa da muhallinsa, Leila ki cire damuwa a ranki just pray bana son kina saka kanki cikin damuwa”

Ta yi murmusa a karo na biyu tana kallonsa da idanuwanta da sukai ja.

“Ka fi Talba zuciya mai kyau Ali, a duk lokacin dana shiga cikin damuwa kana kokarin ganin ka cire ni a ciki ka kwantar min da hankali, but Talba...”

Sai kuma tai shiru.

“Na aje soyayya a gurin da ba muhallinta ba, and yanzu ina tausayin kaina”

“No you shouldn't, ba ko wace mace mai sa'a samun saurayi kamar Talba ba, I'm his friend Talba yana da hali mai kyau Leila, kuma nasan zaki fahimci haka idan zaman aure ya hada ku, a krakashin inuwa daya”

Ta daga masa kai.

“Zan tafi gida kar Momy ta nemi ne”

“Okay”

Ya bude motar ya fita, sai da ya isa gurin motarsa sannan tai reverse, ta hau titi. Hannu ya saka aljihunsa ya ciro wayarsa da zimmar kiran Talba, sai kuma wani tunanin ya zo masa, a take ya maida wayar aljihu ya nufi motarsa ya bude ya shiga yai mata key, reverse yai ya fita daga harabar sannan ya hau babban titi, yana driving tunani har ya isa gaban gate din gidansu Madina zuciyarsa bata natsu da canja manufar labarin da Leila tai ba. Wayarsa da ya saka aljihu dazun ya sake cirowa ya shiga ma'adanar numbobinsa ya nemo number Madina, shi kansa ya manta when last yai waya da ita. Da sim 2 ya kirata line da be saba kiran mutane da shi ba. Wayar bata wani dade tana ringing ba ta dauka, sai dai jin muryar Ali ya saka ta dan yi jimm kamar ba zata amsa ba.

“Na'am Ali ya gida”

Ta fada bayan ta dauke wayar daga kunnenta ta duba number da babu ita a wayarta.

“Lafiya Kalau ya kike?”

“Lafiya Kalau”

Ta amsa gabanta na faduwa tsoro ya gama cika mata zuciya.

“Kina gida?”

“Lafiya?”

“Ina son na yi magana da ke”

“Da ni kuma akan me?”

“Magana ce mai muhimmanci, idan kuma baki da time yanzu zaki iya saka min lokaci sai na same ki same ni”

Shiru tai kamar bata tare da wayar, tsoro take ji wata zuciyar na raya mata yana tare da wasu ne, sai dai kuma su waye? Idan har police ne kai tsaye za su shigo cikin gidan ba tare da an kirata a waya ba. Amman kuma me zai saka Ali ya nemi magana da ita?

“Zan iya sanin akan me kake nemana?”

“Zai fi kyau idan kika fito sai ki ji”

“Ka yi horn a bude maka, sai ka shigo harabar gidan mu”

“Okay”

Ya sauke wayar ya danna horn din kamar yadda ta bukata, he know akwai wani abu a kasa domin yanayin yadda take magana da shi ya nuna haka, domin akwai rashin natsuwa da yarda a tare da ita. Ana bude masa gate din ya kunno kai harabar gidan ya faka a inda ya hango wasu motoci biyu fake, sannan ya bude motar ya fito ya jingina yana kallon harabar gidan. Ta windows ta hango shigowarsa har zuwa fakin din da yai, daker ta iya tattara yawun bakinta ya hade sannan ta mike tsaye ta dauki hijab ta saka, wani irin zallo zuciyarta take na tsoro da fargaba, me Ali ya zo mata da shi? Ya ji wani abu ne? Ko kuma Leila ta fada masa wani abun ne? Ta kasa raba dayan biyu har ta fito dakin not just her heart even jikinta shaking yake. Fitowa tai falon ba tare da ta shiga dakin Hajiya ta sanar da ita komai ba ta nufi kofar fita falon, sai kuma tai tsaye ta jin wani sabon tashin hankali na kusantota.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ta furta a hankali, sannan ta kai hannu ta bude kofar ta fita cikin rashin kuzari da natsuwa, ga fuskarta dake kara nuna tashin hankalinta domin ta rame sosai kana kallonta kasan ta rasa natsuwa da kwanciyar hankali. Tafiya take kamar mai koyon tatata har ta isa gurin motarsa suna hada ido gabanta yai mugun faduwa

domin ta lura da fuskarsa ba kamar yadda ta saba ganinta ba, dauke kai tai ta kalli wani gurin.

“Gani”

“Zamu shiga cikin mota ne mu yi magana ko akwai gurin saukar baki a gidanku?”

Ya fada yana kara karantar yanayinta, sai da tai fasahar aje numfashi a hankali sannan ta kalli garden din gidansu.

“Akwai kujerun zama a can”

“Bismillah”

Yai mata alama da ta fara wuce da hannu sannan ya bi bayanta, ta riga shi zama domin ta riga shi isa gurin da aka wadata da kujerun roba na zamani masu kyaun da dadin zama. Kallonta yai bayan ya zauna ita kuma ta ki yarda su hada ido sai yawo take da idon nata a kasa.

“Abun da na ji ban yi tsammanin jinsa ba Madina?”

Ta dauke kai da sauri tana fisgar numfashin dake son dauke mata.

“A yadda kuka da Leila be kamata ace an samu haka a tsakaninku ba”

He just decided yai mata magana ta wannan sigar, saboda ya samu abun da yake so.

“Sam ban yi tsammanin haka daga gareki ba Madina, a tunanina ke mai sharewa Leila hawaye ce, ina tunanin idan Leila tai wani aika aika zata gudu ta zo gareki kuma ki boye ta ki goya mata baya ko da bata da gaskiya, kun tashi tare kun girma tare sai da kuka kai matsayin da ya kamata ku dora yarankun akan tafarkin zumunci sai kuma ku bari sheidan ya shiga tsakaninku? Why?”

Hawaye ya fara mata zuba, hakan ya bawa Ali gwarin guiwar dorawa daga inda ya tsaya.

“So i just come here to talk to you, maybe zamu iya samun mafita, but i won't force you, domin babu wanda ya san na zo nan daga Talba har Leila?”

Ta kalleshi da sauri.

“Talba ya san abun da ya faru ne?”

“Be sani ba, a yanayin da yake yanzu baya bukatar wani tashin hankali ko bacin rai, ban fada masa komai ba kin san Leila kuma ba zata fuskance shi ta fada masa irin wannan abun da babu dadin ji ba”

Ta sauke idon da hawaye ya ki tsaya mata.

“Na yi nadamar abun da na aikata Ali, na san na jefa rayuwa a hatsari, duk abun da na yi na yi saboda Talba zuciyata tana matukar kaunarsa Talba Ali ina cikin damuwa, lokacin da zan aikata idona ya rufe bana iya ganin komai, i thought

dauke Aminatu zai sama min mafita saboda na kusan haukace a dare dana gansu tare but....”

Sai kuka ya ci karfinta. Suma ne kawai Ali be yi a gurin ba, tsakanin furta tana matukar kaunar Talba da kuma dauke Aminatu sai ya rasa wanda ya fi bashi mamaki, be san lokacin da yawun bakinsa suka tsarke shi ba ya fara tari tana kallon wani gurin daban.

‘Kenan ita ce ta gansu a daren nan? Kuma ita ta shirya yadda za a dauke Aminatu? And how tana son Talba? Daman duk zaman da take da Leila tana son Talba, amman shi be taba noticed ba? For how long?’

Be samu amsar tambayoyin da zuciyarsa take masa ba ya hangota tana kuka tana fadin.

“Na jefa kaina a matsala, ban samu biyan bukata ba na shiga wani tasko”

Sai da yai hanzarin tattaro natsuwarsa sannan ya samu gwarin guiwar sake yin magana.

“Kidnapping wani ba mafita bace Madina, a lokacin da kika dauke ta idan wani abu ya same ta ya zaki yi? And kina tunanin Talba zai so ke saboda kin aikata wannan abun? Sai dai ya kara tsanarki”

“A wacan lokacin duk ban ga wannan ba, domin wata haya mai fadi ta rufe min ido wacce ta hanani ganin komai, zuciyata tana raya min idan nai haka zan samu mafita, ashe ina kara jefa kaina a halaka ne ban sani ba”

“Idan kin ji kina son Talba, ba wani sabon abu bane, wata kila yana da wasu siffofi da dabi'u da kike so a namiji. Misali kamar ni ba laifi ba ne idan na ji ina son Leila wata kila tana da wasu siffofi da mu'amala da nake son a nace amman ba zan taba yarda son ta yai tasiri a zuciyata ta yarda zai bata alakata da Talba ba, irin wannan abun ya kamata ki yi, and ina ganin laifinki a gurin Leila na son Talba ne kawai bayan shi duk wani abu daya biyo bayan haka bata dauke shi da girma ba saboda Leila tana da sauki kai”

Madina ta kalleshi tana girgiza masa kai.

“Barazanar da na yi mata ma ta dauke shi da girma, domin Momy ta turo min sako cewar na saurare abun da zai same ni, kuma Wallahi na karshen ba ni na saka shi shi ya aikata da kansa wai kudi yake so sai na bashi miliyan talatin sannan zai rabu da ni”

“Shi mutumen da kuka yi aikin da shi?”

Ali ya tambaya tana kara nitsawa cikin labarin ta yadda zai fahimci komai da kyau. Sai ta daga masa kai tana kuka sosai.

“Ina kika hadu da shi?”

“Wani ne ya hada ni da shi, besty amman Wallahi duk wani abu da yake aikawa Leila na Baaba ba ni na saka shi ba, ni dai kawai na fada masa ina son a tsoratata ta yadda hakan zai yi sanadiyar fasa aurenta da Talba, shi ya tsara

komai hakora da aika mata shekaran jiya na ba ni na saka shi ba Wallahi ta ya zan ce ya taba gawa har ya ciro hakoranta saboda rashin imani”

Wani irin bugawa gaba Ali yai da sauri, take zuciyarsa ta fara raba jini da gudu.

“Ina gawar Baaba take? Kin canja mata guri ne?”

Ya tambaya yana son kara tabbatar da abun da Talba ya dade yana zargin Leila da shi.

“Aa ni ban ce ya canja mata guri ba, idan ma ya canja shi yai hakan a karan kansa amman ni ban saka shi ba, na san akan kuskure Leila ta aikata kisan Baaba, kuma na san be kamata na aikata mata haka ba, sheidan ya rinjaye ni”

Ya sauke ajiyar zuciya a hankali, yana jin tausayin Leila na kama shi.

“Shikenan, zan yi magana da Leila sai na ga yadda za'ayi mu samu mafita, amman bana son kowa ya san maganar nan bana son kowa ya san na zo nan okay”

Ta daga masa kai, sai ya mike tsaye.

“Zan tafi, wata kila na dawo wata kila kuma wayarki zan kira”

Ta daga masa kai, sannan ta rufe fuskarta da hannayenta tana kuka. Fitowa yai gurin cikin rashin kuzari ya nufi motarsa, yana mata key ya danna horn sau biyu, ko kamin yai reverse mai gadin ya bude masa gate din gida. Yar tafiya kadan yai ya hau babban titi babu komai a zuciyarsa sai tausayin Leila, sai a yanzu ya fahimcin kukan da take dazun, da kalaman da take cewar Madina ta butulce mata Daddy da Talba kuma za su tsane ta Momy kuma ta ki ta saurarenta, sai a yanzu ya fahimci dalilin zuwa gurinsa da tai, ta rasa wanda zai fahimce ne.

“Idan Talba ya san wannan ba zai raga miki ba Leila, kamar yadda Daddy ba zai saurara miki ba”

Ya fada yana shafa kansa zuciyarsa na masa ba dadi.

“Daman Talba ya dade yana zarginki komai akai ke yake dorawa Laifi”

Ya sake furta yana jin cewar Leila ba zata kashe Baaba da ganganci ba, zai fi yarda da maganar Madina cewar ta aikata hakan akan kuskure kuma kaddara bata wuce kan kowa ba. Tausayinta ya kara rufe shi, domin ya san Talba ba zai mata da sauki ba, a yanzu ya fahimce dalilin da ya saka dazun take cewa tana nadamar komai, domin a yanayin da take ciki a yanzu tana bukatar wanda zai rarrasheta ya kwantar mata da hankali, Allah ka dai ya san abun da take ji a zuciyarta, bayan abun da ya same ta kuma Madina ta kara mata da wani? Ga kuma bakinciki da Talba yai ta cusa mata kala kala.

A harabar gidansa ya faka zuciyarsa fal da tausayinta, ji yai yana bukatar yai magana da ita, akwai abun da ya kamata ya tambaye ta, kuma akwai wanda ya kamata ya fahimtar da ita amman ta yaya? Zata yarda tai magana da shi? Zata fada masa komai? Ta ya mai zai fuskance ta? Iskar bakinsa ya busar ya bude motar ya fita ya nufi cikin gidansa, be yi one hour ba a cikin gidan ya fito da

shirinsa na office Haulat ta rako shi har gurin tana masa addu'a, sai da ya bude motar sannan ya juyo ya rikota ya sumbanci bakinta.

“Sai na dawo”

“Allah ya kiyaye”

Ta fada tana kallon yadda mood dinsa ya canja, domin fuskarsa ta nuna akwai damuwa kuma ba haka ya saba mata ba idan zai fita, a kofar falo suke sallamarsu, but this time around har sai da ta biyoshi gurin motarsa sannan ya tuna da zancen yi mata kiss kamar yadda ya saba mata. Sai dai bata shirya yi masa magana a yanzu ba saboda ganin zai tafi gurin aiki, hakan yasa ta hadeye abun da ke ranta har sai ya dawo tukuna.

Yana fita daga gidansa faka motarsa ya shiga kwararon makotansu, domin gabatar da abun da Talba yai requesting. Be tarar da shi a gidan sai ya karbi number wayarsa ya kira yai magana da shi ya fada masa inda za su hadu. Ko da karfe biyu na rana tai Ali ya kammala komai tare da Bashir ciki har da awon DNA da Talba ya bukata, sai dai an yi fama da Aminatu kamin a dauki jininta domin shi yake ganin yafi sauki kuma Talba zai fi gamsuwa da shi.

AMINATU POV.

gaba daya ta kasa sakewa ayau, saboda mutanen da suke zuwa ganin Talba, most of them yan'uwan Daddy ne sai na Momy da kuma makota da abokan arziki sai kuma wasu daga cikin ma'aikatansa. Gashi a dakin ta wuni domin bata da gurin zuwa, Momy bata sake mata fuskar da zata je waje ta zauna ba a cikin, domin ko shigowar da take da mutane masu dubiya, daurewa Aminatu fuska take babu wanda ya san matsayin Aminatu a gurinsu domin bata fadawa kowa, bata ma son a sani. Zuwan Hajiya Laraba ne ya saka Aminatu ta ji sanyi sanyi ta samu sakewa har tana dariya kamar ba ita ba, Hajiya na zaune kan kujera tana nunawa talba rashin jindadinta na kin yarda da yai a fadawa Kaka abun da ya faru.

“Idan ta ji zata ji ba dadi, kasan halin tsofin nan sai tace wulakanta ta za'ayi, kuma kai kanka abun farincikinka ne yadda mutane suke ta shigowa ace ga dangin mahaifiyarka amman ace idan ba ni ba babu wanda ya zo kamar wanda ba shi da uwa”

“Ke din ma kin wadatar Mama, kuma ina ganin kamar be kamata a fada musu mummunan labari irin wannan ba, kamata yai ace idan na samu lafiya sai na bi na ziyarce su na san kowa kowa kuma ya san ni, idan wani abu ya taso za su sanar da ni nima zan sanar musu”

Hajiya Laraba ta kebe baki

“Allah ya sa zaka iya, ni din ma daka sani yaushe rabonka da gidana? Sai zuwan Aminatu ka san da wani zuwa gidana yanzu ma kana dauketa yanke zumuncin zaka yi”

“Idan ma na yanke, ai ban iya na yanke na tsakaninki da Aminatu ba, kin ga kuwa dole ne na yi zumuncin ko dan ita”

Ya karasa yana murmushi.

“Ni na san saboda ita zaka yi ai ba san Allah ba”

Wannan karon dariya yai.

“Haba an taba zumunci ba domin Allah ba, saboda Allah zan yi”

Hajiya Laraba ya tabe masa baki.

“Gamu gani ai, Allah yasa wannan uwar taka ta barka ka kula dangin mahaifiyarka”

Kusan Hajiya Laraba ta yi sara akan gaba ne, domin fadin hakan yayi daidai da turo kofar dakin da akai Momy ta shigo tare da wasu friends dinta. Kana ganinsu kaga manyan mutane sai kamshin tsadaden turare suke dayar idonta sanye da gilashi irin na marasa lafiyar ido. Sosai Aminatu ta sha jinin jikinta ta dawo kusa da Hajiya Laraba ta tsaya ko ido ta kasa dagawa, tsoron Momy take sosai da dai Leila ce ba zata ji komai ba, amman bata da natsuwa a guri idan Momy na kusa. Yanayin yadda Talba yake masa musu ya tabbatar ma da Hajiya Laraba cewar ya san su, suma kuma sun san shi farin sani, ko da wasa Momy bata kalli inda Hajiya Laraba take zaune ba, sai wani shan kamshi take, tana jiran Hajiya Laraba ta fara nata magana.
Hajiya Laraba kuma ta hakimce saman kujera ta kawar da fuska kamar bata san da Momy a dakin ba, irin sai dai ki ci kanki.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Ganin Momy zata wuce ba tare da sun gaisa da Hajiya Laraba yasa Talba ya kira sunan Momy tana juyowa ya nuna mata yar'uwar mahaifiyarsa.

“Momy ga Mama Laraba nan”

“Na ganta ai”

Momy ta amsa a takaice, sai Hajiya Laraba tai dariyar raini ba tare da tace komai ba, haka Momy ma bata ce da ita komai ba ta fice, domin a ganin Momy ita ya kamata ta fara yi mata magana ko dan rainon Talba da tai, kuma a tunaninta matsayinta da nata ba daya ba. Fitar Momy da minti biyu zuwa uku Ali ya shigo dakin, sai da ya gaisa da Hajiya Laraba sannan ya karasa gurin Talba yana tambayarsa jikinsa, duk kuwa da kasancewar be wani dade sosai da ita daga dakin ba haka yake masa a duk lokacin daya shigo sai ya tambayi jikinsa. Har yayi kamar yai masa magana Leila da yalshen nasara, sai kuma wata zuciyar ya hana shi a ganinsa Talba ba zai fahimta ba, ba lallai ne yai ma Leila uziri ba kamar yadda yake yi ma Aminatu.

“An gama komai, shi kansa ya matsu ya ganta”

“Yeah Lawyer na ya fada min komai, thank you so much”

“A shigo da shi?”

“Eh mana”

Talba ya bada go ahead, ido Aminatu ta gwalo waje tana jin zuciyarta na bugawar dadi. Cike da farinciki take kallon Talba ba dan Hajiya Laraba na gurin ba da rumgume Talba za tai domin ya faranta mata rai a yau. Ali ya kalli Aminatu ta dauke kai shi dai kam jininsa ba hadu sa nata ba, wani lokacin ma sai ya ji kamar tana ba shi haushi domin saboda ita Talba ke yi ma Leila wani abu, wata damuwar kuma saboda saurenta ne da Talba yai Leila ta shiga damuwa.

“Bashir din ne?”

“Eh”

Aminatu ta amsa mata da sauri cike da zumudi tana kallon kofar shigowa, har wani jimke hannayenta take tana matsasu saboda jindadi. Ali ne ya sake turo kofar ya shigo sannan Bashir dake biye da shi ya shigo, da gudu Aminatu ta nufeshi ta rumgume shi sosai tana jin kukan farinciki na sallamo mata, shi kansa hawaye sun cika idonsa ita da shi suka duke a gurin jikinsa sai rawa yake, iyayensu ya tuna da su, ita kamta rayuwarta ta gidansu ta dawo mata.
Hajiya ma sai da idonta ta cika da kwalla saboda tausayi, Ali kam kallonsu kawai yake, Talba ta ba shi tausayi sosai domin ya karanci farincikin da dukansu su biyu suke ji, musamman ma ita.

“Aminatu...”

Sai kuma ya kasa magana sai kuka yake, be taba mafarki haduwa da yar'uwarsa ba, kamar yadda tunaninsa be kawo masa cewar tana raye ba, ya dauka ya rasa kowa kenan. Daga ita jar shi kuka suke aka rasa mai rarrashin wani, banbancin nasa kukan da nata gurin sauti ne, domin nata sautin yana fita, na shi kuma baya fita sai zallar hawaye. Mutuwar Inna da Baba da sauran yan'uwa sai ta dawo musu sabuwa. Ali ya nufi kofar fita ba tare da yace komai ba ya bude kofar ya fito ya fara tafiya ward din yana lasa wayarsa. Can kuma ya kara wayar a kunne yaja ya tsaya gaban wani daki ya jingina da dakin yana kallon mutanen dake kai da kawo.

“Hello Leila”

“Na'am”

Ta amsa masa muryarta na bayyana damuwarta.

“Baki shigo asibiti ba?”

“Eh zan shigo maybe sai gobe ko anjima”

“Magana nake son yi da ke, zan iya tararda ke a gida, ko na jira ki zo?”

“Akan me zamu yi maganar?”

“Akan Talba ne”

“No I'm not ready bana son karin damuwa a yanzu, and i know duk abun da zai zo daga gurin Talba ba abu ne da zai kwantar min da hankali ba”

Wannan furucin da tai ya saka shi kara jin tausayinta sosai a zuciyarsa.

“Maganar tana da muhimmanci Leila”

“Okay idan na shigo zan kira ka”

Ya sauke wayar ba tare daya sake cewa da ita komai ba. Sannan ya juya ya koma dakin. A lokacin ya samu Aminatu na zaune kusa da Talba har lokacin bata daina hawaye ba, shi kuma yana tsaye kusa da kofa idonsa sun rikide saboda hawayen da yai da kuma bakinciki da bacin rai na tunawa da iyayensu.

“Na dauka na rasa kowa, abun nan akwai matukar ciwo da tashin hankali, har abada ba zaka taba manta komai ba, rana guda ace komai naka ya rushe”

Bashir ma maganar Talba na kallon Aminatu ita yake tausayi.

“Kai da kake namiji kenan balle ita da take mace, and lokacin data rasa kowa nata bata da ni bata da Mama, but she kept going, sannu sannu tana samu farinciki, a lokacin nan bata san kana raye ba”

Talba ya fada sannan ya mika hannunsa yana murmushi ya rika hannun Aminatu.

“Ka ga irin mutanen nan, suna da wata baiwa da Allah yai musu ta hakuri, wanda ba kowa yai ma domin wani idan ya wayi gari ya samu kansa a yanayin da Aminatu ta samu kanta, zai iya taba kwakwalwarta ko kuma ya saka zuciyarta bugawa. That's why na yi ma kaina alkawarin ba zan taba aikata wani abu da na san zai taba zuciyarta ba, idan har wani bacin rai ya same ta Wallahi ban sani ba ne, ko kuma babu yadda za'ayi na haka hakan faruwa”

Ali ya dan tabe baki kadan yana yana kallon Talba, a ransa yana cewa idan Leila ce ba zai mata haka ba. Bashir yayi murmushi yana kallon kanwarsa da yake jin kamar ya bude cikinsa ya saka ta a ciki saboda kaunarta da yake, domin ita kadai ta rage masa a rayuwar duniyar nan, sai yan'uwa na nesa.

“Allah sarki, Allah ya baku ikon hada kanku, yanzu sai ka ji sanyi ita ma sai ta ji, ta samu dan'uwa a raye”

Cewar Hajiya Laraba tana kallonsu cike da tausayi. Talba ya ce

“Ya akai kai ka rayu? Ina lokacin da aka kai harin?”

“Ina nan garin, na fada musu zan taho a ranar na tafi da Inna da su Baba, sai Inna ta dage akan cewa ita dai ba zata je ba, ta fi son ko mutuwa ce ta mutu a can, amman hakan be saka na hakura ba saboda ina gudun kar wata rana a zo a kashe su, ashe ban tsira ba kuma ban isa na tsiratar da su daga mutuwa ko kaddara ba, a ranar da na ce zan ta ho a ranar komai ya faru, sai dai ni Allah be kaddara min zuwa a rana ba, wata kila da ni ma wani labarin ake a yanzu ba wannan bane, domin washe garin na ji abun da ya faru a radio, cikin tashin hankali na isa garin a lokacin gawar iyayena da yan'uwana kawai na tarar, kuma mutane suka tabbatar min da barayin nan sun tafi da Aminatu, mun yi ta sauraren ranar da za su aiko sako ko kuma su kira wayar wani su ce suna bukatar kudi amman shiru... Da farko na yi tunanin wata kila saboda bata haddace number na ba ne sai ta Baba shi kuma baya raye, hakan ya saka na dauki line sa na saka a wayata ina ta sauraren kira amman shiru, sai daga baya muka samu labarin cewa sojiji sun kai samame a gurin kuma sun bukutar da mata da yawa, na je can na duba Asbiti ban ganki ba, na zo nan gari na duba asibitocin gwannati ban ganki ba, har wasu daga cikin private hospital na duba, ban ganki ba, daga lokacin sai na sadakar cewar ko dai kin mutu ko kuma kin zauna can har abada”

Aminatu ta lumshe idanuwanta hawaye na zubo mata, the pain is unforgettably, kamin ka yi accepting reality kai moving up da rayuwarka.

“Sun kashe Baba, da Inna kisa na wulakanci da kaskanci, sun tarwatsa rayuwarmu, ko kadan wadannan mutanen basa da tausayi, su rasa wani abu mai girma da ake kira da imani, sai su kashe mutane ta tashi gari su kwace mata, ban san abun da suke so ba, ban san abun da muka yi musu ba, basa tsoron hakki”

Aminatu ta fada cikin kuka, sai Ali ya busar da iska bakinsa a hankali ya saka hannayensa aljihu. Hajiya Laraba ta ce.

“Ni abun da nake ganin, mun riga mun riski wani zamani da Annabi ya fada cewar kisa zai yawaita har wanda za a kashe be san dalilin da ya saka aka kashe shi ba, wanda yai kisan kuma be san dalilin daya saka ya aikata kisan ba, mu shigo wani zamani da ake fito na fito da Allah, kuma ba a jin tsoronta ba a fargabar azabarsa, mun riski wani zamani da ake kaunar haram ana ganin kamar ba komai bace, so idan Allah ya maka imani baka daga cikin mutanen dake aikata abubuwan da Annabi ya fada sai ka godewa Allah, domin hakan yana nuna zuciyarka mai kyau ce, domin dole ne wadannan abubuwan za su yi ta faruwa tun Annabi ya fada, sai dai ga wa za su faru Allah masani, kuma alkawarin Allah ba zai taba tashi ba, cewar Allah yayi alkawarin sai ya cika wuta, kuma a wata fadar Allah yace ki kare rayuwarku da iyalanku daga wuta, domin makamashinta shi ne mutane da duwatsu Allah ya tsare mu”

Sai duk suka amsa da Ameen.

“Ameen”

Sun dan dade suna tattaunawa da shi da Talba, da Hajiya Laraba kamin Ali ya katse su.

“Ya kamata ka huta nan, ina jin yau mutane da yawa sun ziyarce ka, kuma you talk alot marar lafiya kuma hutu ake so a gurinsa”

“Ai bari mu tashi, ka samu ka huta zan tafi da Aminatu domin ba zan barta nan tana ta kura ba, na lura da yadda take kin sakewa idan Momy ta shigo ba son haka nake ba”

Talba yayi murmushi yana kallon Hajiya Laraba da tai maganar.

“Idan kika ce zaki m rika dauke ta, ya azayi su saba? Momy dole na ta karbi Aminatu kamar yadda ya zama dole Aminatu ta karbi Momy a haka har su saba”

“Humm. Idan dai Allah ya baka lafiya, Aminatu zata tare a gidanta Inshallah”

“Daddy ma ya bani sati daya, ba dan ciwon nan ba da yanzu muna nan muna shirye shirye tarewar, ni kaina kuma na yi wannan tunanin”

“Ya dai kamata, Allah ya baka lafiya”

“Ameen”

Hajiya Laraba na mikewa tsaye, Aminatu ta mike tsaye Bashir ma haka, sai da ya mikawa Talba da Ali hannu sukai sallama yana yi ma Talba fatar samun sauki.

“Sai na samu lafiya zan zo har gidanka mu san juna da yardar Allah, amman kamin nan ka saka min number ka a wayar nan”

Talba ya fada yana mika masa wayar, sai ya karba ya saka masa number.

“Amman dai zai fi kyau Aminatu ta kwana a gidana ita kanta zata fi sakewa”

Talba ya karbi wayar yana jin kamar ya musanta hakan kuma baya son musantawa domin hakan na nuna be aminta da shi bane, ya san idan ya hana Aminatu ba zata jidadi ba, shi ma kuma ba zai ji ba. Sai dai halin da suka fito baya son wani abu ya sake faruwa da Aminatu.

“Ba a dade da sace yarinyar nan ba, idan kun zauna zata fada maka abubuwan da sukai ta faruwa, even Mama bana iya ce mata aa ne kawai Wallahi, domin har yanzu ba mu san wanda ya aikata hakan ba, kuma ba mu san dalilinsa na aikatawa ba, domin ba su yi requesting na kudi ba, that's mean akwai manufa a kasa”

Hajiya Laraba ta wara ido tana kallon Talba da mamaki. Can kuma ta girgiza kai ta yi murmushi ba tare da ta ce komai ba, shi kuma yaki yarsa ya dago kai su kalli juna ita da shi.

“Amman dai yanzu za su iya tafiya ku gaisa da a gidanka tare da matarka”

“Inshallahu babu abun da zai same ta”

Talba dai be sake cewa komai ba, har Hajiya Laraba ta fice Bashir ya fita sai ya rage daga shi sai Aminatu da Ali.

“Ranka ya dade zaka ba ni dama na yi sallama da matata ko kuma ya?”

Talba ya fada yana kallon Ali ya kalli Aminatu sannan ya nufi kofa ya fice daga dakin. Talba ya mike tsay still yana jin ciwo a kirjinsa sai dai ba kamar jiya da dazun ba.

“Come here”

Ya ware mata hannayensa sai ta matsa kusa da shi ta rumgume shi sosai.

“Na gode”

Ya saka hannunsa ya dago fuskarta yana kallon kwayar idonta dake yawo cikin nasa kwayar idon.

“I love you so much yarinyar nan”

Ya sauko da fuskarsa saman nata ta dora bakinsa saitin nata ya fara aikin nasa daya saba, sannan ya cire ya tsotsa tsirin hancinta yana shafa bayanta a hankali.

“Pray for me, in two days time na samu lafiya mu koma gidanmu”

“Allah ya baka lafiya”

Ta fada da yar siririyar muryarta.

“Ameen”

Ya sake maida bakin nasa cikin nata, wannan karon yawo yake da hannunsa a jikinta har zuwa gurin cikinta, sai ya dan rika mararta kadan ya matsa.

“Please ki kula da kanki, ban da wani ya zo yace ana sallama dake ki fita, ban da zuwa bakin gate ma ko da da yan gida ne, yanzu sai mun gano ko waye ya aikata wannan abun sannan hankali zai kwanta mu samu natsuwa”

“Tau”

“Tafi kar mu bata musu lokaci”

Ta sake shi ta nufi kofa, sai kuma ta juyo ta dawo ta rumgume shi. Murmushi yai ya shafa kanta dake cikin hijab yana jin kaunarta na kara shiga ransa. Sakinsa tai ta nufi kofar tana jin kunyar rumgumarsa da tai ta bude ta fice ba tare da juyo ba. Zaunawa yai saman gadonsa yana kallon kofar kamar ya san Ali zai shigo, yana kallon yanayinsa har ya iso kusa da shi, daya daga cikin alluran da suke gurin ya dauka ya fara hadawa.

“Kamar akwai abun da yake damunka”

“No gajiya ce kawai”

“A tunanina bama boyewa juna matsala ko damuwa”

“Wannan tana da banbanci, be zama lallai ka fahimta ba, kuma be dace ma fada maka a yanzu ba, maybe idan ka ji sauki”

“Na samu sauki sosai Ali, you know ina samun kulawar daya dace, kuma Alhamdulillah ina jin sauki sosai a jikin nawa fiye da jiya ko shekaranjiya, ni da nake fatar jibi na koma gida ma kasan bana son zaman asibiti ba”

Ali yayi murmushi, because he's friend was right ko kadan Talba baya son zaman asibiti sai idan ta kama dolen dole.

“Ba ni hannunka”

“Bana son allurar bachi ba”

“Bachi kake bukata yanzu, kai da kake son ka yi saurin warkewa kuma kake musu da likita”

Talba yayi dariya, ya mika masa hannun.

*** *** ***

Sai da suka fito sannan Hajiya Laraba take maganar Momy da Aminatu domin tun a dazun da ta marairaice a gabanta saboda shigowar Momy dakin ya tsaya mata a rai.

“Wannan tsoro tsoro da kike da Momy wahala zaki sha, wannan matar da kika gani bata da tausayi bata da imani ko kadan ga son kai, da ganin ta fi kowa saboda tana da dukiya, jira take har sai ni na fara mata magana saboda ba baiwa ta aje, bata san ko jin kai na fita ba, ayi mutum ace babu tunani babu Allah a ransa, wannan matar sai na ke ganin har wani abu zata iya yi ta raba tsakaninku da Talba, saboda yarta kuma kina ganinta kin san bata kaunarki”

Bashir ya girgiza kai duk da kasancewar ba san wanda ake magana akai ya ce.

“Wallahi bata iya komai da Aminatu, Auta…..tab muma da muke maza Baba ya tsaya mana da maganin kariya balle auta da yake ji da ita ba, ai ka'ida ce indai zuri'ar gidan mu ne, basa yi ba a musu”

Hajiya Laraba ta kalleshi da mamaki.

“Toh ashe ba banza kuka ba”

Yayi dariya yana shiga Napep dinsa, su kuma suka shiga baya yai ma Napep din key ya fara tukawa yana fadin.

“Indai asiri ne, ba dai ya kama mu ba, sai abun da Allah ya riga ya rubuta zai same ka iri wanda ba zaka iya tsallakewa ba din nan, amman ko iska bana jin zai iya zama a jikin Aminatu balle asiri, kuma duk wanda yai zai koma masa kai ma idan kai ma wani zai dawo maka”

Hajiya Laraba ta kalli Aminatu da mamaki ta ce.

“Toh mutanen kauye fa basa wasa, ka ce nan da nake gani an girka Aminatu”

Aminatu ta yi murmushi. Shi ma Bashir din murmushi yai ya ce.

“Babu wani girka, ai yan bori suke wannan, wannan ayoyin kur'ane da kuma abubuwan tsari irinsu kainuwa da kaikayi da su tunfafiya da ake hadawa ana sha, sai kuma addu'o'i ina dai ba a nan ba, kin ga ko wannan na tunfafiya idan mutum ya sha shi je kai bachinka, to sai idan boka zai iya zuwa saman ruwa ya shimfida Buzunsa (Windi) ya hau ya zauna a kai ruwa be natse da shi ba sannan zai maka aiki ya kamaka kin ga kuma abu ne mai wahala ko ma na ce ba zai taba faruwa ba, kin ga Bismillah dubu idan kika sha ta koma kawai ki kwanta, musamman kika hada da kai ka yi koma kan mashekiya da kula'uzai hmmm ba dai mutum sai dai Allah, ga kuma addu'a Aminatu ai ba ta wasa da addu'a domin tun muna kanana Baba yake koya maka ita kuma ya nuna maka muhimmancinta sai dai idan ka watsar dan kanka”

“Toh ai kin ji, haka ake so to ki kara rike addu'o'in nan da kyau ban da wasa, domin na tsorata sosai da matar nan wannan kiyayya ina dalili, ni ma fa saboda ke ne nake jin yau ta kara dauke min kai, domin can da ai ta kan dan gaisa da ni sama sama, yanzu kuma gani take mun aura miki Talba mun zama mikiyanta”

“Wacece wannan matar?”

Hajiya Laraba ta fara bashi labarin Momy da yadda akai ta rika shi har zuwa auren da akai da Aminatu, yadda komai ya wakana sai da Hajiya Laraba ta fada masa. A gidansa kofar gidansa ya faka Napep dinsa sannan ya fito tare da su Hajiya suka shiga cikin gidan, Maman Walida kamar ta hade Aminatu dan murna har da hawayenta, a gidan Aminatu ta wuni, Bashir ya tafi kai Hajiya Laraba na nata gidan domin a lokacin mijinta na gurin aiki balle ya zo ya dauke ta, tafiya kuma sai ta zama ta dole sannan yake aiko mata da direban gurin aikinsu ko kuma kannensa yace ya kaita inda zata je.
 Aminatu kam sai kusan Isha'i sannan ya kaita gidan Hajiya Laraba, bayan sun sha hira da matarsa da kuma shi kansa har yana kiran wasu yan'uwa da yake da numbers dinsu ya fada musu Aminatu tana raye gashi ma tare da ita, duk wanda ya kira aai ya bata wayar ta gaisa da su, a gidan ma Aminatu ta sha kuka sosai saboda zancen mutanen da aka kashe da suke, da kuma labarin da take ba shi na yadda akai ta fito daga dajin. Be sha wahalar gabe gidan ba, domin ya ga gurin dazun da ya kai Hajiya, a hanya ya kashe mata kudin da ya kai 5k duk abun da ya gani sai ya tsaya ya siya mata, ban da kayan dadin da yai ta kwaso mata dazun da rana.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son

gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

FARUK POV.

Bayan ya gama wayar da yake da Shamsu ya saka wayar aljihu ba tare da ya duba sakon daya shigo masa ba.

“Ya ce yayi magana da mutumen, akwai wasu a kasa kuma zai saka cijiya, zai nema min”

“To Allah ya taimaka, yanzu zaka je ka duba wadanda suke nan kenan”

“Eh haka ya ce”

“Allah ya tsare ya saka alheri”

“Amin”

Ya matsa kusa da cooler abinci ya bude ya dauki guri ya zuba, ya zauna saman kujera da zimmar ci amman ya saka cin saboda farinciki kuma ba dan baya jin yunwa ba. Two spoon yai ya aje ya dauki ruwa ya sha, Mama dai sai kallonsa take cike da kauna da kuma farinciki a lokaci daya.

“Ba zaka iya cin abincin ba?”

Yayi murmushi mai sauti

“Da ka daure ka fita ka siyo ko lemu ka sha, na san farinciki ba zai barka ka ci abincin ba”

“Wallahi ga kuma yunwa ina ji amman bana jiya cin komai”

Ya fada yana ciro wayarsa daga aljihunsa da zimmar tabawa, sai idanuwansa sukai arba da mail din dake saman screen din, hannu na rawa ya bude mail din, karantawa yake amman ya gagara kai wa karshe dai ya tsallake ya duba wanda ya turo masa sakon.

“What... ”

Ya furta kamin ya sake komawa farkon sakon yana karantawa, haka yai ta maimaita sakon tun yana karantawa a hargitse har ya natsu yana karantawa wai ya tabbatar ko ba gaske ba. A take ya aje wayar ya dubi inda yake kyautata zaton nan ne gabas a asibitin yai sujadar godiya ga Allah, Mama sai kallonsa take da mamaki sai dai tunaninta be bata cewar wani abun bane sabo, a zatonta

duk murnar kudin daya samu ne. Dagowa yai daga sujadar hawaye na bin fuskarsa.

“Mama aiki na samu?”

“Da gaske? Aiki dai? Baban yarinyar ne ya baka?”

Ya kasa amsa mata tambaya ko daya, zuciyarsa sai bugawa take da mugun karfi yana jin wani irin farinciki marar misaltuwa, farincikin da be taba jin irinsa ba, hannu ya saka ya dage kansa yana hawaye.

“Alhamdulillah Allah, Faruk baka amsa min ba? Baban yarinya ne ya baka aiki?”

“Aa aiyukan da nake ta applying ne wani ya fito, Mama daga Xullers Company, wani babban kamfani kasar China ne dake hako ma'adanai a Nigeria, Wallahi na kasa yarda”

Mama ta rufe baki da mugun mamaki tana zaro ido.

“Kai da kanka Faruk? ”

“Mama gashi”

Ya mika mata wayar duk kuwa da kasancewar ya san ba zata iya karantawa ba.

“Kuma ba yan dafara ba ne? Na ji ana fadar mutane suna damfara ba, balle kai da aka ji ka samu kudin nan”

“Yau kwana uku da turo sakon Mama, ba damfara ba ce”

“Allahu akbar Allah mai kyauta da kari, Allah mai yadda ya so a lokacin da ya so ga wanda ya so, Allahu Akbar”

Mama da fada ita kanta tana hawayen farinciki. Komai ya zo musu kamar mafarki, tsakamin shi da Mama sai ka rasa waya fi wani farinciki.
A daren ranar Faruk kwana yai yana godiya ga Allah ya raya dare da sallah nafila. Washe gari ya tura musu duk wani abu da suka bukata ta mail din. Within a week rayuwar Faruk ya canja ya koma wani mutum na dabam da be taba mafarkin zama ba, balle tunaninsa ya bashi wata rana haka zai faru da shi. Gida suka kamfanin ya bashi a Lagos inda babban branch dinsu yake, da kudi mai yawa da zai wadatace shi ya kimtsa rayuwarsa na wani lokaci. Kwansa biyu a Lagos ya suka masa booking din jirki ya sauka sokoto, daga can ya hau mota zuwa Gusau, yana isowa wanka kawai yai ya shirya cikin wasu tufafin masu tsada da yai kuzurinsu tun daga can ya nufi asbitin gurin Mama, domin har lokacin tana asibitin suna bata kulawa da ya kamata. Tun kamin ya tura kofar dakin ya shiga ya ji dariyar Rukaiya, na fada musu yau zai dawo sai dai be fada musu lokacin da zai sauka ba sai ganinsa kawai sukai kamar daga sama.

“Yan Tafiya har an sauka”

Mama ta fada, sai Ramla tai murmushi ta dauki kular da ta kawo ma Mama farfesu kamar yadda ta saba kullum sai ta shigo mata da wani abun idan zata zo.

“Sannu da zuwa”

Ta fada tana kallonsa, sai ya amsa mata da murmushi a fuskarsa.

“Sannu Ramla ya aiki”

“Alhamdulillah”

Ta amsa tana murmushi sannan ta nufi kofa ta bude ta fice, for no reason ya juya yana kallonta har ta fice, sannan ya juyo ya kalli Rukaiyah dake kallonsa tana murmushi, dan hade rai yai gudun kar ta samu wata dama ta yin masa zargi ko wani tunanin.

“Sannu da zuwa”

“Yauwa”

Ya amsa sannan ya zauna kusa da mahaifiyarsa da ita ma kanta ta canja kala. Balle kuma shi da har wani kamshin tsadadden turare yake.

“Mama ya jikin?”

“Alhamdulillah Wallahi na samu sauki sosai, na ji ma suna maganar sallama ta gobe”

“Maa Shaa Allah, haka Rukaiyah ta fada min jiya a waya ai”

“Ya hanya? Ina ta tunani da zullumin ashe har ka dawo”

“Na dawo, shiyasa ai ban fada miki lokacin da zamu ta so ba na san zaki yi ta jin tsoro, duk da jirgi muka hau da zamu tafi a dawowa ma jirgin muka hawa”

“Laaa Yaya jirgi ka shiga?”

“Ni kaina na ji dabam, i never thought wata rana zan shiga jirgi zuwa wani gari da sunan aiki, ko gidan da suka ba ni abun kallo ne Mama ga motar kamfani idan ina bukata, amman na fada musu zan siye tawa motar”

“Gaskiya kam, kara dai ka siye taka to wai yanzu a can zaka zauna kenan?”

“Eh a can zan zauna, amman aikin ana canja zai iyu yuyuwa a canja ni zuwa wani gari nan gaba ko ma zuwa wata kasar, amman for now dai a Lagos zan zauna”

Mama ta yi murmushin jindadi.

“Shamsu yana ta hidima yaron nan yana da kirki, duk abun da ya saka a sabon gidan nan sai ya zo ya fada min, wani lokacin har a wayarsa yake nuna min hotuna gida yayi kyau kamar ba naka ba”

“Kamar ba na mu ba dai Mama, ni ma yana kirana a waya ya fada min komai da yake, yana kuma turon min hoton komai. Da na yi tunanin a can zamu zauna ashe Allah yana nan yana nasa tsarin na dabam yanzu sai dai mu rika zuwa muna duba gidan ko kuma idan mun sauka”

Sanin manufarsa ya saka Mama murmushi ta girgiza kai.

“Aa ni kam ina nan, a can kuma sai ka tare tare da matarka, ni kuma nan ya ishe ni har sai na nemi abokan zama ma, tun da wata rana Rukaiya aure zata yi”

“Mama ba zaki je Lagos din ba?”

“Aa ban dai hana naje ganinku ba, Sultan ma da zaka yarda da ka bar min shi a nan sai a saka shi makaranta mai kyau in ya so idan an yi hutu sai ya je can yai hutu”

“Amman Mama zan fi jindadi idan muka zauna a can tare”

“Aa ni dai shawarar da zan baka da zaka dauka da ka cire komai a ranka ka natsu ka samu wata wanda ka natsu da ita ka barwa Allah zabi kai aurenka, a ganina zaka fi kima idan kana da aure”

Ya dan yi murmushi yana karbar abincin da Rukaiya take mika masa, a kokarinsa na kawar da maganar ya ce.

“Ina Sultan?”

“Yana gurin Anty a can ya kwana”

Rukaiya ta amsa masa, sannan ta koma ta zauna a inda ta tashi.

“Yaya yaushe zaka siye motar?”

“Sai na karbi certificate na tuki, ina son na samu natsuwa na shiga makarantar koyon tuki, a can lagos domin sati daya suka ba ni na shirya komai nawa na koma can na kama aiki”

“Haka ya kamata, Allah ya taimaka maka”

Mama ta fada sai duk suka amsa da Ameen. Sannan Rukaiya ta mike tsaye tana fadin.

“Bari na karbo maka lemu shagon waje”

“Okay”

“Idan kuma zai sha Lemun Kwakwa gashi nan wanda Ramla tai min”

Mama ta fada tana nuna masa jug din.

“Wai ita yaushe zata daina wannan wahalar ne?”

“Sai ranar da ka karbi soyayyarta Yaya, kai baka lura duk sabida kai take somai ba”

Rukaiya ta fada tana dariya, sai ya tabe baki.

“Ashe ko tana da aiki, ni a yanzu babu mace a gabana, Rafi'a ma ina son na samu lokaci tsakanin gobe da jibi, na kai mata duk abun da ya kamata kuma na biya hakkinta data kashe na”

“Ni fa sai nake ganin kamar babu cikin nan, domin da akwai shi da yanzu ta zo karbar wani abu, kuma ni ko mutane ban ji ana labarin cikin ba”

“Aikuwa da ta ga tijara, ta zubar min da ciki? Hmmm”

“To ya zaka yi? Dan Allah ka saka mata ido kawai ko a yanzu ai Allah ya nuna maka mai hakuri mawadaci ne, domin na tabbatar da zata san haka zai faru da kai da bata maka wulakanci ba balle ta guje ka”

“Koma dai minene gaskiya ba zan kyale ta ba, idan ta zubar min da ciki”

“Allah ya sauwake”

Ya amsa da Ameen. Sannan Rukaiyah ta fice ganin alamar ba zai sha lemun kwakwa ba ta fita siyo masa na gora. Tana fita daga ward din ta hango Kabir tsaye yana waya dayan hannunsa sanye a aljihu, ita yake ta kallo har ta karaso kusa da shi.

“Ina wuni”

Ta gaishe shi ganin yadda yake sakar mata murmushi alamar dake nuna hankalinta na gurinsa. Sauke wayar yai daga kunnensa ya katse kiran.

“Matar nan kina da tsada, tun wacan ganin da na yi miki ban sake saka ki a idona ba”

“Ashe kana gane ni”

“Really? Ni makaho ne da ba zan gane ki ba? Amman yarinyar nan kin sha da ni”

Ya fada yana murmushi mai sauti, ita ma murmushin tai ta cigaba da tafiya sai ya juyo ya jera tare da ita yana takawa.

“Ya mai jikin?”

“Ta ji sauki, ina tunanin ma gobe za a sallame mu”

“Okay, ni ma wanda nake zirga zirga a kansa yau aka sallame shi ya samu sauki”

“Allah sarki Allah kara lafiya”

“Ameen”

Rakata yai har wajen asibitin ta siyo abun da zata siyo suka dawo tare suna tafe yana janta da hira, shi yake rike da ledar lemun har suka iso cikin asibitin.

“Ina zuwa dan jira ni zan dauko abu a mota please”

“Ba matsala”

Ta fada, sai ya juya da sauri ya nufi bangaren da ya faka motarsa yana isa ya bude motar ya dauko katinsa ya saka mata a ledar sannan ya rufe motar. Ko da ya iso har ta nemi guri ta zauna kusa da inda ya barta tsaye.

“Da alama dai wannan matar raguwa ce, i don't even know your name”

“Rukaiya”

“Nice name, ni kuma sunana Muhammad Kabir”

Ta yi murmushi sannan ta mika hannu ta karbi ledar.

“Na gode sosai”

“Amman kamin ki sha lemun ki duba gorar da kyau so that ki tabbatar be yi expire ba”

“Inshallah”

Ta amsa ba tare da tunanin komai ba, ta nufi ward dinsu, shi kuma ya nufi wani bangaren na asibiti. Taba shiga ta samu guri ta zauna ta bude ledar da zimmar duba lemun sai tai arba a katinsa, saurin rufe ledar tai ta ciro lemun cikin hikima ta mikawa Faruk.
Washe garin ranar aka sallami Mama, da kafafuwanta take takawa sam ba zaka ganta ka ce ita ce wanda aka shigo da ita jiki a mace bata iya tafiya ba. A tsohon gidansu suka sauka, wanda hakan ya bawa makota da basu samu damar zuwa asibitin dubata ba sukai ta shigowa wasu na mata ya jiki wasu kuma na mata barka da arzikin siyen gida da danta yai ba ma daya ba. Domin labarin siyen gidan ya karade ko'ina a unguwar. Sai da Mama ta kwana a gidan sannan ta shirya tarewa a sabon gidan da Faruk ya siya musu, bata bukatar zuwa da komai sai dan abun da ba a rasa ba. Shi ma wanda ya zame mata dole ita da Rukaiya, duk wani abu na al'ada sai da Faruk ya ware kudi akai na dafa abincin a rabawa makotan da suka zo rakiya, daman ya fadawa Shamsu cewar ayi karatu a gidan tun a lokacin da yake aikin zuba furnitures a gidan.
Kamar yadda ya fada gidan bangare biyu ne bangaren Mama da kuma nasa bangaren, an gyara bangaren Mama an saka mata komai da take bukata ciki har da kayan kallo. Nasa bangaren kuma katifa ce kawai sai yar kujerar zama da dan abun da ba a rasa ba. Kusan duk wanda ya zo gidan sai yayi mamaki ace gidan Faruk ne, Faruk dai da wasu ke ganin kamar ba zai iya samun wannan rufin asibiti ba, gidan ne madaidaici ba kato can can ba kuma ba karamin gida ba, tsakar gidan interlock ne main house din kuma ko'ina tiles ne har jikin ginar gidan ga shuke shuke da akai ado da su daga cikin gidan gurin gate zuwa bakin kofar falon.
Washe garin ranar da suka tare a gidan, Faruk ya shiga wata sabuwar super market da aka bude a unguwar Lalan, tare da dansa Sultan ya siye dan abu bukata na yau da kullum da salulai. Bayan ya biya kudin ya fito ya hadu da Fahat wanda shi ma ya fito daga cikin super market, sai dai Fahat din be lura da shi ba, ko da ma ya ganshi ba gane shi zai yi ba, sai dai Faruk ba zai taba manta fuskar mutumen da ya so taimakonsa ba.

“Ranka ya dade”

Fahat ya juyo ya kalleshi yana murmushi irin na wanda ya ga fuskar sani amman be gane wanene ba. Ya mika masa hannu

“Sannu ya gida”

“Ranka ya dade baka gane ni ba”

“Na dai ga fuskar sani amman na manta sunan da inda na san fuskar Wallahi”

“Allah sarki ni ai ba zan manta ka ba, sunana Faruk...”

In brief Faruk ya yi masa bayanin inda suka hada har suka san juna, sai Fahat ya washe hakora yana dariya.

“An yi haka, tabbas, ka ce ka yi kudi shiyasa baka nemi ni ba, yanzu ai kai ne ranka ya dade ba ni ba”

Ya fada yana kallon dress din Faruk na kananan kaya da suka fito da shi. Faruk yayi murmushi.

“Ba haka bane, ina da niyar zuwa, kasan tafiyar da na yi ne ya saka ban samu na zo ba, lokacin da na dawo kuma na tarar mahaifiyata ba lafiya, sai hankali ya tafi can muna cikin haka sai ga aiki na fito mun Lagos daya daga cikin wadanda na yi applying”

Fahat ya mika masa hannu yana taya shi murna.

“Maa Shaa Allah, Allah ya tabbatar da alheri ya bada sa'a”

“Amin Amin na gode”

“Wannan yaron ka ne?”

“Eh Sultan she's my first born”

“Maa Shaa Allah, Allah ya raya. Ba dan kar na yi karabanni ba da nace a kafa kake ko da abun hawa?”

“Tukuna dai abun hawan muna da biki nan gaba kadan”

“Gaskiya ya kamata, ni ma ai sai a labani na samu wata, amman kamin nan mu je na sauke ka”

“Aa ka bar shi kawai,mun gode”

“Ka raina kenan yanzu ka fi karfina bari na ja baya”

Faruk yayi dariya ya kama hannunn Sultan yana fadin.

“Ina gudun wahalar da kai ne kawai”

A tare suka nufi motar Fahat din da hannunsa ke rike da Arabian Perfumes masu tsada da kamshi. Fahat ya budewa Sultan gidan baya ya shiga Faruk ya shiga Front seat, Fahat kuma ya shiga mazaunin direba ya ja motar suka hau titi. Suna tafe suna dan taba hira can Fahat ya tambayi inda zai sauke shi, Faruk ya fada masa unguwarsu Rafi'ah, wani irin faduwar gaba Fahat ya ji wanda ya haddasa

masa ciwon kai. Faruk yana ta kwatancin inda za su bi har suka gisa bakin gate din gidansu Baturiya, ba karamin mamaki ne ya kama Fahat ba, ta madubin motar ya rika satar kallon Sultan zuciyarsa na raya masa shi ne yaron Baturiya, domin sai a yanzu yake ganin kamaninta kadan a fuskar Sultan.

“Ka san wata a nan gidan ne?”

Fahat ya tambaya yana kallon gate din gidan.

“Eh Ex-wife dita na zo gani zan bata hakkinta kuma Sultan yana son ganinta”

“So ka rabu da matarka kenan?”

“Yeah mun rabu”

“That's mean Baturiya matarka ce?”

Faruk ya masa kallon mamaki.

“Ka santa ne?”

“No...”

Sai kuma ya rasa mai zai ce. Faruk ya ce.

“Karka maida ni yaro mana, ya akai kasan sunanta?”

“Abun da nake son sani, kun rabu gaba daya”

“Mun rabu ba gaba daya ba, domin akwai cikina a jikinta shiyasa ma nake son bata hakkinta a yanzu”

“So duk abun da aka fada min gaskiya ne about her, sai dai ni na so ta ba da sanin ta taba aure ba ma, domin bata taba fada min ba, sai bincike ne ya gano min haka”

Faruk ya runtse ido ta bude yana mamakin furucin Fahat.

“Ka taba son Rafi'a ne?”

“Yeah, amman yarinyar nan ta yaudare ni, shiyasa bana shakkar fadawa kowa I'm sorry to say baka yi dacen mata ba, duk da yake kun rabu amman akwai da a tsakaninku”

Ya mikawa Faruk wayarsa da number Baturiya da ya goge ya saka a blacklist yana nuna masa sakwannin da take tura masa. Faruk yayi murmushin takaici.

“If na fada maka abun da ya raba ni da ita you will be shock”

Fahat yayi murmushi.

“Lemme text her yanzu nan zata fito”

Kusan a tare suka bude motar suka fito, Fahat ya zagayo bangaren da Faruk yake tsaye da Sultan yana aika mata da sako cewar yana kofar gida, domin baya jin zai iya kiranta ma. Har yanzu akwai sauran sonta a zuciyarsa domin cire so lokaci daya ba abu ne da zai iya yi a take ba, sai dai yafi tsanarta fiye da son ta a yanzu saboda sanin true color ta, musamman alakar dake tsakaninta da mahaifinsa, ko da wani dabam take wannan alakar ba ya ji zan iya zaman aure da ita bayan ta yi masa karya, balle kuma a yanzu da yake jin aure ya haramta a tsakaninsu.

BATURIYA POV.

Kamar wanda akai wa bushara da daren mutuwarta, haka Baturiya ta rika kuka tun daga kofar gidan har cikin gidan, tsabar bakincikin da ya rufe mata zuciya ya rufe ya tafi har cikin ido ya rufe su, ga hawaye da ya hana ta ganin komai sai lallaben kofa take har ta shiga cikin gidan. Umma na ganinta ta yo kanta da sauri ta rikata.

“Subhanallahi lafiya? Miya same ki?”

“Umma na rasa Fahat rashi na har abada, na rasa shi Umma, Fahat ba zai taba aurena ba”

Ta fada cikin wani irin kuka da bata san ranar da zai tsaya mata ba, kukan da take ne ya bawa Umma tausayi ba wai domin Fahat ya fasa aurenta ba, domin a tunanin Umma Baturiya zata samu wanda ya fisa ma nesa ba kusa ba, amman saboda ta shaku da soyayyarsa ya saka bata ganin komai idon ya rufe har bata iya komai sai kuka kamar wanda akai wa mutu.
Tun daga ranar Baturiya bata sake wani abu wai shi walwala, abinci ma sai Umma ta matsa mata take ci, da zarar ta tuna da Fahat sai ta ji kamar ta cire ranta daga jikinta ta huta.
Cikin kwana biyu ta koma kamar ba ita ba, daman can jiki babu wani dogon afki balle kuma yanzu da damuwa ke son cinyeta. Ba tana bakincikin rabuwa da Fahat saboda fargaban samun wani wanda ya fi shi ba, no soyayyarsa da tai tahiri a zuciyarta ya saka take jin abu ne mai wahala ta sake samun wanda zata so kamar ranta irin Fahat. Gashi a yanzu da ya nisance ta sai sonsa ya kara shiga ranta ya hana ta sukuni, motsi daya da biyu sai ta tuna yadda suke son junansu. Har yanzu bata fasa tura masa sakon ban hakuri ba, ta kara hakura ta goge number sa balle ta cire shi a ranta, idan ta kira number shi bata shiga saboda yayi blocking dinta, sakonta da kiransa duka ba za su yi appearing a wayarsa sai a block list dinsa. Karya tai ma Umma cewar wai ya bi zabin mahaifiyarsa ya hakura da ita, ba ta yarda ta fadawa Umma komai ba, Umma kuma bata fasa nuna mata gari da yawa maye ba zai ci kansa ba, maza suna nan da yawa, kamar yadda ta same shi haka zata samu wani. Sai dai duk kalaman da Umma take mata na son kwantar mata da hankali, be yi tasiri a zuciyarta ba.

As always da ta sabawa kanta da zaman kadaici a daki, tana zaune dakin ta yi ruf da ciki tana ta karatun jaki, sako ya shigo wayarta, cikin rashin kuzari ta dauki wayar tana duba sunan wadan ya sakon mata da sakon sai ta ji kamar an mata allura, da sauri ta zabura ta mike tsaye ta, a gaggauce ta cire daurin kirjin dake jikinta ta saka zane da riga na atamfa ta rufe jikinta da Hijab ta fito da sauri zuciyarta na rawa ta saka talkamin Umma ta fice daga falon zuwa gate ko wayar

bata fito da ita ba, tsabar zumudi da rawar kafa Fahat ya turo mata sako cewar yana waje yana jiranta akwai maganar da zai yi da ita.

*_(Kun ga Labarin Aminatu da Faruk? Wallahi True life ne, amman na canja abubuwa da dama akai, but cikin kankanen lokaci Allah ya canja masa rayuwa)_*

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

FARUK POV.

Bayan ya gama wayar da yake da Shamsu ya saka wayar aljihu ba tare da ya duba sakon daya shigo masa ba.

“Ya ce yayi magana da mutumen, akwai wasu a kasa kuma zai saka cijiya, zai nema min”

“To Allah ya taimaka, yanzu zaka je ka duba wadanda suke nan kenan”

“Eh haka ya ce”

“Allah ya tsare ya saka alheri”

“Amin”

Ya matsa kusa da cooler abinci ya bude ya dauki guri ya zuba, ya zauna saman kujera da zimmar ci amman ya saka cin saboda farinciki kuma ba dan baya jin yunwa ba. Two spoon yai ya aje ya dauki ruwa ya sha, Mama dai sai kallonsa take cike da kauna da kuma farinciki a lokaci daya.

“Ba zaka iya cin abincin ba?”

Yayi murmushi mai sauti

“Da ka daure ka fita ka siyo ko lemu ka sha, na san farinciki ba zai barka ka ci abincin ba”

“Wallahi ga kuma yunwa ina ji amman bana jiya cin komai”

Ya fada yana ciro wayarsa daga aljihunsa da zimmar tabawa, sai idanuwansa sukai arba da mail din dake saman screen din, hannu na rawa ya bude mail din, karantawa yake amman ya gagara kai wa karshe dai ya tsallake ya duba wanda ya turo masa sakon.

“What... ”

Ya furta kamin ya sake komawa farkon sakon yana karantawa, haka yai ta maimaita sakon tun yana karantawa a hargitse har ya natsu yana karantawa wai ya tabbatar ko ba gaske ba. A take ya aje wayar ya dubi inda yake kyautata zaton nan ne gabas a asibitin yai sujadar godiya ga Allah, Mama sai kallonsa take da mamaki sai dai tunaninta be bata cewar wani abun bane sabo, a zatonta duk murnar kudin daya samu ne. Dagowa yai daga sujadar hawaye na bin fuskarsa.

“Mama aiki na samu?”

“Da gaske? Aiki dai? Baban yarinyar ne ya baka?”

Ya kasa amsa mata tambaya ko daya, zuciyarsa sai bugawa take da mugun karfi yana jin wani irin farinciki marar misaltuwa, farincikin da be taba jin irinsa ba, hannu ya saka ya dage kansa yana hawaye.

“Alhamdulillah Allah, Faruk baka amsa min ba? Baban yarinya ne ya baka aiki?”

“Aa aiyukan da nake ta applying ne wani ya fito, Mama daga Xullers Company, wani babban kamfani kasar China ne dake hako ma'adanai a Nigeria, Wallahi na kasa yarda”

Mama ta rufe baki da mugun mamaki tana zaro ido.

“Kai da kanka Faruk? ”

“Mama gashi”

Ya mika mata wayar duk kuwa da kasancewar ya san ba zata iya karantawa ba.

“Kuma ba yan dafara ba ne? Na ji ana fadar mutane suna damfara ba, balle kai da aka ji ka samu kudin nan”

“Yau kwana uku da turo sakon Mama, ba damfara ba ce”

“Allahu akbar Allah mai kyauta da kari, Allah mai yadda ya so a lokacin da ya so ga wanda ya so, Allahu Akbar”

Mama da fada ita kanta tana hawayen farinciki. Komai ya zo musu kamar mafarki, tsakamin shi da Mama sai ka rasa waya fi wani farinciki.
A daren ranar Faruk kwana yai yana godiya ga Allah ya raya dare da sallah nafila. Washe gari ya tura musu duk wani abu da suka bukata ta mail din. Within

a week rayuwar Faruk ya canja ya koma wani mutum na dabam da be taba mafarkin zama ba, balle tunaninsa ya bashi wata rana haka zai faru da shi. Gida suka kamfanin ya bashi a Lagos inda babban branch dinsu yake, da kudi mai yawa da zai wadatace shi ya kimtsa rayuwarsa na wani lokaci. Kwansa biyu a Lagos ya suka masa booking din jirki ya sauka sokoto, daga can ya hau mota zuwa Gusau, yana isowa wanka kawai yai ya shirya cikin wasu tufafin masu tsada da yai kuzurinsu tun daga can ya nufi asbitin gurin Mama, domin har lokacin tana asibitin suna bata kulawa da ya kamata. Tun kamin ya tura kofar dakin ya shiga ya ji dariyar Rukaiya, na fada musu yau zai dawo sai dai be fada musu lokacin da zai sauka ba sai ganinsa kawai sukai kamar daga sama.

“Yan Tafiya har an sauka”

Mama ta fada, sai Ramla tai murmushi ta dauki kular da ta kawo ma Mama farfesu kamar yadda ta saba kullum sai ta shigo mata da wani abun idan zata zo.

“Sannu da zuwa”

Ta fada tana kallonsa, sai ya amsa mata da murmushi a fuskarsa.

“Sannu Ramla ya aiki”

“Alhamdulillah”

Ta amsa tana murmushi sannan ta nufi kofa ta bude ta fice, for no reason ya juya yana kallonta har ta fice, sannan ya juyo ya kalli Rukaiyah dake kallonsa tana murmushi, dan hade rai yai gudun kar ta samu wata dama ta yin masa zargi ko wani tunanin.

“Sannu da zuwa”

“Yauwa”

Ya amsa sannan ya zauna kusa da mahaifiyarsa da ita ma kanta ta canja kala. Balle kuma shi da har wani kamshin tsadadden turare yake.

“Mama ya jikin?”

“Alhamdulillah Wallahi na samu sauki sosai, na ji ma suna maganar sallama ta gobe”

“Maa Shaa Allah, haka Rukaiyah ta fada min jiya a waya ai”

“Ya hanya? Ina ta tunani da zullumin ashe har ka dawo”

“Na dawo, shiyasa ai ban fada miki lokacin da zamu ta so ba na san zaki yi ta jin tsoro, duk da jirgi muka hau da zamu tafi a dawowa ma jirgin muka hawa”

“Laaa Yaya jirgi ka shiga?”

“Ni kaina na ji dabam, i never thought wata rana zan shiga jirgi zuwa wani gari da sunan aiki, ko gidan da suka ba ni abun kallo ne Mama ga motar kamfani idan ina bukata, amman na fada musu zan siye tawa motar”

“Gaskiya kam, kara dai ka siye taka to wai yanzu a can zaka zauna kenan?”

“Eh a can zan zauna, amman aikin ana canja zai iyu yuyuwa a canja ni zuwa wani gari nan gaba ko ma zuwa wata kasar, amman for now dai a Lagos zan zauna”

Mama ta yi murmushin jindadi.

“Shamsu yana ta hidima yaron nan yana da kirki, duk abun da ya saka a sabon gidan nan sai ya zo ya fada min, wani lokacin har a wayarsa yake nuna min hotuna gida yayi kyau kamar ba naka ba”

“Kamar ba na mu ba dai Mama, ni ma yana kirana a waya ya fada min komai da yake, yana kuma turon min hoton komai. Da na yi tunanin a can zamu zauna ashe Allah yana nan yana nasa tsarin na dabam yanzu sai dai mu rika zuwa muna duba gidan ko kuma idan mun sauka”

Sanin manufarsa ya saka Mama murmushi ta girgiza kai.

“Aa ni kam ina nan, a can kuma sai ka tare tare da matarka, ni kuma nan ya ishe ni har sai na nemi abokan zama ma, tun da wata rana Rukaiya aure zata yi”

“Mama ba zaki je Lagos din ba?”

“Aa ban dai hana naje ganinku ba, Sultan ma da zaka yarda da ka bar min shi a nan sai a saka shi makaranta mai kyau in ya so idan an yi hutu sai ya je can yai hutu”

“Amman Mama zan fi jindadi idan muka zauna a can tare”

“Aa ni dai shawarar da zan baka da zaka dauka da ka cire komai a ranka ka natsu ka samu wata wanda ka natsu da ita ka barwa Allah zabi kai aurenka, a ganina zaka fi kima idan kana da aure”

Ya dan yi murmushi yana karbar abincin da Rukaiya take mika masa, a kokarinsa na kawar da maganar ya ce.

“Ina Sultan?”

“Yana gurin Anty a can ya kwana”

Rukaiya ta amsa masa, sannan ta koma ta zauna a inda ta tashi.

“Yaya yaushe zaka siye motar?”

“Sai na karbi certificate na tuki, ina son na samu natsuwa na shiga makarantar koyon tuki, a can lagos domin sati daya suka ba ni na shirya komai nawa na koma can na kama aiki”

“Haka ya kamata, Allah ya taimaka maka”

Mama ta fada sai duk suka amsa da Ameen. Sannan Rukaiya ta mike tsaye tana fadin.

“Bari na karbo maka lemu shagon waje”

“Okay”

“Idan kuma zai sha Lemun Kwakwa gashi nan wanda Ramla tai min”

Mama ta fada tana nuna masa jug din.

“Wai ita yaushe zata daina wannan wahalar ne?”

“Sai ranar da ka karbi soyayyarta Yaya, kai baka lura duk sabida kai take somai ba”

Rukaiya ta fada tana dariya, sai ya tabe baki.

“Ashe ko tana da aiki, ni a yanzu babu mace a gabana, Rafi'a ma ina son na samu lokaci tsakanin gobe da jibi, na kai mata duk abun da ya kamata kuma na biya hakkinta data kashe na”

“Ni fa sai nake ganin kamar babu cikin nan, domin da akwai shi da yanzu ta zo karbar wani abu, kuma ni ko mutane ban ji ana labarin cikin ba”

“Aikuwa da ta ga tijara, ta zubar min da ciki? Hmmm”

“To ya zaka yi? Dan Allah ka saka mata ido kawai ko a yanzu ai Allah ya nuna maka mai hakuri mawadaci ne, domin na tabbatar da zata san haka zai faru da kai da bata maka wulakanci ba balle ta guje ka”

“Koma dai minene gaskiya ba zan kyale ta ba, idan ta zubar min da ciki”

“Allah ya sauwake”

Ya amsa da Ameen. Sannan Rukaiyah ta fice ganin alamar ba zai sha lemun kwakwa ba ta fita siyo masa na gora. Tana fita daga ward din ta hango Kabir tsaye yana waya dayan hannunsa sanye a aljihu, ita yake ta kallo har ta karaso kusa da shi.

“Ina wuni”

Ta gaishe shi ganin yadda yake sakar mata murmushi alamar dake nuna hankalinta na gurinsa. Sauke wayar yai daga kunnensa ya katse kiran.

“Matar nan kina da tsada, tun wacan ganin da na yi miki ban sake saka ki a idona ba”

“Ashe kana gane ni”

“Really? Ni makaho ne da ba zan gane ki ba? Amman yarinyar nan kin sha da ni”

Ya fada yana murmushi mai sauti, ita ma murmushin tai ta cigaba da tafiya sai ya juyo ya jera tare da ita yana takawa.

“Ya mai jikin?”

“Ta ji sauki, ina tunanin ma gobe za a sallame mu”

“Okay, ni ma wanda nake zirga zirga a kansa yau aka sallame shi ya samu sauki”

“Allah sarki Allah kara lafiya”

“Ameen”

Rakata yai har wajen asibitin ta siyo abun da zata siyo suka dawo tare suna tafe yana janta da hira, shi yake rike da ledar lemun har suka iso cikin asibitin.

“Ina zuwa dan jira ni zan dauko abu a mota please”

“Ba matsala”

Ta fada, sai ya juya da sauri ya nufi bangaren da ya faka motarsa yana isa ya bude motar ya dauko katinsa ya saka mata a ledar sannan ya rufe motar. Ko da ya iso har ta nemi guri ta zauna kusa da inda ya barta tsaye.

“Da alama dai wannan matar raguwa ce, i don't even know your name”

“Rukaiya”

“Nice name, ni kuma sunana Muhammad Kabir”

Ta yi murmushi sannan ta mika hannu ta karbi ledar.

“Na gode sosai”

“Amman kamin ki sha lemun ki duba gorar da kyau so that ki tabbatar be yi expire ba”

“Inshallah”

Ta amsa ba tare da tunanin komai ba, ta nufi ward dinsu, shi kuma ya nufi wani bangaren na asibiti. Taba shiga ta samu guri ta zauna ta bude ledar da zimmar duba lemun sai tai arba a katinsa, saurin rufe ledar tai ta ciro lemun cikin hikima ta mikawa Faruk.
Washe garin ranar aka sallami Mama, da kafafuwanta take takawa sam ba zaka ganta ka ce ita ce wanda aka shigo da ita jiki a mace bata iya tafiya ba. A tsohon gidansu suka sauka, wanda hakan ya bawa makota da basu samu damar zuwa asibitin dubata ba sukai ta shigowa wasu na mata ya jiki wasu kuma na mata barka da arzikin siyen gida da danta yai ba ma daya ba. Domin labarin siyen gidan ya karade ko'ina a unguwar. Sai da Mama ta kwana a gidan sannan ta shirya tarewa a sabon gidan da Faruk ya siya musu, bata bukatar zuwa da komai sai dan abun da ba a rasa ba. Shi ma wanda ya zame mata dole ita da Rukaiya, duk wani abu na al'ada sai da Faruk ya ware kudi akai na dafa abincin a rabawa makotan da suka zo rakiya, daman ya fadawa Shamsu cewar ayi karatu a gidan tun a lokacin da yake aikin zuba furnitures a gidan.
Kamar yadda ya fada gidan bangare biyu ne bangaren Mama da kuma nasa bangaren, an gyara bangaren Mama an saka mata komai da take bukata ciki har da kayan kallo. Nasa bangaren kuma katifa ce kawai sai yar kujerar zama da dan abun da ba a rasa ba. Kusan duk wanda ya zo gidan sai yayi mamaki ace gidan Faruk ne, Faruk dai da wasu ke ganin kamar ba zai iya samun wannan rufin

asibiti ba, gidan ne madaidaici ba kato can can ba kuma ba karamin gida ba, tsakar gidan interlock ne main house din kuma ko'ina tiles ne har jikin ginar gidan ga shuke shuke da akai ado da su daga cikin gidan gurin gate zuwa bakin kofar falon.
Washe garin ranar da suka tare a gidan, Faruk ya shiga wata sabuwar super market da aka bude a unguwar Lalan, tare da dansa Sultan ya siye dan abu bukata na yau da kullum da salulai. Bayan ya biya kudin ya fito ya hadu da Fahat wanda shi ma ya fito daga cikin super market, sai dai Fahat din be lura da shi ba, ko da ma ya ganshi ba gane shi zai yi ba, sai dai Faruk ba zai taba manta fuskar mutumen da ya so taimakonsa ba.

“Ranka ya dade”

Fahat ya juyo ya kalleshi yana murmushi irin na wanda ya ga fuskar sani amman be gane wanene ba. Ya mika masa hannu

“Sannu ya gida”

“Ranka ya dade baka gane ni ba”

“Na dai ga fuskar sani amman na manta sunan da inda na san fuskar Wallahi”

“Allah sarki ni ai ba zan manta ka ba, sunana Faruk...”

In brief Faruk ya yi masa bayanin inda suka hada har suka san juna, sai Fahat ya washe hakora yana dariya.

“An yi haka, tabbas, ka ce ka yi kudi shiyasa baka nemi ni ba, yanzu ai kai ne ranka ya dade ba ni ba”

Ya fada yana kallon dress din Faruk na kananan kaya da suka fito da shi. Faruk yayi murmushi.

“Ba haka bane, ina da niyar zuwa, kasan tafiyar da na yi ne ya saka ban samu na zo ba, lokacin da na dawo kuma na tarar mahaifiyata ba lafiya, sai hankali ya tafi can muna cikin haka sai ga aiki na fito mun Lagos daya daga cikin wadanda na yi applying”

Fahat ya mika masa hannu yana taya shi murna.

“Maa Shaa Allah, Allah ya tabbatar da alheri ya bada sa'a”

“Amin Amin na gode”

“Wannan yaron ka ne?”

“Eh Sultan she's my first born”

“Maa Shaa Allah, Allah ya raya. Ba dan kar na yi karabanni ba da nace a kafa kake ko da abun hawa?”

“Tukuna dai abun hawan muna da biki nan gaba kadan”

“Gaskiya ya kamata, ni ma ai sai a labani na samu wata, amman kamin nan mu je na sauke ka”

“Aa ka bar shi kawai,mun gode”

“Ka raina kenan yanzu ka fi karfina bari na ja baya”

Faruk yayi dariya ya kama hannunn Sultan yana fadin.

“Ina gudun wahalar da kai ne kawai”

A tare suka nufi motar Fahat din da hannunsa ke rike da Arabian Perfumes masu tsada da kamshi. Fahat ya budewa Sultan gidan baya ya shiga Faruk ya shiga Front seat, Fahat kuma ya shiga mazaunin direba ya ja motar suka hau titi. Suna tafe suna dan taba hira can Fahat ya tambayi inda zai sauke shi, Faruk ya fada masa unguwarsu Rafi'ah, wani irin faduwar gaba Fahat ya ji wanda ya haddasa masa ciwon kai. Faruk yana ta kwatancin inda za su bi har suka gisa bakin gate din gidansu Baturiya, ba karamin mamaki ne ya kama Fahat ba, ta madubin motar ya rika satar kallon Sultan zuciyarsa na raya masa shi ne yaron Baturiya, domin sai a yanzu yake ganin kamaninta kadan a fuskar Sultan.

“Ka san wata a nan gidan ne?”

Fahat ya tambaya yana kallon gate din gidan.

“Eh Ex-wife dita na zo gani zan bata hakkinta kuma Sultan yana son ganinta”

“So ka rabu da matarka kenan?”

“Yeah mun rabu”

“That's mean Baturiya matarka ce?”

Faruk ya masa kallon mamaki.

“Ka santa ne?”

“No...”

Sai kuma ya rasa mai zai ce. Faruk ya ce.

“Karka maida ni yaro mana, ya akai kasan sunanta?”

“Abun da nake son sani, kun rabu gaba daya”

“Mun rabu ba gaba daya ba, domin akwai cikina a jikinta shiyasa ma nake son bata hakkinta a yanzu”

“So duk abun da aka fada min gaskiya ne about her, sai dai ni na so ta ba da sanin ta taba aure ba ma, domin bata taba fada min ba, sai bincike ne ya gano min haka”

Faruk ya runtse ido ta bude yana mamakin furucin Fahat.

“Ka taba son Rafi'a ne?”

“Yeah, amman yarinyar nan ta yaudare ni, shiyasa bana shakkar fadawa kowa I'm sorry to say baka yi dacen mata ba, duk da yake kun rabu amman akwai da a tsakaninku”

Ya mikawa Faruk wayarsa da number Baturiya da ya goge ya saka a blacklist yana nuna masa sakwannin da take tura masa. Faruk yayi murmushin takaici.

“If na fada maka abun da ya raba ni da ita you will be shock”

Fahat yayi murmushi.

“Lemme text her yanzu nan zata fito”

Kusan a tare suka bude motar suka fito, Fahat ya zagayo bangaren da Faruk yake tsaye da Sultan yana aika mata da sako cewar yana kofar gida, domin baya jin zai iya kiranta ma. Har yanzu akwai sauran sonta a zuciyarsa domin cire so lokaci daya ba abu ne da zai iya yi a take ba, sai dai yafi tsanarta fiye da son ta a yanzu saboda sanin true color ta, musamman alakar dake tsakaninta da mahaifinsa, ko da wani dabam take wannan alakar ba ya ji zan iya zaman aure da ita bayan ta yi masa karya, balle kuma a yanzu da yake jin aure ya haramta a tsakaninsu.

BATURIYA POV.

Kamar wanda akai wa bushara da daren mutuwarta, haka Baturiya ta rika kuka tun daga kofar gidan har cikin gidan, tsabar bakincikin da ya rufe mata zuciya ya rufe ya tafi har cikin ido ya rufe su, ga hawaye da ya hana ta ganin komai sai lallaben kofa take har ta shiga cikin gidan. Umma na ganinta ta yo kanta da sauri ta rikata.

“Subhanallahi lafiya? Miya same ki?”

“Umma na rasa Fahat rashi na har abada, na rasa shi Umma, Fahat ba zai taba aurena ba”

Ta fada cikin wani irin kuka da bata san ranar da zai tsaya mata ba, kukan da take ne ya bawa Umma tausayi ba wai domin Fahat ya fasa aurenta ba, domin a tunanin Umma Baturiya zata samu wanda ya fisa ma nesa ba kusa ba, amman saboda ta shaku da soyayyarsa ya saka bata ganin komai idon ya rufe har bata iya komai sai kuka kamar wanda akai wa mutu.
Tun daga ranar Baturiya bata sake wani abu wai shi walwala, abinci ma sai Umma ta matsa mata take ci, da zarar ta tuna da Fahat sai ta ji kamar ta cire ranta daga jikinta ta huta.
Cikin kwana biyu ta koma kamar ba ita ba, daman can jiki babu wani dogon afki balle kuma yanzu da damuwa ke son cinyeta. Ba tana bakincikin rabuwa da Fahat saboda fargaban samun wani wanda ya fi shi ba, no soyayyarsa da tai tahiri a zuciyarta ya saka take jin abu ne mai wahala ta sake samun wanda zata so kamar ranta irin Fahat. Gashi a yanzu da ya nisance ta sai sonsa ya kara shiga ranta ya hana ta sukuni, motsi daya da biyu sai ta tuna yadda suke son junansu.

Har yanzu bata fasa tura masa sakon ban hakuri ba, ta kara hakura ta goge number sa balle ta cire shi a ranta, idan ta kira number shi bata shiga saboda yayi blocking dinta, sakonta da kiransa duka ba za su yi appearing a wayarsa sai a block list dinsa. Karya tai ma Umma cewar wai ya bi zabin mahaifiyarsa ya hakura da ita, ba ta yarda ta fadawa Umma komai ba, Umma kuma bata fasa nuna mata gari da yawa maye ba zai ci kansa ba, maza suna nan da yawa, kamar yadda ta same shi haka zata samu wani. Sai dai duk kalaman da Umma take mata na son kwantar mata da hankali, be yi tasiri a zuciyarta ba.

As always da ta sabawa kanta da zaman kadaici a daki, tana zaune dakin ta yi ruf da ciki tana ta karatun jaki, sako ya shigo wayarta, cikin rashin kuzari ta dauki wayar tana duba sunan wadan ya sakon mata da sakon sai ta ji kamar an mata allura, da sauri ta zabura ta mike tsaye ta, a gaggauce ta cire daurin kirjin dake jikinta ta saka zane da riga na atamfa ta rufe jikinta da Hijab ta fito da sauri zuciyarta na rawa ta saka talkamin Umma ta fice daga falon zuwa gate ko wayar bata fito da ita ba, tsabar zumudi da rawar kafa Fahat ya turo mata sako cewar yana waje yana jiranta akwai maganar da zai yi da ita.

*_(Kun ga Labarin Aminatu da Faruk? Wallahi True life ne, amman na canja abubuwa da dama akai, but cikin kankanen lokaci Allah ya canja masa rayuwa)_*

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□ Tsaye tai bakin gate din with shock tana kallon Fahat bata yarda da gaske yake ba har sai da ta ganshi. Sai dai ga mamakin sai tana ganin wani mai kama da Faruk a kusa da shi rike da hannun Sultan, ko kadan gabanta be fadi ba domin bata yarda Faruk ne a kusa da shi din ba, ta fi kyautata zaton aljanine yai mata siffarsa, ko kuma idonta ne suke mata gizo saboda halin data shiga na kaunar Fahat. Tafiya ta fara yi a hankali har ta isa kusa da inda suke tsaye but still tana ganin Faruk. Lumshe ido tai ta bude a zatonta zata daina ganinsa ne sai ta ga yana nan a lokacin ne hankalinta ya fara tashi ta maida idonta akansa tana kallonsa kamin ta mika hannu da zimmar taba fuskarsa domin tabbatarwa idan shi din ne ko gizo idanuwanta suke ma. Jin tai an buge mata hannu da mugun karfi, muryar Fahat ta daki dodon kunnenta.

“Da gaske shi ne mijin na ki kenan?”

Ta kalli Fahat sannan ta sake kallon Faruk da sauri, sai kuma ya sauke idonta gurin Sultan dake rike da hannun babansa.

“Far... ”

Ta kasa furtawa, sai ta sake maida dubunta gurin Fahat dake mata kallon tsana da mamaki. Ta nuna masa Faruk, so take ta tambaye shi a ina ya san Faruk a ina suka hadu ya akai sukai hadu amman ta kasa furta komai sabida tsabar mamaki da kidemiwa. Sai hade yawu take da karfi tana tara wasu tana hadewa.

“Faruk...”

Ta furta daker hawaye na saikowa idanuwanta. Sai yai murmushin takaici.

“Rafi'a, ashe baki mantawa ni ba, na dauka sunana ma ba zaki iya furtawa ba”

Faruk ya fada sai Fahat ya dora da na shi.

“Baki ji kunyar kanki ba? Kin boye cewar kin taba aure ashe har da ďa kina da! Kuma a haka kike biyewa rudin zuciya kina zina”

Faruk ya kalleshi da sauri cike da mamakin yadda akai ya sani, Fahat ya daga masa kai.

“Yes na sani, saboda ta yi mu'amala da wani na kusa da ni, a haka kuma take shirin aurena”

Faruk ya bude motar Fahat ya kalli Sultan dake tsaye yana kallon Baturiya kamar ya ga bakonsa.

“Sultan shiga mota”

“Dady ba Momy ce wannan ba”

Baturiya ya lumshe ido hawaye masu zafi na sauko mata. Har cikin zuciyarta ta ji kalmar da ya ambace da ita da Momy. Faruk kuma ya hade abu da karfi ya daka masa tsawa.

“Shiga na ce”

A take jikinsa ya fara rawa, sai ya shiga motar da sauri yana fashewa da kuka. Faruk ya kalleta hawayen bakinciki na taruwa a idonsa.

“Ban tana jin nadamar wani a rayuwata, kamar yadda nake jin nadanar aurenki ba, taya zan kalli mace kamar ke na kirata uwar da na? How? Wani irin kwadayi ne a zuciyarki Rafi'ah? Taya zaki bata rayuwar yaron da be san komai ba? Ta hanyar aikata mummunan aiki irin wannan? Saboda wannan abun na rabu dake, kuma na ki na fadawa kowa dalilina na rabuwa da ke, kin san saboda me?”

Ta bude ido sai dai hawayen dake sauko mata sun hanata ganin fuskarsa da kyau.

“Saboda d'ana, bana son a kalleshi ace uwarsa tana aikata wani abun da idan ya girma ya ji zai ji bakinciki, yace mahaifinsa be zaba masa mata ta gari ba. A rayuwata ban taba jin na tsani kowa ba, amman ke na tsane ki Rafi'a na tsaneki fiye da yadda na tsani mutuwata”

Ta busar da iskar bakinsa a hankali, sannan ya cigaba.

“Daman na zo nan ne saboda na tambayi adadin abun da kika kashe na barinki da dawainiyar cikina da na yi, but it seems like kin zubar da cikin ma, har kina shirin auren Fahat.. Kuma... ”

Faruk ba karasa ba Fahat ya tari numfashinsa yana daga hannanyensa sama.

“No no no... A a a, wannan da ne, yanzu kam Allah ya tsare ni da bakar macijiya”

Ta maida dubanta gurin Fahat tana jin kamar ta hade zuciya ta mutu, tana jin kamar kasa ta bude ta shiga, ina ma ace ba a halicce ta kamin zuwan wannan ranar.

“Wata kila nan gaba idan Sultan ya mallaki hankalin kansa zai nemi sanin mahaifiyarsa, amman for now ina son ki nisanta kanki da shi, kamar yadda kika nuna masa baki kaunarsa saboda talaucin ubansa, ina daf da sama masa wata uwar mai tarbiya, kuma zan nisanta ki da shi zan koma da shi a inda na samu aiki Lagos na mu zauna can, cikina kuma da kika zubar na barki da Allah”

Yana kaiwa nan ya juya ya bude motar ya fito da Sultan dake kuka ya dauki ledarsa, ya rika hannun Sultan din suka nufi titi. Fahat ya bishi da kallo har sai da yai nisa sannan ya kalli Baturiya.

“Yanzu kin yi farinciki? Kin guji mijinki da danki saboda abun da ba su suka bawa kansu ba? Kin kyamaci mijinki saboda jarabawa ta talauci? Kenan ki nima saboda dukiyata kike so na”

Ya girgiza mata kai yana murmushi.

“Kin ga wancan mutumen da kike gudu? Ya samu aiki, kuma kamin samun aiki ya tafi nema wata kasar, kuma ina kyautata zaton ya samu abun da zai canja masa rayuwarsa, wace riba kika ci kenan? Kin samu zunubin zina, kuma baki yi hakuri cin jarabawar da Allah yai miki ba na aura miki talaka balle ki kai ga cin ribar hakurin, kuma kudin da zaki samu ba zai amfana miki komai ba saboda ba ta hanyar halal kika samu ba, ba zai taba miki albarka ba”

Ya juya a hankali ya zagaya gurin driver seat ya bude ya shiga ya zauna sannan ya sauke gilashin motar ya kalleta.

“Zaki iya komawa, daman na kiraki ne saboda mijinki yana son magana da ke, i mean tsohon mijinki...”

Ya daga glass din sannan yai reverse ya fisgi motar yana watsa mata kura ya bar line da gudu. A maimakon ta koma gida sai ta cira kafarta da tai mata mugun nauyi ta fara takawa a hankali ta nufi hanyar fita daga layin, wani abu take ji ya tsaya mata a zuciyarta kamar mashi, ta tare mata numfashi dake fita ta hancinta sai ta baki take samun damar numfasawa, wani abu take ji kamar kuda yana mata yawo a cikin kai, karar ababen hawa tana shiga da fita a cikin kunnuwanta

da wani kalar sauti da bata taba saninsa ba. Tafiya kawai take badan ta san inda zata je ba. Sai da tai nisa sosai da unguwar sannan ta samu simintin wani gida ta zauna tana ta murda yatsun hannunta hawaye sai zuba suke mata. Ta zauna a gurin har na tsawon awa daya bata komai sai hawaye, maganar da Fahat da Faruk sukai mata yai ta maimaita kansa a cikin kanta. Duk yadda ta so taga komai daya faru ya zama mafarki ta masa.

“Ni wai... Ni... Ni... ”

Ta fada tana nuna kanta, sai kuma ta mike tsaye ta juya hanyar data fito ta fashe da kuka.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un garin na shigo tara ni Baturiya na lakace”

Ta dora hannu saman kai kamar ta manta a hanya take. Tana tafe tana kuka kamar karamar yarinyar mutane sai kallonta suke.

“Ke lafiya”

Wani mutumen ya tambaya, ko kadansa ba tai ba, ta cigaba da tafiyarta tana fadin ta shiga tara. Haka ta shiga gida da hannu saman kai tana ihu da kokuwar ta shiga uku, a tsakar gidan ta zube ta fashe da sabon kuka.

“Umma na shiga uku na lalace, Umma rayuwata ta kare, Umma na shiga tara na lalace, shikenan na gama rayuwa Umma”

Umma ta fito daga bandakin da sauri ta nufo tsakar gida ta dafa Baturiya cikin tashin hankali.

“Lafiya.... Miya same ki?”

“Komai ma ya same ni Umma ya same ni, Umma rayuwata ta lalace, Umma shedan da zuciya sun kai ni ga halaka...”

“Miya faru?”

“Umma Faruk....Fahat.... ”

Ta kasa furta komai, sai ta kuka take, Umma ta rikata ta mikar da ita tsaye suka nufi falon. Saman kujera ta zaunar da ita ta zauna kusa da ita ta kwanto da ita jikinta.

“Rafi'a kina son wahalar da kanki sa saboda maza, haba dan Allah, ji yadda kike kokarin fita hayyacinki saboda namiji”

“Umma ba zaki gane ba, na sake reshe na rika ganye, Umma duniya ta yi min juyin masa, Umma na rasa komai yanzu, asirina ya to nu, Ramlee ta kai ni ga halaka, zuciya ta kai ni ga nadama da bakinciki....Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un Umma...Umma mutuwa zan yi”

Wani irin kuka take na fitar hankali, jikin Umma yayi sanyi sosai jin ta ambaci Ramlee hakan na nuna akwai wani abu a kasa, domin tun tana budurwa aka rabata da abota da Ramlee.

FAHAT POV.

Har ya isa gida hamdala yake yi ma Allah, da be saka ya auri Baturiya ba, da ya aureta da ya jawa kansa bala'in da be san karshensa ba. Lokuta da dama mutum ka so abu ya zama ba alheri ne a gurinsa ba, ko kuma ya ki abu kuma ya zama alheri a gurinsa. Kamar yadda be zama lallai idan ya ki ya zama alheri ko kuma idan ya so ya zama sheri.

This is the first time da yake jin farincikin rashin auren Baturiya, domin a yanzu nw true color ta ya kara fitowa fili. A harabar gidan ya faka ya bude ya fito, sai kuma ya koma ya dauko ledar turaren da ya siyo sannan ya rufe motar ya nufi entrance din cike da kuzari, tura kofar yai ya shiga, kamshin turaren wuta da sanyi ac suka masa lale marhabun, maida kofar falon yai ya rufe ya nufi dakin mahaifiyarsa, zaune na same ta saman carpet hannunta rike da carji tana sanye da Hijab, da yau ta yi latti sallah la'asar. Kusa da ita ya karasa ya zauna yana kallonta cike da kaunarta

“Mommy sallah kika yi?”

“Eh, yau na yi latti ne, ka siyo surarukan”

Ya matsar da ledar kusa da ita.

“Ga kamshi ma kina ji”

Ta yi murmushi tana jin dadi.

“Yau ya kamata ka tafi ko sai gobe”

“Duk ranar da kika ce Mommy, ni yanzu bana ja da ke, kawai ina fatar wannan zabin da zaki min ya zama alheri”

“Zai zama Inshallah, yarinya ce mai kyau ga natsuwa, sai dai ba wata babba ba ce domin yarinya ce bana zata gama secondary school”

“Indai kin yarda da tarbiyarta bana da matsala ni”

“Gaskiya ban tana jin iyayenta ko su yayanta da wata matsala ba, kuma an manyan mutane ne”

“Ba matsala Mommy, duk yadda kika ce haka za'ayi”

Ta yi murmushin jindadi.

“Allah yai maka albarka Fahat”

“Ameen”

Ya fada yana kwantawa a carpet din ya dora kansa saman cinyarta.

FARUK POV.

Yana janye da hannun Sultan dake kuka yana tafiya, zuciyarsa na tafarfasa kamar zata kona kirjinsa. Ta dayan bangaren kuma yana jin tausayin dansa da be dacen uwa da gari ba. Tafiya yake yana jin kamar ace zai iya dawo da baya ta cire Baturiya daga rayuwarsa. Wata kyakkyawar mota ce ta faka gabansa kadan, matukiyar motar ta fito sanye da abaya ta karaso inda suke da saurinta.

“Miya samu Sultan?”

Sai a lokacin da tai maganar sannan Faruk ya kalleta, ya gane fuskar da ya sani ce.

“Ba komai”

“Ba komai haka kawai zai yi kuka”

Faruk yayi gaba kamar ba zai amsa mata ba, sai ta saka hannu ta rika hannun Sultan, hakan ya saka Faruk juyowa ya kalleta ganin yana jan hannun Sultan tana jansa.

“Sake shi mana”

“Ba zan sake ba, yaro yana kuka kana cilasta masa tafiya haba Faruk”

“Gida zamu je, sake shi na ce”

Bata ce masa komai ba ta saka hannu ta dauki sultan din wanda hakan ya cilasta masa sakin hannun dansa, ya bita da kallo, ta rumgume Sultan tana rarrashinsa, can kuma ta dauke shi ta nufi motarta da shi ta saka shi front seat ta zagaya driver seat ta shiga ta tashi motar tai gaba ta bar Faruk tsaye yana kallon ikon Allah. Da farko abun haushi yake bashi but this time around abun da tai ya saka shi dariya.

“Yarinyar zata kashe ni”

Ta fada with smile, sannan ya karasa gurin titin ya tari abun hawa ya hau. Mama na ganinsa da ledar siyayya ta san ko dai be je ba, ko kuma yaje ba tararda ita ba, ko kuma ya kai ta ki karba.

“Siyayyar da kai mata ne?”

Mama dake zaune Rukaiya na matsa mata kafafuwanta ta tambaya tana kallon ledar da ya aje kusa da shi. Ajiyar zuciya ya sauke yana girgiza kai irin na takaici da bakinciki sannan ya labartawa Mama abun da ya faru, ba karamin mamaki tai ba jin cewar Baturiya tana shirin yin aure, sai dai ko kadan batai mamakin ace Baturiya ta zubar da cikin ba daman can ta ayyana hakan a ranta.

“Amman daman ko da ta fita gidanka tana soyayya da shi ko kuma yanzu daga baya ta same shi?”

“Wata kila tun tana gidan ne, wata kila kuma bayan ta fita ne, amman shi ba san ta taba aure ba ma”

“Allah ya tsare mu da aikin dana sani, kuma ya ba mu ikon cin jarabawa mai kyau ko marar kyau”

Rukaiya da Faruk suka amsa da amin, sannan Rukayyah ta dora da tambayar Sultan.

“To can ka bar mata Sultan din?”

Faruk ya ce.

“Haba dai ya za'ayi na bar mata shi? Matar data gagara takowa ta ga danta ma, kike tsammani ni idan na kai mata shi zan baro shi can? Boye ma fa take bata son asan tana da da, kuma gidan da bana tarbiya ba, bari dan ka ya zauna a can ai sai dole”

Mama ta ce.

“To ya za'ayi tun da an hada jini, sai hakuri da addu'a kawai, ina ka bar shi?”

“Yana gurin yarinyar nan Ramla”

Mama da Rukaiya suka hada baki gurin cewa.

“Ramla kuma? A ina kuka hadu”

“A hanya kuma ta nuna min fin karfi ta tafi da Sultan”

Mama ta yi murmushi.

“Allah ya hada jininta da kai, kai kuma ka gagara gane manufarta”

“Mama kenan, kai na nunawa mace kauna ya aka kare balle ita ta nuna maka”

“To ai ta nan zaka gane banbancin, idan mace tana sonka to kwanta ka huta kawai, balle wannan da take yar gidan masu hannu da shunu kaga babu abun da zai burgeta, sai da ma ta taimaka maka wani bangaren, kuma ka san dai ba dan ta rasa miji ba, yadda take da kyau nan Maa-Shaa-Allah ga kuma ubanta da kudi ai dole za a so ta kam”

Rukayyah ta kalli Mama dake maganar ta ce.

“Kuma ni dai wallahi tana burge ni, bata da girman kai gata kyakkyawa, ranar da muna hira da ita cewa min tai wai ita duk a cikin samarin da suke zuwa gurinta babu wanda ya kwanta mata, tace wasu yayan manya mutane ne, wasu kuma za su so ta ne saboda kudin mahaifinta ko kyauta, ita tafi son wanda zai so ta tsakani da Allah”

Faruk ya mike tsaye yana fadin.

“Ba daga nan take ba, ba a fuska ko kalamai ake gane mutumen kwarai ba, sai da a kwakwatanta, kuma a kyautata zato, amman mutane da yawa fuskarsu bata nuna abun da ke zuciyarsu har sai an zauna da su”

“Amman dai wannan muna kyautata mata zato yaya, da zaka bada kai da buri ya hau”

Mama ta kara da cewa.

“Ni da zaka bi shawarata da ka auri yarinyar nan, ta kwanta min a rai, kuma kaga faduwa ta zo daidai da zama, tun da ga aiki ka samu sai aure ka tafi da matarka can”

Wannan karon dariya yai yana jin yadda Mama da Rukaiya suke lissafin duna.

“Mama kenan, yarinyar nan fa ba cewa tai tana so na ko ina sonta ba, amman har wani lissafin aure kuke”

Suma dariyar sukai. Mama tace

“Da ka bata dama ai sai komai ya kama, ni da zaka dauki siyayyar nan ka kai mata ma daga can ka karbo Sultan din da ka burge ni”

Yayi murmushi.

“Wannan dai ya zama na ku, ita kuma zan siya mata wani abun idan zan karbo shi”

“Yauwa Allah yai maka albarka”

Ya amsa da Ameen sannan ya fice. Sai bayan sallah Magariba, ya koma Super market din da yai siyayya a dazun ya sake siyen turarukan masu kyau da dadin kamshi, ya siye chocolate masu tsada ya hade a leda daya. Bayan ya biya ya fito ya nufi gidansu, kamar yadda akai masa wacan karon da ya zo wannan ma sai da suka so hana shi shiga, sai ya fada musu Ramla yake son gani. Dayan ya kirata a waya ya fada mata sai da ta bada izini sannan wani yai masa iso har cikin falon gidan, a lokacin ne ya gane wacan karon karramashi tai da ta kai shi a wani falon na dabam da ba wannan ba, domin wacan ya fi kyau da tsaruwa nesa ba kusa ba.
Zaunawa yai ya ciro wayarsa yana ragewa kansa lokaci kamin ta fito.

“Allah yasa dai ba Mahaifina ka zo nema ba, domin baya nan”

Juyowa yai a hankali ya kalli inda Ramla take tsaye tana masa maganar, sai yai murmushi.

“Wannan zuwan ba na Abbah ba ne”

“Okay Sultan ka zo dauka kenan, baya ka gama saka shi kuka?”

Ya sake yin murmushi, sai ta karaso cikin falon ta zauna nesa da shi.

“Ni ai na dauka baka son shi har ina shirin bude masa sabon file a familynmu, na saka a gyara masa daki a kusa da nawa”

“Ki ce gata kika shirya yi masa kenan”

“Sosai ma, yanzu dai bari na kawo maka ruwa ka sha sai na kawo maka Sultan din”

Ta mike tsaye sai yai hanzarin dakatarta ita.

“No ni dai ban ce ina jin kishin ruwa ba, dazun ma da kika ga muna tafiya a rana ai danki kawai kika dauke kika bar ni tsaye a rana”

“Kai din ne rigimame ba lallai idan na ce maka ka shiga motar na taimaka maka ba ka shiga”

Ta fada tana murmushi.

“Ko kuma ni na taimaka miki na shiga motar ki samu albarka ba”

“A yanzu an fada maka ban samu ba, Sultan fa ya shiga”

“Shi ai ba lada ba la'ada, amman da ni kika dauka da lada zaki samu ninki ninki”

Ta kara fadada murmushinta tana mamakin yadda Faruk ya sake yana jera mata kalamai kamar ba shi ba.

“Ga wannan ban san ra'ayinki ba, sai na zabo miki ra'ayina, zan yi farinciki idan baki raina ba”

Ya mika mata ledar sai da tai kamar kar ta karba sai kuma ta saka hannu biyu ta karba.

“Na gode sosai, Allah ya saka da alheri”

“Ameen, za'a min izinin tafiya da danki?”

“Eh amman na kwana biyu kawai”

Tana fadar hakan ta juya ta fice daga falon.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don

neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Washe garin ranar da Hajiya Saratu taje gurin bokan ta dawo tana bawa Momy bayanin yadda sukai da shi. A lokacin Leila na zaune dakin tana cin yayan itatuwa, sai dai hankalinta gaba daya yana gurin maganar da Momy take da Hajiya Saratu.

“Ya ce komai a daidai yai shi, kuma sunan Aminatun ya saka, na tsakanin Talba da Leila kuma ya bada wani amman yace duk da haka sai ta zo”

Ta bude jakarta ta dauko kulli magani a cikin wani kyale ta mikawa Momy, kana ya dauko wani rubutu a gora.

“Ya ce ranar da zata ci shi kar ta ci gishiri, wunin ranar, wannan kuma sha zata yi, kuma ta tambaya wai layar da aka bada an saka a karkashin gadon na ce masa an saka”

“Allah yasa kin tambaye sa dalilin daya saka Leila take jin warin jaba”

Momy ta fada.

“Tabbas kuwa na fada masa, sai yace wai zata daina, shi ma be san abun da ya saka hakan yake faruwa ba, amman dai yace zata daina jin komai, kuma na Aminatu ya ce zai canja wani kalar wanda ba sai ta ci ba”

“Yauwa haka nake so, b aki masa maganar Madina ba?”

Leila ta dago ta kalli Momy, wacce tai tambayar.

“Haba dai ke ma dai ai kin san ba zan mata ba, na masa magana na fada masa sai yace zai yi aikin a samu sabon zane a kai masa, zai yi aiki a kai sai a bata zanen ta daura, na ki kuma ya ce na dawo rana wata yau na karba miki na ki”

Momy ta yi murmushi.

“Nawa yace zai yi aiki?”

“Na Madina 30k yace a bashi, na ki kuma 15k sai na Leila ne be fada ba, ina jin nata sai idan ta je din kamar yadda ya bukata”

Da mamaki Momy take kallon Hajiya Saratu.

“Da arha haka? Allah yasa dai aikin zai yi”

“Ai da ace be iya aiki ba da ba zan batawa kaina lokaci ba, kin san mutanen kauye ba su san darajar naira ba da dan birni ne da kudi zai zurara miki da yawa, shiyasa ai ban taso ba sai da na bashi kudi”

“Duk da haka dai zan bada 100k ki kai masa, wata kila zai fi maida hankali yai aikin”

“Momy har na Madina za'ayi?”

Leila ta tambaya, sai Momy ta kalleta da duba irin wanda yafi kama da harara.

“To ko a fasa ne? Sai a kai ki gidan yari kin ga rayuwarki zata kare a can”

Shiru Leila rai kamar bata gurin, bata sake cewa komai ba har Momy da Hajiya Saratu suka gama maganar da za su yi. Mikewa tai tsaye ta dauki wayarta dake aje ta fice daga dakin, shiga tai dakinta ta karasa gurin kofar dake sadata da backyard ta bude ta taka a hankali tana kallon harabar, wani iska mai dadi na bugunta. Rumgume hannayenta tai ta kara matsawa zuciyarta cike da tunani kala kala, ta sani abun da Momy ke kokarin aikatawa ba abu ne mai kyau ba, amman babu yadda zata yi ta hana hakan faruwa domin ba zata tonawa kanta asiri ba. Hannayenta dale rungume ta saki ta duba wayarta dake ringing. Ganin Number Ali ya saka ta saurin picking.

“Hello”

Ta fada da muryar dake nuna akwai damuwa ko akasin haka a tare da ita.

“Leila kina gida?”

“Eh ina gida”

“Na shigo, ina compound ina son magana dake”

Haka nan kawai sai ta ji gabanta ya fadi for no reason.

“Okay”

Ta sauke wayar, sannan ta dawo cikin dakinta ta nufi gurin windows dinta ta daga curtains dinta sai ta hango shi tsaye jikin motarsa yana kallon kofar falon. Ba al'adarta bace saka mayafi idan zata fita, hakan ya saka bata saka komai ba ta fito dakin holding her phone kanta ko dankwali babu, sai dai tana sanye da gown doguwa har kasa, tana saukowa downstairs din karaurawar gida tai ta kara alamar akwai bako a bakin kofar, karasawa tai ta nufi bakin kofar ba tare da tunanin komai ba ta kai hannu ta bude. Sai tai arba da jikan Baaba tsaye sanye yana kallon kofar kamar yana jiran shigowarta.

“Hajiya..”

Ta amsa a tsorace gabanta na tsananta faduwa.

“Na'am”

“Ya gida ya kowa?”

“Lfy Kalau”

“Ko Hajiya tana ciki?”

“Eh”

Ta amsa tana hade yawu, sannan ta saki kofar wanda hakan ya bashi damar shigowa, sai ta juya da sauri ta haye sama, cikin tashin hankali ta tura kofar dakin Momy ta shiga.

“Momy ga jikan Baaba nan ya zo?”

Kusan a tare Hajiya Saratu da Momy suka kalleta.

“Miya zo yi to?”

“Ban sani ba”

Ta amsawa Hajiya Saratu jikinta sai rawa yake. Momy ta tashi tsaye

“Ki kwantar da hankali, abun da nake fada miki kenan, iyalanta kawai idan suka zo gidan nan damuwa suke kina shiga tashin hankali balle kuma a ce an kaiki kotu ya kike tsamanin komai zai kare kenan?”

Leila ta kasa cewa komai, Momy ta ratsa gefenta ta fito daga dakin ta sauko kasa fuska a hade tana kallonsa kamar wanda tai arba da bakin maciji. Shi kam yana ganinta abun ka da mutumen kauye dake da girmama mutanen da sanin darajarsu sai ya mika mata gaisuwa daga inda yake duke bakin kofar.

“Lafiya Kalau, ya mutanen can?”

“Kowa Lafiya Kalau yake Hajiya, ya hidima da jama'a?”

“Lfy kalau”

Amsa masa take kamar an mata dole.

“Daman na ce bari na zo na ji ko an samu wani labari akan Baaba ne?”

“Ba a samu komai ba, ina ganin maganar ai tana gurin police ko? Can ya kamata ka rika zuwa kana bincikawa, ba nan ba”

“Ai ina zuwa can kusan duk bayan kwana biyu idan na shigo garin nan sai na je na bincika ko an samu wani abu amman ba wani labari”

“Muma muma bincikawa kuma abun da suke fada muku shi ake fada mana, na san idan an ganta za su kiraka, ba sai ka wahalar da kanka kana zuwa nan ba”

Ya kalleta sai kuma yai saurin sauke ido kasa saboda matsayinsa da nata ba daya ba.

“Toh Hajiya Allah yasa mu ji alheri”

“Ameen, a gaishe da mutanen gida”

Bata jira abun da zai ce, ta tura kofar ta rife falon, sannan ta nufi upstairs, tana shiga dakinta ta haw Leila da fada ta inda take shiga bata nan take fita ba.

“Idan kin ga iyalan matarki sai ki rika wani dari dari, ke da kanki ma baki isa ki yi magana da shi ya wuce ba, sai ki wani dawo kamar mai jin tsoro ki kira ni”

Daga nan Hajiya Saratu ta dora da nata, sai dai hakan be saka Leila ta tanka ba, sai kawai ta juya ta fice daga dakin. Da fargaba da ita gurin kofar ta bude ta fita zuwa gurin motar Ali dake fake a kusa da ta Momy. Karasawa tai sai ta zame shi zaune cikin motar domin ya ya soma gajiya da jiranta ya shiga motar ya zauna. Front seat ta bude ta shiga ta zauna sannan ta rufe kofar ta kalleshi.

“Sorry na barka kana jira”

“Karki damu, you can take your time, idan akwai abun da kike yi zan iyar jiranki ki gama sai mu yi maganar”

Ta masa kallo mai cike da alamar tambayoyi.

“Magana zamu yi?”

“Yes, shiyawa ai na kira ki jiya na tambayaki zaki shigo kika ce min eh, amman ba ki shigo ba”

“Bana son zuwa ne sai dole, domin bana son ganin abun da zai bata min rai a yanzu”

Ya dan yi jimm sannan ya sake kallonta ya ce.

“Yeah na sani, amman duk da haka be kamata ace kin wuni kin kwana baki je kin duba shi ba”

“Zan je anjima”

Ta fada atakaice. Numfashi yaja ya aje sannan ya soma magana ba tare da ya kalleta ba.

“Na yi magana da Madina, kuma ta fada min komai”

Ta kalleshi a dazane kamar wanda tai arba da wani mugun abun cutarwa.

“Me ta fada maka?”

“Komai da komai Leila”

Ta fito mata free, wannan karon yana kallonta with serious face.

“Cikin har da kidnapping din data aikata, and now i understand why kika zo gurina kina kuka da fadar wasu kalamai”

Ta yi saurin kai hannu ta bude motar ta fita sai ya dakatarsa ita ta hanyar fada mata cewar.

“Guduwa, da boye boye ba mafita ba ne a gareki Leila”

A take ta fashe da kuka da bata san ta inda ya zo mata ba, sai tausayinta ya kara kama Ali.

“Ban aikata da niya ba”

“Shiyasa nake son mu yi ma tukar hanci tun yanzu, ina son na fuskanci Talba da maganar, amman hakan ba zai samu ba sai da hadin kanki”

“Idan maganar nan ta fita Ali rufe ni za'ayi, kashe ni za'ayi, ka taimaka min dan Allah ka rufa min asiri”

“No ba mafita ba ne, domin komai daren dadewa dole wannan maganar zata fita, kuma ina ji miki tsoron abun da zai biyo baya”

Ta dafe kanta da take jin kamar zai rabe mata biyu saboda tashin hankali.

“Madina ta same ka ta fada maka ne?”

“Aa ni na same ta na tambaye ta abun da ya shiga tsakaninku”

“Ali ka taimaka min dan Allah, kar Talba da Daddy su ji maganar nan, Talba zai tsane ni, Daddy ma ba zai saurara min ba...”

Kuka ya ci karfinta.

“Look Leila idan har kina son na taimaka miki to ki fara taimakonki, abun da duk mutum be aikata shi da ganganci ba, ba a yanke masa hukunci kwatankwatan wanda ya aikata hakan da gangan, idan har an yi bincike an tabbatar akan kuskure kika hukuncin da za'ayi miki diya ce kawai”

“Ali ba zaka gane halin da na jeda kaina ba, i regret everything wayyo Allah...na... ”

Ta kara fashewa da kuka.

“Miyasa Madina zata min haka? Miyasa mutanen dana yarda da su suke nisantata ne? Ali zan iya mutuwa i will lose everything...”

“No idan zaki kwantar da hankalinki ki yi tunanin abun da na fada miki, Madina ta tsorata da sakon da Momy ta aika mata, which means Momy zata ita aikata wani kuskuren a kokarinta na faranta miki, duk wata illa dake tattare da hakan ba zata gani ba, so da yawa abubuwan da kake ganinnsu a wahala masu sauki ne, I'm here to help, tsakani da Allah na damu sosai a lokacin da Madina ta fada min”

“Ba da gangan na aikata ba”

“Shiyasa zaki samu mafita ai”

Ta share hawayenta da sauri ta girgiza masa kai.

“No, ba zan bar duniya ta san da wannan ba, mutumcin gidamu da na mahaifina zai zuba, rayuwar da nake mafarki ba zan taba samunta ba”

“Miyasa zuciyarki ke raya miki zaki iya boyewa Allah? Baki yi tunanin zai iya jefaki a wani tashin hankali ba saboda wannan abun da kika aikata kuma, Leila ki daina tunanin irin wadannan abubuwan domin idan ba a yi hukunci a nan ba, za'ayi a gaban Allah”

Ta kalleshi hawaye na mata zuba kamar ba gobe tana girgiza masa kai.

“No i don't want to lose everything, tsoro nake ji, Talba ba zai aure ni ba, wata kila Daddy ba zai sake saurarena ba, shikena rayuwata zata juye, ban aikata da ganganci ba, ban yi da niyar kashe ta ba, kuskure ne Ali.. Kuskure...”

Ta bude motar da sauri ta fita tana kuka, ta gilashin motar yake kallon yadda ta nufi kofar falon. Har cikin kahon zuciyarsa yake jin tausayinta, ya san yadda ake ji idan ka aikata wani abu akan kuskure balle kuma kisa. Ya san duk yadda zai yi kokarin fahimtar da ita a yanzu ba fahimta zata yi ba. Bakinsa ya cikawa iska ya busar sannan yai baya ya juya motar ya fice daga gidan.
After ya koma gida yai ta kiranta taki dagawa, daga karshe ma sai ta kashe wayar gaba daya, washe gari ma haka yai ta kiranta bata dagawa.

*** *** **
Leila na kwance dakinta after sallah la'asar Momy ta turo kofar dakin ta shigo, sai ta tsaya daga bakin kofar tana kallonta.

“Zan koma asbitin ni, ko zaki je?”

“Aa”

Ta amsa daga kwance da take, sai Momy ta tura kofar dakin ta rufe sannan ta karasa kusa da ita saman gadon ta zauna tana kallonta.

“Leila me ke damunki? Na ga yanayinki kamar akwai damuwa! And yaushe rabonki da ki je duba Talba?”

Ta dago da idanuwanta da su kai yi zurfi ta kalli Momy, bata son ta fada Momy maganar Ali, kar shi ma tace za ayi masa wani abun.

“Bana son ganin yarinyar nan ne”

“Leila wani lokacin kina ba ni mamaki, kamar ba yar boko ba, yanzu Fisabilillahi Aminatun ce abar zaki yi ma zuciya da Talba har ki bar mata shi? Taya ke da kike birni yar kauye zata baki tsoro?”

“Ba wai na bar mata ba ne, Momy kin san yadda nake son Talba, bana son ganinsa da kowa, sai dai kuma ina jin kamar... ”

“Kamar me? Kar ma ki fara ke kadai kike da Talba, ki saka wannan a ranki, na san idan mahaifinki ya ji ba zai jidadi ba, shi kansa Talba ba zai jidadi”

“Zan je anjima”

“Good, sai kuma abu, za'ayi Madina ta saura zanen nan? Idan an kawo?”

“Ni ma ban sani ba Momy, amman da zaki yarda Momy da an canja a yi mata wanda ba zata iya fadar komai ba”

“Mun riga mun gama wannan maganar, zuwanki ne kawai zai zama aiki domin ina jin tsoron hanyoyin yanzu, gashi Saratu ta fada min daji ne gurin sosai”

Leila bata ce Uffan ba sai tunani take ta yi. Momy ta mata kallon rashin yarda.

“Akwai dai abun da yake damunki Leila, ki fada min idan akwai wata matsalar”

“Babu komai Momy”

“Okay, ina fatar hakan”

Ta mike tsaye ta fara tafiya.

“Mun yi magana da Hajiya Tsahara, next week zaki tafi Abuja a can za ayi mikin gyara jiki, ba son nake a canja time ba”

“Okay”

Ta amsa, sannan ta bi Momy da kallo har ta fice. Bata son zuwa asibitin ne saboda maganar da sukai da Ali, ta san yadda Ali da Talba suke basa boyewa juna abu, gani take idan ta je Talba zai mata maganar ne. Ta dayan bangaren kuma tana ganin kamar ya daga mata kafa ne saboda yana asibiti wata kila yana dawowa zai fadawa Daddy. Zabura tai saboda yadda Amal ta turo kofar ta shigo da saurinta, domin Momy na kasa tana jiran saukowarta su koma asbitin tare.

“Gashi wani yace a baki sako”

Leila ta gyara zamanta tana kallon Envelop din dake hannun Amal.

“Waye waya baki?”

Ta tambaya a tsoratace tana kallon Envelop din.

“Wani ne dazun da muka taso daga makaranta, sai ya tsayar da driver na yana cikin mota ya ba bashi yace ya bani wai na baki”

Cike da karfin hali ta mika hannu ta karba, sai Amal ta kalleta kamar ta tambaye ta miye a ciki, sai kuma ta juya ta fice ba tare da tace mata komai ba.
Amal na fita, Leila ta tashi ta rufe dakin ta dawo ta dauki envelop din ta bude, a tunaninta wani abu ne a ciki sai ta yar kasa kadan a ciki da kananan duwatsu.
Cige baki tai

“Wato Madina ba zaki daina ba ko?”

Ta furta sannan ta nufi bandakunta ta juye kasar ya dawo dakin ta kwanta.

AMINATU POV.

“Wani zai iya shigowa”

Ta fada tana kallon kofar cike da tsoro, sai yai murmushi ya cire hannunsa daga jikinta ya koma ya zauna yana kallonta.

“Idan likita ya sallame ni, tare zamu koma gida gurin Momy ko?”

Ta kanne kafada.

“Aa ni gurin Mama zan zauna”

Hannunsa ya mika mata, alamar ta zo, sai ga Ali ya turo kofar dakin ya shigo hannunsa rike da takardu. Aminatu ta sauke kanta kasa, dan murmushi yai yana kallon Talba.

“Jiki yayi kyau”

“Idan ina fada maka na ji sauki kai da Daddy sai ku ki yarda”

“Ba yarda ne bana mu yi ba, gata ne ake nuna maka da kulawa”

Yayi murmushi.

“I see”

Ali ya kalli Aminatu sannan ya sake kallon Talba.

“Ina son mu yi magana da kai”

Talba yai masa alama dake nuna yana saurarensa ba tare data furta ba. Sai ya sake juyawa ya kalli Aminatu.

“Or Maybe zai fi idan ka koma gida, but magana ce mai matukar muhimmanci”

Aminatu na jin haka sai ta matsa kusa da inda Talba yake zaune ta dauki dankalinta ta fice. Ali ya sauke ajiyar zuciya ya cika bakinsa da iska ya busar.

“Ban san yadda zaka dauki abun ba”

Talba ya kalleshi with confused.

“Miya faru?”

Sai kuma yai dan murmushi kadan ya ciro takardar ya mikawa Talba, yana kokarin canjawa topic din ganin kamar be dace yayi masa wannan magana a yanzu ba.

“Takardar sallamarka ce”

“Maganar da zamu yi ta shafi Aminatu ne?”

Talba ya tambaya, sai Ali yai murmushi.

“Ita kadai ce damuwarka? Aminatu ce kawai take da matsala?”

Talba ya masa wani kallo.

“Kafi kowa sanin abun da yake faruwa da ita, so ina fargabar wani abu ne”

“Maybe idan mun je gida zamu yi magana, kamin lokacin ta huta”

Ali na fadar hakan ya nufi kofar fita, sai Talba ya bishi da ido ganin yanayinsa ya canja. Aminatu na ganin fitowarsa ta juya ta koma cikin dakin idonta ya sauka akan takardar dake hannun Talba.

“Takardar me ce?”

“Sallama”

“Da gaske?”

Ya mika hannunsa ya rikonta, yana kallon wayar idonta.

“Na taba miki karya?”

Sai ra girgiza kai tana murmushi.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Momy na shigowa Aminatu ta sha jinin jikinta, ta koma kusa da Talba ta tsaya kanta a kasa. Kallonta Talba yai ya kalli Momy be ce komai ba sai dai ko kadan hakan be masa dadi ba, duk wani abun da zai saka Aminatu ta kasa sakewa bana sonshi.

“Ali yace an baka takardar sallama”

Momy ta fada, kamin ya amsa mata Amal ta shigo sanye da uniform dinta Mairo na bayanta.

“Eh, daman na fada masa ko be sallame ni ba zan tafi yau”

Momy ta yi murmushin karfin hali, domin ko kadan bata son bude hakoranta a gaban Aminatu.

“Daman kai ai ba son asibiti kake ba sai ta kama dole, Mairo zata kwashe kayan da suke da muhimmanci a nan, sauran da bama bukata sai a barwa Aminatu ta tafi da su gida”

Talba ya kalleta

“Momy ai tare zamu je...”

Kamin Momy tace komai, Aminatu ta tari numfashin Talba.

“Aa ina son na zauna gurin Yaya, ban taba kwana can ba”

Momy ta yi murmushin gefen fuska.

“Daman idan ba Hajiya Laraba ba ai sai dai idan a asibitin nan zaki kwana, domin kin nuna kiyayyarki ta kwana a gidanmu tun farko yanzu kuwa saboda rashin kunya ba zaki dauki kafa ki ce zaki bi mu ba”

Aminatu bata ce komai ba, ta nufi kofa sai Talba ya kira ta.

“Ina zaki?”

“Gida”

Ta fada ba tare da ta juyo ba, sai yai hanzarin dakatar da ita.

“Dawo, zamu je gida tare sai ta akai ki can, ko kuma na sauke ta yanzu”

Momy ta masa wani kallon mamaki.

“A baka key ka tuka mota ka kaita gida? Daga tasowarka daga aaibiti? Bayan kuma saboda yarinyar komai ya same ka? Ba zata bi mu ba, kuma ba zamu fara zuwa a sauke ta ba, sai dai ta hau abun hawa tafi a kafa ko kuma ta jira har sai matar ta zo”

Talba ta runtse ido ya bude alamar maganar Momy ba ta yi masa dadi ba.

“Momy, yarinyar nan fa Matata ce idan kika wulakantata kamar ni kika wulakanta, idan kika ci mutuncinta ba zan jidadi ba, rashin sakewar da kika mata ya saka bata son zuwa gidan nan, kuma kin san yadda basa jituwa da Leila, yanzu kuma taya kika ganin ni zan tafi na bar ta nan ko kuma na turata ta hau napep bana da tabbacin ta san gidan ma”

Momy ta nuna Aminatu.

“Wai jaririya kake daukar yarinyar nan ne? Okay sai ka haw Napep din kai da ita ka kaita gida idan ka sauketa sai mai Napep din ya wuce da kai gidan”

Ta fada a fusace sannan ta kalli Amal.

“Muje Amal, Mairo kwaso kaya ki saka min a booth”

Talba be ce uffan ba har ta fice, Mairo kuma ta shiga hada abubuwan da Momy ta fada mata, kuloli da jug kawai ta kwashe, ta bar bed sheet da pillow da wasu abubuwan da ta san Momy zata yi kyamar tabawa ko amfani da su. Tana ficewa Aminatu ta kalli Talba da sauri.

“Zan iya gane hanya fa, ko kuma na jirata ta zo, dan Allah ka tafi”

Mikewa yai tsaye ya karasa inda take tsaye ya riko hannunta yana duba yatsunta kamar mai son tantance abu.

“Indai Momy ba zata iya yi min lamanin na sauke ki gida ko ta sauke ki ba, ko kuma mu tafi gidan tare be kamata na tafi na barki ba”

Ya mika dayan hannunsa ya dago kanta daga kallon yatsun nata da yake murzawa ta kalleshi.

“Shalelena ina jinki a zuciya kamar sabon kwai, wanda idan ya fadi zai fashe, idan kuma kai masa rikon ganganci zai samu matsala, bana son ki sake facing wata damuwa ko bakinciki a rayuwarki”

Hawaye ya cika idonta, ba hawayen na bakinciki ko fadan da sukai da Momy ba, hawayen farinciki da sauraren kalamansa. Hannunsa ya saka ya share mata hawayen sannan yai amfani da babban yatsansa yana shafa laulasar fatar kumatunta.

“Zan iya daukar komai a rayuwar nan, ban da hawayenki bana iya jure bacin ranki, kin rasa abubuwa da yawa, baki cancanci komai ba sai farinciki da kulawa, ina sonki irin son da kalmomi sukai kadan su zayyana”

Ya rumgume ta a kirjinsa.

“Idan nace zan kyale Momy ta cigaba da musguna miki, kamar na bata goyon baya ne, nuna mata bana son abun da take yi zai sama miki salama a gurinta, saboda na san Momy tana son yayanta fiye da tunaninki ciki har da ni, to me zai saka ke ta tsane ki?”

Ka ji muryarsa kasan kalaman da Momy tai ma Aminatu dazun ba su masa dadi ba, ciki har da cewar da tai abun da basa so a bawa Aminatu, ya san Momy da kyamar abubuwa sai dai ba kasafai take alheri ba, yawancin duk abun da zaka ji tace a kyautar musamman idan an yi amfani da shi ko kuma tsohon yayi ne to bata son sa ne. Momy na daga cikin irin matan nan wadanda ko ba san son abu sun fi son su bar shi ya lalace.
Hawaye take a hankali kamin ta dago hannunta ta rumgume shi, har cikin ranta take jin kaunar mijinta, ta sani indai Talba yana raye a duniyar nan babu abun da zata nema ta rasa.

Unexpected Ali ya turo kofar dakin ya shigo, Talba ya juyo ya kalleshi sai dai be ce masa komai ba, kasancewar ya bashi baya ne baya iya ganin Aminatu sai dai hannunta data zagaye Talba da shi.

“Ranka ya dade idan ka shirya sai ka fito na sauke ka gida, Momy ta tafi”

Aminatun na jin muryar Ali tai hanzarin dauke hannayenta saboda kunya, kar ya ga ta rumgume Talba.

“Zamu fara kai Shalele gida”

Talba ya fada, ba tare da ya sake juyowa ba, Ali be ce komai ba ya juya ya fice daga dakin. Dagowa tai daga jikinta ta daga kai ta kalli fuskarsa.

“Zai yarda”

Ta fada da rada, sai ya kai bakinsa saitin kunnenta.

“Aa ba zai bari ba”

Ta yi murmushi ta boye fuskarta a kirjinsa, shi ma murmushin yai ya shafa bayanta. Sun dade haka sannan ya dago ta jikinsa.ya rika hannunta

“Zo mu je”

Cire hannunta tai daga nasa, be ce mata komai ba suka nufi kofar fita, da kansa ya fara bude mata ta fita sannan ya fito yaja kofar. A tare suka jera suna tafiya, gwanin sha'awa tana sanye da brown din Hijab dago har kasa, shi kuma yana sanye da kananan kaya komai black har shoe dinsa. Ko da suka isa parking lot din Ali har ya fito da motar harabar, Talba ya kai hannunsa ya bude mata back seat ta shiga ya rufe sannan ya bude front seat ya shiga. Ali ya ja motar suka fita daga asibitin ba tare da yace masa komai ba, Talba ma yayi kamar be san da shi a gefen ba, sai nunawa Aminatu gurare yake kamar wadanda suka fito yawon shakatawa, sam ba zaka ganshi kace shi ne marar lafiyar ba.

“Faka a nan zan siya mata wani abu”

Ali ba dan ransa ya so ba, ya faka gefen titi har lokacin be ce komai ba, and yana ta kokarin ganin be kalli Aminatu ba ko da a madubin dake gaban motar ne.

“Kina da kudi”

Talba ya tambaya yana kallon katuwar restaurant din dake gefensu.

“Aa”

Aminatu ta amsa daga back seat din da take zaune murya kasa kasa. Juyowa yai ya kalleta.

“Amman kina jin lokacin da na ce a tsaya kuma kika kyale”

Aminatu ta zaro ido.

“Ni ban ce a tsayar da shi ba, amman ai”

Ya kashe mata ido daya sannan ya sakar mata murmushi, ya juya ya kalli Ali.

“Bani cash ko Atm”

Sai a lokacin Ali ya kalleshi, ya dauke kai ya saka hannunsa aljihu ya ciro wallen dinsa ya cire atm din ya mikawa Talba. Bude motar Talba yai ya fita bayan ya karba, ya budewa Aminatu, domin be yarda ya barta daga ita sai Ali ba a motar,

haka nan kawai yake jin kamar wani abu Ali zai mata ko kuma ya saka ta gaba yai ta kallon. Fitowa tai sai ya rika hannunta, kallon mutane tai tana mai tsanannin jin kunya ta fara kokarin janye hannunta, a space din yatsunta ya saka nasa yatsun wanda hakan ya bashi damar rike ta da kyau.

“Baki son ina rika ki ne?”

Ya fada yana kallonta kamar wani maye.

“Akwai mutane fa”

Ya fada a shagwabe, sai yai murmushi ya dauke kansa suna kara dosar restaurant din.

“Ba haramun mu kai ba, wasu ba su ma aure ba suke haka, balle mu da muke da lasisi, kuma babu mutanen da ya kamata kiji ma kunya a nan ai, ba Momy Daddy ko Mama babu kowa even Yaya”

Ta yi dariya da yar siririyar muryarta.

“Kai ma Yayanka ne?”

“Yes, saboda ke”

Ya fada yana dayan hannunsa ya ja zirin hancinta, sannan suka shiga ciki, har ya gama zaba mata abubuwan da yake kyautata zaton zata iya ci be saki hannunta, ganin za su fito be siye mata kilishi ba ya saka ta nuna masa shi, sai ya kai bakinsa saitin kunnenta kamar zai shige cikin bakin.

“Me kike so?”

“Kilishi...”

Ta fada a shagwabe lips dinta na taba fatar kunnensa, sai a lokacin ya sake ta ya karasa gurin kilishin ya dauko mata leda 5 ya dawo ya zuba a inda ake lissafin. Bayan sun gama ya mika musu atm din suka cire kudinsu suka mayar masa da abunsa, sannan suka saka masa kayan cikin leda, hannunsa biyu ya saka ya dauko ledadin be yarda ta dauki ko daya ba, suka fito suna tafiya tare har suka iso gurin motar, Ali ya bude musu booth din zuciyarsa nata raya masa rashin adalci da Talba yake yi, because ya san idan Leila ce ba zai mata haka ba, Talba ya saka ledodin a booth sannan ya rufe ya zagayo, ya sake bude mata back seat ta shiga ta, ya rufe sannan ya bude front seat ya shiga, a kusa da sitiyarin motar ya dora ma Ali atm dinsa ba tare da yace masa komai a ba.

“Ban fa san inda zamu je ba”

“Zamu fara sauke Shalele gida”

Talba ya amsa masa, can kuma ya fada masa unguwar, daga haka be sake ce masa komai ba sai da suka isa liyin su Hajiya Labara sannan ya ce.

“Dama... Hagu... Ya isa”

Haka yai ta yi har suka isa bakin gate din gidan. Kusan a tare ita da shi suka bude motar suka fito, Ali ya sake bude musu booth din sai Talba ya isa gurin ya fiddo ledodin suka nufi gate, sai da ta kwankwasa mai gadin ya leko ya ga ita ce sannan ya bude ta shiga ciki, da sauri ya mika hannunsa ya karbi ledar dake sai Talba ya sakar masa, yai gaba ita da shi suna baya. Ko da suka isa kofar falon tuni mai gadin ya shiga cikin falon ya aje kayan a saman kujera sannan ya juyo ya fito. Aminatu ta nufi kitchen inda take jin kamshin soye soye, bata dade ba ta fito tare da Hajiya Laraba da fuskarta ke kumshe da murmushi.

“Maraba da mai Talba, kai da kanka?”

Talba yayi murmushi.

“Eh daman an sallame ni ne, sai tace ita a nan zata zauna shiyasa na kawo ta”

“Okay, To ya jikin naka?”

“Na warke Mama”

“Maa Shaa Allah, haka ake so Allah ya tsare gaba”

“Amin Amin, zan koma daman dai nace bari na fara sauketa sannan na wuce gida”

“Okay Allah ya kara lafiya, an gode sosai”

Be ce komai ba, sai ma kunya da ta rufeshi domin be riko mata komai ba, sai matarsa yai ma siyayya. Yana fita Hajiya Laraba tai mata alama data bishi da baki, sai Aminatu ta nufi kofar, ashe kuwa ta yi sara akan gaba, tana fita sai ta ganshi tsaye gefen kofar yana jiran fitowarsa, kallon harabar gidan yai ya ga babu mai ganinsu, mai gadin kuma hankalinsa yana ta wani gurin sai yai saurin kai bakinsa ya sumbance.

“Sai mun yi waya, i love you”

“Toh”

Ya sakar mata murmushi sannan ya nufi gate, ta bishi da kallo tana jin wata kalar kaunarsa na fisgarta. Sai da ya fice sannan ta juya ta koma ciki. Sai a lokacin ya rufe bayan motar sannan ya bude gidan gaba ya shiga ya zauna.

“Idan kana wani abun sai na rika ganinka kamar ba kai ba”

Ali ya fada sannan ya juya motar suka koma ta inda suka biyo.

“Ka san ba a sanin maci tuwo sai miya ta kare”

Talba ya fada yana kallonsa da murmushi a fuskarsa.

“Yeah sometimes, amman mafi akasari mutane irinka suna nuna soyayya ne a muhallinta, abun da kake is too much, Momy ta fada min abun da kai mata dazun saboda tace ba zata je da Aminatu ba, bayan kuma. Yarinyar nan ta nuna bata son zama a can, ka ga…”

“Karka nuna min abun da zan yi da wanda ba zan yi ba, akan Shalele na, you're my friend bana fatar jin wata kalma da zata sosa raina akan Mamata daga bakinka”

“Leila was right...”

“Leila is always right a gurinka ai, kana da wani abu mai muhimmanci sa zamu tattauna akai ba, ko kuma waka zaka kunna mana a motar mu saurara?”

Ali yayi murmushi ba tare da ya kalli Talba, sannan ya faka motar gefen titi karkashin wani itacen dogon yaro, ya busar da iskar bakinsa ba tare daya kalli Talba ya ce.

“Talba ina son na tambaye ka wani abu”

Talba ya kalleshi ba tare da yace uffan ba, Ali be damu ba ya aika masa tambayar domin ya san be zama lalle idan ya

“I want you to be honest, idan Leila ta samu kanta a wani hali, zaka iya zama da ita? Staying by her side ka kwantar mata da hankali kuma ka jata a jiki ka bata kariya?”

“Me zai haka? As long as tana da gaskiya”

Ali ya sauke ajiyar zuciya secretly.

“After Daddy da Momy i don't Leila tana da gata daya wuce ka, ko da ace gida daya kuka taso ta cancanci kariyarka da soyayya, balle kuma har ta hada jini da kai karewa da karau ma kai ne mijin da zata aura, idan kowa zai guje a duniyar nan ina tunanin kai ba zaka gujeta ba, ina tunanin you're the first person daya kamata ace ka kasance a tare da ita, a yanayin bakinciki ko farinciki”

“Wait...miya saka tsara wannan zancen?”

Talba ya tambaya with confused.

“Just to remind you how important you're to her, Leila tana son ka sosai Talba, wani irin so da take tsoron rasaka in every minute every second, and ina da yakinin da wani abu zai same ka a yanzu Leila zata zauna da kai no matter what, so a yau ina son ka kasance a tare da ita ka kwantar mata da hankali”

Jimmm Talba yai yana nazari, at first ya dauka ko Ali zai yi magana ne akan Aminatu, domin ko daina zuwa asibitin da tai dubashi ya san saboda Aminatu ne, sai da yadda ya zayyago masa wasu kalaman ya saka shi mamakin dalilinsa na yi masa wannan maganar.

“Leila ta aikata wani abu ne?”

Ya tambaya tana juyowa ya kalleshi. Ali yaja dogon numfashi ya sauke a hankali.

“Yes, amman akan kuskure ne wanda be wuce kowa ba, ko kuma na kira shi da kaddara”

“Please go straight to the point”

Talba ya fada cike da kaguwa.

“Abun da ka dade kana zargin Leila.da shi na kisan Baaba, ta aikata amman ba da gangan ta aikata ba, kuskure ne!”

Baki sake Talba ke kallon abokinsa.

“How do you know?”

Ali ya gyara zamansa, sannan ya kwashe labarin yadda komai ya faru ta fadawa Talba.

“I knew it”

Talba ya fada yana buga gaban motar.

“You shouldn't be angry”

“Why?”

Talba ya tambaya da karfi, sannan ya ware hannayensa.

“Ta san da wannan amman ta kyale iyalan matar nan suna da wahala? And before that Leila har marin tsohuwar nan ta taba yi, that's means tana da intention na aikata komai, saboda bata iya controlling kanta, ji yadda suka mai da komai ba komai ba suna rayuwa kamar babu abun da ya faru?”

“Wata kila tana jin tsoro ne!”

“Tsoron me? Ta kashe rai kuma ta boye, ta karyata kuma ka kira haka da tsoro”

“Amman a yanzu ta yi nadama, kuskure ne babu wanda ya wuce kuskure Talba, kai kanka ka auri Aminatu akan kuskure, duk kuwa da kasan da cewa a lokacin Daddy ya hanaka, kuma idan yaji ransa zai bace, haka Momy da Leila amman a haka ka aureta, so Leila ta aikata kwatankwacin abun da ka aikata, ya kamata kai mata uzuri, ta yi nadama sosai Talba”

Talba ya girgiza masa kai.

“I marry Aminatu because we're mean for each other. Kuma ta yi nadama ne ba dan Allah ba, there must be a reason wanda hakan ya saka kai ma kanka ka sani”

“Yeah saboda Madina ta fara yi mata barazana a rayuwarta tana kokarin ganin ta hana ta aurenka, saboda tana sonka and Madina ce ta saka a sace Aminatu... Saboda tana sonka”

Tsanananin mamaki ya saka Talba tsayawa kamar hoto yana kallon Ali ko yatsansa ya kasa motasawa, har na tsawon dakika ashirin sannan ya runtse ido ya matse su sosai.

“Wow.... ”

“Ko a kotu ba za a yankewa Leila hukuncin kisa ba, domin ba da ganganci ta aikata ba, kuma ta yi nadama”

Talba ta bude ido cikin wani irin bacin rai da be taba sanin yana da shi ba.

“Ta turo tsohuwar mutane daga sama zuwa kasa, ka kira hakan da kuskure? Ta kyale iyalan matar nan suna ta wahala da nemanta na dare ba rana ka kira hakan da kuskure? Ta dauki gawa su je su binne ta ta dawo ta musa cewar ta aikata hakan kuma ka kira haka da kuskure? Da ace Madina bata yi mata haka ba kana tunanin zata bayyana gaskiya ne? Wanda yai nadamar aikata abun yana fitowa ya nunawa duniya nadamarsa ne, kuma ya karbi hukuncin da za ayi masa ba ya boye gaskiya ba, after that Leila ta sake buga kan Aminatu still kana kiran hakan da kuskure? Ta yi nadama? And you expected me na goya mata baya mu rufe wannan sirrin?”

Ali ta ji kamar ya daki Talba, cikin fada ya ce.

“Baka taba iya daga mata kafa, baka tana shiga side dinta saboda magancs mata matsalarta, tabbatar da Aminatu ce zaka daga mata kafa ka nuna mata abun da ta aikata kuskure har ma ka sama mata mafita, but you can't do this for Leila even for once!”

“Yes i can't do that to her because you love her!”

Talba ya fada masa kai tsaye, yana kallonsa kamar yadda Ali ma yake kallonsa irin kai tsaye ni tsaye. Talba ya bude motar ya fita tare da buga ganbun motar da mugun karfi kamar zai ballashi.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Ali ya bude motar ya fita da sauri ya sha gaban Talba. Sai ta Talba ya kauce ba tare da ya kalleshi ba ya cigaba da tafiyarsa, Ali ga juya ya kalleshi yana fadin.

“You can't face her with this face Talba, you can't, ba zaka iya ruguza farincikin Momy ba, macen da ta dauke ka kamar danta, matar da ta raine ka ka girma a hannunta, ka fi kowa sanin yadda take son Leila ba zaka jawa yarta zuwa gidan yari ba, ba zaka saka mata da wannan ba, and Leila ma bata maka komai ba, bata nuna maka komai ba sai kauna, bata cancancin wannan daga gareka ba, and ba zaka iya sakawa Daddy da wannan ba, you can't do this Talba, you can't... Idan ka zama silar kai Leila gidan ka so Daddy ba zai manta da wannan ciwon ba”

Tun da ya fara maganar Talba ya tsaya cak yana saurarensa har sai da ya gama sannan ya cigaba da tafiyarsa ba tare daya juyo ba. A ka'ida idan tafiya ta kama shi a wani gurin direban gidansu yake kira ya zo ya dauke shi, sai dai wannan karon abun hawa ya tara ya hau ya kai har bakin gate din gidan. Knocking yai aka bude masa sai ya saka mai gadin gidan ya sallami mai achaban sannan ya shiga cikin gidan, kallo daya yai ma part din Momy ya dauke idonta ya nufi bangarensa, tura kofar dakin yai ya shiga, sai ya nufi bakin gadonsa ya zauna ya dafe kansa, ba abun da Leila tai yafi ba shi mamaki ba, na Madina ne, domin be taba tsammanin haka daga gareta ba, ko kadan be taba kawowa ransa cewar Madina zata iya aikata wannan abun ba, and he can't believe Ali yana son Talba all this while, sai a yanzu yake fahimtar dalilinsa na bawa Leila gaskiya a ko da yaushe. Ya busar da iskar bakinsa ya mike tsaye ya nufi bandakinsa sai da ya raba jikinsa da tufafi sannan ya sakarwa kansa ruwa ya lumshe ido yana sauraren yadda ruwan ke dukan kansa, zuciyarsa na wani irin zafi kamar ana soyata. Be san ya zai yi ba, zai fuskanci Daddy ne da maganar abun da Leila tai? Ko kuma na Madina? Ko kuma zai rufe duka maganar biyu ne? No taya za'ayi maka sata ka kama wanda yai maka satar sannan ka bar shi ya tafi ba tare da ka hukunta shi. Ya dade a tsaye jikin shower sannan ya fara murza sabulu ya wanke jikinsa ya daura tawul ya fito rike da karamin tawul yana goge jikinsa. Gaban madubi ya zo ya tsaya yana kallon kasan. Jin an taba kofar dakin ya saka shi juyowa sai yai arba da Kabir dake rike da wayarsa.

“Na kira Ali yace min ka dawo gida”

Talba ya kalleshi kawai ya dauke kai ba tare da yace komai ba. Hakan ya saka Kabir tunanin wata kila abun da Momy ta fada masa ta yi ma Talba ne ya saka shi damuwa. Zuwa yai ya zauna saman gadon Talba

“Don't tell me abun da Momy tai maka ne ya saka ka damuwa?”

Talba ya sake kallonsa a karo na biyu yana tunanin abun da Momy tai masa domin shi har ya manta.

“Look, ni da kai fa mun san halin Momy, be kamata mu rika damuwa da abun da take yi ba, i know ba dadi ace maifiyarka bata son matarka, kuma ta nuna maka a fili har ta musguna mata, domin ni ma na san ba lalle ne yarinyar nake hari Momy ta so ta ba, idan ma ta amincen min na aureta kenan”

Talba ya zauna kusa da shi yana kallon wani bangaren na dakin.

“Ba abun da Momy tai ya bata min rai ba, na manta da wannan”

Da mamaki Kabir yake kallonsa.

“Me ke damunka?”

Talba yayi shiru kamar ba zai ce komai ba, wanda hakan ya bawa Kabir damar karantar damuwar dake fuskarsa.

“Akan Momy ne ko Leila ko Daddy?”

“Idan na fada maka cewar Madina ce ta saka aka sace Aminatu zaka yarda?”

“Aa me zai saka tai yi haka?”

“Shi ne abunda nake ta tunani, soyayya ta iya ta saka ka cutar da wani”

Kabir ya nuna da alamar rashin yarda.

“Don't tell me Madina son ka take yi?”

“Yes, saboda hakan ta saka aka dauke Aminatu?”

Kabir ya mike tsaye da sauri.

“What...? Taya akai ka sani? Waya fada maka?”

Talba ya kalleshi.

“Ali”

“Ya akai ya sani?”

“Saboda ya bugi cikinta ne”

“Wane irin kalar bugun ciki? Ban gane wannan maganar ba how?”

Talba ya sauke ajiyar zuciya, ya mike tsayen.

“Ban canja saka kaya yanzu, idan na fito anjima zamu yi magana”

“No please wannan ba maganar anjima ko gobe ce ba, shiyasa ta bada number ta? So that ka zarge ni da sace ta? Daman na dade ina zargin cewa na gida ne kawai zai iya wannan abun”

Ya juya ya juyo yana ta mamaki har da rike habarsa.

“Na kasa yardar da wannan Wallahi?”

“No nima yanzu na sani, kuma ina tunanin barin maganar saboda da wani dalili but sometimes ina jin kamar ba zan iya runtse ido na toshe kunne kamar ba zan ji komai ba”

“Wait saboda tana kawar Leila zaka kyaleta? Ko kuma kana zargin da hannun Leila a maganar ne?”

“Babu hannun Leila kuma ba dan tana kawar Leila zan kyaleta ba”

Da mamaki Kabir yake kallonsa.

“No please karka ma kawo wani excuse, idan ma kana ganin kamar baka da evidence ne ita da kanta zata sama mana evidence ai, idan ta ji wahala zata fadi mutanen da ta saka sukai wannan aikin”

“No...”

Talba be fadi abun da zai fada ba, Kabir ya daga masa hannu.

“Ya kake abu kamar ba kai ba, ka manta kalaman da kai cewar sai ka hukunta wanda ya aikata mata haka? Kyaleta kamar wawanci ne, kuma ka bata damar da zata sake yin wani abun, abu na biyu wannan abun ba kai kadai ya shafa ba, ni ma ya shafe ni”

Kabir na fadar hakan ya juya ya fice daga dakin cikin bacin rai. Talba ya busar da iskar bakinsa, ba wai baya son hukunta Madina ba ne, sai dai baya son rushe farincikin Momy kamar Ali ya fada, kuma ba Leila kadai za a kama ba, kamar yadda ba ita kadai za a hukunta ba, har da Momy, ya Daddy zai ji? Ace matarsa da yarsa sun aikata babban laifi kamar wannan? Shin zai ba sirrin ya kasance a rufe ne, ko kuma zai dauki wani mataki? Har ya saka tufafinsa ya fesa turare be raba dayan biyu ba.

Kabir na fitowa bangarensu ya kira Daddy a waya ya fada masa abun da ke faruwa, sannan ya karasa bangaren Momy rai a bace jikinsa har rawa yake, kamin a bude masa kofar falon ya danna door bell din yafi a kirga. Da sauri Amal ta bude masa, ya shiga cikin falon ya doshi inda Momy take zaune saman couch Leila na kokarin mika mata kofin tea yana fadin.

“Momy kin ji wani abu? Wai Madina ce ta saka aka sace yarinyar nan saboda tana son Talba”

Leila bata san lokacin da ta saki kofin shayin ba, ya fadi kasa ya fashe Momy kuma ta kalleshi cike da tashin hankali, Amal kuma ta karaso kusa da su da sauri tana zaro ido tare da saka hannunta ta rufe bakinta.

“A ina ka samu wannan labarin?”

“Yanzu Talba yake fada min”

“Ta ina Talba ya ji?”

“Gurin Ali”

“Shi Alin ta ina ya ji?”

Kabir ya daga kafadunsa, alamar be sani ba. Sai Momy ta kalli Leila ta daka mata tsawa.

“Ya akai Ali ya sani?”

Kallon mamaki Kabir yake musu.

“That's means kun sani kenan?”

Momy ta mike tsaye tana amsawa Kabir.

“Yes, amman na bar maganar saboda tunuwar asirin Madina yana nufin na Leila, ina fatar ka gane, saboda hakan dole ne ka rufe bakinka”

“Taya abun da Madina ta aikata zai shafi Leila? A tare suka aikata ne? Ko kuma da hadin bakinta aka aikata?”

“Babu ko daya, amman bayyanar sirrin Madina cewar ita ta saka a dauke Aminatu shi ne bayyanar sirrin yar'uwarka cewar ta kashe Baaba”

Da wani irin karfin murya Momy take magana da Kabir, murya dake bayyana bacin ranta karara. Sannan ta nufi kofar fita kanta babu ko dankwali ta bude kofar ta fita, Kabir da Amal suka bita da kallo, ban da Leila da ta kasa yin kwakkwaran motsi sai hawaye take kuma ta ki ta yarda ta daga kai ta kalli kowa. Zaunawa Kabir yai kusa da inda Momy ta tashi ya dafe kansa yana tunanin maganar Momy, domin har yanzu be gano ta inda tonun asirin Leila ya shafi Madina ba. Tafiya Leila ta fara yi kafafuwanta na hadewa kamar mai koyon tafiyar, ta fice daga falon ta bi bayan Momy.

Kai tsaye Momy bangaren Talba ta nufa, kamar zata balla kofar dakin haka ta tura kofar da karfi ta shiga ciki, Talba dake tsaye yana kokarin saura agogon hannunsa ya juyo ya kalleta, sai ta maida kofar ta rufe kana ta juyo ta kalleshi da wani irin duba dake nuna ko kasheshi zata iya a halin da take ciki a yanzu.

“Iyakarta ka ce ka fasa auren Leila, ko kuma ka koma kana yi mata wani kallo na dabam, wata kila musgunawar da kake mata ta karu, amman ba zan tana yarda ka bude wannan sirrin ba, ko da sama da kasa za su hade ba zan aminta a hukunta Madina ba, ba kuma zan bari ka fadawa police komai a kai ba, indai na isa da kai, kuma rainon da nai maka baka dauke shi a banza ba, kuma baka son bacin raina to kabar maganar nan a cikinka Talba! Karka kuskura kace zaka hukunta Madina”

Hankali kwance Talba yake kallon Momy.

“Saboda kina tsoron kar Madina ta fadawa yan sanda cewar Leila ta kashe Baaba?”

Kusan suma Momy ta yi, domin ko kadan tunaninta be kawo mata cewar Talba ya san da wannan maganar ba.

“Ba zan bari maganar ta fita Momy, ba dan saboda kowa ba sai dan saboda ke, idan aka ce za a hukunta Leila na san zaki damu, kuma damuwarki zata haifar min da damuwa, amman idan aka ce za a hukunta ki, ban san iya halin da zan shiga ba, ba zan iya jure wani abu ya same ki ba Momy”

Ganin hawaye ya cika idonsa ya saka ta tako a hankali ta karaso inda yake, sai kuma ta rasa kalma fada masa, she seat there helpless gaba daya ma ta rasa tunanin da zata yi, jikinta yayi sanyi sosai. Talba ya zauna a kasa ya dora kansa saman cinyarta.

“Ina son ki Momy, na bude ido dake, kin min gata kin nuna min soyayya, tun da na bude ido ban san wata uwa ba bayan ke, ko da aiki aka dauke ki a gidan nan

na kula da ni, kin cancanci na girmamaki na mutuntaki na karramaki, kuma na nema miki farin ciki a duk inda yake, saboda na girma a hannunki, balle kuma ace kin rike ni a matsayin da, kin rainene har na girma na mallaki hankalin kaina”

Ta lumshe ido hawayen da suka zubo mata suka sauka saman kansa, na shi kuma suna sauka a cinyarta, fashewa Momy tai da kuka mai karfi kamar ba ita ba, sai Talba ya dago ya kalleta, Leila kuma dake labe jikin kofar ta turo kofar dakin ta shigo fuskarta da hawaye shabe shabe, ta tako ta shigo cikin dakin.

“Na rusa farincikin mutane da dama, bana tunani mai kyau wani lokacin, bana iya yin komai a natse, zuciyata tana saka ni aikata ta abubuwa sai daga baya na dawo ina nadama”

Ganinta ya saka Momy ta yanke kukanta a take ta kalleta. Talba ma dagowa yai ya kalleta sai ya mike tsaye yana jin kamar ya saka bindiga ya halbeta.

“Kamin ki aikata hakan ya kamata ki yi wannan tunani ba bayan kin aikata ba, kin bata Komai Leila, saboda son zuciya da nuna isa, kowa wulakantattace ne a gurinki, idan zuciyarki ta raya miki abu baki iya hanata sai kin aikata, saboda muguwar zuciyarki da baki iya controlling kika jefa kanki cikin fitina kika jefa Momy da ni, kuma kika jefa iyalan matar nan cikin tunani da zullumi, and i know wata rana gaskiya zata bayyana domin karya fure take bata yaya, kuma duk ranar da gaskiya ta bayyana duniya Daddy zata zarga, za ace matarsa ta boye gawar yar aikinsu a gidan gonarta, mutane da yawa za su ce tsafi akai da ita, ba kowa zai kyautata mana zato ba, all this because of you LEILA”

Ya karasa yana furta sunanta a fusace in capital letters, jijiyar wuyansa har tashi take saboda bacin rai. Ba karamin razana tai ba kamin yadda Talba ya taso mata kamar zai dake ta, da sauri tai baya baya.

“Wata kila zan iya gyara komai...”

Bata karasa ba ya isa gurinta ta rika kafadarta duka biyu da hannayensa yana girgiza zata.

“Ta ya? Ta ya...? Wannan maganar b zata fita ba Leila, ba zaki cusa bakinciki a zuciyar Daddy ba, wannan da kika mana ya wadatar”

Momy ta yi saurin karaso gurin ta fisge hannayen Talba ta raba jikin Leila ta hannayensa sannan ta shiga tsakiya tana girgiza masa kai.

“Talba... Ya isa... Baka san ya take ji ba.. Ni ma ina ji na a wani yanayi balle kuma ita, don't hurt her please”

Ta karasa muryarsa na fita slowly. Talba ya kalleta with angry face.

“I hate you”

Ya furta, hakoransa na sama suna haduwa dana kasa tsabar bacin rai.

“I'm sorry, I'm sorry... I'm sorry...i know this is not easy... I'm sorry ”

Ta fada sannan ta juya tana fice daga dakin tana tafiya kamar bata son motsa kafafuwanta, Momy ta rufa mata baya. Talba ya nufi inda yake aje keys din motarsa ya dauka ya fito daga dakin yana jin gidan gaba daya ya fice masa a rai. Yana fitowa ya nufi motarsa ya bude da zimmar shiga heading to gidan Marayu sai gashi an bude gate din Motar Daddy ta kunno kai.

BATURIYA POV.

Tana zaune dakinsu saman prayer mat hannunta rike da carbi tana ja, bakinta kumshe da addu'o'i kala kala, ita kanta bata san ta iya tasbihin da hailala da kyau ba irin yau. Ji take kamar ta runtse ido ta bude ta ji zuciyarta wasai babu son Fahat kuma babu sanin Faruk a cikinta. Tun jiya da abun ya same ta ta saka magana da kowa ta maida lamarinta ga Allah tana ta fada masa bukatarta tare da jero masa matsalolinta da fatar zai mata magani. Tun da take a rayuwarta bata san wani dare da ta taba tsayawa ta hana idonta bachi saboda neman biyan bukata ko kuma kai kukanta ga Allah ba irin wannan. Tsakanin jiya zuwa yau ta yi rama kamar wanda ta kwanta ciwo, daman can ba jikin ne da ita ba ga kuma damuwar Fahat da ta fara yi mata sannu sannu, sai dai bata taba rama da jin tashin hankali irin na jiya ba. Har yanzu wani abun ganinsa take kamar mafarki. Umma ce ta shigo dakin rike da kofin fura da aka dama da kankara ta aje mata kusa da ita sannan ta zauna.

“Ga fura na dama miki idan zaki iya sha, tun da komai aka baki ba iya ci kike ba”

Ta kalli furar.

“Na gode”

Sannan ta cigaba da jan carbi. Umma ta ce.

“Tun jiya nake son magana da ke, sai dai ganin kina cikin damuwa ya saka ban takura miki ba”

Ta dan kalli Umma kadan.

“Jiya na ji kina maganar Ramlee, har kina cewa ta cucece, Rafi'a miya hada ki da Ramlee? Yarinyar da aka hana ki abota da ita tun kina makaranta? Kuma har yanzu baki fada min takaimaman abun da ya faru tsakaninki da Fahat din da da kuma Faruk din da naji kina ambata”

Rafi'a ta ji gabanta ya fadi, domin An hanata abota da Ramlee saboda rashin tarbiyarta da kuma wasu halaye da ake ganin ta kirkiro ma kanta tun suna secondary school a lokacin Mahaifinta yana da rai, babu irin jan kunne da be yi mata ba, akan kar ya sake jin sunan Ramlee ma a bakinta, kasancewar sun shaku a makaranta sanadiyar kudin da Ramlee take samu a gurin maza tun tana da kurciya, tana kashewa yan makarantar sai dai ta fi kyautata Rafi'a domin jininsu yafi haduwa not because of Baturiya tana yar iska ko wani abun makamancin haka, sai dan jininsu da Allah ya hada, Ramlee tana son Baturiya sosai, ita kuma Baturiya ta tashi da kwadayi abun hannun Ramlee na burge ta hakan ya saka suke shiri sosai, ada can har gidansu Rafi'a Ramlee tana zuwa ta wuni ko ta kwana, sai dai daga lokacin da Mahaifinta Baturiya ya samu labarin abubuwan da Ramlee take sai ya datse abotarsu ya hana ta zuwa gidan kuma ya ja kunnen Baturiya akan Ramlee.

Duk irin tsoron da Baturiya take yi Mahaifinta be saka ta rabu da Ramlee ba, tana abota da ita a boye, har zuwa lokacin da Ramlee ta zama rikakkar yar duniya ta waye ta iya barikin ta gwane, sai dai babu wanda ya taba sanin alakarsu ta cigaba saboda bata nunawa a gidansu. A kokarinta na dauke hankalin Umma daga zancen Ramlee ta dauko mata labarin abun da ya faru a ranar, a lokacin ne wani sabon kuka ya zo mata, Umma kuma ta cika da tsakanin mamakin yadda akai Fahat da Faruk suka san juna, amman bata yarda da zancen da Baturiya ta fada mata cewar Fahat ya ce Faruk ya samu aiki ba, idan ma ya samu bata tunanin wani babban aiki ne, kai koma dai babban aiki ne, tana jin yarta ta fi karfinsa a yanzu, kuma zata iya samun wanda ya fishi ya fi Fahat komai da komai.

“Lallai ma Fahat din nan ya cika tsohon dan iska marar mutunci, bayan yace ya fasa aurenki sai kuma ya biyo ki da wasu kalaman banza har yana dauko Faruk ya kawo miki, ke kika son saka kanki cikin damuwa tun farko, namijin da ba shi da tabbas zaki zauna kina wahalar da kanki akansa? Ba gashi shi har ya manta ba? Har yana neman ci miki fuska, da acw da gaske yake sonki so na tsakani da Allah ai da ba zai biyoki da wata maganar banza ba, sai rarrashin”

Baturiya dai ban da zallar hawaye babu abun da take, ba zata iya fadar cewar ta yi nadamar saka son Fahat a ranta ba for now, kamar yadda ta kasa ayyana bakincikinta na rabuwa da Faruk a yanzu tana ganin wata aikata laifi ba, sai dai ta kasa natsuwa da ko wanne.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Fasa shiga motar Talba yai sai ya baro jikin motar ya nufo inda Daddy yake faka motarsa. Direba na yin parking Daddy ya bude da kansa ya fito yana kallon Talba.

“Ina zaka je?”

Talba yayi shiru kamar mai tunanin abun da zai fada.

“Daddy sannu da zuwa”

“Jikin da sauki sosai? Na fadawa Ali kar ya bari ka dawo sai ka samu sauki sosai”

“Na ji sauki Daddy”

“Haka ake so, amman karka ce min driving me zaka fara yanzu”

Ya dan yi murmushi ba tare da ya ce komai ba, suka jera shi da Daddy zuwa bangaren Momy. Talba ya mika hannu ya danna door bell din kofar yana kallon Daddy dake fadar.

“Kabir ya kira ni yanzu, wai an gano Madina ce ta sace yarinyar nan?”

“No, ba Madina ba ce gaskiya, me zai saka Madina tai haka?”

“Ni ma abun da nake tunani kenan, abun ya daure min kai sosai”

Wannan karon ma Amal ce ta bude kofar falon. Ganin Daddy yasa gabanta faduwa kamar ta san ya ji abun da ke faruwa.

“Daddy sannu da zuwa”

“Yauwa Amal”

Ya amsa sannan ya shigo cikin falon Talba na biye da shi. Kabir na ganin Daddy ya mike tsaye Momy kuma ta dago jajayen idanuwanta ta kalleshi. One seat ya nufa ya zauna yana kallon fuskokinsu musamman na Kabir dake nuna tashin hankali karara, fuskar Momy kuma tana nuna alamar ta yi kuka.

“Ba Madina ba ce Daddy, Kabir kai ka fada masa? Ai ba a tabbatar ba”

Talba ya fada yana yi ma Kabir alama da ido.

“Yeah ba a tabbatar ba Daddy”

Daddy ya kalli Talba ya sake kallon Kabir sannan ya kalli Momy.

“Akwai matsala a cikin gidana, kuma idan har ba Madina ba ce dole wani na gida ne ya aikata wannan abun”

“Wallahi ba cikin gidan nan ba ne Daddy kuma ka ji na rantse maka”

Daddy ya kalli Talba da yai maganar yana murmushi.

“Hakan na nufin kasan wanda ya aikata”

Talba ya sauke kai kasa ya kasa kallon Daddy domin ba al'adarsa ba ce yi ma Daddy karya, even for once be taba ba, ko minene zau fade shi kai tsaye ko da ba zai yi ma kowa dadi ba.

“Akwai abun da kuka boyewa, anyway zan yi magana da CP za a bincike ta, akwai wani evidence?”

“Babu Evidence Engr, ba mu da tabbacin ita ta aikata ko ba ita”

Wannan karon Momy ce tai maganar, gaba daya jikinta ya kara mutuwa tun da lokacin da ta fahimci Kabir ya kira Daddy ya fada masa. Daddy ya mike tsaye

“To bincike zai tabbatar da haka, idan babu rame miya kawo maganar rame? Dole akwai wani abu a kasa”

Har ya fara tafiya, Momy ta mike tsaye tana fadin.

“Alakar Madina da gidan nan, be kamata ace an mata haka ba, ko da ace ita din ce ta aikata ballantana babu tabbacin hakan”

Daddy ya juyo ya kalleta ya fara magana cikin fusata da daga murya data cika duka katon falon.

“Ita bata kalli alakar gidan nan ba ta aikata abun da ta aikata, surukata fa aka dauka matar ɗana, kuma kina tsammanin saboda wata alaka ta banza da ba yan'uwanta ba sai ta saka na kyale ta? Wallahi ko da ace Leila ce ko Amal ko Talba kansa ya aikata wannan mummunan abun sai na hukunta shi! Idan ma bata aikata ba bincike sai tabbatar da haka, saboda kidnapping din nan na kusa rasa ɗana kwanakin baya, kuma kike ganin zai duba alaka na kyale shi”

Sautin muryarsa ne Leila dake dakinta ta ji, sakamakon barin kofar dakin da tai a bude, sai ta taso da sauri ta fito ta fara saukowa stairs din hawaye na sauko mata. Daddy ya daga kai ya kalleta, sai dai be ce komai ba, ita kuma ta gagara saukowa gaba daya sai ta tsaya rabin stairs din tana kallonsa.

“Ka dubi girman Allah ka bar maganar nan Engr, a yafewa Madina har sai idan ta sake aikatawa dan Allah”

Momy ta fada cikin kuka, tana hada hannayenta alamar rokonsa. Kabir ya matsa kusa da Daddy

“Daddy please”

Daddy ya dauke idonsa daga kallon Momy ya kalli Kabir sai kuma ya kalli Talba da fuskarsa ke cike da rauni, kamin ya kalli Amal da ita ma hawayen take, sai kuma ya sake maida dubansa gurin Momy zuwa ga Leila.

“Da hadin bakinki aka aikata”

Talba ne ya amsawa Daddy amadadin Leila da kanta.

“Bata sani ba Daddy, ba da hadin bakinta akai ba, lokacin da Madina zata aikata bata fada mata ba kuma bata nemi shawararta”

Daddy ya kalli Talba, sai dai be ce komai ba, ya juya ga cigaba da tafiyarsa, sai Leila ta kira shi muryarta na rawa.

“Daddy...”

Ya tsaya sannan ya juyo, Momy ta yi saurin kallon Leila.

“Je ki dakinki ki huta, zan masa magana da kaina”

Ta girgiza kai alamar aa tana takowa a hankali ta sauko. Talba ya nufeta

“Leila yanzu Daddy ya shigo, ki bari idan ya huta sai ki je bangarensa ki riko shi akan maganar Madina”

Leila ta kalli Talba.

“Ba rokonsa zan yi ba”

Ta kauce daga tare ta da Talba yai ta fuskanci Daddy dake tsaye.

“Akwai abun da ya kamata na sani ne?”

Daddy ya tambaya yana kallon fuskokinsu daman zuciyarsa ta raya masa akwai abun da ake boye masa.

“Daddy akwai”

Leila ta fada, sai Momy ta daka mata tsawa da wata irin muryar.

“Leila... Ki wuce dakinki na ce”

Leila ta kalli Momy ta girgiza mata kai.

“Aa Momy, lokaci yayi daya kamata Daddy ya san komai, idan aka cigaba da boyewa ba mu san iya inda abun zai kai mu, wata kila lokacin da gaskiyar zata bayyana zai fi yi mim ciwo da Daddy fiye da yanzu”

A hankali take furta ko wace kalma kamar ba ita ba, idanuwanta har wani lumshewa suke saboda hawayen da dake mata zuba.

“Daddy... Na san kasan da zancen batan Baaba.... Ba bata tai ba Daddy... Ni na zama silar ajalinta, ta hanyar turo ta da na yi daga stairs ta fado kasa, a bisa kuskure ban yi dan ta mutu ba, kuma ban yi dan ta fado kasa ba, kawai dai na fisgota da karfi ne na jefar... ”

Ta yi shiru saboda kukan dake cin makoshinta, Momy sai girgiza mata kai take, alamar kar ta fadi.

“Mun dauke ta mu kai ta asibiti, kamin mu isa ta rasu.. Na binneta a tsohon gidan gonar Momy... Wannan ya saka Madina take min barazana saboda tana son Talba, shiyasa ta sace Aminatu...”

Ba Daddy kadai ba, Har Kabir da ya san da zancen kisan sai a yanzu ya san yadda akai da gawar Baaba da kuma dalilin Momy na hana a kama Madina. Tsaye Daddy yai kamar hoto yana kallon Leila, zuciyarsa na bugawa da karfi sai ya ji kamar an watsa masa ruwan zafi a kirjinsa. Can kuma ya sauke kansa kasa ya runtse ido sai dai ya masa motsawa har lokacin. Amal ta nufo shi da sauri ta taba shi.

“Daddy ka ce wani abu please...”

Shiru be furta komai ba kuma be dago ta sake kallon kowa ba.

“Na san na aikata kuskure, sai kuma na sake yin wani kuskuren na boye abun da na aikata, duka na yi hakan ne saboda ina jin tsoro, kuma ina kallon irin kimarka da abun zai taba, Momy tana tsoron kar a akama Madina ne, saboda zata iya bayyana cewar ga abun da na aikata. Ni kuma na zabi fada maka gaskiya ne saboda na gyara abun da na bata kuma na shirya karbar kaddarata da hannu biyu Daddy Kwatankwacin hukuncin da zai wanke ni a gaban Allah domin ni na san rayuwa a nan ta kare, wannan kaddarata ce Daddy na yarda a hukunta ni...”

Ya kara fakowa ta mikawa Daddy hannyenta alamar ta shirya a saka mata handcuffs, hawaye na sauko mata. Momy ta fashe da kuka ta zube a kasa ta dora hannunta a saman kai. Amal ma kukan take, Kabir ma hawaye yake, ban da Talba da ya kasa yin ko daya sai kallon Leila yake, tun da yake a rayuwarsa be taba jin yana tausayin Leila matuka gaya ba irin na wannan ranar. Tabbas kaddararta ce, wala mai kyau ko akasin haka, ya'alla ta ture Baaba da niyar kasheta ko kuma aa, an rubutu faruwar hakan tun gabanin ta fito duniya, hadisi ne ingantacce daga bakin wanda baya karya, Annabi Muhammad Sallalahu Alaihi Wassalam. Daddy ya daga kai ya kalleta a yanzu dai ba zai ce yana tausayinta ba, kuma ba zai ce ya tsani yarsa ba.

“Kin shirya amsa laifinki har gaban alkali?”

Leila ta daga masa kai.

“Na shirya Daddy”

Talba yayi saurin juyowa ya kalli Daddy.

“Aa Daddy dan Allah kar maganar ban ta fita, zata taba kimarka ba kowa zai maka fahimta mai kyau ba, kuma zata shafi dukanmu”

“Ni ma wannan yana daga cikin kaddaratata, ku ma ku dauke shi a haka, ko kake na boye abun da ta aikata saboda wata biyan bukata ta duniya? Na tashi a gaban Allah ka rasa kalmomin da zan kare kaina da su a gabansa? Bayyanawa duniya abun da ya faru, da kuma karbar hukuncin da duk aka yanke shi zai tabbatar da cewar Leila ta yi nadama, kuma shi zai nuna cewar dukanmu mu karbi hakan a matsayin kaddararmu”

Daddy ya karasa muryarsa na rawa, alamar yana daf da fashewa da kuka domin hawaye tuni suka wanke masa fuska. Sannan ya juya ya fice daga dakin zuciyarsa na rawa kamar yadda jikinsa ma yake yi.
Leila kuma ta juya a hankali ta fara tafiya har ta haye sama, Talba ya rasa wa zai rarrsa tsakanin Momy da Amal, Kabir ma zaune akan cushion din ya dafe kansa yana jin wani kalar yanayi mai wuyar fassara. Talba ya nufi kofar fita falon sai ya ji muryar Amal tana fadar.

“Yaya dan Allah ka roki Daddy yayi hakuri, idan aka fita da Leila daga gidan nan za a iya kasheta dan Allah dan Annabi ka roke shi ya canja shawara kar ya kaita gurin police”

Talba ya juyo ya kalleta sai kuma ya juya ya cigaba da tafiyar har ya fice na tare da ya ce mata komai ba. Bangaren Daddy ya nufa yana isa sai ya samu kofar a bude, Daddy na zaune falon farko ya soke kai kasa ya hade hannayensa duka biyu guri daya, kana ganinsa kasan maganar ce take cinsa. Talba ya karasa kusa da shi a hankali ya zauna kasa yana kallon fuskarsa.

“Saboda gudun shiga damuwarka, ya saka na yarda na bar maganar a boye, idan akwai abun da nake gudu nake tsoro yanzu a duniyar nan tashin hankalina ne da na Momy, babu bawan daya isa ya wuce kaddararsa Daddy, idan har wani abu ya samu mutum na alheri ko sheri daman can an rubuta masa hakan zai kasance, kamar yadda idan kaddara ta wuce ka, ko ka tsallake ta daman can an rubuto abun ba zai same ka ba, kowa da inda Allah yake jarrabarsa na yarda wannan jarabawar ta Leila ce da kai da Momy da mu gaba daya, amman Daddy dan Allah kar wannan abun ya saka ka yanke hukuncin cikin bacin rai, kuma kar wannan ya saka kai fushi da ita ko da Momy”

Daddy ya dago kansa ya kalli Talba da idanuwansa da sukai ja sosai, ba kuka yake ba, sai dai bacin rai da bakinciki ya saka fuskarsa yamutsewa haka zalika idanuwansa ma sun canja kala.

“Miyasa ma boye min babban abu mai girma kamar wannan Mu'azz, miyasa?”

“Ni ma ban san da faruwar hakan ba sai dazun dazun nan, kuma Ali ya sanar min, shi ma ya ji ne ta hanyar Madina...”

Talba ya fadawa Daddy kadan daga abun da Ali ya fada masa ta yadda akai ya ji. Kamin Daddy ya ce komai Momy ta shigo dakin ta karaso gurinsa ta zube kasa zaune ta kama kafafuwansa tana wani irin kuka na tashin hankali.

“Ban tana bukatar wani abu mai nauyi a gareka ba Engr, a tsawon shekarun da muka yi tare kullum muna rufawa junanmu asirina, na sani kana da iko da karfin duniyar da zaka iya binne labarin kamar ba ayi ba, ko da kuwa ace duniya ta sani, balle a yanzu da duniya bata san komai ba. A yau ina son na roki wata alfamar a gurinka”

Momy ta hade yawu sannan ta kirashi da asalin sunansa.

“Mu'azu... Ka dubi girman Allah, dubi shekarun da muka ayi a zaman aurenmu, ka dubi mutuncinka da kimarka da mutane suke ganinka da shi, ka duba makomar yata, ka tausaya mata, ka rufa mata asiri ka yardar da cewar kaddara ce ta fada mata, ka bar maganar nan a cikin gidan nan! Leila bata aikata hakan da ganganci ba...”

Daddy ya kalleta yana murmushin da hausawa ke cewa ya fi kuka ciwo.

“Wannan shine yardar da kaddarar, Tabbas ina da iko da karfi da dukiya zan iya magance komai, amman ba zan yi haka ba saboda tsoron Allah, idan na yi haka ban karbi tawa kaddarar ba, kuma ba zan jidadin karbarta ba lokacin da Allah zai yanke min hukuncin a kotunsa. Kin ba ni mamaki Amina, taya zaki boye abu mai girma irin wannan? Har ki bar yarki ta binne gawa saboda gudun a yi mata hukunci? A ace Leila ta san kima da girman Baaba, Wallahi da ko a hanya Baaba zata wuce Wallahi sai Leila ta kauce ta bata hanya ta wuce, amman ace har Leila zata iya saka hannu ta janyo Baaba ta jefar saboda tana jin ita din ta isa, shin idan mahaifiyata ce ko taki mahaifiyar zaki yarda Leila ta yi mata abun da tai ma Baaba? A kullum kokarinki na nuna yayanki ba su da laifi ne, abun da suke so shi kike ba su damar yi ba wanda ni ko ke ko addini ya ce ayi ba? Shin Amina arziki hauka ne? Dukiyar da Allah ya ba ni ba kisan jarawa ba ce? Idan Yayana suka ci mutuncin wani ko suka musguna masa saboda dukiyata ko kuma ni na bi ta wata hanya da bata kamata ba da dukiyar, Wallahi sai Allah ya tambaye ni, matukar

ina sane akai komai, naira biyar sai na fadawa Allah yadda na same ta da yadda na kasheta, ashe ko arziki jarabawa ce mai girma wanda ta wuce ta talauci”

Hawaye ya saukowa Daddy.

“Kina raye, kina sanye aka binne gawar matar nan ba tare da an yi mata sallah ba, irin wanda addinin musulunci ya shar'antawa mamaci, ya rasa wannan sallah, ta rasa sutura irin wanda ake yi ma musulmi idan ya mutu, kin hana a kwantar da gawarta cikin gawarwakin musulmai yan'uwanta, a haka mata rame kamar yadda addinin musulunci ya ce, shim Amina ba ki san ana cutar da dan'adam bayan rai ya fita daga jikinsa ba? Kun cutar da Baaba, kuma kika bar iyalanta cikin zullumi da tunanin inda take wace irin mace ce ke Amina?”

Momy ta saka hannunta ta share hawayenta, sai dai hakan be hana wasu zubo mata ba.

“Ko wace uwa tana son yayanta, ba zata yarda su cutu ba sai inda karfinta ya kare, taya zan zuba ido a tafi da yata a kasheta akan laifin da ta aikata a kan kuskure? Idan ban rufa mata asiri ba wa zai rufa mata a duniyar nan? Zamu iya biyan diyya yallabai, zamu iya biyan diyar rai ka taimaka min dan Allah karka bari a tafi da Leila kotu”

“Kotu zata yanke hukunci idan diya za'a biya ko akasin haka”

Daddy na kaiwa nan ya mike tsaye, sai Momy ta juyo gurin Talba tana rokonsa.

“Talba ka taimaki yar'uwarka ka taimaka min, Daddynka yana jin maganarka ka roko min shi dan Allah, idan wani abu ya samu Leila ban san iya halin da zan shiga ba, Wallahi Wallahi na muku alkawari Leila ko hararar wani ba zata sake yi ba”

Daddy da be karasa shigewa ba ya juyo yana nuna Talba.

“Karka kuskura, rokona wani abun akan maganar nan! Wallahi ko ka aikata wannan laifin sai na hukuntaka, son da nake yi ma yayana be kai son da na ke yi ma Mahallincina ba, kuma be kai ya saka na saba dokarsa ba”

Ya fada sannan ya juya ya karasa shigewa dakinsa, zaunawa kawai yai saman gadonsa ya ciro wayarsa ya kira CP. Ko gaisuwa be tsaya sun yi ya ce.

“Allah yasa kana office”

“Ina Office amman yanzu nake shirin fita”

“Ina bukatar police zuwa gidana”

“Lafiya?”

“Yata ta aikata kisan kai, ina son a tafi da ita ne?”

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un.... Garin ya?”

“Labari mai tsawo zan same ka office”

“Okay”

“Amman ina bukatar idan sun zo za a tafi da ita a motar gida ba motar yan sanda ba”

“Zan aiko da police yanzu nan, Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ya katse wayar, a lokacin Leila Daddy ya fashe da wani irin kuka kamar ba shi ba, jikinsa har jijiga yake.
Momy na ganin Daddy ya shige ta tashi da sauri ta fice daga bangaren, part din ta nufo da gudu ta hau stairs ta tura kofar dakin Leila ta shiga sai ta zame ta zaune a kasa ta takure guri daya ta rumgume kanta.

“Tashi Tashi tashi... Ki dauko passport dinki da duk wani abu daya kamata, zan saka a miki transfer kudi yanzu a account dinki, ki tafi.....”

Sai kuma ta kasa karasawa saboda tashin hankalin dake tafiya da numfashinta. Gafen gadon ta rika ta zauna.

“Ki tafi hotel, zan miki visa zaki bar masar nan...”

Leila ta tashi ta zauna kusa da Momy.

“Ba zan iya guduwa ko'ina ba Momy, abu daya nake son ki min, ko da sama da kasa za su hade karki yarda ki amsa cewar a tare muka aikata binne Baaba, ina son ki amsa cewar bakin san komai ba”

Momy ta girgiza mata kai ta rika ta tana girgizawa tana kuka.

“Baki da hankali? Leila baki da hankali? Tafiya fa za'ayi da ke? Leila baki da hankali? Kin fita hayyacinki ne?”

Cikin wani irin kuka mai kamar na fitar rai Leila ta amsawa Momy.

“Ina da hankali Momy ina da hankali”

Momy ta rumgume ta da karfi tana jin kamar ta fasa cikinta ta saka Leila ta dinki, sai dafa kanta take tana dafa bayanta kamar ta rikice, Leila ma rumgume take da Momy tana kukar fitar hankali, ita da Momy aka rasa mai rarrashin wani.

Allah ka raba mu da aikin da na sani 😭 ni dai kam yau Leila ta ba ni tausayi

---

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu

sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Momy kamar wanda aka tsikara sai ta tashi da sauri ta fice daga dakin zuwa dakinta wayar ta dauka ta hau kiran Hajiya Saratu. Leila kuma ta mike tsaye hawaye na sauko mata ta nufi backyard din gidan tana karewa harabar kallo, domin ta ayyana a ranta cewar idan har ta bar gidan ba zata sake dawowa ba, sai dai gawarta. Ya kai hannu ta share hawayenta ta juyo ta dawo cikin dakin sai kuma ta nufo kofa ta fita tana saukowa stairs a hankali, bankwana take son yi da gidan, ko wane abu ta kalla sai ta tuna yadda take taba shi ko take amfani da shi. Har lokacin Kabir na zaune ya rasa abun da zai yi, dagowa yai a hankali ya kalleta.

“Ina zaki je”

Ta daga masa kafadunta domin bata jin zata iya wata magana a yanzu. Ganin tana kallon kofar kitchen yasa ya tashi ya nufi kitchen din ya dauko mata ruwa ya zuba mata ya mika mata, sai ta karba ta rike tana kallonshi. Can kuma ta dauke kai tana kallon kallon hawaye na sauko mata, ji take kamar bankwana take da komai na cikin gidan. Door bell din gidan aka danna da karfi hakan ya saka Kabir ya nufi kofar ya bude gabansa na faduwa, a tunaninsa Police ne, duk kuwa da bashi da tabbacin Daddy ya hakuri ko kuma yana nan akan bakarsa. Ali ya gani tsaye jikin kofar rike da wayarsa.

“Dan Allah ina son magana da Leila”

“Bata cikin natsuwar da zata iya magana da kai a yanzu”

Kabir ya fada masa yana kokarin maida kofar dakin ta rufe, sai Ali ya rike.

“Please... Na yi magana da Talba ya fada min komai, magana kawai nake son yi da ita”

Kabir ya juyo ya kalleta sannan ya bude masa kofar, sai ya shigo cikin falon da saurinsa sai da ya karaso kusa da ita sannan ya juya ya kalli Kabir alamar yana bukatar privacy. Ganin hakan ya saka Kabir ya bude kofar ya fice daga falon ya tsaya bakin kofar falon ya saka hannayensa aljihu yana sauke ajiyar zuciya.

“Ban yi magana da Talba saboda haka ya faru ba, na masa magana ne saboda ya zama a side dinki, na san yanzu kina jin damuwa marar misaltuwa”

Ali ya mika hannunsa ya karbi kofin ruwan dake hannun Leila ya aje kasa, sannan ya rika hannayenta duka biyu.

“Ina son ki sani, no matter what happens i will always be on your side, and wannan abun zai wuce kamar ba'ayi ba, ba za a yanke miki hukuncin kisa ba, saboda ba ku aikata kisan da ganganci ba, you will be free”

Ta dan sakar masa murmushin karfin hali hawaye na sauko mata.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, ki yi ta nanatawa kin ji?”

Ya fada yana jin kamar ace zai iya saka hannunsa ya yaye mata damuwarta, ya maida komai ba komai ba. Ya sake hannayen nata yana jin kamar ba zai iya numfashi ba, yana yin baya kadan sai ga Momy ta sauko da saurinta da mayafi hannunta rike da makullin mota, wata uwar harara ta watsawa Ali domin ganin take kamar shi ya sassa komai.

“Me kake yi nan? Bayan halin daka jefata har kana da karfin halin da zaka tako kafarka gidan nan ka zo gabanta ka tsaya?”

Momy na fada tana yin cikinsa kamar zata dokeshi. Leila ta mika hannu ya rika Momy ta riko Momy ta girgiza mata kai. Momy ta kama hannunta tana fadin.

“Zo muje”

Nan ma fisge hannunta tai tana girgiza mata kai. Sai ga Kabir ya shigo da sauri.

“Momy police ne, waya kira su?”

Momy ta kalli Kabir cikin tashin hankali, Leila ma kallonsa take tana jin kamar mafarki take, domin tun da take a rayuwarta bata taba zuwa police station ba, ko da sunan beli ko ganin wani, balle ace yau ita za a kai. Momy ta kalli Ali

“Kai ka zo da police?”

“Aa ba ni ba ne”

Ali ya amsa, ana danna door bell din Momy ta maida Leila bayanta. Kabir da Ali suka kalli kofar aka rasa wanda zai karasa ya bude. Sai kuma Momy ta juyo ta kama hannun Leila.

“Zo nan na boye ki”

Leila ta fisge hannunta tana girgizawa Momy kai, Momya ta mata wani kallon tsoro.

“Karki je Leila, karki bar ni dan Allah, yar'uwarki tana bukatarki... Kabir....Talba... Ni... Leila burikanki....”

Momy ta kasa karasawa sai wani irin rausaya take kamar zata fadi. Cikin karfin hali da dakewar zuciya Kabir ya karasa gurin kofar ya bude falon, sai yai arba da Daddy da Talba sai kuma police guda uku maza biyu mace daya.

“Daddy Police...”

Kamin Kabir ya karasa Daddy ya amsa masa.

“Ni na kira su”

A dole ya matsa baya ya ba su hanya, tun da yake a rayuwarsa be taba jin son yar'uwarsa Leila a ransa ba irin yau, sai ya ji kamar ya dauke ta ya goya a baya yai ta gudu har ya tsirarta da ita. Da hannu Daddy ya nuna musu ita, sai suka nufeta Momy na kara boyeta. Talba ya kalli Daddy da sauri kamar yayi wani abu babu dama.

“Aa dan Allah, haba Yallabai Leila fa yarka ce jininka ce”

Sai kuma ya nufi gurin Talba ta rika shi.

“Dan Allah kar a tafi da ita”

Ta koma gurin Daddy.

“Ka yi hakuri dan Allah”

Ta sake juyowa.

“Kabir za a tafi da yar'uwarka, Amal... ”

Momy ta kwalawa Amal dake dakinta tana kuka kira. Sai ga Amal ta sauko da gudu a lokacin Police din har su saka mata handcuff a hannu, mace ta rika ta za su fara tafiya.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un, Leila ki yi ta maimaitawa”

Ali ya fada sai Talba ya kalleshi. Leila kuma ta juyo tana kallon Momy da yan'uwanta, Kabir ya rike Momy da mugun karfi domin so take ta rike Leila ta hana a tafi da ita.

“La'ilaha Illalah... Wayyo Yata... Leila...”

Tana kawawa kusa da Daddy sai ya kai hannunsa ya taba kanta.

“Allah ya miki albarka, kuma ina kyautata zaton kotu zata yanke hukuncin daya dace a bisa adalci, i forgive you Leila”

Ta daga kai hawaye na sauko mata, domin har lokacin bata iya furta komai. Momy ta zube kasa tana kuka kamar ranta zai fita. Daddy ya kalli Talba.

“Muje ka ja mota...”

Talba ya girgiza kai da sauri.

“Daddy ba zan iya ba, ba zan iya tuka mota na kai Leila Station ba”

Daddy ya kalli Kabir shi ma ya girgiza masa kai, sai Daddy ya ciro wayarsa yana kiran direbansa. Amal nufi kofar da gudu ta sha gabansu ta rumgume Leila tana kuka.

“Daddy a gabana komai ya faru, ba da gangan ta aikata ba”

Amal ta fada tana wani irin kuka sosai, Daddy ya saka hannunsa da kansa ya jamye ta daga jikin Leila, sannan yai ma police din alama da su tafi da ita. Motar gida suka shiga sannan Daddy da Talba da Kabir suka shiga mota daya, Ali kuma ya shiga tashi motar, sai aka bar gidan daga Momy sai Amal, daga bisani Hajiya Saratu ta iso ta shiga rarrashin Momy.
Kai tsaye state icd aka wuce da ita, duk wani bincike da ya kamata su yi mata sun mata sannan suka saka ta a cell da sunan Monday za su shiga da ita kotu. Babu yadda CP be nunawa Daddy cewar za a iya canja komai kamar be faru ba, amman Daddy ya ki aminta sai cewa yake a bar doka tai aikinta, duk hukuncin da alkawali ya yanke ya shirya daukarsa. A lokacin ne Daddy yake bada report din Madina a rake Cp ya tashi yaransa aka tura su gidansu Madina. Police suka kira yan'uwan Baaba suka nemi ganinsu station din, wadanda suka garin suka riga na kauye isowa, har cikin office din CP aka shiga da su, saboda Daddy yai magana da su ya kwantar musu da hankali sannan ya fada musu cewar Leila tana gurin kuma zata fuskancin hukunci.
Sannan aka gabatar musu da gawar Baaba da police suka hako a tsohon gidan Momy, a lokacin ne suka fashe da kuka.
Ko da yamma tai na wadanda suka kauye sun samu labarin har sun iso, alfamar da Daddy ya roka daya ce, na hana a fadawa yan jarida.
Sai kuma addu'o'in da yan'uwan Baaba suka rika yi suna tsinewa Leila ko kadan be yi ma Daddy dadi ba, duk kuwa da ya san yarsa mai Laifi ce.

Ba karamin tashin hankali Madina ta shiga ba, ganin Police sun ta ho zasu tafi da ita, da fari boyewa tai aka ce bata nan sai da Police din suka nuna za su shiga su fito da ita da karfi sannan Hajiya ta fiddo da ita, kuka sosai Madina take tana faduwa tana tashi tana rike Hajiya, tana rokon Hajiya tai wani abu kar a tafi da ita. Hajiya kam ban da kuka babu abun da take, suna kasata a motarsu ta kira yan'uwanta da ma mahaifinta da mahaifinta ta fada masa sannan ta bi bayansu tare da direbanta.
Sai da aka saka ta a cell sannan su Daddy suka dauko hanyar gida ko da suka dawo gidan ya cika da yan'uwan Momy, sai taya ta jimami suke, ita kuma tana kwance a dakinta kan tile, babu yadda ba su da ita ba akan ta koma saman gado ko kuma ta tashi a shimfida mata wani abu amman ta ki tai ko daya.
Bayan sallah Isha'i Amal ta fito ta zauna a waje tana ta kuka ita kadai, sai dai abun da bata sani ba Talba na zaune nesa da ita yana nashi tunanin, sai dai ganinta ya saka ya taso ya dawo kusa da ita ya zauna, sai ta kalleshi ta share hawayenta.

“Kai da Daddy zamu iya yin wani abu, Leila ta dawo gida, amman baku ba, yau zata kwana a inda ba gida ba, bana tunanin zata iya yin bachin ma”

Talba ya sauke ajiyar zuciya.

“Ya kike ji a ranki?”

Ta kalleshi tana jin wani sabon kuka na taso mata.

“Da zafi sosai, ina jin kamar kashe Ya Leila za'ayi, kuma idan aka kasheta ba zamu sake farinciki ba”

“Zamu sake, ko da kuwa an kashe ta din kamar yadda kike hasasashe, ballana ina kyautata zaton ba a za a kashe ta ba”

“Ba zan sake farinciki ba, ba zan sake dariya ba har sai ta dawo”

“Zaki sake, na san wata yarinya sa'arki wanda ta rasa iyaye ta rasa yan'uwa ta rasa muhalli, kuma ta jure, aka wulakantata ta dauka kuma a yanzu haka ta maida komai ba komai ba tana rayuwa cikin farinciki”

Ta kalleshi domin ta san kai tsaye wanda yake magana akanta.

“Aminatu?”

Ya daga mata kai.

“Duk wani halin rayuwa da zaki shiga a yanzu ki rika tunawa da ita, ta shiga taskun rayuwa da damuwa fiye da naki, kuma har yanzu bata gama fuskanta ba, kowa da kalar kaddararsa Amal this too shall pass”

Ta kwantar da kanta jikinta Talba tana hawaye.

*** *** ***

At first Madina ta so ta musa cewar ta sace Aminatu, sai dai bincike da police sukai a wayarta sai suka gano akwai alaka a tsakaninsu, duk kuwa da kasancewar tana goge kiran da yake mata ko take masa, sai dai tuntubar kamfanin sadarwa da sukai an ba su duka record calls dinta, sun saurara sai suka gano wanda ta yi da Alfa. Plan aka hada da ita ta kira sukai magana akan kudin da zata ba shi, 30 million, ta fada masa inda za su hadu sannan aka je gidansu aka dauko motarta aka bata ta tuka kanta police na biye da ita cikin hikima da gwarewar aiki har suka isa meeting point din daya zaba. Madina ta yi amfani da wayarta ta kira shi ya sanar masa daidai inda take tsaye, sai gashi ya fito cikin wata farar mota ya nufo motarta, yana bude motar ya shiga ya zauna, sai ya fahimci ba lafiya ba, domin yanayinta da fuskarta ya nuna haka, da sauri ya bude motar ya fita, sai dai kamin yai wani yunkuri police sukai nasarar cafkeshi.
Kamar taron kasuwa haka mutane suka taru suna kallon abun da ke faruwa, domin ya nuna tirjiya sosai na kin son zuwa, har sai da suka masa rauni a jiki. After an kama Alfa aka kama Bestyn wanda ya hada Madina da wadancan mutanen nan da suka hada ta da Alfa, sannan suma aka kama su.
Washe garin ranar aka zo da Aminatu ta shaidi fuskar Alfa mutumen daya sace ta, sai ta amsa cewar shi din tana ta jin tsoro sosai, dan ma Talba yana kusa da ita, kuma ta san a police station suke.

Duk irin tambayar da aka yi na Leila bata yarda da saka Momy a ciki, ta guri daya sunan Momy ya fito inda ta fadi cewar ta taimaka mata ta saka Baaba a mota sai ta koma cikin kamin ta dawo taja motar zuwa asibiti, sai dai kamin ta isa sai ta ji kamar Baaba ta mutu hakan ya saka ta nufi tsohon gidan gonar Daddy ta yi magana da Mai gadinta ya haka mata rame da sunan zata saka zinari da kudi, hakan yasa dole ta saka gawar a zaune ba a saboda yanayin yadda aka gina ramen. Sosai Momy ta so ta daukarwa yarta Lawyer Daddy ya hana, sannan ya gargade ta akan cewa be yarda ta bawa Alkali cin hancin ba ko ta nemi wata alfama ya fi son abar Alkali yai shari'a a bisa gaskiya.

FARUK POV.

Wajen falon ya fito wato harabar gidan ya tsaya yana jiran ta fito masa da Sultan. Ya kusan minti talatin a tsaye sannan ta fito tana rike da Sultan dayan hannunta rike da wata yar jaka mai kyau, dake cike da chocolate. Gafenta Sultan ya tsaya ala dole shi fushi yake yi ba zai je gurin Faruk ba, dayan hannunsa rike da chocolate daya bata masa baki.

“Sultan zamu je gida ko?”

Ya lake kafada, ya juya baya alamar ba zai je ba. Ramla ta yi dariya har sai da dimples dinta suka lotsa.

“Ga ma baya son zuwa, amman ka takura masa sai ya ji, yanzu ma fa sai da na yi masa wayo ya fito”

“Kawai dai ba ki ce kin sace min zuciyar da, gashi nan kin hada shi da chocolate ai dole ya ce ba zai zo ba”

“Aa ba dan chocolate ba ne, ka yi masa laifi ne kuma baka ba shi hakuri ba, kuma da alama baka iya rikon yara ba, da wahala yara su saba da kai”

“Ke suna saurin sabo da ke?”

“Sosai ma, ga zahiri kana gani”

Ta masa alama da ido tana nuna masa Sultan.

“To ai kin ga ta kwana gidan sauki, zuwa zuwa sai ki koya min ni ma su suka saurin sabo da ni”

Ta yi murmushi ta duka gurin Sultan tana magana da shi, hakan ya bawa Faruk damar bawa idanuwansa abinci, tana da kyau da haiba ta fuska, sai a halin yanzu ba kyau fuska ne abun da yake bukata ba, kyau hali.

“Idan ba zai je ba, ka bar shi a nan ya kwana mana”

Ta fada tana dagowa ta kalleshi.

“Yaron nan da kika gani, shi kadai na mallaka fa, ba zan iya ba ina gari daya da shi”

“Aiko wata rana sai na lallaba na bi sawunka ma sace shi, farat daya ka nemeshi ka rasa”

Ya daga kafadunsa.

“Shikenan ai, sai na dawo kofar gidan nan na tare nai ta kuka, da an tambaye ni miye sai na ce Ramla ce.... ”

Kyakyalewa tai da dariya, domin yanayin yadda yai maganar abun dariya ne. Shi kansa dariyar yake, yana kallon yadda nishadi ke kawata fuskarta. Sannan ya mika hannu ya riko Sultan.

“Zo nan, mu tafi gida Mama Rukaiya tana jiranka”

Daker ya yarda Faruk ya dauke shi, sannan ta mika masa jakar hannunta mai kyau irin ta biki wanda ta saka masa chocolate din ciki.

“Dan Allah ka gaida min Rukaiya sosai, da Mama na ma manta ban tambayi jikinta”

“Ta ji sauki sosai gaskiya, Rukaiyah ma tace na karba mata numberki”

“Ka fadawa Rukaiya Number ta mai tsada ce”

“Please”

Ya roka yana bata fuska kamar zai mata kuka.

“Shikenan ka tafi zan kirata”

“Ai bata da waya, daman a wayata ne tace ki saka mata number”

“To zan kira ka”

“Ina zaki samu number”

“Babu ruwanka, kai baka san duk abun da nake so da na yi haka da hannu zan samu ba”

Ta fada tana nuna masa da hannunta da take budewa ta rufe. Sai ya wara ido.

“A takaice ce da aljana na yi arba”

Ta yi murmushi ta juya ta shige ciki, sai ya bita da kallo yana murmushi, sannan ya fice dauke da Sultan din. Kamar wasa yana isa gida ta kira shi ta ce ya bawa Rukaiyah wayar, ba karamin mamaki yai daya daga kiran ya ji muryarta. Sai dai be musa ba ya bawa Rukaiya suka gaisa kamar yadda ta bukata, kuma ya bawa Mama.
Tun daga lokacin sai wani irin shakuwa da alaka mai karfi ta shiga tsakaninsu, cikin kwana biyu suka koma kamar wadanda suka san juna shekaru da yawa, sai dai be yarda ya nuna mata yana sonta ba, Ko muma yana son fadada alakarsu zuwa wani mataki ba, karantar halinta da rayuwarta yake ta yi a hankali. Kamar yadda ita ma take kara fahimtarsa, ga son Sultan da Allah ya dora mata saman can Ramla mace ce mai son yara balle kuma Sultan da take jin kamar ba sonsa ne kadai ke dawainiya da ita ba.
Every morning before ta fita aiki yana kiranta ya bata Sultan su gaisa, wani lokacin ma bata magana da shi, iyakacinta ta ji muryar Sultan, wani lokacin kuma Sultan din ne da kansa zai saka Dadynsa ya kira masa ita su gaisa, ya fada mata duk abun da ya faru a gidan, a irin halinsu na yarinta.

Hmmm idan kaga anzudda Miya to cinikin tuwo yakare.Kowa yace wutar Kara ta kwana to shine baiyi bacciba.Arashin Kira Karen Bebe ya Bata.Ina ma,abuta son gyara Manyan Mata idan nace mata Ina nufin wadanda suka San ciwon kansu sukasan darajar gyara da mutuncin da yake kankarowa□to kuzu kumatso kusa taku dai dindaice Yar Gidan maifata Yar mutan Zamfara tazomaku da kalar nata ingantattu km gangariyar kayan gyara wadanda suka gwada sungani km sun sani wadanda km Basu gwadaba karkubari abaku labari kayan Basu bukatar dogon biyani sai dai gawadanda Basu sanmuba kayane kala kala iri daban daban, amma munhi gwanewa wurin gyaran matsaloli irin na aure da km gyaran amare da tsofi masu son tada komada Kai abundai sai Wanda ya gwada Don neman Karin bayani ko walwale rashin fahimta za'a iya tuntubata a number waya kamar haka 08169311410 ko km chat 09029891757 Ko km a address Dina dake Nasarawa Gusau wurin masallacin Mai solar Allah yasadamu da alkhairansa□□□

Kamar yadda suka fada cewar ranar Monday za su turasu zuwa kotu. Ranar na yi aka shigar da su a gaban kotu. Alkali Dahiru Sulaiman ne ya fara gudunar da shari'a. Lauyan gonatin jiha ya gabatar da karar tare da karanta laifinsu, sannan ya umarce alkalin daya tasa keyar Madina a gidan gyara hali, Leila kuma a yanke mata hukuncin kisa.
Alkalin ya dage sauraren karar har zuwa 24 ga sabon watan mai shigowar sannan ya bada umarnin samawa Leila da Madina Lauyer kamar yadda doka ta tanadar, duk kuwa da kasancewar shari'ar ta zama kala biyu ne, domin ta Leila dabam ake ta Madina da dabam.
A ranar Momy ta ci kuka kamar zata mutu, a kotu ta zube kasa ba dan ta zuma ba sai idan kafafuwanta da suka kasa daukarta saboda kuka, Daddy ma ransa be yi dadi ba ganin yadda Leila ke rusar kuka tana kallonsu, musamman da aza wuce da ita a motar gidan yari. Talba da Kabir ma daker suka iya rike hawayensu, Amal ma ta yi kuka kamar wanda akai ma mutuwa. Kamin yadda labarin abun da Leila ta aikata da kawarta Madina ya karade social media. Wani bangaren har an samu hotonsu da basu san an dauka ba.
Ta hanyar Kabir Ali ya samu labarin yadda aka gudanar da shari'ar, domin be hallarci zaman kotun ba, saboda kar ya ga Leila a halin da ba zai iya jurewa ba, sai a yanzu yake ta nadamar fadawa Talba maganar da yai, wata kila da bar maganar a sirrance kamar yadda take da yanzu komai be faru ba, da yanzu babu bakincikin a zukatansu, kuma ya be jefa Leila a wannan halin ba.
Two days da faruwar hakan Ali ya samu Daddy da maganar Lawyer, suka tattauna ya gabatarwa Daddy da wani babban Lauyer da zai daukar ma Leila, Daddy ya yaba masa sosai kuma ya jidadin yadda abotarsa da Talba ta saka ya dauke shi kamar uba. Sai bayan ya bar gidan ya kira Talba ya fada masa yadda sukai da Daddy.

“Allah ya ba mai gaskiya gaskiyarsa”

Shi ne kawai abun da Talba ya fada masa sannan ya kashe wayar, Ali yayi mamaki sosai a zatonsa Talba zai yi murna ya nuna masa jindadinsa akan abun da yai sai ya ga akasin haka, wata kila saboda tana tunanin ina son Leila na aikata ko kuwa saboda baya son Leila ta fito? Ya kasa raba dayan biyu a tunaninsa, shi dai ya san yayi hakan ne kawai saboda Allah da kuma tunanin halin da iyalan gidan suke ciki, ta wani bangaren yana ganin kamar shi ma yana da laifi na fallasa sirrin da yai.

Ana sauran sati daya a shiga kotun Daddy yake tambayar Talba Aminatu sai ya amsa masa.

“Tana nan lafiya kalau”

“Kana zuwa dubata?”

“Eh ina zuwa”

“Tana ina?”

“Gurin Hajiya Laraba”

“Bata maka maganar tarewarta ba?”

Talba ya kalli Daddy da mamaki

"Haba dai Daddy muna cikin wannan halin kuma?”

“To miye a ciki? Idan ka ce zaka dauki lokaci baka tare da matarka ba saboda shari'ar nan ai zaka dauki dogon lokaci, wata kila za ayi shekara uku biyu har fiye ba a kare ba, kuma duk a tsawon lokacin sai kace kana zaune baka tare ba? Ai ko hidima ake yi ta aure, idan akai mutuwa ba a son a dakatar da ita saboda mutuwar, balle wannan da ba mutuwa ba?”

“Amman ba kowa zai fahimta ba, sannan Momy ma zata ji ba dadi”

“Abubuwa da yawa mutane basa fahimtarsa, idan ka biye musu sai ka kai kanka ka baro, kuma mutanen nan a cikinsu babu mai wuta babu mai aljanna babu mai baka ci ko sha, balle ya hanaka, karka damu da wannan, ka samu lokaci ka yi duk abun da ya dace ka tare da matarka karka yarda na sake maka magana a karo na uku”

“In Shaa Allah Daddy”

Ya fada sannan ya tashi ya fice, y amsawa Daddy ne kawai saboda ba zai iya musa masa ba, amman har ga Allah baya ganin ya dace ya tare a yanzu da gidansu suke cikin tashin hankali, musamman Momy. Be karasa part dinsa ba wayarsa tai ringing, ciro wayar yai aljihunsa ya duba sai yai arba da Number Kaka. Sallama yai bayan ya danna gurin amsawar ya kara wayar a kunne.

“Ai da fushi na yi, ina ta jiran sai ka fara kirana amman baka kira ba”

Ya shafa kansa ya juyo yana kallon harabar gidan.

“Kaka tun lokacin da akai auren nan abubuwa suke ta faruwa na rashin kwanciyar hankali, shiyasa ban kira ba, wani abun kuma na hana a fada miki”

“To ai na ji, shiyasa na kira Laraba ta fada min komai, ashe sace yarinyar nan akai? Amman baka fada min ba, kuma ita Leila ance tana gidan maza? Kaga alhaki?”

“Ita wannan maganar har abar yadawa ce da Hajiya zata kira ta fada miki? Ke kuma ki ce alhaki?”

“Kiranta na yi ina ta masifa nace baka kawo yarinya ta gaishe ni ba, kuma kai baka zo ba, shi ne ta fada min abun da ya faru, shine na ce bari na maka jaje”

“Toh na gode, idan abubuwa sun daidaita zamu zo mu gaisheki, amman a yanzu hankalinmu ba kwance yake ba”

“Toh Allah ya kyauta, kara ma da Allah yasa ba a riga an yi auren ba, ita kuma wacan kawar tata bata da tarbiya ita ba”

“Yadda Allah ya tsara haka yake kasancewa Kaka”

“Allah ya sauwake ya tsare gaba”

“Amin”

Ya sauke wayar, sannan ya karasa part dinsa. Keys dinsa ya dauka ya fito ya nufi motarsa. Tafiyar minti talatin da biyar ta kai shi cikin gidan Hajiya Laraba, sai da ya kashe motar sannan ya bude ya fito ya nufi entrance din gidan. Hannunsa ya kai ya murda kofar ya shiga, sai ya samu yaran gaba dayansu a falon daga manya har kanana, idon Aminatu na rufe da karamin da kwali tana laleben mutanen dake falon, tana jin an bude kofar sai ta nufo inda sautin kofar falon take, a zatonta wani ne ya fita ko ya shigo a cikin mutamen da suke yar nikau din da ita. Talba na kallonta har ta karaso kusa da shi yaran kuma suka rufe baki suna mata dariya, hannu ta kai ta fara laleben wanda ta canka kamin kamshin turarensa ya daki hancinsa sai ta saka hannunta da sauri ta bude idonta. Sai tai arba da fuskar Talba, zaro ido tai ta jiya tana kallon yaran Hajiya Laraba da suka shige dakin da gudu suna dariya. Sannan ta juyo ta kalleshi.

“Yi hakuri ban san kai ba ne”

Yayi murmushi yana jin kamar ya rika hannunta yaja jikinsa ya rumgume, domin yayi marmarinta sai dai ba dama kasancewar karamar yad Hajiya Laraba tana falon tana kallonsu.

“Blind man suke yi?”

Ta daga masa kai, sai ya nufi kujera ya zauna yana ta kallon yadda tai free ta kara kyau, atamfar dake jikinta ta fito da shafe din jikinta kuma ta karbe ta sosai domin jar atamfa ce mai ratsin fari.

“Ina wuni”

Ta gaishe shi a kunyace, be amsa ba sai kallonta yake yana murmushi kana ganin yadda idonsa ke yawo a kyakkyawar fuskarta zaka san kallonta na daya daga cikin abun da ke saka shi mantawa da damuwarsa.

“Kawo min ruwa”

Ta dan saci kallonsa sannan ta nufi kitchen, ya bita da ido har ta shige kitchen din sannan ya dauke idonsa ya maida gurin Hajiya Laraba wanda ta fito sanye da Hijab fuska sake tana masa maraba da zuwa.

“Lfy Kalau Alhamdulillah”

Ya amsa sannan ya maida hankalinsa gurin tv.

“Mun yi waya da Hajiya ai”

Ya sake kallonta.

“Eh ta kirani”

“Ta dame ni da maganar ba kuje kun gaishe ta ba ne, shiyasa na fada mata abubuwan da suka faru”

Yayi shiru be ce komai ba, Aminatu ta fito rike da tray ruwa da cup ta aje masa a gabansa, sannan ta mike tsaye ta nufi dakinsu, a nan kam yayi kokarin ganin ya hana idonsa kallonta har ta shige dakin saboda Hajiya Laraba na gurin.

“Dazun Daddy yake min maganar tarewa da Aminatu, na fada masa be dace ayi haka a irin wannan yanayin ba, amman ya kasa fahimta shiyasa na zo nan gurinki wata kila ke idan kika masa magana zai fahimta”

Wani kallon rashin fahimta Hajiya Laraba tai masa.

“Ban gane ba”

A nan ya fede mata tun daga biri har wutsiya, na yadda suka yi da Daddy. Ba karamin mamaki ne ya kama Hajiya Laraba ba hannu ta saka ta rike habarta cike da tsananin mamaki ta ce

“Na dade a rayuwarta ban ga wani mutum mai karamci da dattako da sanin ya kamata ba irin Alhaji Mu'azu, yana daga cikin mutanen da, kuma mutanen da ke wahalar samun a zamanin yanzu, matsalarsa daya be yi dacen mata ba, ya auro matar data gurbata masa iyali”

“Hajiya Abubuwan da suka faru kaddara ce, kuma kowa be wuce kaddara ba”

Ya fada yana jin tausayin Momy. Hajiya Laraba ta tabe baki.

“Haka ne, Allah ya sauwake. Ya kyauta gaba”

“Ameen”

Ya amsa yana bude ruwan ya sha. Hajiya Laraba ta dora da cewa.

“Ni kam ba wata magana da zan masa, ai shi ya fika sanin abun da ya kamata, kuma wannan abun ai kamar shi akai ma, amman nuna maka haka, kamata yai kawai ka bi umarninsa, domin shari'a ba abu ce da za a ce za'ayi yanzu a kare ba, musamman ma irin wannan ta kisan kai sai ka ga an dauki shekaru ana abu daya”

“Amman Momy ba zata jidadi ba, kuma mutane za su ga kamar ban kyautawa Leila ba”

“Ka aje wannan a gefe, ka bi umarnin mahaifinka, idan kuma kana ganin rashin dacewar hakan to ni ba zan cilasta ka ba, sai ka bari har lokacin daka shirya

sannan ka tare da matarka, sai dai kamin nan zata shiga makaranta ta koyi karatu dan abun da bata sani ba ta sani, zai fi zaman banzan da zata yi”

Yayi shiru yana nazari, ita da Daddy dukansu suna da gaskiya, sai dai baya ganin ya dace ya aikata hakan a Yanzu, ba dan baya bukatar matarsa ba ko kuma dan matarsa bata bukatarsa ba, sai dan ganin ko wata biyu ba ayi ba da faruwar abubuwa marasa dadi a gidansu kuma ace ya tare da amaryarsa a gidansa? Kamar Hajiya Laraba ta san abun da yake tunani sai ta ce.

“Ba biki za'ayi a tara jama'a ba, aa kai kadai zaka dauki matarka ka tafi da ita gidanka, dan abun da Allah ya hore mana ni da yayanta sai mu yi na iya karfinmu a siya mata abun da ba zai gagara ba”

“Idan har zata tare, ni zan mata komai Hajiya zan bada kudi a siya mata duk abun da ake yi ma kowace ya mai gata idan za a aurar da ita, but before that sai idan na yi magana da Momy na ji idan hankalinta ya kwanta da tarewar tukuna”

“Toh Allah ya taimaka”

Ta fada sannan ta mike tsaye, shi ma tsaye ya tashi yana amsawa da Ameen.

“Daman dai na ce bari na zo na gaishe ku”

“Ka kyauta kuwa, a gaishe da Alhaji”

“Zai ji In Shaa Allah”

Ya amsa yana takawa zuwa gurin kofar Hajiya Laraba ta bishi da ido tana kallon yadda ya dan rame. Sai da ya fice sannan ta kwalawa Aminatu kira, sai gata ta fito da Hijab dinta.

“Je ku yi sallama da mijikinki”

Kamar wanda bata son tafiya haka ta fita kofar, tana fito ta hango shi jikin motarsa ya rumgume hannayensa yana kallon kofar kamar mai jiran fitowarta, da gangan tai tsaye tana kallonsa da alama shawarar tafiya take gurinsa ko kuma komawa cikin falon ganin fuskarsa ba yabo ba fallasa, dan murmushin daya saba yi mata babu shi a fuskarsa. Sai gashi ya mika mata hannunsa alamar ta zo gareshi, saukowa ta fara yi a hankali a tsakanin stairs din dake kofar zuwa interlock din gidan, da sannu take takawa har ta isa gurinsa sai ta sauke kai masa tana kallon shoes dinsa. Bude mata back seat yai, yai mata alama data shiga da kai, sannan ya zagaya dayan hannunsa side din ya bude ya shiga, sai da ya rufe kofar sannan ya matsa kusa da ita sosai ya rumgumeta.

“I miss you”

Ya fada yana jinta har cikin ransa, ita ma kanta yi marmarinsa domin ya kwana biyu be zo gidan ba, saboda baya cikin natsuwa.

“Tun da muka yi aure kullum da matsalar dake faruwa, duk yadda nake son damuwa ta nisance mu na kasa samun hakan”

Ya furta yana dora kansa saman nata.

“But komai zai wuce, ya zama labari komai zai zama kamar ba ayi ba, sai dai ban sani ba anan kusa ne ko kuma nesa”

“Kowa ka gani a cikin duniyar nan baya tare da farinciki dari bisa dari, dole akwai inda aka jarrabesa, sai dai ta wani ta fi ta wani kuma wani ya samu riba biyu a nan da kuma can, wani kuma sai ranar lahira, ka saka a ranka Allah yana jarrabaka ne saboda yana sonka, kuma komai zai wuce kamar yadda ka fada”

Yayi murmushi ya dago kanta yana kallon fuskarta kamar ya cinyenta.

“Ban taba kawowa a rana cewar wata rana zan samu karfin hali kamar haka na yi magana da wani ba, an jarraba ni jarabawar da sai dai na kasa gane kaina, amman a yanzu ba kowa zai gan ni yace ina da damuwa ba, na rasa uwa sai Allah ya wani wata uwar da kaka, kuma ya bani kai a matsayin miji kuma uba mai share kukana mai gudun damuwata, abun da ban taba mafarki ba, shiyasa aka ce wanda yai hakuri saboda Allah sakamakon hakurinsa mai girma ne, kuma duk yadda Allah ya jarrabe ka, ka duba na masa da kai wani ya fika shiga uku a rayuwa, sai kai hamdala ka godewa Ubangijinka”

Ya sumbance saman idonta yana murmushi.

“Shiyasa na ke sonki, kina da zurfin tunani da basira”

Ta yi murmushin ita ma tana ta shakar kamshin turarensa. Kamin ya saka hannunsa ya dago kanta a hankali ya hade bakinsu yana sotsar lisp dinta cike da kwarewa da shauki, tun yana yi tana amsar sakonsa jikinta na amsa amo har ya fara kokarin wuce gona da iri, hakan ya saka tai saurin rike hannunsa tana kokarin matsawa baya sai dai ta saka samun damar hakan saboda dayan hannunaa yana rike da kunkurunta ne. Daker ta samu ta cire bakinta daga na shi.

“Kar Mama ta ga na dade”

“Mama ai ta san sallama zaki yi da mijikinki”

Ya fada yana kallon lips dinta da take motsawa a hankali, tun da yake tare da ita be san ya gundura da kissing dinta ba, sai dai ya kawar da kai kawai idan ta kama, amman ba dan baya so ba ko kuma ya gaji. Ta saka dayan hannunta jamye hannunsa daga rikon da yai mata sannan ta bude motar ta fita, bata ko tsaya ce masa komai ba ta nufi kofar falon ta bude ta shige, sai da ya ga haka sannan ya bude side dinsa ya fita ya shiga driver seat yai ma motarsa key ya fice gidan.

Kwana biyu da faruwar hakan, ya shigo falon ya samu Amal zaune ita kadai a falon kwance saman kujera plasma na kunne amman idanuwanta suna ta wani gurin kana ganinta kasan tunani take yi. Sai da ya zauna kusa da ita sannan ta ankarar da shi din ta kalleshi da sauri.

“Laa Ya sannu da zuwa”

“Little Sis me mike tunani?”

Ta kalleshi.

“Momy”

“Miya same ta?”

“I don't want to lose her”

“Waya ce zaki rasa ta?”

“Tun da aka kama Leila bata sake lafiya ba, kullum acikin ciwo take”

“Zata ji sauki, tana kewar Leila ne kawai amman very soon zata daina saboda zata saba kamin a yanke hukunci”

“Amman Ya Leila zata dawo ko?”

“In Shaa Allah, but you have to be strong saboda Momy Okay”

Ta daga masa kai tana share hawayen da suka zubo mata.

“Tashi ki ci abinci na san baki yi lunch ba, zan yi magana da Momy yanzu amman make sure before na fito kin gama cin abincin kin ji yar kanwata”

“Toh”

Ta amsa a shagwabe, sannan ya mike tsaye ya nufi upstairs, ita kuma ta nufi dinning taja kujera ta zauna. A hankali ya tura kofar dakin ya shiga sai ya same ta zaune karbi rike a hannunta tana ja, idanuwanta sanye da farin gilashi. Cire gilashin tai tana kallonsa da idanuwanta da bata iya gani sosai da su saboda kukan da take a kullum yana taba idonta. Kusa da ita ya zauna yana kallon kofin tea dake aljihun gadon.

“Wata kila tea din nan kawai kika saka a cikinki?”

Ta dan yi murmushin karfin hali.

“Kasan bana iya cin abu mai nauyi Talba”

“Momy miyasa mike ta damuwa da Leila ne kawai? Kin manta kina da ni da Amal da Kabir? Dukanmu ba zamu iya jurewa idan wani abun ya same ki, and Leila ma ba zata jidadi ba idan ta san irin wannan halin kike, dubi yadda kika rame, me kike son mu yi ne Momy? Why not ki barwa Allah komai”

“Na barwa Allah komai Talba, amman na kasa cire a abun a zuciyata, ko a mafarki ban tana tsammanin Leila zata yi rayuwar gidan yare ba, kuma ace mahaifinta yana a raye be yi komai ba dan ganin ya ceto rayuwarta”

“Idan kin barwa Allah to ki daina ganin laifin kowa, kuma ki yi ta godiya ga Allah kina neman yafiyarsa”

“Ina ta yi Talba, ina ta kokarin ganin al'amurra sun daidaita ko dan saboda ku, kawai dai na kasa cire abun a raina ne, kuma ina ta jin tsoro ina ganin kamar kashe Leila za'ayi”

Ya matsa kusa da ita ya rumgumeta, irin rumguma ta ďa da uwa, domin ta ba shi tausayi matuka.

“Duk yadda Allah ya tsara haka zai kasance, ki saka wannan a ranki, kuma ki daure ki rika cin abinci dan Allah Momy”

Ya tsagaita hawayen da take.

“Allah ya maka albarka Talba”

“Ameen”

Ya amsa yana jin kamar yayi kuka, domin har ga Allah baya son damuwar Momy musamman irin wannan da ba asan ranar da zata daina ba.

Wannan karon har da yan jaridu na social media da kuma na newspaper. Daddy ba jidadin hakan ba sai dai babu yadda ya iya domin aikinsu suke yi kuma da Leila bata aikata ba da basu mata haka ba. A wannan ranar kam Leila ta rufe fuskarta da mayafinta ta zauna a inda aka tanadar mata kusa da lawyer dake tare da rakiyar duka lawyers din chamber su. An gabatar da shari'a biyu kamin ayi ta Leila, kasancewar Lauyer kwararen ya gabatar da da kansa a matsayin lauyan da zai tsaya mata. Sannan aka shiga cikin shari'ar. Iyakacin abun da Lauyer yake nunawa Leila ta aikata hakan ne a kan kuskure, wanda hakan ya bawa Lauyan gwanati karyata ta shi da nashi hujojin. Daga karshe Barrister Fatihu ya nemi a bada belin Leila sai dai hakan be samu ba, alkali yayi duba da laifin data aikata ya sake bada umarni tsareta a gidan kaso.
A ranar ma Momy ta dawo gida cikin wani irin yanayi mai wuyar fassara, domin jikinta a kullum sanyi yake tana ganin kamar Leila ba zata samu sassaucin kotun ba, musamman lura da tai da yadda Alkalin yake da zafi.
Yan'uwan Baaba suka tafi gida cikin farinciki kamar wacan karon, domin suna ganin alamun kamar za ayi musu adalci.
Bayan sallah azahar Talba ya shigo dakin Momy domin dubata sai ya same ta zaune kasa tana ta jan carbi. Karaso yai kusa da ita ya zauna al'adarsa a yanzu duba lafiyarta safe rana dare. Kallonsa kawai tai ta sauke kai kasa ba tare da tace komai ba.

“Ina tunanin daina shan maganin nan zaki yi ma Momy kar yaje ya sama miki matsala”

Ta kalleshi sai dai bata ce komai ba har lokacin, fatar idonta har wani baki tai saboda bakinciki da kuka.

“Kina ji lokacin da Kabir ya fada miki cewar shan magani da kike ba zai amfana miki komai ba matukar baki daina tunani ba, haba Momy kalli yadda kika rame abinci ma baki iya ci, kullum sai kuka da tunanin Leila, ba laifi ba ne tunaninta amman zaki iya kamuwa da wani ciwon kin ga an yi ba ayi ba kenan”

“Ina ta kokari amman na kasa, ji nake kamar na mutu na huta Talba, zuciyata har wani zafi take”

Ta fashe da kuka sosai jikinta na rawa.

“Komai zai wuce Momy, ake rasa rai ma a hakura balle ke da Leila take a raye, kuma ina kyautata zaton zata dawo gareki”

“Ban ga alamar hakan ba, tun da gashi ko belinta sun ki bada ba”

“Ba daga nan take ba, Alkali yana bada beli ne idan ya gamsu da hujojin da aka bashi da kuma duba da yanayin shari'ar, Leila tana amsa laifinta a duk inda aka je, kin ga bata wahalar da kotu ba kuma hakan ya nuna ta yi nadama duk kotu zata duba wannan kamin yanke hukunci”

“Allah ya sa hakan ya kasance”

“Ameen, bari na kawo miki wani abu ki ci dan Allah”

Ya mike tsaye sai ta kalleshi tana jinsa kamar dan cikinta, domin kulawar da yake bata da nuna mata damuwarsa ko Kabir da yake danta baya mata shi.

“Ina Aminatu?”

Ta fada a yayinda ya kusa isa gurin kofar dakin, sai ya juyo da sauri ya kalli Momy cikin tsananin mamaki yana kokarin tantancewa ko dai be ji daidai ba ne. Sai dai murmushin daya gani a fuskarta tare da hawaye ya tabbatar masa da muryarta ya ji.

“Tana Lafiya?”

Kallonta kawai yake kamar mai shawarar amsawa.

“Lafiyarta kalau Momy”

Ta daga masa kai, sai ya juya ya fita. Downstairs ya sauko ya dauki plate ya zuba mata abinci ya dora a tray ya shiga kitchen ya dauko lemu da cups da ruwa ya dora a tray sannan ya dauka ya nufi upstairs, yana kallom Kabir dake zaune a sofa yana waya da Rukaiya. Sannu sannu yake takowa har ya hauro sama ya shiga cikin dakin ya aje tray gabanta.

“Shimkafa da miya ne, kuma na san kina sonsa”

Ta kalli abincin sannan ta kalleshi.

“Kwanakin baya, Daddynka ya min magana akan matarka yace ya maka maganar tarewa ka nuna masa baka son na shiga damuwa, ka ce ya bari sai gaba”

Ya mika mata plate din abincin yana fadin.

“Ba yanzu ba Momy, muna cikin wannan hali be kamata Daddy yayi wannan maganar da ke ba”

“Amman yana da gaskiya Talba, za a iya daukar lokaci ba a gama shari'ar nan ba, ka ga mun shiga hakkinka da na matarka, karka dubi halin da nake ciki ka hana matarka tarewa a gidan ta, daman ance kana naka Allah na nashi, muna ta zancen aurenka da Leila sai gashi ka auri yarinyar nan, yanzu kuma ana son yin auren sai ga wannan abun ya faru, mu barwa Allah ikonsa mu yarda da kaddara kawai shi ya fi”

Da ya kalleta sai tausayinta ya rufeshi, ya sani da can ba son Aminatu take ba, saboda Leila a yanzu kuma ita da kanta take bashi damar tarewa da ita.

“Shikenan nan Momy zan duba”

“Dan Allah kai yi abun da mahaifinka yake bukata, na san na shiga hakkinku kai da matarka amman duk...”

“Shikenan Momy ki ci abincinki dan Allah, zan yi”

Ya share hawayenta kamar karamar yarinya ta fara kai abincin a baki tana taunawa duk kuwa da kasancewar ta daina jindadin abincin tun daga lokacin da wannan tashin hankalin ya sameta, sai rashin lafiya ga rama da yawan kuka kullum Leila na cikin ranta ga zullum shari'ar da ake bata san yadda karshen zai kasance ba.

FARUK POV.

Sannu Sannu alaka mai karfi ta shiga tsakaninsa da Ramla, har ya fara zuwa Lagos gurin aikinsa yana dawowa gida yayi weekend. Kullum sai ya kirata sun yi hira, idan kuma ya dawo week zai yi mata tsaraba duk kuwa da kasancewar ta nuna masa bata so.
A wani kamfanin siyar da motoci da koyar da tuki ya koyi yadda ake tukin motar, bayan ya kamalla suka ba shi certificate, ta waya ya dauki hoton ya turawa Ramla ta rika masa dariya wai ta ya sani ya bari ta koya masa ai ta iya.

“Ai ko yanzu dare be mana ba, kuma ba a kure lokaci ba”

“Aa yanzu ai ka rika ka je wani gurin ka koya, dan haka ni zan koya maka ba tun da an rigani”

“Ki ce duk abun da ya kwana baki cin dumame kenan?”

“Wani abun ba...”

Ta fada, sai yai dariya ya dauki chocolate ya kai bakinsa.

“Me kake ci?”

“Dan gidanki”

“Let me guess i chocolate”

“Yes kin koya min shansa yanzu, na zama kamar wani karamin yaro kullum sai na sha”

“Aa ni fa ba kai na koyawa ba, da na Sultan”

“Ke kika koya min mana, na lura yana cikin favorite dinki, shiyasa ni ma na ko yi ci, kar wata rana ki zo kina ci kina min kori”

Ta yi dariya mai sauti.

“Saboda Chocolate din?”

“Yes, Mama ta fada min duk wani abu da kike so na koyi sonsa, wanda kuma nake so na koya miki sonsa, idan kuma tsanarsa na yi to na koya miki yadda zaki kiyaye aikata abun so that mu samu zaman lafiya”

Ta yi murmushi mai sauti tana ta saurarensa. Sai kusan goma dare suka yi sallama, ba dan ya gaji ba sai dan baya son shiga hakkinta domin ya lura ta fara jin bachi.
Haka suke kullum sai yayi waya da ita da dare, idan kuma yana Gusau Saturday da Sunday yana gidansu sai goma na dare zai dawo. Wani lokacin zata shirya masa abun da ta san yana so ta tarbe shi da shi. Every weekend idan ya zo sai ya bawa Mama kudi ta siya masa wani abu ta aje tana ta tara masa kayan lefa masu kyau da tsada, idan kuma ba shi a gari aka kawo kudin shagon daya bude ya saka wani yaro yana siyar da kayan electric sai ta fada masa a waya ta shiga kasuwa ta siya masa tufafi masu tsada. Ita kanta a yanzu bata daura karamar atamfa sam ba zaki ganta a gidan ita da Rukaiya ba ki ce ita ce, sai ka dauka daman can masu rufi asirin ne. Wannan weekend din ta fi sauran da yake zuwa yi masa dadi domin zai zo ya nunawa Mama da Ramla motar daya siya ne, ba ta iso ba sai yanzu, sai dai be fada musu cewar motar ta iso ba, duk kuwa da irin tambayarsa da Mama take kullum har tana cewa Allah yasa mutumen be gudu masa da kudi ba. Karfe biyar na yamma ya sauka Gusau bayan ya baro Zaria garin daya yada zango ya huta bayan fitowarsa daga Lagos.
A bakin gate din gidan ya faka motar sannan ya bude ya fito da tsararba sa yai musu ya nufo cikin gidan rike da makullin motar da farinciki ya shigo, sai dai yana shiga falon na su da aka kawata da kayan alatu sai fuskarsa ta canja ya nemo farinciki ya rasa, sakamakon arba da yai da Baturiya tana zaune saman kujerar falon da aka kawata da kayan alatu tare da kanwarta, Sultan na zaune saman jikinsa ta rike hannunta kanta a kasa. Tana jin sallamarsa gabanta yayi mugun faduwa wata kalar kunya ta lullubeta sai ta ji da ma ace bata shigo ba.

“Yaya sannu da zuwa”

Rukaiya ta fada sai ya amsa, mata ya kalli mahaifiyarsa dake masa murmushi.

“Faruk ya hanya?”

“Alhamdulillah”

Da gangan ya share Sultan dake masa ayoyo yana saukowa jikin Baturiya ya nufo shi da gudu. Kanwarta gaishe shi sai ya amsa ya dauke kai ya nufi dakin Mama, sai da yai daf da shiga sai kuma ya juyo ya kalli Baturiya da har ta mike tsaye jikinta na rawa, domin bata san zai dawo ba a yanzu ba, domin ta san ba anan yake aiki ba, bayan Fahat ya fada mata ta fara bibiyar rayuwarsa har Ramla da yake da nufin aure ta sani a yanzu.

“Me kika zo yi nan Rafi'ah”

Kamin ta amsa masa Mama ta ce.

“Aa waje ta tsaya ta ce a kira mata Sultan ta ganshi ni na aika na ce ta shigo cikin gidan”

Faruk ya kalleta cike da rashin jindadi abun da Mama tai ya ce.

“Saboda me Mama?”

“Saboda mahaifiyarsa”

Mama ta amsa masa tana mikewa tsaye, be sake cewa komai ba ya shige dakin nata ta bi bayansa. Baturiya ta fito da sauri ko sallama bata tsaya yi ma Mama ba, Rukaiya da bita da harara tana tabe baki, daman bata so shigowarta cikin gidan ba saboda kawai Mama ta ce ta kira ta ta shiga ciki ne wai kar ta a fitar mata da Sultan din a waje ta dauke shi ta tafi da shi. Sauri kawai take zubawa gumi na tarar mata a hijab har ta fito gate din, tsaye tai cak tana kallon sabuwar motar Faruk, ko ba a fada mata ba ta san motarsa ce domin ya faka ta daf da gate din gidan wanda ke nuna alamar cikin gidan yake da niyar shiga da ita, wani abu ta hade da karfi sannan ta bi bayan kanwarta wanda tai nesa tana tafiya saboda haushin shiga gidan da sukai daman ita bata so suka shiga ba. Tafiya Baturiya take tana waigen motar kamar wanda bata son tafiya, bata hankaro ba ta ji sanyin hawaye a kumatunta. Hannu ta saka ta share hawayen da sauri ta cira kafa tana tafiyar sauri sai dai duk da haka bata cin ma kanwarta tuni ta tari abun hawa ta hau ta yi gaba ta bar Baturiya a nan. A kafa ta rika takawa har ta isa wata unguwa dake kusa da unguwar wani dan guri ta samu ta zauna tana hawaye. Wani irin bakinciki take ji wanda bata taba jinsa a rayuwarta, ta dade zaune a gurin tana ta aikin kuka kamar wanda akai ma mutuwa. Sai dai abun da bata sani ba tun a lokacin da take tafiya a kafa wani mutumen yana biye da ita da motar har ta iso gurin ta zauna tana aikin kuka. Matashi ne da ba zai rasa mata daya da yara biyu ko uku ba, yana zaune cikin motarsa nesa da ita sai dai ba sosai. Ganin kukan nata ba mai karewa ba ne ya bude motar ya fito ya zari tissue ya nufo inda take zaune. Zuwa yai gefenta ya tsaya yana kallon harabar da take kallo.

“Hey pretty kina kukan rashi ne?”

Ta dago ta kalleshi a hankali still hawaye na sauko mata.

“Ka san zafin rashin wani ne?”

Sai a lokacin ya kalleta.

“Yeah zafi na rashi i lost my son zafi rabuwa i lost my wife”

Wani sabon kuka ya zo mata

“Kuma abun nan akwai bakinciki sosai”

“Sosai ma”

Ya furta da muryar dake nuna tsantsar bakincikinsa, yana kallon wani gurin dabam tsabanin ita da take kallonsa, sai kuma yai murmushi mai kyau ya kalleta.

“Fada min wa kika rasa?”

Ta yi kasa da kanta hawaye na sauko mata.

“Wani ne, mai kyakkyawar zuciya, mai kyakkyawar makoma, mai kyakkyawar fuska amman na rasa shi...!”

Ya mika mata tissue dake boye a hannunsa, sai da ta kalli tissue din sannan ta karba.

“Ya mutu ne?”

Ta share hawayenta.

“A idanuwana ya mutu domin na rasa shi har abada, amman a zuciyata rayayye ne har abada”

Ya zauna kusa da ita yana kallon kyakkyawar fuskarta wanda taja shi zuwa gareta.

“Did you he break ur heart?”

Ta girgiza kai.

“No i break his heart, yana so na nima ina sonsa, amman kaddara ta raba mu”

“Mijinki ne?”

Ta kalleshi kamar zata amsa masa, sai kuma ta ga babu dalilin yin haka ga mutumen da bata sani ba be santa ba. Mikewa tai tsaye.

“Zan tafi gida”

Sai shi ma ya mike tsaye.

“Da zaki ba ni dama da na saukeki gidan”

Ta girgiza masa kai ta fara takawa tana tafiya.

“Please, akwai abun da nake son fada miki”

Ta tsaya sai kuma ta juyo ta kalleshi sai yai mata alama da motarsa, sannan ya jera da ita suka nufi motar da kansa ya bude mata ta shiga sannan shi ma ya shiga driver seat yai ma motar key. Suna tafe yana mata hira yana kokarin kwantar mata da hankali, ciki har da gabatar masa da kanshi da yayi sai dai gaba daya hankalinta baya kansa yana can gurin faruk tana mamakin yadda rayuwa ta sauya shi ita kuma kaddarar ta canja ta duniya tai mata juyin masa, ta rasa Faruk ta rasa Fahat, gashi yanzu Faruk yayi kudin da take da buri amman a tare da ita ba. Kamar marar lafiya haka ta shiga cikin gidan. tana sai ta samu Umma zaune tana gyaran shimkafa suna hada ido Umma ta banko mata wata uwar harara.

“Sai yanzu kika ga damar dawowa? Allah yasa ba tsayawa kika yi magana da Faruk din ba”

Ta zauna a bakin kofar falon ba tace komai ba.

“Wai dan baki da kunya har ki dauki kafa ki shiga cikin gidan Faruk? Miya kai ki bi ta kofar gidan ma?”

“Mun fito gidansu Anty Halira ne, sai muka biyo ta kofar gidan, na aika yaro a kira min Sultan sai Mama ta dage sai na shigo ciki”

“Sai kuma kika shiga saboda baki da zuciya”

“Saboda Sultan na shiga Umma, yanzu ba ni da kamar da na”

“Allah yasa dai ba zawarcin Faruk kike ba, abun da kafi karfi ka koma kana shimshina”

Bata ce komai ba ta tashi ta shiga ciki dakin tana jin ranta ba dadi.

*** *** ***

“Mama saboda me zaki mata izinin shigowa cikin gidan nan?”

Mama ta zauna kusa da shi tana murmushi.

“Faruk idan wani abun ya wuce, a bar shi ya wuce har a bada, ita kanta a yanzu ta san ka mata nisa, kuma babu yadda zaka yi ka yanke alakar uwa da danta, zuwan ta gidan nan baya nuna komai sai nadama wanda ke haifar da dana sani, da can ai bata kula da Sultan din ba, sai yanzu ta zo kofar gida ta aiko a kira mata shi ta ganshi amaimakon na tura mata shi can waje sai na zabi ta shiga saboda ban san abun da zai faru ba idan suka tsaya a wajen, daker ma ta shigo cikin gidan baka ga farincikin da yaron nan yake ba da yai arba da mahaifiyarsa”

“Duk da haka dai, bana son zuwanta gidan nan, da kin san yadda na tsani ganin fuskar Rafi'a Wallahi da ko mai sunanta ba zaki kira ba a kusa da ni”

“Abun da ya wuce ai ya wuce, sai ka gode Allah gashi ta zo ta ganka a yadda ba ta yi zato ba, ta guje ka saboda talauci yanzu gashi Allah ya rufa maka asiri, kuma ya baka mata mai wanda ta fita kyau ta fita asali kuma yar manyan mutane, ya baka aiki ni kaina da nake mahaifiyarka ina zaune a gida mai kyau, kuma baka san me Allah ya tanadar maka gaba ba nan gaba”

Ya sauke ajiyar zuciya.

“Haka ne, amman bana son ganinta kusa da dana sai idan ya zama dole”

“Ai yanzu idan kai aure ya samu wata uwar zai samu kwanciyar hankali fiye da yanzu kuma zai ji sanyi, fatana dai Allah yasa ta rika shi kamar danta, soyayyar da take nuna masa a yanzu Allah yasa ta nuna masa shi idan ta shigo”

“Ameen, na zo da mota waje”

Mama ta wara ido.

“Motar waye?”

“Tawa, motar da kika ta jira ta zo”

Ya fada yana murmushi, Mama ta fito dakin da sauri tana fadawa Rukaiya shi kuma ya rika hannun Sultan suka fito tare. Mama ta riga Rukaiya fita waje gurin ganin motar farincikin da ya lullube zuciyarsu da fuskarsu marar misaltuwa ne. Rukaiyah bata san lokacin san lokacin data rumgume yayanta ba tana murna, Sultan ma da yake karami murna ya rika yi yana ta tsalla, a daren ba su kwana ba sai da Faruk ya saka su mota ya zagaya gari da su cikin motar suka je har gidan kanwarsa wato yayar Rukaiyah. Bayan ya dawo da su gida ya shirya cikin wasu tufafin ya fesa turare sosai sannan ya shiga motar ya dauki hanyar gidansu masoyiyyarsa Ramla.

Wannan karon har da yan jaridu na social media da kuma na newspaper. Daddy ba jidadin hakan ba sai dai babu yadda ya iya domin aikinsu suke yi kuma da Leila bata aikata ba da basu mata haka ba. A wannan ranar kam Leila ta rufe fuskarta da mayafinta ta zauna a inda aka tanadar mata kusa da lawyer dake tare da rakiyar duka lawyers din chamber su. An gabatar da shari'a biyu kamin ayi ta Leila, kasancewar Lauyer kwararen ya gabatar da da kansa a matsayin lauyan da zai tsaya mata. Sannan aka shiga cikin shari'ar. Iyakacin abun da Lauyer yake nunawa Leila ta aikata hakan ne a kan kuskure, wanda hakan ya bawa Lauyan gwanati karyata ta shi da nashi hujojin. Daga karshe Barrister Fatihu ya nemi a bada belin Leila sai dai hakan be samu ba, alkali yayi duba da laifin data aikata ya sake bada umarni tsareta a gidan kaso.
A ranar ma Momy ta dawo gida cikin wani irin yanayi mai wuyar fassara, domin jikinta a kullum sanyi yake tana ganin kamar Leila ba zata samu sassaucin kotun ba, musamman lura da tai da yadda Alkalin yake da zafi.
Yan'uwan Baaba suka tafi gida cikin farinciki kamar wacan karon, domin suna ganin alamun kamar za ayi musu adalci.
Bayan sallah azahar Talba ya shigo dakin Momy domin dubata sai ya same ta zaune kasa tana ta jan carbi. Karaso yai kusa da ita ya zauna al'adarsa a yanzu duba lafiyarta safe rana dare. Kallonsa kawai tai ta sauke kai kasa ba tare da tace komai ba.

“Ina tunanin daina shan maganin nan zaki yi ma Momy kar yaje ya sama miki matsala”

Ta kalleshi sai dai bata ce komai ba har lokacin, fatar idonta har wani baki tai saboda bakinciki da kuka.

“Kina ji lokacin da Kabir ya fada miki cewar shan magani da kike ba zai amfana miki komai ba matukar baki daina tunani ba, haba Momy kalli yadda kika rame abinci ma baki iya ci, kullum sai kuka da tunanin Leila, ba laifi ba ne tunaninta amman zaki iya kamuwa da wani ciwon kin ga an yi ba ayi ba kenan”

“Ina ta kokari amman na kasa, ji nake kamar na mutu na huta Talba, zuciyata har wani zafi take”

Ta fashe da kuka sosai jikinta na rawa.

“Komai zai wuce Momy, ake rasa rai ma a hakura balle ke da Leila take a raye, kuma ina kyautata zaton zata dawo gareki”

“Ban ga alamar hakan ba, tun da gashi ko belinta sun ki bada ba”

“Ba daga nan take ba, Alkali yana bada beli ne idan ya gamsu da hujojin da aka bashi da kuma duba da yanayin shari'ar, Leila tana amsa laifinta a duk inda aka je, kin ga bata wahalar da kotu ba kuma hakan ya nuna ta yi nadama duk kotu zata duba wannan kamin yanke hukunci”

“Allah ya sa hakan ya kasance”

“Ameen, bari na kawo miki wani abu ki ci dan Allah”

Ya mike tsaye sai ta kalleshi tana jinsa kamar dan cikinta, domin kulawar da yake bata da nuna mata damuwarsa ko Kabir da yake danta baya mata shi.

“Ina Aminatu?”

Ta fada a yayinda ya kusa isa gurin kofar dakin, sai ya juyo da sauri ya kalli Momy cikin tsananin mamaki yana kokarin tantancewa ko dai be ji daidai ba ne. Sai dai murmushin daya gani a fuskarta tare da hawaye ya tabbatar masa da muryarta ya ji.

“Tana Lafiya?”

Kallonta kawai yake kamar mai shawarar amsawa.

“Lafiyarta kalau Momy”

Ta daga masa kai, sai ya juya ya fita. Downstairs ya sauko ya dauki plate ya zuba mata abinci ya dora a tray ya shiga kitchen ya dauko lemu da cups da ruwa ya dora a tray sannan ya dauka ya nufi upstairs, yana kallom Kabir dake zaune a sofa yana waya da Rukaiya. Sannu sannu yake takowa har ya hauro sama ya shiga cikin dakin ya aje tray gabanta.

“Shimkafa da miya ne, kuma na san kina sonsa”

Ta kalli abincin sannan ta kalleshi.

“Kwanakin baya, Daddynka ya min magana akan matarka yace ya maka maganar tarewa ka nuna masa baka son na shiga damuwa, ka ce ya bari sai gaba”

Ya mika mata plate din abincin yana fadin.

“Ba yanzu ba Momy, muna cikin wannan hali be kamata Daddy yayi wannan maganar da ke ba”

“Amman yana da gaskiya Talba, za a iya daukar lokaci ba a gama shari'ar nan ba, ka ga mun shiga hakkinka da na matarka, karka dubi halin da nake ciki ka hana matarka tarewa a gidan ta, daman ance kana naka Allah na nashi, muna ta zancen aurenka da Leila sai gashi ka auri yarinyar nan, yanzu kuma ana son yin auren sai ga wannan abun ya faru, mu barwa Allah ikonsa mu yarda da kaddara kawai shi ya fi”

Da ya kalleta sai tausayinta ya rufeshi, ya sani da can ba son Aminatu take ba, saboda Leila a yanzu kuma ita da kanta take bashi damar tarewa da ita.

“Shikenan nan Momy zan duba”

“Dan Allah kai yi abun da mahaifinka yake bukata, na san na shiga hakkinku kai da matarka amman duk...”

“Shikenan Momy ki ci abincinki dan Allah, zan yi”

Ya share hawayenta kamar karamar yarinya ta fara kai abincin a baki tana taunawa duk kuwa da kasancewar ta daina jindadin abincin tun daga lokacin da wannan tashin hankalin ya sameta, sai rashin lafiya ga rama da yawan kuka kullum Leila na cikin ranta ga zullum shari'ar da ake bata san yadda karshen zai kasance ba.

FARUK POV.

Sannu Sannu alaka mai karfi ta shiga tsakaninsa da Ramla, har ya fara zuwa Lagos gurin aikinsa yana dawowa gida yayi weekend. Kullum sai ya kirata sun yi hira, idan kuma ya dawo week zai yi mata tsaraba duk kuwa da kasancewar ta nuna masa bata so.
A wani kamfanin siyar da motoci da koyar da tuki ya koyi yadda ake tukin motar, bayan ya kamalla suka ba shi certificate, ta waya ya dauki hoton ya turawa Ramla ta rika masa dariya wai ta ya sani ya bari ta koya masa ai ta iya.

“Ai ko yanzu dare be mana ba, kuma ba a kure lokaci ba”

“Aa yanzu ai ka rika ka je wani gurin ka koya, dan haka ni zan koya maka ba tun da an rigani”

“Ki ce duk abun da ya kwana baki cin dumame kenan?”

“Wani abun ba...”

Ta fada, sai yai dariya ya dauki chocolate ya kai bakinsa.

“Me kake ci?”

“Dan gidanki”

“Let me guess i chocolate”

“Yes kin koya min shansa yanzu, na zama kamar wani karamin yaro kullum sai na sha”

“Aa ni fa ba kai na koyawa ba, da na Sultan”

“Ke kika koya min mana, na lura yana cikin favorite dinki, shiyasa ni ma na ko yi ci, kar wata rana ki zo kina ci kina min kori”

Ta yi dariya mai sauti.

“Saboda Chocolate din?”

“Yes, Mama ta fada min duk wani abu da kike so na koyi sonsa, wanda kuma nake so na koya miki sonsa, idan kuma tsanarsa na yi to na koya miki yadda zaki kiyaye aikata abun so that mu samu zaman lafiya”

Ta yi murmushi mai sauti tana ta saurarensa. Sai kusan goma dare suka yi sallama, ba dan ya gaji ba sai dan baya son shiga hakkinta domin ya lura ta fara jin bachi.
Haka suke kullum sai yayi waya da ita da dare, idan kuma yana Gusau Saturday da Sunday yana gidansu sai goma na dare zai dawo. Wani lokacin zata shirya masa abun da ta san yana so ta tarbe shi da shi. Every weekend idan ya zo sai ya bawa Mama kudi ta siya masa wani abu ta aje tana ta tara masa kayan lefa masu kyau da tsada, idan kuma ba shi a gari aka kawo kudin shagon daya bude ya saka wani yaro yana siyar da kayan electric sai ta fada masa a waya ta shiga kasuwa ta siya masa tufafi masu tsada. Ita kanta a yanzu bata daura karamar atamfa sam ba zaki ganta a gidan ita da Rukaiya ba ki ce ita ce, sai ka dauka daman can masu rufi asirin ne. Wannan weekend din ta fi sauran da yake zuwa yi masa dadi domin zai zo ya nunawa Mama da Ramla motar daya siya ne, ba ta iso ba sai yanzu, sai dai be fada musu cewar motar ta iso ba, duk kuwa da irin tambayarsa da Mama take kullum har tana cewa Allah yasa mutumen be gudu masa da kudi ba. Karfe biyar na yamma ya sauka Gusau bayan ya baro Zaria garin daya yada zango ya huta bayan fitowarsa daga Lagos.
A bakin gate din gidan ya faka motar sannan ya bude ya fito da tsararba sa yai musu ya nufo cikin gidan rike da makullin motar da farinciki ya shigo, sai dai yana shiga falon na su da aka kawata da kayan alatu sai fuskarsa ta canja ya nemo farinciki ya rasa, sakamakon arba da yai da Baturiya tana zaune saman kujerar falon da aka kawata da kayan alatu tare da kanwarta, Sultan na zaune saman jikinsa ta rike hannunta kanta a kasa. Tana jin sallamarsa gabanta yayi mugun faduwa wata kalar kunya ta lullubeta sai ta ji da ma ace bata shigo ba.

“Yaya sannu da zuwa”

Rukaiya ta fada sai ya amsa, mata ya kalli mahaifiyarsa dake masa murmushi.

“Faruk ya hanya?”

“Alhamdulillah”

Da gangan ya share Sultan dake masa ayoyo yana saukowa jikin Baturiya ya nufo shi da gudu. Kanwarta gaishe shi sai ya amsa ya dauke kai ya nufi dakin Mama, sai da yai daf da shiga sai kuma ya juyo ya kalli Baturiya da har ta mike tsaye jikinta na rawa, domin bata san zai dawo ba a yanzu ba, domin ta san ba anan yake aiki ba, bayan Fahat ya fada mata ta fara bibiyar rayuwarsa har Ramla da yake da nufin aure ta sani a yanzu.

“Me kika zo yi nan Rafi'ah”

Kamin ta amsa masa Mama ta ce.

“Aa waje ta tsaya ta ce a kira mata Sultan ta ganshi ni na aika na ce ta shigo cikin gidan”

Faruk ya kalleta cike da rashin jindadi abun da Mama tai ya ce.

“Saboda me Mama?”

“Saboda mahaifiyarsa”

Mama ta amsa masa tana mikewa tsaye, be sake cewa komai ba ya shige dakin nata ta bi bayansa. Baturiya ta fito da sauri ko sallama bata tsaya yi ma Mama ba, Rukaiya da bita da harara tana tabe baki, daman bata so shigowarta cikin gidan ba saboda kawai Mama ta ce ta kira ta ta shiga ciki ne wai kar ta a fitar mata da Sultan din a waje ta dauke shi ta tafi da shi. Sauri kawai take zubawa gumi na tarar mata a hijab har ta fito gate din, tsaye tai cak tana kallon sabuwar motar Faruk, ko ba a fada mata ba ta san motarsa ce domin ya faka ta daf da gate din gidan wanda ke nuna alamar cikin gidan yake da niyar shiga da ita, wani abu ta hade da karfi sannan ta bi bayan kanwarta wanda tai nesa tana tafiya saboda haushin shiga gidan da sukai daman ita bata so suka shiga ba. Tafiya Baturiya take tana waigen motar kamar wanda bata son tafiya, bata hankaro ba ta ji sanyin hawaye a kumatunta. Hannu ta saka ta share hawayen da sauri ta cira kafa tana tafiyar sauri sai dai duk da haka bata cin ma kanwarta tuni ta tari abun hawa ta hau ta yi gaba ta bar Baturiya a nan. A kafa ta rika takawa har ta isa wata unguwa dake kusa da unguwar wani dan guri ta samu ta zauna tana hawaye. Wani irin bakinciki take ji wanda bata taba jinsa a rayuwarta, ta dade zaune a gurin tana ta aikin kuka kamar wanda akai ma mutuwa. Sai dai abun da bata sani ba tun a lokacin da take tafiya a kafa wani mutumen yana biye da ita da motar har ta iso gurin ta zauna tana aikin kuka. Matashi ne da ba zai rasa mata daya da yara biyu ko uku ba, yana zaune cikin motarsa nesa da ita sai dai ba sosai. Ganin kukan nata ba mai karewa ba ne ya bude motar ya fito ya zari tissue ya nufo inda take zaune. Zuwa yai gefenta ya tsaya yana kallon harabar da take kallo.

“Hey pretty kina kukan rashi ne?”

Ta dago ta kalleshi a hankali still hawaye na sauko mata.

“Ka san zafin rashin wani ne?”

Sai a lokacin ya kalleta.

“Yeah zafi na rashi i lost my son zafi rabuwa i lost my wife”

Wani sabon kuka ya zo mata

“Kuma abun nan akwai bakinciki sosai”

“Sosai ma”

Ya furta da muryar dake nuna tsantsar bakincikinsa, yana kallon wani gurin dabam tsabanin ita da take kallonsa, sai kuma yai murmushi mai kyau ya kalleta.

“Fada min wa kika rasa?”

Ta yi kasa da kanta hawaye na sauko mata.

“Wani ne, mai kyakkyawar zuciya, mai kyakkyawar makoma, mai kyakkyawar fuska amman na rasa shi...!”

Ya mika mata tissue dake boye a hannunsa, sai da ta kalli tissue din sannan ta karba.

“Ya mutu ne?”

Ta share hawayenta.

“A idanuwana ya mutu domin na rasa shi har abada, amman a zuciyata rayayye ne har abada”

Ya zauna kusa da ita yana kallon kyakkyawar fuskarta wanda taja shi zuwa gareta.

“Did you he break ur heart?”

Ta girgiza kai.

“No i break his heart, yana so na nima ina sonsa, amman kaddara ta raba mu”

“Mijinki ne?”

Ta kalleshi kamar zata amsa masa, sai kuma ta ga babu dalilin yin haka ga mutumen da bata sani ba be santa ba. Mikewa tai tsaye.

“Zan tafi gida”

Sai shi ma ya mike tsaye.

“Da zaki ba ni dama da na saukeki gidan”

Ta girgiza masa kai ta fara takawa tana tafiya.

“Please, akwai abun da nake son fada miki”

Ta tsaya sai kuma ta juyo ta kalleshi sai yai mata alama da motarsa, sannan ya jera da ita suka nufi motar da kansa ya bude mata ta shiga sannan shi ma ya shiga driver seat yai ma motar key. Suna tafe yana mata hira yana kokarin kwantar mata da hankali, ciki har da gabatar masa da kanshi da yayi sai dai gaba daya hankalinta baya kansa yana can gurin faruk tana mamakin yadda rayuwa ta sauya shi ita kuma kaddarar ta canja ta duniya tai mata juyin masa, ta rasa Faruk ta rasa Fahat, gashi yanzu Faruk yayi kudin da take da buri amman a tare da ita ba. Kamar marar lafiya haka ta shiga cikin gidan. tana sai ta samu Umma zaune tana gyaran shimkafa suna hada ido Umma ta banko mata wata uwar harara.

“Sai yanzu kika ga damar dawowa? Allah yasa ba tsayawa kika yi magana da Faruk din ba”

Ta zauna a bakin kofar falon ba tace komai ba.

“Wai dan baki da kunya har ki dauki kafa ki shiga cikin gidan Faruk? Miya kai ki bi ta kofar gidan ma?”

“Mun fito gidansu Anty Halira ne, sai muka biyo ta kofar gidan, na aika yaro a kira min Sultan sai Mama ta dage sai na shigo ciki”

“Sai kuma kika shiga saboda baki da zuciya”

“Saboda Sultan na shiga Umma, yanzu ba ni da kamar da na”

“Allah yasa dai ba zawarcin Faruk kike ba, abun da kafi karfi ka koma kana shimshina”

Bata ce komai ba ta tashi ta shiga ciki dakin tana jin ranta ba dadi.

*** *** ***

“Mama saboda me zaki mata izinin shigowa cikin gidan nan?”

Mama ta zauna kusa da shi tana murmushi.

“Faruk idan wani abun ya wuce, a bar shi ya wuce har a bada, ita kanta a yanzu ta san ka mata nisa, kuma babu yadda zaka yi ka yanke alakar uwa da danta, zuwan ta gidan nan baya nuna komai sai nadama wanda ke haifar da dana sani, da can ai bata kula da Sultan din ba, sai yanzu ta zo kofar gida ta aiko a kira mata shi ta ganshi amaimakon na tura mata shi can waje sai na zabi ta shiga saboda ban san abun da zai faru ba idan suka tsaya a wajen, daker ma ta shigo cikin gidan baka ga farincikin da yaron nan yake ba da yai arba da mahaifiyarsa”

“Duk da haka dai, bana son zuwanta gidan nan, da kin san yadda na tsani ganin fuskar Rafi'a Wallahi da ko mai sunanta ba zaki kira ba a kusa da ni”

“Abun da ya wuce ai ya wuce, sai ka gode Allah gashi ta zo ta ganka a yadda ba ta yi zato ba, ta guje ka saboda talauci yanzu gashi Allah ya rufa maka asiri, kuma ya baka mata mai wanda ta fita kyau ta fita asali kuma yar manyan mutane, ya baka aiki ni kaina da nake mahaifiyarka ina zaune a gida mai kyau, kuma baka san me Allah ya tanadar maka gaba ba nan gaba”

Ya sauke ajiyar zuciya.

“Haka ne, amman bana son ganinta kusa da dana sai idan ya zama dole”

“Ai yanzu idan kai aure ya samu wata uwar zai samu kwanciyar hankali fiye da yanzu kuma zai ji sanyi, fatana dai Allah yasa ta rika shi kamar danta, soyayyar da take nuna masa a yanzu Allah yasa ta nuna masa shi idan ta shigo”

“Ameen, na zo da mota waje”

Mama ta wara ido.

“Motar waye?”

“Tawa, motar da kika ta jira ta zo”

Ya fada yana murmushi, Mama ta fito dakin da sauri tana fadawa Rukaiya shi kuma ya rika hannun Sultan suka fito tare. Mama ta riga Rukaiya fita waje gurin

ganin motar farincikin da ya lullube zuciyarsu da fuskarsu marar misaltuwa ne. Rukaiyah bata san lokacin san lokacin data rumgume yayanta ba tana murna, Sultan ma da yake karami murna ya rika yi yana ta tsalla, a daren ba su kwana ba sai da Faruk ya saka su mota ya zagaya gari da su cikin motar suka je har gidan kanwarsa wato yayar Rukaiyah. Bayan ya dawo da su gida ya shirya cikin wasu tufafin ya fesa turare sosai sannan ya shiga motar ya dauki hanyar gidansu masoyiyyarsa Ramla.

Goyon bayan daya samu gurin Momy ya saka ya maida hankalinsa gurin tarewar matarsa duk wani abu daya kamata ayi mata ya cire kudi mai yawa ya ba Hajiya Laraba a siya mata komai. Furniture masu kyau masu tsada aka zuba mata a gidan bayan an yi masa sabon fenti.
Aka zuba kujeru masu kyau a falon da blue curtains kamar kujerum falon, plama ma da aka saka mata abar kallo ce. Kayan kitchen ma sai abun da Hajiya Labara ta manta bata siye ba, har wanda bata taba gani ba aai da Hajiya Laraba ta siya mata saboda Talba ya bata kudi enough. A cikin kudin ta diba ta Yar gidan mai fata ta kara mata wani gyaran a saman wacan da akai. Kusan komai da akai ma Aminatu tare Hajiya Laraba tai da matar yayarta, kuma duk abun da zata yi sai ta yi shawara da Bashir.
Within two weeks aka zuba komai a gidan aka kawata shi da kayan alatu, sai ka rantse da Allah yar wani babban mutum Talba ya aura mai kudi, saboda dukiyar da aka zuba a gidan, dinning table dinta ma abun kallo ne. Balle kuma Bedroom dinta, da aka kawata da fafaren furniture, Talba kuma akai masa dakinsa daban sai gadon dake dakinsa aka saka shi a dakin visitors. Shi kansa da ya shiga duba gidan sai ya ganshi kamar ba nashi ba. Daman can gidan an tsara sji a fasali mai kyau balle kuma yanzu da a kawata shi da kaya. Sai da ya gama duba ko'ina sannan yayi recording gidan da wayarsa. Yana barin gidan ya nufi gidansu Hajiya Laraba, sai da ya shiga ciki ya gaisa da ita sannan ya fito, kamar Kullum Aminatu ta biyo shi da sunan sallama, a nan yake nuna mata gidan a wayarsa annashuwar da ya gani a fuskarta ya saka shi jindadi, daman a yanzu ba shi da burin daya wuce ganin farincikinta.
A week later Hajiya Laraba da Matar yayanta da wasu abokan Hajiya Laraba suka dauki Aminatu zuwa gidanta, bayan an yi mata nasiha sosai, bayan sun yi musu addu'a aka dora da yi ma Talba tasa nasihar sannan suka fito suka baro musu gidan. Sai da Talba ya ji kara ruge gate din da sabon mai gadinsu yai sannan ya matsa kusa da matarsa sosai ya saka hannu ya bude mayafinta, sai yai arba da fuskarta dake dauke da hawaye, da ita kanta bata san na minene farincikin auren mutumen dake sonta kuma ya san kimarta? Ko kuma na ganin ranar da zata tare a gidan mijinta ba tare da uwa da uba ba? Dukawa yai ya leki fuskarta dake cike da kwalliya idanuwanta a lumshe. Sai ya saita goshinsa ya hade shi da nata ya rika hannunta ya saka yatsunsa cikin nata, yana ta kallon fuskarta ita kuma tana tana maida numfashi da numfashinsa da suke musanya yana shakar nata tana shakar nasa. Dauke kansa yai ya rumgume ta jikinsa yana murmushi.

“Alhamdulillahi Rabbil Alamin”

Ta kara lumshe idon gabanta na bugawa da karfi.

“Zamu je mu gaishe da Daddy da Momy yanzu kin ji?”

Ta yi shiru kamar ba zata ce komai ba jin ya ambaci Momy, domin ta san yadda ta tsane ta balle kuma yanzu da tare kuma yarta na gidan yari.

“Ba zata maka fada ba?”

Muryarta ta fita a hankali. Yayi murmushi yana shafa bayanta a hankali.

“Zata min fada mana, zata ce Talba miyasa baka tare da kyakkyawar matarka tuntuni ba sai yanzu?”

“Ko kuma tace miyasa ka tare yanzu ba...”

Ta fada a shagwabe, sai ya kai hannunsa ya lalaba kunnenta ya ja kadan.

“Kunnen ki ba ya ji daidai, Momy ba zata ce haka ba”

“Na san ai bata so na”

Ya dagota jikinsa yana kallon fuskarta kamar yadda take kallonsa.

“Wannan da ne, a yanzu Momy bata da damuwar data wuce ta Leila, ita da kanta ta bukaci na tare da ke, kin ga kuwa da tana tsanarki har yanzu ai ba zata yi haka ba”

“Da gaske”

Ya ja hancinta.

“Na taba miki karya?”

Ta girgiza masa kai alamar aa sannan ta maida kanta jikina.

“Tashi muje mu gaishe su”

Ta daga jikinsa ta mike tsaye shi ma tsaye ya mike ya rika hannunta zuwa bedroom sannan ya shiga da ita bathroom din dake dakin da kansa ya wanke mata kwaliyar dake fuskarta sannan ya juyo ya ita yana kallonta.

“A haka ma kin fi kyau”

Ta yi murmushi ta sauke kanta kasa, yau dai kam tana jin kunyarsa fiye da kullum wata kila saboda kusancinsu ya karu ne fiye da, ga kuma kimarsa data cika mata ido. Bata hankaro ba ta ji bakinsa cikin nata yana neman halshenta sai tai saurin rufe ido tana son ja da baya, hannunsa ya mika ya rikata yadda ba zata fadi ba idan kuma yai baya ba zata tsere masa ba. Cikin kwarewa da salon lagon halshe da baki yake sumbantarta yana zukar yawun bakinta a hankali yana sha. Jin kamar tsayin ba zai wadatar da shi ba ya saka ya jinginar da ita ya saka hannayensa duka biyu ya rike fuskarta yana sumbantarta, ita kanta sai da ta karbi sakonsa jikinta ya amsa gaba daya. A hankali ya zare bakinsa yana kallon fuskarta da idanuwanta dake rufe kwayar idonsa har ya canja kala sai numfashi yake ajewa a hankali. Can kuma ya mika bakinsa ya fara lasar wuyanta da halshensa ya rabo da jikin ginin ya mika hannayensa ya fara jan zip din rigarsa zuwa masa sai tai saurin rikewa ta matsa bayan gabanta na faduwa.

“Ka ce zamu je gurin Momy”

Ya bude idonsa daker yana kallonta.

“Eh”

Ya fada kamar an masa dole, sai hade yawun dake tarar masa a baki yake.

“Toh muje”

Ta fada tana kara yin baya ganin yadda yake kallon kirjinsa kamar wanda aka budewa su aka ce gasu ka kalla har ka kure ganinka, murmushi yai ya shafa kansa ya juya ya kunna tap din ya wanke fuskarsa sannan ya dauki tawul ya goge ya rika hannunta suka fito. Sai da yaja kofar bathroom din ya rufe sannan ya duka ya dauki matarsa cak yana dariya.

“Guduna kike yi sarkin wayo? Idan mun dawo ai babu inda zamu kara zuwa, kwanakin da na yi ina ta jira yau sai idonki ya raina fata”

Ta rufe fuskarta tana jin kunyarsa da kuma tsoro a lokaci daya domin bata mata wacan dare da aka keta haddinta ba har sai da ta fita hayyacinta. Be direta ko ina ba sai gaban motarsa ya bude mata ta shiga sannan ya zagaya ya shiga mazauninsa ya mika hannunsa ya rika nata kana yai ma motar key yai reverse da dayan hannunsa. Ko kamin ya isa gate din mai gadin ya bude masa gate suka kama hanyar gidansu Momy. Kamin su isa gidan ya sumbanci hannun Aminatu yafi a kirga sai kallonta yake kamar yau ya fara ganinta. A harabar gidan ya faka sai da ya fita sannan ya zagaya ya bude mata ta fito faganta sai faduwa yake, yana rike da hannunta har kofar falon sai da ya danna door bell din sannan ya saki hannunta. Amal ce ta bude musu kofar tana ta kallon Aminatu da mamakin daya hana ta yi masa sannu da zuwa. He got lucky Daddy na zaune falon da Kabir da Momy da Hajiya Saratu alama wata maganar suke tattaunawa. A take Hajiya Saratu ta hade rai ta bata fuska tana hararar Aminatu. Momy kam kallon Aminatu kawai take irin kallon nan na marasa lafiya har ta zauna. Kabir yayi murmushi kamar yadda Daddy ma yake yi, ganin fuskar Daddy a sake ya saka Aminatu ta sauko kasa ta gaishe da Daddy sannan ta gaida Hajiya Saratu da bata amsa mata ba, ta gaishe da Momy da ke kusa da Hajiya Saratu, a mamakinta sai Momy ta amsa mata muryar can kasa alamar magana ma sai idan ta zama dole take yi. Daddy ya kalli Amal dake tsaye tana kallonsu ya ce.

“Amal baki ga matar yayanki ba ne?”

“Na ganta”

Ta fada sannan ya kalli Aminatu ta ce.

“Ina wuni”

“Lafiya kalau”

Aminatu ta amsa mata, sannan ta gai da Kabir. Daddy na dariya ya ce.

“Kai fa ya kamata ka gaishe ta”

Kabir ya shafa kansa yana murmushi.

“Daddy karka karawa Talba girma ka sa yarinyar nan ta raina ni fa”

Sai Daddy yai murmushi, sannan ya kalli Talba ya fara masa nasiha kan rayuwa da zamantakewar aure, a cikin abubuwan da ya fi jadda masa shi ne hakuri da kaiwar da kai. Ita ma Aminatu yayi mata nata sannan ya saka musu albarka ya kalli Momy ya tambaye ta ko zata ce wani abu ta girgiza masa kai alamar bata da wani abun cewa. Sannan Daddy yai masa umarni daya dauki matarsa su tafi gida, haka kuwa akai ya tashi tare da Aminatu sukai musu sai da safe suka fice. Hajiya Saratu ta bisu da kallon wulakanci tana yatsina fuska, sai dai babu damar fadin wani abu saboda Daddy na nan.

“Wai yanzu Alhaji haka za a zubawa shari'ar nan ido? Babu wani abu da zaka yi dan fitowa ya yarka daga wannan hali? Kowa fa ya san kaddara kuma idan har ka yardar da kaddara kamar yadda kake fada kamata yayi ka yi duk wani yunkuri daya kamata ka ceto rayuwarta”

“Ina ganin mun yi maganar da Amina ya fi a kirga, babu abun da zan yi kuma ban ce ku kuyi ba, a asiye alkali ko lauya duk ban yardar ba, ki da bayan idona ne ba zan yafe ba, ku bar shari'a tai aikinta duk hukuncin da aka yanke mu a shirye muke mu karbe shi”

Yana fadar hakan ya mike tsaye ya nufi kofar da zata sadashi da part, Kabir ya bi bayansa. A nan Hajiya Saratu ta samu damar kallon Momy ta ce.

“Haka zaki zuba ido? Ace mijinki baya jin maganarki? Ba dan tashin hankalin nan da ya faru ba ai ya yanzu wani labarin ake ba wannan ba, amman ko yanzu ba mu makara ba, shiryawa zan yi na tafi daman tun da yace na dawo ban koma ba, na karbo aikin da yace zai yi na Alhaji, wannan yarinyar ma ni ban ga alamun aikin nan yayi ba tun da gashi har tarewa zai yi yau saboda ba shi da kunya”

“Karki Wahalar da kanki Saratu, ki watsar da wannan abu Aminatu da Talba da kika gani kawai ki barwa Allah komai ki saka musu ido, ki yanzu ba ni damuwar data wuce ta Leila”

“To ai idan aka masa aiki, sai ki ga ya dawo yana jin maganarki har ya yi abun da ya dace, ke Bokaye fa har alkalai suna yi ma aiki su yanke hukunci yadda suke so ba yadda alkalan suka yi niya ba”

“Saratu na ce ki watsar da maganar nan, ki bar ni da abun da ya dame ni dan Allah”

Hajiya Saratu ta cika da tsananin mamaki tana kallon Momy data tashi ta nufi upstairs ta barta nan zaune tare da Amal.

*** *** ***

Bayan sun dawo gida suka yi alwala a tare suka gabatar da sallah nafila suka kai addu'a sannan Talba ya rika goshin matarsa yai mata addu'a, sannan ya dauko musu kaza da yogurt ya zuba ya shiga feeding din matarsa, a hankali yake saka mata a baki tana karba tana ci har ta koshi. Sannan ya kwashe komai ya kai kitchen ya dawo dakin ya dauko musu tufafin bachi ya aje mata nata ya shi kuma ya saka wandon kadai daman ba al'adarsa ba ce kwana da riga balle kuma yanzu. Daukar kayan tai ta nufi bandaki.

“Me zaki yi?”

“Canjawa zan yi”

“Okay muje can sai mu yi brush”

Be jira cewarta ba ya rika hannunta suka shiga bandakin, ya zuba man goge baki a brush dinsa ya zuba mata a nata sannan ya mika mata. Kusan a tare suka kare wanke bakin, sai ta tsaya jiran ya fita ta canja kayan. Shi kuma ya ki sai kallonta yake yana murmushi.

“Ki canja ma?”

“Sai ka fita ai”

“Ashe kina da aiki”

Jin ya fadi hakan yasa ta juyo ta fito gabanta sai faduwa yake ta fito, shi ma fitowa yai sai ya nufi makunnun wutar yana fadin.

“Bari na kashe miki wuta sai ki cire”

Kamin ta ce komai ya kashe wutar dakin, a take hudu ya baibaye dakin baya iya ganinta kamar yadda ita ma bata iya ganinsa sai dai tasan inda yake tsaye shi ma haka. Da sauri ta shiga canja kayan cikin duhu sai jin hannunsa tai a jikinta ya rike rigar da take kokarin sakawa ya karba ya aje gefe, ya mika hannunsa ya kwance zagane dake daure jikinta ya aje ya cire underwears din dake jikinta sannan ya mika bakinsa ya hade da nata. A nan jikinta ya dan fara rawa, sai dai yanayin yadda take karbar sakon nasa ya saukar mata da natsuwa tana jin dadi abun da yake mata. Daukarta yai ya dora saman gadon, anan wasan ya sauya salo, labarin kuma ya zama babba kamin safe. Talba ya zama cikakaken namiji duk wani gyara da akai ma Aminatu a dare ya lalata shi, ita kanta sai da dandani kudarta domin azabar da ta ji a wannan daren rabin wanda ta ji nw a wacan daren, domin gyara akai mata ba na wasa ba. Shi kansa be yardar wadandan kaskatattun mutanen sun taba martarba ba.
Da asuba shi ya taimaka mata tai wanka ta gyara kanta sannan shi ma ya shiga ya tsabtace jikinsa.
A tare suka yi sallah, bayan sun gama ya juyo ya rumgume matarsa, yana jin wani irin sonta na karuwa a ransa, sannan ya dauke ta ya kwantar da ita saman gadon ya kwanta gefenta ya rumgume ta yana ta saka mata albarka. Kan kace kwabo ita da shi bachi ya dauke su, domin ba ita kadai ta gaji ba har da shi daya raya dare yayi yin abun da ne taba ba, balle ace ya saba, shi kansa sai da jikinsa ya fada masa.

FARUK POV.

A lokacin da Faruk ya gabatar mata da kudurinsa na son aikawa gidansu, bata musa masa ba, daman ita ma abun da take jira kenan domin a ganinta yanzu sun gama fahimtar juna. Faruk ya fara shiryawa da kansa ya je ya gaishe da mahaifinta sannan ya fada masa manya za su shiga cikin maganar, mahaifinta yayi murna sosai sai dai ya bukaci a ba shi lokaci kamin manyan su shiga domin

yin bincike kamar yadda addinin musulunci ya tanada. Sai da yai duk wani bincike da ya kamata ya tabbatar Faruk ba shi da wata matsala kuma yarsa tana sonsa sannan ya aminta ya hadu da iyayen Faruk din, wadanda suka hada da kannen babansa da kuma kawunsa. A cikin satin aka kawo kayan baiko aka saka musu ranar aure. Murna a gurin Mama da Rukaiya ba a magana shi kansa sai yake jin kamar yanzu ne zai yi auren farin.
Ana tsaka da shagulgulan biki mahaifinta yai masa kyauta wani ƙaton gida na ji da fadi, mai matukar kyau gidan sama ne mai hawa daya. Ba karamin dadi Faruk ya ji ba, ba dan ba shi da muhallin da zai aje mata Ramla ba, sai dan karamcin da mahaifinta yai masa na bashi ita kuma ya kara masa gida, mace mai kyau yar daya tilo a gurin hamshakin dan kasuwa Alhaji Isma'el Zabarma.

A lokacin da Labarin auren Faruk ya samu Baturiya ba karamin tashin hankali ta shiga ba, ganin zai yi aure ya barta kuma yar babban gida zai aura wanda ta fita komai a duniyar nan. Daman a duk lokacin da tsohon miji ko tsohuwar mata suka ji daya zai yi aure hankali daya tashi yake balle kuma ita, da ta san abun da ta aikata. Gashi Yayanta ya matsa mata da maganar fitar da miji tun daga lokacin da ya gane sana'arta hankalinsa ya tashi balle kuma yanzu da suka san halin da Faruk yake ciki na rufin asirin daya samu, sai yake dora mata laifi yana kara tabbatarwa cewar Faruk ne mai gaskiya, domin gashi tun a nan sallah ya masa sakamakon. Umma na ta fara damunta da maganar aure ganin kanwarta ta tsayar da nata mijin, ita kuma har yanzu shiru sai yawan zuwa da ake mata sallama ko da yaushe. Ga kuma Faruk da ta ji zai yi aure bata son ya riga Baturiya.
Sai dai har yanzu bata samu wani wanda yake son kamar Faruk da Fahat ba, mostly ma wadanda suke zuwa gurinta duk ba zancen aure ke kawo su ba,wasu ma ta hanyar Ramlee take saninsu domin ita take hada ta da su, duk kuwa da kasancewar ta nuna mata bata son wannan bakar sana'ar amman ta ki yarda ta kyaleta saboda tana samun kudi da ita sosai.
Yau ma tana fitowa wanka Umma ta hau ta da fadan ta fitar da daya a cikin masu zuwa gurinta.

“Kin fi son Faruk yayi aure ya bar nan makiya da yan gulma suna miki dariya”

“Umma zan fitar akwai wanda na yi ma magana, ya ce na dan bashi lokaci zai yi magana da iyayensa ne”

Ta fada sannan ta nufi dakinsu ta shige, kasancewar a bandakin falo tai wanka. Ko da ta shigo wayarta na ringing sai ta karasa da sauri ta dauka ganin number Al'Qasim ya saka tai saurin picking. Sai da suka gaisa sannan ya jata da hira daga bisani suka yi sallama, a laifi tana sakin jiki da shi kasancewar shi din ba a hanyar banza suka hadu ba, kuma ya fada masa matarsa da rasa da dansa tun a wacan yammacin da suka hadu a lokacin data fito gidan Faruk.
The following day da ya zo zance gurinta take gabatar masa da kudinta na aure, ganin sun riga sun fahimci junansu a yanzu, ya san wacece ita ita ta san waye shi. Domin babu abun da ta boye masa na rayuwarta sai bakar sana'arta. Yadda ya amsa mata kadai ya isa ya bayyana irin kaunar da yake mata, jiki na rawa ya turo magabansa aka biya sadaki.

Ranar Assabar aka daura auren Faruk da Ramla, daure aurene da ya samu halarta manyan mutane daga gari gari wasu ma har daga waje, kasancewar

mahaifinta babban mutum kuma dan kasuwar zinari dake leka Dubai da india gurin sana'o'insa.
Duk wani abu na al'adar an gabatar kabanin dauren auren, wato event, sannan aka yi dinner a dare da aka daura auren. Washe gari bayan Amaryar ta gaishe da danginta an gabatar da ita ta sauran yan'uwansu aka kaita gidan mijinta da aka kawata kamar ba za a mutu ba. Kana ganin gidan da irin dukiyar da aka bata a gidan zaka san Ramla yar gata ce, domin an yi wasa da nera kamar ba a san zafin nemanta ba. A sabuwar mota aka kai amarya wanda Mahaifinyarta tai mata kyauta, duk uban lefen da Faruk yai mata baka saka kala ko daya a cikin kayansa ba kasancewar mahaifinta yayi mata kayan cin ciki masu mugun tsada zinarin dake wuyanta kadai abun kallo ne. Sai da suka cika sati biyu da tarewa mahaifinta ya biya musu kudin jirgi ya bawa yarsa enough kudi da zai ishesu Honey moon.

*** *** ***

Maganar auren Baturiya da Al'Qasim ta fara nisa domin iyaye sun shiga ciki, duk dai ba wani sonsa sake sosai ba kusan yanzu a kullum zuciyarta da tunaninta yana gurin Faruk, rayuwar da suka yi a baya yana ta dawo mata sabo, daman can tana kaunar Faruk sosai kawai dai talaucinsa ne bata so, yanzu kuma ya samu rufin asiri, duk yadda take jin son Fahat na Faruk ya dara a yanzu saboda shi ta rayu da shi ta san yadda yake da hakuri da iya mu'alama kuma ga da a tsakaninsu, sai duk wannan abun da take ji bata yardar da nunawa kowa ba musamman ma mahaifiyarta da tasan zata iya yi mata fada sosai idan ta san da zancen.
Ranar da tasan an daura auren Faruk da Ramla mutuwa ne kawai batai ba amman ta ci kuka har ta gode Allah ga wani uban kishi da bakinciki daya tsaya mata a zuciya, tana ganin ta wahala da shi shekara da shekaru sai yanzu da arzikin ya zo wata zata zo ta cinye ta jidadin mijinta ita tana gefe kamar yajin kosai.
A gashi a cikin mutanen da suka hallarci daurin auren har da yayanta domin har gobe akwai mutunci a tsakaninsa da Faruk, bayan alaka ta zumunci. A week later da auren Faruk ta fara canjawa Al'Qasim idan ya kirata a waya ba zata daga ba sai ta ga dama, idan ya zo zance bata son amsa masa kamar ba ita ta gabatar da shi a idansu da sunan wanda take son auren ba, gaba daya sai ta canja masa daman can ba wani sonsa take ba kawai dai ta fitar da shi ne saboda Umma da Yayanta sun matsa mata, ba wani babban aiki ne da shi kamar yadda take so ba, ko ma yana da shi ita yanzu zuciyarta Faruk yake hange ba kowa ba.
Ana sauran sati biyu aurensu ya fara ja da baya, shi ma yana dan janye jikinsa kamar yadda take bukata saboda kananan maganganun da yake ji ana kawo masa na suka a cikin kuwa har da Ramlee sai dai be san akwai wata alaka tsakaninta da Baturiya ba, domin bata nuna masa haka ba, sai dai ta fada masa Baturiya bata tsaya ga kanta ba, wai mace ce mai kwadayi shiyasa ta fito gidan mijinta, kuma wanda ta fasa aure kamin shi ya fasa aurenta ne saboda ya gano alakar dake tsakaninta da babansa. Daina zuwan da yai na kwana biyu har yana maganar daga auren zuwa gaba ba karamin dadi yai ma Baturiya ba, domin ita a yanzu burinta ya auren ya fasu ta komawa tsohon mijinta Faruk.

“Gaskiya idan har zaka daga auren nan zuwa gaba sai dai a fasa shi gaba daya, taya sai da aka tsayar da magana zaka maida mu mutanen banza yanzu ka zo da wani zance wai a daga aure har gaba? Gaba yaushe? Zaunawa zan yi na yi ta jiranka har gaba? Ga dana yana da bukatata ina son dana a kusa da ni”

Ya mata kallon rashin fahimta.

“Ban gane kina son danki a kusa da ke ba! Ba kin ce yana hannun mahaifinsa ba?”

“Eh amman idan na yi aure ai dole karbo abuna zan yi, za ban barshi a can matar uba tana azabtar da shi”

“Amman ba mu da ke cewar zaki karbo dakin ki tafi da shi ba?”

Ta masa kallon rainon wayo.

“Okay so kake na je kawai nai ta renon wadancan yayan naka da matarka ta mutu ta bari ko? Wato ga yar aiki ka dauko? Amman ni dan yaro daya da zan tafi da shi zaka yi complain, to Wallahi karka dauka zan iya rika maka yaranka kai ma”

Da mugun mamaki yake kallonta domin can da bata fada masa haka ba, shi kuma irin mazan nan ne da basa kaunar yaron wani a gidansu, kuma basa bari a fita da nasu. Da gangan Baturiya ta kirkiro wannan abun saboda ta lalata alakar dake tsakaninta da shi so that ta samu yacw ya fasa ko ba zai iya ba. Sai faduwa ta zo daidai da zama domin shi ma abun da yake da buri kenan a yanzu. Musamman da yaji cewar da danta zata tafi ga kuma abun da Ramlee ta fada masa har tana nuna masa hotonta a wayarta.
Kamin ya bar kofar gidan sai da Baturiya ta fusata shi suka yi rabuwar rashin dadi sannan ta shigo cikin gidan tana jindadin abun da tai. Shigowa ta dauki buta ta shiga toilet din tsakar gida tai zawo ta fito, kwana biyu haka take fama da yawan ba haya kuma idan ta shiga bata komai sai tsawo sai yawan ciwon kai da ciwon kashi bone pain duk inda kashin jikinki yake ciwo yake, sai dai bata dauki abun so serious ba ganin dan kanoma yana saka haka, sai tai ta shan maganin hausa na dan kanoma amman na canji. A ranar da sukai fadan be kwana ba sai da ya samu Yayanta wanda yake a matsayin ubanta ya fada masa yadda sukai, yayanta ya bashi hakuri ya ce zai same ta yayi mata magana, amman Al'Qasim ya nuna masa shi dai ya hakuri da ita gaba daya. Haka kuwa akai auren ya fasu kamar yadda take so, sai dai ta sha fada a gurin Yayanta da Umma sosai musamman ma Yayanta da yace ya bata sati daya ta kawo wani wanda take so.

“Ni ba ni da kowa yanzu”

“Ban gane baki da kowa ba? Baki da kowa kuma kika ci wa wannan yaron mutunci?”

“Wai Rafi'a mi yake damunki? Ko dan wannan yaron Fahat daya fasa aurenki be kamata ki auri wani ba saboda ki bashi kunya? Ga kuma Faruk din nan shi na har yayi aurensa”

Yayanta ya kalli Umma.

“Wannan yarinyar da kike gani, bata da mutumci, kuma a zaman su ita take cutarsa shiyasa yanzu amanarsa take fita shi kuma yana ta yi gaban”

Umma ta tabe baki.

“Kai dai har gobe ba zaka daina ganin laifin Faruk ba, a kullum shi ne mai gaskiya ne a gurinka”

Ya girgiza kai yana murmushin takaici.

“Umma baki san halin wannan yarinyar ba, Wallahi makira ce kina ganinta kamar ta kwarai babu alheri a zuciyarta, ni kadai na san ko wacece ita”

Baturiya dai kansa na kasa domin tasan abun da yayanta yake magana akai.

“Kar na sake ganin wani a kofar gidan nan idan ba aurenki zai yi ba, na fada miki ko?”

Ta daga masa kai alamar gamsuwa.

“Babu wanda zai sake zuwa Yaya ba zan sake sauraren kowa ba”

Umma ta kalleta baki sake.

“Ban gane ba zaki sake sauraren kowa ba”

Sai kawai ta fashe da kukan munafurci.

“Duk wanda ya zo ya ji cewar kana da da sai yace ba zai aureka ba, ko kuma ba zaka tafi da shi ba”

“To ina ruwanki, yaron dake hannun ubansa?”

“Ni ba zan bar shi a can ba, ban san iya azabar da matar uban zata masa, ina yin aure zan dauke ɗana, idan har na bar shi ya zauna a gidan nan sai idan ni ce a tare da shi”

Yayanta yayi murmushi domin ya fahimci manufarta. Umma ma haka.

“Kar dai ki ce min so kike ki koma a gidan mutumen da ya gama wulakantaki?”

Ta yi shiru bata ce eh ba balle aa.

“Aa Faruk be mata komai ba, ai da ya ci amanarta da yanzu shi ne Alhaki zai bibiya ba ita ba”

Cewar Yayanta sannan ya kara da cewa.

“Kar ma ki kuskura ki ce zaki tunkari wani da wannan maganar, ta ya zaki bude ido yanzu ki ce kina son komawa a gidansa saboda yayi kudi ko? Bayan can da ki murje ido kin ce ba ki bukatar zama da shi sabida taja talaka”

Tashi tai tana turo baki gaba alamar maganar bata mata dadi ba ta nufi dakinsu, daga Umma har yayan nata kallo suka bita da shi. Takaici ya hana Umma cewa komai, da tunani kala kala ta kwana a ranta, na yadda Faruk zai yi mu'amalar zamantakewar aure da amarya ita tana nan gidansu, ta dayan bangaren kuma tana tunanin yadda zata bullowa labarin ta haddasa musu fitina a cikin gida ta hana su zama lafiya, da kuma hanyar da zata bi ta koma gidan Faruk so that a kwashi romon dimukuradiya da ita.

Washe ta shirya da wuri saboda zuwa asibitin da take son yi domin tsawon da take ya matsa mata sai haifar mata da rama yake ga ciwon jikin dake damumta. Shiga tai ta mutunci ta ta dauki jakarta da wayarta sannan ta fito ta fadawa Umma dake shirya abun karyawa cewar zata je asibiti. Umma ta kalleta sama da kasa sannan ta kira kanwarta tace ta rakata domin a yanzu bata yarda da ita ba, gani take kamar gurin Faruk zata je ko Mamansa. A dole kanwarta ta fasa zuwa makaranta a ranar ta rakata asibitin. Bayan ta samu ganin likitan ne ta fada masa dukan wani abu da yake damunka, sai ya dubuta mata awon jini da fitsari sannan ya dora ta akan wani maganin kamin washe garin ranar da zata dawo ta kawo masa sakamakon gwajin nata.

Sai da ta fara zuwa gurin dauki jinin sai suka fada mata sai ta zo gobe da safe kamin ta ci komai za su dauki jinin nata, sannan ta siye robar fitsari sauka ce ta kawo fitsarinta na farko da zata fara yi bayan ta tashi daga bachi. A tare suka dawo da kanwarta gida. Washe gari ma sai da Umma da saka kanwarta ta sake rakata har aka dauki jinin nata sannan ta mika musu fitsarin da tai. Sai suka fada ko karfe nawa zata dawo ta karba, cikin asibitin ta dawo ta zauna suna da hira da yar'uwarta har lokacin ya cika sannan taje ta karba, sai da dakin ganin marar lafiya ba wacan likitan na farko ta tarar ba, wani ne dabam yana duba marasa lafiya. Sai da tai masa bayani sannan ta mika masa takardar da awon da kuma takardar maganin da aka rubuta mata.
Ya dade yana kallon takardun sannan ya kalleta.

“Kin taba aure?”

“Eh na taba?”

“Kin dade da yin auren? Kina tare sa mijin ko kun rabu?”

“Eh mun rabu”

“Mutuwa yai ko kuma yana raye?”

Gabanta ya soma faduwa ganin likitan yana mata tambayoyi.

“Lafiya Doc?”

“Lafiya Kalau, kawai ki amsa min”

“Yana da rai?”

“Kuma lafiyarsa kalau?”

“Aa gaskiya ba shi da lafiya”

Ta fada ne kawai saboda ta ji abun da Likitan zai fada, domin hankalinta ya fara tashi.

“Kin san abun da yake damunsa?”

“Aa be taba fada min ba, gashi har mun rabu”

“Okay yanzu zan rubuta miki wani gwajin ki tafi kai tsaye dakin gwaje gwaje na masu cutar HIV za su yi miki wannan gwajin babba ne so that mu tabbatar da abun da yake damunki”

Ta dora hannu saman kai tana zaro ido.

“Doc HIV fa kace? Na shiga uku na lalace, rayuwata ta kare”

Sai yayi kokarin kwantar mata da hankali.

“No No no ba mu tabbatar ba tukuna har sai kin yi wannan gwajin, kuma ko da ta tabbata shi din ne zamu dora ki akan magani, zaki yi rayuwa ki samu lafiya fiye da wanda ba shi da shi, ki kwantar da hankalinki HIV ba yana nufin karshen rayuwa ba ne”

“An ki a kwantar, tun da ciwon ba a jikinka yake ba ai dole kace na kwantar da hankali, ina kwanciya hankali ga wanda rayuwarsa ta kare? Wayyo Allah ni Rafi'atuuuuuu”

Ta fashe da kuka, sai kuma tai saurin share hawayenta ta fito kamar mahaukaciya ta fice fuuu kanwarta ma sai da ta hada da dan gudu sannan ta cin mata.

“Anty Rafi'a Lafiya?”

“Ba lafiya Ba lafiya....”

Ta fada tana kuka, kamar kuma wanda ta tuno abu sai ta share hawayen dake zubo mata.

“Sun ce wai dankano ma ne, ya kamani wai sai an yi min aiki idan ban warke ba? To ina lafiya take a nan”

Ta sake fashewa da kuka ta dora hannu saman kai.

“Wayyo Allah na shiga uku rayuwata ta zo karshe”

A cikin satin Asibiti kusan hudu ta tafi ana mata gwanji yana bada result daya cewar tana dauke da cuta mai karya garkuwar jiki. A lokacin ne Rafi'ah ta samun kanta cikin tashin hankali wanda ya amsa sunansa tashin hankali. Da kukanta ta isa gidan Ramlee tana shiga ta rufe ta bakar addu'a da tsinuwa.

“Kin kai ni kin baro, daman abokin mutuwa kike nema kuma kin samu, Ramlee kin gama da rayuwata, ba zan tana yafe miki ba, Allah ya isa tsakanina da ke macuciya Azzaluman ko a lahirar wutarki dabam ce Ramlee magajiyar karuwai da kurciyarki kin bata rayuwarki kin bata tawa”

Ramlee dai sai kallonta take, a tunaninta Baturiya na mata masifa ne saboda ba je ta tsoke aurenta da Al'Qasim.

“Haba Baturiya, ya kike wannan harkowa kamar baki san inda na fito ba?”

“Da ace ban san inda kika fito ba, da yanzu ina nan cikin koshin lafiya da kwanciyar hankali,amman saboda na sanki kin fitine rayuwata kin jefa ni a bala'i da masifa”

“Wai me ya faru ne?”

Ramlee ta tambaya a tsawace.

“Sanadiyarki na kwasowa kaina bakar cutar da bata da magani, hiv Ramlee HIV saboda muguwar hanya da turbar da kika dora ni”

Ramlee ta bushe da dariya.

“Wai daman baki shirya kwasar Hiv ba kika fito bariki? Ni na dauka ma wani babban abu ne kika ta wannan haniniyar saboda shi? To kwantar D hankalinki ni da ke duk kanwar ja ce, daman duk wanda ya fito bariki ai ya bude mata hanyar shiga ne”

“Barikin uwarki? Ai ke kika lalata ni kika dora ni a muguwar hanya marar kyau tsinanniyar Allah ba zan taba yafe miki ba”

“Ai kowa ya ga zabuwa da zanenta ya ganta, daman can dama kike nema ba wai ni na lalata ki ba, kuma kudi kike so Baturiya su kuma masu bada kudin suna son abun kudi, sai kuka yi canja to miye kuma na ganin laifin juna a cikin? Taimake ni na taimake ka ne muka yi, kika ba su suka baki, ni kuma kika taimaka min na samu kudi, kuma ni ma da kika ganina ina dauke da cutar nan fa, kawai dai bana wasa da shan magani ne shiyasa kika gan ni haka”

“Amman baki tana fada min ba, ba zan biye miki ba shaidaniya, da ba zN bari ki halaka ni ba, kin bar gidan iyayenki ki dawo a nan kin lalata min tawa rayuwar”

Baturiya ta fada cikin kuka tana nuna Ramlee.

“Ai ni na kona, bana jin kauri. Tun farkon fari ya kamata ki san da cutar amman mugum son kudinki ya rufe miki ido, kara ni ai, ban tana aure ba balle na aje yaran da zasu gi bakincikin abun da na aikata nan gaba, kuma ban aikata zina da aurena ba, ke fa duk kin hada, har cikin sunna kika zubar saboda son kudi kuma da cikin kika aikata zina, Allah ya tsare bawan Allah mijinki be da hakkinki shiyasa ya rabu da ke tun kamin ki laka masa cuta”

“Wato kin san mutanen da nake mu'amala da su, suna dauke da cutar amman kika kyale ni saboda kina azzaluma macuciya”

“Ah kudi fa kika so, daman shi Alhajinki na farko a likita daya yake ba mu magani ni da shi, saboda bama shiga asibiti kar a gane mu, ni baki ma fada min yadda akai kika gano kina dauke da cutar ba sai masifa kike ta yi, mutane da yawa zaki same su dauke da cutar nan fa yanzu, ba wani abu bane indai zaki tsare shan magani tun da kowa ya siye rariya ai ya san zata zub da ruwa”

Tsabar bakinciki da takaici Baturiya bata sake ce mata komai ba, ta juya ta fita wasu hawaye masu zafi na sauko mata. Tana isa gidansu ta shige cikin dakinsu ta fashe da kuka tana jin kamar ta kashe kanta ta huta. Kukanta ne ya saka Umma ta shigo dakin da sauri tana tambayar abun da ke faruwa.

“Umma ina son na koma gidan tsohon mijina, ina son na koma gidan Faruk na kula da dana, na yi nadanar duk abun da na yi nasa, Wallahi duk wai abun dana fada karya nake masa Umma, dan Allah Umma ki yi duk yadda zaki yi na koma gidan mijina, ina son Faruk Umma ki taimaka min dan Allah”

Wani irin kuka take na fitar hankali tana riko Umma. Umma kam sai kallonta take tana mamakin ikon Allah, a tunaninta wani asirin ne Faruk yai mata ta haukace tana wannan abun, wata kila ma shiyasa ta fasa auren Al'Qasim. Wani irin zillo Baturiya take tana jin kamar ta dawo da aurenta da karfi ita da Faruk, a yanzu ta san bata da wata mafita kamar ta lallaba ta koma gidansa ko da zai gane Cewar tana dauke da cutar ta riga ta shafa masa dole ta rayu ita da shi a haka. Sai a yanzu take bakinciki da nadamar zubar da cikinsa da tai wata kila da ya dubi yayanta ya dawo da ita.

“Ashe ka tare”

Talba ya kalleshi sai dai be ce masa komai ba. Ali yayi murmushi ya zauna kujerar dake office din.

“Har yanzu zuciyarka na raya maka ina son Leila? Idan ta raya maka haka, bata maka karya ba, Tabbas ina kaunar Leila sai dai a irin son da kake mata ba, so na yan'uwanta na aboki da aboki kuma na yaya da kanwa, Talba saboda kai na san Leila da babu kai wata kila ko sunan taba zan taba sani ba, shakuwar dake tsakanina da ita, kai ka sassasata saboda sasanci da nake yawan yi muku, ita kanta ta shaku da ni saboda haka idan har kana ganin na zufafa akan abun da nake, kai ka bada dama Talba, har abada ba zan iya auren Leila ba ko da baka raye, amman tabbas ina tausayinta, kuma ina son farincikinta, ba zan taba lalata alaka da kai saboda mace ba, amman ka bani mamaki ta yadda ka tare da matarka yau kusan wata daya amman baka fada min ba, na so na kyale na bar magana a yadda ka tsarata kuma ka so ta tafi amman sai na ji ba zan iya ba, i wish you success in your marriage Allah ya ba ku zama lafiya”

Har ya gama fadar abun da zai fada ya fice Talbe be ce masa uffan ba. Fitarsa office din da minti arba'in Talba ya gama abun da zai yi, ya fita office din ya nufi gidansa, sai dai be isa ba sai da ya tsaya ya siya mata kayan kwadayi a hanya. Horn daya ya danna mai gadin ya bude masa gate ya shiga cikin gidan. Ya bude motar ya fito ya rike da ledar da yai mata siyayyar sannan ya isa gurin kofar ya kwankwasa. Ba jimawa ta bude masa tana sanye da wando da riga na Turkish kanta ba dankwalin ta daure gashinta gwanin sha'awa. Kamshin turaren wuta ne abun da ya fara yi masa lale marhabun sai kuma sanyi ac da kuma Aminatu da ta rumgume shi tana masa sannu da zuwa.

“Kin yi kyau Shalele na”

Ya fada yana kare mata kallo sai tai murmushi ta mika hannu ta rika ledar hannunsa, shi kuma ya miko hannunsa ya dafata yana shafa bayanta zuwa mazaunanta.

“Me kike dafawa?”

“Doya”

“Wow kamar kin san ina kwadayin doya yau kuwa”

“Da gaske”

Ta fada bayan ta aje ledar hannunta kan kujera ta juyo ta saka hannayenta duka biyu ta rumgumo wuyansa.

“Uhmmm”

Ya fada yana sumbantar kirjinta, sai ta sake shi tana kokarin juyawa ya rike ta yana shafa shape dinta yana sumbatar wuyanta kamin ya juyo da ita ya hade bakinsa da nata. Rayuwa ta zame musu mai sauki idan yana cikin gidansa har mantawa yake yana da da wata damuwa kamar yadda ita ma yake matar da ita duk wata damuwa tata yana faranta mata rai, idan yana gida tana jikinsa idan baya gida suna tare da juna waya. Sai da ta wata biyar a gidan sannan ta samo wanda zata rika koya mata karatun bokon, a lokacin tana da karamin cikinta dan wata uku da Talba ke ta tattali kamar zai cinye.

Nine months later

Dan dan zon mutane ne suka cika bakin kotun cikin har da yan jarida, yan'uwan Baaba da wasu daga cikin dangin Daddy da Momy wasu a cikin kotu wasu a waje. Suna sauraren hukuncin da yankewa Leila da Madina tare da mutanen da ta aikata mummunar ta'asar tare da su hukunci a zaman kotu na karshe. Shari'ar Leila ce ta farko da aka fara yi sai da Alkalin ya bawa duka lauyoyin damar magana idan da mai karin bayani kowa yayi maganar. Lawyer Leila ya roki alfamar kotu ta yi ma Leila sassauci ta hanyar biyar diyar Baaba, duba da akan kuskure ta aikata abun da ta aikata kuma ta amsa laifinta ba tare da ta wahalar da kotu ba. Alkalin ya karanta dokoki da kuma hukuncin da dokar kasa ta criminal code ta tanadarwa wanda ya aikata kisan kai.

“Akan wannan hukuncin koru ta yankewa Leila Mu'azu Shimkafi hukuncin kisa ta hanyar rayata....”

Wani irin ihu Leila tai ta zube kasa tana hargagi da kuka marar misaltuwa, Daddy yai saurin yin masa da kansa hawaye suka zubo masa, Momy kuma ta fashe da kuka ta dora hannu a kai.

“La'ilaha Illalahu Muhammadu Rasullulillahi”

Talba ma sai da hawaye suka zubo masa, Kabir ya mike tsaye yana kallon Alkali cike da tashin hankali, Amal kam bata san lokacin da ta bar inda take zaune ba ta nufi inda Leila take tana wani irin kuka domin ganin take kamar a lokacin za a kasheta. Sai dai kamin ta karasa gandireba suka rike Amal wasu kuma suka tashi Leila ta mike tsaye tana zubewa kasa sai sunan Daddy take kira.

“Daddy.... Daddy.... daddy.... Momy.... Momy.... Talba... Kabir.... Wayyo Allah Allah ya tuba ka yafe min Allah.... Wayyo Allah na.... Kashe ni za'ayi Daddy..... Daddy.....Daddy su kai ni inda ba a dawowa babu wanda zai sake ganina.... Ba zan sake ganin kowa ba..... ”

Wani irin kuka Leila take na tashin hankali da taba zukata, kusan duk wanda yake kotun sai da yayi hawaye, shi kansa Alkalin sai da abun ya taba masa zuciya. Zubewa take kasa gandirobobin dake tare da ita suna rikonta. Ali ma kuka yake sosai yana jin kamar ace akwai wani abu da Ai iya yi.
Can ta samu sa'a ta fisge kanta ta ruga da gudu ta rumgume Daddy sai ya fashe da kuka da kuka ya rumgumeta sosai Momy ta mike tsaye da sauri ya rumgumeta ta baya tana kuka.

“Daddy karka bar ni, Momy ki taimaka min don't leave me”

Da karfi suka bata da Daddy da Momy dake ta uhu cikin kotun, daker aka fito da ita Amal kuka Kabir kuka Talba kuka Daddy kuka Momy kam ana kawowa bakin kofar fita kotun ta yanke jiki ta fadi. Sai da aka dauke ta zuwa asibiti. Leila kuma aka wuce da ita gidan yari. Madina ta aka yanke mata hukuncin shekara goma a gidan yari kamar yadda dokar kasa ta tanadarwar wanda ya aikata kidnapping. Alfa aka yanke masa hukuncin kisa ta yankar harbi da bindiga tare da yaransa.
Daga asibitin Talba ya wuce gida gurin matarsa tun cikin mota yake ta hawaye har ya isa gidan, Aminatu na ganinsa ta san mijinta yana cikin damuwa kamin tace masa komai ya rumgume ta ya fashe da kuka. Ko ace be hada komai da Leila ba ya san an yanke mata wannan hukuncin dole ya tausaya mata balle kuma har sun rayu tare da shi da ita.

“You got lucky kaddararki mai sauki ce Aminatu, idan kika ga kaddarar wasu sai kin gode Allah”

Ya fada yana shafa fuskarta.

“An yankewa Leila hukuncin kisa ta hanyar rayata”

Wani irin sanyi jikinta yayi take hawaye ya kawo a idonta.

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un yanzu ba kasheta za'ayi?”

Ya daga mata kai, alamar eh

“Innalillahi Wa'inna Ilaihirraji'un”

Ta furta tausayin Leila ya cika mata zuciya. Ita da Shi sai suka koma kamar marar lafiya. Ta kasa ce masa komai, shi kam yana shiga dakinaa sai bachi yai gaba da shi. Sai da gama komai sannan ta zo gabansa ta zauna ta kai hannunta hannunta tana shafa kansa dayan hannunta kuma a kan cikinta. A hankali ya bude idonsa ya tashi zaune yana kallonta damuwa ce karara a fuskarta idonta yayi ja sosai ya kumbura alamar ta yi kuka sosai.

“Zan tambaye ka wani abu”

Ya kalleta.

“Minene burin Leila na karshe a duniyar nan?”

Talba yayi shiru yana nazari, sannan ya sake kallonta.

“Ban sani ba”

“Aurenka....”

Ya fada wani sabon kuka na zo mata, sai ta mika hannunta ta rika hannunsa ta matsa sosai cikin nata.

“Dan Allah ka cika mata wannan burin, ka aureta ko na rana daya ne, ka rumgume ta ka fada mata kana kaunarta ka cika mata wannan burin kamin ta

koma ga mahaliccinta dan Allah Talba... Ka yi min wannan saboda ni saboda abun da zamu haifa”

Ta dora hannunsa saman cikinta dan wata shida, sai ya daga mata kai ya kwantar saman cinyarta hawayenta na sauko suna diga gefen fuskarsa. Washe garin ranar da aka suka yi haka, ya samu Daddy da zancen, kuma Daddy ya goya masa baya aka tara few people aka daura musu aure ba tare da sanin Leila ba. Sannan Daddy ya kira Lauyerta ya zo gida suka tafi tare da shi da Daddy da Alhaji Tukur abokin Daddy. Domin har lokacin Momy tana asibiti. Ba au sha wahalar ganinta ba kasancewar suna tare da Lauwyer ta ne, Talba na tsaye har ta gama gaisawa da da su Daddy da Alhaji Tukur, Leila na zaune kanta a kasa, ta ki yarda ta kalli kowa, har lokacin hawaye take, zuciyarta har wani zafi take saboda bakinciki. Agaban Talba Daddy da Alhaji Tukur suka yi ta bata magana suna kokarin kwantar mata da hankali, har suka yi suka gama sannan ya zauna daga shi sai ita yana kallonta hawaye na sauko masa.

“Na sani wannan ba abu ne mai sauki ba Leila...”

Sai kuma ya kasa karasawa saboda kuka. Ya mika hannunsa ya riko hannunta ya saka a gefen fuskarsa.

“I'm sorry...”

Sai ya mike tsaye ya mikar da ita tsaye ya ya zagaya gafen da take ya rumgumeta.

“Na san burinki na karshe Leila, aurena an daura mana aure da ke yau”

A take ta fashe da kuka mai karfi ya rumgume shi.

“Ina kaunarki sosai, ina son ki Leila”

“Ka yafe min Talba ka yafe min duk abun da na yi maka please forgive me, kudi da yan'uwa ba su amfana min komai ba, mummuman halina ya kai ni ga halaka”

Talba ya rumgume ta sosai.

“Ya isa Leila, kaddararki ce a haka I love you so much”

Ya dagota jikinsa ya hade bakinsa da nata, sannan ya cire ya jingina goshinsa da nata, ita da shi suna maida numfashi, sai gata tana murmushi.

“I'm happy zan tashi da aurenka Lahira, i will be among your wife's”

“I will hold your hand to janna In'Shaa Allah Leila i love you so much”

“Ina Momy tana lafiya?”

“Tana asibiti”

“Please take good care of her, and Amal duk wani abu da kasan ba shi da kyau da kake hana ni na aikata ka cigaba da hana Amal”

Ya girgiza mata kai, sannan ya sumbanci hannayenta.

“Duk wanda kasan na taba mu'amala da shi ka roke shi ya yafe min, ni na yafewa kowa, build a huge Mosque for me, and ask Allah to forgive me”

“I will Leila a will i love you do you know that?”

“Now i know....”

Ya sake hannunta bayan ya sumbanci hannun, saboda security dake fadar lokaci yayi. Sai ta rike masa hannu ya rumgume shi.

“Stay here one more time...I'm so weak...”

Daker ta barshi ya tafi tana kuka shi ma yana kuka suka rabu, a ranar Leila ta raina kanta, tarin dukiya da sutura da dangin da iko ba su kwace a gaban alkalin duniya ba, idan ta tuna cewar zata goge laifinta ne har a gurin Allah sai ranta yayi sanyi.
Ranar da za a zatar mata da hukuncin aka fito da ita duka danginta suna nan, sai da tai magana da kowa ya nemi yafiyar kowa ta rumgume Kabir da Talba da Amal da Momy da Daddy, sannan ta shiga mota aka wuce da ita tana kallon yan'uwanta ta bar nan duniya. Tafiyar da ba a dawo da ita ba kenan sai gawarta, addu'a sosai akai mata kuma ta samu jama sosai saboda mutuwarta ta zama darasi a gurin mutane da dama musamman masu rayuwa irin nata.

“Allah ga yata nan ta dawo gareka, Allah ka yafe mata, ka karbi bakuncinta ka saka mutuwa ta zama hutu a gareta, kuma ya karbi tubanta, Annabi ya san da zuwanta”

Shine abun da Daddy yake ta fada har aka kaita gidanta ma gaskiya bayan ayi mata sutura an mata sallah. Kusam wata biyu Momy tai asibiti bayan rasuwar Leila sannan aka sallamota bayan ta fawwallawa Allah komai.

BATURIYA POV.

Sai da Umma ta saka ta gaba da fada ta tambaya sannan ta fadawa Umma gaskiyar komai, da kuma turba da Ramlee ta dorata, da irin cin amanar da tai ma Faruk. A lokacin ana ta shirye shiryen auren Fahat da Amal d kuma na Kabir da Rukaiya da za'a hade ayi lokaci daya. Faruk kuma matarsa Ramla na daf da haihuwa, karamin bakinciki da kunya Umma ta ji na jin cewar yarta ce marar Gaskiya, domin ita ma ta yi ma Faruk rashin mutumci da kyautawa. Hankalinta be kara tashi ba sai da fahimci yarta na dauke da cutar nan mai karya garkuwar jiki, ita kanta Baturiya a lokacin ne ta gane rayuwarta ta kare domin Faruk Fulani din da ta so komawa ya mata nisa har bada, duk hanyar da zata bi ya kula ta ta bi amman ba ta yi nasara ba, har Sultan dake gurin Mama kasancewar ya bar mata shi ne a gurinta ya zauna. Ta bi ta bi ta hanyar Mama amman ba wani alamun nasara.

BAYAN WANDASU SHEKARU....

A hankali aka yaye kyallen da aka rufe wani dan karamin asusun tallafawa yan gudun Hijira da marayu da Aminatu da kaddarar tare da Yayanta Bashir. Sai kowa ya ware hannun yana taba musu yan jarida na dauka. Babban dakin taro ne mai dauke da mutunen kusan dari biyar. Faruk da Ramla suna zaune a teburinsu Faruk na rike da Nimra, Ramla kuma na rike da Namra second set of twins dinsu da suka haifa. Rukaiya da Kabir a tebur daya, rike da dansu Abul-khairi. Yayinda Amal da Fahat suke zaune a guri daya yaronta Affan a kujera daya, sai tsohon cikin dake jikinta. Mommy da Daddy kuma na zaune da gaba rumgume da Little Leila wato yar Aminatu ta farko sai yaron cikin dake jikinta a yanzu. Sai da Talba ya gabatar da yawajin godiya na masu halarta taron sannan Aminatu ta kaddamar da asusun tallafi da naira miliyan goma. Kana ta kora da wajabin dalilin na som tallafawa yan gudun hijira da marayu a cikin halshen turanci. Kusam duk manyan bakin da Talba da Daddy suka gayyato sai da suka bada na su tallafin har Daddy da Momy. Sannan aka tashi taron bayan anci ansha kowa yana hamdala.

Ni ma na ce Alhamdulillah! Alhamdulillah!! Alhamdulillah!!!
Fatar Allah ya datarda mu ya tsare mu da aikim dana sani, kuma ya tsare mu da sherin yan bindiga.

For wadanda suka karanta ba su biya ba, ku sani wannan shari'ar sai gaban Alkalin da babu Lawyer ba mai kariya, shi zai mana hukunci.

For those who patronized me, na gode Allah ya bar kauna ya rufa muku asiri duniya da lahira. I love you All 😍 Zan yi missing dinki sosai more especially yan Comments Group😭

Subhanaka Allahumma wa bihamdika, ashhadu an la ilaha illa Anta, astaghfiruka wa atubu ilaika